TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

DUTSE

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

1 □□□

*Darasinmu na yau, hadisin da ke da ala'ka da hali 01 cikin 46.*
□
□
_*Manzon Allaah(□ □)* *ya ce:{WANDA MUSULUNCIN SU YAFI KYAU DAGA CIKINKU SUNE WA'DANDA SUKA FIKU KYAWUN HALAYE, IN SUN FAHIMCI ADDINI.}*
```[Sahihul Adab;285]```
_Wannan hadisin yana nuna mana cewa a cikin musulmi, wanda halinsa yafi kyau to shine kuma musuluncinsa yafi kyau. Ai kyawun hali shine mutum, shine dottaku. Allaah Ya azurta mu da halaye masu kyau. Allaahu aalam.)

A hankali ta lumshe idannuwanta cike da wani irin mad'aukakin shauk'i, leb'unnanta ta d'an cije sai kuma ta bud'e tana kallonsa a sanyaye cike da wata irin k'aunar jar rigar dake jikinsa mai had'e da wani shar shar sai rawanin da gaba d'aya ya rufe masa gaban goshinsa.

Cike da shauk'i tace "Dogarina, ina sonka, ina sonka kamar na mutu, ka ganni a nan tsabar k'aunarka ya sakani a kullum sai na je wajen hanyar ficewarka, sai nai ta ganninku ku dayawa kuna wucewa ashe dai kai d'in har an d'aura mana aure oh dad'i kasheni."

Wata murya marar dad'i ya bud'a yace " Ke yi min shiru, ni bana son hayaniya ni nan da kika ganni sai dogariya nake iya so dan haka ki min shiru."

Hannayenta ne ta had'e cike da tsoron ganin suturar jikin nasa na son komawa irin ta mutane sak sak ta had'e hannayen da kyau tana girgiza kai cike da hawaye take
```

fad'in " A'a, a'a kar ka b'ace, kar ka saka irin kayan al'umma sak mutuwa zan yi idan baka zo min a mutun ba na ganka gani gaka kar kar ka min haka dan Allah!"

Marin da aka kwad'awa fuskarta ne ya sakata bud'a nanauyan idannuwanta da suka gama rinewa suka gama macewa suka tafi duniyar mafarki, a firgice take kallon mutanen da suka zagayeta kafin ta ringa jin dariarsu sama sama sunna yi da dan karfinsu

A birkice ta kuma zuba masu ido kafin ta kai dubanta kan hannayenta dake rawa ta kara jimke su da wani irin karfi a bayane ta sauke wata irin nanauyar ajiyar zuciya kafin ta ji muryar kawarta na fadin " Sai ki tashi mu tafi, an tashi fa kina barcin asara"

Da sauri ta kuma kai dubanta kan allon rubutun kafin ta mike tsaye daga bajewar da ta yi tana duba jikinta cike da tsoron kar a je ta kwala fitsari sakamakon marin da ta sha, ita bama wannan ba shin kawarta ce ta kwada mata shi ko waye?

Da sauri ta suri jakarta ta juya ta bi bayan kawar tata tana kara hararar du wanda suka yi ido hudu da shi har suka fito tsakiyar titi sosai

Ba wada ta yiwa yar uwarta magana sai cen kamar an tukota ta nisa ta ce" Abin da mamaki, yadda kika san a gaskene haka na ganshi kai jama'a ko dai mahaukaciya ce ni?"

Juyowa kawar tata ta yi da dan bacin rai ta ce" Ai in dai a da ke ba mahaukaciya bace a yanzu zaki ja a maki irin mugun kallon nan, haba dan Allah kin ga yadda kike makyarkyata kina magiyar kina sonsa? Kina son waye ne? Ke haka zaki yi ta yin abin nan?"

Tsayawa ta yi jikinta ya yi mugun sanyi muryarta a sanyaye ta ce" Ko dai na haukace din ban sani ba?,

Juyowa Amina ta yi tana kallonta, irin yadda idannuwan nan nata masu kwayar ciki mai blue mai duhu da dan baki tsakiyarsu suka tara ruwa suke wul wul da su ta tabe baki kafin ta cije bakin nata ta kara fara tafia

Da sauri ta kamo hannunta a sanyaye ta ce" Amina, dan Allah ki fada min ko dai alamu ne na ciwon hauka ya kama ni? AMINa ni ko dan aiken gidan sarki ne a aura kin ina so, da na tsaya a dogari dan na ga a duniya idan kana son gannin wanda ya fi kusanci da sarki to dogari ne, dogari fa shi ke gyarawa Sarki zama a saman doki, ya gyara masa babar rigarsa ya saka masa lema ya rikw masa, a duniya sirrin sarki sirrin dogari an ce fa har bayi yake raka sarki, idan Allah ya amshi adu'ata da na jima ina yi na kasancewata yar uwar sarki ya bani dogari na aura ai na gama zama dangin sarki"

Galala Amina ta yi tana kallonta kafin ta janye hannunta da sauri ta ce" Walahi ki nutsu , kulun ina fada maki ki fa nutsu, ba dai sirrin sarki ba shine matar sarkinma! Wannan abin na tabata baki da lafia a kan maganar sarauta ke kam a nan kika kare, a duniyar nan du labarin wata masarauta a tafin hannunki take, idan ana history na sarakai har lumshe ido kike , kai ina kwakwaluwar nan taki da sake walahi!"

Kanta ta ringa gyadawa kafin ta tabe lebenta na kasa ta juya kwayar idannuwanta da yannayi na dan fada fada irin ta ji haushin nan ta ce" Sai me? Inace ke a duniya dan wake ko a gaban waye akai maki tayi zaki ci? To kowa da irin jarabawar da

Allah ya dora masa, ni tawa ta dogari ce idan ana budar kaini dakinsa ki fadi ki mutu don Allah!"

Itama bakin ta tabe kowace ta juya cike da bacin rai ta kama gabanta

Jira nake na ga ta nufi wani lalatacen gida duba da yannayin suturar jikinta, jira nake na ga ta shiga wani gidan namu na yaku bayi duba daga makarantar da ta fito, sai dai wani rantsatsen gida mai shegen kyau ta kutsa kanta kai tsaye ba tare da shayin mai gadin dake zaune yana busar tabar sigarinsa ba, shi din kansa sai na ga bai wani yi yinkuri na dakatar da ita daga kokarin shiga gidan da yake ba nasu ba wanda ga dukan alamu aikota aka yi

Kai tsaye ta zagaya ta gefen da yake kamar madafa ne , mace biyu ta wuce sunna zazaune sunna cin abinci ko ci kanku basu yiwa junna ba har ta karasa madafar nan ta shiga da sauri ta shiga bubuda kwanikan da ta tabata a nan ake saka mata nata kason abincin da sam mutun ba zai yi tunanin a gida irin wannan ana rabon abinci irin haka ba

Gannin wayam babu ya sakata fitowa rai bace ta kare masu kallo kafin ta girgiza kanta ta koma cen hanyar shigar ta buda tankameman falon da yake falonsu ne

Ja ta yi ta tsaya tana karewa falon kallo bata san lokacin da ta saki jakarta ta makaranta a nan ba ta janyo wani ashar ta dire tana kallon falon ta ce" Kai uban kowa ya fito daga wajen da ya shiga ya labe yau a yita ta kare a gidan nan"

Ba wai maganar a fito din ba, ko wa'inda ke zaune wani shashakai suka kaleta suka juyar da kansu

Kanwarta ce ta zo wucewa da roba a hannunta ta ce" Ke kauce zan shige"

Hannunta ta saka ta janyota kiiii baya ta yada sai da ta yi tangal tangal kafin ta juyo da yannayi na tashin balagar rashin kunya ta buda baki zata yi magana maganar ta makale mata sakamakon shako wuyanta da ta yi tana firfito mata idannuwa ta ce" Ke yaushe na zama sharar da zaki bangajeni ki nemi wucewa ko tunani kike kin fara tara mazaunan da suka kai nawa da zasu iya bangaji a bakin hanya? Bama wannan ba uban wa ya bata falon nan da na tashi tunda safe na share dan na ji dadin zama idan na dawo?"

Muryar maman wace aka shake din ce ta fito tana zarro ido cike da mamaki tana tafa hannu ta ce" Ke ke ya haka, yaya zaki kama min y'a ki makure haka salon ki saka fatar jikinta ta yi birdi bayan yar ja ce ba bak'a ba?"

Da yannayin jin haushi ta hankadata tana kallon kishiyar maman nasu da kuma kanwar tata dake gudu tana ihun sai ta halakata tana neman mabugi ta ja wani uban tsaki ta ce" Dan Allah mama kin ga ni ba wannan ne ya tsayar da ni ba, idan kin tuna tun da safe na gyara dakin nan aman shine dan rashin tarbiya yaren nan suka lalata kuma ba zan san waye ba dan na hukunta shi?"

Maman ta gyada kai tana kallonta ta ce" Ke yanzu banda jarabar tsafta me kika iya da har zaki tisa mutane a gana daga dawowarki ki shakar min yarinya ne, wai ko dai kin manta yadda aka haifeki da jinni a gidan nan haka na nakudo yar nan na haifi abina ko wani shegen ne ya rada maki a daki cewar kin fita iko da gidan ubanta? To ki shiga taitayinki, ki je ki ja tsuman rayuwarki ta kamaceceniya da namiji sannan ki iya da rashin lafiar dake damunki na haukan son dogari ki barmin yata ta wala son

ranta a gidan ubanta, waje ne idan kin yi niya ki gyara idan baki yi ba ki matsa abinda ke ajiye ki zauna ehe!"

Tana gama fada ta ja hannun yarta suka yi waje tare, uta kuwa ta kuma bin falon da kallo kafin ta girgiza kanta cike da takaici ta dauki jakarta ta nufi dakin mahaifiyarta

Tana zuwa ta tura kofar ta ja ta tsaya tana kallon maman nata du wannan hayaniyar barci take kashirban a irin wannan lokacin da aka yi salar la'asar aka gama har duhun magariba ya fara shiga

A hankali ta karasa bakin gadon ta tsaya a sanyaye ta shiga dan kiran sunnanta tana kallonta

A firgice ta farka suka yi ido hudu da yar, da sauri ta maida idannuwanta ta rufe tana girgiza kanta ta kuma budewa a kanta ta ce" kai subahannalahi wannan ido naku na gado ba dai abin tsoro ba, ke wai ban ce da ke ki ringa barina ina barcina idan ta kama ba yanzun da kika tasheni muka hada ido da ke da magagin barci yaya kike so na yi ne? Idanfa na firgita na zo ina mafarkinki kai ku dai kun dauki jinnin wahala walahi gashi tun kina jaririya nake kaiwa sarkin mayu ya duba min kar a je mayu ne ku ban sani ba aman amsar daya ce ku din ba mayi bane kuna dauke da baiwa ce idon mage ba kowa ke samu ba domin idon wanda ya fi kowa daraja ne a cikin masu daraja mafi kusancin Allah, to ama nakin nan ya girma da yawa ga wani shegen dogon hanci uwa zanen cartoon!"

Du cikin yannayin jin haushi ne ta fadi magangannun nan ga y'ar cikinta , wanda na so gannin mutuwar jiki da bacin rai a bayane a fuskar yarinyar, sai dai ga mamakina hankali kwonce ta ce" Abincina ne ban samu ba, gashi bani da cenji komai a jikina ki dan zuba min madara da garin cen na sha na kwaso yinwa yau mafarkin dogari na yi a aji."

Hannunta ta saka ta talabe habarta cike da mamakin yar tata, kafin ta girgiza kai ta ce" To a kan me zan baki garina bayan kin san ina ajiye da shi ne dan shegen koma bayan tayan ubanki na sai an gama raba abinci su dawo su cinye nasu kuma su cinye na mutane, ke dai bara in lalubo maki hamsin a cikin kudin da kika banin nan, ni an kwana biyuma baki bani komai ba Allah dai ya sa ba daina kula saurayin naki mai bamu kika yi ba dan haukan da ake kadawa cewar kina fama da shi?"

Wannan maganar ma sam bata wani d'ad'ata da kasa ba, saima kallonta da ta yi na maganarta ta karshe da ta sanyayar mata da gabai ta ce" Yanzun kema kallon mahaukaciyar kike min kennan oan maganar dogari? Ku dukanku zan baku mamaki ne a kan maganar dogari, sai na kawo dogari har gidan nan ya aureni mun koma kusa da sarki sai na ga mai k'yamata dan Allah."

Tana gama fad'a ta juya zata fita ta kuma juyowa tace "Kuma ma rik'e garinki, kuma shima mai banin zan kore shi yau tunda dai kema baki yarda cewar ni ba mahaukaciya bace ba, kuma kin ga insha Allahu karatun matuk'iyar jirgi sai na cinma burina koma menene ni da Allah na dogara."

Tana gama fad'a ta kuma juyawa ta yi tafiarta ranta a b'ace, hakan ya saka uwar rakata da kallo kafin ta yi hamma da mik'a tana girgiza kai tana d'an shafa dokin wuyanta da take ji ya d'an rik'e mata a bayane tace "In ba hauka ba ina kalar fatarki ina zama ko kalar shiga jirgi ne bale zama matuk'iyarsa? Kaf a afrikama mace nawa ce take tuka jirgi? Bayan wannan ko a karuwan jirgin nan ai babu bak'ak'e bale a d'auke ki , kawai b'ata lokaci nasarun da suka bud'a wannan makaranta sune yan

iska, ke dai kawai ki auri masu zuwar maki, suma na tabbata wannan k'irar taki ce ba wani abin ba, bari dai na mik'e na d'an watsa ko na jini garas."

_____

Tana shiga d'akin da yake mallakinta bayan ta bud'e da ky d'inta ta jefar da jakar makarantarta kafin ta cire hijab dinta ta k'arasa bakin katifarta ta zauna tana kallon waje d'aya.

Abinda take tunawa irin kayan da aka ce lalle lalle shi za suna sakawa gabanan dan fara d'aukan darasi na wa'inda suke da ra'ayin aiki irin nata, ita fa babar damuwarta shin oga dogari zai yarda ta yi aikin jirgi? A duniya burinta biyu ne auren dogari ne na farko sai ko kasancewa matuk'iyar jirgi, wannan buri ya shiga ranta ne daga ranar da ta ga farar banasariar dake matuk'iyar jirgi, daga ranar ta gama yankewa kanta hukuncin a duniya bata da wani aiki sama da shi, aman fa idan dogari ya yarda.

Kuma d'aga kanta ta yi tana duba 'yar k'aramar agogon d'akinta, yunwa take ji sosai fa, irin sosai d'in nan, gashi ba abinci
Dolema ta yi zance yau idan tana son kwana lafia ba tare da ana yak'i irin na sambisa a cikin tumbinta ba.

□□ my alkalami

A pages na gaba in sha Allah.....

WACECE ITA?

MEYE LABARINTA

SU WAYE DANGINTA?

WAYE MAHAIFINTA?

WAYE DOGARI?

MENENE TAKAMAIMAN MAFARKINTA?

.....RAI DA LAFIA DAI IN SHA ALLAH...

DAGA ALKALAMIN SAJIDA YAR MUTAN NIGER.
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)* □□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

DUTSE

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□ □ □ □ □

2 □□□

An haifeta a shekarar 1997 a jamhuriyar Niger
Ita din y'a ce ga Elhaji Yunusa mai sari da kuma Rukayatu. Ta taso cikin gida mai tarin y'aya domin mahaifiyarta nada kishiyoyi har uku kwarara da suka san da su

Ahalin gidan elhaji Yunusa wasu irin ahali ne masu wuyar kwatance, sun kasance sakaku, bodararu, mararsa kunya da tarbiya, lamarin ya kasance abin tsoro domin ko a tsakanin iyayen da y'ayan ba jin kai da soyaya da ja a jiki bale tsakanin yayun da kannan.

Gida ne ginane mai shegen kyau, gida ne da ya gina shi dan ya yagawa makota da makiyansa, ya dage ya faso gari ya yi ginnin kece raini ne dan kawai ya keta raini a anguwa da jama'ar gari.

Yawancin y'ayan Elhaj Yunusa sun kasance masu girman kai, fadim rai, jiji da kai ko dan suna gannin gidan da suke fitowa a ciki ne? Sam basu dauki halitarsu ta dan adam a matsayin kasa wace gobe ana iya wayar gari su tsinci kansu a nanage a cikin kabari
Rayuwa ta yanci ce ake yi a cikin gidan Elhaji Yunusa, ba abinda ya dame shi da biyan karatun yaro na islamiya ko na gwamnati, idan kana so kar ka yi karatunma ba abinda ya dame shi, sannan idan mace na so kar ta yi aure ta yi ta zamanta a gidan matsalarta ce da ta uwarta, shi dai ba zai kori kowa ba, ba kuma matsalar wani zata saka masa ciwon kai ba, shi din kansa yana rayuwa ce tamkar ta marar adini, shi ba mai zage zage bane, sannan ba mai daurewa yaro gindi bane, shi ba mai yiwa yaro nasiha ko fada bane haka zalika idan ya ga ka matsawa yaronsa yakan ce da kai wai ina dalili ka yi rayuwarka ka sakarwa yaronsa mara shima ya yi fitsari son ransa.

A takaice rayuwa ce marar tsari, a cikinta ta taso mace daya tak a cikin yayunta maza uku, yayun da sai su tashi basa yiwa junna magana bayan ba fada suka yi da junna ba, ba wanda ya damu da dan uwansa, ba wanda yake da ra'ayin damuwa da dan uwansa domin mahaifiyar tasu kanta da ta haife su bata nuna masu mahinmancin hakan ba, a wajenta ita kanta bata damuwa da wani a cikinsu sai idan yana anfanar mata wani abin, sam bata damu da lamarin wani ya kula wani a cikinsu ba, bata tunanin wannan din matsalarta ce, ita dai ta yi mai wuyar tunda ta haifa idan sun ga dama su yi zumunci idan sun kiya su kashe kansu matsalarsu ce!, domin ita a rayuwarta ko kokowar ajiye masu abinci gaskiya ba zata iya ba, wasu iyayen zuwa suke su dibarwa y'ayansu dan kar su dawo su rasa abincin, ita ta fada masu gaskiya idan sun zo da wuri su samu idan basu samu ba su nema su ci a waje itama ta kanta take bata son damuwa
A duniyarta wanda take iya zabura a kowani lokaci ta biya masa bukatarsa mijinta ne, gyara take yiwa kanta na mamaki wanda hakan ya sa shi din kansa baya dadewa bai je mata ba, wannan kawai ya isheta farin ciki domin bata rasa na kashewa in dai zai zo inda take.

Sai dai du iya gyaranta a banza ya tashi domin y'ar da ta haifa da cikinta ba abinda ta iya na fannin gyara, ko girki bata iya ba, abinda kawai ta iya a rayuwarta shine tsafta, bata gajiya da shara da wanke bayi da wanke tufafinta da abin shinfidarta, takan share falonsu a kowani lokaci hakan baya hanna daga ta gama shararta su lalata mata su dawo su yi ta masifa a tsakaninsu tamkar zasu cinye junna danye

MUNEERATH ta taso a cikin rayuwa mai duhu, tun Muneerath na da shekaru goma sha daya da ta taba cin sa'ar gannin irin hawan sarki ta dawo gida cike da bege da wani irin tunani, tashin farko ta sanar da mahaifiyarta magana kamar haka" Mama, na ga kwaliya, mama ina burin na auri sarki"

Sai dai amsar da ta samu ita ta saka gwuiwowinta da mafarkinta cenzawa nan take a lokacin da mahaifiyarta ta yi daria tana fadin" Ke mumunan namiji mai kudi kyawawan mata ke wawa, mace bak'a mai muni irinki ai sai dai ki dan lalaba da rokon Allah ko Allah zai sa a cikin bayin gidan wani ya ce yana so, idan kin taki sa'a Dogaro ya yaba kuma shikenan ko ba komai sunnanku yan kusa da sarki!"

Daga wannan rana ta ringa kokaron sannin shin wai wanenema shi *DOGARI* din nan?, meye kusancinsa da sarki? Shin akoy dogari a duniya? Domin sam batama san menene dogari din ba.

A hankali ta gane meye hakan kuma waye hakan, sannan ta ga haza cewar dogari yana da kusanci da sarki har ya taki mukamin rike lemarsa, hakan ya saka ta sauko daga burin da ta ci na sarki ta dawo dogari.

To abin ne yake ta hauhawa, a hankali lamarin yake neman yin kamari da wuce tunanin bawa, ta saka abin a ranta ta yadda ya zamo burinta na biyu a cikin gidan duniya, wanda na farkon kuwa mahaifinta da kansa ne ya yi mata daria kafin ya girgiza kansa ya barta nan tsaye a lokacin da take sanar masa burinta na karatun da take bayan ta kawo masa sakamakon makarantar gwamnatin da take wanda tunda ta shiga makaranta itace ke cin ta farko a kowace jarabawa ta dadage ta ce" *Pa*, da ka ga ina kokarin nan burina na biyu a duniya shine na zama *HOTTEST* "

Da matukar mamaki ya tambayeta " Hottest fa? Na jirgi? "

Cike da kwarin gwuiwa ta gyada kanta tana kallonsa

Idannuwanta dake da color blue mai duhu ya kala da kalar datar jikinta , Muneerath dai ba fara bace ko daya bata da hasken fata aman kuma ba bak'a bace lut, fatarta kalar fatar hausawa ce mai kyan gaske domin a fatarta babu wani waje fari wani waje bak'i, ta yi uniform ne gaba dayanta ta yadda take ba ko fararen sha'a, ba a nan abin yake ba, ba wai matsalar fatarta ba duda a yanzu an waye ba sai farare kawai ake dauka a matsayin hottest ba dan kuwa yanzun ana anfani harda bak'ar fatar da kuma yannayin tsarin halitar mutun da irin yaren da ya iya da iliminsa , sai dai halitar MUNEERATH halita ce da bawa ba zai fahinta ba sai a nan gaba, da ace ita din ta san me Allah ya tara mata a wajen duwawunta da ta ja wa'inda ke yawo da zariyar wando a hannu a kasa ba da komai ba sai da kada luntsuma luntsuman duwawunta da gaya, sai dai rashin sannin ya saka take rayuwarta a yadda ta zo mata
Kansa ya kada ya barta a nan tsaye ba tare da ya bata amsar burinta ba, haka kuma bai karfafa mata gwuiwa ba, sai kishiyar mahaifiyarta da ta gyada kai ta shige dakinta take sanarwa da d'anta cewa lale a yau ta kara yarda cewa MUNEERATH bata da hankali, domin kuwa a yanzu bayan mafarkin dogarin da take ta dawo burinta na kasancewa Hottest, in ba jaraba irin na yarinyar nan ba ina ta ga yannayi na Hottest? "

A haka ta ci gaba da tafiar da tata kalar rayuwar, karatu take ba ji ba gani, abin birgewar sai ka ji tana karatun alkur'ani, tamkar ba yar cikin wannan gida mai wuyar rayuwa ba

Da farko MUNEERATH bata kula samari, bata kula da ko dan gidan waye, daidaikun samarin da a yanzu suka ja suka tsaya suka rike nasu ra'ayin na ba zasu taba kula matan zamani da koda da farinmu muke kara bealiting ba bale bakak'en da muke zama farare dare daya dan lalacewar abokanan rayuwar da suka nuna su sai hasken gida, sai alkyabar mata ba, suka jajirce suka nuna mata kauna, da wa'inda suka gane wannan yarinya mota ce da za'a jima ana tukawa nan gaba, irin manyan motocin zamani masu tafe da bed, watau hutu ce, dunia ce guda suka lalabo dan gwada tasu sa'ar ko za'a dace sai dai ina haka ta ringa tizgawa duda rashin kwaliyarta, haka ta ringa nuna cewar lalala bata yi komai kyankya da kudinka! , sai da ta zauna ta yiwa kanta karatun ta nutsu a kan halayar mahaifiyarta da ta kula cewar eh lale uwarta ce ita ta kawota dunia, aman idan so take mu'amalarsu ta dore ya kasance tana da saurayi mai dan yi mata ihsani , hakan zai saka itama ta samu yanci da soyayar uwa irin na kowa, ba wai dan mamansu bata samu bane, aa, tana samu na mamaki a wajen abansu da yayansu, aman cewa take yaro tun yana yaro ya san ciwonta ya yi mata idan ta mutu ba shikenan ba? Ta more tun harshenta na gane dandanon magi da siga, a haka ta dage, ta mike tsaye, take kula samari daidaiku daga nesa kafin Dogari yake kawo kansa inda take, dan kuwa a soyayarta da dogari Allah kadai take fadawa , ba zata taba iya tarbar namiji ta ce da shi tana sonsa ba, ba wai dan ta san irin ilar da hakan zai iya haifar mata ba, aa, sai dan kawai ita bata ga anfanin aikata hakan ba!

A yanzu shekarun MUNEERATH goma sha takwas ta kawo matakin zana jarabawar dake iya bata damar ahiga University a maysayinta na wace ta bada hankalinta kai da fata take karatunta ya kasance a jarabawar uku sa ake yo har zuwa yanzu bata fadi a ko daya ba, haka kuma a ci gaba daga karamin aji zuwa na gaba da shi ba'a taba mayar da ita baya ba

BAC shine jarabawar da ta damka, wace ta zama mai wuyar samu, a yanzu da shugaban kasarmu ya tsaya tsayin daka ya rufe ido kan irin yadda wasu malaman makarantar da iyayen da son y'ayansu suka rufe masu ido suke mika dan abin ihsani ana tsalakar da y'ayansi, da samarin dake yiwa yan matansu, da mazan dake tsalake matayensu, da dangi, da sannin sanni du ya ture ya ja ya tsaya a kan kafafuwansa

ya kafa matalan tsaro ta yadda iliminki zai kwato maka, sai ta kara daura damarar karatu ba dare ba rana, idan suka je aji suka dauko karatun da malamai ke masu duda yawanci a irin shekarun nata yan mata kai na hayaki, ido na tsaitsaye, abinda suka fi hangowa shine show.....a je makarantar a ki yin karatun a hade da yan mata a restaurant a ci abinci a bige da selfi, a saka kida a sha casu, a ringa kule kulen samari ana abubuwa sai an zo shiga a haukace ana kame kame.....sam sam Muneerath bata kasance a cikin irin yan matan nan ba, wannan abin ya saka take da masu son kulata sosai, ko dan mutun ya karu da baiwar ilimin da Allah ya yi mata, ita din ba za'a kireta da mafadaciya ba domin bata fadan da ba dalili, idan ka ga fadanta tabata an tabata ne, wannan kuma takan ce a gaskiya ba zata iya kawar da kai a mayar da ita sakarai ba

.....back

Yinwar da take ji tun ta rana da ta riko daga makaranta ita ta ci gaba da rikewa har dare ya yi kafin ta cenza tufafin jikinta ta shanya wa'inda ta cire din bayan ta wanke su a bayin tsakiyar gidan ta zo ta dauki litafinta ta zauna ta dukufa ta shiga karatu tana jin juwa na son kadata a zaunen da take

Yayanta ne daya daga cikin yayunta mudaseer ya shigo har dakinta

Ido hudu suka yi kafin ya zauna saman yar kujerar dakin nata yana bin dakin da kallo ya ce"

Sajida ce
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)* □□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

  □□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

□□□□□□□

3 □□□

Ido hud'u suka yi kafin ya samu waje ya zauna saman kujerar d'akin nata yana bin d'akin da kallo kafin ya sauke idonsa a saman kanta ya ce "Kin tabata cewar ba shashancin mafarka mafarkan dogarin bane kila yi ya saka ki zama hottest? Kin kuwa san menene hatsarin aikin hottest? Kin yarda zaki iya d'aukan risk d'in kasaccewa Hottest?"

Littafin dake hannunta ta ajiye da sauri tana kallonsa a sanyaye ta buda bakinta mai dauke da fararan hakora tas tas da yar siririyar wushiryarta tana kallonsa ta ce" Aa, walahi ba dogari ya sakani ba, hasalima bana tunanin idan har dogari zai hanna ni wannan aiki domin aikin da nake mafarki ne, shi kuwa ai masoyina ne kau?"

Dan k'aramin tsaki ya ja yana karkacewa ya zaro wata takarda a aljihun wandonsa ya ajiye mata a nan kusan litafinta ya mike ya kama hanyar fita yana fadin" Ni na koma makarantata wannan jaraba ta Dogari Allah dai ya sa ba mahaukaciya bace ke ake zaune da ke kalau ana tunanin mai hankali ce!"

Yana fad'a har ya fice, ita dai da sauri ta saka hannunta ta d'auki takardun ta bude ta maida hankalinta ta zuba idannuwanta tana karantawa cikin nutsuwa, suna d'asawa da wannan yayan nata sama sama ba dan komai ba sai dan irin yadda take kaunar karatu, shi din kuwa a rayuwarsa mutun ne mai shegen son karatu hakan ya sa yake dan sauraronta shima ba wai cen cen din nan ba aa, yakan tsayawa ya ce anya ba ta yi gamo ba kuwa? Wani sa'in maganama yake daina yi mata kwata kwata aman da zarar ta kawo sakamakon makaranta sai su shirya, har taimaka mata yake da litatafai da sauransu, ko yanzun ta jima ta yi masa tambayar ta yaya zata iya samun damar kasancewa Hottest? Shine yau ya kawo mata information din da ta ji kamar gaba daya dukan mafarkanta ne zasu tsaya a iya wajen nan.

Na farko dai idan kana son kasancewa Hottest ba kai tsaye bane zaka zo da dukkan yannayin jikinka ka ce ka zo neman aikin.

Ya zama wajibi jikinka kar ya zama katon jiki kar kuma ya zama busashen jikin da ba za'a anfani komai da shi ba, kai dai kar ka wuce kl sittin da biyar haka kuma kar ka yi kasa da arba'in da biyar.

Na biyu kalar fatarka, basa daukan fatar da bata zamo daya baki dayanta ba, ina nufin idan baki ne kai ya kasamce bak'in nan naka mai kyau ne ta yadda baki daya jikinka bak'in ne kar ya zamo wani wajen fari wani wajen bak'i hakama idan fara ce ya zamo duka fari ne babu digo digon baki ko ja, ko ylw d'in fata.

Baban tashin hankalin shine bayan mutun ya yi Bachelor's degree ya samu, ya zama wajibi ya je ya yi shekara biyu na wani karatun domin ana son mai Bachelor's degree +2

Dole mutun sai ya iya yaren inglish ba lale a rubutu ba aman ya iya a harshensa idan da hali da wani yaren ko wasu yarukan.

Ya zama dole mutun ya iya Ruwa watau ace ya iya iyo.

Ya zama wajibi ka samu CCA watau CABINE CREW ATTESTATION.

Idan da san samu ne ka samu experience a harkar kasuwanci, watau kana iya karantar harkar Marketing □□□□□□□□□□

A hankali ta ajiye takardun tana jin wani salamamen ciwon kai na son salamo mata a irin wannan lokacin
Wacece ita? Waye babanta? Ko tace shin babanta ya san da zamanta? Mahaifiyarta kanta daria take yiwa furucinta, shin ko dai zata kare a mahaukaciyar ne? Ina zata shiga da baban burin nan dake cikin zuciyarta?

.....

Talatainin dare ne , a irin wannan lokacin da yawancin bayi ke baci wasun sunna bauta wa ubangijinsu, da yawan passinger dake cikin ROYAL AIR Plane na baban birnin LONDRE barci suke, kadan daga cikinsu ne suke farke suma sun kasance wa'inda basa iya barci idan sun tsinci kansu a cikin jirgi komai tsayin tafia.

Ya d'auko su daga DUBAI international airport, daga baban birnin Dubai tun karfe Shida na yama sun dauki tsayin awa takwas da minti hamsin da hudu kennan yana tuki ba tare da sun tsaya a wani garin ba cikin amincin Allah ya ringa rage gudu a lokacin da service na duban yannayin garin da zai iya sauka suka bashi tabacin yana iya sauka lafia domin babu gagarumin hadarin dake iya hadasa muguwar iskar dake iya kayar da jirgi ta hanyar hanna masa ganninsa ne ya samu ya yi ta zagaye a tsakanin Airport din Londres Heathrow har sai da ya samu confirmation din yana iya dira kafin ya koma daidai hanyar da zai dira saman doguwar kwaltar shafafiya mai haske wace ta dauki hasken wutacen dake zagaye
A hankali tayoyin jirgin suka fito daga maboyarsu suka yi wata dira jib mai nauyi kafin su falfala da gudun da tamkar ba zasu taba tsayawa ba.

Ba kowa a hanyar, ba wani a tsakar hanyar tun yana gudu sosai har ya dawo ya rage sosai kafin yake kara ragewa cikin nutsuwa ya idasa baban wajen da ya dace ya parker.

Zuwa yanzu motoci ne biyu a gaban jirgin dake nishi da masu jansu a ciki sunna sanye da cask a kunnayensu.

Cike da kulawa wanda ke tafia a hankali a tsakanin motocin cikin yaren turanci ya kuma maimaita tambaya ga matukin jirgin, sai dai still bai samu amsa ba hakan ya saka shi cike da yar damuwar jin shirunsa ya tabo cen manyan dake gaban computer sunna biye da dukan motsin jirgin ya sanar da su cewar matukin jirgin har yanzu bai basu amsa ba.

Amsar da aka bashi da sunnan wanda ke jan jirgin ya saka shi gyada kansa a hankali ya ci gaba da yi masa nuni yana ta jest da hannayensa da kafafuwansa da gudu gudunsa su kuwa masu tuka moyar suka zagaya gefe da gefe aman nesa da jirgin sosai sunna ta biye da dukan takunsa har suka karaso wajen da zai tsaya kafin ya samu ya tsaya a wajen tsayuwarsa.

Ya dauki yan mintuna kafin kofarsa ta bude, kamar da minti biyar mutane suka fara fitowa HOTTEST na tsaye a bakin hanya sunna masu barka da sauka da fatan hutar da gajiya lafia ta yaren Inglish sunna kara nunawa mutun hanya sannan wasunsu na kara duba wajen ajiyar kaya na cikin jirgi da waje zama idan wani bai manta wani abin nasa ba.

Sai bayan kowa ya gama fita sannan wasu yan sharsharun mata biyu suka sauko cikin shiga mai kyau duda ba shiga ce irin ta y'ayan musulmai ba aman dogayem wandunansu da rigunnansu basu dame su ta yadda zasu hanna su tafia ko su hanna su walawa ba.

Wani irin tukuki ne ya taso mata mai nauyi ya dane gaban kirjinta, a hankali ta lumshe idannuwanta cike da takaicin halayan *PRINCE*.

A hankali ta jingina da jikin doguwar farar motar dake nishi a parker, da sauri wasu tsala tsalan yan mata maratsa kiba masu shiga iri daya sket marar tsayi sosai da kuma fararan rigunna suka shiga bata kulawa ta musaman ta tambayarta ko zata koma ciki ne ta huta idan ta gaji da tsayuwar?

Kai kawai ta iya dan girgiza masu kafin ta ci gaba da hangen hanyar da yake iya fitowa.

A kala sun dauki minti arba'in a wajen nan tun sunna saka ran fitowarsa har aka bude mata ta koma ciki ta zauna tana sauke ajiyar zuciya tamkar wace ta yi tsere.

A nutse yake dano kansa kafin ya shiga hada tafiarsa sannan ya idasa bayana.

Ya rab, Barakhallah masha Allah, Lalle halita mai kyau akoyta a dunia, kuma du yadda marubuci ya kai da zuzuta kyau ba wai kowane ne ya zarce misali ba, waima da zaka karyata kyau din kai iya ina yawonka ya tsaya?, akoy halitu a duniya akoy kyawawa a duniya kuma ba lallene ka ce ka gama ganninka ba.

HANJA ABEDEEN PRINCE din babar kasar Ingla, wanda yake na farko a cikin su ashirin da hudu daga matan har mazan.
HANJA dogo ne ba irin tsayin da ya wuce musali ba, HANJA a fatar jikinsa idan akoy baki to yana wani wajen boye wajen da idannuwana ba zasu hango min ba, domin ko gashin kansa ba baki sidik bane no maroon yannayi yannayin pink haka.

Hanja nada kakarfan jikin da ba zaku fahimci inda na dosa ba sai mun kai ainahin wajen da ya samo yannayinsa, Sanye yake da sutura irin ta Pilots, Pilots dinma masu manyan matsayi, domin yana sanye fararan kayansu ne masu dauke da galoli a kasa da galalin an makala farin azurfar na karfe dake nuni da bayan matsayinsa na GENERAL yana daya daga cikin masu d'aukan ma'aikata a abinda ya shafi jirgin watau cikin jirgin ba wajensa ba.

A nutse yake tafia sai dai yannayin fuskarsa zai bak'a tsoron tunkararsa

Tunda ya fito ya sauko d'in suke gaishe shi, bai kula kowa ba sai da ya karasa kusan farar motar nan ya bud'e bayan ya saka k'afarsa ta dama ya zauna da kyau yana kwonce abin dake hannunsa a d'aure wanda ke nuni da yannayin bugun zuciyarsa da kuma zafin jikinsa ya ajiye sannan ya saka hannunsa na dama a hankali yana barbaza gashin kansa kafin ya dan saci kallonta sai kuma cen k'asan mak'oshi cikin yaren turanci ya ce" Ina take (Where is she)?"

Ajiyar zuciya ta sauke cike da tashin hankalin irin yadda ko a kwalar rigarsa kafin ta bud'i bakinta kamar wace zata balbaleshi da fad'a sai dai abin mamakin ta sanyayar da muryarta sosai ta k'ara tausasa kalamanta ta shiga fad'in "...

Masha'Allah
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*
□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

4 □□□

"Barka da sauka Londre"

Bai amsa gaisuwarta ba sai fitar da dayar kafar tasa ya yi ya fice a motar gaba dayansa

Da sauri ta raka shi da kallo tana kallonsa ta ga an bude wata bak'ar mota kirin da ita kirar kampannin Bintley Limozine

Bai kuma kallon kowa ba aka ja su a cikin motar tare da yan matan nan biyu da suka fito daga cikin jirgin

Wannan karron kasa rike abinda ke zuciyarta ta yi a hankali ta hade kanta da jikin kujerar bayan sun taso ita daya kwal a bayan sai masu tsaronta a gaba wasu a wasu motocin da gayar da suka zo dan tarbarsa sula juya palas ta hade kanta ta fashe da wani irin kuka mai cin zuciya tana girgiza kanta, sam bata san me ya dauki kansa ba aman ba komai zata je ga Sarki ta sanar masa komai shi ya isa da shi ai

Wani irin falelen plt
Wajen ba a wani zagaye yake ba sai shukoki da suka zagaye shi
Wani bangare guda daya ne tal mai dauke gls wajen kamar an yi shi a tsakiyar filin ne wanda yake da kofar shiga daya tal

Fitowa ya yi ko matan bai yiwa magana ba bale wanda ya tuko shi ya yi ciki cikin nutsuwa

Yar yatsarsa ya dora a kofar shigar wajen wani farin madubin da na yi tunanin na kallon kai ne, sai dai yana dorawa wajen ya bude bayan ya gama scanning ya gane mai wajen ne ya bashi damar shiga

Da sauri masu biye da shi din du suka shige sai iya masu escorted dinsan ne suka ja suka tsaitsaya sunna kara expect din place din

Dan ja ya yi ya tsaya a lokacin da ya ga yan matan nan biye suke da shi

A nutse ya juyo yana kallonsu sai da ya bale babar rigar dake saman jikinsa yana kallonsu da yar yatsarsa ya masu nuni mai hade da tambayar da suka gane ba tare da ya yi masu magana ba

Kallon kallo suka shiga yiwa junna su biyun, du da irin tarin jin haushin junna da suke ji aman basa taba bari su nuna a gabansa

A hankali dayar cikin sanyi ta dan daga kafarta da nufin karasawa inda yake tsaye muryarta na dan rawa ta ce" My Prince, ka gama da ni ne?"

Dayar kuwa bata matsa din ba aman kuma ta tsura masa ido tana karantarsa, domin ita din ta kasance baba yar manya kuma mai tarin ilimi, tana tare da shi ne dan nata manufar ba dan wani abin daban ba

A hankali ya motsa labansa cen kasa ya ce" Ku tafi ba zan yi fly ba "

Kallon junna suka kuma yi a lokacin da ya juya ya nufi babar kofar da zai fita gaba dayansa a falon nan

Murmushi ta yi ta juya ta nufi waje dayarma ta bita dan sun gama sannin tunda ya ce su tafi hakan na nufin ya gama morar ganga zai yarda kwalonta ne

Da dan sauri sauri ya karasa wakeken kejin, hankalinsa a tashe ya karasa wajen da take kwonce
Cike da tausayawa y kai gwuiwarsa kasa ya dora hannunsa a hankali yana shafata yana karawa kafin a sanyaye da yaren turanci ya ce" i'm sorry, yaya jikin ki?"

Da kyau na kara wara idannuwana cike da tsoro da kuma mamaki kafin na fala a guje gefe na labe sosai ina hangen ikon Allah
Wani dankareren kosashen ZAKI ne mai tarin gashi da yannayi na karfi mai dogayen hakora ya je ya rungumunma a irin wannan lokaci da ba dan haram bane mutun ya ci naman mutun ba da wasu sun yanka junnansu sun cinye dan halin rayuwa bale shi da ya zame masa wajibi kuma aikinsa kisa da cinyewa ya bi ya farauta ya dane ya cinye tas bale har an kawo masa a gida? Aman maimakun ya dane ya saka kan wannan bawan Allan da na kasa tantance balarabe ne ko jar fata ne ya masa danysa daya tak ya raba kashin wuyansa da dogon wuyansa da gangar jikinsa ya masa tauna daya ta yada kwala kwalan idannuwansa zasu bultso ya taune su tas ya hadiye kafin ya farwa sauran jikin ya dandantsa cikin nutsuwa ya yi karin safe da shi ya kora da ruwan dake ajiye, sai na ga ya dan jijiga daga inda yake ya mike tsaye kan kafafuwansa kafin ya shiga wani irin jijiga yana cira daga inda yake yana dora jibga jibgan hannayensa masu dauke da tarin gashi a wajen kafadun *HANJA* sannan

yana kawo bakinsa dake bude yana shafa masa uban gashin dake wuyansa yana ta karra goga masa

Sai a wannan lokacin na ga yana ta sakin murmushi kamar ya samu dan uwansa ya bashi kyakyawab runguma yana karra shafa shi a sanyaye ya ce" Nima na yi farin cikin ganninki, na damu da rashin lafiarki sosai, ina fatan yanzun da sauki my royal freind?"

Kamar wace take jin yarensa haka ta sake shi ta yi baya baya tana tafia cike da kasaita da karfi da jin kai da wata irin isa wace daga inda nake a labe nake jin takun a cikin kirjina haka kuma zuciata ke yin dak dak dak domin wannan zaki ko nace zakayar ba karama bace , tabas da ake cewa yannayin girman kashinsu da zakin kiwo na gidan zoo da na jeji sakaku ba daya bane sai yau na yarda, tsarin kwalin dake cikin idannuwansu kadai abin shagala da kallo ne, sai da ta yi nesa nesa kadan da shi kafin ta wani irin girgiza sannan ta durfafoshi a gujen da ya saka na nemi sakin mutumen daga tsaye, aradu ban taba yarda cewar akoy masu wasa da rayukansu ba sai yau, tsaye yake a gabanta jama'ar rasululahi (S.A.W), ba tsoro, ba firgici, ba alamun zai juya ya fita a guje, baya tsoron kar a je koda mugun sabo ne suka yi da junna a yanzu kwakwaluwarta ta juye tana isowa inda yake ta cire masa kai? Bama wannan ba shin jama'a dama Zaki abin sabo ne? Kai jama'a

Haka ta iso inda yake ta kuma neman dare shi, tagal tagal suka yi da sauri ya iya rike kansa da karfi yana murmushi ya kai hannunsa har kusa da bakinta hakan ya saka na kwalalo idannuwana ina kuma kallonsa kafin ya karra shafa gashinta sosai sannan ya saketa ya shiga tafia hankali kwomce tana gefensa itama tana tafiarta cike da kasaita har suka fito daga wajen da yake rufeta idan zai yi tafia
Wani wajen suka je ya tsaya ya kurawa wani tableau ido, ita kuwa ta shiga dan zagaye shi cike da kasaitarta
Habarsa ya dan dafe ya juyo inda take zagayen nata ya dan dafe kugunsa yana kallonta a hankalin nan dai kamar wanda yake yin rada dan baya so wani ya ji shi ya ce" Kin kyauta kennan? Kin rage cin abinci sosai dan baki da lafia ko? Idan nine kin iya zuwa kina son tayar da ni na ci ko? Zan rama ne"
Ajiyar zuciya ya dan sauke dan hutawa da doguwar maganar da ya yi kafin su ci gaba da tafia, da hannunsa ya ci gaba da nunawa ya ce" I'm tired, u see ko cofee ban sha ba tafia ta tsayin awa takwas dan ina tunaninki "

Ita dai Allah bai bata damar magana ba, aman wani ikon Allah idan ya fara magana har kamar mai dago kai ta kale shi kafin ta ci gaba da tafiarta
A haka suka karasa kusa da bayinsa, abin mamaki a lokacin da ya saka kafarsa ciki sai na ga ta shiga kai kawo a kofar maimakun ta bi shi

Wanka ya yi mai daukan lokaci kamar rana ce bayan yanzun lokacin sallar asuba ne ya gabato, hasken fitilun garin da gidan kansa sai ya saka bawa a cikin tunanin ko dai safia ta waye ne idan ba sama ya daga kansa ko ya kai dubansa waje da zai nuna masa cewar dare ne

Yana fitowa daure da tawul kadai a kugunsa ya nufi wajen da suturarsa take,
Iya gajeran wando ne ya saka kafin ya muke tsaye yana lumshe idannuwansa ya kai dubansa wajen agogon dakin dake kafe

Kuma lumshe idannuwansa ya yi ya dauko wata jalabiya fara ya saka kafin ya nufi wajen da yake kebance a cikin wannan tankamemen falon ya mayar da gabansa gabas ya tayar da sallah

Kwarai na yi mamakin ganninsa yana sallah, a irin wannan gari a yannayin halitarsa, irin shigarsa, irin yadda yan mata suka shige gidansa wa'inda na kasa gane mene dinsa ne, wace ya yiwa magana irin shigarta, kai lamarin da yawa, sai dai a irin yadda ya gabatar da ibadarsa ya tabatar min cewa idan ya tsinci kansa gaban mahalincinsa bashi da wani abin daban a gabansa sai shi, ya dukufa ya gabatar da sallarsa kafin ya yi adu'o'i sosai ya shafa ya kuma mikewa ya cire wannan jalabiyar ya mayar da ita wajenta
Ido nake rinrintsewa, kai shi haka yake ne? Wane Wardugu (Na cikin Bak'a ce) a kirar diraran jiki, ginanen jiki, mai sanka sanka, shin karfe yake dagawa ko menene?

Saman lalausar shinfidarsa ya haye a hankali ya lalubo commande biyu dayan fari dan karami dayan kuwa bak'i

Daga kwomcen da yake ya gyara kwonciyarsa da kyau ya kara gudun AC sannan ya danna na labule suka rufe kansu su dukansu kafin ya karra rike bargon nan a jikinsa yana lumshe idannuwansa kasan zuciyarsa yana adu'a dan samun barci cikin tsari da amincin Allah

Saman ta cira ta haye kusa da kafafuwansa ta kwonta saman lalausan bargon wutsiyarta cen gefe kanta ta kai ta shigemar da shi wajen kirjinta ta kwontar da kyau itama ta shiga neman barcin hankali kwonce

A kalla ya yi barcin kusan awa biyar kafin ya ringa jin yadda take ta goga masa gashin wuyanta da ta karra buda shi sosai tana ta son juyo da shi tana ta cinninsa kan dole sai ya tashi

Manyan idannuwansa ya dan buda da mayen barci da jan da suke dauke da shi ya juya a hankali a kasan makoshinsa kuwa cike yake da jin haushin yannayin jikinsa a cikin ransa fadin yake"Ya rab, yanzun kuma ina zan samu mace?"

Dan tsaki ya ja a dan bayane, ita kuwa zakayar nan sam ta ki ta barshi sai kara cinashi take kan sai ya tashi domin gari ya waye ita yinwa take ji, shima haka

Mikewa ya yi ya kuma nufar bayi dan yin wani wankan
Sai da ya kimtsa jikinsa tsaf sannan ya fito ya yi gaba tana biye da shi
Sai da suka zo wajen cin abincinsa ya zauna kanna ta juya ta shige gaban mai ciyar da ita suka fita suka yi bangaren cin abincin da manyan cinyoyi na manyan saniyoyi ke jiranta ta shiga dandatsa

Sai da ya ga tafiarta kafin ya mike da sauri da goran madarar nonon saniya da aka yi masa sabon tatsa aka tace shi sosai ya nufi PALAS watau baban GIDAN SARAUTAR dake ake kira da BUCKINGHAM

A nutse yake tafia bayan sun karaso doguwar tafiar yana duba time din sallah gannin da saura sosai sai kawai ya yi kwana ya karasa wajen da ya tabata ba zai rasa wace ta kawo kanta dan hakan ba

Yan mata uku ya tarar a bangarensa dake cikin gidan wanda yake malakinsa, wa'inda idan zai rantse ba zai yi kafara ba dayar a kadan ta yi sati a wajen tana jiransa, biyun ne dai bai san yaushe suka zo ba

Ido hudu suka yi da junna gaba dayansu kafin ya cire dubansa ya ja ya tsaya yana dan kare masu kallo a fakaice
Kai da ba dan abu daya ba da ya hadda su ukun nan ko kishirwarsa zata mutu, da yawan lokuta yakan ji haushin aikinsa ne ba dan komai ba sai dan irin jarabar nan

da suke fama da ita, shin ina dalili? Dan kawai kana Pilot kamar a kanka aka halici Jaraba?

Bai ce da su komai ba ya wuce ya shige baban dakin da a nan yake baje kolinsa da ire irensu, dakin da ko sallah baya yi a ciki

Umarni ya ba yaron dake biye da shi kan a shigo masa da daya a cikinsu sauran su tafi, dayar kuwa ya bada yannayinta domin Allah yana gani shi ko sunnanta bashi da shi

A lokacin da ta shigo a zaune yake bakin gadon, da idonsa yake biye da ita da kallo har ta gama tube dukan wani abu mai sunna sutura a jikinta kafin ta shiga jujuya jikinta tana son lalle sai ta birge shi har ya amsa gayatar da take masa

Idannuwansa ya lumshe, domin ya amsa, ya fa amsa a yanzun yana iya sukuwa har tsakiyar dare danma kar ya ce har gobe i warhaka ne ya yi karya?

Yana kokarin saka hannunsa dan ya janyota gaba dayanta jikinsa ya mata tashi daya ta yarda idan ya mata murza daya sai ta ji ba zata iya kaiwa gobe ba ya ji an turo kofar an shigo da yannayi kamar da dan bacin rai

Da sauri ta juya kafin da gudu ta fada saman gadon tana son janyo abu ta dan kare gabanta domin shi kadai ne abin rufewar a jikinta

Irin kallon da take binta da shi ya sakata jin kamar fitsari zai sako mata dan haka da gudu ta mike a yadda take din ta fice a dakin gaba daya

Kansa kasa yake kallo, bai iya dagowa ya kaleta ba, ba dan komai na sai dan ita din mai daraja ce a duniyarsa, kuma yana matukar jin kunyar ita da kanta ta kama shi a irin wannan hali, aman me yasa ta shigo kanta tsaye dakinsa da yanzun sunna harkar nan ta same su fa?

Muryarta a sanyaye ta ce" Khalb?"

Kansa ya kasa dagowa ya kaleta dan jin kunya
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)* □□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

  □□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

□□□□□□□

LABARINA NA: *10*

5 □□□

A hankali ta karasa inda yake zaune, lalausar alkyabar dake jikinta ta Veloor mai ruwan baki da duwatsu farare kal kal kal ce ta jata sosai a jikinta ta gyara ta zauna tana kara kallon lalausan gashin jikinsa kafin ta saka hannayenta ta janyo shi jikinta sosai ta dora kansa saman cinyarta

Gashin kansa take ta shafawa a hankali kafin ta ci gaba da fadin" Haramun ne aikata zina, Allah ya yi alkawarin azaba ga mazinaci idan bai tuna ya daina ba, ina matukar mamakin kasarku da ake yinta a bayane, harma gidanku gida mai daraja, shin baku da kyankyami ne?"

Idannuwansa dake lumshe kamar ba zai taba buda bakinsa ya yi magana ba da kyar ya iya budawar a sanyaye ya ce" Me na yi?"

Ajiyar zuciya ta sauke cike da kwarin gwuiwar son gannin ya cenza ya dawo mutun sak irin na kowa ta ce" Abinda na tarar da kai kana shirin yi"

Lebensa na kasa ya cije a hankali ya ce" Khalb, i'm sorry to say ts aman yaya zan yi ne? Aikina ne "

Muryarta still a nutse ta ce" Aikin da ba kowa ne yake sonka da shi ba? Wai yanzu du darajarka ka gwamace ka je ka yiwa wasu karti aiki? Kai fa Allah ya haliceka ne da darajarka , HANJA kana kwonce sai a yi maka komai, ka bar aikin nan ka yi aure ka dauki lamarin sarautar dake rataye a wuyanka"

Idannuwansa yake lumshewa ya mata shiru bai bata amsa ba hakan ya sa ta dora da fadin" Zina mugun aiki ce , mai cinye alkhairi, Zina na hanna sukuni tana saka bakin fuska komai hasken mutun, zina na bin dangi , idan ka yi da y'ar wani sai an yi da taka, idan da matar wani ne za'a yi da taka, aya ce, shin yaya zaka yi da ranka idan ka wayi gari ka ga ya faru da matarka?"

Still idannuwansa a lumshe suke cen kasan makoshinsa ya ce" Khalb, idan ta zabi bin wasu bayan gani ba shikenan ba ai yancinta ne sai ta je ta yi dan kanta"

A dan rikice ta ce" Baka da kishi ne? "

Kansa ya dago yana kallonta, a hankali ya saki dan lebensa da ya cije a sanyaye ya ce" Ta ina ake jinsa? Ni na kasa ganewa, kin ga fa kika ce idan na yi budurwar da nake so na ganta da wani nan dina za yana min zafi na ji kamar zan kama da wuta dan azaba, ai nan na zo na ce maki na kama su Rozario a hotel sunna hvng sex aman ni komai ban ji ba, da ta bani hakurima nu mantawa na yi sai dai na bara masu soyayarsu ita da shi dan na ga ya fini sonta ko? To wai ko dai ana haihuwar mutun ba kishi ne? KHALb ni ban ga abin damuwa a irin abin nan ba, abu ne na ra'ayi, ka yi da wace ya kama ka ji kana ra'ayin, kuma ni ban taba zuwa na kwata ba, su suke zuwa sunna rawar jiki su kawo min, sannan maganar aure ni yanzun idan na ce zan yi aure har ba zaki hanna ba? Kin fa san meye yake jira, jira yake na ce ai zan yi

aure ya nemi sakani a harkar sarautarsa, ba zan iya ba, na fada maku idan har na zauna to fa babu jirgi a duniya!"

Shirun da ta yi a hankali tana ta shafa gashin kansa dan ta ga ya fara caza ne ya saka shi kara komawa a hankali ya kara kwontar da kan nasa kafin ya ringa sauke ajiyar zuciya wata na korar wata har yana jin makogwaronsa na masa zafi dan maganar da ya zuba mata

Bata karaya ba a sanyaye ta ce" Sai na ji tsoro na kama min zuciya, sai na ji kamar zan fashe da kuka, ka kuwa san meye rashin kishi? Du namijin da baya kishin iyalinsa ba zai shiga aljana ba, Khalb me yake damunka ne? Ko dai a gaba ka san shi ainahin kishin kansa ne?

A hankali ya ce" Kamar yaya?"

Itama a hankalin ta ce" Ina nufin a gaba ka samu wace zaka yi kishinta "

Da dan murmushi ya dago gaba dayansa ya mike tsaye kafin ya dan rankwafo a hankali ya rike hannunta na dama ya manawa bayansa kisss a sanyaye ya ce" Na kula yau horon da kika yi niyar bani shine hadani da ciwon kai, zan he office now plz ki ce masa na yi tafia kin ji? "

Yana gama fada ya juya ya yi gaba ita kuwa ta raka shi da kallo kafin ta dan dafe habarta ta yi wani yannayi na tagumi a hankali ta ce" Ya Allah, ka karra jadada rahama ga abokiyar zamana mahaifiyar yaron nan, ka shiryar min da shi"

Mikewa ta yi ta gyara gadonsa da kanta ta dauke rigar da yarinyar ta cire tana girgiza kanta cike da jin tausayi da kuma haushin tarbiyar yarenmu, shin ina zamu je? Ta sani a wajenta wannan ba wani abu bane domin ba musulma bace ita yarinyar, aman duda haka shin ina akida?

Jikinta dai a sanyaye ta fito nan aka amshi abin hannunta ana rike da kayanta suka juya suka shiga watsetsiyar motar da ta kawota nan din suka kama hanyar baban bangarenta

A lokacin da ta fito bayan an bude mata ana ta gyara mata hanyar wucewarta suka yi ido hudu da kanwar tata

A kasan zuciyarta take ayana.....' Lalle ita kanta zata so gannin yarinyar da zara motsa zuciyar yaronta, wace kala ce bata kawo bukatarta da harinta ba, farar ce, yelow din ce, fararenma irin mai dau din nan ba wai sama sama ba, kai ba'a maganar kyan aman cikin ikon Allah cikin biyu ne ki zabi daya ko ku ga walen junna ko ki kama gabanki ba abinda ya dada shi da kas, shin wacece? A ina take? An halitota ko a gaba?.....'

.....

"Kwana biyun nan kina cikin yannayi na rashin karfin jiki Muneerath, me yake damunki ne dan Allah? Kin ki ki fada min gashi ana ganninki za'a gane cewar kina cikin damuwa, me yasa kike da zurfin ciki mai tsanani a gareni? Ko kamar yadda kika saba ce min ba zaki taba fada min abinda ya shafi cikin gidankun bane?" Amina ta karasa fadi tana kallon Muneerath

Murmushi mai ciwo Muneerath ta yi tana kallonta ta ce" Ba zaki gane bane Amina, ina cikin tsaka mai wuya, na tambayo nawa ake koyar da iya ruwa na garin nan an

ce du awa daya jaka uku, Amina idan na ce zan saka kaina a wannan sha'ani ai sai a yi tunanin ko na fara rashin jin magana ne, waye zai bani kudin nan? Ta ina zan samu na cika burina?"

Amina ta zauna kusa da ita itama jikin nata ya yi sanyi sosai da wannan lamari na kawar tata, dunia na fadar abubuwa a kan gidan nasu, ana fadar lamari marar dadi, fadi ake ko a wajen cin abinci kowa ta kansa yake yi, ana fada cewa komai na gidansu tamkar na mutanen da kowa ke ikon kansa, irin gidan yan barikin nan, gida ne da iyayen kansu basu da tarbiya bale y'ayan, aman ita sam bata yarda da wannan magangannun ba domin kawar tata ko kudi ta bata bata amsa, ko wajen cin abinci idan ta zo gidansu in sukai mata tayi bata ci kiri kiri take nuna ta ci a gida, bale a rayuwarta ta ki jinnin ta yi hirar gidansu, mugun zurfin cikinta baya iya barinta ta budi baki ta yi bayanin damuwarta, wani lokacin haka kawai zaka ga ta fashe da kuka mai tsanani idan an taru anai mata tambayar lafia? Sai ta ce mutuwa ta tuna, daga haka kuma waye zai ce wani abu? Mutuwa ai ta isa idan aka tunata a yi kuka ga mai tunanin makomarsa
A sanyaye ta ce" Me yasa irin naki ra'ayiyikan suka kasance masu tsauri ne? Me yasa idan Allah ya cida mu muka samu bac din nan mu je mu karanci fannin likitanci ko fannin koyarwa ko abubuwa da yawa gasunan wa'inda mun tabata koda iyayenmu basu da karfin talafa mana idan muna karatu a Niger zamu kai ga ci har mu zama wasu gobe? MUNEERATH ni bana hangowa mace musulma mai tunanin yin aure da haihuwa a kusa yin irin aikin nan, bama wannan ba ki duba fa ki gani ko a y'ayan masu kudin da suka samu damar shiga makarantar nan sai masu gagarumin ilimi da kuma tsari kamar an zana su, Muneerath ba raina halitar da Allah ya maki ko nasabarki na yi ba, ko daya matakan da ya dace a taka a hau a kai wajen da kike so din nan ne ya fi karfinmu nesa ba kusa ba, waye zai tsaya maki? Ta ina zaki samu shiga makarantar da ko ka shiga ba yana nufin ka samu bane aa yana nufin ka je ka sha gwagwarmaya ne idan da rabonka ka wuce idan babu kima ka bata shekaru ka dawo gida?"

Muneerah ta mike daga zaunen da take tana kade sket din dake jikinta mai ruwan blue budade da ta siya a wajen gumama ta ce" Amina, zan je na ci gaba da fadawa Allah, zai tsaya min, na tabata alkhairi ne domin du idan na yi sallah fada masa nake idan ba alkhairi bane ya cire min a raina, aman kasancewar kulun karuwa yake a cikin ran nawa inaga idan na zauna na zuba ido zan kasance cikin masu fada nan gaba ina karkata kai cewar a da fa burina shine na zamo hottest, idan akai min tambayar shin yaya aka yi ban zama ba, cike da mutuwar zuciya sai na tabatarwa wanda ya tambayenin cewa dan ya fi karfina banma kwatanta ba!, na fi son na fadi cewa ban zama bane dan haka Allah ya hukunta domin na gwada dukan damata Allah ne bai yi ba"

Cike da tausayi Amina ta rakata da kallo har ta yi gaba

Shigar Muneerah ba shiga bace ta y'ayan masu kudi, domin a jikinta riga ce bak'a ta gwonjo da blue din sket shima na gwonjo wa'inda ta siya da kudinta abinta, sai blue din mayafi tamkar matacin koko da ta yane kan nata da ita, sai jakar tata ta gado ta zuwa makaranta wace bata rabo da ita koda yaushe tana bayanta

A sanyaye take tafiarta a yauma domin bata da kuzari ko daya baki daya tunanin yarda zata fitowa matsalarta ta gama cike mata kwakwaluwarta,
Sam bata ji tsayuwar motarsa a gefenta ba sai kalmar Dogari da ta sakata juyowa tana kallonsa a sanyaye

Sani dake tsaye jikin motarsa, matashin saurayi mai jinni a jika mai nema da karfinsa dan kasuwa ne ginane sannan dan bayan layin su Muneerath ne, kuma a da

kawance suke na kud da kud da junnansu aman daga bakin lokacin da ya nuna shin zata iya aurensa? Ta nuna masa aa, ita kawancensu shine ya sa take kula shi ai ya san wa take so dan Allah kar ya kawo mata wannan maganar, shi kuwa Sani a duniyarsa yana son macen da bata bleating, irin rayuwar da Muneerath ke fuskanta a gidansu bai dame shi ba, ai lowani gida da nasu irin kwamacalar, gwara su ba a munafurce suke rayuwar ba, a bayane take ita cema bata son a yi maganar gidansu shima kuma ba dan tana karyata rayuwarsu ba, Muneerath ta masa gaba da baya da zata lamunce masa da ya je gidansu ya yi birgimar ko a aura masa ita ko ya fasa fita kasuwa, kasancewar shine ci da shan gidan baya tunanin zasu yi saken ya ajiye nema ah tam

Dan murmushi ta sakar masa a hankali ta karasa inda yake tsaye ta ce" Lah, Sanini ban ganka ba, daga ina haka? Ina yini ya kasuwa "

Murmushin ya mata shima yana fadin" Alh Muneerana, daga kasuwa nake zan koma gida nake kiran Munee, munee shiru sai da na ce ta Dogari, hop kina lafia yaya dogari?"

Dan sakai ta yi da bakinta kafin ta watsa hannunta a sanyaye ta ce" Nima ban san yaya yake ba "

Sani ya dan zarro ido ya ce" Ba dai har yanzu baku hade ba?"

Kanta ta dan sada cike da jin ciwo a zuciyarta , sai kuma ta watsar tana zagayawa gefen daya ta bude motar ta shige gaba tana fadin" Oya direban Munee karasani gida mana "

Daria ya yi cike da jin dadin da alamu zata dawo masa irin na da yarda suke zumuncinsu ba wani kwane kwane ya shiga motar yana fadin" Daga nan har wucin gari zan kai Muneerar dogari"

A lokacin da ta shiga gidansu dai yannayi ne irin na kulun, da alamu kuma tsohon gidan na nan dan kuwa yawancin zaman nan da suke na yama kowa a wajensa yana tsula mai gyara shi idan uban gidan na falon ne, ba wai dan su bashi waje ya huta ba fa suke haka, no iyayen kowane ke koro shi waje da dan cin hanci dan ya samu zama kusa sa ogan gidan ba dan tana ranar girkinsa ba, aa , dan kawai a samu na fafatawa a tashi a yi ta masifa har makota na samun jifan marfin kwano

Bata yiwa kowa magana ba, duda wasu cikin yayunta yan matan sunna kugin kiranta da *Ta Dogari* da sigar neman fada dan ta biye masu a yi masifa, aman sai ta share kowa abinta ta yi shigewarta ciki dan a yau so take su zanta da shi mai gidan, tana son su dan tatauna ko yayane

Da salamarta ta shiga a bakinta, sai dai abin haushin daga matan har mijin ido suka dago suka zuba mata an rasa mai amsa mata salamar da ta nemar masu amincin Allah ya tabata a gare su cikake

Bakinta ta dan yatsina tana kallonsu kafin ta karasa kanta tsaye ta shiga ta zauna a gabansu baki dayansu hakan ya sa suka yiwa junnansu kallon kallo ciki kuwa har abokan zaman majaifiyarta suka kamu da jin dadin ga ta inda zasu jata fada ya fado masu a banza

Ido hudu suka kuma yi da mahaifinta kafin ya dan yi murmushi yana kada kansa ya ce" Ruky, duba ki gane min kyankyasata, in ba dan ni kaina ina tsoron kwakwaluwar

muneerath ba ai da na ce na samu jari, kin san fa akoy mazan da dan sakarci su kawai bak'sr mace ta masu a rayuwa, wai har fadi suke su idan suka samu bak'a a wannan zamanin da bata shafe shafe ko nawa zasu batar dan ita basu da bakin cikin hakan, kuma fa manyan masu kudi fa, sai na yi mamaki sosai har na ringa tunanin su kuwa ko magaya ne basu da shi?"

Ya karashe yana dauko wayarsa lokacin da matarsa Ta budi bakinta irin da yannayin kisar nan ta ce" Shine ai boss abin ke damuna, ka ga yarinyar nan mace har mace, eh lale bakinta ya yi yawa sosai aman duba ka ga kafma a cikin yaren wa ya yi fitowar gashinta da kirarta?, aman ka ga a banza tunda ba zamu anfana da shi ba, y'a kamar wace aka zara a cikin taran?, duba ka ga tana tafe tana mafarkin dogari...." ta karashe tana kilkilewa da daria

Dayarma ta ce" Ni du ba wannan ba, du kyan bakin mutun ai ba abin yabawa bane da zaka yaba kyanta, kuma tun kyanta ai a banza tunda a bayane take Muneerath mahaukaciya ce"

Mahaifiyarta dake zaune cikin shiga ta atampa an mata wani shegen dinkin da ko y'ar a yanzu da wahala ta saka irin rigar nan haka ta fita da ita tana dan gyara farcenta tana kallon kowa tana girgiza kafarta daya dake saman dayar tana kallonsu bata ce kun ci kanku ba, domin ita a yau ta yi niyar sai ta caji oga ba zata kula ko wani shege ba

Zamanta ta gyara a sanyaye ta ce" Baba, dan Allah wajenka na zo ina son ganawa da kai"

Wayar da yake dannawa ya dakatar yana kallonta , sai kuma ya ce" Ba dai a kan maganar Dogari da kuma son zama Hottest bane? "

Sai da ta hadiyi yawu marar dadi da jin ciwon irin yadda suka dauketa kafin ta lumshe idannuwanta a hankali ta gyada kanta a lokacin da ta samu wata idea ta gyara zamanta ta ce" Ba su bane, ina so ne ka bani kudi ko yayane na nema na karra na je na shiga clob din da ake koya ruwa, ina son na iya ruwa"

Wannan karron mamanta ce ta ce "TO FAH" tana kallonta

Lishiyar mamanta ta fashe da daria tana fadin" Yau mun yi abin kanmu mun karra kankaro wulakanci mun samu buri na uku, sai yar Oga naki salon daban ne"

Muneerath da ta tsare shi da ido ba irin adu'ar da bata janyowa tana kallonsa tana tofe shi a kasan zuciyarta, ita bata iya karya ba da ta yi masa dan ya bata yan cenji, yana basu kudi fa ba baya basu ba matsalarsa ba zai yi asarar kudin makaranta ba a cewarsa dan ya tabata ba karatun zasu yi ba wai basu da takaici

Da daidaya ya ringa bin matan da kallo kafin ya ce" Ni ina mamakin matan gidan nan, yanzu da kuka tsatsaremu da y'ata ta kawo magana mai mahinmanci na farko a rayuwarta so kuke na zageta ko me? Kai ban taba gannin yan bakin ciki irinku ba, ai ni abin alfaharina ne a ce daya cikinsu ta iya ruwa, baki ga wani abokinmu da dansa ya iya ruwa ba yadda motsi kadan zai ce wane ya ciyo gasar kaza a gari kaza dan tsabar kwarewa, dama haushinsa nake ji idan yana irin maganar nan, aman yanzun nima zan faso zai ga rashin mutunci, Ke yar oga nawa ne kudin?"

Ba Muneerath ba harta mahaifiyarta sai da ta zarro ido bale kishiyoyinta

Da sauri ta sanar masa kudin na tsayin wata biyu har jikinta rawa yake lokaci daya mahaifiyarta ta ce" Aa oga gaskiya ba haka za'a yi ba, to ni nawa bukatar fa, na fada maka ina son kudi wayata ta fara samun matsala tun ranar nan ka ce na bari ranar aikina na faranta maka ka bani kuma yau ne ranar zaka wani bata kudi?"

Da sauri kishiyarta ta cafa da fadin" Ke bama wannan ba, a kan me zai bata kudin koyon wani ruwa na kaniya? Ai muma nakuda muka yi muka haifa sai ka zana na kowa ka bada dan ba wanda ta fi a gidan nan Walahi ko a yi tashin hankali!"

Murmushi ya yi ya mike ya soka wayarsa a aljihunsa ya kalli Muneerath ya ce" Sai ki san irin zaman da zaki yi da kowani shege a gidan nan, kina dai gani irin bakin cikin da suke maki, idan kika kware kika zama hamshakiya kika kula su inaga a nan zan tsine maki kowama ya huta!, bari in je in biya da kaina ki shirya gobe ki fara abinki yar oga!"

Yana gama fada ya yi waje, nan da suka juyo gaba dayansu kanta, ba wanda baya fadin abinda ya zo masa bakinsa cike da bakin ciki da jin haushinta tamkar zasu cinyeta danya
Ita kuwa gaba daya sai abin ya kara sace mata gwuiwa, mahaifinta ne wannan, ta zo masa da maganar da mai yiwuwa namiji ne zai koya matan, sannan ta yiwuwu su ki yarda da cewa zata yi da wando mai dan tsayi dan kare mutuncin kanta, aman bai wani dan tsaya dan binciken komai ba ya kada kai ya tafi, ga kuma mahaifiyarta na mata fada a kan dan me ta kawo bukatar kudi a lokacin da ita ta so kawo tata? To ta nemo mata cikon kudin wayarta ko ta ga iskanci
.....idannuwanta ta lumshe a lokacin da ta rufe dakinta ta fada saman gadonta a sanyaye ta furta "YA ALLAH"
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)* □□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

Da kyar ta iya samun barcin da take son samu, da wuri wuri ta farka ta fada wanka , a gagauce ta gama shiryawa cikin shiga ta wani zumbulelen hijab mai ruwan madara ta dauki byro da convocation dinta na shiga aji da takardar shedar yar kasa ce ita da dan sauran cenjin da ya rage mata a jakarta ta makaranta

Sauri take zubawa sosai domin a kafa take tafiar tana yi tana duba lokaci da kyar Allah ya taimaketa tana isowa ana ta kirate kirayen sunnate , harma an kirayi nata sunnan dan haka ta dakata a kofar ajin da zata gabatar da nata jarabawar sai da mai kiran ya gana kiran sunnan kowa sannan ya amshi convoction dinta ya duba sunnanta da number table dinta, gannin tana cikin wa'inda zasu shiga ya bata hanya ta shige

Tunda ta shiga ta kurawa waje daya ido , gaba daya hankalinta take son kwontarwa a zaunen nan da take dan ta samu gabatar da jarabawarta cikin nutsuwa hakan ya sa ta shiga tunanin abinda zai sakata farin ciki, a sanyaye ta afka begen abin bege, cikin nutsuwa ta kama salati a kasan zuciyarta idannuwanta lumshe, a hankali take begen daha, dan aminatu sayadi, d'a ga abdulahi, sidi baban kasum, ya abul Ibrahim, shi dai Abul fatimatu zaharau, a hankali take dan motsa bakinta har wata dake bayanta ta dan tabota

A hankali ta buda idannuwanta tana kallonta

A sanyaye matar mai dauke da tsohon ciki sosai ta ce da ita" Kanwata lafia? "

Kai ta gyada tana kallonta alamun eh lafia kalau

Matar ta yi murmushi itama bata kuma ce mata komai ba

Sunna haka aka fara shigowa sa takardun harabawar ,
Bayan malaman sun gama caje kowa da duba yannayin zama sun tabatar kowa na zaune a saman kujerarsa suka nuna masu camerar da aka saka dan su kula kowa ya yi aikinsa wannan rana bata kai ranar tsayuwa a gaban Allah ba aman itama kowa ya yi ta kansa ne, mulkin sabon shugaban kasarmu ya tsaya tsayin daka ya toshe dukan wata hanya ta sata a kasa komai kankantarta kuwa idan dubunka ta cika komai kusancinka da shi ba zai sasauta maka ba

Takardun da aka raraba masu suka dukufa karantawa, sun fara ne da FRAN □ AIS dukan seri din da shi suka fara ba A ba D ba C domin shine yaren da kowa ke anfani da shi dan magana a makaranta watau school , shine yaren da nasariya ta kawo mana

Tunda ta sada kanta kasa ta nutsu take rubutunta bata dago ba sai idan ta ji ta kage sosai take dan dagowa ta dan huta kadan sannan ta mayar da kan nata ta ci gaba da aikinta, lura da masu tsaron suka yi ita kanta bata damu da kallon wasu ba ya saka su yin cen ciki
Cikin ikon Allah ba ita ta tashi daga zaunen da ta yi ba ko da ta kare ta ci gaba da biyawa sai bayan awa uku da mintunna kafin ta mike a hankali ta kai ta ajiye ta saka hannu a wajen saka hannu sannan ta fice a class din

Tana fitowa ta nufi wajen masu siyar da abinci, dala arba'in ta bayar aka zuba mata dambu na dala talatin da biyar aka bata piyawata na biyar

Cikin nutsuwa ta samu wajen zama ta kebe ta karya ta kora da ruwa, bata nemi komawa gida ba a nan ta zauna har ta shiga aji ta yi na yamma kafin ra kama hanyarta a kafarta ta koma gidansu

.....

A ranakun nan da aka yi na jarabawa kwana biyar cif matar nan na hankalice da irin hankali da nutsuwar Muneerath, kasancewar ba wanda ya santa a ajin hakan ya sa lamarin dogari bai bayana ba har aka gama jarabawar lafia sannan suka je gida zaman jiran result

A tsakanin ranar da jarabawar zata fito ta rasa gane kanta ita kanta, ta matsa da adu'a da tashin tsakiyar dare kamar yadda malaminsu ya basu adu'o'i tana fadawa Allah kan ya sa da rabonta a wannan jarabawa, kokari take, burinta ta wayi gari ta ga ta fado cikin masu sa'ar samun cin wannan jarabawa hakan ya sa take wuni da azumi sannan ta rike kafarta domin daga ita har kawar tata hankalinsu ba a waje daya yake a kwonce ba tunanin result ya saka su sun zama wasu shiru shiru da su sam basa iya anfanarwa kowa da komai bale kansu

A yau kwana hudu kennan da gama exam dinsu kuma a yau suke tsaitsaye cirko cirko gaban manyan makarantar da suka zo daga wani garin dan gabatar da jarabawar sunna jiran jin sakamakonsu

Idan ka dubi fuskar kowa a birkice take da tarin tsoro, ba mace ba namiji, ba mai kannanun shekarun ba datijo, sannan yawancinsu sun zo da masu rakiyarsu ne wasun iyayensu ne , wasun yayunsu ne, da wuya dai ka ga mutun shi daya kwal a irin wannan lokacin sai Muneerath kawai dake tsaye kafafuwanta na yi mata rawa
A cikin zuciyarta maganar da ta rubuta ta shanye take maimaitawa kanta, kin ga Muneerath idan baki samu ba ba komai, haka Allah ya yi, kuma Dogari ba sai kina da BAC zai soki ba, kin ga muneerath ki kwontar da hankalinki burinki na son kasancewa HOTTEST ba dole a tashi daya zaki iya zama ba, idan kika jure a gabama sai ki ga an dace

A hankali ta lumshe idannuwanta a lokacin da suka yi ido hudu da yayanta, tsayen yake shima kuma ya kurawa waje daya ido shima sakamakon yake jiran ji, 'Ko wa ya zo dubama?' Ta tambayi kanta a kasan zuciyarta sai kuma ta cire dubanta ta maida wajen masu fadin sakamakon a lokacin da suka fara bayanin sakamakon ta hanyar fadin adadin da suka fado Ecrit, da oral, da kuma adadin da basu samu ba
A kashi dari 37% gaba daya suka samu , sauran nan sai dai su sake wata shekarar
Nan fa ciki ya duri ruwa, iyayen yara da y'ayansu du suka shiga kama sunnan Allah, harta kiristocin sun rintse ido sunna tasu sallar

"Wanda ya zo na farkon Centre, ya samu wannan kwali tare da mention TRES BIEN shine *ABDUL KARIM MUNEERATH*"
Baban Jurry din ya fada wanda yake ba'adare ne, sai da ya fada ya dan saurari na kusa da shi da abinda yake fada masa kafin ya cenza maganar tasa cewa "TA MACE TA" (MACE CE DA YAREN ADARANCI), "TA Mace TA"

A tsayen da take zata rantse da Allah a yau bata gane sunnanta ba, BAC jarabawa ce mai matukar wahala a kasar Niger, idan yaronka na yi kai hankalinka a tashe nasa a tashe, burinka ya samu jarabawar koda ita kadai dinta ne, ko a scnd grup ya fado akan yi maka barka bale idan ya fado a na farko, uwa uba ta zamana kaf school din ta dauke makin kowa, sai ita kanta ta kasa gaskatawa a lokacin da ake fada har ana maimaita sunnan a tsayen da take ta kasa wani motsin kirki bale ta iya gane da ita ake

Da wani irin ihu ihu yayanta ya girgizata yana fadin" Ke muneerath kina ji kuwa? Kin samu fa"

Idannuwanta da sukai mata nauyi ta lumshe da dukan karfinta ta bude a kansa, da kyar ta budi bakinta ta ce" Da gask....."

Bata idasa fada ba ta tafi luuuuuuuuuuuuuu gaba dayanta zata jirkice kasa aka kakamata aka riketa cikin yan kamatan harda mai cikin nan kafin sojojin dake tsaye suka karaso suka amsheta suka nufi asibiti da ita da yayan nata domin sunna wajen ne dama dan hanna fada da dauke masu sume sume da matsar da masu ihun kuka
Mai cikin nan ce ta mikawa yayan Muneerath wata yar farar takarda ta ce da shi" Dan Allah ka bata ta taboni idan ta ji sauki "

Shi dai amsa ya yi ya soke a aljihunsa ya shige wuleliyar motarsu suka yi asibitin yana cike da jin dadin abinda ta samun, daga ball yake ya ce bara dai ya tsaya ya ga in da gaske karatun take, a rayuwarsa yana son karantun boko kamar me, shi yasa yake dan shiri da ita a gidansu, ba wani uwarsu daya ba uba ne kawai daya aman shi ba ruwansa ko wanda basu hada komai da shi ba idan ya ga mai ra'ayin karatu ne sukan dinke abinsu sunna shiri sosai

Sunna isa aka amsheta bayan sun yi bayanin komai suka so ya bada number iyayensu, budar bakinsa sai ya nuna marainiya ce shi kadai ya rage mata, ba dan komai ba sai dan ya san idan ya bada din ba wanda zai zo ciki kuwa har mamanta domin shi kansa shaida ne ya sha jin sunna shewar wai ita ce ke yin bac ko wa zai bata? Dan haka sai ya ki badawa kawai ya zauna da ita aka shigar da ita wajen mararsa lafia dan a bata taimakon gagawa kasancewar asibitin gwamnati ce aka kawota

..... .

Zaune suke su su uku, likitoci ne manya domin su dukansu doctarori ne, tataunawarsu ne suke cikin hira da raha kamar aminan junna , aiki suke sunna shiri tsakaninsu, kasancewar babu emergency ya sa suke zaunensu sunna hirarsu hankali kwonce

Macen dake zaune itama doctern ce mai sunna Halima ta ce" To yanzu Moise kai ka yi hakurin ka aureta mana, kar ka ce dan ta kiya da farko yanzu ta dawo zaka kiya kaima"

Moise din ya yi daria, da ganninsa Bashi da adinnin musulunci a tare da shi, bakinsa ya buda ya ce" Kya ji ki da wani lalatacen magana nan niya, ji ke an ce da ke ni din Doguwa ta min baki na da zan yarda mu koma da wancen makirar yarinya? Ni ai ba dan shagiya bana bale na yarda, ta je ta amri wanda taka so lumui nima na samo tawa lumui na amre abina mu yi zamanmu, ke ni nan da kika ganeni bana kara yarda da waral matata, zan samo bak'ata mu jesu zuwa mu yi amrenmu dan na gane wararen tunaninsu halitar na aljana aka zuba masu suke daga kawuna da su"
Ba'adare kennan, cikin hausarsa ta adarawa (*Ki ji wani banzan zance a nan wajen, an ce da ke Doguwa ta min baki ne da zan yarda mu koma soyaya da wancen makirar yarinyar? (DOGUWAR WATA ALJANARSU CE A CEN GARIN DOGON DUTSI), ni ai ba dan shegiya bane bale na yarda, ta je ta auri wanda take so lafia kalau, nima na samu tawa lafia kalau na aure abata mu yi zamanmu, ke ni nan da kika gan ni ba zan kuma yarda da farar mace ba, zan samo bak'ata mu je mu yi aurenmu dan na fahimvi fararan fatar nan tunaninsu halitar matan Aljanna aka zuba wajen hakitarsu shi yasa suke girman kai*)

Dayan likitan namijin ne ya yi daria yana girgiza kai ya ce" Kai Moise to meye dan ta dawo? Kai ba musulunci bama ka zubar ka dauki Christanci ai bamu ce mun fasa zama da kai ba ko?"

Zai bashi amsa nurse din dake gadi ta nemi izini ta shigo, cikin ladabi ta sanar masu an kawo wata da ta suma a wajen fadin sakamakon jarabawar da aka gama

MOISE ne ya dubeta da kulawa kasancewar shine babansu ya ce" kya ji balaki bata samu ba ko?"

Da ladabinta ta ce" Aa itacema premiere du centre, emotion din ne ya sumar da ita, a yanzu dai mun yi mata dukan abinda ya dace dan gannin ta farfado harma ta farfado din , kudin treatments ne muke son sannin a asusun gwamnati ko mu ba yayanta ordonance?"

Kallon junna suka yi, haka kawai Moise ya ji yana son zuwa ya ga Premiere du centre din da ta sume dan tsabar jin dadi ko me? Yana son ya ga irin farin cikin da iyayenta suke yi a irin wannan lokacin, yana so ya ga irin nata farin cikin itama, dan haka ya mike yana gyara rigarsa ya ce da sauran yana zuwa sannan ya fito a office din suka raka shi da kallo

Ajiyar zuciya Halimar ta sauke tana dan girgiza kanta
Dayan abokin aikin nata ne ya dan rage muryarsa ya ce" Har yanzu sonsa kike ko?"

Da sauri ta kale shi kafin ta dan girgiza kanta a sanyaye ta ce" Wani irin so kake so na yiwa mutumen da ya yi gagawar sakin adininsa dan kawai ya tsinci kansa a cikin hali na damuwa? Ka duba ka gani Musa daga fadawa halin kangin rayuwa mutanen nan suka ribance shi ya zama kirista shi kadai a familly dinsu, a da fa mahaifinsa baya amsa gaisuwarsa har ya dawo yake amsawa, shin baya tsoron mutuwa ta masa zuwan da bai shiryawa ba? Ko baya tunanin shiryuwa ? Ko har cen kasan zuciyar Musa ya gama zubar da adinin gaskiya adinin musulunci ya dauki na kafurci ne?"

Shima ajiyar zuciyar ya sauke ya dauki byro ya shiga rubutu a baban kundunsu , tabas abin nan ya matukar girgiza su, basu taba tunanin wahala zata saka mutun ya bar adininsa ya fada wani ba a lokacin da yan wani adinin suka nuna masa idan ya shiga nasu adinin zai ji saukin wahalar dake damunsa, bale Musa nasu, Musan nan ba'adare ne gaba da baya, haifafen garin dogon dutsi ne, Musa akoy mutunci da faran faran shi yasa komawarsa dan yesu yake masu ciwo a zukatansu

Tunda ya shigo ya ja ya tsaya yana kallonta
A yanzu zumbulelen hijab din da ta zumbula baya jikinta yana ajiye saman gadon sai wata riga marar nauyi aman ba gajera ba a jikinta wace ta siyi abinta a gwonjo, rigar mai ruwan orange ce da dan baki baki kadan a jikinta, tana da kyau sosai rigar bata da dogon hannu gajeru ne aman kuma ba sirara ba
A zaunen da take hawaye take wani na korar wani ta rike hannun dan uwanta gagam
Cike da shashakar kukan ta ce" Ka gani kau? Inaga fa Aurena da Dogari zai tabata , ka ga na samu BAC yanzun sauran koyon girki, koyon ruwa, koyon allura da zama Hottest, daga nan Dogarina zai zo inda nake, ka ga ni ba mahaukaciya bace ko"

Da mamaki yayan nata take kallonta kafin ya dan janye hannunsa ya ce" Ke tunda kin warware tashi mu je gida, ko in da hali ki ga likitan mahaukata kafin mu bar nan din, ke yanzu ina hadin samun Bac dinki da wani aljaninki wai shi dogari? Kai in ba dan ba da na ce Dogarin nan naki ya ci ....."

Da sauri ta mike daga zaunen da take a saman gado ta kai hannunta ta rufe masa baki ranta ya soma baci , yannayi na tsiwar da ra watsar kwana da kwanaki ya dawo sabo fil a saman fuskarta ta ce"

A sha weekend lafia
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)* □□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

7 □□□

Muryarta na fitar da amo marar dadi, sai dai ba zagi ba munanan kalamai, a yannayin maganarta zaka gane ciwon maganarsa take ji har kasan zuciyarta ta ce" Yanzu tsakani da Allah me na yi maka kuma? Du ka tsalake ka rasa wa zaka zaga sai mijin mutun? Ka ji tsoron Allah idan kana abubuwanka, shi dogarin me ya daka

maka ne yo? Ka ga bana son tashin hankali a yau dan haka ka je kai da Allahnka ko ba dogari ba zaka zo neman Alfarmar a hadaka da sarki kiri kiri na kiya"

Galala yake kallonta haka shima doctern, gaba daya rigar dake jikinta ya zubawa ido da wannan tsari na halitarta, dankari makari wannan kayan nasa ne, kuma zasu zama nasa, shi Moise ya wayi gari da wannan kaya? Ai wannan yarinya ko yar waye ko meye take takama da shi zai jure ko su waye samarinta zai kasa su ya riketa tasa shi kadai ya more iya morewarsa

Murmushi ya yi a lokacin da ta juyo suka yi ido hudu bayan yayanta ya mata wani irin riko da yannayin fushi fushi ya ce" Ke, cika ni "

Ido ta kikifta tana kallonsa
Da hargagi ya ce" in baki cikani ba na wanka maki mari sai sun kara dana maki kirji zaki farka a wajen wannan!

Yawu ta hadiye ta sake shi tana kallonsa cike da jin haushinsa, kai in ba dan tana tsoron ya nanata da kasa ba da ta tirje masa, da mace ce yar uwarta ta zagar mata dogari sai ta fyala mata mari ko wacece

Wucewa ya yi fuuuu yana fadansa a bayane yana fadin" Na gama yarda baki da hankali, ba dogari ba dai jar rigama ta ci....." ya kuma auna ashar din abinsa

A sanyaye ta dauki hijab dinta ta saka, Moise ya gyara tsayuwarsa yana gyara rigarsa ya dauki takardarta yana dubawa, cike da tausayi da son ya fara share fage ya kaleta ya ce" Aya Allah jikansu "

Turus ta yi tana kallonsa kafin ta dan tsaya gannin docter din ne ta ce" Su wa fa? "

Karra kallonta ya yi da kyau irin wushiryar bakinta ta matukar birge shi ya ce" Su iyayen namu "

A yanzun kam ya kara dulmiyar da ita hakan ya sakata gyara tsayuwarta ta ce" Iyayen su? "

Shima sai ya fara jin kamar kalaman bakinsa zasu kubce masa ta hanyar rasa me zai fada, da dan sauri ya ce" Ke ba marainiya bace?"

Bakinta ta dan tabe kafin ta girgiza kanta a hankali ta ce" Basu mutu ba "

Kwarai ya ji mamakin gannin an saka bayanin cewa marainiya ce, hakan ya sa ya kalli Nurse din da jiran karrin bayani

Itama har tana inda inda ta ce" Yayanki ne ya ce shi yayanki ne iyayenku sun rasu"

Muneerah ta girgiza kanta ta ce" To ni dai a fitowata daga gida da ransu ban sanba ko yanzun suka mutu, bara na je na gani"

Kallon junna suka yi Moise da Nurse din suka kuma kaleta, ba komai ya basu mamaki sai irin maganar kamar ta daketa kamar bata daketa ba, domin da farko wani dan turus ta yi , sai dai amsar da ta bada kamar bata shaku da iyayen ba ko kamar idan sun mutun ba zata damu ba?
Nurse din dai juyawa ta yi ta fita dan a yadda ta ga Moise na ta magana da sanyi da lalami ta tabata da abinda yake so, dan haka ta basu waje

A sanyaye ya ce" Ki yi hakuri kin ji? Kamar ranki ya bace"

Wannan karron ita din ce mamakin hakurin da ya bata ya kamata, wannan fa docter ne, a asibitin gwamnati ba na kudi ba, yake rarashin patient?, kowa ya san wasu likitocin yadda suke da gwagira da kwasar marar lafia bale a irin asibiti irin namu yaku bayi, lalamatan da yake ya sakata tsayawa da kyau tana fuskantarsa , a sanyayen itama ta ce" Ka yi hakuri dan Allah "

Murmushi ya saki yana kallonta ya ce" Kina da kyau sosai Muneerath ko?, ina tayamu murnar samun Bac "

Hannun da ya miko mata dan su gaisa irin yana tayara murnan nan ta bi da kallo aman ta kasa bashi hannun sai murmushi da ta masa da kuma nanata "MU" din da ya yi anfani da shi a karro na biyu kennan dan zai yi maganar da ta shafeta

Da dan sauri ya ce" Sunna na Moise Ibrahim Mustapha, Docter ne ni ina aiki a nan da kuma manyan clinik din dake cikin gari, na jima ina aikin na samu abin hannuna daidai misali, bani da aure, kuma bani da budurwa bani da yaro ko yarinya bani da wace na ajiye a gida muke zaman Conquivinage (Zaman da christoci, ko mararsa adinin musulunci ke yi da budurwarsu kamar matarsu, ta masu girki su zo su ci su yi mu'amalar aure da ita harma su hayayafa, wasun sai sun tsufama suke yin auren wasun kuwa sai an hayayafan kuma a dawo a watse kowa ya kama gabansa dama ba aure aka daura ba) da ita ba"

Kwarai ta yi kokari da bata ce da shi ba' Ni kuwa ina ruwana' , aman kuma irin kallon da take masa ba sai ta fadi cewar ina ruwan nata ba shi da kansa ya fahimci cewar abinda yake fada bai dameta ba dan haka ya gyara tsayuwarsa kamar a gaban sarakuwarsa yana jin nauyinta sosai ya ce" Ko zan iya samun number wayarki?"

Wannan karron tsakaninta da Allah ta ce" Wani abin na yi ne? Idan kudin maganin ne dan Allah ka min alfarmar na je gida na samo na kawo maka, idan babanmu na nan zai bani na kawo maka ka ji? Yanzu so nake na je na ga aminiyara ta samu? Na tabata itama tana nemana ne"

Dan matsowa ya yi kusa da ita sosai hakan ya sa ta dan matsa tana kallonsa da kuma kallon gadon wada ke kwoncen mace ce kuri kuwa su take kallo marar lafia ce

Cike da kwarewa wajen sace zuciyar yan mata ya dadafe abinsa ya fitar da dukan iliminsa ta wannan fannin ya gyara tsayuwarsa da kyau danfa ta gane namiji ne a gabanta ya ce" Ba abinda kika yi, ko kin yi kina tunanin akoy wanda ya isa ya tanka ki a gabana ne? Ina so ne dan ina son kiran ki domin ina son sannin ina ne gidanku dan kin min"

Sakalau ta yi da bakinta cike da mamaki, gana shirin kankance ido ta zuba masa hauka daidai da cinikin nasa haukan Amina ta shigo da sauri cike da farin ciki

Hannun Muneerath ta damka da sauri ta jata wahe sai da suka fito tsakiyar asibitin suka kwala ihun murna suka aniyar dane junna

Da kuka kuka Muneerath ke fadin" Kema kin samu ko? Wayo Allahna dadi kema kin samu? Alhamdulilah "

Amina kanta hawaye take na farin ciki tana fadin" Kece kika lashe kowa wayo kawata ra zama Cele, baki ga yadda ake nemanki a maki tambayoyi ba, kina da damar zuwa ki amshi kyaututukanki zo mu je harda kudi fa "

Farin ciki ya hannata musa mata da gudu suka fice kamar ba ita bace aka kawo a talabe , da sauri Moise ya laluba ky din motarsa shima da gudun ya fita a emergency din ya nufi motarsa yana waiwayen lambar adaidata sahun da suka shiga ya tayar ya bi bayansu, ya fa yi niya ya ga mata , shi kam ya yi mata.....

..... *□□□□ R □* .....

a saman keken motsa jiki yake yana ta motsawa da wani irin sauri ga wani irin zufa dake tsatsafowa daga jikinsa ta kowani lungu

Bashi da riga a jikinsa hakan ya sa du idan ya dan daga daga zaunen dan kara gudun tukin nasa sai gaba daya manyan damatsunnansa sun wani irin bayana jibga jibga da su da yannayi na karfi kafin ya mayar da su,
Fatar jikinsa ta yi ja duda sanyin da dakin motsa jikin yake da shi sakamakon yin da yake tun karfinsa kai da fata yana ta hada zufa
Sai da agogon ya yi karra kafin ya dakatar da motsa jikin da yake
Wata dira dira ya yi daga saman abin ya nufi tawul ya dauka yana goge jikinsa ya yi cikin dakinsa

Ruwa ya sakarwa kansa daga tsayen da yake a cikin bayi ya dauro tawul a kugunsa ya fito

A gaban wawakeken mirror dinsa ya ja ya tsaya a lokacin da ya dauko turaran ruwa marar karfi mai sansanyan kanshi yana dan shafawa a lungu da sako na jikinsa kuma idonsa na dan kallon bayanta a lokacin da ta juya ta idasa cire dan pant din da ya rage mata

Idannuwansa ya lumshe yana tunanin 'to ita wannan haka kirjinta yake ba mamora ga wasu duwawa kasa kasa kamar na kura?'

Karasowa ta yi inda yake tsaye cike da zumudin son ta fara taba jikinsa ta shiga shafa shi a sanyaye tana kara shafar kirjinsa

Bai hannata ba sai dan dakatawa da ya yi dan yana so kwarai ya sauke kafin ya dauki doguwar hanyar nan
Hannunta ya damka lokaci daya ya yi kasa kasa da ita, daga tsayen da yake kikam ya wara kafafuwansa kafin ya cire tawul din dake kugunsa ya yar
Idannuwanta ta zarro haka nima na juyo a guje na bar wahen cike da mamakin wannan dan ta'adan □□

Sosai ya daki abin anfaninta, sosai ya kwakuleta har sai da ta kai da sana'arta yana son kureta, ita dai wannan din sana'arta ce, kuma ko a kampaninsu sun yarda da kwarewarta da juriyarta, da tsaftarta, da iya haukata mazanta, sai gata ta yi wuri wuri ta amshi kaya a lokacin dake son ture kaya a lokacin kaya ke karra lume mata, har sai da ta ji gaba da baya tana neman sumewa ta yi narai narai ta nemi ajiye aiki gaba daya

Sai da ya jijigata iya jijigawa kafin ya cire ya juye zufar tasa a saman tawul din da ya cire idannuwansa a rintse

A lokacin da ya tashi dan komawa bayi ya tsaftace jikinsa ya tuna cewar Mamansa zata zo fa, dan haka ya dubeta irin yadda take ta maida numfashi wai kuma a nan kwarariyar ce ya dan girgiza kansa kamar wanda zai yiwa kashi magana ya ce" Ki tafi "

Daga haka ya juya ya yi bayi yana dan lumshe idannuwansa

A dan gagauce ya yi wanka na sabulu ya dora da na tsarki kafin ya fito

Da dan sauri ya shiga shiryawa cikin shigarsa ta GENERAL DIREBAN JIRGI □□, farar riga mai dogon hannu ya saka a ciki kafin ya fito da dayar a hannunsa ya ga bata falonma ya idasa fita cen baban falonsa a ransa yana tunanin yaronsa ya salameta ta tafin

Yana fitowa ya ga mamansa, Matar da ta raine shi, matar da ta saka shi a adini mai sanyayar da zuciyar, matar da mahaifinsa ya aura a wara tafia da ya yi aiki saudiya, wace ta kasance jinni ce ga gidan sarautar SAUDIYA, mata mai daraja, mai hakuri, mai kawar da kai, wace ta fada masa cewa mahaifiyarsa ta karbi kalmatu shahada a lokacin da ta haife shi take kan gadon asibiti kafin ta yi kaura wahen da ba'a dawowa, ita din dai mai hakuri da munanan halayansa wace ta iya zama da shi a kowani yannayi na halin dan adam , wannan dayar tak da ya rantse a kanta yana iya yin komai kuma ya jure komai watau *ALEESA* idannuwansa suka sauka a kan fuskarta, tana sanye ne da abaya fara kal ta dafe nikaf dinta saman kanta, ita daya yake gani duda a gefenta yar zumunta ce dake kwana tana tashi da shi a zuciyarta ta dauki wanka bayan kyan da gareta ta haske wajen ga kanshi tana bazawa sai dai kasancewar ba a kanta ya fara gannin kyau din ba kuma zata nuna masa haske waje ba kai gaba dayama hankalinsa ya raja'a ne a kan babarsa da yake yiwa murmushi yana kuma karantar fuskarta da fatan Allah ya sa bata ga wace ta fita yanzu a dakin nasa ba

Murmushi ta fadada fuskarta tana kallonsa kafin ta dan mike tsaye ta wara hannayenta ta kamo nasa da suka girme nata sosai da girman da tsayin a sanyaye ta ce" Khalb, zan je"

Murmushi ya sakar mata yana kallon fuskarta muryarsa cen ciki ya ce"
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

Muryarsa cen ciki ya ce" Mam, ba zan jima ba fa "

Kamar wata mai kannanun shekaru ta make kafadarta tana dan jujuya kanta zata yi magana daya daga cikin masu kula da gidan nasa ta zo ta ja ta tsaya kanta kasa cike da ladabi ta ce" Mai kula da Tigre ya ce ya fito da ita ne ko ya barta?"

Bai juyo inda take tsayen ba, gaba daya hankalinsa a kan datijuwar dake gabansa mai cike da annurin fuska, kamar ba zai yi magana ba cen kasa da yaren turancin ya ce" Ku bamu waje "

Yana fada mai aikin ta fara ficewa kafin kyakyawar budurwar nan ta mike tana kallon fuskarsa ta yi murmushi ta fice ta tsaya jikin kofar ta jingina tana lumshe idannuwanta

Ita dinma sai da ta ga du sun fice ta ringa dan matsa hannunsa ta shiga fadin" ALLAH shi ya haliceka, ya baka damar numfashi, ya ara maka daula dan ka sarafata ta hanyar da ta dace, Yarona baban tashin hankalin babu inda bawa zai shiga ya labe kida a tandun kwali ne bazai boyewa mahalicinsa abinda yake aikatawa a aikace da wanda yake cikin zuciyarsa ba, Khalb shin baka tsoron haduwarka da Allah?"

Idannuwansa ya lumshe a sanyaye ya dora gefen fuskarsa a hannunta, bayan hannunta, cen ciki ya ce" Ina jin kunyar mahalincina, ina jin tsoron haduwata da shi, Mam, ko ni dan wuta ne shi yasa na kasa rabuwa da aikata alfasha? Kin ga Jirgi zan hau na ja na tsayin awa bakwai ban san yaya zata kaya da ni ba a cikin tafiata , aman sai na zabi aikata zina kafin na shiga.....na tsani wannan halaya nawa, kuma ina matukar jin tsoron kar a je ko dan wuta ne ni, ko Allah ba zai yafe min ba, ko ba zan shiryu ba?"

Da sauri take dan girgiza kanta a sanyaye ta ce" Abinda Allah baya so shine bawa na neman yafiya kuma yana kara dulmiya "

Idannuwansa da suke da launin ja ya dora a saman kanta ya ce" Shi yasa ai nake jin kunyar na kuma zuwa da kokon barata da neman yafiyata"

"Gaban wanda ya haliceka? HANJA wanda ya ce da kai rokeni ni kuwa zan baka? Shi din shi kadai ya isa ya shiryar da bawansa, HANJA ina so ka ringa kokarin hanna kanka aikata zinar na tabata zaka fasa zan wayi gari HANJA dina ya fasa wannan mumunan aikin? Da na fi kowa farin cikin haka domin zina bashi ce My Son" ta karasa fada cike da yannayi na rarashi tana kara fuskantarsa

Idannuwansa ya lumshe yana sauke ajiyar zuciya, dama ya san du saurinsa a kadan mamansa na daukan minti arba'in tana nasiha shi yasa yake gagawa dan kar ya shiga lokacinta kafin ya tafi, a nutse ya ce" Ta yaya? "

Bata gajiya ba ko yanzun , ba zata taba gajiyawa da maimaita masa ba hakan ya sa yanzunma ta bashi amsa cike da fatan samun nasara ta ce" Ta hanyar yin aure, ta hanyar kyamatar taba wata macen da ba taka ba, ta hanyar kwadaituwa da son samun ladan aikatawa idan da igiyar aure a kanka"

Murmushi ya yi ya tsurawa fuskarta ido, yakan ji baban muradin son budar bakinsa ya kaleta ya ce da ita' Ta yaya zan iya auren wace ta gama rabawa? Ba dan ina jin

zan ji haushin hakan ba, a tunanina da tunanin samawa y'ayana uwa mai mutunci wace zata basu tarbiya, tabas a zamanin nan da ya kazamce ko a garin da musulmai suka fi yawa ana aikata alfasha, bale garin INGLA, bai san ta yaya zai kwatanta mata cewar a tsarin rayuwarsa bai tsara tara mace sama da daya tak ba, domin sunna da yawan tafiye tafiyen da suke yi da matayensu, baya son ya zamana yana yawo da wannan yau gobe da wancen, kai bama zai iya wai wani tsayawa shirmen mata ba, tsakani da Allah ko mace ya aura idan tana bashi ciwon kai zai saketa ya dauki wata dan ba zai iya wahala ba, babar damuwar ita ce shin wacece zata iya da shi?, wacece zata iya hakuri da lalurarsa? Shi ya san wannan abin lalura ce, wada sai wace ta jajirce, ta jure, ta zama jarababiya fiye da shi zata iya da shi, ba wai shi kadai ba haka yannayinsu ke dawowa koda kuwa halitarka yar karama ce'

Ajiyar zuciya ya kuma saukewa a sanyaye ya ce" Ki ci gaba da yi min adu'a, Allah ya bani wace zata iya zama da ni"

Murmushi ta yi har cikin ranta, ta tabata sannu sannu bata hanna zuwa, a da ba nasiha ba ko kuka ta masa zai fada mata kiri kiri cewar bai shiryawa hakan ba ba zai yi ba, yau har ya ce ta masa adu'a kuma ya nuna mata shima yana son dainawa? Ita kuwa zata yi ta yi masa da dukan karfinta da lokacinta zata fadawa danginsu su kama mata sosai a yi ta masa adu'a a saudiya

Mikewa ya yi da hannunta a cikin nasa suka nufi hanyar wajen da Zakanyarsa ke ajiye

Da sauri ta ja ta tsaya tana turo bakinta , shi kuwa ya yi murmushi ya shige ciki abinsa kasa kasa ya ce" Na sha fada maki ba zata iya yi maki ila ba, domin tana anfani da bugun zuciyata ne, ba zata iya ilata abinda yake saka zuciyata gudu ba komai kankantarsa"

Ita dai kin binsa ta yi daga tsayen da take tana kallonsa du irin motsin da zasu yi shi da zakanyar sai ta ji tsoro, irin yadda yake yiwa zakanyar murmushi kuwa sai abin ya birgeta sosai, idan ta dan daga bakinta hakoranta suka fito a kusa da kansa kuwa sai ta ji kamar gudun jinninta zai tsaya da sauri ta rintse ido da rufe baki, sai kuma ta ga sun kara gaisawa, a kadan ya dauki minti ashirin a wajen nan bayan ya gama gaisawa da ita ya kuma kara gargadin mai kula da ita kan tsaftar wajen kwonciyarta, abincinta, lafiyarta, ya shaida masa cewa ko yatsarta ke ciwo a sanar masa kafin ya fito

Rakiya suka yi masa har airport kamar wanda zai yi tafiar kwanaki masu yawa, a lokacin da ya fitar da ita daga babar motar ma'aikatar da ya sakata ya rakota har kusa da mitar masarautarsu bayan an bude ya kamata ta shiga ta zauna da kyau sannan ya shiga ya zauna yana mata murmushin da kowa ke son gannin yana yinsa ba dan komai ba sai dan shi din ba ma'abocin yin murmushi bane
Hannunta ya rike kamar yadda suka saba, a yanzun kuma bai kori yaringar ba ta kuma zuba maasu ido tana kallonsu

A sanyaye ta ce" Yau kwana goma sha daya baka je ka gaishe da mahaifinka ba, ba zaka daina yin fushi da shi ba ko?"

Kansa ya sada, bai bata amsar wannan maganar ba ya dago hannunta na dama ya dora saman kansa a hankali ya ce" Ki min adu'a"

Ajiyar zuciya ta sauke ta shiga jero masa adu'o'in tsari idannuwansa lumshe hakama nata, har sai da ata gama sannan ta dago habarsa tana kallonsa ta ce" *yarona DUTSE ne, DUTSE AJIYAR ALLAH KA FI KARFIN GARA, DUTSE A DAKA A BARI*, in

sha Allahu rabih zaka je lafia ka dawo lafia, kar ka manta mutun bai haliceka ba ba abinda ya isa ya yi maka, aman Allahn da ya haliceka yana kallonka a dukan motsinka"

Murmushi ya yi ya manawa bayan hannunta kiss sannan ya fita

Yana nan tsaye har motocinsu suka wuce kafin ya saki ajiyar zuciya ya juya lokaci daya masu tsaronsa suka mara masa baya

Bai zame ko'ina ba sai tankamemen ofice dinsa, saman kujera ya zauna likitar dake sanye da shiga ta likitoci ta shiga auna shi , kama daga zafin jikinsa, matsalar ciwon ciki, matsalar ciwon kai, matsakar kafa ko hannaye, irin yannayin mood dinsa, komai da komai sai da suka tabatar normal ne kafin ya mike ya yi dakin da kayan aikinsu suke

Cikin nutsuwa ya dauki yar karamar bindiga bak'a ya kara dubata ya duba alburushinta da securit dinta kafin ya soketa a jikinsa ta baya ya rufeta ta yarda idan ba sannin akoyta a jikinsa ka yi ba ba zaka taba tunanin akoyta ba, sauran galarsa da ba zai iya shiga gari da su ba ya ciro ya sakala ya dauki dan abin kunnen ya saka sannan ya fito
Yana fitowa ya ga HOTTEST din a laye kowace ta kama kanta ta nutsu irin nutsuwar da baka son a ga laifinka ko a kamata da wani laifin dake iya janyowa a koreka, HANJA mai gidansu ne, kuma duda kasancewarsa mutun mai harkar mata ba dai na wajen aikinsa ba, ya kasance mutunmen da ko magana bata hada shi da su idan har ba dile ta kama ba, sunna iya yin doguwar tafia sosai su dawo komai bai hada su ba ciki har gaisuwa domin ba amsawa zai yi ba
A yanzunma a tare suka gaishe shi cike da ladabi da biyaya ta yada ba zasu rasa aiyukansu a wannan baban kampanin da kaf fadin duniya suke son kasancewa ma'aikata a karkashinsa domin kampani ne mai biyan albashi mai tsoka ga mutunta ma'aikata

Bai amsa su ba daga tsayen da yake fuskarsa tamkar an ce da shi babarsa(□□) ya kara gimtsewa sosai ya ce" A cikin tafiyarmu du wace ta yi wasa da oasinger a bakin aikinta, du wace ta ga abin fada irin ta ga alamun miyagun kwaya ta rufe ko ta amshi cin hanci da gangan sai na rufeta!, du wace ta yi prostitution a tafiarmu hukunci zai hau kanta domin HOTESTE ba karuwa bace!, ba yar amsar cin hanci bace!, ba kuma shagaltaciya! INA FATAN KUN FAHIMTA?" Ya karashe maganarsa sama sama kamar wanda yake bawa sojoji horo a filin daga,
Dama sun san hali hakan ya sa gaba dayansu suka amsa masa cike da nutsuwa

A haka ya amshi litafin da aka rubuta irin shirin da suka yi, irin turaran da zasu yi anfani da shi ba mai karfi ba dan kar su takurawa pasinger, irin tsaftar da ta dace da su har dawowarsu ya mikawa banasariar dake jira ta amsa da sauri ta ja gabansu du suka yi cen ciki suka shiga dogon coridor din nan ya kaisu wajen da zasu yi yar tafia kafin su isa inda jirgin da zai tashi nan da minti arba'in suka shiga

Shima ya gama daidaita komai sannan ya tafi ya shige wajensa ya rufe ya shiga kara duduba komai na jirgin cikin nutsuwa dan tafiar ta shi kadai ne, watau matukin shi kadai ne kasancewar tafiar ba mai daukan lokaci da yawa bace kuma idan an je sai an kwana za'a juyo zai huta iya hutun da yake so

.....MUNEERATH
11/14/21, 12:43 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE

□□□

dubu naki ba zai daga mana hankalo ba, kin san ai yadda ake koyawar kika nace a haka kike son koya"

Ranta ya fara baci fa da irin magangannunsa, ya kuwa san ko ita wacece? Mace ce ita mai daraja da nan gaba kadan ko ganninta sai an dage, to ka zama matar Dogari ai ganninka sai an dage, aman shine yake son ta banzatar da jikin da Allah ya ce ra rufe? Mtsssss uban kuturuma ya yi kadan alkur'an!

Juyawa ta yi ta koma ta dauki doguwar rigarta ta shige wajen saka kayansu, ta saka dogon wandon na ciki sannan ta dora abayarta ta yane kanta ta fito

Yana tsaye ta ganshi har ta tsargu ko dai lekata ya yi?, tsayawa ta yi a gabansa ta ce" Na dubu ka gani, ba na Muneerath ba, in sha Allahu na muneerath ko a gawarta ne ya fi karfin ganninka na hakura!"

Da mamaki yake kallonta, saboda saka kayan ne ta hakura? Da yawa a wajen nan har fata suke a ce su tube su shiga ruwa nan zasu tube da rawar jiki su fada a guje su yi ruwa iya ruwa a hakan suke mamatse y'ayan mutane wa'inda suka nuna jin dadin hakan kuwa shikenan sun kula alaka da shi

"WAI ba kece Oga ya rubuta ba?, ko ba yarsa bace har da zaki ringa wasu abubuwan Oga fa namu ne" ya fada da wani sigar da kamar wanda yake son nuna mata tsohontama na aikin hakan ya kara tunzurata ta ja wani uban tsaki ta kai dubanta wajen ruwan ta kare masa kallo shi dinma, itafa bata son abinda zai taba lafiyarta sannan idan ta tura shi suka fada ruwan tare itace gajiyaya koma a ce marigayiya dan bata tunanin wani zai ceceta daga shan ruwan nan sai dai a jefo banza a wuce wajen

Kanta ta gyada ta kara kallon kamaninsa, ta yi alkawarin idan ta auri Dogari sai ta kawo masa matsalar wajen nan an dauki mataki a kansa da kan wajen baki daya munafukan Allah kawai

Juyawarta ta yi ta ringa tafiyarta shi kuwa harda wani fito fito yana kallonta har ta bacewa ganninsa da jakarta a bayanta zuciyarta na mata tukiki

Tafia take cike da tunanin yanzun yaya kuma zata yi? Ina zata je? Me zata yi? Yaya ta yarda bacin rai ya sakata barin wajen da zata fara taka mataki dan samun cikar burinta ? Anya tana tunanin sakamakon bacin rai kuwa?

A kafarta take tafe kamar yadda ta saba, ita din ba ma'abociyar kwaliya bace, Muneerath ko kwali bata da shi a dakinta ba zaka taba ganninta da shi ba bale maganar kayan kwaliya, idan ta ga fuskar mace da hoda sai ta ji fuskarta na mata nauyi kamar ita aka shafawa sai ta hau mamakin ta yaya suke iya jure zama da irin wannan abin a fuskarsu haka

Doguwar tafiya ta yi a irin wannan lokacin har ta wuce kostan din bakin KANYA
A nutse ta juya ta shige wajen tankamemen tafkin dake wajen, wanda ke buso iska sansanya yana zagaye da shukoki cikinsa kuwa kainuwa ta masa yabanya

A hankali ta ringa kallon ruwan, gayanan ruwan Allah wanda ido ba zai hangi karshensa ba
Yamyamyan jikinta ke mata a hankali ta zauna ta hade hannayenta tana ta adu'a tana kallon yadda ruwan ke kai kawo

Wannan ruwa shine baban ruwan da du shekara sai ya ci mutun mut har lahira, ruwan ya kasance mai karfin gaske da idan ka san kai din ba kwararan wanda ya iya ruwa bane kar ka rabe shi, mutanenmu na gida ke shigarsa su din kasancewar yayan gado ne

A kadan ta dauki minti goma tana kallon ruwan ita kadai tana murmushi dan gannin motsin kifaye kasancewar damuna ta wuce ruwa ya taru kifaye na fitowa su wataya abinsu ta ko'ina

Wani irin alamu na baban motsi ne ya sakata jin gabanta ya fadi, a hankali ta kurawa wajen da ta tabata ko kifi ne ba fa karamin kifi ba tana kallonsa

A hankali take dan kokarin tashi dan ta tsorata da alamun nan kar a he kada ne ya cinyeta a huta

Dan saurayi ne ya fito yana ta kilkila daria yana waige waige ya ce" Na rigayeki, yihu yau na rigayeki kuma gata nan tsakuwar na daukota ta cen kasa tsakanin dutse hudu na yamacin kudu da kusurwar gabai!"

Shiru ya yi sakamakon ido hudun da suka yi da Muneerath da gaba daya jikinta je rawa shima yana kallonta

A hankali ya ce" Baki ga Zeinab ba? "

Muneerath ta matse kafafuwanta sakamakon jin fitsari zai sauko mata, yau ta ga ikon Allah yau ta yi mumunar fitowa, ita ba jaraba gareta ba yau gaba ga aljani kuma har ya ganta shima yana mata magana, da sauri ta duka ta hade hannayenta ta ce" Idan kai musulmi ne ka yiwa Allah ka rufa min asiri kar ka ilatani, ina matukar kaunar koyon ruwa dan ina da buri na karatu a rayuwata shine na zo nan yau ashe da rabon ma hade ni da jinsinku, ka yi hakuri idan lokacin wasanku ne na zo ni kaina ban san bani da hankali ba sai yau, in ba karshen kwana ba me zai kawo mutun nan shi kadai? Ka yafe min ba dan hakina ba"

Daria ce ke son ciyo shi aman ya ringa rikewa sa dukan kokarinsa

Zainab dake dayan gefen da basu ga fitowarta bane itama ta bushe da dariar har tana rike cikinta

Da sauri suka kai dubansu ga budurwar da zata yi sa'ar saurayin, da sauri ya ce" Ke Zainab ki yi shiru kar a jiki kin san fa an hanna shiga ruwan kar sojojin cen su jimu su kama mu, waima ke Bingel ta ina kika shigo nan?"
Ya jefawa Muneerath tambayar da ta kasa bashi amsa ita dai ta kale shi ta kuma kalli Wace yake kira da Zainab, gannin ta rufe bakinta da sauri tana zarro ido ya saka Muneerath yin sakalau da sanyayar murya ta ce" Aya zainab ku mutanene hala? "

Zainab ta karaso kusa da ita tana daria kasa kasa ta zauna kusa da ita ta ce" Mu mutane ne bana, ni da shi tagwaye ne a nan muke wanka kulun aman idan sahu ya dauke dan an hanna shiga wai kar ruwa ya tafi da mutane, yo in ba yan birni ba mu nan ruwa wani iri ne bama shiga? Ai idan aka hanna mana shiga ruwa an kashe mu, mahaifinmu fa shine sarkin ruwa, yakan yi awa daya a kasan ruwa tun muna jarirai ake saka mu ruwa fa"

Muneerath ta sauke ajiyar zuciya tana murmushi tana gannin yadda saurayin yake dan zagayawa abinsa yana kallonsu sunna hirar kafin ya ce" Taso ki zo ki gani "

Muneerath ta ki tashi tana kallonsa cike da tsoron girman ruwan

Zainab ta ce" Idan kina so sai mu koya maki walahi "

Muneerath na kallonta ta ce" Tsoro nake, kin ga zurfi ne da shi fa, kuma idan ya tafi da ni fa?"

Murmushi Zainab ta mata ta kama jakarta ta amsa ta ajiye nan ta ce" ki cire hijab dinki ki daure iya kanki da shi, ki cire wannan diguwar rigar dan kar ta bace ki rasa wace zaki shiga gari da ita ko kija da wasu a cikin jakar?"

Muneerath cike da mamaki ta ce" Dama ina iya shiga da wannan kayan basu yi nauyi ba?"

Kai zainab ta girgiza ta mike tsaye, jikinta sket ne kasansa da dogon wando aman sket din mai budewa sosai ta juya ta kara juyawa tana wara kafafuwanta ta ce" da sket din da zai hanna kafafuwanki yin taku taya biyu a second daya ne ba zaki iya iyo ba, aman idan kayanki a bude suke komai gimansu zaki iya yin iyo dinki hankali kwonce, tsoro kuma ki cire a ranki na cire maki kadara idan hukuncin Allah ne ruwa zai ci ki ba yadda muka iya, aman idan ba karshenki ruwa bane ba abinda zai maki"

Cike da jin dadin hakan Muneerath ta ajiye jakarta, ta nade gashin kanta da dan kwalin sannan ta bi bayan zainab

A hankali Zainab ta riketa da kyau suka fara shiga ruwan da ta ji sulbi na kwasarta zai dimata da kasa da sauri ta yi niyar ririke zainab sai dai ina Sakinta zainab ta yi ta dimu a kas din kanta ya fara yin salama cikin ruwan ta kuwa shaka ta sha ta hancinta hakan ya sa ta gigice sosai zata fara harbe harbe ta ji an rikota an fito da kanta sosai, tuni dan kwalin ya fece abinsa a nan asirin gashin da take rufewa ya budu ya jike ya yi lub abinsa

A rikice ta dan fara ihun wahala Zainab ta yi yar daria ta ce" Masha Allah kin ba sarakan ruwa rabonsu, yanzun shikenan ke da su ba zasu kuma shaka maki ba, kar ki tsorata babu wanda ya koyi ruwa bai shaka ba ko a garin nasaru ne bale a nan, kuma akoy rabo na sarkin ruwa koda baya nan idan muka koya maki bamu cire rabonmu ba akoy matsala"

Tabas ta ga abu, da farko sun gigitata, sun rikitata, a hankali kuma suka shiga bin bayanta a hankali da raha, suka shiga gabatar mata da koyo irin namu na gida, koyo na kai tsaye wanda a nan take za'a yi abin kuma a tsareka da ido ka maimaita, ba tare da an maka theori ba Ke durfafar pratique hakan ya sa abin ya shigota kai tsaye ta bada dukan hankalinta tana kallo

Sun dauki lokaci mai tsayin gaske kafin suka fito, cike da gajiya ta baro wajensu ta dauki hanyar gida kamar an tika mata dukan tsiya

Layi take da haka ta idasa cikin gidansu, tana shigowa ta yi turus tana kallon yau kuma wani sabon lamarin

Oga ne tsaye yana zuba balaki hakan ya sa ta kara kashe kunne ta ji yana fadin" Ni zata yiwa rashin mutunci , nawa na biya? Zata dawo gidan ne kai gaba dayankuma zaku fada min a me kuka daukeni ne a gidan nan!"

Ido ta kikifta kafin ta yi kundunbala da du wani tsoro ta danna kai kanta tsaye ta ce" GANI MEYE? "

Gaba dayansu suka juyo gareta, tun daga Oga , mahaifiyarta har karamin autansu sunna kallonta, Oga ne da bacin rai ya nufota ya budi bakinsa ya ce"
11/14/21, 12:44 PM - Allah Akbar: □□□□

Dayar ta yatsina baki mai sunna Huwaila ta ce" Daga gidan wa kuwa take banda yawon sakarcin nata ko dai Dogarin ya samu ne yana kwakuleta a lungu, ke yanzun in banda rashin kunya da iskanci irin naki mu zaki kalla ki ce tarbiyar wani bai maki ba, nan fa kije fita tun safe sai talatainin dare ki dawo kuma ki shige ki ci abinci ki kwonta a gado ki yi barci ki tashi ki sala wanka da ruwan pampo ki kuma fita, in ba sana'a ce da ke ba tsayayiya wai me kike yi? Ki dai bi dunia a hankali idan maza ne sai sun gama tsotseki tas zasu yar da honkon, gaki ke ba kyau ba, ke ba farin ba bale ace ko dan su a so ki duwawu kuwa akoy wadda nata ya dame naki ya shanye bariki ta gama da ita ta yar"

Oga ne ya juyo cike da mamaki yana kallonsu su dukansu , kansa ya gyada ya kalli sauran yan matan su ko a kwalar rigarsu wai rigimar da ake , sam bata dada su da kasa ba, kansa ya kuma gyadawa ya dafe kugunsa da hannunsa ya ce" Yau na ga jaraba, kai wai kudinku ko nawa? Kamar wadda kuke jira uba ya bata da yarsa a gidan nan ko? Har a ringa fadin wai ranar wance ko na wane, ke huwa Huwaila da maza na karar da alheri ai da an karar da naki sai da aka gama da duk wani alherin naki fa na kwaso nima dan jaraba kamar wanda iya ke min baki walahi, to yanzu ai sai ku bari in mata tambayoyin daya bayan daya ta bani amsoshina dan kun sani sarai ba karya ba zata mini ko kasheta zan yi, dan yar nan jaruma ce kamar ubanta ko a gaban uban waye zata yi magana kanta tsaye ba da dar dar ba ko tsoron wani abin ba!, to Allah tunda na ga so kuke ku nuna min kun shanye ni ta yadda idan na yi niyar yin fada kuke amshewa ba za'a mata fadan ba, kudi kuma nawa ne ba na uban wani ba a barmin yara su sha iska!"

Huwaila ta tabe bakinta da bacin rai da bambami ta ce" Ni dai ba ubana ba a zagin nan, kuma da kake cewa kudi ba zaka amso ba dama ta ina zaka iya amsowar kai da mutanenka abokannan sana'a! Ai gado ta yi na iskanci"

Daga muryarsa ya yi ya ce" Ke dama yaya za'a yi na raba zagin uba da ke? Da masu uban nake ki bari in dawo layin yan layi a tudun jamus sai ki sako bakinki ki ce da ni oga du buro'ubarka kar ka zagi yan sholishow hegiya mai kirar muciya!"

Jin yadda ya barowa Huwaila ruwa du sai suka ringa watsewa ba wanda ya karra sekwani ya rage daga shi sai Muneerath sai mahaifiyar Muneerath

Zama ya yi saman kujera yana dafe gaban goshinsa kafin ya mike tsaye ya ce" Kai dolema na fara nema maki walahaula da su karya tambaya, dolema na fara nema maki na tsari da na yan uba a yada babarki ke maki hasada gwara in yi da gaske, ni Rukaya mamaki kike bani yar nan kamar wata kishiyarki ke kin fi shiri da kishoyoyinki a kanta, wai kina zaune ana cema yarki na bin maza kin kyale? Ni da kanwata ce ke ba matata ba sai na zane ki tas, ki gode Allah matata kike ni kuwa mai tsoron Allah ne" yana fada ne yana kamo hannun Muneerath dake kallonsa galala hakama mamanta ya turata dakinta yana fadin" Kin ga je ki labe abinki kafin in kawo na turare da wanka ki maida hankali , kai ni ko layama nake basu gaba daya yan gidan nan ko sa shafa maki lafia? Bari dai in je stade in dawo mu yi shawara da abokina idan ya ga ya dace in maka su gidan mai damagaran a mana tsakani da ke da su har ita ruky din sai na yi sauko na amso masu samaci, dan na kula so suke su idasa haukata min ke"

MUNEERATH na jin maganar gidan sarki ta juyo ta kale shi da yannayi na son ta yi magana, sai dai bai bata dama ba har ya rufe kofar ya juya hakan ya sa ta raka shi da kallo kafin ta juya tana kiciniyar cire soguwar rigarta, sai da ta cireta sannan ta cire dogon wandon ta kuma cire breziyar dake jikinta kafin ta cire rigar da ta yi dan kwali da ita domin dan kwalinta ruwa ya tafi da shi

Ya Allah..... MUNEERATH ban san da yaya zan kwatanta ba, dole ta rufe jikinta domin idan har ta kasance mai budewar da da karfi da yajima za'a cin mata
Ya ilahi, yarinyar a cike take iya cikowa, sannan ba shafafen ciki ne da ita ba gaskiya, cikinta na tafe da yannayin da take ciki ne na halin koshi ko jin yinwa yana nunawa, abinda ya rufa mata asiri wadinan dima diman duwawu dake bayanta, irinsu ne ko sun kunso ciki sai dai ka ji haihuwarsu ba dai ba ya nuna kansa domin irinsu ne cikinsu ke bin cinyoyinsu ya lafe abinsa
Wasu irin cinyoyi ne masu fadi hadi da fafadan duwawun da na yi mamakin yarda ta samu pant ya dane su daf ya kama su taf da su.
Mamanta kau ba manya bane sosai domin sam basu da girman a zo a gani, aman kuma wani abu da garesu shine bakin shantu, a cike suke taf basu da ramar da za'a ga kanantarsu, su dai daidai wa daita ne daidai hannun mutun □□

Juyawa ta yi ta nufi wajen hijab din da take zumbulawa ta je wanka
Tana sakawa ta kama hanyar bayin tsakar gida

Ya kai da mutun uku da suka yi gware, ba na wani abu ba sai na raini, irin gwaren nan na ana jiranka ana jira a yi masifa da kai ana jiran tashin hankali da kai ana jin haushinka
Ba wanda ta kula dan a gaskiya gajiyar da ta kwaso ta fi karfin ta tsaya ta yi wata rigima da kowama , ta kanta take yanzun so take ta rama salolin dake kantama

Wankan ta yi sosai ta fito ta daura alwallah
Mikewar da zata yi Rumaisa ta kifa mata mari,
Mugun mari ne, gigitacen mari ne mai saka bawa ya rasa inda zai saka ransa
Sai da ta kwala ihun azaba idannuwanta a rufe kafin ta bude a firgice ta sauke a kan Rumaisa

A yau bata tunanin oo ogo zai iya tsayar da ita daga lalata fatar Rumaisa, bata san lokacin da ta yi kan Rumaisa idannuwanta rufe ta hankadata jikin garun kofar shiga dakin gaba daya suka rikita kasa suka zube
Kamar taya haka suke juye juye a kan junna kafin Allah ya bata sa'a ta dane kan ruwan cikin Rumaisa
Ihu yan matan gidan ke yi da samarin ba wanda ya yi kokarin raba su, hasalima nishadi suka samu ciki harda yan uwan Rumaisar na jinni da na Muneerath din

Mahaifiyar Muneerath na tsaye ta harde hannayenta tana kallon du abinda yake faruwa, bata ankara ba sai gani ta yi maman Rumaisa ta yi kan Muneerath ta kama hijab din Muneerath din tana fadin" Walahi baki isa ba ki ilata min yarinya , ai baki isa ba ki daketa ki hannata kuka gwarama ita tana da zuciyar ta tarbe ki a kan me za'a ringa nuna mata fin karfi haka kawai?"

Idannuwanta ta rintse tana jin wani irin abu na sukan zuciyarta, a hankali ta kara sauke dubanta tana gannin yadda ake son fin karfin Muneerath din domin sarkin yawa ya fi sarkin karfi ai
Wani irin abu ya kara sukar mata kahon zuciyarta, da sauri ta daga kafarta tana nufar wajen duda wani irin nauyi da kafafuwan nata suka yi mata aman haka take cirawa har ji take kamar numfashinta zai bar gangar jikinta aman irin wulakancin da idannuwanta ke hango mata a kan yar tata sai ta kasa hanna kanta isawa

Ja ta yi ta tsaya sakamakon gannin yayansu ya warce Muneerath din da karfi a hannun kannensa biyu da kuma matar baban nasu, da inda indarsa ya ce" Kakkkkkkkkai na fa ci.....uuuuuuuuuuuuuuwaynnnnnkkkkkku, an fada makkkkkkkkkkkkku bata da gatttttttta ne ?"

Du kasa karasawa suka yi, dan shi dai sun fi kowa sannin bashi da hankalin, a gaskiya idan ya damki daya a cikinsu sai ta gane bata da wayau shi yasa kowace ta yi baya sosai

Muneerath dake layi da kyar ta iya dubansa a lokacin da ya dungure kanta ransa bace ya ci gaba da magana da inda inda yana fadin" kema bakya jiiiiiiiiiiiiii" da kyar ya karasa yana doka kafarsa ta dama a kasa ya dora da fadin" Na sha fada maki idan fada ne ki daina yi kina barin min na maki, kar abin ya maki yawa ga haukan dogari ga fadace fadace, yanzun dai jeki daki na sayi fadan kyaleni da su yau in sun rintsa shege nake"
Da wani irin inda inda ya karasa maganar yana wawurar ice a gefe hakan ya sa da ihu du suka dare masu ridar daki na yi masu yin waje na yi, fadi suke kurman gidansu abin ya tashi

Haka gidan su MUNEERATH yake, a kowani lokaci cikin tashin bom yake kashe wutarsa kuwa sai Allah

.....
Kwonci tashi, Muneerath na gannin rayuwa ta kowani fanni, a kadan ta dauki wata daya tana haduwa da abokananta filani masu iyo yayan sarkin ruwa gaba da baya, sun dauki lokacinsu sun kashe aiyukansu sunna koyar da ita yin iyo da soyayar abin a rayukansu, sau kusan hudu sunna gwada nutsewa ciki da ita, na farko da na biyun kusan a sume suke fitar da ita a na ukun ba karamin mamaki ta basu ba, na hudun kuwa sai suka sara mata kawai, ya zamana har gidansu ta sani wajen da mahaifiyarta ke zama aman bata taba haduwa da mahaifinsu ba, sukan kama kifaye su kasa , nata sai dai ta je ta bayar dan ita dai ba iya gyaransa ta yi ba
A cikin haka ta ringa neman wajen da zata koyi girki, sai dai abin ya gagara, sam ta kasa samu, sai a gidan su Amina ake koyar da su abinda kamar ana zubawa ana wankewa ne a kanta, du yadda amina ta kware ita ta kasa dafa abin kirki, ta kasa dafa abu ya dahu ya yi dadi sai dai ta kona ko ta cika wani abin da zai kasa ciyiwa

A haka yayanta ya kawo mata journal din da aka fadi bayanin za'a dauki sababin HOTTESTE a babar makarantar da ake horar da su

Ta jima tana jin juwa, makarantar tsakaninta da gidansu tafia ce mai nisan gaske wace ake cin kusan rawa biyu da rabi a mota, kuma a cikin garin take
Bayan wannan irin tsarabe tsaraben da za'a kawo kafin a samu shiga, uwa uba gwamnati na biya maka rabi ka biya rabin da ta tabata ko ita aka siyar ba zata yi kudin aikin nan ba

Kamar yadda ta saba kadaice kanta a gaban matsala dan ta sanar da wanda ta san shi kadai ke fitar da ita, shi kadai ke bata hanya, shi kadai ke rufa mata asiri ta yi, takan raba dare tana hawaye a cikin sujadarta ta fada masa ta sanar masa ga abinda take so, aman idan alkhairinta ne
Ta mayar da yin azumi abu mafi sauki a duniyarta, ba rana kulun yi take
Ta kwatanta yiwa oga zancen ya ce bata da hankali
Ta tunakari Mama ta ce da ita" Munne in dai ba so kike na fita yawon banza ba na tara kudin nan, ke ko karuwanci muke ai yanzun ba tsada bale mu iya tarawa dan Allah ki raba kanki da shirmen banza , yo ni ko dudin nan gareni ai ba zan zuba ba domin abin nan ba lale ne ka samu ci ba, kana oya zuwa ka fadi shikenan an yi asara"

Haka ta dawo ta kara kusanta kanta da Allah, tuni Amina ta fara karantun likitanci kuma tana jiranta ta tardota dan ko ita bata bata kwarin gwuiwar wannan shirmen

Tana ji tana gani ranar da aka saka ta zo ta wuce, wace ta tabata da an yi an gama, hakan ya sa ta yi kuka, kukan rashin rabo ne ko na gannin mafarkinta ya barta ne?

A haka ta dawo ta ci gaba da rayuwa shiru shiru da ita
Da yawan yan cikin gidansu kan yi daria su ce ta dogari yanzun aljannun shiru shiru ta dauko

Yayan nan nata daya kwal shi ya san me take ciki, kuma abin na damunsa, ba dan komai ba sai dan ya san a kan sannin ciwon kanta take damuwa ba a banza ba

Shawarar ta je zuwa University bya bata, ta tafi ta yi karatunta ya bata, a dole ta harhada ya nata ya nata ta fara tafia jami'a

Abinka da abinda baka so, baka yi niyar yinsa ba gaba daya ba gane komai take yi ba, a UIT din idan ta je tana yin jeka ka dawo ne kawai, gashi wataran abinda zai maidota kadai tashin hankali ne dan har labe take dan kar a rage mata hanya, gashi babu yan anguwarsu a nan bake su ringa yin hanya daya

Da yawan lokuta takan yi wani tunani , sai ta basar ta yi murmushi kawai idan ta tuna cewa ba lalene abinda bawa ke so ya zamo alkhairi a rayuwarsa ba, ba lale ne Allah ya bata burikanta duka biyu ba, ta tabata rashin wannan aiki na nufin zata samu Dogari ne

Ta kasance mai fitowa da jakar makarantarta a baya, a cikin jakar nan tana dauke ne sa takardunta kaf na anfani harta da na Bac dinta dan bata barin takardunta na anfani dan gudun a shiga a cicira mata su

Tafe take sanye sa doguwar riga irin yar kanti din nan, du yadda rigar ta kai da budewa daga kasa sai dai idan iska bata kado ba sai ta nuna abinda bata so a gani din
Kanta sanye da farin dan kwali bata yane shi ba, sai farin silifas mai tudu

Tafiarta take tana shawagi kamar wata tauraruwa duba da safia ce karfe takwas ne da kwata

Bim bim bim..... motar dake biye da ita sai kara yi mata oder take aman sam ta ki ta tsaya ko ta kula shi

Danewa ya yi da karfin da ya sakata juyiwa rai bace ta zo wajen motar

Tana zuwa gannin ya tsaya sai da ta fara dukan tayar da kafarta kafin ta leka rai bace ta ce" Kai wai meye? "

Jan buzun dake zaune ya tsume abinsa ya ga kalaci da safiar nan sai ya sakar mata murmushi da hausarsa irin ta bugaje ya ce" Sannu yan mata, yi hakuri yar budurwa shigo mana na kaiki inda zaki je"

Kallonsa ta yi gannin bama wani baba bane sosai aman sai wani abu yake wai shi ya ga mace , da gatse ta samu kanta da fadin" Baka da isashen man da zai kaini har gidan Hottest "

Gannin ba wani yannayi na yayan da zasu iya shiga wajen ta yi ba sai ya yi tunanin ko aiki take a cen na iirn wanke wanken bayinsu, ko kuwa gidansu a wajen yake,
Cike da shakiyancin koma menene shi fa gidan hutu ya gani ya ce mata" Shigo mana ki gani idan ba zai kaimu ba"

□□□□□□
11/14/21, 12:44 PM - Allah Akbar: □□□□□□□

Karra kallonta ya yi ya ce" Ciki kuma? Ta yaya ? Ina Baje dinki ne?"

Karra kura masa ido ta yi kamar yana mata yaren shainanci,
Hannayensa ya watsa ya ce" ai in aiki kike a ciki kina da baje dinki na shiga, idan ba haka ba ai kin san ba zaki shiga ba ko? Ina fatan dai ba gannin wani bane kika zo dan bafa sa bari a shiga"

Muneerath muryarta a sanyaye ainun ta ce" Yanzun sunna nan ciki? Da su din da masu basu horon harma da jiragen?"

Birki ya ja a lokacin da suka kusa isa yana kallonta, sai ya fara yi mata wani kallo daban domin tambayarta ta bashi mamaki ainun da kuma shaku a kan kwakwaluwarta, waye bai san makarantar nan ba? Waye kuma zai yi tambayar idan har mutanen da masu basu horon na nan ciki?

A hankali ya ce" Ina fata dai mai lafia na dauko ba ruwa biyu ba "

Sai a lokacin ta dan gane abinda ta fada din, dan haka sai ta sakar masa dan murmushi ta ce" Dan Allah mu zagayeta mana makarantar mu ganta da kyau?"

Fuskantarta ya yi da kyau ya ce" Yar budurwa, kin ga ko sunnanki ban sani ba, ni walahi kin yi min ne soyaya ce nake so mu yi da ke idan har ban takuraki ba, ina fatan kina fahimtar yarena?"

Murmushi abin ya bata dan a yadda ya yi maganar zaka gane ya fara tsorata ne da ita, hakan ya sa ta masa murmushi na kirki kafin ta ce" Ka san meye, na jima ne ina son gannin makarantar nan, shine yau na samu mai kawo ni, bayan shi ba komai fa, dan Allah ka zagaya da ni sai mu zauna mu yi zancen fahimta da junna"

Haka kawai ya ji ya yarda da ita dan haka ya kunna motar tasa ya tayar ya juya da ita a hankali sunna tafe tana kallon yannayin ginnin da irin camerar da ba'a yin doguwar tafia ba'a ga wata camerar ba

A hankali ta kurawa wani waje ido, ba komai ya sakata kurawa wajen ido ba sai gannin wannan wayar mai kayoyin tsini a jikinta ta nan ta dagu sosai, kuma an yi wani irin katari da irin abin ginnin nan irin mai hawa hawa waje waje haka

Kara kurawa wajen ido ta yi kafin ta ce" Dan tsaya a nan mu gani "

Tsayawar ya yi kuwa yana kallon inda take kallo, sai gani ya yi ta bude ta fita daga motar

Kara gyara zama ya yi yana bin bayanta da kallo a lokacin da ta juya ta nufi wajen katangar nan

Kara gyara zamansa ya yi da kyau irin ya samu abin kallo din nan, sannan yana gannin irin yadda take ta aune aunenta shi dai bai kawo komai a ransa ba sai a lokacin da ya ga ta dauko wani busashen ice dan dogo haka sannan ta nufi wajen abubuwan nan kamar matatakala

Dan kwalin kanta ta cire ta kara daure jakar dake bayanta a jikinta da kyau sannan ta kamo kasan rigar nata ta sakota ta tsakiya ta hade ta yarda cinyoyinta suka kusan bayana sosai ta daure su da kyau ta ci damara da shi sai ya yi kamar wandon indiyawan nan burkumeme

Kara zubawa kwaurinta da wajen cinyarta da ya bayana ido ya yi lokaci daya yana shafa wajen kansa a hankali ya ce" Ke ko mahaukaciya ce zan yi manage, sai na auri biyu tashi daya da mai hankali da mai kayan kwonciyar hankali"

Lokaci daya kuma ya shiga zarro idannuwansa sakamakon abin al'ajabin da idannuwansa suke gannin masa

Da sauri ya bude motar a tsorace ya ce" Ke baki da hankali ne? Baki san sojoji ke gadin gidan nan ba idan fa suka zo harbe ki zasu yi kamar barauniya, sannan baki san karafunnan nan sunna hade da wutar lantarki bane? Yana taba ki fa sai dai gawarki a nan ko bakya ji ne?" Ya karashe da taratsun ihu gannin bata kula shi ba kara hawa take

Bata kula shi ba da sauri ta kara kaimin hawan nata, wannan busashen icen ta saka ta shiga ture karfen nan, a firgice ta dan tsaya sakamakon kukan jiniyar da gaba daya wajen ya dauka sannan motocin da ta juya ta hango suka kara tsoratata, aman bata tunanin zata tsaya dan motocin nan da sauri ta karra ture shi sosai sannan ta haye saman katangar ta kuma juyowa tana kallon yadda dan saurayin buzun nan ke tafa hannu yana ta nuna masu yana magana aman cikin ikon Allah neman tsatsara shi da bindiga suke

Da sauri ta zarro idannuwanta gannin an tsare shin sannan wani rufcece ya durfafo inda take da yaren freinch tun karfi yake fadin" Tsaya a inda kike, ki sauko ko na harbe ki!"

Idannuwanta ta rintse cike da firgicin gannin kamar an zo kama gagarumin barawo ko za'a gabza yaki tsakanin yan boko haram da sojoji? Ihun da ake mata ya sakata rintse ido da baya baya ta juya ta shiga kokarin dirawa ta bayanta

Da wani irin karfi suka kuma kwala kiran ta sauko hakan ya sa ta saki garun gaba daya tana ambatar Allah a ranta ta tafi ba tare da tunanin zata dira da ranta ko a mace ba

Wani wahaltacen ihun ta saki a lokacin da ta ji wani irin abu shi ba wutar nepa ba shi ba wutar kiyama ba ya hade an jona mata a wajen wuyanta kiiiiiiiiii gaba dayanta karkarwa kafin ta zube kasa warwas tana wani irin abu tamkar ana jan wata jijiya a jikinta

Ribom din dake kanta ne ya kwonce gashin kanta ya bayana mai baki sosai da kuma tsayi lumbuk da shi , ta kasa kasa take bin manyan takalman sojojin da suke nan tsaitsaye da kallo gaba daya kwakwaluwarta take jin zata tarwatse mata , bata taba jin azaba irin wannan ba, bata taba jin muguwar azaba irin ta yau ba, ta rantse da Allah ta saki fitsari mai zafin gaske dan bata san abinda ke jiranta kennan ba

Bata shirya ba ta ji an kwasheta kiiiiiiiiiiiiiiiiiiiiii an saka a bayan motar nan sannan an kwace jakarta an saka abin detecten bom da dukan abu na cutarwa an tabatar babu a ciki sannan suka yi ciki da ita

Tafia suka yi mai nisa kafin suke isawa office din nasu na bincike

Kuma fitar da ita suka yi suka yi wani janta janta tafia tafia da ita suka kaita wani daki mai duhu suka jefata ciki suka rufo

Da sauro ta dukunkune kanta cikin cinyoyinta gaba daya jikinta na bari ta kasa katabus sai karkarwa take kamar zata mutu

A firgice ta dago kanta jin motso kamar a kusa da ita,
Shiru ta yi sai kuma ta ji muryar namiji yana fadin" Walahaula wala kuwata ila bilahi yau me na aikata na dauko mahaukaciya yau na mutu na lalace Annata batama san na dauko motarta ba, wayo Allahna"

Da sauri ta kai dubanta wajen duda duhun da dakin ya mamaye da shi , a hankali take ta ambaton sunnan Allah kafin da kyar ta ji wasu hawaye sunna fitowa ta cikin idannuwanta

Wani dan haske ne ya bayana mai ruwan blue, wanda mutanen dake tsaye gaban Computer kama tun daga shugaban makarantar , da shugaban masu bada tsaron, da shugaba mai kare hakkin yara, da mai kare hakkin mata, da dai sauransu suka zubawa Alon madubin da ya raba dakin da inda suke sannan sunna sauraron amon muryoyin dake tashi

Ido hudu Suka yi Muneerath da saurayin nan, da sauri ya ja baya cike da tsoron ganninta kafin da muryarsa sama sama ya ce" Ke wacece ke? Me na gaba maki da yau kika zabi shiga motata na kawo ki nan, cewa suke wai wa ya aiko ki dan girman Allah ki fada masu ni dai ban sanki ba a sakeni na tafi gidanmu wajen Annata"
Ya karashe yana hade hannayensa yana fashewa da kuka tamkar ba shine dazun ya dauko yar mutane cike da shakiyanci da mugun nufin son samun lagonta dan ya far mata

A tsorace itama take kallonsa kafin ta ce" Walahi walahi ni babu wanda ya turo ni, ka ga tun ina karamata burina na zama HOTTEST, ko a yau ni kaina ban yi tunanin zan shigo gidan nan, nama fa hakura da zama domin iyayena basu da halin biya min, kai ko kudin da zai kawoni nan ni bani da shi dan ka ce kana iya kawoni ne na biyoka muka zo, ashe haka gidan yake?"

Da karfi ya ce" Kin kuwa kashe mu, wayo Allahna na shiga uku to kin san baku da halin biyan uban me ya kawo mu nan din? Gashi yanzun banma san a me suka dauke mu ba!"

Kallon ogansu daya daga cikin masu bada tsaron ya yi ya ce" Oga wannan fa ina ga shirya abinsu suka yi, ka barni na shiga na jigata su ta yadda zasu yi bayani da kansu!"

Ogan nasu ya dan daga masa hannu yana kallon itin yadda suke maganar , a hankali ya kai dubansa wajen shugaban makarantar da ya tsura masu ido su dukansu ya ce" A jikinsu babu mai dauke da wani micro komai kankantarsa a kowani irin lungu ko sako na jikinsa dan mun duba, sannan ga takardun bayannan ko su su waye nan yanzun aka miko daga dakin bincike na computer bango, inaga da gaske ba turo su aka yi ba dan cutar da kowanmu, dan karrin bayani kuma muna iya zuwa cen gidan iyayen nasu su duka biyu, idan kuwa kun yarda da maganata ban ga wani abu mai duhu ba kawai a sake su "

Malamin Psychologist ne ya juyo da byro a hannunsa yana dan cicijewa ya ce" Ban karanci wani yannayi na munafurci a kallonsu ba, ga yadda computerna ta nuna min aman zan so na shiga koda na second goma ne na gansu gani ga su dan karrin yarda, aman koda ban shigan ba na yarda da irin abin nan da nake gani na computerna dan ban taba aiki da ita na ga ba haka ba, ana iya korarsu su tafiarsu"

Shugaban mai kare hakkin mata ce ta dauki magana tana fadin" Na tausaya mata, aman dan Allah ku bani jakarta ina son gannin meye a ciki ?"

Sai a lokacin suka dauko jakar suka budeta, baki daya abubuwan dake ciki suka zazago saman table din
Su dukansu ido suka zubawa kayan kafin su dauke takardun su raraba wa junnansu suka shiga karantawa dan gannin ko na meye? , takardunta ne kama tun daga na Entrer en 6eme, na Brevet dinta da na Bac dinta wanda yake hade da yar takardar dake nuna ko wace ita a bac dinma, takardunta na jarabawarta kaf sunna ciki, sai wani turare na fesawa sai litafi na rubutu kamar kwaya uku da byro kalar ja da blue, sai dala ashirin
Junnansu suke kallo gaba dayansu kafin ta kara gyara tsayuwarta ta tausasa muryarta ta ce" A wannan zamanin da wahala ka ga budurwa irin wannan ba ja gira ko jan baki da madubi harda su pant a cikin jakarta ba, tabas ni na yarda da kalaman yarinyar nan, ina kuma rokon oganmu da ya duba wannan lamari ya taimaketa ya saka hannu ya kai maganar ga gwamnatinmu mai adalci a zuba mata ta samu horo ta fito a cikakiyar ma'aikaciyar Hotteste "

Daya daga cikin sojojin ne ya dauki magana da dan zafi zafi ko kuwa dan muryarsa ce mai gautsi ko meye oho ya ce" Eh ban ki ba, kuma tana iya zama haka idan aka tsara ta zamo hakan, abinda nake nufi a nan shine ba zamu saki mu yi gangancin da zamu dauki wada zata cutar da y'ayan mutane ba, ku fa tuna irin yanda duniya ta rikice, lale yarinyar nan tana iya zama innocent mai tafe da buri na son zama hottest kamar yadda kuma take iya zama makashiyar dake da burin kashe mutane da kanta"

Mai kula da yannayin yan matan wajen, watau mai tsaban tsarin halita, tsarin fata, tsarin yannayin jiki da irin gogewar mutun ta sha sket dinta damame fuskarta dauke da farin gilas na gayu ta sha madaidaicin jan bakinta ta ce" Bama wannan ba, in ba shirme irin nata ba a Niger kasa mai dauke da buzaye, filani, kyawawan hausawa , kyawawan yan mata na kabilu daban daban ne zata saka irin wannan ra'ayi a ranta? Ta kuwa san menene girman kalar da ake so a hotteste? , Bakinta ya min yawa sannan bani da tabacin idan kaf jikinta ne haka, hausarta wata gatse gatse ban ji ko kadan ta sako turanci tsaftatace ba, eh lalle takardarta ta nuna tana da ilimi aman ai ba shi zai tabatar min ba sai idan na gani a aikace, duwawunta sun yi girma da yawa mu da bama daukan masu katuna katunan duwawu?, idannuwanta sun wani lumseh sosai ta haka zata ringa yiwa pasinga magana? So kuke a fara samun matsala ne da zaki ce a duba lamarinta ? Bayan an rufe dauka kuma yanzun ita aka dauketa yaya zamu yi da iyayen yaren manyanmu da suka kawo muka kiya?"

Da sauri mai kare hakkin yara ya dauki magana ya ce" ina da magana, ni kuwa mai zai hanna a duba irin yadda take da motivation? Ku juya ku gani har yanzu kuka take tana kuma jadada masa , idan har ta samu aiki irinsu ne masu aiki da zuciya daya, ya dace a ringa duba yayan talakawa, da yaran da suke da burin aman ana dane masu dan son zuciyar iyayensu"

Dukan wannan tataunawa sa suke shugaban makarantar matashin datijo dan ba zai fi shekara arba'in ba mahaukacin iliminsa ne ya kawo shi matsayin da yake kai yanzu yana tsaye ne yana bin kowa da kallo sannan yana marantar dukan abinda suke fada, a wannan makaranta a nan dukan wani shugaban kare kare da rikice rikice yake , hakan ya sa basa daukan decision kai tsaye sai a jima ana rigima a kan abu

Sai da wajen ya nemi rikicewa kafin ya yi gyaran murya da takardun da aka yi bayanin ita din wacece da makarantar da ta yi ya ce" Takardunta sun nuna shaidar ita din yar kasa ce, haifafiyar kasa kuma girman kasa, da farko dai dukan bayanan

takarda ba su kadai ke gamsar da ni ba, dole zan baza yara kasa a min bincike a kanta, idan ta fita ina take zuwa? Me take yi? Da su wa take? A bincikar min malamanta na makaranta, a duba min gidansu yar ciki ce ko sunnan tana haifafiyar gidan ce? Ina nufin barci ke kawota ita din ko kuwa sai ta yi kwanaki bata ciki?, koda ta kama sakin nata ta koma gidansu ne sai mun yi hakan"

Dan jim ya yi ya kuma kallonsu baki dayansu ya tsaida dubansa a kan mai zaben yannayi da sauransu ya ce" Da ace abubuwan da kika zana za'a bi kafin a dauki mutun da wannan wajen bai dace da ke ba domin kina kan dogon takalmima tsayinki bai fi 1m 60 ba"

Ya maida kan wanda ke maganar a koreta ya ce" Da taka ce zaka fadi haka? Ko ka san naka da suka fito a yanzun me suke aikatawa a cikin gari?"

Sai kuma ya ja gabansu gaba dayansu ya ce" Muna haihuwarsu ne mu zubar, idan na ce mu zubar ina nufin ba mu ke binsu waje dan gannin me suke aikatawa ba, su din sunna tashi da burikansu, da yawansu sukan dauki hanyar lalacewa dan neman samun cikar burinsu, shin idan muka dubi lamarin daya cikin dubu muka tsamo muka talafa matsala ne? Maganar nan zata iya mutuwa a tsakaninmu na sai ta hau sama ba domin mu ke basu horo mu ke kaisu kampani ya zaba, idan har ita din ta cencenci zama hotteste abin a talafa mata ne ta zama ba mu koreta ba!"

Ya dora da fadin" Ku kun san menene aikinmu, shin wannan ta iya ruwa? Idan bata iya ba ba mu zamu koya mata ba!, shin ta iya Inglish kamar ruwa? Idan a takardarta satar amsa ta samu ta rubuta ta cuci kanta dan koda mun zauna a nutse mun baiwa kanmu amsar riketa mu talafeta dan talafawa yara su zamo wani abu ya kasance bata iya ba dole zamu saki hannun junna, Aikin Hotteste ba aikin direban mota bane ko kwondastan mota ba, sai ka zauna a table ka kuma kawo sakamakon jarabawa koda zaka samu ci!"

Karra dubansu ya yi da kyau ya ce" Ba zamu koreta ba, ba kuma zamu riketa ba"

Shugaban mai bada tsaron da kwarai ya ji dadin hakan a ransa a bayane ya ce" Yaya zamu yi da ita kennan sir?:

.....sorry yan uwa □□
11/14/21, 12:44 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 2 □□□

Wajen madubin ya kai dubansa, ba komai yake gani ba sai jaruma, ba komai idannuwansa ke gane masa ba sai mai baban mafarkin rayuwar dake shirin rushewa, ba kowa yake gani ba sai yar yarinyar dake neman zama wani abu da karfin zuciyarta bayan tana da abubuwan da take iya zuwa ta banzatar dan samun kudaden aman ta ki yi sai ta fi kaunar ta rufe ta nemi na kanta, kwarai ya yarda da kalamanta bayan a yanzun mutun ba abin yarda bane, haka kawai yake gannin darajarta bayan baima san ko wacece ita din ba! , hannunsa ya dora saman madubin yana kara jin magangannunsu ita da buzun nan da ya gama fahimtar yanzu suka san junna yana ji a ransa idan suka katse mata tafiarta sun shiga hakkinta, yana ji a kasan zuciyarsa dukan yaran matasa masu tsaye a kan burinsu na alkhairi kamarta basu cencenci a katse masu shi ba, idan da halin a kama masu za'a iya kama masu ne, a yadda yake tsayen ya gama hasaso mutanen da suke aiki da su wa'inda yake sama da su aman kuma suke da damar dole sai an shawarci junna dan aiki ya je a tsare ba tare da tangarda ba
A cikinsun wace ta fi zama da Hotteste din ta nuna rashin amincewarta da hakkan,
Sai dai kamar yadda ya kasance mai talafi da jajircewa ba zai saki hannun yarinyar nan ba, dan ya tabata da wani wanda ya daure mata gareta da shi zai kawota su shigo ta babar kofa sunna takama da daga kai ko dan iliminta da kuma kudinsu su zo su nuna ko dan dukiyarsu a dauki yarsu, da yawansu idan ba'a dauki y'ayan nasu ba sukan nuna mune da asara ba su bafa □□□□□□□□□, aman a wannan yarinyar sai yake gannin ba haka ba

Juyowa ya yi ya harde hannayensa , sai da ya dauko yannayinsa na jajirtacen matashin saurayi ko nace matashin datijo ya ce" Kamar yadda nace da ku da farko zamu tabatar da magangannunsu, sai option ta gaba zamu hada conseil, a cen zamu gabatar da matsalar wa syndicat, sannan zamu yi Vote! Wa'inda suka fi yawa a kan *A KORETA* ba zata karra koda second daya a gidan nan ba zamu sakata a mota a maida ita gidansu, wa'inda kuwa suka fi yawa a *BARINTA* ta zama HOTTESTE a tare da mu zamu karbeta da hannu bibiyu mu hadu mu bata horo ba hantara, ba kyara, ba zagi, ba cin zarafin halitarta, ba komai na wulakanci har ta fito a matsayin Hotteste horon kampaninmu, na tabata komai muninta ba zata rasa kampanin Jirgin da zai dauketa ba!"

Dan kus kus kus ne ya dan tashi kasa kasa kafin du su bada amanarsu duda ita mai alhakin daukan yannayin mutun din ta gama daukan hakan a wani abin daban dan ita gani take zagayeta zai yi da wuya ta iya kayar da shi, aman duda haka itam zata gwada nata chanc din dan gannin ba'a dauki yarinyar nan ba, ita kawai bata yi mata bane! (Rayuwa kennan, ba mai ba in baka nan, rayuwar kennan ka hadu da mutun yau bai taka maka ba, bai kashe maka ba aman sai ka ji ka tsane shi iya tsana kamar zaka kashe shi dan jin haushinsa.....Allah ka sa mu ki mutun domin ka, sannan mu so shi domin ka)

.....wannan kennan

Murginawa ya yi daga kwoncen da yake a bed din dakin hotel din da ya sauka a Europe
Dakin yana bada wani dumi mai dadin gaske wanda du wanda ya fito daga waje cikin kakausan sanyin mai ratsa kashi mai saka bawa ya yi kiskirim ya kamo wata tashar bayan ba abinda yake tunani sanyin ke neman kasara tunaninsa dan tsabar karfi idan ya samu wannan dumi na dakin da yake kwonce inaga kafin ya fito sai an hada da motar yan sanda a ciro shi da karfin tsiya
Dan dakin ya samu chaufage watau na'ura mai dumama daki da dumi, ga kuma wutar garwashin rushi mai zafin gaske da aka hura ake kuma kulawa da kara masa gawayin marar kauri da kama daki a kai a kai, ga sanyayen kanshin turaran ruwan da na'urar watso kanshi ke watsowa a hankali ba da yawa ba tana jone tana aikinta wanda shine ya gama dakin ya kasance zaman dakin ba zai gunduri wanda ke cikinsa ba

Dan Blutouphe din dake kunnensa na iPhone original fari ne ya dan haska haske blue mai haske halan ke nuni da dayan biyu ko yana sauraron wani abu daga cikin wayarsa ko waya ce yake yi, aman irin shirun da ya yi yawa sosai din nan ya saka ni tunanin ba waya ce yake yi ba, domin waya a garin nan tsadar balaki ne da ita koda a cikin garin zaka yi in dai ba irin wayar cikin gida bace watau ta jikin bango ko ta ajiye telephone, sai ko idan whatsup ne, idan kao tsaye ne ba zaka iya jimawar nan haka ba zaka kashe ko kudin wayar taka ta katse kanta ba

A hankali ya yi dan murmushi ya mika hannunsa ya dauko byro da Bloc note din gefen bed din ya bude a hankalo ya shiga rubuta adu'ar da take karanto masa cikin harshenta na jinnin larabawa da nutsuwarta ta nutsatsiya, da kauna irin ta uwa a gareshi kafin ya budi baki cen kasa kasa ya ce" Mah, na rubuta ki kwonta ki huta plz dare fa ya yi a wajenku "

Kamar jira take ta ji ya mata magana sai ta ji wata hamma ta zo mata, a nutse ta rufe bakinta ta yi tana adu'a kasa kasa

Murmushi ya yi dan sarai ya ji hamma ce ta yi aman kuma ba zata kwonta ba sai ta gama yi masa nasiha , muryarta tausashe ya ce" Yanzun sai kun kara kwana nawa? "

HANJA ya kai dubansa kan agogon dakin kafin ya ce" Uku "

Kai ta gyada, sosai take son ce masa dan Allah a kwana ukun nan ya tsare kansa da aikata zina, sai dai kasancewar ba a kowani time take masa irin maganar nan ba sai ta wayance ta ce" A duk lokacin da ka ji zuciyarka na ingizaka ga aikata aikin da ubangijinka ya hane ka da aikata shi komai kankantarsa, ka yi gagawar hasaso amsar da zaka bashi a lokacin da ka zamo daga kai sai shi, ka saka zuciyarka koran shedan ta hanyar sakata furta A'UZUBILAHI MINA SHAIDANIN RAJIM, ita da kanta ba a kan lebenka ba, a haka zaka ji koma menene yana kasa da son kauce fushin wanda ya hakiceka, shi kuwa du wanda ke yinkurin barin sabon Allah ana masa kyakyawan zaton zai daina kwata kwata wata rana"

Murmushi ya yi har cikin zuciyarsa yana lumshe idannuwansa bai yi magana ba, Murmushin nasa shine amsarta wanda ta ji dadin jin murmushin dan alama ce ta ya dauki maganar

Da kyar ta katse kiran shima sai da barci ya farra daukanta kafin ta katse dan kanta ta silale saman bed dinta , dama dan ta masa nasiha ne ta yi masa dogon kiran nan

Murmushi yake da byron a hannunsa

A hankali ya dora ya rubuta *MOTHER* a saman farar takardar, kafin ya dora a kusa da sunnan MOTHER din kalmar *I LOVE YOU*
Wayarsa ya janyo ya bude ya dauki hoton hakan sannan ya tura mata ta whatsup dinta ya ajiye wayar yana dan murza gefen wuyansa daga zaunen da yake

Knocking din da aka yi ya saka shi kai dubansa wajen kofar

A hankali ya mike tsaye daga kwoncen da ya koma ya yi ya ja ya tsaya
Kaffafuwansa ya dan wara ya mike hannayensa sama ya yi mika da salati a kan labansa kafin ya nufi wajen kofar kasancewar rufeta ya yi da ky

Bai wani leka dan gannin ko waye ba, murdawa ya yi ya bude
Ido ya zuba masu, yan mata ne biyu tsala tsala sun dau wanka cikin shigar kananun kaya watau dayar na sanye da dogon wando dayar kuwa da riga doguwa aman bakin tsayinta gwuiwarta kuma a gwuiwarta tana da tsaga, irin dai an gama damewa iya damewa

Idannuwansa ya lumshe ya kai dubansa kan yaron da shi da kansa ne ya saka shi dauko masa gidan hutun nan

Ka sani kora ka yi nisa ka boyewa ganina wanda ya halice ni, ya haliceka, ya isa da ni mamanka ba kai ba yana kallonka, shin baka tsoron a taba ni mamanka? da sauri ya buda idannuwansa yana kawar da dubansa a kansu , kwata kwata ya ji abin ya fice masa a rai duda idan jikinsa za'a buda za'a ga ba haka ba, aman a hankali abin ya fice masa a ransa

Kofar ya mayar ya rufe ba tare da ya ce da su komai ba ya koma saman bed sin yana dafe kansa da yake jin ya masa nauyi ya kwonta a hankali yana lumshe idannuwansa

Kallonsa suka yi, mai sanye da doguwar rigar ta dan watsa hannayenta ta ce" Yaya haka ?"

Shima gaban goshinsa ya dan dafe ya ce" hakan na nufin baya ra'ayi"

Mai sanye da wandon ce ta juya kwayar idannuwanta ta ce" Ban gane ba, ba shi ya saka ka kawo masa mu ba? Shine ka sa muka ajiye du wani costomanmu na yau muka biyoka ka mana alkawarin in dai kudi ne damuwarmu zamu samu isasun da sai mun ji dama mun bishi?"

Kalonsu ya yi daya bayan daya ya fara tafia yana fadin" Mu je ku amshi kudinku dan ba sune damuwarsa ba!"

Da wannan ya yi barci, aman a mugun jigace, irin mugun barcin nan da kana yinsa ne kawai aman farkawarka zata fi zame maka alkhairi a kan rintsa idannuwan naka, tun karfe hudu ya farka a jigace ya samu da kyar ya yi wanka ya dauro alwallah ya fito

Saman darduma ya hau ya mayar da gabansa gabas ya tsaftace tunaninsa, ya tsayar da dubansa, ya dorawa harshensa ambaton wanda ya isa ya bashi ko ya hanna masa, wanda ya isa ya karre shi , wanda ransa ke hannunsa, mai dora cuta mai kuma bada magani, gagara misali sarkin sarakuna

Sai da ya gabatar da azhkar dinsa cikin nutsuwa kafin ya mike
Kayan gudu ya saka ya fice a dakin jikinsa ba kuzari sosai dan mararsa ta masa nauyi

Bai samu ya yi gudun yadda yake so ba ya koma dakin hotel dinsa ya zauna sai hada rai yake dan bai fa ci abincinsa ba, ko yinwar dake cikinsa bata kai damuwar da yake ji ba
Kasancewar pc dinsa a kunne yake, sannan connexion ba saukewa ake yi ba vidio calll ya shigo masa

Ya jima yana kallon sunnan kafin ya dauko ya daga yana kallon screen din

Kallon junna suke da hakimtacen mutumen da ya bugo masa wayar,
Da dukan alamu a wajen wannan kamilalen ya gaji wannan shariya da iza irin ta sarauta

Kamar ba zai yi magana ba ya kalli agogon hannunsa ya kuma kallonsa ya ce" Ina kwana "

Kansa ya dan sada ya sosa girarsa sannan ya dago yana kallonsa

Kuma gimshe fuskarsa ya yi ya ce" Abinda ya gani a takarduna ba su ba zai fada min? Meye laifinsa dan ya fadan cancerta ta kai stade na karshe har da zaka kore shi a kasa? Wannan fa shine likitan mamanka a hannunsa ta rasu, kuma nima shine likitana tun ban san zan haifeka ba, meye laifinsa? Ko dai tsoron kujerar da ta zame maka dole hawanta ne ya saka ka korar shi?"

Idannuwansa ya rintse cike da jin zuciyarsa na tsintsinkewa, kuma budewa ya yi ya sauke a kan fuskar mahaifin nasa kafin ya saka hannunsa ya rufe computer ya jinginar da bayansa a jikin garun dakin yana jin kansa na juya masa.....da ace shi din mai magana ne da ya budi bakinsa ya sanar da su abinda yake ji a cikin zuciyarsa, ba zai iya fasara masu ainahin me yake ji a zuciyarsa a yanzu ba, baya tunanin harshe zai iya sanar da abinda ya dane masa zuciyarsa ba, shin ina zai shiga? Ta ina zai fara? Me zai rika?.....

Kukan da wayarsa ke yi ne ya saka shi kuma bude idannuwansa ya dauko,
A nutse ya daga da salama a kan labansa

Sama sana yake jiyo muryarsa yana fadin" Ki fadawa yaronki ni ubansa ne ba yaronsa ba, ni zai rufewa call? Bani shi"

Sai da ya saki murmushi a sanyaye ya ce" Mahhhhhhh "

Tsai ta yi jin yannayin muryarsa, a hankali ta ce" Son lafiyarka? Baka da lafia ne? "

A sanyaye yana fatan idan ya budi baki ya rushe mata da kuka ya ce"

Ya Allah ka amshi ibadunmu, ya rab ka yafe mana zunnubanmu □□□□□□
11/14/21, 12:44 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

SADAUKARWA GA : *SIS MUNEERATH MARUBUCIYARMU BABAR MARUBUCIYARMU LIKITARMU KUMA HAJIARMU*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 3 □□□

TASO DA NONO

Ki samu ayaba (plantain) ki yanyanka ta ta bushe sannan ki daka ta ta zama gari, saiki samu aya ki wanke ta ki saka gyada ki markada sai ki tace ruwan kina diban wannan garin plantain din kina zuba madara peak kinasha kamar sau biyu arana kafin sati daya zakiga canji sosai nononki zasu tashi su ciko..in shaa Allah.

Sannan ki samo APKI ki dake shi sosai ki tankade shi ya yi laushi sosai ki kawo garin Hulba ki hade da Bulanga (Man kade) ki cakude su sosai ki ringa shafawa mama da hips, su maman ki ringa daure su cikin bra dan idan sun dauko cikowar su dauki yannayon tsayawa ciirrrrrr a kirjinki ki yi ta yi har su tsaya iya yanda kike so hajia, sirri ne wanda aka gwada □□□

A hankali ya kuma maimaita sunnanta yana lumshe rinanun idannuwansa

Mahaifinsa da ya dauki zafi sakamakon kashe masa kira da ya yi ne ya tsaya a gaban matarsa uwar gidansa kwalin kwal yana kallonta gabansa na faduwa
Tamkar kurma ya shiga yi mata nuni da tambayar bashi da lafia ne?

A hankali ta kai zaune dan jin zuciyarta na luguden kida da tsoro fal a cikinta ta ce" Fada ya maka ne? Menene? Ka ci abinci?"

Da kyar ya iya sakin lebensa da ya cije da karfi muryarsa cen ciki ya ce" Wai likita ya ce masa ya kusa mutuwa, kin sani? "

Idannuwanta ta rintse da dan karfi sakamakon tabo mata abinda ke sakata kwana da tashi tana kuka , takan wuni zuciyarta cinkushe, takan so zama da shi su yi maganar da zasu tsayar da maganar zama tare daga ita sai shi sai mahaifinsa aman kwata kwata ya kiya, ashe gudun maganar ne yake? Ashe abin na masa ciwo ne?

A hankali bayan ta aro dukan jarumta ta ce" Na sani "

Idannuwansa ya buda da sukai masa ja muryarsa a sanyaye ya ce" Yaya kike iya shanyewa? Yaya kike iya walwala?"

Idannuwanta da suka kawo kwallah ta bude ta sauke a fuskar mijinta dake zaune yana kallonta, da wani irin yannayin da ta kasa gane shin shirin fashewa yake yi da kuka ko murmushi ne kwonce a kan fuskarsa?

A hankali ta ce" Dan na yarda cewa dukan mai rai mamaci ne, dan na kwana na kuma tashi da sannin cewa du daular nan da muke ciki du irin girman sarautarmu , du gatanmu, du masu tsaronmu bamu isa mu ja da wannan kakarfan lamarin ba, idan lokacin ya zo babu tsumi babu dabara dole zamu mika wuya".....dan sasautawa ta yi hawaye na zirarowa ta kurmin idannuwanta, muryarta ta yi rauni ainun ta ce" Dan na san kuma cuta ba mutuwa bace, ta yiwu shi aka ganowa haka aka fada, hasashen kennan, wanda babu wanda yake tsaye a lokacin da Allah ya hukunta bale ya tsaya ya fadi cewa ga rana, ko boka, ko malan, ko likita ba zai ce wane ga ranar da zaka mutu ba, komin zafin ciwo, Son mun san da ciwonsa.....cancer, ya ki a yi treatment dinsa.
Son na kwana da sannin shi mai wannan ciwo yana iya murjewa ya tashi kalau wanda yake tafe da lafia ya zama gawa, idan na tuna haka idan na tuna cewa idan ba lokacin bawa ya yi ba ba zai mutu ba, sai na dan ja numfashi na sauke,
Son ka fa sanshi ina fada maka ka zauna mu yi maganar kana gudu, Son sai na zabura na farka na fashe da kuka idan na tuna yar uwata ....."
Ta karashe tana fashewa da kukan da ya saka HANJA mikewa tsaye yana cakuda gashin kansa a hankali ya ce" Plz , Mah, plz li bar kukan "

A hankali ta ringa rage kukan nata tana ta shasheka, idannuwanta ta lumshe ta kuma budewa tana kallon yadda mijin nata ya bude mata hannayensa yana nufin ta zo gareshi

A hankali ta karasa gareshin tana karra rike wayar da kyau ta shige jikinsa ta dora kanta saman kirjinsa, muryarta cen ciki ta ce" Bana so ka mutu "

A hankali yake tapping din bayanta a cen ciki ya ce" SHIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIIT "

A hankali Hanja ya kashe kiran ya kai zaune saman bed dinsa
Dubansa ya kuma kaiwa wajen agogo kafin ya mike ya yi bayi
A gurguje ya shiga shiryawa yana duba time din da jiragen zasu tashi dan zuwa gari gari
Idan ya ce a yau zai tafi ya tabata sai ya sha yawo, zai sha wahalar zaman jirgi da cenza jirgi, aman kuma zai je din dan zuwan shine abinda yake ji a gaf da zuciyarsa, zai je ya fuskanci mahaifinsa a yau su zauna su tatauna, ya hanna mamansa kukan nan da ta dauka take yi, ashe shi yasa kwanakin nan bini bini ta zo wajensa ta zo ganninsa? Ya rab

.....

Barkarmu da wannan rana
11/14/21, 12:45 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 4 □□□

Ta jima Kanta sade tana kallon takardar da kwaro kwaro sa hannun mahaifinta da na mahaifiyarta suka bayana kafin ta dago kanta ta kuma danna recodern da akai masu dan ta tabatar ta kuma yarda da maganar da aka fada mata

Zuciyarta ce ta ji ta mata rauni, a hankali ta kai dubanta kan Buzun da ta jaza masa yin kwararan kwana biyu a cikin gidan nan, du ya firgice ya fita a hayacinsa, gaba dayansa ya firgice, a sanyaye ta ce" Baka daina kukan ba? "

Dubanta ya yi, shi yanzun tsorontama yake har ga Allah, bai san wani irin damuwa iyayensa suka shiga na rashinsa ba

Shugaban makarantar ne ya dube shi ya yi murmushi ya ce" Mahaifinka na waje, kai kawai yake jira ku juya gida, mahaifiyarka kuma ta ce bata yi fushi da kai ba "

Muneerath ya kali shugaban makarantar, gaba daya sai ta ji ta karra muzanta, ita bayanan nata iyayen banda tsabagen turewa da nuna halin ko in kula da nuna kai gwarama da ta tafi dan mahaifiyarta cewa ta yi Allah ya sa su su gane bata da lafia su bema mata magani kafin su dawo da ita, babu wanda ya nemi zuwa ya ganta, oga daria ya yi ya ce kai aman yar oga an yi nataciya, to idan so take ku bata mana ni ai bana hanna yarona yin aiki ko wani iri ne, ai gwara ita aikin nata a bayane yake idan ta samu kuma zan fi kowa daga kai da tunkaho a gari, wasun fa ba'a san ko me suke so takamaimai ba gasunnan shagu a zube sai kwarewa a iskanci!
Ko da akai masa tambayar zai je ya ganta ? Dan idan aka rufe aka fara masu horo ba wanda zai shiga , cewa ya yi kai ina akoy inda zai je kawai a gaisheta

A hankali ta hade hannayenta ta dora kanta saman table din dake gabanta ta dora hannayen nata saman kanta watau saman gashin kanta da rabonsa da abin daurewa dan kwali tun da ya kwonce ya fadi a wajen da aka jona mata chok din nan,

Kunnayenta ke jiyo mata takun tafia da budewa da tafia da kuma rufewa

Shiru ne ya dauki sal din, kanta a saden nan sanyin wajen na ratsa gabai din jikinta baki daya

A hankali ta karra jan shashekar kukan da take ta danewa, jin shirun ya karra ratsa wajen sosai ya sakata dan dagowa a hankali

Ido hudu suka yi da shi, a hankali ya sada dubansa sakamakon yadda gabansa ya fadi na hada idon da ya yi ido cikin ido da ita

Kuma juyowa ya yi yana kallonta a hankali cikin yaren turanci ba freinch ba, gogagen turanci dan ya fara gwada ilimin nata ya ce" Me yasa kike kuka "

Gashin kanta ta ture da hannunta a hankali ta karra cije lebenta na kasa ta hade gashin girarta mai bakin gashi sosai wanda tamkar an mata gyaran gira irin gyaran girar nan mai shegen kyau , hannayenta ta hade wajen kirjinta ta kara busa iska wajen gashin da ya kuma zubowa gaban goshinta

A hankali ya zauna saman kujerar yana kallon iya fuskarta da lebenta ya yi ja , kasancewar tana da baiwar lebe mai ruwan pink na kasan nan sannan ko yaya ta dan dantse shi sai ya dan karra kumburi ya kuma dauki shekin dan yawun dake gogarsa sakamakon takan fitar da harshenta ta dan lashi leben nata ta mayar
Fuskar nata sai ta masa kama da shekarun da ba nata ba, tamkar bata kai shekarunta ba, fuskar tata ta masa kama da fuskar yara kanana irin fuskar mage, gaba daya a yanzun da idannuwan ke cika da hawaye sunna zuba shar shar shar yadda ka san a mayar da ita TV abin kallo

A hankali cikin yaren turancin ya ce" Bakya son aikin ne ?"

Kanta ta girgiza tana kallonsa , a nutse ta budi bakinta cikin wani irin kalmasashen turancin da idan ba fada maka aka yi ba zaka yi tunanin yarinyar au tunda ta budi baki da shi ta buda, ko kuwa shine kadai yaren da ake mata a makaranta kuma ta kasance mai maida hankalinta wajen iyawa dan a yanzu da yawa sun amsa sunnan yan makaranta aman kuma cikin ikon Allah ko yaren da ake masu a makarantar ya zama aiki yinsa daidai, ko su yi magana mai dan tsayi da shi, a hankali ta ce" can you introduce yourself plz? " (□□ saura ku ce na yi kwabar ni ba iyawa nabyi ba ah toh □□)

Da mamaki ya karra kureta da ido kafin ya dan yi gyaran murya yana gyara igiyar cravatte din dake wuyansa yana shirin yin magana aka yi knocking

Kafin ya bada damar a shigo aka shigo
Fuskarta a hade hannunta dauke da wata leda
Da kallo ta bishi irin zaman da ya yi kafin ta kai dubanta kan Muneerath

Kayan ta ajiye mata saman table din sannan ta ajiye mata wani dan litafi mai dauke da sunnan makarantar kafin ta dora hannayenta biyu saman table din da yaren freinch ta ce" ina fatan kin fahimci wajen da kika sako kafarki, a yanzu zaki tashi ki je ki yi wanka, ki cire dukan dattin nan na jikinki , ki cenza pant da bra ga kayan da yan makarantar ke anfani da su nan ki saka, a cikin dakinki akoy turare, akoy komai

na bukata ki gyara jikinki kafin ranar shigarku saloon ta zagayo, ki fito ki same ni a wajen piscine zaki shiga mu ga irin yadda kika iya ruwa"

Shugaban makarantar ne ya ce" Aman ai ba haka aka tsaida maganarta ba ko?"

Da yannayin ladabi mai hade da jin haushin mutun ta sada kanta ta ce" Ka yi hakuri Sir, gani na yi sun mata nisa ina so ku bani damar da zan horata da sauri ta yadda zata kamo su, wannan formation din kai ka san idan mutun na wasa nan da shekarama ba zamu iya yayeshi ba bale a wata uku"

Fuskarsa ya fara hadewa dan yana son gane kamar tana da wata takakiyarta da ita ya ce" Idan bata iya ba zaki saka yar mutane cikin ruwa ta sha ruwa ne?"

Zata bashi amsar da zata yi convincd dinsa suka ji muryar Muneerath da yaren hausa yanzun ta dago dubanta sosai tana kallonsu su dukansu ta ce" Kuna magana bayan ban san ko su wanene ku ba? "

Da sauri ta juyo tana kallonta, irin yadda ta tsare su da maganisun idannuwanta masu lu'u lu'un kore mai ruwan ruwan tafki wanda yake da haske aman mai dauke da shukokin kainuwa ga gazar gazar din gashin idannuwanta da ruwan hawaye suka jika su suka yi luf su kadai suke hade junnansu sai ta ji wani irin dar dinta, aman kasancewar ta san dole ta sada mata ta mata biyaya dan itace mai gidanta a nan sai ta wani kausasa yannayinta ta kara rage tsayinta ta hanyar kuma dora hannayenta saman table din ta yadda iskar bakinta zata doki fuskar Muneerath din idan ta fara magana a kausashe ta ce" Wani irin rashin hankali ne zaki mana tambaya haka kai tsaye tsakaninki da mu baki da kunya ne? Sannan wannan ya zama na karshe da zaki yi magana da yaren hausa a cikin gidan nan idan kika kuma yi zaki fuskanci punishment "

Muneera dake zaunen nan bata tunanin wai akoy macen da zata wani yi mata ihu a kai haka kawai batama san ko wacece ita ba zata zuba mata hauka a wajen nan bayan zuciyarta a cinkushe take so take ta je ta sha kukanta na irin rayuwar da iyayanta ke gabatarwa wace bata ga irinta ba har yanzu, ace wai ta kwana biyu a wani wajen ba abinda ya dame su, bakin fuskar da basu sani ba sun zo masu da wasu zanceceku mararsa tsari dan ba sannin komai suka yi a kan maganar ba aman ba bincike ba komai suka nuna hakan ya fi masu zamanta a kusa da su, shine wannan mai sket a tsagen kusan pant a waje ta wani zo tana mata maganar ta saka pant sabo a gaban wannan gardin harda su maganar bra tsabar rashin kunya kuma ta wani fara yi mata ihu an yi hausar ba punishment ba ta yankata dan kaniya hausar ai ba ta uban wani bace! Ido cikin ido ta ce" idan fa shi kadai na iya? "

Ji ta yi kamar ta gaura mata mari, kan balaki wannan fitsarariyar ce zasu kawo mata ta hora? Ko freinch bata iya ba? Bale turanci?
Rai bace zata fara magana ya daga mata hannu ya karra kallon Muneerath dake zaune tana kallonsu kafin a nutse ya ce" Ki yi hakuri, ki je waje ina zuwa "

Kallonsa take tamkar zata hadiyi zuciya ta kuma kallon Muneerah da mugun tsanarta ta yi kwafa ta juya ta fita ta tsaya gak da kofar tana jijiga

Zama ya yi ya aro jarumta ya hade ransa sosai ya bude litafin dake gabanta yana kallonta ya ce" Kamar yadda kika san kowani enterprise na dauke ne daga sama zuwa kasa, idan na ce kasa ina nufin harta mai goge gogen gidan nan, kamar yadda a kowani gida akoy baba, mama, yaya, har zuwa auta, wanda ya dace ka yi respectin din du wanda ya girmeka haka ne....."

A sanyaye ta ce" kar dai ita ce mai wajen? "

Irin yadda ta tsakure dan tsukeken bakinta ya saka shi karra shagalta da lamarinta kafin ya tunawa kansa ko waye shi a gabanta da dan sauri ya kawar da dubansa ya ce" nine mai ja gaban wajen, nima ba wajena bane "

Ido ta kwalalo ta rufe bakinta da hannunta tana kallonsa ta ce" Wayo Allahna, ka ga da na sani da ban maka tambaya kai tsayen nan ba, kuma fa asalina ni din ba fiysarariya bace ko daya, an samu akasi ne a rikice nake na kwan biyu ban sadu da iyayena ba na san hankalinsu a tashe gashi ni sata na yi ba an rufe ni a nan....."
Sai da ta gama fada kuma ta tuna shi fa ya kunna mata abinda iyayen nata suka fada hakan ya sa ta shiga murza hannun nata tana fadin" Ba ainahin wa'inda suka haife ni ba, makotanmu "

Kansa ya gyada a dai yannayinsa na ya dauki yannayin serius Ya ce" An yi accepting dinki a wannan makaranta bayan an yi vote masu son ki zauna suka fi masu son ki tafi yawa, sai da na je da kaina na samu amanar mahaifanki kafin na zo nan, daga yanzu har zuwa lokacin da zamu yaye ku a nan zaki zauna da mu, ya zamana dole a gare ki ki girmama du wanda yake gidan nan shima kuma zai girmama ki komai karantan shekarunki dan kece mafi karama cikin yan uwanki, ya zama wajibi ki bi du wani dokoki na gidan nan dan ki samu zama lafiya da masu koyar da ke harma ki samu fitowa a cikakiyar HOTTESTE "

Da wani irin madaukakin emotion tana kallonsa ta ce" Kana nufin kun yarda zaku bani formation? Wa ya biya min? Wa ya saka ni? Wayo Allahna"

Irin yadda madaukakin farin ciki ya bayana a fuskarta ya tsaya kallo ko amsa bai bata ba, lokaci daya ta mike tsaye da hannunta tana nunawa ta ce" Ka ga na iya ruwa, na iya turanci kadan kadan, bana fada, bana sata ko daya walahi"

Stilll dai kallonta yake yadda take kai kawo da doguwar rigarta tun ta ranar ita ce bata cenza ba ta juyo ta yi takwaf takwaf da fuskarta ta ce" Matsalar daya ce ban iya girki ba, na yi na yi na kasa iyawa, ko tea ban iya hadawa ba, dan annabi kar ku koreni dan wannan"

Idannuwansa ya lumshe haka kawai yarinyar ke kashe shi, motsinta komanta ke haukata shi, a hankali ya dan karra bubuga byronsa yana son aro nutsuwa dan bai dace ya jima a haka da ita ba aman kwata kwata baya son motsawa ko nan da nan ya ce"

A sha 8knd lafia na people □□□□□□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:45 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 5 □□□

GODIYA TA TABATA GA ALLAH SUBAHANAHU WATA'ALA, DUBUN GAISUWA DA FATAN ALKHAIRI YA TABATA A GAREKU MUTANEN KWARAI DA ALLAH YA HADA MU DA SU BAMU SAN JUNNA BA AMAN MUKE KAMANTA KYAUTATAWA JUNNA TA HANYAR ALKHAIRAI DA DAMA, JINJINA A GARE KU MUTANEN GIDAN DUTSE .....A DUNIYA DU WANDA YA TASHI YA YABA MAKA DA ADU'A MASOYINKA NE, KU HARDA KOKARI TA HANYAR MOTSA ACCT DINKU KUKAI MANA KYAUTA KUKA CE A SAKA KATI A YI DATA, TO BARA KU JI MAMAN JARIRI TA CE KAZI ZAMU CI ALKUR'AN □□ ....., KUN GANE, MUN GODE, BAMU DA BAKIN GODIYA SAI ADU'A A GARE KU, ALLAH YA KARRA MAKU BUDI YA KARRA RUFA ASIRI DUNIYA DA KIYAMA DA WA'INDA SUKA SAMU DAMAR SAKAWA DA WA'INDA SUKE DA NIYAR SAKAWAR ALLAHNE BAI YI BA, DA WA'INDA SUKA LULUBE MU DA ADU'O'I NA FATAN ALKHAIRI BAMU DA BAKIN GODIYA SAI DAI MU CE DA KU ALLAH YA KARRA RUFA MAKU ASIRI DUNIYA DA KIYAMA AMEN.....MR SPECIALLY AMINENENMU, DA ALEESA DA SUKA JAGORANCI WANNAN CONTRIBUTIONS, DA SISINA MAH SISI, HAJIATA, SISINA SIS BILKISU KANAR DA TA CE SAI AN AMSA AKA KUMA AMSAR DAN TA ISA, SAI MARUBUTAN DA SUKA NUNA FARIN CIKINSU HAR SUMA SUKA ZUBA DAN KARRIN KWARIN GWUIWA DA TAYA MU MURNA, DA MAS7 HALIN DATAKON BAYIN ALLAH DA SUKA ZUBA SUKA CE A BOYE.....ALLAHU YA BARMU TARE, YA SA SOYAYAR DA MEKE YIWA JUNNA DOMIN ALLAH CE WACE ZAMU SAMU KYAKYAWAN SAKAMAKON A RANAR KIYAMA AMEN..... DAGA BAKIN MAMAN JARIRINA WARAI SAMIRA HARUN...DA NI SAJIDA KULEY DAN BUZUWA MUNNA MASU YI MAKU FATAN ALKHAIRI DA ADU'A TA DARAJA DA FATAN GAMAWA DA DUNIYA LAFIA AMEN

Sosai ya ari jarumta dan ya iya tsare dukkan yannayin da zai nuna mata da al'amarinta na neman saka shi a hali na tunani ya ce" Zamu koya maki a nan"

Ajiyar zuciya ta sauke sai kuma ta karra rage muryarta sosai ta ce" Ka ga ita wannan din me yasa ta cika fada? Ni kuma tunda na ganta da sket a tsage uwa karuwa na ji bana sonta"

Dan gimshewa ya yi ya yi gyaran murya ya karra hade fuskarsa sosai ya ce" Yanzun na gama ce maki dole ki darajata, kina so mu fitar da ke a nan ne? "

A hankali take girgiza kanta ta matsa ta yi tsaye tana kallonsa

Mikewa ya yi yana sauke ajiyar zuciya a boye kafin ya juya ya bude ya mata umarnin ta shigo

Tunda ta shigo take son gannin wani abin da zata ce Muneerath ta mata aman bata ga komai ba, hasalima tunda ta yi tsaye a gabanta da yaren freinch tana yi tana jefo turanci a ciki tana mata bayanan dukan abinda ya zama wajibi ta kiyaya kanta a sade tana gyada mata kai cike da ladabi har sai da ta gama sannan ta bata minti talatin dan ta je ta kimtsa jikinta ta dawo

Kayan ta dauka cike da ladabi ta tambayi inda zata je din?

Shi dai yana jingine da garun yana kallonta, nan ta yi gaba ta ce ta biyota

Sai da ta dan dago ta saci kallonsa kafin ta bi bayanta jikinta a mace aman a kasan zuciyarta cike take da yannayi biyu masu karfin gaske

Farin ciki da murnar sabon al'amarin da ya sameta sai kuma yannayi na rashin jin dadi na irin yadda iyayenta suka banzatar da ita, aman kuma idan ta tuna ta fara taka matakin samun dogari sai kawai ta kawar da kai ga dukan damuwarta ta fawalawa Allah komai

A haka ta sadata da dakin da zai kasance nata har barinta a gidan baki daya
Dakin dauke yake da bed daya madaidaici, sai wrdrb da wani irin sif dauke da kayan kwaliya bitjik, sai madubi tafkeken gaske wanda zaka iya kallon kanka a ciki
Dubanta ta maida wajen bayin a hankali ta karasa ta shige da adu'ar shiga bayi a bakinta
Tsayawa ta yi tana kallon yadda bayin ya hade, ba wani mai girman a zo a gani bane aman irin tsarin da aka bashi ya isa ya birgeta duba da nasu bayin na gidansu yadda yake
A bayin kama daga abin wanke masai, da su Hypo da clean, da tsintsiyar wanke bayi, da soson wanka da broch da maclean , da sabulun wanka da na wanke gashi, da abin wanke kafa da abin aske gashi, da su abin jona turaran ruwa da na wuta kusa da soket dinsu
Komai a kilace yake harta da tawul kwaya biyu a ninke suke

A hankali ta idasa shiga tana karra bin ko'ina da kallo kafin ta gyara tsayuwarta ta kai dubanta wajen kayan wanke bayin, ba wani dati gareshi ba, aman haka ta maida hankali da gagawa ta shiga wankinsa, tana yi ta jona abin turaran ruwan sannan ta ci gaba da aikinta

Sai da ta gama tas sannan ta dauko tawul din masu dan girma ne dan zasu iya kawo mata cinyarta idan daurin kirji zata yi da su
Su dinma wanke su ta yi tas da hannunta bata saka su a washing machine ba ta shanya su a igiyar da ta gani duda ta cika da tunanin ta yaya zasu bushe a haka duba da nauyinsu da kuma yannayin wajen a dan matse ba iska bale rana

Daidai da pant dinta sai da ta wanke shi da rigar da ta cire tas sannan ta zuba ruwa masu zafi a bokicin ta dauki soson wanka sabo ta saka shi a ciki, harta da brush din wankin bakinta da macaji sai da ta dafa su da ruwan zafi kafin a gagauce ta yi wanka ta wanke bakinta sosai kamar wace zata dawo fara haka ya dirji fatar jikinta sannan ta ringa sanda dan fitowa domin ta wanke komai nata ta shanya bata sanye da komai a jikinta

A hankali ta bude ta leko kanta gashin kanta na digar ruwa ta dududba sosai, gannin hajiar dinkim ta yi waje ya sakata fitowa da sauri tana adu'ar fitowa a bayi a zuciyarta ta nufi kayanta
A gagauce ta saka suturar da aka bata cike da mamakin yadda ta rike mata jikinta taf bale wandon shi ya fi kamata du irin fadinsa ya rike mata kugu taf aman kuma na kaushu ne domin jayuwa yake sosai sai dai wata irin kunya ta sakata ja ta tsaya tana karra bin jikin nata da kallo tamkar zata fashe da kuka a bayane ta ce" Anya kuwa zan iya da matsalar fitar da tsiraici? Dama zasu amince min su bani wa'inda suka fi wannan girma da sun taimakeni"

Gashin kanta ta kama ko bushewa bai gama yi ba ta hade shi sosai ta dunkule shi cikin ribom ta masa dauri kamar na huhun goro sannan ta dauki dan kwalinta ta yi jeka ka dawo da shi ta daure kan nata taf kafin ta ringa sauke ajiyar zuciya tana kallon madubi sai kuma da sauri ta kalli agogo
Idannuwanta ta zarro dan ta karra mintunna har ashirin da bakwai a kan wanda aka bata.....
11/14/21, 12:46 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 6 □□□

Da sauri ta saka slifas dinta ta yi waje , da sauri sauri take tafia tana dube dube, sai dai bata ga kowa ba sannan bata jin maganar kowa

Turus ta yi gannin wani gabjejen soja a gabanta , cikin daure fuska ya ce da ita ta biyo bayansa

Sai da ta yi dan jim kafin ta bi bayan nasa cikin sanda dan tana tafe ne tana tunanin idan fa ya juyo ya jibga mata dukan mutuwa? To ita bata ga alamun daria ko fara'a a tare da shi ba ko dai wani ya zage shi?

Sai da suka yi tafia mai nisa kafin su bayana a wajen da take hangen alamun ruwan sweeming pool

Sai a lokacin ta fara jiyo magana kasa kasa ba sama sama ba, sannan ta fara hango ikon Allahn

Gaba dayanta ta idasa bayana a wajen a lokacin da suke tsaitsaye

Zuwanta ya zamanto suma sun juyi sunna kallonta cike da mamakin wacece wannan kuma?

Gaba daya ta sare, gaba daya ta ringa jin wani abu makamancin sagewar gwuiwa da tsoro kasancewarta a gaban yan matan nan, yan matan tamkar wa'inda ke rayuwa a kasar kankara, mulmulmul fatocinsu suke kuma ba bak'ar fata a cikinsu dan ko mai duhunsu banasaria ce a kusa da tata fatar, irin shekin kuma da suke zai nuna maka koda a nan din ana basu gyara cen dama y'ayan hutu ne

A hankali ta kai hannayenta wajen kirjinta ta rungume tana kifta ido tana kallonsu

Atu ce ta yatsina fuska kasa kasa ta ce" Wannan fa mai sanye da irin kayanmu? "

Kafada Humaira ta guada itama ta kuma juyowa tana karra kallon Muneerah

Muneerath kuma kallon suturun jikinsu take, su dukansu sun saka kayan shiga ruwa ne irin yadda ake gwadowa a tv bakaken fatar ko nasaru na sanye da su, watau dai pant da bra, kowace tamkar cikinta zai hade da bayanta , kowace gashin kanta a fili da mai gashin da mai kurkur din kan ya sha gyara sai kyali yake yana karrawa

Kasancewar basu sanma da ita a gidan ba, dan ko ranar da ta diro an mayar da su dakunnansu ne an rurufe su an basu damar yin kalo ko au shiga internet su yi dube dubensu ba'a fada masu dalili ba, su dai an gwada masu cod Red an zanna masu kurtun ba zasu fito ba, hakan ya sa a yanzun da suka ganta sai suka ga kamar daga sama dai? A sanninsu an rufe dauka ai

Matsowa ta yi ko a yanzun dai sket din ne tsagage in ji Muneerath ta tsaya tana fuskantarta ta ce" Ki gabatar da kanki! "

Muneerah ta hadiyi wani yawu mai nauyi a makogwaronta a sanyaye ta ce" ASALAMU ALAIKUM "

su dukansu , baki daya taronsu ta kasa samun wace zata amsata, saima kallon kallo da suka shiga yi sannan su sauke dubayansu a kan AMEERAH wace take uwar gidansu

Gabanta ne ke faduwa da tsoron yannayinsu dan bata saba mu'amala da abokai ko yan makaranta da irin shiga haka ba, sannan ta gama yanke humuncin ba musulmai bane baki dayansu duba da salama ta masu ba wace ta iya amsata saima wani kallo da ta kasa gane na mamakin gannin bak'ar fata ne suke ko na kaskanci?

Murmushi Ameerah ke yi a kasan zuciyarta tana ayanna 'zaki fita ne da kafafunki, dan ko su basu ga irin fatarsu ba, in ba wulakanci irin na PPM (Shugaban kare yancin mutane) ba meye na wani dorawa da dafawa sir a dauke ki rana tsaka ko iliminki bamu tantance ba sai wani tuwon takashi dake rinjayarki ta yaya zaki iya kula da manyan mutane na jirgi? Wani kampani nema yana kallon yan matan nan namu sala sala zai dauke ki? Tun daga yanzu zan shaka maki azaba ta hanyar saka ki a cikin ruwan nan ke kadai!'

"Amen wa alaiki salam" wata siriryar murya ta amsata tana tahowa daga gefe , ita dinma sanye take da pant din da bras din sai dai ita ta saka wani dan kwali ta daura a kugunta ba daga ita sai pant din bane, duda wajen daga su sai su aman ita din tana daure da shi ne

Haka kawai Muneerath ta ji sanyi harda sauke yar ajiyar zuciya tana kallonta, ita dinma ita take kallo kafin itama ta kai dubanta wajen Ameerah su dukansu sunna jiran karrin bayani

Ameerah ta gyara tsayuwarta ta gabatar masu da ita a matsayin daya wace zata kasance a cikinsu ta amshi horo tare da su, sannan sunnanta Muneerah ta yi rashin lafia ne ya sa bata zo a kan lokaci ba

Da tsaftatacen faransanci ta masu bayanin , ba turanci ko daya a ciki hakan ya sa kowace ta gane bayaninta, da yawansu nan suka juya suka shiga harkarsu, su dai basu mata oyoyo ba, kuma basu nuna alamun ta gaje masu waje ba dan kuwa suma zuwa suka yi kuma ko dari aka karro basu da yancin hannawa

Wasun kuwa kawai kallonta suke yannayinta bai masu kama da yar gayu ba, kwata kwata irin shirin nata bai dauke su ba duda suturar dai iri daya ce aman sakatama iyawa ne, ga kuma dauri da ta daure ta matse kai

Hannun da yar budurwar nan ta miko mata tana murmushi ta ce" I'm Saudat Muhammad frm Arlit , nc to meet u Muneerath "

Muneerath ta lumshe idannuwanta kafin ta saki sansanyan murmushi a hankali ta bata hannun itama muryarta cen ciki ta budi baki zata yi magana Ameerah ta ce" Gaishe gaishen ya isa hakanan, oya ki zo ki shiga na ga yadda kika iya ruwa kafin mu je bangaren girki "

Sai da gabanta ya yanke ya fadi da ta ji maganar girki, aman kuma sai bata nuna komai ba, jikinta a mace ta kalli irin shigarsu cike da tunanin wai a haka zata shigan ne itama ko yaya?

Bata dai tambaya ba sai ji da ta yi kafafuwanta na neman makata da kasa domin gaba dayansu dakatawa suka yi da abinda suke yi sunna kallonta, ciki kuwa harda wa'inda suke kai kawo da wani zungureren takalma a kafafuwansu sunna wani irin laudi sannan su dauki tafiyar gagawa duka da takalmin da ta yi imanin idan ta cira kafarta a samansa sai ta karya kugu kafin cinya a gangaro gwabri da tafin kafa, kai harta da wanda ke cikin ruwan sai ta kama karfe kawai ta hau hawa har na uku ta fito sosai itama tana kallonta

Yawu ta hadiya, rana jin kamar ta je ta kama hannayenta ta ce da ita'ki rufan asiri mana na shiga daga ni sai ke?' Sai dai ta kula wannan mata ba mai rufa mata asiri bace

Kasa kasa saudat ta ce" ko baki iya ruwa ba?"

Juyowa Muneerath ta yi da sauri tana kallonta ta kasa magana
A hankali Saudat ta ce" Kar ki ji tsoron kowa a nan, yadda kika zo haka kowace ta zo, idan kina baya baya ko kina boye iyawarki rainaki zasu yi, idan kuwa HOTTESTE suka ga damarki kin bani, dan zaki zamo tamkar yarinhar aikinsu, ki daga kafarki ki shiga ruwan nan idan har kin iya iyo, duda basa daukan wanda bashi da takardar shedar ya yi cour na natation ba, aman duda haka ki nuna masu in ba haka ba harta a wajen Ameerah zaki sha wahala"

Shin ta yaya zata iya sakin jikinta da su, gaba daya jinta take bare a cikinsu tamkar ba halitu irinta ba haka take ganninsu, sun cika mata ido sannan du jinsu take tamkar ba yarenta ba

A hankali ta nufi ruwan da kayan dake jikinta, wanda hakan ya kuma saka Ameerah sakin murmushi a boye dan ta tabata in dai ta iya ruwa ba zata shige shi a haka ba domin babu picsine din da aka basu damar koya ruwa da sutura haka a jikin mutun

Sai da ta lumshe ido ta yi adu'a a kasan zuciyarta kafin ta cire slifas dinta tana kallon ruwan yadda yake kyali harma ana iya hango kasansa dan duka duka 3 mtr ne tsayinsa bayan ita ta koyi ruwa ne a wajen da bawa ba zai fadi zurfin ruwan ba sai wanda ya tara shi a wajen watau Allah
Kai ita gaba dayama sai take tsoron kar a je idan ta shiga ta ji ta buga kai da kasan nan dan kuwa a kusa kusa yake gashi irin shigar da suka koya mata ba ta a taka matatakalar a shiga cikin nutsuwa bane, na a shiga da karfi ne ta yadda za'a dira harta da ruwan sai ya yi karra ba wai kai ba

Kuma kallonsu ta yi ta ga kowace na kallonta da yannayi na son gannin me zata yi, a hankali ta juya wajen AMEERAH da ta tsareta da ido itama tana kallonta bata ce da ita komai ba

Tana kallon Ameerar, ya kasance ruwan na bayanta, ta dago hannunta na hagu a hankali ta kai wajen hancinta a bayane cen kasan makoshinta ta furta" Tawakaltu AllaLah.... "
Basu kawo haka a rayukansu ba, du jira suke ta dawo da sauri ta ce ba zata iya ba tsoro take ya mata zurfi , du jira suke ta fashe da kuka ta ce a taimaka mata kamar yadda da yawa suka yi sai a hankali suka iya shiga ruwan nan dan ya masu zurfi su ba da irinsa suka koyi ruwa ba a 2 mtr ko a 1,5 suka koya sai gashi a lokacin da su duka suke mata kallon bagidajiyar nan a ina zata ga ruwan da zata iya shiga har ta koya , ai iya ruwa a abin wasa bane ta fada cikin makeken ruwan nan ta baya baya bayan ta dan cira kafafunta ta tafi gaba dayanta wanda hakan da ta yi ruwa ya bada wani sauti Bacal.....mai karfin sauraro kafin wajen ya yi shiru domin a lokacin da ta fada ta nutse kasansa dan gannin yaya zurfinsa yake me da me ya dauka a kasansa, shin kamar ruwan tekun da suke shiga ne da kawayenta , shin akoy kifaye da halitu kala daban daban da cikin ruwa a nan ma? Shin ruwan na shiga ido ya hadasa kaikayin ido dan yar lakar dake kasansa idan suka tasheta?.....wannan nutsewa da ta yi dan son gannin ainahin tsayinsa shi ya kayarwa da kowa gaba, a zabure Ameerah ta matso kusa da ruwan lokaci daya tana kallo tana kuma bale botiran gaban rigarta sannan ta danna a bin dake cikin kunnenta da zai sadata da office din Shugaban makarantar a dan tsorace sa furuci rake shaida masa ai yarinyar nan ce ta fada ruwa da baya gashi kusan minti uku bata fito ba bata bayana ba su a hangenta da suke ta yannayin kalan suturar cikinta kamar wace ke kara shigewa kasa ne

Shi dinma a tsorace ya fice da gudu gudu da kuma equipe din dake ciro da mutun daga cikin ruwa suka nufo wajen, a lokacin yan matan du suka yi cirko cirko kowace a tsorace suka jira su ga ta ina za'a ciro da gawarta? Domin su dai a TV suke gannin mutun na iya daukan dan lokaci a kasan ruwa, kai yawancinsuma a cikin irin film din Sirene suke gannin hakan dan basu taba ganni ko ji a labari cewar mutun na iya rike numfashinsa a kasan ruwa ba, ta yaya? Ya rike numfashinsa kuma ya jima a ciki? Wannan sai SARAKAN RUWANMU NA GALGAJIYA.....sai ko wanda ya dauki lokaci mai tsayi yana faman koyon hakan

Sunna zuwa ya ringa jin hankalinsa na neman tashin da zai fara rufe kowa da fada a wajen, a hankali ya ringa rike kansa ta hanyar yin tambayoyi da hannayensa, gannin Ameerah na cire kayanta hakan na nufin tana gaf da fadawa ne

A kausashe ya ce" Kai tsaye kika sakata shiga ruwan bayan kin san baban burinta ta zamo Hottest ne ba zata yi maki gardama na shine kika sakata shiga ba tare da kin duba faiblesse dinta ba , ba tare da kin gaskata idan zata iya shigarsa ba , ba tare da kin kaita ta fara shiga wancen marar zurfin ba?"

Bakinta na rawa cike da tsoron kar dai ta kashe yar mutane ta janyowa kanta hawa media da balakin duniya baki daya da rasa aikinta da rasa komai nata ta budi baki zata yi magana a lokacin ne kuma du sun gama shiryawa dan bin bayanta sun saka abin numfashi a kasan ruwa dan a yanzu mintinta takwas har da yan sekwani a cikinsa sai dan buiiiiil dake dan fitowa jefi jefi a nesa da nesa da ba za'a taba kawowa cewar itace ke iyo da gudun nan ba , Ameerah ta budi bakinta dan ta kare kanta suka ji yan matan sun kwala ihun "Gata nan gata nan"

Da sauri Ameerah ta juyo , haka shima da sauri ya taka ya matsa yana kallon wajen da ta fito din, ta tafi cen fiye da rabin ruwan kuma bayanta suke gani gashin kanta ya warware ribom dinta da dan kwalinta sun zube a cikin ruwan gaba dayansu , bakin gashin kanta ya malalu a cikin ruwan , ruwan ya dago shi haka, kafin ta juyo a hankali tana karra kallon ruwan cike da shinfidadiyar fara'a ta jin dadin jinta kwalim a cikin ruwa, dan tana matukar jin dadin ta jita a cikin ruwa a rayuwarta
A hankali ta ringa binsu da kallo su dinma ita din suke bi da kallo, idan bata manta ba da zata shiga babu wadinnan tarin mutanen, hakan ya sa take kallonsu da mamaki sai kuma jin da take sunna cewa "Da ranta, abin mamaki, da ranta"

Idannuwanta ta kifta ta shafa kanta, sai kuma ta zarro idannuwan nata da dan daga murya ta shiga eaige waige tana karra tatara gashin kanta a bayane ta ce" dan kwalina, Ribom dina...." da yaren hausa kafin ta hango dan kwalin nata ya yi sama sosai kasancewar na raga ne , ribom din ne ya sha ruwa ya yi dan kasa kasa domin baya sama
Tsayin da dan kwalin yake akoy nisa kadan, kafin su ankara ta nufi wajen tana wana kafafuwanta da hannayenta ta kwaratiyar kwarewar iya ruwanta har ta idawa wajensa ta kamo shi ta rufa a saman kanta tana karra kallon mutanen da yar yatsarta ta nuno masu ta dan daga murya ta ce" Minti daya zan dauko ribom dina "

Bata tsaya ta ji amsa ba ta yi kasa abinta, a tare suka kalli junna da ameerah da Sir

Ameerah zata yi magana ya girgiza mata kai ya mata nuni da su je sannan ya salami wa'inda zasu bita cikin ruwan ya rage daga daliban sai ita suma sunna jira ta fito sun yi cirko cirko aman a yannayin fuskarsu yannayi ne na mamaki da sakin fuska

Bata jima irin na dazu ba ta samo abinta ta fito, tana fitowa ta nufo su ta kama katangar tana kallonsu

Wata mai sanye da wani tsohon kashi na punichment wato symbol wanda kana yin hausa za'a rataya maka shi du inda zaka shiga da shi zaka shiga gashi har wani dan wari wari yake na wuya du dan ka daina yin hausa ta duko tana dariya ta rataya mata da yaren freinch ta ce" Muna maki oyoyo a gidan HOTTEST"

Gaba daya suka saka ihun daria wanda sai da ta zabura sai kuma ta kura masu ido ta ga sunna ta daria, a hankali ta ji wani farin ciki da murmushi na wanzuwa yun daga cikin zuciyarta har saman fuskarta

Du zama suka yi a waje ruwan kowace na jefo mata tambayar a ina ta koyi ruwa, a wani club aka koya mata, waye ya koya mata dai da sauransu.....

Kallonta yake tana kai kawo kafin ta tsaya, har yanzun hannayenta rawa suke muryarta na rawa ta ce" Baka tsorata da irin iya ruwanta ba? Wa ya aikota? A ina aka koya mata ruwa? Wai shin anyama mutun ce? Iyayenta da suka nuna halin ko'in kula da kasancewarta tare da mu su suka haifeta kuwa ko kuma an saka su nuna su suka haifeta ne?"

Rai bace ya ce" Ya isheki haka, zaki rufe min tabarmar kunya da hauka ne? Yau da wani abu ya sameta na sakakinki ko tsanarta da kika dorawa kanki ta dalilin da ban ko na meye ba me zaki ce?, kina da bakin kare kanki ne ko zaki ce baki san lokacin ba ? Da kin ja ba kalacin ke ba ni kaina an maka ni a kaso na sakena da na yi na baki amana a kan y'ayan mutane! Nan fa ba filin daga bane, ba filin tsanar junna bane, ke kin san yanzu aka fara idan an saka su dakin da jirgi yake yaya kike tunanin koyar da su aikin da ya fi wannan tsauri?, idan kin nuna iyayenta an fada masu su ce su suka haifeta mutanen anguwa da makarantar da ta yi da doguwar takardun tarihin makarantun da ta yi da kawarta dake kuka na jin ana bincikarta duka mugayen da suke son cin mana ne suka tsara haka?.....ina gannin kin fasa tunani da kwakwaluwarki sai da kanki!"

Rai bace ya barta nan tsaye ya koma wajen computer dan karra bincike a kan lamarinn Muneerath~~~~~~~~~~~~

_____

Girgizar da jirgi ya yi da shi ya saka shi karewa jirgin kallo a lokacin da ya samu kafafuwansa a kasa a baban birnin garin da mahaifinsa yake sarki

Da sauri ya saka hular rigar darin dake jikinsa dan ya kare kamaninsa dan kar a gane shi a masa caaaaaaa gashi tafiar ba zata ce au kansu sai sun duba zasu ga harda shi a cikin jirgin da ya kawo pasingern yau ba

Idannuwansa ne suka sauka a kan wani datijo yana tafia a hankali, tafiar irin idan ya cira kafarsa guda kafin ya cira dayar sai ya jima kuma a dukan yannayin tafiarsa zaka gane cewar a wahalce yake yinta

A hankali ya dan girgiza kansa ya juya ya fita kwata kwata ya tsayar da makekiyar motar da ake taxi da ita a kasar ya yi bayanin wajen da za'a ajiye shi domin taci bata bin hanyar palas

A hankali ya jinginar da bayansa ya ciro blok note dinsa da byro ya bude a shafin ranar ya rubuta da manyan harufa kamar haka....." *ASHE KO BABU MUTUWA, TSUFAMA AYA NE* ", rubutun ya kurawa ido yana kallo kafin a hankali ya rufe ya rufe golding brnsa ya saka a gaban aljihun wandonsa ya dauki karamar wayarsa ya danna kira ya karra a kunnensa a sanyaye ya ce"

□□□□
11/14/21, 12:46 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 7 □□□

A sanyayan da yake tun jiya haka ya yi yar gajeriyar magana ya kashe yana kallon makeken titin baban birnin ingila har suka karaso daidai wajen da yake son sauka

Budewa ya yi ya fita ya shiga makekiyar motar da aka zo daukansa da ita wadda wani soja ya bude masa mai sanye da kaki irin na masu gadin gidan sarautar

Mai taxi din baki hangame yake son gane wai wa ya dauko? Sai dai ina yana kallo aka miko masa kudin da ya tabata ko a wata da wuya ya kama su kafin motocin su ringa tafia har sai da mota biyar ta wuce a gurguje kafin ya sara da hannunsa yana fatan prince dinsu ya gaji babansa dan akoy kyauta sosai

A gajiye yake, sai dai burin ya gansa gashi gasu ya hanna masa jin gajiyar

A hankali ya saka lalausar kafarsa cikin wawakeken falon da wani sojan ya bude masa bayan ya sara masa da yi masa welcom

Idannuwansa lumshe suke sai dai dubansu a kan mahaifinsa yake

Sanyin falon ya yi yawa sosai, hakan ya sa ya fara zarcewa wajen farin gilas din ya dauki remot din AC din dakin su biyar du ya kashe su

A hankali ya karasa yana kallon kan mahaifin nasa da ba gashi ko dis a sama, daga bakin lokacin da gashinsa ya fara zubewa ya daina barin komai kankantarsa a kansa,

daga bayama sai ya daina fitowa ko kadan din ya zamana kan taltaltal ba gashi duda tarin gashi irin na baturen mutun

Hannun da mahaifinsa ke miko masa ya bi da kallo kafin gaba dayansa ya kai gwuiwoyinsa kasa ya kama hannayen na mahaifinsa yana kallon fuskarsa a hankali ya saka tasa fuskar a tafin hannayen mahaifinsa

Ajiyar zuciya mahaifin nasa ya sauke, cikin yaren turanci ya ce" Yaya zaka kashe min sanyi ina shan dadina bayan ka san bana jure zafi ka barni na mora kafin na je wajen da ban san ba shin sanyin irin mai daskarar da jinni ne ya daskarar da zuciya da kuma kwakwaluwa ko kuwa tsananin zafi ne mai zagwanyar da fata da hanji da tumbi....." da sauri ya yi shiru da maganarsa sakamakon jin ya matse masa kafarsa da dan karfi

A hankali ya ce" Zaka karya ni kai"

A hankali Hanja ya dago kansa yana kallon fuskar mahaifinsa, bai dauko kamarsa ba aman ya dauko jinninsa, kakarfan jinninsa ya dauko, irin jinnin nan da baka kama da mutun aman ana ganninka za'a ce wannan mahaifinka ne ko danka

A hankali ya ce" Ka daina fadin irin haka "

Mahaifinsa ya kama fuskarsa mai dauke da madaidaicin saje aman bashi da gemu ya ce" Lokacina ya zo yarona, yaushe zaka yarda ka dauki hakuri kamar yadda na dauka"

Idannuwansa ya karra rintsewa muryarsa cen ciki ya ce " Dan ko a da baka son kanka kamar yadda nake sonka"

Murmushi ya yi masa yana kallonsa kafin ya kara rike hannunsa murya cen ciki ya ce" I'm sorry "

A hankali Hanja ya dora kansa saman cinyarsa ya rintse idannuwansa, shin yaya zai kwatanta rauninsa a gaban mahaifinsa? Yaya zai kwatanta irin yadda yake jin zuciyarsa zata tsaya sakamakon zafin da yake ji? Gashi a gabansa ya zo, sai dai ji yake a yanzu ya fi jin tamkar bashi da lakkah a jikinsa baki daya jikinsa ba wani karfi, irin wannan yannayin yake saka shi guduwa sam baya son fuskantar mahaifin nasa, irin wannan sensation din ke saka shi gudun dukan abinda zai hadasa masa bugun zuciya, ina zai iya a girman jikinsa ya zauna yanna kuka? Idan sautin muryarsa ta fito yana gurza kuka ai sai ya tsorata du wani na kusa da shi ta ina ake so abin ya fara ne?

Idannuwansa ya lumshe sakamakon jin lalausan hannunta a cikin gashin kansa mai baiwar baki da santsi da sheki
A hankali ya karra lumshe idannuwansa jin shashekar kukanta kafin ya ji tsugunninta a kusa da shi sai kuma ya ji ta janyo kafadunsa daga jikin mahaifin nasa ta kawo shi jikinta
Duda irin yadda ya girmeta sosai a haka ya karasa jikinta sosai duda ba shine ya rungumeta dan kuwa a cikin kirjinsa take sosai kafin a sanyaye ta ce" Cry, cry bab"

A hankali ya karra rungumarta sosai yana jin hawayen idannuwansa na zubowa, kamar jirra hawayen nasa suke ta yi magana su bale, sun balen kuwa domin nan da nan ya jike mata wajen wuyan abayar dake jikinta da hawaye masu dumin gaske, idannuwansa suka kade sukai jajajir da su sosai

Mahaifinsa kansa sai da ya share hawaye cike da kaunarsa a kasam zuciyarsa, shi walahi a yanzu zai iya rantsewa cutarsa ta daina damunsa kamar irin yadda yaronsa ke tsaye masa a zuciya da kuma matarsa

Hannunsa ya saka daga zaunen da yake ya janyo su jikinsa shima a hankali ya ce" Sai nake gannin kamar muna so mu nuna bamu godewa Allah ba, bayan kune masu taro mutun ku ce ya kasance mai tawakali fa?"

Ajiyar zuciya Hanja ke saukewa kafin ya dago dubansa ya sauke a fuskokinsu, dan murmushi ya yi irin mai ciwon nan sannan dan ya saka su murmushin suma ya ce" Kai jan mutun bai yi ba kun ga yadda hancinku ya yi jajir?"

Daria mahaifinsa ya saka marar sauti kasa kasa yana doke kafadarsa ya ce" Kai ka ga yadda ka jeme?"

Aleesa kam bata iya yin dariar ba sai kawai ta karra barkewa da kukanta wanda ya saka HANJA tashi da sauro ya shiga tsakaninsu ya kama hannunta da na mahaifinsa a hankali ya ce" Mah, kin ga abinda ya sa bana zaunawa da ku, kin ga abinda ke tayar min da hanlali kennan har nake neman fada da shi mu yi na tsere, Mah yaya kike so na yi idan kina min kuka haka? Bana iya hakuri na jure jin kukanki a kunnayena, dan Allah ki yi hakuri ki ji wani zance"

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:46 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

1 □□□ 8 □□□

A hankali ta ringa sasautawa har ta daina gujin kukan hakan ya saka shi sauke ajiyar zuciya yana dan murza hannayensu su dukansu ya ce" Nawa suka warke masu dauke da ciwon nan? Shi likitan da wa suka tara sani da har zai yanke ranar mutuwar mahaifina?"

Da dan fada fada abansa ya ce" Ba wannan zaka yi ka birge ni ba HANJA, abinda nake so da kai shine ka ajiye tukin jirgi! Kai direba ne? Me aka yi aka yi aikin tuka mutane a lokacin da suke barci sunna shagalinsu? Ka kuwa san irin darajar dake tare da kai? Allah ne ya darajaka, ya baka damar da za'a yi maka biyaya, kai za'a tuka kana barci ko kana farke, kai za'a amsa kiranka a duk lokacin da ka yi gyaran murya ko ka so, aman ina kana zaune kaine ka zama abin gani ga kowa? Kaine ka zama abu mai arha ga kowa? Abinda nake so da kai ka ajiye jirgi, ka ajiye mata ka samu mace daya kwakwarar da zaka iya zama da ita, kai idan kana so ka dauki hudu ka zuba a inda kake so HANJA ka nutsu ka dauki mulkin da yake naka ka ja ragamar kasata! Hakan shine zai sa na je makwoncina cikin salama!"

Hanja ya cije lebensa na kasa kafin ya dago yana kallonsa ya ce" Meye a ciki dan ina tukin jirgi? Haramun ne dan ina dan sarki kar na yi tuki? Kai ka san bana son mulkin kasarka , ka ba dan uwanka mana? Ka maida sarauta gidan dan uwanka menene a ciki? Ko daga kasar nan muka fita zan iya yawon duniya da mamana na bata kyakyawar kulawar da ya dace da ita!"

Aleesa muryarta a sanyaye ta ce" Zaku fara ko? Fadan ne zaku fara ko? Maimakun mu yi zaman lafia ba zaku iya jimawa ba sai kun yi kau? Huby ba mun gama maganar aikinsa ba? Yaya kake so mu yi bayan aikin nan ya tashi ne yana hade haden abubuwansa? Lamarinsa da jirgi ya zama baban lamari mai ban mamaki, shi ba za'a ce jinnu ke bashi ba shi ba aljanin kansa ba, ka manta tun yana da shekara nawa ya gwada tuka jirgi? Ka manta irin faman da muka yi a shekarar da ka hanna shi tuka jirgi? Ina so mu fahimci junna bana son rigima dan Allah....." ta karashe maganar muryarta a sanyaye tana kallonsu su dukansu kamar ba yanzun suka gama kukan kaunar junna ba shine har zasu hau sama su fado dan kawai rigimar da basa gajiyawa da yinta

Ajiyar zuciya Hanja ya sauke ya kara lalubo hannun mahaifinsa da shima jikinsa ya yi sanyi, muryarsa a sanyaye ya ce" Ba mamaki ni da ake yiwa kallon mai lafia na rigayeka shiga kabarina Papa"

Kallonsa ya yi da sauri hakan ya sa Hanja sakar masa murmushi ya ce" Mutuwa yanzun ta zama lafia lau ka ji an ce mutun ya mutu, idan lokaci ya yi za'a mutu koda ba'a shirya ba, idan lokacin ne ya zo ko ana barci za'a mutu ne, ko ana tsere a doki za'a mutu ne, bale masu hawa abin hawa....."

Yanzun kuwa Aleesa ce ta masa kallo irin na ka tausaya min ka daina maganar nan, aman bai daina ba ya ci gaba da fadin" Mun kasance musulmai ne mu, hakan ya sa muka taki baban sa'a ta rayuwa ta imani da daukan komai daga Allah ne, Mutuwa hutu ce ga mumuni, sannan bawan da ya kasance mai kare dokokin ubangijinsa ne, mai jin tsoron Allah a badininsa ba wai kawai a bayane ba aman kuma a cen cikin zuciyar ba haka ba sai ka ga bai kasance cikin annabawa ba aman kuma kasa bata ci namansa ba, nawa ginni ya biyo ta kansu aka tono su kamar yanzu aka birne su? Papa ka kasance mai kamantawa, kana bayar da sadaka da hannunka na dama ba tare da na hagun dinka ya sani ba, kana ta yakin yada adinin musulunci a kasarka ba dare ba rana, ka gina masalatai, ga gina rijiyoyi, ka gina gidan marayu bila'adadin a kasarka, kai din mai lazumtar Suratul *Mulk* mai falala ce, kana karantata ba dare ba rana wace ko ni nan kai ka sabar min da karantata maimakun zancen zuci sai na yi nisa a ita nake gane ita nake karantawa, wace idan bawa na karantata bale

idan ya zo kwonciya kabarinsa zai kasance yana wani irin kanshi koda yaushe kanshin nan yana nan, sannan tana taya ka hira a cikin kabarinka, tana cikin surori masu ceto, koda yaushe tana tare da kai Papa, Papa ko kana aikata wani aiki a boye ne mumuna wanda ya dace mu fito da shi mu zanta a kansa? "
Ya karashe yana tsatsare mahaifinsa dake jin wata salama a kasan zuciyarsa da idannuwa

Mahaifinsa ya sauke ajiyar zuciya ya ce" Eh "

Su dukansu kallonsa suka sake yi da jiran jin karrin bayani a kan hakan

Mahaifinsa ya hade hannayensa ya ce" Laifuka bawa na aikata su a ko wani motsinsa, sai dai ina astaghfari a kowani motsin nawa, baban laifina Hanja shine na kasa hanna ka baban zunubi a cikin zunubai, an ce idan mutun ya mutu in yaronsa na aikata laifi za'a tashe shi a nuna masa, shin yaya zan yi da tashina da za'a ringa yi ana nuna min kai kana aikata ZINNA?"

Idannuwansa ya lumshe cike da jin kunyar maganar, kafin a sanyaye ya ce" Na san zan daina, dan ina kokarin son gannin na daina din Papa....."

Aleesa ta sauke ajiyar zuciya tana dai kallonsu

HANJA ya hade hannayensu a hankali ya ce" Zan daina aikata zinna in sha Allahu, ba zan dauki alkawarin na daina ba, aman zan kasance mai tuna nasihohinku a duk lokacin da hakan ya nufo ni, kuma zan tuna azaba da bin bashi irin na zinna na tabata in dai a hankalina nake zan hanna kaina aikatawa"

Murmushi Aleesa ta yi tana jin sanyi har a kasan zuciyarta kafin ta mike ta nufi wajen table din nan na gilas ta kunna AC dan har zufa take ita ta dawo ta zauna wajen da suka ci gaba da tataunawa

Cen Hanja ya bushi iska ya ce" A yanzu burina shine na zaga duniya da ku, zan debe ku mu tafi yawon kasashe da ku, ina kuke son zuwa? Ina da ina?"

Murmushi mahaifinsa ya yi cike da jin dadin irin yadda yake karra dauko jarumta yana yafawa kansa ya ce" Baban burina shine na ga aurenka, na biyu na je saudiya na jima ina bauta, na uku na taka kasar AFRICA na ga namun daji...."

Aleesa na yar daria kadan kadan ta ce" Yeah, ka kuma min alkawarin zaka kaini ka hauda ni Giwa"

Shima da yannayi na farin ciki ya ce" Eh ban manta ba, da kuma....."

Hanja dake kallonsu cike da kaunar iyayensa a sanyaye gannin karfi da yaji su so suke su nuna masa sun fa sakar basu da wata damuwar a ransa yana ayana ba Africa ba , ko kudus idan kafa na takawa zan kai ku, a bayane kuma ya ce" zamu fara shiga Africa, mu je ka ga dukkan abinda kake so, akoy jirgin da zan ja nan da sati uku zuwa Africa, in sha Allah zamu je tare , yanzun Ku tashi mu yi sallah, lokaci ya yi....."

Kwarai murnar ganninsa ya shashantar da su duba lokaci, duda ba kira aka yi ba aman sun saba da alwalarsu ake kiran, nan kowa ya tashi ya nufi bayi dan daura alwallah dan su samu sallah a kan lokaci zukatansu cike da farin cikin jin yau shine ya yarda zai fita da su.....
WANNAN kennan

.....

A kwana a tashi yau kwananta goma talatib cif a wannan gida
A wajen nan ta hadu da mutane kala daban daban masu halaya kala daban daban
Har yanzu tsakaninta da Ameerah ba wani jituwa, to da wa Ameerah ke jituwa? Bata jituwa da kowa dan dai na wani ya fi na wani ne
Rayuwarta take a nutse, tana kokarin daukan dukan horon da ake basu, duda har yanzu ta kasa yin tafia ras da dogon takalmi, ta kasa iya yin kwaliya uwa uba Girki ya gagareta, dan ko dan wulakancin Ameerah ya ci ace ta iya abubuwan nan aman cikin ikon Allah ta kasa iya su, wanda hakan ke sakawa Ameerah fadin cewa ina za'a yi zama da Hottest din da bata iya girki ba, bata iya tafia da takalmi a saman kasa bama bale a cikin jirgi? Da bata iya kwaliya ba? A yaya take so ta tsaya gaban Pasinga da katon tuwon takashi? Dan kuwa duwawunta sunna samun hutu karra bajewa suka yi abinsu, Ita kawai ta san asara ce da bata lokaci bayan wannan ina yarinyar nan ina wannan aiki mai daraja?

A haka take karra dadafawa,

A tsakaninta da daliban nan babu tsana ko bakin cikin junna dan ba wanda yake gefen mamansa ko abansa kowa kansa yake nema kowa kuma horo yake dauka, abotarta da Saudat ta zama kut da kut domin sunna taimakon junna ainun sai dai gaba daya Ameerah ta dora mata karan tsana, da tana nan da bata nan idan abu ne ita take dorawa, ya kasance kowa ya gane tsanar da ta yiwa ameerah mai yawan gaske ce

Gefe daya kuma Sir na nan, Sir ya kasance mutun mai taimaka mata sosai, ita har mantawa take cewar shine shugabansu a wajen nan dan idan waje ya kasance daga ita sai shi takan yi mamakin irin yadda yake mu'amala da ita, tana jin dadin mu'amala da shi domin har kiransa take da freind ya kuwa amsa mata cike da farin cikin tana sakewa da shi yana mutunta ta, yana mata tambayoyi kan rayuwarta, yakan kwontar mata da hankalinta, ya mara nasiha sannan ya shaida mata ta ci gaba da kokari kar ta gajiya, domin babu maraya sai rago! Walahi zai iya rantsewa rabonsa da ya ji mace har tsakiyar ransa har ya manta .....□□.....

Kamar yadda aka saba sau uku ake shiga kicin dan girki, yau asabar ranar girki ce
Gaba dayanta a tsorace take, hankalinta a tashe yake
Du sun halara aman bata wajen, tana labe ne bata fito ba

Ameerah dake tsaye sanye da wando da riga farare irin na chef da hula fara ta kalli Saudat a dake ta ce " Ina isashiyar kawar taki?"

Saudat ta sosa kanta a hankali ta ce" Muneerath ki fito mana "

Muneerath ta sauke ajiyar zuciya bila adadin kafin ta fito tana sanda ta zo ta layu da su

Ameerath ta yatsina bakinta ta mika mata takardar da abinda za'a girka ke ciki a dake ta ce" Ki dafa mana kina mana bayani"

Ido Muneerath ta kurawa rubutun cike da tausayin kanta , ita sai ta rantse da Allah bata san meye ktp ba, ta taba ganninsa ne? Wani abin takaicin wai atahugun da ake jajagawa a nan aka ce ta yanka salon ta manta ta murza ido ko ta kama ruwa ko?

Juyowa ta yi ta mikowa Ameerah takardar ta ce" Ni ban iya ba!"

Ameerah ta zarro ido , yau kam ta kai bango walahi yau ba zata iya ba, watan yarinya guda cir a tare da su aman bata iya girki ba? Rai bace ta ce" Ku biyo ni ku dukanku dakin taro! Yau za'a yita ta kare dan walahi yau sai kin bar wajen nan!"

A tare suka fito su dukansu sunna son su bata hakuri da sauri Muneerath ta sha gabanta jikinta na rawa ta hade hannayenta kamar zata fashe da kuka ta budi bakinta zata yi magana aka danna laluwar makarantar tasu
Kasin su ankara suka hango an wangale katoton get din

Kafin suke yin wani yinkuri suka ringa gannin wasu irin dakarun mutane masu sanye da kakin da a inda suke ba zasu iya cenko ko na wani gari bane , sai dai abinda suke ganni na ban mamaki ya saka su dukansu maida hankalinsu

Tarin dakarun sojojin nan ne suka layu tun daga bakin babar kofar shigowa har inda suke tsaitsaye
Jeruwa ne suka yi sunna facing din junnansu gaba dayansu ririke da wasu dogayen wukake farare tastas sannan sun hade wukaken waje daya su dukansu

Waji dankareran namiji ne ya shigo ta tsakiyarsu rike da bindiga da wani usur mai karran balaki, lokaci daya kuma SIR da sauran sojojin gidan masu nasu tsaro suka fito suka nufi wajen su dukansu a hanzarce sai dai basu karasa ba aka dakatar da su kan su tsaya a inda suke har bakin su tardo su

Zuwa yanzu sun fara tsurewa da wannan lamari, Saudat jikinta na rawa kasa kasa ta riko hannun Muneerath da ta saki baki da hanci tana ayana abin mamaki baya karewa a wajen nan ta ce " Muneerath mu gudu kar a je kashemu aka zo yi "

Muneerath ta ji cikinta ya bada wani irin kuuuuuuuuu ta juyo da sauri tana kikifta ido zata yi magana da baban abin magana aka ce" KU SADA DUBANKU, KU DUKA KAFAFUWANKU, KU KASHE WAYOYINKU, KU BADA HANKALINKU DAN KUN SAMU ZIYARAR.....

Shin waye ya zo?

Me yake shirin faruwa?

Wai yaya kuke jin labarin nan?

Taku ce yar mutan niger

Na yi mantuwa AKPI ne sunnan ba APKI ba

11/14/21, 12:47 PM - Allah Akbar: □□□□

Ameerah ce ta yi saurin kallon yan matan ita kanta bata gaskata abinda kunnayenta suka jiye mAta ba, abinda dai ta sani mutanen nan da suka fito daga cikin mota na kasarmu manyan mutane ne da haka kawai ba zasu tashi su tako su zo nan ba koda kuwa makarantar babar makaranta ce da ake ji da ita a niger baki data dan tana daya daga cikin manyan abubuwan dake shigo da gunduma gunduman kudade a kasarmu, aman abu daya ne ta sani "Prince" din ingila da aka ce shine baban ogansu a cen baban kampanin jirgin air peace, shine baban matukin jirgin da kampaninika da dama ke kokowar son gannin ya zama nasu, yana daya daga cikin masu kwakwaluwar kera wannan abu mai shegen nauyin dake tashi a sararin samaniya tamkar leda, shi din nan shine mai jiran gadon mahaifinsa, ko dan aikin gidansa ka samu gani kai din kanka ka zama cele bale shi da kansa, kai baima taba saukar da jirgi a africa ba , koda ya saukar a yanzun bata tunanin idan zai dauko passinger niger, bale har a yi tunanin ganninsa a wannan waje kamar a mafarki, kai da suma sun zama cele, makarantarsu kuwa da ta gama zama babar makarantar da a gabanan gaskiya har yan kasashen ketare zasu dauko ,

Kasancewar sunna sanye da kayan girki ne kowace wando da riga mai dan tsayi har kusan gwuiwa da abin girki a daure a gaban rigarsu da farar hula ba komai a hannayensu bale a yatsotsunsu dan idan zasu yo girki komai cirewa suke dan samuwar tabataciyar tsafta a wajen aikin abincim nasu, da dan saurin magana ta ce" kowace ta koma dakinta ta rufe ta yi connectd ta yi abin karuwa mun yi baki idan sun tafi zan kiraku mu je wajen Sir kan maganar yarinyar nan, du wace ta so rufa mata asiri ko ta yi niyar kareta dan kar na ci galaba a kanta a koreta sai dai a kore su su biyu dan na rantse maku sai na jaza maku matsalar da ba zaku taba fitar da kanku a ciki ba! Sai na maku shari da ba zaku tana samun lafia a cikin duniya ba dan kuwa sai na saka ku a ukun da baku taba zato ba! Bale ke Saudat kin san ni ma saka hannu aka dauke ki ba dan kudin papanki ya isa ba sai dan muna mutunci da shi, a yanzuma na saka ki koma masa abu me mafi sauki a wajena idan kika min rashin mutunci!"

Muneerath na kallonta hawaye aun cika mata idannuwanta muryarta a sanyaye ta ce" ke bakya taimako domin Allah? A cikinmu shin kowa ne ya iya komai yadda ake so? Da yawa sunna da matsaloli a wurare daban daban, me yasa ba zaki taimaka min na iya ba? Me yasa ba zaki talafa min na samu cikar burina ba?"

Sai da Ameerah ta yatsina fuskarta kafin ta juya rai bace tace" Dan baki yi min b.....," bata kai ga karasa maganarta ba ta tsaye mata a saman harshe sakamakon gannin abinda idannuwanta ke gane mata
Shin shi din ne da take gani a jaridu ko mai kama da shi ne? Dan bakin dan kwalin dake jikin mamansa yake gyara mata sai wata zukekiyar yarinya a gefensu matashiya da zata kai shekara ashirin da bakwai haka danma yannayin dadi ya boye yawan shekarunta balarabiya ce sak sai shinning take yi

A bayane ta shiga fadin" what? HANJA? "

Kamar a mafaki suke kallon wannan lamari, daga inda suke ba zasu iya cewa ga kamaninsa ba dan ya yi nisa da su sosai sa dai irin yadda haskensa ya kawo inda suke da irin yadda gaba daya aka aniyar kokarin kakare shi kamar wa □□ nda suke tsoron kar kuda ya taba masa lalausar fatar jikinsa sai dai ina tsayinsa ba zai basu wannan dama ba uwa uba irin yadda ya daure fuskarsa kamar wanda yake daf da fashewa da kula mai tsanani dan kuwa ba karamin takaici ya ji a zuciyarsa ba a lokacin da mahaifinsa ya matsa sai sun gana da sarkin garin harda fadi da babar murya cewa ai tun yanzu ya dace ya saba da sarakai dan kuwa babu sarkin da zai ce ya isarma kansa sai wanda ya halici sarakai, wannan shi kadai ne ya isarma kansa

A dake sannan cen kasa kasa yace □" Mah, ku koma cikin mota mutane sun yi yawa, ba wani zama zan yi ba zan amshi wata ne a nan da zata mana rakiya har zuwa cen din plz □□

Aleesa ta yi murmushi tana girgiza kanta ta ce" Tunda ka li yarda cewar ko bamu dauki wata ba muna iya ci gaba da tafiarmu nima sai ka barni na ga yadda kuke daukan yan matan cikin jirgin nan □"

Murmushin yake ya yi da idannuwansa ya zabgawa budurwar nan harara ya mata nuni da motar da idannuwansa ba tare da ya buda bakinsa ko ya yi anfani da hannayensa ba

Da sauri ta juya har kamar zata kifa ta yi gagawar shigewa cikin motar da aka bude mata tana sauke ajiya zuciya kafin ta hangi bayansa ta kura masa ido tana kallonsa

Karasawa ya yi wajen mahaifinsa, muryarsa ya rage sosai kafin yace" ya dace ka ja matarka ku koma mota sir "

Mahaifinsa ya kale shi ya tabe baki ya ce □" idan aka ki fa? "

Dan murmushi ya yi a hankali ya ce" na sanma ba zaka ki ba, ina son na gana da su ne aiki ne fa?□"

Murmushi ya yi yana kallon matarsa yadda take kallon mutanen wajen cike da admiration shima ya rage muryarsa sosai ya ce" ka ga kaunarta ta gama mamaye min kaf jinnin dake gudana a jikina, tun daga lokacin da zamu taso take cewa kafarta kafarka, kawai ku je ku yi aikin tare mana dan ba zan iya bata mata rai a dan lokacin da ya rage mana da junna ba □"

Kallon mahaifin nasa yake nan da nan ya yi kici kicin da fuskarsa rai bace yace" bamu dora dokar ba zaka ringa min maganar nan ba?□"

Mahaifinsa ya sakar masa murmushi ya ce" sorry "
HANJA ya ce" ka sha maganinka?"

Mahaifinsa ya kai hannunsa eajen gaban goshinsa ya sara masa ya ce" Yes sir "

HANJA ya dan girgiza kansa yana kallonsu suka juya suka yi gaba tare da sarkin da dogarai kama daga masu rike lema da masu tafe sunna kirari abinsu suka nufi cen ciki dan zagayen makarantar

Magana ake yi mata aman har ga Allah kunnayenta basu ji ba, a gabanta Saudat ta tsaya da sauri da murya mai amon gaske sannan tana jijiga hanayenta ta ce" Muneeraht ki wuce mu je dakin taro sun tafi sun barmu ta baya tun dazu"

Firgigit ta yi cike da zabura a tsorace da jin ihun a kanta tana kallonta ta ce □" Lafia?"

Saudat ta juya ta fara tafia tana jan hannunta ta ce" ki wuce mu je ciki kina gannin sn shige gaba dayansu!"

Biye take da ita dan janta take da sauri sauri har suka bude kofa ta baya suka sanyo kansu Muneerath tace" Saudat baki ga dogarai ba? "

Kasancewar kawancensu sun san sirrin kowace wanda take da burin aure sai hakan bai ba Saudat mamaki ba , ita dai janta ta yi suka zauna a layin kujeru na biyu dan na gaban yan matan sun cike su sai Ameerah da sir da sauran manyan ma □□ ikatan gidan da suka halarta nan da nan
Daga gaba kuwa wajen kujerun alfarma sojoji ne a tsaitsaye du sun zagaye dakin taron ta yadda idan mai rabon daukan ba dadin zara iya sauka akansa

Kasa kasa Muneerah ta ce □" Saudat, mu yi mu tashi mu je wajen su kafin su tafi dan Allah na gaishe su"

Saudat itama kasa kasa ta ce" Da alamu fadan Ameerah baya zuciyarki ko? Kina ji fa abinda ta ce maimakun mu yi tunanin abinda zai raba mu da ita lafia ke ta wani dogarim cen kike dogain banza dogarin wofi!"

Muneerath ta ce " ranki ne ya bace ban sani ba? Ki yi hakuri Saudat kin ga ameerah babu abinda zan yi na birgeta, na tabata Allahn dake tsaya min shi zai tsaya min, kuma kin ga idan freind ya ji abinda ya faru in sha Allahu ba zai kore ni ba, ni na tabata yadda na samu kaina a gidan nan Allah ba zai bada damar a wulakanta ni ba, aman tsakani da Allah shin zaki ce dogarin banza ? A da fa du wanda ya ce da dogari banza ne walahi sai infa karfina ya kare fa"

Wani irin abu da aka busa ya saka su baki dayansu tsorata kafin nan da nan a bude wajen su shigo

Shigarsa ce ta kaki irin na matuka jirgi, a yau bakake ne a jikinsa sannan galolinsa na jikinsa
Gashin kansa gaba daya baya yake dan ya mayar da shi baya , yannayinsa na ingarman namiji ya karra karuwa a tare da shi, idan ka kale shi dole ka ji gabanka ya fadi dan mutun ne tsayaye ga fuskarsa a hade take tamkar bai taba yin daria ba

Baki dayansu tsayawa suka yi, dan kuwa da hannu Sir ya masu nuni kan su mike, su din kansu sun nutsu dan kuwa nutsuwar da suka ga uban gidansu ya yi ta fi basu mamaki

Kujerar da aka ja masa bai je inda take ba, daga tsayen da yake a tsakiyar dakin taron kowa yake bi da kallo kafin yabudi bakinsa kasa kasa ya ce □ " Asalamu alaikum "

Baki Muneerath ta hangame jin ya yi masu salama kasa kasa ta ce □" Ke saudat kin ji salama fa ya yi cikakiya, ko dai musulmi ne?"

Saudat gannin ya masu nuni da hannayensa kan su zana kuma Sir ya nufo inda yake yana masa bayani da wasu file file a hanayensa Ameerah na gefe ita kanta ta wani nutsu tanamikowa sir yana mikawa HANJA sai ta rag muryarta sosai duda hankalinta ba a kwonce ba tsoron mutumen take haka kawai a zuciyarta ta ce □" Muneerath bakya karanta jaridar da ta shafi manyanmu ne?, wannan fa sarki ne kuma baban matukin jirgi ne wato pilot, sannan da kika ganshi a nan ya iya kera jirgi"

Muneerath ta mata galala da ido jin wani rainin hankali kafin takai dubanta kansa zuwa lokacin ya tsaya kikam a gabansu yana karewa na gaban kallo balema wa □□ nda ameerah ta yarda da kwarewarsu a aikin, da tsarin kyansu da komai da komai tana karra yi masa bayani
Tun daga kasa har sama ta karra debowa ta sake binsa da kallo kafin ta ji wani irin tashin hankalin da baa tana tunanin zai sameta a irin lokacin nan datake tsaka mai

wuya ba, walahi ba kowa ya cuceta ba sai Saudat da ta kaleta ta kalli wannan mai kirar yan dben yaro karamin mai taa gashi irin na yan iska, ga gunduma gunduman hannaye soja sak ta ce wai sarki, fisabililahi sarautar iskanci ta zama ko dai rabon karshen kwananta ne ya zo mata a haka a yau? Ko dai irin ta ga samu ta ga rashi ne zai idasa samunta a aikace ba labari ba, a lokacin da ta ji wannan dariar da sai an hannaka yinta take cizo ka, irin dariar nan da bata zuwa sai wajen jin kunya, wannan dariar marar mutunci da bata tashi zuwarma bawa sai ta ga wajen kumya ko wajen ya shiga uku ce ta kubce mata hade da yannayi mai karra neman fitina ga mai lafiama bale wanda yake jira a daku, ta dubi Saudat da ta ji fitsari ya faa zubo mata sakamakon gannin ikon Allah da bakar rana gannin idannuwanta da kawancenta da Muneerath ke shirin janyo masu shiga uku da tashin hankali marar musaltuwa, lokaci daya ta ji dama summa ta yi da wannan idannuwan da suka zubo maa riiiiiiiii tamkar mujiya ciki kuwa harda masu ja uwa gauta uwa uba malamin dake tsaye wanda ko uban gidansu na tsaye a kusa da shi ne jinni a akaifa shine Muneerath ta budi bakinta ta saki yar iskar dariarta a irin wannan lokacin da take bakin kofa
Bata idasa tsurewa ba ta zube kasa kan gwuiwoyinta hannayenta saman kanta ba sai da ta ji Muneerath ta budi bakinta ta cenza garshe zuwa gogagen turancinta ma hade da hausarta gogagiya da french dinta gogage ta ce" Ke lear ko? Wannan mai kama da yan damben ne sarki?"

Rabon a yi, baban rabon a yi, a hankali ta yi maganarta bata san wa ya murda waje karin volume din makogwaronta ba sauti ya fito ba Kukan da Saudat ta fashe da shi tana fadin mun shiga uku mun lalace, da irin yadda Sir ya aniya rike igoyar wandonsa wato belt tamkar wanda za zuba da gudu ya je ya zuba zawo ba, da zaburar da Ameerah ta yi ta nufo su ramta bace tana zuwa bata yi wata wata ba ta daga hannunta ta

Da kyar wollah □□
Sorry d errr typng
11/14/21, 12:47 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 0 □□□

Tana zuwa bata yi wata wata ba ta falawa fuskar Muneerath mari wace sai a lokacin ta dawo cikin hayacinta gaa dayanta ta kurawa kowa ido

A yanzun ta gama yada cewa tata ta sameta, idanma suka koreta ta komawa oga mutun cikakiya ai sun masu mutunci

A hankali ta lumsheidannuwanta daga jin yadda juwa ke neman dimata da kasata sauke dubanta a kan Ameerah tana dane kanta da daukan hannunta ta kwada mata marin idan ya so a yi wace za □□ yi dan kuwa darajar kanta ta sani ba zara kyale yar iskar nan ba

"Ya salam, me yake faruwa harda mari? Yaya haka da saurin mari a fuska waje mai daraja, Son me yasa ta mareta?" Aleesa ta fadda da muryata a sanyaye aman kuma kalamanta na nuni a hankalinta a tashe yake

Da sauri sir ya hade hannayensa biyu shima da yaren turancin ya ce" dan Allah ku yi hakuri sir, yarinya ce bata san abinda ake ciki ba aman zan mata fada sosai ita da kanta tana baka hakuri "

Ameerahma ta dawo da sauri tana hade hannayenta tace" wani hakuri zata bada? Sir yarinyar nan bata da kunya, sam bata san girman manya ba, tunda muke bata formation ta kasa koda dafa tea mai kyau ne, bata iya tafia da dogon takalmi ba, bata iya kwaliya ba, ko kitso bata so a mata sai shirme da raina mutane bayan ko sisi bata biya a nan!"

Sai da ta gama fada kafin kuma ta tuna cewa idan ruwa ne ta balo ta balo harda ita a ciki, domin kuwa vote aka yi da tawun bakinta Muneerath ke gidan, bandama wannan ba zata taba son wani abu ya samu aikin Sir ba, dan ita kanta tana zaune ne da taimakonsa domin kuwa da farko gaba suka sakota sosai

Da ido yake bin kowa, irin yadda dakin taron ya rikice kowa ka kalla sai zarro ido yake sannan du sunna nunata irin ta dai daukowa kanta ruwan dafa kanta

Bakinsa ya tabe ya kama hannun mamansa dake ta kokarin ta karasa wajen Muneerath yana karra yatsina fuskarsa a sanyaye ya ce " ina zaki je Mah? "

Mamansa ta ce" kuka fa take kana gani ta mareta kan me? Dan ta yi daria? Dama haka aikinku yake da tsauri?"

A hankali ya dawo da ita kusa da shi kafin ya juya da ita ya kaita wajen kujerar da aka janyo masa dan ya zauna ya janyota da kyau ya zanar da ita yana kallonta a ransa yana ayanna □□ ta yaya zaka iya aiwatar da aikinka idan Mah na nan, ba zata taba bari ba □□

A hankali yace" zauna bara na je na ji a kan me ta mareta "

Kanta ta gyada tana kallonsa ya sauko daga wajen ya nufo inda suke

Da hannunsa yamasu nuni kan su karra matsawa kusa da yan matan

A lokacin da suke matsowa Muneerath sai a lokacin ta ji kafafuwanta sunna neman tona mata asiri ta hanyar yi mata tawaye, domin sau uku tana gwada daga kafarta dan ta arta a guje aman sai ta ji an riketa a wajen mugun rikon da ta kasa tsawatarwa kafafun nata har suka cin mata

A dake sannan kasa da muryarsa sosai ya ce" du wata dake min kuka ta hadiye haukanta a wajen nan kar ta tadawa mamana hankali, sannan kowace ta matso sosai ku saurare ni!"

Kasancewar da ainahin inglish ya yi maganar kwararen inglish tatace a cikinsu idan ka cire sir da Ameerah sai Muneerath sai ko Saudat da ta tsinci dan abinda ba □□ rasa ba

Yana hankalce da su da sauri Ameerah ta tatabo su da hannayenta ta daidaita su, sai dai Saudat da Muneerath da kansu suka matso din suka bada hankulansu

A dakensa ya ce" ina son a bani bayani dala dala na abinda yake faruwa a gidan nan! Wani irin abu ne kuke kwabawa? Wace irin tarbiya ce kuke bawa dalibanku? Meye maganar ba sisi da kuma maganar komai baa iya ba? Ina so maganarku ta kasance kasa kasa ta yadda ba zai kai kunnan mahaifiyata ba!□"

A dake ne ya yi magangannun nan, sannan a cicire ne ya yi su, haka kuma tsayuwarsa ya yi wace zata kare Aleesa da gannin komai, haka kuma yana yin maganar ne yana karra dunkule hannunsa dake nuni da da ace babu wani shigen dake hanna masa rawar gaban hantsi da koda bai iya ashar ba da an ji duka irin mai gigita bawan nan

Sir ne ya dauki magana da sauri sauri da inda inda kafin ya karasheta yana mai sadda kansa cike da firgicin ranar da nan da Muneerath ta aikata aikin nan, zai iya cewa a yau ya yi nadamar kafafiyar zuciyarsa da ta nace kan sai an dauketa, shi din da kansa ya san ya gama yawo

A kausashe ya ce" wani irin banzan zance ne kake fada min haka? Baka ga takardunta na shaidar ta yi karatun girki ba, baka ga na shaidar ta iya ruwa ba, a kasashenku da ake kawo maku hare hare, idan har da gasken turota aka yi ta ilata ku?□□

A sanyaye ta budi bakinta ba tare da ta jira an bata damar magana ba, ita fa hasalima gani ta yi normal magana ce ake yi da kowa ta yadda kowa ke fahimta kuma tana iya karre kanta daga kokarin da ake a hadata da yar ta □□ da ta fara magana da tsadadan turancinta wanda bata yi wasa wajen iya shi ba ta ce" walahil azim ni ba yar ta □□ da bace, ban san menene kalmar nan ba, ban rayu da wannan a zuciyata ba, alfarmar Allah nake ci, ni ba yar kowa bace dan ko iyayena basu waiwayeni a nan ba, abinda na sani na rayu da burin zama HOTTESTE shi yasa na dage ma yi karatu da dukan karfina da nutsuwata, ban zo nan da na lalata komai ba sai dan na ga yaya gidan yake na fada a tarihin rahuwaa cewar na yi yaki da son zama hotteste na kuma fadawa Allah kan ya datar da ni na zama mafarkina ne bai cika ba ba laifina bane, ban kasance mai zubar da burina da sauki ba shi yasa kulun nake tare hanya dan na kalli dogari, ni ba mahauk..,,,,,,,,,,"

Da dan daga murya Ameerah dake jin kamar ta rike makogwaron Muneerath dan haushi ta ce" zaki mana shiru a man uban wa ya baki damar yin magana ko dan baki da tabiya?"

Wani mugun kallo da ya watsawa ameerah sakamakon daga muryar da ta yi na uku kennan tun da ya zo wajen nan har tana neman hadasa masa ciwon kai ya sakata yin shiru tana rage muryarta sosai ta ce" ka yi hakuri sir, wannan yarinyar sam bata da yannayi da tarbiyar hottes, caractere dinta ba na irin aikinmu bane, wannan tana iya zubawa pasinger tea mai zafi a jikinsa ko ta tsoratar da shi "

Muneerath kam yanzun ta shaka , ranta bace sannan kasa kasa sosai ta ce" akoy marar tarbiya irinki ? Shin kin tsane ni ne domin na kasance mai taka dokokin Allah ko kin tsane ni ne dan bakya son kalar fatata? Ke wai Allahn da ya yiki ya maki albishir din a haka zaki gama da duniya ko tunaninki ke zaki zauna a wajen nan har duniya ta nade? Kafin ki zo wata ke wajen haka kuma zaki bar wajen du nacinki wata ta hau dan babu abinda ke zama dindindin a duniya ita dukanta karya ce! Kuma idan takamarki ke wata ce ni nan zan auri dogari kwana kusa zan zama yar uwa sarki kwana kusa zaki dawo talakata zan zo nan na hanna ki wulakanta mutane! Ku rike Hotteste dinku haka Allah yahukunta min ba wani ba! Takai dubanta kan ameerah da gaba daya ta gama tsurewa da kuma yarda cewar muneerah fa mahaukaciya ce ta ce" ke kuwa da kika mareni Allah in dai tsautsayi ya hadani da ke a waje sai na nanaga keyarki a kasa, idan ba haka ba kuwa na barki da Allah wuta balbal!".

Wato Allah na yin bayin Allahn da sam basa tsoron budar bakinsu su fadin abinda ke cikin zuciyarsu ko a gaban waye, bale rayuwar Muneerath ta yita ne cikin ihu a makwontai, watau tana magana ne tun tana tsoron fadi har ya zamana fadi take tun karfinta kuma s take dole a saurareta

Walahi bai taba gannin fitinaniya, fitsarariya, tsayayiyar yarinya irin wannan ba, a yau da ace Mah bata dakin taron nan da sai ya tsiyayewa yarinyar nan kaf man dake kanta!

A yanayinsa na nutsuwa koda ransa a bace , sannan muryarsa cen kasa kasa dan kar ya masu ihun da gaba daya za shiga uku ga mamansa ya zaunar da ita a cen bayansa a tunaninsa bai san ta taso tuni tana bayansa tana saurare da kuma bin kowa da kallo ba a hankali yana kallonta yadda ta tsafe abinta ita ta san korarta za yi kennan ko wace wace ya ce"Hey"

Ga mamakin kowa na wajen nan juyoea ta yi ta ce" tsaya in gama sai ka kore nin kai kuma!"

Ta dora da fadin" Saudat ba abinda ta yi, kuma ita ta iya girki, ta iya ruwa, ta iya tafia saman dogon takalmi na tabata ko dan kar ranmahaifinta ya bace zata jure wulakancinku na adadin kwanakin da kuke son tafka mata, ku rufa asiri dan soyayarku da fiyayan halita kar hukuncina ya shafeta! A kore ni ni ita a barta ta yi abinta, ga dukkan alamu aikin Hottest din nan karuwanci ne dan gashi dan ban iya tafia da dogon takalmi ina karairaya ba za kore ni!"
Baiwar iya yarensu da Allah ya bata ne ya sakata zagewa ta fadi komai da turanci kafin ta juya da niyar tafiarta tunda ta gama fada zuciyarta cike da tunanin me zai kaita gida? Abu daya dai da ta sani shine a yau idan ta je gida yayan gidan oga sai ta fasa kan kowani shege, dan ta tabata sai sun mata dariar da suka saba

Muryarta kasa kasa ta ce" Kar ka barta ta tafi "

Da sauri ya juyo jin muryar mamansa gaf da su, idannuwansa ya zarro ya kuma damkar hannunta zai maida ita wajen zaman ta tirje tana kallonsa ta cenza harshenta zuwa larabci ta shiga magana a sanyaye tana watsa hannayenta ta ce"

Allah fa ta ce ya tsaya mata, cewa fa ta yi Allah take fadawa ya cika mata burinta, haka fa ta ce bata wasa da buri akan karatunta, zuwa fa ta yi dan ta ga makarantar ta tsinci kanta a ciki, shin wannan bai zama babar hujar da ta isa a rike dan a kamawa yarinyar nan ta kai ga cinma burinta na son kasancewa Hotteste ko kana cikin manyan da suke da damar talafawa talakawa aman kuma suke take su sunna karra murje su dan basa son su ga sun ci gaba?"

A hankali ya kamo hannunta dan so yake ya zaunar da ita ko zai gabatar da aikinsa sai dai ta ki basi dama, a hankali ta fara yar gargadar murya irin hawaye fa zata masa a nan gashi yarinyar nan mahaukaciya sai ihun a bude mata ta fita take masu a sanyaye ta ce" kai ne fa uban talakawa, sarki mai taisayin talaka ne koda ba a kasarsa ba, kai ne fa Allah zai tambaya yaya ka tafiar da naka ikon? Kaine fa ya dace ka talafawa du wani wanda ya kasa ,"

A sanyaye ya ce" Mah, kar ki yi kuka mana a kan wannan, kin ga aikinmu yana da tsaurin gaske, sun taka doka ta hanyar daukan yarinyar nan bayan bata da cikakun takardun da aka saka dokar sai da su, ni ba dan tana daukan horo kyauta ba, ko daya, sai dan bata bi tahanyar da ya dace ace tana nan ba, mama bata yi makarantar hoton girki ba, bata yi ta horon ruwa ba, bata yi ta horon tafia ba, ta ina zan iya kyale haka?"

Aleesa ta dan fara daga muryarta dan ita fa so take tun yanzu ta fara tankwasa shi ta faa ganewa idannuwanta ya yi act irin na saraki a kasar da ba tasa ba dan haka ta dage kai da fata ta ce" kai zaka tsaya mata, kai zaka cike mata takarduntata hanyar sakata ta koyi girkin a makarantar daya dace"

Gashin kansa ya dan yamutsa yana dan dama bai fito da su ba ya ce" Mah ta yaya? A yanzu idan na saka kaina a wannan rigimar ina cikin matsala nima dan kuwa cewa zasu yi na take dokar da na dora, Mah ki fahimta zan bata makudan kudaden da zara tafi ta yi abinda take so da su, aman idan kika ce a yi haka ban san ta ina zan fara ba"

Mah ta juya tana kallon Muneerath da ta juyo ta nufi wajen su Ameerah da sukai tsuru tsuru ita da sir

Murmushi ta yi ta ce" Bana tunanin idan kudinka zai saka ta ajiye burin aikin nan, aman me zai hanna mu yi wani abu? Ban ki ka katanta mata maganar kudin ba, idan har ta zabi ka bata kudin a kan aikin nan bani da ja, bt idan har ta zabi aikin a kan kudin zaka yi du yadda zaka yi dan ka kama mata, ciki kuwa koda a nan ba zai yiwu ba mu tafi da ita"

Fuskarta ya kurawa ido, a duniya wannan mata tana da karfin iko da shi, tana dora abinda take so koda baya so kuma ya ji ya gani dan kuwa babarsa ce yana son abinsa baya tunanin akoy abinda zai sa ya mata rashin biyaya,

Matsawa ya yi kusa da ita sosai ya rage tsayinsa a hankali yakai lebensa kan goshinta ya mana mata kiss kafin ya ciro fari kal din papier a hankali ya shiga goge mata yan kananun hawayenta da ta fitar da rigima kafin ya jimke hannunta ya maida dubansa kansu sunna faatawa dayaren hausa shi kuwa baya jin yarensu abinda dai ya fahimta sojojin dake tsare da kofar take nunawa tana magana tana hade hannayenta

Lebensa na kasa ya cije cike da tsaa yadda zasu kwashe da su baki dayansu, dan kuwa shi ya tabata ko a kasarsa kasar arziki da wuya ya nunawa yarinya irin kudin nan ta wani zabi wai aiki bale a nan!, abinda dai zai so shine kafin ya salameta da

kudinta sai ya koya mata hankali! Uwa uba masu gidan nata da suka dauketa a kan tsarin da ba shi ba, su da kansu a yau zai mayar da su terrain! Zasu koma bakin aikin cikin jirgi daga Ameerahn har sir din, dama shi mai kula da tafiar da aiyukan Hottest ne a cikin tafiar jirgi ci gaba ne ya samu aka bashi wajen nan na horo, ita kuwa Ameerah tsohuwar hoteesss ce da tayi yawon kampaninika daga karshe itama ta samu mukamin nan ta sauko kasa, horon da zai masu a yau shine ya mayar da su saman su koma su kara daukan lesson kafin su sauko su ba wasu lesson din

A hankali yake nufarsu Aleesa na biye da shi itama a hankalin , a kasan zuciyarta kuwa adu □□□□ take yi kan Allah ya sa kar yarinyar nan ta bata kunya, ita so take ta ga yaronta na taimako, so take yaronta ya kasance daya daga cikin manyan mutanenmu masu talafawa yaa sunna taimaka masu wajen gannin sun tashi suma sun zama wasu gobe, ya kasance mai tausayin talaka mai talafawa matasa masu zuciyar yi

Yana karasowa du suka yi cirko cirko sunna kallonsa, sai a yanzu muneerath ta bi hannunsa daa dake dunkule da kallo
Allah bata shirya ba ta hadiyi wani dunkulalan yawu kafin a hankali ta labe a bayan sir dan kuwa wani tunani ya zo mata yanzun idan ya kima mata hannun nan nasa ai ya kasheta ya kare, gwara ta labe a bayan freind duda ta ga sai fada yake mata kan kar ta kuma yin magana idan wannan na waje wai shima mai gidansa ne, in ba sir ba ai shi yake mai gidansa ita ai bata sanshi ba dan haka ba mai gidanta bane sir shine mai gidanta, baban bakin cikinta ta fita ta ga babu dogarai, kai yau da sai ta tada hankalin kowa a wajen nan walahi!

A dake ya budi bakinsa bayan ya ba kansa hakuri da lalashin zuciyarsa sannan ya jure irin magangannun da yake ta yi a yau a yanzun nan ya ce"
11/14/21, 12:47 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 1 □□□

Ya ce □" Zo nan "

Irin yadda ya yi maganar da sauri Sir da Ameerah suka matsa dan gabansa kadan suka wani irin nutsuwa sunna jiran jin abinda zai ce

Sai da ya kare karantar yannayinsu kafin a nutse ya ce" milliard goma ko aikin hostess " (SORRY, da yawa zasu ga ina rubuta Hotteste, da yaren faransanci haka ake rubutawa , da turanci kuwa Hostess, ina fatan kun fahimce ni duka kalmar daya ne)

Kallon junna suka yi kafin a nutse sir ya ce" ka yi hakuri sir, ban gane ba "

Shiru ya yi bai yi magana ba, sai Aleesa ce da ta shaka jin ha milliard goma ya saka dan ta bar maganar cike da jin haushi ta ce" yana nufin ta zaba tsakanin aikin ko kudin "

Ido ameerah ta kwalalo cike da mamakin furucinsu, da kyar ta iya hanna kanta doro tambayar dake kan lebenta dan ji tayi dama ita ce? Aman ko yanzu fatanta yarinyar nan ta yarda kudin su biyo ta hannunta Allah sai inda karfinta ya kare dan kuwa sai dai su ci tare

Shi da kansa jikinsa ne ya mutu, Munneraht dai yarinya ce karama, gata budurwa, yan matan yanzu da wasun a kan waya suke rasa darajarsu ta mata bale ita buri ne sama sama wanda da yawa sunna tashi da burin abu kalilan ke saka su sakinsa ya bi iska? Ya gama sakawa ransa cewa zata yarda ne da maganar kudin nan bama sai an yi jayaya ba, kai dama ba □□ tura shi tambaya ba kawai a bata ta tafi dan kuwa baya tunanin zata ki amsa

Aleesama jikinta ne ya mutu, gashi ta rigaya ta zartar da hukuncin ta yarda kuma da haka, sai take ji a ranta damanma kai tsaye ta bashi umarnin da ta san ba zai taka ba, damanma ce masa ta yi ka shige gaba ta zama wani abu, aman a yanzun ita kanta ta tabata yarinyar nan ba zata bar kudin nan masu yawan da idan ta malake su ta zama sahun hajiyoyin garinmu ba ta dauki wani aikin irin na masu rabon kayan jus da sauransu a cikin jirgi ba

Hankalinsa ba a kwonce ba ya tsaya a gaban Muneerath da take kawar da kanta a duban wannan mutumen, ita walahi haske mata ido suke daga shi har matarsa da yake runguma a gaban mutane dan rashin ta ido

A sanyaye ya ce " Muneerah, sir ne ya aiko ni ya ce ki zaba cikin milliad goma da kuma aikin Hostess? "

Hankalinta ta bashi sosai ta daina hangen hanyar waje dan kar dogarai su tafiarsu baa samu wanda ya kyasa ba ta ce" Ban gane me kake nufi ba Freind"

Sai da ya hadiyi yawu jin tace masa freind a gaban su ya kara cijewa ya ce" yana nufin idan kudi kika zaba shi za baki Milliard na kudi har goma, idan kuwa aikin zama Hostess kike so zai baki"

Jinninta ne ya fara gudu hakama tunaninta, nutsuwarta ta bashi sosai kafin ta budi bakintatana nuna masa yan yatsunta ta ce" Milliard? Daidaidai har goma? Ka kuwa san me yake bada milliard? Millions dubu ne zai bada milliard, to shi din a ina zai sato kudaden nan?"

Da freinch suke magana hakan ya sa Aleesa bata ganewa aman shi Hanja yana gane dukan abinda take fadi

A dakensa yake dai yana kallon gefen da Aleesa ta bada dukkan nutsuwarta

Sir ya ce" eh haka ne "

Gaban goshinta ta dafe cike da wani yannayi shi ba na takaici ba , shi ba na neman ta fashe da kuka ba

A hankali ta ce" su din basa jin hausa ne? "

Sir ya dubi wajen da ta nuna, a sanyaye ya gyada mata kai

Bai aune ba ya ga ta nufi wajen su Aleesa dake binta da kallo, tsayuwarta ta gyara tana kallonsu ta tataro dukan turancin dake kwakwaluwarta tana dubansu ta ce" kun kuwa san shekara nawa na dauka da wannan burin a zuciyata? Ha Allah nake fadawa ba dare ba rana sai na ga alkhairi idan na kwanta da abin a raina a cikin mafarkina, a haka nake karra kwonciya ina tashi ba dare ba rana, kun san saboda na yi shi nake hanna kaina ci da sha dan na je na dauki karatu?"

Yan hannayenta ta nuno still tana kallonsu da kwayar idannuwanta irin na mage ta ce" Hannayena sun yi kunna fiye da a irga dan na koyi girki, ban samu na koya ba, kun san a ina na koyi iyo? A tafkin garin nan mai dauke da kada da manyan kifaye da macizan ruwa da komai dakomai na kasan ruwa, a haka na nutsu na sha ruwan nan kafin na iya iyo!"

Ta langwabar da kanta ta ce" shine kake son siyan burina da kudi? Ba zan iya siyar da shi ba, bana tunanin ko jirgin da nake hangowa a sama ka damka min zai sayi burina , ni burina na zamto Hostess "

Da wani irin admiration Aleesa ke kallonta, a hankali ta juya zata koma hanyar fitar dan ita fa sun gama bata mata rai, sai dai ji ta yi an rike mata hannunta raf da wani lalausan hannu

A hankali ta juyo dan gannin ko waye idannuwanta suka sauka a kan fuskar wannan mata mai kyan aljannu tana mata murmushi da hakoran makanta masu kyan gaske sai walwali suke abinsu

Gilas din dake idannuwansa ya cire ya sauke a kan fuskarta, tunda abin nan yake faruwa sai yanzu ska yi ido hudu domin itama a lokacin ta dago da dubanta dan ta kale shi suka yi ido hudu

Gabanta ne ya kwonci kwonci ya wani irin tsinkewa ya fadi da sauri ta cire dubanta a cikin nasa lokaci daya kuma ta samu kanta da karanta dukan ayar tsarin da ta Sani tana tofawa ko zata ji faduwar gabanta ya daina

A hankali ya kai idannuwansa gefen kunnenta , gashin dake kwonce tamkar na jariri ya taurawa ido shi kansa bai san me yake kallo ba,
Cire dubansa ya yi a nan din ya maida kan Aleesa da ta tsura masa ido tana kashe shi da murmushin kauna cike da matsananciyar kaunar yarinyar da irin abinda ta fada din

Ajiyar zuciya ya sauke a hankali ya saki hannun Aleesa ya juya kasa kasa ya ce" nan da minti talatin zamu tashi destination Ingila!"
11/14/21, 12:47 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 2 □□□

Murmushi Aleesa ta saki ta janyo hannun Muneerath dake biye da ita ba dan komai ba sai dan bata so ta janye hannuntada karfi ta yi mata sartse duba da laushin hannun matarsa ita kam ta janyowa kanau ya kashe su baki dayansu a kanta, aman in ba dan wannan ba ita ai so take ta yi ta koma ko zata dace da dogari daya

Da sauri sir ke biye da shi da takarda yana rubuta dukan abinda ya fada a rarabe ba wani a fayace ba, shi dai burinsa su rabu lafia
Sosai jikinsa ya yi sanyi a lokacin da ya ji an tashe shi a wannan waje da yake, sai dai a lokacin da ya ji cewa a gabanan aikinsa zai dawo yawo tare da hanja ne sai ya samu farin ciki maimakun bakin ciki, dan haka nan da nan ya koma office dinsa ya bugawa mahaifin Muneerath waya ya sanar masa abinda yake faruwa a ruffe, dan an shaida masa ne kawai za □□ yi tafia da ita kasar ingila dan ta fara aikinta

A mamakance ya ce" wai yar ogan? To aikin ma meye kuma? Jirgi ne yar oga zata taka ta daga?"

Sir ya bashi tabacin hakan ne, mahaifinta maimakun ya zaburo ya zo ya duba, ya ga yarinyarsa sai kawai ya tayata murnar hakan ya ce a hada su a waya

A lokacin da ya karaso da gagawa ya mikawa sojan dake tsaye ya kusa da motar da Aleesa ta sakata kawai tana kallonta cike da admiration ya shaida masu cewar mahaifin yarinyar ne aka bata waya ta kanga a kunnanta , abinda mahaifinta ya fada ya sakata yin tsuru tana sauraronsa

Walahi, bilahi, rashin kulawar iyaye ciwo ne, du irin zumudinta da wannan aiki jin yadda mahaifinta ya mata magana sama sama da alamun yana tayata murnar cikar burinta da son sannin wai da gaske zata daga ko yayane? Sai ta ji gaba daya duniyar ta yi mata zafi, a hankali ta janye hannunta daga cikin na aleesa dake kallon yannayinta ta kwontar da kanta a gefen kujerar ta jinginar, muryarta na rawa ta ce □" Oga, ina mama "

A wani shanshakai ya ce" ni dai da safe da zan fito mun hade da ita zata je wajen biki yanzu ban san ba ko a ina take gaskiya"

Wani irin zazafan hawaye ne suka shiga kokarin zubo mata a kan kuncinta, gaba daya sai ta dantse lebenta na kasa ta kasa ci gaba da magana dan tsoro take kar ta budi bakinta ta fashe da matsanancin kukan da kowa zai rasa gane kanta

Ba □□ dawo amsar wayar ba a haka har sarakan suka dawo kanta a jingine da madubin mota idannuwanta lumshe bata ga lokacin da dogaran da take zumudin su hade ba suka zo kusa da motar tasu aka hanna su matsowa kusa sunna yiwa HANJA kirarin da bai san yaren da suke yi ba har ta ji motar tasu ta tashi ta buda idannuwanta da sauri tana kallon mutanen dake cikin makarantar tare da waigawa idannuwanta na karra budewa tana kallon komai wasu hawayen na zubo mata

Budurwar dake tare da su ne take kallonta, ita mamakin da take irin yadda ta ga Mamansu ta rike hannun yarinyar nan, ko dai ya sarkin garinsu ce?

A haka suka nufi filin jirgi, kwata kwata bata tare da wani zumudi ko yannayi na farin cikin tafiar nan, bata nuna komai ba koda ta zo shiga jirgin da take mafarki ba dare ba rana, iyaye ba abin wasa bane, a zuciyarta ta dauke su da wani irin daraja, a yadda take gannin y□□ ya da iyayensu sunna mu□□ mala ta kula da kaunar junna ita ba haka bane, shin iyayensu aun haife su dan dole ne ko menene? Halin ko in kula na kan mahaifinsu, ba ruwansa da abinda ka fita yi ko kake yi, shi a tunaninsa ai kauna kawai ya sakar masu mara su yi fitsari ne, ita kuwa mahaifiyarsu bata san yaya zata kwatanta irin nata abin mamakin ba, sam bata san a wani waje ya dace ta ajiye mamansu ba,
Sosai take hawaye bata kula kowa ba, Aleesa kuwa sunna shiga Hanja ya kaita wajen zamanta du yadda ta so ya kawo yarinyar ya kiya ya ce da ita ta zauna har Allah ya sauke au lafia sai ta ganta

A dakin da yake na hostess a nan Sir Muhammad ya laya su, kai yake yana kawowa yana hankalce da hawayen da ya ki tsayawa Muneerath da kuma Ameerah da gaba daya ta fice a hayacinta itama kan wannan koma baya da ya sameta domin koma baya ne a wajenta bayan matakin da ta taka yau a wayi gari ta ganta a wannan matakin kuma?

A nutsensa ya ce" tafia ce da manya, ko bai taka matsayin babanmu a wajen aiki ba shi din baba ne a duniya, ku sani biyayar da zaku yi masa ita ce ribarku, ko me ya ce kar ku daga kawunnanku har sai ta bar wajen dan ko da abokan aikinsa baya gardama bale a yi musu da shi, ku kula ku kiyaye dukkan wani motsinsa baya korar mutun a dawo da shi ko wa ta tsaya masa sai dai iko na Allah, kuma yana da damar dakatar da kai koda a tsakiyar tafia ne bale a kasa!"

Takun tafiarsa ya saka Sir M dakatar da maganarsa sannan ya koma gefe ya ja ya tsaya

Kamar yadda ya saba kai kawo haka ya yi kamar sau biyu yana karewa kowace kallo kafin ya ja ya tsaya a tsakiya

Muryarsa a dake ya ce" Aiki ya kawo kowace, du wace ta yi abinda ba aiki ba a tsayin tafiar nan ba zan iya tafia da ita ba, mahaifiyata bata cin abu mai zaki, haka mahaifina baya cin abu mai magi da sanyi a kiyaye"

Yana gama fada ya juya ya yi dakin Pilot shima dan madaidaicin daki ne mai dauke da bayi da madubi wanda suke shiga su shirya kansu kafin su dauki jirgi

Sir ne ya dawo gabansu ya shiga rabawa kowa aiki cike da kula , sai da kowa ya nufi wajen da aka bashi kafin ya maido dubansa kan Muneerath dake kallonsa tana kikifta idonnuwanta

A sanyaye ya ce" me yasa kike kuka? "

Kanta ta girgiza har yanzun hular na kanta , stil dai a sanyayensa ya ce" mu je na nuna maki dakinku, ki yi wanka ki zauna har mu sauka, idan kuwa barci zaki yi sai ki kwonta har mu sauka in sha Allah"

Kamar ta ce da shi ba zan je ba, kamar ta saka ihun a sauketa ta koma gida, ji take kamar zata hadiyi zuciya dan damuwa sai dai bata musa din ba ta bi bayansa lokacin ne kuma ta ji an ja jirgi ya fara yar tafia hakan ya sa ta ji zara fadi, sai a lokacin ta tuna ko a cikin me suke, sai a lokacin ta yi sauri ta bi bayansa cike da tsoro suka shige dakin nasu

Turus ya yi gannin sandukin da idan an yi mutuwa ake sakawa, watau a nan aka saka gawar wace ta rasun kuma aka ajiyeta a nan maimakun a kaita cen cikin da ake ajiye sandikan gawa na cikin jirgi?

Juyowa ya yi da ita ya fito da ita ya nuna mara eajen zama ta zauna ya nuna mata yadda zata daure jikinta da kuma abinda idan tana son yin baci bata son haske zata sakawa idannuwanta da na kunne da safa kafin ya juya ya koma wajen aikinsa zuciyarsa cike da damuwar halin da take ciki, kwarai ya san dAmuwar ta iyayenta ce, aman kuma ya mara uzuri dan ya kula da ake cewa Allah mai fitar da kafuri a cikin musulmi, musulmi a cikin kafiri hakan ne, su suka haifeta aman halayensu ba iri daya bane

Sun yi tafia mai nisa kafin suke sauka dan bai yi biye biyen ko □□ na ba ya dauro niya sai ya ajiyeta kafin ya ci gaba

Sun sauka gaba dayansu cike da gajiya, du irin halin da take ciki sai ta ringa jin idan ta daga kanta juwa zata kifata a kas, sannan ta ringa gannin abubuwan mamaki da tsoro na yannayin ginnij da idannuwanta suka iya ganni
yinwar dake cikintama ta isheta dan kuwa ta nuna cikin nata ya dan fada ga juwa na damunta
Kwata kwata bata gane komai har aka sakata a wani daki mai masifar sanyi da kyau a nan filin jirgin dauke da gado daya tak

Bata iya tsayawa yin wata wata ba ta faa saman gadon nan bayan ta cire dan sosonta dake kafarta ta kifa kanta kafin ta fashe da wani irin kuka mai karfin gaske tana karra cusa kan nata cikin matashin kan lalausa da shi a hankali take fadin" Mama, Abanmu, shin ina rayuwar nan zata kaimu? Bayan nesan cen da na yi da ku a yanzun na yi mugun nisan da ba zan iya kai kaina inda kuke ba ko a guje na fita koda wani jirgin zan shiga ba, ya Allah ka kare ni da kariyarka, kar ka bari wani ya shiga lamarina ya lalata min rayuwata, Ya Allah kar ka bari kudi ko saurayi su rude ni na bar hanyarka, ya Allah kar ka ba talauci ko kangin rayuwa damar da zasu saka ni manta ka, Allah ka shiryar min da iyayena su gane cewa amanata ka basu zaka tambaye au a gobe kiyama, ya Allah kar ka kashe ni a nesa da dangina ta yadda ko gawata ba zasu gani ba bale au salaceni, Allahna ka.....,.,"

Bata karasa ba ta ji wata ya suwaiwai din murya na yi mata magana ta hanyar kiranta da mssz,

Da sauri ta dago fuskarta cike da hawaye tana gogewa ta sauke dubanta a kan matar

Taf, sai kawai ta saki baki da hanci tana kallonta dan kuwa budurwa ce ko na ce mace ce yar gayu iya gayu sanye da dan bintilin sket da riga mai dogon hannu yan berayen mamanta sun matsu bayin Allah gashinta daure a tsakiya ta gyara tsayuwarta da kulawa tana mamakin to a ina sir ya samo wannan yarinyar da sam bata shige da yar kasarsu? A mutunce duba da wanda ya damkata a hannunsun mai kasar ne ya kuma jadada kan ta kasance kwarariya a aikinta dole zasu kula su yi taka tsantsan ta yadda zai kasa ganeta koma me dinsa ce a tausashe sannan a mutunce cikin yaren turanci , irin kwararan nan da sai da ta dage ta saurara da kyau kafin ta gane me take fadi ta ce" ki taso mu tafi cen school din"

Sai da ta kikifta ido kafin ta karra gyara zamanta tana kallonta ta ki yi mata magana sannan ta ki tashi

Karasa shigowa ta yi ta zauna kusa da ita ta karra tausasa kalamanta sosai ta ce" ki yi hakuri zai dawo da wuri, sun tafi saudiya ne da mahaifinsa da mamansa, ya ce mu kula da ke sosai a makarantar ta yadda zaki goge ki iya komai na aikin hostess kin fahimta?"

A hankali ta gyada kanta duda bata san wa ake baa hakurin a kansa ba, abinda dai ta sani shine kawai zata bi su, ta je ta koyan, tana kwarewa a maida ita kasar iyayenta dan ba zata zauna a garin nan ba , ta ina zata iya rayuwa da arnawa

Da dan sosinta take biye da ita da sauri dan gaba dayanta a tsorace take balema da ta fito waje ta ga garin ya ganta

Wata galeliyar mota ce wani soja ya bude suka shiga kafin a ja su a yi gana da su

A yanzun kam makarantar da aka zo da ita sai ya zamana tsoron fitar da kafarta waje ya kamata dan tana tsoron ta taka ta saka masu dati

Wasu mata ne a tsaye su uku kowace cikin shigar dogon wando da riga da dogon takalmin hils sunna jiran fitowarsu
Da mamaki suke kallon Muneerath tun daga sama har kasa kafin su ringa kallon junnansu

Babarsu ce da kusan idannuwanta kadai ke nuni da ta dauki shekaru sosai sai ko wuyanta da ya dan nuna shima da turancinta ta ce" ina yarinyar ne?"

Wace ta kawota ne ta nuna mata Muneerath dake tsaye ta hade hannayenta a jikinta tana ta waige waige cike da tarin kauyanci da tsoro kafin ta maido dubanta kansu taga suma dukansu ita suke kallo sai du ta tsargu ta tsinci kanta da hade kafafuwanta waje daya kamar mai jin fitsari

Kai babar ta dan juyar kafin ta nuna da hannayenta ta ce" Me da me yake bukata gyara a tare da ita?"

Wata kyakyawar budurwa ce da cikinta tamkar zai hade da bayanta itama da kula ta ce" da farko dai fatarta, tana da kalar fata mai kyau sai dai hankalin fatar ba a kwonce ba, ba santsi ba alamun laushi, sai fuskarta tana bukatar gyaran da zai cire mata wannan fari farin abin na hancinta da wajen idannuwanta, tana da lebe masu kyau sai dai basu da laushi, gashin dake kwonce a kusan kunnayenta sun nunna yana da kyau gyara ne yake so, tana dauke da manyan bombom dan suke da bukatar

kara rike kansu, sai matsalar tumbinta da dole a yi aiki kansa, sai mu dawo kan gwuiwar hannayenta da tafin hannayenta da faratunnanta sai wajen farin idannuwanta da yake da duhun haske yana da bukatar ya samu gyara, ni dai iya abinda na gani kennan"

Dubanta ta maida kan dayar itama ta matso sosai kusa da Muneerath da ta saki baki da hanci tana kallonsu da mamakin wai du ita ce ake zancenta ko wa? Ai kam zata masu barin mahaukaciya a wajen nan idan suka nuna ita din kazama ce, yo kaf gidansuma waye yake wanka biyu in ba ita ba?

Dayar ta ce" tana da matsalar tafia da dogon takalmi idan kun kula kafafuwanta sunna da matsala"

Daga su har Muneerath din sai suka kai dubansu kan kafafuwan nata, da sauri ta dago gannin matar ta amshi waya tana maganar ttana son gannin docter kafin ta kale su ta ce" Gimbiya Aleesa ce ta ce ta zama perfect.....dan haka zata zama perfect "

Tana gama fada ta yi gab
Daga wannan lokacin Muneerath ta shigo sabuwar rayuwa,
Watau tana gannin rayuwa mai sunna rayuwa
Airfa kala daban daban ta yau da kulun , ga wankan da ake darza mata ita kanta ta san da ace faa na kodewa dan wanka da tata ta gama kodewa ,
Hakowaranta kansu sai da aka sake koya mata yadda zata wanke su
Abinda ya fi bata takaici irin yadda ake koya mata magana, yo in ba iskanci ba yaya ake so ta zama ne wai?
Duwawunta kuwa haka za □□ daura masu wani abu kamar igiya a tsayar da ita a kunna ya ringa rawa a jikinta

Baban bakin cikinta cin abinta lokaci gare shi, kuma zaba mata ake, sanan bashi da yawa, tana gama ci ake bata wani hadin su lemun tsami ta sha ba dan dadi ba sai dan wahala
Cikin nan nata da take alfahari da shi ne yake lumkewa yana shigewa sanann ana shafa mata abun nankarwa dan kar aje mai fitar da nankarwa ce fatarta ta fitar ta lalata mata fata duda bakin fatarta ba mai gagawar nuna nankarwa bane

Yan guli guli din mamanta ne ta ga sunna dan girma duda ba cencen ba aman ta kula kumbura suke ga rigunnan mama kala daban daban a laye da pant dinsu wai du nata ne
Abinda ta kasa ganewa shine a haka har yanzun bata dawo yadda babar take so ba dan da sasafe auke fita gudu tare tana karra koya mata karuwancin da ta rasa na uban menene wai du a aikin ne ko meye?
A ranar da ta shiga ruwa da su kuwa su kansu sun sarawa iya ruwanta kuma sun shaida koda bata iya komai ba ta iya ruwa

Sannu a hankali ta fara shiga kicin
Yannayinta ya fara dauka, fatarta ta dauki gyara ta dawo wata irin bakar fata mai masifar kyau din man da maza ke hari, cikinta ya lafe sosai sai duwawunta suka kara budewa suka baje sosai abinsu gwannin kyau da su idan ta tsaya a tsaye daga sama kirarta kamar ta rihana zuwa duwawunta kuwa ta kusan kamo niki minaj sai dai basu yi girman na niki minaj din ba, kalar fatar tata kuwa kamar ta rihana din dan kuwa ta amshi guara ta kuma saje da sanyi ta yi minas da ita

Tashin hankalinta bai wuce ko girkin nasarun ta kasa iyawa ba

Yi ake a nutse, a rrubuce ake bata, a bayane ake bayana mata aman cikin ikon Allah ko wainar kwai da ta gwada soyawa ita kadai sai da ta kone kurmus tana shawarar ta soyu bata soyu ba!

A haka take tare da mutanen nan da suke darajata ko dan wanda ya bada ita, sai kuma uwa uba su din sunna daraja kowa din ne

Kusan watanta daya kennan tare da su bata ga kowa nata da ya kawota wajen ba, a yanzu ta fara damuwa da son gannin Sir dan ta tabata shi din zai kaita inda ya daukota

.....

Gaskiya ne, masu abu da abinsu,
A wannan kwanaki HANJA da iyayensa sunn zaga kasashe masu yawan gaske, sun yiwa saudiya shiga biyu kafin su fara shirye shiryen dawowa kasarsu

A yau bayan ya dawo daga masalaci ya zame a falon da iyayensa ke zaune ya nemi waje ya zauna cike da gajiya yana kallon mahaifinsa da ya ga ya kura masa ido yana kallonsa

Abansa ya yi takwaf takwaf da fuskarsa a sanyaye ya ce"
11/14/21, 12:47 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 4 □□□

Ba edditing fa

Sosai yakara kausasa fuskarsa kafin ya ce" ba zata zo inda kuke ba, ba wata bakuwar fuskar da zan kawo gidan nan kun ji na fada maku gaba dayanku"

Tsuru ta masa da ido tana kallonsa har ya gama saukowa daga saman bed din fuskarsa a hade din nan ya nufi bayi ita kuma ta raka shi da kallo kafin ta cire dubanta ta mike ta nufi wajen suturarsa tana dan cije lebenta na kasa a ranta tana fadin 'ba dai naci kake so na maka ba? Zan maka shi har sai ka ji kamar zaka saka kuka domin yarinyar nan ni shaida ce bata da kowa a nan, sannan irin damuwar da na gani karara a kwonce a fuskarta sai na maye mata da farin ciki a kansa'

Kaya ta ciro masa bakaken swttt da abubuwan hadinsa harta da agogo sai da ta ciro ta ajiye kafin ta tafi falonsa ta zauna ta gyara zamanta sosai tana jiransa da karamar waya a hannunta ta kirayi yarinyarta da take wajenta ta shaida mata abubuwan da take so sannan ta dora zaman

Ta dauki a kadan awa guda har bayan kanta ya fara sara mata kamar yadda ya saba yi mata sukan nan tana zamanta sai ya soketa ta dafe kadan ta lumshe idannuwanta tana tofa adu'a ya fito daga dakinsa

A hankali ya karasa ya duka gabanta yana kallon fuskarta kafin ya saka hannunsa ya shafa gefen fuskar tata a hankali ya ce" Me yake damun Mah? "

Mah ta sauke ajiyar zuciya ta cire hannunta tana kallonsa ta dan girgiza kanta a sanyaye ta ce" ka dauko min ita, ina so ta zo kusa da ni please"

Kansa ya kawar ya kama hannayenta ya juyo yana facing dinta a hankali kamar baya son magana ya ce" Duniya ta rikice, mugayen mutane sun cikata da muguntarsu a cikin zukatansu, ku....kune duniyata, kune farin cikina, sai yaushe zaku gane cewa bana tunanin idan har zan iya aikatuwa idan bakwa gefena? U see da hannuna zan shaketa sai ta daina motsi koda musu ta yi da ke bale ta ilata min ke, Mah koda tokarta ce sai na kona na kuma konawa na kuma konawa, na shiketa na busarta na kuma jiketa na zuba a kwata!, Ba zan iya kwatanta maki tsorona da dukan halitar da zata rabeki bayana da abuina, kin ga ko wannan da kike riko mai kallon tsiyar nan ba wani yarda na yi da ita ba!"

Murmushi ta yi cike da kaunarsa a kasan zuciyarta inda fuskarta ta bayanar da shaukin kauna irin na uwa tana tuna yarintarsa da irin yadda ko bata da lafia yake adu'ar Allah ya sauke mata ya dora masa,watau wata irin shakuwa ce ta ban mamaki a tare da su, ko mamansa da tana raye da iyakar shakuwar nan kennan
A hankali ta shafa itama wajen sajensa a sanyaye ta ce" Burina ka zama mai tausayi, ka zama mai taimaki, ban ki ba duniya yanzun ta zama abin tsoro sosai, aman kuma a cikinta akoy na kirki cike fall, hakama akoy innocent cike da ita, Son akoy marayun da suke da iyaye, akoy bayin Allahn da suke manyan mutane ne a boye abinda ya hanna su bayana just dan taimako ne na manyan da suke sama da su, Son ka faranta min dan Allah"

Idannuwansa ya lumshe yana kallonta a hankali ya kawo hannayenta wajen bakinsa ya lumshe idannuwansa ya manna mata kiss a bayan hannayenta sannan ya dago da dan tsugunnin da ya yi a gabanta ya mana mata wani kis din a saman goshinta a hankali ya ce" I love u "

A bayane ita kuwa ta dafe saman gashin kansa ta shiga kwararo masa adu'o'in tsari kafin ta karashe da furta masa kalmar Allah ya yi masa albarka sannan ta mike ya riko hannunta sunna tafe a hankali har suka fito waje kafin ya yi gaba tana daga masa hannu ya je wajen motar da aka bude masa ya shiga sauranma du auka shishige da gudu suka tada suka kama hanyar tafe tafen da zai yi ciki harda zuwa ya ga Zakanyarsa.

Da dan sauri ta koma bangaren mijinta, tana zuwa ta zauna kusa da shi tana murmushi ta ce" Idan ya zo da ita Khalb sai ka soya min kwon nan yau"

Murmushi ya yi mata yana daga kafadarsa yana yatsine baki na maganin da ta matsa masa ya sha wanda a saudiya aka yi ta saukar alkur'ani aka hada da wasu ganyayaki nasu wai ya ringa sha in sha Allah sai dai idan ciwonsa ba na warkewa bane, idan dai na warkewa ne zai warke ne cikin sauki a lokacin da shi kansa bai tsamata ba, watau sun nuna masa cewar ayar Allah ita ce magani, babuaganin da ya kaita karfi hakan ya sa yake sha aman ba wai dan ya saka a ransa wai zai warke ba, wani warkewa kuma? Ai warkewa mai gaba daya na tunkaro shi a kowani second wanda ya tabata yana yinta an kare, haka kulun ta dafa masa su percil, su sasake sasakenta ita dai mijinta kar ya barta, sai da ya yatsina fuskarsa kafin ya ce" Wanene zai daukota? Kin manta irin tsanarsa da mutun bako? Bama zai daukota ba"

Kanta ta dora a gefen kafadarsa jikinta a sanyaye ta ce" ni kuwa da sai na masa kuka, kuma na je na daukota da kaina"

Murmushi ya kuma yi yana girgiza kansa a hankali ya ce" Noor, ba zaki zubar da kwalarki na ko na wasa ne idan dai ina raye "

Shiru ta masa dan bata so a yi nisa da maganar idan yana rayen nan domin ba abinda ya gagareshi yanzun ya zurmiyar da ita a kogin tunanin rayuwa babu shi

.....

Idan aka ce nutsuwa, ana nufin nutsuwa,barci ne take na nutsuwa, cikin nutsuwa, bayan tarin gajiyar da ta kwasa na yau
Tabas kasashen waje sun yi nisa irin nisan nan da hankali ba zai dauka ba sai idan ido ne ya gani

Na sha gani a cikin familly Kardashian da cikin emission kala daban daban na irin yadda mutun ke sawaya lokaci daya watau a cikin sati daya idan aka fara bashi kulawar idan ka ganshi zai zama bako a wajenka har sai ka kuma tambayar kanka da kokowa da tunaninka kafin ka tirsasawa zuciyarka yarda cewa shine ba
Girman jikinka na iya ragewa ya koma sakwaikwai , tumbi na iya shafewa ya komai luwaiwai ba tare da ya bar tarin fata ba ko nankarwa irin na mai jiki idan ya rame ba domin akoy mayuka da kuma sport din da zai ja maka fatarka sosai ta janyu ta yi kyau sosai
Shi ba shirurgi ba, ba kuma tsafi ba, reality ne wanda sai ka bi tashohinsu zaka ringa gani ko idan ka je inda suke zaka karda du girman jikinka yana iya raguwa ya daidaita ya yi kyau, haka kuma du tumbinka yana iya shafewa ya dauki kala, komai girman duwawunka idan baka so akoy irin aport din da zaka yi su ragu da irin kalar cimar da za'a doraka a kai .....watau zaka cenza iya cenzawa sai dai halayenka su shaida ko wanene kai domin hausawa na cewa idan ka rabu da mutun tambaya idan ya yi arziki aman halaya na nan.....

Shi ne ya faru da rayuwar MUNEERATH a tsayin sati uku, wanda ta amshi wani irin kulawa tun daga yannayin jikinta da sam ta ki a rage mata duwawunta ta nuna a kan me a barta da halitar da Allah ya mata, sai dai tumbin nan nata gaba dayansa ya lafe ya shafe ya tafi duniyar da takan kamuwa da mamaki ta ringa shafarsa tana juyawa dan son gannin ina ya je ya lafe, domin ko ta ci baya nuna kansa ya rigaya ya amshi gyara mai yiwuwa shi da ya tasa sai ko yaro ya shiga,

Fatar jikinta kuwa ta hadiyi na hadiya ta shafa na shafawa, bakin nan nata ya zama baki na mararin farar fata ko wacece, bakin nan ya zama baki mai birge kowa, fatarta ta yi wani irin laushi na mamaki domin tun AC na sakata mura har ya yi hakuri ya ba kansa lafia ya zubawa sarautar Allah ido dan kuwa duda kasancewar garin garine mai sanyi shi yasa ba ko'ina suke da AC ba yawancin guraren sunna dauke ne d chauffage, aman haka Take kwonciyarta a cikin sanyin nan ko ta yi kai kawonta a cikinsa ba tare da tana makuarkyatar sanyi ba, har wani sa'in takan tambayi kanta to yaya aka yi take jin tsoron sanyi a da a yanzu kuma bata tsoro?
Gashin kanta ya gama bayanar da bakinsa da tsayinsa da laushinsa, ita kanta a yanzun takan saki murmushi tana hangota a Niger idan aka mayar da ita gata ga Oga ga mamansu ga yan gidansu uwa uba idan ta zagaya ta tabata a yanzu dogari sai ya yi kuka kafin ta yarda da maganarsu ita da shi! (Ciwo na dogari yana nan dan har yau har gobe tana kan bakanta)

Ga sir a gefe guda ya zamto mata aboki, aminin shawara a ganninta, inda shi kuwa ya zuba mata ido yana son a hankali ya cire mata maganar wani wai dogari , domin ya kwatanta mata cewar wannan mafarki ne, inda ta shaida masa ko kasancewarta A wanann waje a matsayin hostess mafarkinta ne ya tabata, ta tabata wata rana zata ganta gata ga dogari a matsayin mata da miji.....watau dai su din zasu taka matsayi na yan uwan sarki, wanna. Daraja tana so ta zamo gaske dan ta san sarki ko dansa sun fi karfin yar oga.....sunna zantawa da shi ne ta yanar gizo gizo domin har yanzu yana nan a hannun HANJA bai sake shi ba

A zabure ta farka daga barcin da take a lokacin da karaurawar da ake tashinta a barci ta dauki kuka kirrrrrrrrr

A firgice cike da mamaki ta kai dubanta kan agogon dakin dan gannin hala har lokacin tafia gudun yama ne ya yi bata tashi na bayan ta kasance mai tashi a kan lokaci?

Maganar dake shiga kunnenta ya sakata yin kasakai tana sauraro kafin ta sauko lalausan kafafuwanta ta zura cikin takalmin dake kusa da bed dinta ta saka hannunta tana kunce hular kanta sannan ta cire dan Siririn ribom dinta ta yamutsa gashin kanta a sanyaye ta ce" Prince kuma sir? Kin fa ganni fa cikin lokacin barcina ne fa ko so kike muna girki ina barci kuma ki ce laifina ne?"

Murmushi ta yi daga zaunen da take tana kallon yadfa take turo baki ta ce" Yan mata, ki rufa mana asiri ki tashi ki je ki kimtsa kamki cikin minti goma ki fito domin nan d aminti talatin zai karaso, ki kula idan har wani abu ya kauce ni da kaina yana iya korata a nan, ko so kike a kore ni?"

Kanta ta dago ta kai wajen camerar ta dan tsura ido kafin ta mike ta ja tawul ta nufi bayin

Ajiyar zuciya ta sauke bayan ta bi bayanta da kallo ta dan dafe gaban goshinta ta kali ta kusa da ita da ta ce" Banan tashin hankalina irin abinda zai faru a kan maganar girkinta da kuma kiyawa da ta yi a taba mata hips dinta, ki duba ki ga a da bai fito sosai ba domin a da tana da tumbi, a yanzu kuwa da tumbin ya shafe kina gannin yadda gaba daya ya gama bayana, bombom dinta ba zai boyu ba koda wandon jine ta saka , ina tsoron sanadiyar wadinnan matsalolin biyu yau ya wanke mu tas"

Mai bima babar tasu ce ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Madame, me yasa wai kika ki taba mata duwawun nan nata kika biye mata aka bar mata su a haka bayan ga yadda suke da girma da fadi?"

Dan murmushi ta yi ta ce" nan fa burinku ku samu duwawu koda rabin rabin nata ne, duda na san ba maganar ra'ayi bane aman wannan wajen fa waje ne da kowa da yadda yake son gannin nasa sai idan bai samu ba"

Dan murmushi ta yi ta ce" ita bama wannan ne damuwarta ba, baki ga abinda ta ce ba, cewa ta yi kar izgilin ya yi yawa a bara mata halitarta haka ita kamta sun dameta aman bata so a rage su dan kamar za'a yi izgili da yawa wai"

Mikewa madame jocyline din ta yi tana harhada takardu da sauri sauri ta ce" Wani lokacin haka musulmai suke, idan zasu yi abu sai ki ji sunna cewa kar su sabawa Allahn su, ban san me hakan yake nufi ba, aman ita da ta hanna a taba mata bayanta ya hauta sosai, wannan bayan nata du nimiji mai lafia zai motsa idan ya kalla , dan dai shi sir din ne ya zama ba wannan ne a gabansa ba, ni dai fatana kar a kore ni yau, mu tafi maza maza mu gama shirya dakin tuhumar, ban san me ta aikata da za'a tuhumeta ba"
11/14/21, 12:48 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 5 □□□

A gagauce ta gama shiryawa, ba kwaliya a fuskarta ko dis domin ba kwali aka koya mata sakawa ba , haka kuma lebunan nata bata shafa masu jan baki ko man lebe ba, abinda ta yi shine saka pant da doguwar riga har kasa wace ta dame mata kirjinta da ya dan yi tudu abinsa itama ta yi mama irin na mata
Rigar kalar orang ce, aman mai duhu bata da kwaliyar komai a jikinta sannan ta auduga ce watau coton hakan ya sa ta lafe mata a jikinta ta bi jikinta har kusan duwawunta kafin ta dan saki kadan ta yi cen kasa

Takalmi ta ciro baki sidik kafa ciki sannan ba mai tsini bane mai dan tudu ne dai kasansa na kwalba

Sai turare da ta wanke jikinta da shi a nutse ta juya ta ajiye laptoo dinta da ta daidaita ta dauki hoto da shi ta ajiye ta juya bayan ta dora bakin dan kwali siriri a kanta hankali kwonce ta nufi wajen da aka ce mata ta je

Kicibis suka yi da daya daga cikin masu basu horo ta damko hannunta bayan ta wara ido gannin riga da ta saka tamkar an zana abinda ba'a so ya fito din ya fito radau da shi gaba dayanta bombe ce yarinyar ko mace tana birgewa bale maza aman sun tabata yau sir sai ya ci ubansu baki dayansu

Ita kanta madame ido ta zarro, da sauri ta kalli wajen da camera ke hasko motocinsa sunna shigowa , bata san lokacin da ta dora hannu daya saman kanta ba ta ce" Yanzu du a cikin kayanki kika rasa wanda zaki sa sai wannan rigar dake maki kyau?"

Rigar ta bi da kallo ta kalli madame din , gani ta yi kaf a kayan wannan itace ta fi sutura kuma suke nuna a kan me ta saka ta? Ita ba zata saka wadinnan dingilalun sket din ba ta fito ko kuma ta saka wandunnan nan nasu matsatsu sun matse mata cinya idan ta wuce mazan cen sunna rakata da kalo haka kawai ba, ita da a niger ne wannan rigarma ba zata saka ba dan ta san sai an ci uwata da ihu rigar fa tsaga gareta fa har kusa da cinya fa! Kai ita ba yar duniya bace walahi

Dan bakinta kawai ta turo tana kifta ido tana kallonta ta ki yin magana aman a kasan zuciyarta fadi take koma uban waye princ din nan ya yi ya gama ta koma ta maida barcinta

Hannunta madame ta kama da sauri ta yi cikin dakin da ita

Dakin ta bi da kallo, yana fitar da sansanyan kamshin da bata taba jin irinsa a duniyarta ba
Table ne madaidaici a ajiye a tsakiyan kujeru biyu lafiyayu da su, sai katon madubi da kuma wani abu dake fitar da amon murya waje sai kuma camera har hudu kusurwa kusurwa da wasu abubuwan da bata san ko na meye ba ita dai, sai mutumen nata watau sanyi karara da dakin yake yi

Wajen da zata zauna ta nuna mata ta tsaya a gabanta ta ce" Muneerah, ki saurara da kyau, mutumen da zai shigo yanzun ban san takamaiman me kika masa ba, domin idan lafia ne ganninsa na iya zamewa har ki koma ga mahalicinki baki samu gannin nasa ba in dai ba a jaridu ba ko a tv ba, abinda nake so da ke ki tsaya a nan ki hade hannayenki waje guda ki yi jira, kar ki saki ki zauna ko ki shiga wani abin daban , idan ya shigo kafin ya shigo sai an shigo am bincika dakin da ke kanki, kar ki yiwa masu bincikarki gardama dan abu kalilan na iya sakawa su sumar da ke a wajen nan, ki kula ki saurara da kyau ladabinki shi zai fitar da mu duda ban san tsakaninki da shi ba domin shi ya sa aka kawo ki nan, aman abinda na sani shine halayansa da kuma irin yadda yake da karfi da mulkim da zai zartar maki da hukinci a nan kuma kin kade har buzunki, ki sani kar ki sake ki zauna sai ya zauna bara na fita ki tsuaa a tsayen nan fa"

Tana gama fada ta fice ta bar Muneerath tsaye baki da hanci da ido a bude ta bita da kallo, wanda ya kawota? Wai tsaya hala sir abokinta? Kai aman kuwa dama shine zai zo bai fada mata ba ko menene? Kuma wai shine ake tsoro haka? Aman kuwa yau zasu sha mamaki idan ya zo yana wangale mata baki tana cin magani dan ba zata sakar masa fuska ba sakamakon zai zo bai fada mata ba walahi!

Tsayawar ta yi tana hamma tana tarewa da hannunta tana dan kale kale a kadan ta dauki minti goma sha biyar ba shi ba alamunsa hakan ya sa ta tabe bakinta ta nufi

kujerar da ba ita aka nuna mata zata zauna ba watau kujerar da shine zai zauna a sama ta hau ta zauna tana lumshe idannuwanta sakamakon barcin dake cike a cikinsu ta dora hannayenta saman table din ta dora kanta a sama ta kwontar tana limahe idannuwanta wani dadadan barci ya zo ba sanya ya sureta irin mai tafe da dadadan mafarkin nan nasa ta lula duniyar gidansu bayan ta gama tsakin wai wani tsaya sai ya zauna ta zauna kamar shine OGA!

Wanda ke zaune a gaban computern ne ya gama kallon ikon Allah gannin ta zauna saman kujerar da Sir ne zai zauna a sama uwa uba ya ga ta kwonta abinta ta yi barci ya mike da niyarr zuwa kusa da abin maganar da zai yi dan ya tasheta ya tuna mata abinda Madame ta fada domin sun fita tarbo shi ne gaba dayansu, kawai sai gani ya yi an bude wajen, sojoji suka fara shigowa dafka dafka da su fuskar nan a hade sunna rike da bindigoginsu lokaci daya suka shiga bincikar wajen baki dayansa kafin oga kwata kwatan ya shigo shima cikin takunsa na kosashen ingarman namiji inda dukan manya manyan wajen ke tafe a bayansa sun yi shiru ba mai kwakwaran motsi

Kai tsaye shine ya fara zuwa kofar da aka saka Muneerath, sannan ya gama fadawa sojojin cewa yarinyar bincikensa ce ya dauki abin nan da ake karawa jikin mutun dan a ji idan da wani mugun abin a jikinsa abun ke yin kara ya shaida hakan ya rike a hannunsa na dama ya nufi kofar da aka bude masa inda wanda aka bari gaban computer ya ji wasu hawaye masu dumi na son zubo masa sakamakon tunanin yau sun cira bata nuna ba du sai sun fadawa yan garinsun da ya yi , sannan ya kalli madame da ido yake nuna mata cewar ba kanta fa idan har ya shiga a yanzu aman sam bata gane ba har sai da ya sa kai sanann aka basu damar su tsaya a gaban alon da zai nuna masu abinda yake faruwa a cikin ne

Cikinta ne ta ji ya mata wani irin kuka a lokacin da ta ga HANJA tsaye da mamaki yana kallon Muneerath kwonce tana sheka barci a saman kujerarsa kafin ta ji kafafuwanta sun gaza daukanta ta yi kasa tana zarar ido jiki a mace

Da mamaki yake kallonta na tsayin minti biyu ya gama yarda cewa da gaske barci ne take yi a saman kujerarsa, ta zauna kafin ya zauna harma ta yi barci, nan da nan zuciyarsa ta fara tafasar bacin rai ya gama yanke nata hukuncin shine zai saka jirgin da zai tafi africa ya dauketa a yau ya watsar da ita a duk inda ya ga dama idan ya so a cen ta nemi danginta bayan ya gama kurce baki daya al'umar kasar da ya daukota a kan list din wa' inda zasu ringa horar da Hostess dan ya kula basu san meye ma'anar hakan ba!

Rai bace ya juya zai bar office din , lokaci daya kuma ya ja ya tsaya sakamakon lalausar fuskar mamansa da ta bayana a cikin kirjinsa da kalamanta da tunanin irin nacin da ta nuna a kan yarinyar

Juyowa ya kuma yi ya kara ja ya tsaya ya kuma zuba mata ido, Bukekiyar banza bukekiyar wofi! Ya saba idan ya zo ma'aikata yan aikin wajen suka yi laifi ya hukunta uban gidansu, aman a yau yana tunanin ya zama wajibi hukuncin nan ya hau kan yarinyar nan kafin ya hade baki dayansu sauran daya bayan daya , kai ya zama wajibi ne yau yarinyar nan ta san menene iko! Ya zama dole ya bata tarbiya ya nusar da tsagerancinta domin ba zai manta irin yadda ta zo masa kai tsaye gabansa tana masa irge da wasu yatsunta ba tana fama da wani shegen tumbin tsiya wai ita Hostess ! Kai dolema ya kara hukunta wa'inda suka dauketa suka sakota a duniyar JIRGI!

A DAKE YA RINGA DAGA KAFARSA YANA KARRA TAKU KUSA DA TABLE DIN, WANDA DU TAKUNSA SAI GABAN MUTANEN DAKE GABAN ALON SUNNA

KALLONSU YA RUGUZA YA DUGURGUZA YA FADI.....INDA DA YAWANSU SUN GAMA SAREWA CEWAR TASU TA KARE A YAU A GIDAN NAN, DADIN ABIN DAYA IDAN YA KOROKAN KO YA MAYAR DA KAI MAKARANTA KO YA BAKA WANI AIKIN BA ZAKA DAI YI ZAMAN BANZA BA

Lokaci daya ya ajiye hannayensa da abin cajetan a saman table din kafin ya dago hannunsa na dama ya daki table din da dan karfin da ya saka ta a firgice tana jan tsaki ta dago kanta a hankali ta saka idannuwanta masu dauke da launin abin barci a cikin nasa masu dauke da kakausan kallo da yannayin fushi a cikinsu

A tsorace ta zabura ta mike tsaye hakan ya sa yan dugwui dugwui din mamanta motsawa dan ba bra ta saka masu ba sanann dan kwalin da ta daurawa kanta ya kunce ya fadi saman dayan hannunsa dake saman table din kafin ta fito da sauri ta zagaye shi ta koma gefen kujerarta da aka ce tata ce ta zauna a rikice ta kuma mikewa tuna maganar Madame ta tsaya ta sada kanta hannayen nata a hade inda shi kuwa mai zai yi banda tsura mata ido mamakinta na neman halaka shi kafin ya mike tsayinsa gaba daya yana kara kare mata kallo dan idasa fitar da dukan abinda ya dace a hukuntata a kansa kafin ya kai hannunsa ya ciro yar Silent bindigar dake jikinsa ya direta a saman table din yana mai binta da idannuwan nan nasa tamkar zasu dauki mutun da kallo a dake ya ce"

More cmmnt.....more pags □□□□□□□□□□
11/14/21, 12:48 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 6 □□□

A mugun dake ya ce" Yaya sunnan ki? "

Muneerath ta dago innocent face dinta a sanyaye ta ce" Muneerath "

Bakin nata ya kala kafin ya yatsina fuskarsa ya gyada kansa da yan yatsunsa ya nuna mata wajen zama yana jira ya ga ikon Allah shin zaman zata yi ko meye?

Ai kam Muneerath, ta gyara tsayuwarta ta zauna abinta tana kara sada kanta, sai dai bata idasa zaman ba ta ji wata irin razananiya firgitaciyar tsawar da ta tabata har na wajen nan idan dai sunna ji Sun firgita da wannan tsawar,
Bata idasa mikewa a kan kafafuwanta ba ta ji an jijigota daga zaunen da take an yi baya baya da ita an hadeta da jikin garu kafin cikin yaren turancin da da kyar take ganewa ya shiga fadin" wacece ke? Me kike takama da shi? A duniyar mararsa kunya wani mataki kika taka? A duniyar yan ta'ada wacece ke? Ko a duniyar yan bariki awa nawa kike iyawa da namiji mai sunnan namiji?"

Da dan ihu ya karashe maganar hakan ya saka Muneerath rintse idannuwanta zuciyarta na dokawa tamkar zata faso daga kirjinta ta fito, gashi dai hannu ne mai laushi ya taba fatarta, ya makureta, sai dai abin takaicin hannun garjejen katon da ba muharaminta bane,
 uwa uba zafin da take ji a makurar nan tamkar za'a kasheta

A gigice ta buda tsumamun idannuwanta da suka tsumu da ruwan hawaye ta sauke a cikin nasa wanda yake binta da wani irin kakausan kallo wanda ya taru da tsagwaron tsana ,

Numfashinsa na dukan nata sakamakon irin matse mata wajen da ya yi , gaba daya numfashinta neman gagararta yake a irin wannan lokacin , jinta ya fara yi mata nisa kafin ta tsinkayo wannan murya tasa mai dauke da amo irin na zaki ya ce" Babu macen da zata shigo ni da raini dan ta birgeni da kowace irin halita take takama da ita domin a mace ba kalar da ban gani ba , ban ganta ba, ba'a haliceta ba, bale a filin aikina dukan mata maza suke a gabana!

 Tsagera kuwa ni babansa ne!, Dan ta'ada ni ubansa ne domin bana daukan kalmar ta'adanci, bama sasancin da dan ta'ada, kuma babu maganar sulhu ko yafiya tsakanina da dan ta'ada! Kin fahimta?" Ya idasa da wata tsawar da ta saka Muneerath kuma rintse idannuwanta kafin ta bude da karfi tana kallonsa

Zuru zuru take yi da idannuwanta kafin ya cikata ta samu didigenta a kasa ta karasa kasa ta zube gaba dayanta yadda ka san an jijiga bera an sake shi sai zarar ido take kamar ta zagi babar sarki , jikinta kuwa yadda ka san an jonna mata soket rawa yake gab gab gab kamar zazabin bana idan ya maka mugun kamu

Kamar ba shi ba ya gama hayaniyar ya juya ya koma saman kujera ya zauna a saman wace ta tashin yana gyara hannayyen rigarsa dan sun dan ja baya zuciyarsa cike da takaicin wannan rana da shi hanja ya kai hannunsa jikin mace ba dan ya yi having sex da ita ba sai dan yamata kashedi, ashe shima zai iya aikata wannan shirmen? Ashe shima aikata wannan shirmen na iya hayo masa kai tsaye? Tabas wanan

yarinyar ko yau ya maida ita kasarsu sai ya rubuta ya ajiye cewar ya kai hannunsa wuyan mace ba namijiba da nufi shaka irin na kashedi

Da sauri madame ta shigo ita kanta jikinta na bari, sai da ta ja kanta a sade ta bashi hakuri kafin ta yi wajen Muneerath ta kamata ta mikar da ita a sannu ta nufo wajen kujerar da ita

Da sauri Muneerath ta ja ta tsaya jikinta na bari ta kalli Madame tana girgiza mata kai ta ce" Me na masa? Kar ki kaini wajen cen kasheni zai yi kin ga bindiga ce ya ciro"

Ita dinma jikin nata na rawar ta ce" No baya kisa ba zai kasheki ba, aman rashin zuwan naki zai hadasa mana matsala baki dayanmu,baku yi maganar ba ai"

Muneerath wannan karron sai ta gama yarda cewa garin jarabarta ta kawo kanta wajen da zata rasa rayuwarta, ya salam wani irin basu yi maganar ba? A wannan maganar ai ya yi ya gama fadin komai kuma ta yarda ta dauka ina ita ina kokowa ko fada ko dayan abin da ya fada wa wannan mai karfin yan film din indian?
Sai dai tana ji tana gani madame ta karasa da ita auka tsaya bata zaunar da ita ba sunna jira ya basu damar zama

Kansa ya dago tun daga kan gashin kanta ya bita da kallo har kafarta kafin ya sake kallonta daga kanta ya dire a wajen tumbin da ya gani wancen karron ya ga yanzun babu shi ko kadan

Kansa ya cire a kanta ya karra hade fuskarsa sosai yana kallon yadda jocyline ke karra hade hannayenta tana karra bashi hakuri kafin da yar yatsarsa ya nuna tana iya zama

Da sauri Jocyline ta zaunar da ita kafin ta juya ta fita tana share kwallah ta tausayin kanta da kanta

Sai da ya gama shan iskarsa kafin ya bude litafin tambayoyin da aka tanadar dan a yiwa wanda ake tuhuma

A nutse ya bi rubutun da kallo kafin ya tabe bakinsa ya rufe ya hade hannensa cikin junna yana kallon yadda idannuwanta ke yin marmarmar ya ce" Ba a maki lesson na ducation ba?"

Muneerath ta ringa hanna kanta sob dagowa ta kale shi, aman cikin ikon Allah sai da ta ji gaba dayanta ta dago da dubanta ta kuma masa duba a karro na uku ido cikin ido

Nasa idannuwan ya cire a cikin nata, ba dan komai ba sai mamakin kwayar idannuwanta da kuma yadda suke da kyan kallo, du irin yadda take cikin tashin hankali basu nuna ba saima wani walwalwal da suke

A takaice ya ce" kin san wanene ni? "

Muneerath ta kuma bin gashin kansa da kallo a sanyaye ta ce" Kaine ka kawo ni daga garin mu, tare da matarka"

Da sauri ya kale ta jin ta ce da matarsa, matarsa kuma? Sai ya kuma cire duban nasa ya girgiza kansa yana ayana ya sani dama bata san waye shi ba, da ta sani du tsaurin idannuwanta ba zata iya fuskantarsa da yannayi na rashin kunya ba

Sai kawai ya ga ashe bata lokacinsa ne ya yi na yin hargagi a gabanta , yanzun tsakani da Allah idan na wajen nan suka fita suka yada yanda ya yi da yarinyar nan me za'a kale shi ? A ce masa me du ya tsalake manyan mutane ya zo kan sa'ar kanwar bayansa ya yi hayaniya?

Dan shafa gaban goshinsa ya yi ya mike tsaye ya dauki bindigarsa ya mayar jikinsa a dake ya ce" Mu je "

Da sauri ta mike tana kallon bayansa ta ga yadda nan da nan ya kai kofa a dan kankannin taku ta waiga ta kuma waigowa ta ga ba kowa bale ta arce ta labe a bayansa, ta ga ba dakin buya bale ta shige ta labe sai kawai ta bi bayansa jiki a mace tamkar kwai ya fashe mata a cikin cikinta

Daga nesa take kallon yadda gaba daya manyan wajen suka nutsu sunna gyada kai sakamakon maganar da ta kula yana yi da yannayi na bacin rai yana nunawa da hannunsa kafin ta ga ya dago dan yatsansa na kusan babar ya kada ya kuma kadawa ya yi wata maganar da bata fi biyar ba kafin ya ga du sun gyada kawunnansu a tare sunna amsawa sannan ta ga ya juya ya yi hanyar dogon coridon da zai fitar da shi waje

A hankali ta sauke ajiyar zuciyata bishi da kallon uma ta gaida asha, sannan a bayane cen kasa kasa ta ce" Who are u?"

" Muneerath tunanin me kike, wuce mu je na raka ki wajen motar, mu kam abin ya zo mana da sauki my munnee sai wata haduwar"

A dan firgice ta kaleta kafin ta ce" Mu je ina?"

Joyceline ta kaleta da mamaki ta ce" tare zaku tafi fa, ya ce kin gama formation din "

Muneerath ta girgiza kai ta ce" kai ina, na je ina? Haba kamar mahaukaciya na bi wannan mutumen mu je ina? Nononono ba inda zan je babu inda zani koda da bindiga a kaina, baki ga matse min wuyan da ya yi ba? Hala so kuke ya kasheni? Me na maku? Ku mayar da ni niger na fasa aikin na fasa walahi"

Wani katon soja ne ya zo fari ya tsaya ran nan a hade ya ce" Sir zai shiga mota fa mu je "

Da ido Muneerath ke girgizawa alamun ba zata je ba, sai dai daga ita har Joyceline din sai suka samu kansu da nufar motar da aka nuna mata zungwui zungwui tamkar zata fashe da kuka har suka karasa aka bude mata ta shiga motar da bata taba tunanin akoy irinta a duniya ba tana ta kyafta ido tamkar zata balo ta bala a guje dan firgici da tashin hankali

Ita kadai ce a bayan a zaune a wawakeken wajen, sai direba da soja daya a gaba hakan ya sa ta yi zama irin na zulumi, ta kurawa waje daya ido tana kalo a lokacin da motocin ke sharara wani matsiyacin gudu har suka karasa ainahin gidansa

Da ido ta bi shi har ya fice ya shige wannan waje na gilas watau falonsa kafin ta kuma duban sojojin da suka hadu suka baje ta ko'ina a wajen kowane ka kalla ba zaka so kuma kallonsa ba domin fuskokinsu sanye da mask, hannayensu da gam, kafafuwansu da manyan takalma hannayensu rike da manyan bindigun da ta tabata da alburusai na balaki a cikinsu

Ajiyar zuciya ta kuma saukewa wasu zafafan hawaye suka zubo mata a hankali ta dora hannunta ta talabe habarta da kumatunta kafin a bayane ta fashe da kuka irin mai karan nan ta ahiga rusa shi tana fadin" Wayo oga, wayo mamanmu, wayo yan uwana ku zo ku dauke ni daga wannan gidan kar su kashe ni, wayo Allahna na shiga ukunna ni ba yar daba ba, ni ba barauniya ba, ni ba karuwa ba, ni ba kisa na yi ba aman an tiso ni da bindiga an tare min hanya bayan an gama cin kaniyata, wayo na shiga ukunna garin nacin son zama Hostess zan zama gawa a garin arnawan da basa sallah bale au salaceni au kilaceni irin na musulmai, wayo ni wayo Allahna ni ta dogari yau kuma a nan na tsinci kaina? "

Hannayenta ta dora saman kanta sosai ta langwabar da kan ta dora da fadin" du wannan wulakancin kaine sanadi, dogari da ka nuna kana ra'ayina da na wuce wulakancin kowani namiji, aman sai ka tashi ka saka kafa ka haure ni ka kasa tunkaro ni ka kasa nuna min so, haka nake hakuri ina kallonka dan ba zan yi irin na yayata ba na nunawa namiji so ya dawo yana wulakanta ni ba, aman ba komai na tabata adu'a nake watarana zaka dube ni, idan kuma ka dube ni wannan garjejen sai ya yi dana sannin sanina, dan daraja ce da ni, ni ba kanwar lasa bace!"

Daga inda yake zaune gaban computer dukan bayananta yana ta saurare ne ba tare da yana gane yarenta ba, daga kasa kuwa dankareriya zakanyarsa ce ke kai kawo tana kada bindinta irin yau a farin ciki take ga wanda ya ajiyeta ya dawo daga yawace yawacensa

Da sauri ya shiga dadana computern nasa yana ta aikin neman yarikan kasar Niger
Nana da nan aka gabatar masa da yarika na kasar niger kwaya takwas daidai

HAUSA

ZABARMANCI

FILATANCI

BUZANCI

TUBANCI

BARBARCI

GURMANCI

Larabci

A nutse ya ci gaba da aikinsa ya nemi translate app na yare kala daban daban
Kasancewar duniya ta ci gaba, abubuwan ci gaba na duniya sun rigaya sun cika duniya, ya sa a zaune da yake a saukake ya samu mai amon murya cikin kwarewa da iya aiki da computer da bincike bincike ya saka wannan yare nata a layin translate na yarukan nan banda larabci domin ya tabata ba shine take yi ba kafin ya mike ya nufi ciki dan ya samu ya yi wanka ya dan taba wani abin

Hankali kwonce ya yi dukan abinda ya saba ga zakin nan du inda ya bi yana biye da shi haka kuma yana mata hira yana dan murmushi itama takan dira ta ringa markayarsa tamkar ta samu jikin dan uwanta zaki, shi'q hankali kwonce ba da tsoro ba yake biye mata har ya cenza kayan nan zuwa sweet maau ruwan Ash ya daure da nekti mai ruwan blue da baki baki ya saka bakar safa da bakin takalmi ya caje

gashin kansa ya saka bindigarsa yana aikin mika ta ainahin abinda yake missing wanda rabonsa da mace a kadan ya dauki wata biyu sakamakon irin tafiar da suke yi shi da iyayensa inda mamansa ke mugun saka masa ido da nasihohi kala daban daban

Tsayawa ya yi yana daura agogo ya saki murmushi gannin zakanyarsa ta nufi wajen kofar fita tana kai kawo kafin ya girgiza kansa a ransa yana ayana 'wai dabama ta san ra'ayin kanta'

Tsayawa ya yi facing din tankamemen madubin falonsa haka kawai ya zo wucewa ta wajen

A hankali ya dan gyara gashin kan nasa kafin ya lumshe idannuwansa ya saki dan murmushi a fili ya furta" Aure zan je nema"

Sai kuma ya dan daga kafada ya nufi wajen computern dan ya tabata zuwa yanzun dukan bayanan da ya dace ace ta yi ta kwatanta zai saurara ya ji yanda ya kamaya yi da ita, ya gama mata shirinta ne idan har dan ta cuci mamansa ne ta biyo su a yau a nan zai harbeta kowama ya huta, idan ya so ya turawa kasarta labarin ta mace, in kuwa bai ga haka ba dole zai kaiwa Mah ita a yau, daga baya ya ci gaba da bin dukan motsinta dan shi sam baya da saurin yarda da kowa a duniya!

Kasakai ya yi da baki yana sauraron shirmen da computer ke fadi a lokacin da ya dana ta karanta masa abinda ake fada, sai dai bata fasara sunnan dogari ba, hakan ya sa ya dafe goshinsa cike da jin haushin bata lokacinsa ya nufi waje da zakanyarsa yana furta "Yanzu haka bata da hankali ganewa ne ba'a yi ba"

Ido ta kwalalo gaba daya a lokacin da taga yadda zakanyar nan ke ta makalkalarsa tana juyi a jikinsa

Idasa sauka ta yi kasa tana rike fitsarin daya gama fara fitowa a mararta tana zarar ido ta ce" shikenan zaki ne ajalina.....

□□□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:48 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□

shige ciki ko kuwa ga yi tafiyarsa abinsa hakan ya sa ta juyo ta dan watsa hannayenta ta ce" Wani zaki? "

Muneerath ta kikifta ido a sanyaye ta ce" Shi zakin da ya kawo ya cinye ni, sunna ina?"

Sai a lokacin Mah ta fara dago zancen, sai a yanzu ta karra lura da irin tsabar firgicin dake tare da Muneerath,

lebenta na kasa ta dan cije tana girgiza kanta a hankali ta karra mikaea muneerath hannunta ta ce" Babu zakin da zai cinye ki, kin baro zakin a cen gidansa, taho mu shiga ciki "

Muneerath ta ringa sauke ajiyar zuciya zuciyarta cike da mamakin irin ci gaban da duniya ta yi, dan har ga Allah a tunaninta wannan mota mai kama da dan daki bacewa ta yi ta bayana da ita a nan

A hankali ta dora hannunta cikin na Mah kafin ta zirro kafarta waje ta karasa fitowa gaba dayanta tana dan zarar ido

Da sauri ta rike hannun Mah tana karra bin irin tarin matan da suke tsaitsaye da kallo , muryarta cen kasa ta ce" Ina ne bayi? Ina son zagayawa"

Mah ta dubeta, kasamcewar mace ce kuma yarinyar da ta tabata ta haifi kamarta sai ta bi jikinta da kallo gannin rigarta fa a jike daga kasa

Cire dubanta ta yi ta jata suka shiga tankamemen falon da sanyinsa kadai ya saka Muneerath jin dan lisilama danma shi oga zawayi ba ruwansa da sanyi ko zafi , idan fa ya karta a kaishi a zubar ko ya fito da kansa dan kuwa shi bai san wata kalma ba wai hakuri ko kunya ba hakan ya sa ta ringa bin Mah da sauri sauri sosai har suka shiga accenceur ya yi sama da su suka kuma mika dan dogon coridor kafin su shiga wani dakin da bata iya gane komai ba zuwa lokacin dan ogan ya fara dan tsartuwa a guje ta nufi bayin da aka nuna mata kan shine wanda zata shiga ta aiwatar da uzurin da ya kamata a yanzu yanzu

Wollah, da ba dan ta jima a garin ba, ta kuma iya gane ramin masai a zamanta da su ba, da babu abinda zai sakata hawa wannan waje mai walwali ta zubar da dati
Kai jama'a, mutane duniya na inda take, yo wannan abin idan musulmi nada hankali an ce aljannah ta fi karfin tunanin bawa ai zai dage dukkan karfinsa ya ringa ibada dan ya ga wannan iko na Allah, haka kuma wanda ke cikin irin wannan idan ya yi wasa ko sallah ba zai yi ba, zai shagala da shagalalan wajen nan ne har sai ya ji guduma a saman kansa ya jishi a matsatsen rami kafin ya gane cewa da gaske fa mutuwa zai yi

Ido ta lumshe tana amayar da ogan mai kukan tsiya wanda yake tafe da damuwarta,
A hankali ta ringa jin sansanyar iska na kadata a lokacin da ta samu nutsuwa hakan ya sa ta ringa buda idannuwanta dan gannin ko a nanma akoy AC ne?
Ai kau akoy din sai dai ba a kunne ba, kawai nutsuwa ce irin ta idan ka gama zubar da wahalar nan hakan ya sakata sakin sansanyan murmushi tana yiwa Allah godiya da bata yi a jikinta ba

A hankali ta gama , nan fa tsaftar ta tashi domin bayan ta wanke da sabulu ta kara wankewa da ruwan dumi sai ta kasa mayar da komai nata daga pant din har rigar, gaba daya sai kyankyamin kayan ya sakata jin tamkar zata kelaya amai

Da sauri sauri ta tara ruwa ta shiga wanke su ba tare da ta tuna komai ba, har sai da ta masu ruwa hudu sannan ta matse su ta karasa ta cire tawul din da ta daura a kugunta ta wanke wajen tas sannan ta shige ciki ta tara ruwa masu dumi sosai ta zauna ta dauki sabulun nan ta shiga darzar fatarta da shi kadai mr spcly wajen da dan fitsarin nan ya bata mata na jikinta du ta wanke har sai da ta ji tana kanshi sanann zuciyarta ta aminta da tsaftar jikinta kafin ta fito tana mamakin kanta irin yadda ta yi wankan nan a wajen nan ba tare da ta wanke ba bayan du tsaftar waje sai ta tisa masa kafin take anfani da wajen

Kafadunta ta daga irin na oho din nan kafin ta dauki wani tawul din kuma ta ja ta tsaya cike da tunanin yaya zata yi ta fita

Mah dake zaune cikin zulumi take

Zulumin da take cikinsa na gannin kanta ba dan kwali da kuma fitsarin dake jikinta
Lale ta san na lalura ne, ba da gangan zata yi fitsari a jikinta ba, abinda ya fi damunta daya ne irin yadfa zata fito mata, shin da rigar zata fito a jikinta ko babu?
Ita mah a duniyarta abu daya ke wahalar da ita shine tsafta, mace ce mai kuguwar tsafta, sannan mace ce mai riko da adinninta, du irin yadda dunia ta rikice ita ta ki ta dauki maganar cewa wai yanzun yan mata basa son saka dan kwali ba, sosai ta zauna cikin tunani bayan ta dauko mata wasu suturun da dan kwali tana jiran fitowarta,
Babar damuwarta shine bata san ta yadda zata zauna da kazamar yarinya ba
Na biyu kuma shine sam bata iya zama da mutumen da baya son rufe suturarsa ba, duda yaronta ba mazaunin gidan bane idan ya ga dama yake zuwa in ya ki kuma baya ko leko su sai dai ita ta je, aman sam bata so ta ga ana yawo ba dan kwali dan ko christocin gidan da yan dan kwalayensu a kawunnansu idan sun hau aiki, idan sunna so in sun tafi gidajenau su cire abinsu

Da sando ta fito da sauri ta ja shinfidar gadon ta aniya cikwuikuyewa a jikinta cike da jin kunyar matar nan wai dama tana nan? Allah sai yanzu ihun kukan abinda ta zubar a masai din cen ya ringa dawo mata hakan ya hadasa mata matsananciyar kunya har ya kasa dago kanta da kyar daga tsayen da ta cuimuimuye ta samu ta dan fitar da fuskarta ta kai dubanta kan Mah da fatan ta bar dakin

Ido hudu suka yi, hakan ya sa Muneerath rintse nata idannuwan a sanyaye da yaren turanci ta ce" Ki yi hakuri, ba da gangan ya kubce min ba, nama wanke kayan na matse su, kuma na yarda mayafina a cen makarantar da mijinki ya dauko ni, dan Allah ku yi hakuri idan wani laifin na maku"

Mah ta saki murmushi tana jin gamsuwa da nutsuwa da bayanan Muneerath kafin ta kuma yin murmushi ta mike ta nufota rike da kayan nan ta tsaya a gabanta kafin ta ajiye a saman bed din dan shinfidar ta zannin gado hudu ce na saman kadai ta yayuma

Dubanta ta yi ta kuma sakar mata murmushi ta ce" Ki cenza kayan ki, ki yi sallah, za'a kawo maki abinci ki ci, sai ki kwonta ki huta kin ji? "

Muneerath na kallonta da mamaki bata iya cewa komai ba

Har ta juya ta dawo ta kama hannunta ta cikin zanin gadon ta ce" Bama kisa, sannan d'ana ne ba mijina ba "

Tana gama fada ta sakar mata hannu ta juya ta tafi tana murmushi

Sakalau munnerath ta yi da bakicike da mamakin dake nemn kasheta kafin ta shiga tafa hannu a bayane ta ce" To ko dai da aka ce a inji ake kyankyashe su hakan ne? Ko kuma irin y'ayan nan ne na kwalba shi din shi yasa ya yi saurin girma?".....karshe dai a hakan ta ajiye ta gyada kanta kafin ta girgiza ta shiga saka suturar ta abaya fara ta kuma furta" Gaske yannayinsa sam ba na mutun bane, ashe shi din mutumen nasara ne gaske hannaye kamar an busa balan balan an saka masa ga karfi irin na aljannu.....Allah dai zai saka min yanzu haka na girme shi a haife ya shake ni munahiki kawai!".....

"Dama har haka suke da iko? Aman ko shi ya kawota a kasar nan na zata dan adam yana da yanci shakar da ya yiwa yarinyar nan ban zata idan na shiga zan ganta a tsaye ba, tunda suka tafi kuma na kasa zaune na kasa tsaye, shin idan fa ya kasheta?". Madame joyceline ta fada bayan ta gama sauraron bayanan jujun dake kare yancin yara da matasan kampanin nasu
Gaba daya ta kasa samun nutsuwa, ta sani sarai wannan abin da ta yi yana iya jaza mata baban balakin da ba zata iya kokowa da shi ba, aman ta jajirce ta dauki risk ba dan komai ba sai dan ta kuma san kasa suke ta yancin kai, yarinyar nan kuwa ko a musulmai ta shiga ranta sosai dan yarinya ce mai dadin zama, gudun nan da suke yi tare sosai ta ahiga ranta, a kasar nan kuwako uba ka kula yana takurawa dansa kana iya shunawa iko su kama shi ram a tuhume shi, idanma gaskiya ne kana iya yin kaso, ko tara mai yawa sanann a amshe rikon dan daga hannunka

Murmushi ya mata bayan ya dan shafa kansa ya ce" meye hujarki na ita din yar kasa ce? Sannan menene hujarki na ba ainda ta yi masa?"

Dan kikifta ido ta shiga kafin ta ce" ta nuna yannayi na innocent"

Kansa ya girgiza ya ajiye byronsa ya ce" Aman yaya aka yi aka baki mukamin nan? Har yanzu baki daina anfani da yannayin mutun ba ba tare da kin yi bincike ba?, Madame da gaske kike saboda yannayinta kika dauki wannan baban risk din MR HANJA ba aiki yake da iko ba shine iko, kina magana da a je a tuhumi sarkin garinki na nan da dan watani kan abinda baki da tabas dinsa? Kin san da dole za'a ambaci sunnanki a gabansa? Kin san da idan lalube kike ba gaskiya bane ni da kaina da kika saka kin saka ni a matsala? Kin fi kowa sannin Me Hanja baya daya daga cikin wa'inda muke neman laifinsa ido rufe domin shi din shi ya fitar da hukunce hukuncen bima mai haki hakinsa , shin zai yi gangancin takewa kuwa? Na san dan adam kowa nada abinda yake boyewa, aman idan har wannan da zamu yi ba shine abinda yake boyewar ba kin san da mu zamu zama boyayu domin lauyansa sai ya yi yadda ba za'a kuma tunawa da mun rayu a duniya ba domin ina mai tabatar maki lauyansa Mockar sai ya goge harta da labarinmu dake cikin yanar gizo dan wasa muka yi da ZAKI!?"

Ya karashe yana kallon yadda du ta rikice kafin ya ce" idan kuwa haka ne mun ciri tuta, zamu yi aunna sannan mu yi kudi, zamu samu mulki domin zamu kasance da masu mulkin, idan har kin yarda da maganarki ba damuwa sai mu fara shigar da kara da camerar abinda kuka dauka a lokacin "

Sai a lokacin wara zufa ta fara tsatsafo mata, a hankali ta zauna cike da tsoro tana tuna kashedin da ya masu na su guji fitar da maganar hannunsa ya taba mace dan gargadi domin yana jin kunyar a ji mace ce ya taba da hannunsa ba namiji ba,

Lokaci daya kuma ta tuna da baban sojan dake bashi kariya ya cire gaba daya vidion abinda camerar ta dauka

Wani yawu ta hadiye da ta tuna Muneerath ta sanar mata cewa tun daga kasarsu ya daukota, a hankali ta shiga girgiza kanta kafin ta mike da sauri ta bar office din cike da dana sannin zuwa da wannan maganar da fatan kar ta je ko kunnen karen gidansu ne!

_____

"She look so so so ya rab she look tn a prncss khalb" ta fada a sanyaye a lokacin da ta kai masa kofin maganinsa ta surba masa a bakin nasa

Murmushi sarki ya yi yana kallon HANJA da yake rike da kofi na kwalba wanda aka zuba wani dan tsurut din jus , hannunsa daya kuma rike da remot ya rage kukan TV din sosai ya maida kallonsa kan Mah ya ce" Yanzun y'ayanki mata biyu, to ita iyayenta suka baki ko cirowa kika yi?"

Murmushi ta yi ta bude rubutun da take shafa masa a kansa mai hade da su ruwan zamzam da su jibda ta diba kadan ta ahiga shafa masa ta ce" Allah ne ya bani,kuma ka ga ka tambaye shi hala shuna mata Zakin nan nasa ya yi?"

Yarinyar dake wajenta ce ta fito mai sunna Iman, sanye take da doguwar riga irin na dubai din nan, sai dai ba yane mayafin ta yi ba a kafadarta yake ta masa irin yadda indiyawa ke yiwa mayafi, ta tufke gashin kanta a bayanta ya mata lufluf abinka da jinnin larabawa

Yarinyar ruwan kyau tana da shi,

Tafe take a hankali gaba daya idannuwanta a kansa hakama tunaninta da hankalinta, ga hannunta dauke da butar shayi da ta dafo Percil din Sarki yana turiri Sam bata san har ta iso kusan dan table din dake dauke da litatafai irin na adini a sama ba, sai da kafarta ta daki wajen ana dayanta ta tafi wajen da Hanja yake zaune ta.....

Comment dinku na kashe ni, ina ji da ku ainun
11/14/21, 12:48 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 8 □□□

Gaba dayanta ta yi wajen da Hanja yake zaune domin nan table din ya wurgar da ita

Ido ta rintse tare da fasa ihu cike da tunanin ta kade har buzunta idan har ta idasa sauka a jikinsa, hakama shayin sai ta nemi azamar neman wurgar da shi gefe daya dan ba zata ao hasaso irin abinda zai iya samunta idan har ta dira kansa da wannan ruwan zafin ta tabata sai dai wata ba ita ba

Mahaifinsa ne ya fara mikewa yana furta" Subahannalah "

Mah da ta rintse ido gabanta na dak dak dak ta bude a hankali dan gannin mai afkuwa ta afku nan ta ga ikon Allah, HANJA ya tareta da abin dake hannunta na dan sekwani ita kuwa tar dubanta a kan fuskarsa tamkar kallon jaraba ta kasa cire duban nata a haka har ya cire butar a hankali kafin ya saketa daga kwonto masan da ta yi sakamakon shagalar da ta yi da kallon fuskarsa ta zube kasa gaba dayanta

Sai a lokacin ta ankare da irin kallon da take masa, lamari na zuciya mai saka bawa yin abu irin na rashin sannin ciwon kai ko mai kamun hauka sai ta kuma raka fafadan bayansa da kallo a lokacin da kama hannun Mahaifinsa ya mayar da shi zaune sannan ya dan rage tsayinsa ya mikawa mamansa butar shayin ya sakar masu murmushi ya juya ya fice a falon baki daya

Sai da ya bacewa ganninta kafin da sauri ta kai dubanta kan Mah da Pah
Bata san lokacin da ta mike da gudu gudu ta bar wajen ba cike da jin kunyar irin kallon nan, cen kasan zuciyarta kuwa cike da begen wannan bawan Allah, walahi har ajiyar zuciya kwace mata take idan har tana kallonsa, bata gajiya da kallonsa a kowani lokaci.....

Barci Muneerath ta sha cike da nutsuwa, duda cenjin waje bata kasa rintsawa ba domin dama ba wai koshi ta yi da barcin nata ba dole aka tasheta

Kiran salar da ya sauka a dodon kunnenta ya sakata farkawa cike da matsanancin mamaki ta je wajen Windows tana lekawa sai dai bata ga inda masalacin yake ba hakan ya sa ta yi bayi da dan sauri da daura alwallah

Sai a lokacin ta ga an shanya kayanta a nan cikin bayin, ita dai ta dauro alwalarta ta fito da sauri ta dauki hijab din da ta yi sallar dazu ta gyara ta kabarta sallah

Tana gamawa ta ci gaba da zama tana adu'a idannuwanta lumshe hakan ya sa sam bata ji shigowa ba har sai da ta gama adu'o'inta ta shafa sannan ta buda idannuwanta dan cikinta fa kiran ciroma yake domin a dazun bata ci abinda aka

kawo mata ba dan ita ba sanninsa ta yi ba tsakani da Allah, gashi yanzun bata da tumbi ba zata ringa fadawa komai ba ta yi tumbi haka kawai

Murmushin da Mah ke yi mata ya sakata dan yin sakalau a ranta ta ayana' ta ina ta shigo? Na shiga uku ita kuma wannan sai fara'a kamar wace bata da damuwa a dunia? Koda yake ina ita ina damuwa matar dake rayuwa a wannan gidan ai ko ita da ta shigo dazun ta sha barci sai da ta farka ne oga da mamansu da Dogari suka fado mata a rai'

A hankali ta ce" Ina yini "

Mah ta kuma sakar mata murmushi ta mike ta karaso inda Muneerath ke zaune sakalau da baki tana kallonta

Hannunta ta mika mata ta ce" Tashi mu tafi falo, ke kadai a daki ga abanku cen da kawarki a zaune "

Ido Munnerath ta kuma kiftawa a bayane ta ce" Wata sabuwa "

Mikewar dai ta yi dan bata iya saurin musu ba tana biye da ita tana shakar wani siritacen kamshi da take bazawa har suka ratsa wani corridor din kafin suka fito wata duniyar da ta saka Muneerath idasa sarewa rayuwa, kai jama'a ina ne nan? Wayo Allah ina ne nan? Sai ta ji gudun zuciyarta ya fara fin bugun normal, da sauri ta ringa saisaita numfashinta tana kale kale kafin ta sauke dubanta a kan datijon dake zaune d jalabiya fara tas shi din kansa fari kal da shi sannan fuskarsa dauke da yalwatacen murmushi da alkur'ani a hannunsa mai girma ya bude yana karantawa a bayane shigowarsu ya dasa aya ya bisu da murmushi kafin ya budi bakinsa a nutse ya ce" Marhababuki yar Mah "

Muneerath ja ta yi ta tsaya a hankali ta ce" Ina ne nan? Ku din su wanene ku? Dan Allah ki sanar min ko zan samu nutsuwa "

Iman dake kallonta cike da mamakin kokari irin na mamansu haka kawai daga gannin yarinya ta kwasota yanzun har falon Sarki yanzu ta mayar da ita kamar yar gida dan rashin tsoron mugwayen mutane, ita kawai haka take tunaninta yadda take haka kowama yake

Mah ta nuna mata wajen zama kusa da Iman dake zaune a saman lalausan kafet din kafin ta karasa kusa da mijinta ta zauna sosai ta ce" Wannan da kike ganni shine sarkin garin nan baki daya, ni kuma matarsa ce, wannan kuwa yar yar uwata ce, yaronmu kuwa shine wanda kika ce ya kawo ki watau HANJA"

Muneerath ta kwalalo ido tana kallonta kafin ta kuma bin su da kallo ta dire a kan Iman dake kallonta

Kaii ta gyada a bayane cike da mamaki ta ce" Sarki kuma? , Sarauniya ce ita? Aman sarki a gansa haka a dasha? Kai ko a garinmu sai a ce ana takama kamar wani sarkin ingila....."
Shiru ta yi ta kuma dubansu gaba dayansu kafin ta dafe gaban goshinta tana girgizawa wannan karron da yaren su watau turanci ta ce" Dama sarautar kasarku haka take? To ina ahalin gidan sarki? Ina su dogarai? Ina dawakai? "

Mah ta ce" Ahalin gidan nan sunna nan cike , basa zuwa nan ne dan basu da wannan damar, dawakai kuwa sunna bangarensu watau ranch, Dogari kuma ban san mene haka ba"

Sai a lokacin ta tuna dogari ta ce da hausa dan haka da sauri ta fada mata cewa masu gadin gidan sarki

Mah ta yi murmushi , sam bata ajiye haka a matsayin kauyanci ba domin idan ba zata manta ba a lokacin da suka je niger ta ga abubuwa da yawa da suka bata mamaki harma ta yi ta tambaye tambaye ana bata amsa a bayane, hakan ya sa ta ajiye Munnerath a matsayin wace ke tambaya dan ta karra sani, sannan ta ringa bata amsa a bayane ta yada zata fahimta, daga karshe dai ta mike da kanta ta kuma kashe Muneerath da wani mamakin a lokacin da ta umarce su kan su tafi kicin

Bata yi kasa da gwuiwa ba sai da ta samu kanta a wani dakin mai dauke da abubuwan aikin kicin wanda ake mata nufin cewa kicin ne duniya guda , sannan ta kuma zubawa wannan mata mai mukami da daraja a duniya baki daya tana kallo ta zagine tana yanka wata kalar albasa ba irin tamu ba domin wannan tasun wata jajawur ce da hannayen nan nata masu laushin na jariri bayan ta saka gan sannan wannan balarabiyar yar tata yar zumunta mai shegen kyau tana yanka mata tomatiri ita kuwa aka miko mata nata gan din da leda mai dauke da zabi fara kal ledar da kwano kan ta gyara sai ta ji wani takaici da zuciya irin ta mata sun motsa, haba ina ai nan da nan ta ji idanma aka bar mata zara iya dafe komai dan kuwa in dai wadinnan larabawan suka iya girki suka barta ta ji kunya ta dirko kasa ba nauyi ta ba batan africa kunya (ehem)

Kamar da gaske ta zagine ta gyara zama a saman kujerar dake kusa da dogon table din ta saka wukar nan ta cira ledar
Zabuwar daya ta ciro tana binta da kallo, ita dai ba gashi a jikinta ko dis, sannan ba abin nan mai saka karnin miya a jiki, aman gaba daya sai ta mata girma fiye da tamu ta gida, ta zama kamar wata dan jariri ,
Kai ta dai samu ta karasata cikin kwanon ta kuma rike wukar ta zuba mata ido tana kallonta, walahi bata san ta inda zata fara sukar zabuwar nan ba, asalima bata san idan har ta yankata bata bata miyar ba.....a hankali sai ta afka duniyar tunanin aminiyarta Amina, da kuma Kawarta saudat kafin murmushi ya bayana a kan lebenta tana ayana inama ace sunna tare, yau da an sha miya alkur'an

"Munnerath ?" Mah ta kuma fada tana kallonta

Firgigit ta yi ita dinma tana kallonta kafin ta mika mata wukar da kwanon da ledar domin hannu ta miko dan ta gama karantar bata iyan bane har yanzu,duda da wuya a koya mata dafa kaza aman ai mace iya girki ne kau? Ita kam zata yi iya kokarinta har Allah ya raba su dan gannin ta iya girki, hakan ya sa da zata juya ta koma gefe ta tsayar da ita ta shiga yanka zabuwar nan tana mata bayani cike da murmushi da fara'a har ta yanke su sannan ta hada su percil da su celerik da garlic aka zuba cikin wani inji inji ya zubo su a dake luf sannan aka cakuda da au mutarde da dan gishiri aka cakudewa zabin nan kafin suke zama su dukansu au dora yar hira, inda hirar gaba dayanta Mah ce ke janta su tsakaninki basu yi sabon da zasu yi hira ba sai dai su yi murmushi kawai

A kadan ta dauki kwana goma tare da wannan ahali bata leka ko nan da kofa ba tana gannin wata irin rayuwa ta mamaki

Soyaya bayananiya da ta badini ke wanzuwa a tsakanin ahalin nan , irin kulawar, irin yadda matar gidan ke tsaye kan kafafuwanta, da irin yadda wanda yake sarki ne ke tafiar da tasa mu'amalar da dukan wani wanda ya kwana ya tashi a cikin gidan bake wanda matarsa ta kira da yaronta shima zai kire shi ne da yaronta, a lokacin ta ringa

tunanin wai dama haka sarakan suke ko menene? A lokacin ta ringa tambayar kanta shin sunna da wani boyayan hali ne da suke boyewa a gabanta ko menene domin wannan zaman lafia da kwonciyar hankali na bata mamaki fiye da tunanin mai karatu, shin su basu da damuwa ne? Menene sirrin haduwar kan ahalinsu? , Komai na ba Muneerath mamaki a wannan gida domin a nasu ba haka ta saba ganni ba, a anguwarsu kuwa yayan gidansu idan suka fita har daga kai da tinkaho suke ana kada masu taken yayan mai kudi dan kawai Oga ya kekyara gini ya zuba su ba tarbiya!, Tabas idan ta ga Mah na girkin abinda su yan matan zasu ci takan ji wani iri domin ba abinda suke ci Sarki ke ci ba, shi nasa girkin tana girka shi ne da sinadarai na magungunnansa sai an zo ci a yi ta daru ya ce sai dai ya ci nasu mai dandanon kayan dadi ita kuwa tamkar jaririn goye ta ringa lalaba shi kan ba zai ci nasun ba a saman makeken table din cin abincin gidan
A kwana goman nan kadai da ta yi da su ita da kanta ta dafa shayi wai ita Muneerath ya kuwa yi mata mahaukacin dadi a bakinta duda Mah ta ce kayan hadin sun yi yawa, watau kayan dafa shayin sun yi yawa ita dai dandano ta ji ram

A kwanakin bata hadu da kyama, ko hantara ba, bata hadu da lukucin dansu ba, aljana ce ta duniya ta samu wace bata hannata tuna gidansu a dukan motsinta ba, wannan yannayi na rayuwar nan ya bata sha'awar da idan ta tuna nata iyayen sai ta labe ta fashe da kuka, akan tambayi kanta anya a yanzu Mah zata iya wuni bata ganta ba bata nemeta ba? Aman gashi wa'inda suka fi kowa sannin ciwonta suka kawota duniya sun manta da labarinta, tana da buri a rayuwarta bayan na dogari da zama hostess wanda suka haifar mata, shine ta ganta a gaban Oga da Mamansu, tana so ta masu tambayoyin da take da bukatar amsoshi, gaba daya ta kasa ajiye tunaninta waje daya, shin matan oga da aure da aure su?, Shin da gaske su suke haifo y'ayan su?, Shin da gaske musulman suke har yanzu ?, A in malsarar take a zamantakewar ne ko a tubalin zamantakewar ne? Watau ginnin auren..... Da yaya oga yake neman aure?, Shin ya yi koyi ne da fadar ma'aiki kafin ya sama masu iyaye ko ya gani ya kyasa yake yi? Da wannan zulumin ta kwonta da kuma zumudin wai gobe zata fara aiki
Hakan ya sa tun karfe biyar ta farka a barci ta yi wankanta na mamaki ta kuma gabatar da salarta sannan ta dauki man da take
11/14/21, 12:49 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

2 □□□ 9 □□□

Shafawa ta shafa cikin nutsuwa ta warware gashin kanta a hankali ta shiga binsa da kumb tana caje shi
Sai da ta gama caje shi ta dauki ribom zata saka Mah ta shigo hakan ya sa ta gaisheta bayan ta rage tsayinta sosai

Wannan gaisuwa a kulun itama mah din sai ta birgeta, ta kula irin nasu ladabin ba'a gaishe da baba a tsaye kikam, hakan sai ya birgeta sosai ita kuwa sai ta matso ta yi mata irin nasu na larabawa watau ta rungumeta

Ribom din ta amsa ta nuna mata wajen zama, hakan ya saka Muneerath zuwa ta zauna ta dan hade jikinta tana jiran gannin abinda zai faru

Ai kam Mah ta hade gashinta ta kame mata shi a tsakiya sannan ta tufke mata shi simple ba da wata kwaliya ba ta nade mata shi a kanta

Kwali ta ciro sabo ta fitar da shi tana kallonta ta ciro tsinken ta kamata ta zira mata shi
Ai kam ido ya kama ruwa ya ki ya bude sai rawa yake da kyar ta daina murzarsa Mah na mata daria har ta daina jin mugun zafin sannan ta saka tissu du ta goge mata bakin kwalin kafin ta umarceta kan ta saka suturar ta ma'aikatarta

Sai da kwallah ta zubo mata a lokacin da ta saka wando kalar fari da dan sket a samansa ta saka rigar ta saka safa ta saka takalmin kafa ciki mai dan karamin tsini sannan ta kalli madubi

Mah ta juyo tana murmushi ta dauki dan abin na wuya ta zagaya ta daura mata shi sannan ta dauki dan karamin fari kal din dan kwalin ta nade mata gashin kanta da shi
Murmushi ta yi mata a hankali ta ce" Masha Allah "

Muneerath ta kalli Mah sai kawai ta fashe da kuka ta dora kanta a saman kirjinta tana yi , ita kuwa Mah na dan tapping din bayanta sai da ta yi ta more sannan ta dago da dubanta tana kallon Mah

Mah ta ce" Ki ce Alhamdulilah"

Munnerath ta gyada kai a hankali ta ce" Alhamdulilh "

Mah ta ja hannunta kusa da bed ta zaunar da ita, itama ta zauna kafin ta ce" Muneerath, a kowace ma'aikata akoy bata gari, akoy na kirki, a cikin manyanku akoy wa'inda sunna nan ne dan su lalata rayuwar yayan mutane ba tare da jin komai ba, basu da haram fa, Muneerath basu da haram domin sunna iya nuna maki soyaya ce suke maki sunna sonki ne zaku yi soyaya ne dan su samu ku yi kyakyawan karshe irin na aure , aman kuma abin takaici karya suke,karya suke yi maki Muneerath ba abinda suke so sai su cinma abinda ke boye a cikin pant dinki, baban burinsu su mayar da ke karamar karuwarsu wace idan sun zo office gaki a kusa sunna iya zubar maki da datin su, Muneerath baban abin takaicin ba dagake zasu tsaya ba domin ba a kanki suka fara ba, kema zaki zamo ne hanyar da zasu hau su bi cikin garaje da iko ba tare da sun biya ko sisin dalarsu ba....."

Ta kamo hannayenta ta rike ta ce" Hakan na saka mu iyaye a cikin zulumi da tashin hankali, da ace zamu iya hanna aikin da mun hanna harta mazan fita nema....., Sai

dai hakan ba zai yiwu ba dan kuwa a yau ilimi anfani ne da shi koda na iya zama da mutane ne,"

Habarta ta kama ta dan dago da dubanta ta ce" Muneerath, zaki hadu da mutane kala daban daban a aikin ki, zaki hadu da na kirki da na banza, aikin ki na iya sakawa ki kwana a wata kasar, wani sa'in kina iya yin kwana biyar ko sama da haka, kin ga idan ke din mai sake ce komai zai iya faruwa da ke....."

Hannayen nata ta kuma jimkewa sosai tana kallonta ta ce" sai dai ina so ki kasance wace ta san ciwon kanta first, ki ringa tunanin cewa idan har kika yarda aka lalata maki rayuwa da farkon fari kanki kika yiwa, Muneerath kanki kika fara wulakantawa, rayuwarki kika tozarta , Muneerath zai bi har yayanki, zai bi gaba daya ahalinki har jikokin jikokinki domin daraja na shafar iyali,..... sannan idan namijin nan ne kika biya ya rude ki ki sani alherin dake tare dake yake yiwa zai gama da shi ya kuma damki na wata kina ji kina gani namijin da ya gama sukuwa a kanki yana murmushi gaisuwar kirki zata gagare ku domin zai dawo kyamatarki ke ya ga damar ya zageki da ke din mazinaciya ce yar iska ce bayan shi ne ya iskantar da ke, harma zaki kula da kunya yake a ga yana maki magana.....wannan shine shari irin na mugun aikin nan, ya fi bibiyar rayuwar ya mace Muneerath, sannan sai ki tuna wanda ya halice ki, shin a rayuwar da ya baki, da lafia, da hankali, da wadata ya cencenci ki saka masa ta haka? Shin idan kina da bukatar namiji ba aure ya fi cencenta ki yi ba?, Idan kuwa wani abin duniyar ne akoy wanda ya isa ya baki ba tare da gori ba bayan shi? Kin roke shi bai baki bane? Ko bakya iya rokarsa ne?.....idan kika mutu me zaki ce da shi? Idan bakya jin kunyar kowa ki ji tasa!,
Sai kuma iyayenki, Muneerath sunna da haki a kanki, shin kina so ki yi abinda Allah zai kama su da shi sannan duniya ta yi ala wadai da su?, Daga su a gangaro kan wa'inda suka amshi amanar horar da ke aikin nan....har zuwa kaina da na amshe ki kike hannuna, Mubeerath muma muna rokon ki da ki rufawa kanki asiri ki kame mutuncin kanki na y'a mace ki yi aikin ki domin Allah domin aiki kika je yi a duniyar jirgi ba yawon ta zubar ba, Muneerath aiki kika tafi yi ba wulakanta kai na, Muneerath burinki muka baki damar cikawa ba banzatar da kai ba, domin ke din mutun ce mai daraja, mace kike uwar al'umah, wace muke so muke fatan gannin mun wanketa cikin salama mun mikata da dumbin daraja Muneerath ki ji tausayin ahalinki, ki tausayawa marikanki ki taya mijin da zai aure ki kishin kanki, ki kare mutuncin y'ayanki kin ji?"

Hawaye ne masu dumin gaske masu tafe da dumbin kauna da bege da madaukakin gannin girma da darajar Mah suka gama wanke fuskarta, bakinta ya mata nauyi ta kasa furta komai, bata taba jinta a matsayin mutun cikakiya ba irin na yau, yau gata itama mutun ce ana mata nasiha irin wannan mai daraja da girma? Ashe dama haka mu'amala take tsakanin datijan kwarai da yara? Ashe ana yiwa mutun fadan ya gyara kayansa?

Ta kasa cire dubanta a kan Mah a lokacin da suka fito kusa da Katon Falon Pah bayan sun masa salama ya gama tsokanarta sannan ya dora mata da tasa nasihar suka rakota harda iman kusa da wuleliyar limozine din dake dauke da direba da soja daya za'a kaita wajen aikinta ita MUNEERATH YAR OGA sai kawai ta samu kanta ta sumbatar bayan hannun Mah kafin a sanyaye ta ce" NA GODE"

Wannan kalma ita kadai ce ta fara fito mata daga bakinta domin ita ce ta fi cencenta da ta furta a wannan lokacin, ta tabata sai ta zauna zata iya gane a wani hali take ciki hakan ya sa ta shige bayan motar da aka bude mata ta zauna ta limshe idannuwanta suka harba hanya zasu sadata da baban a roport din da OGA HANJA

ke janye da ragamomi masi yawa a ciki harda tukin da zai yi na yau dan zuwa kasar malesia

□□□□□□□□ Malamai to wai ba'a hutu hala □□□□□□□□□□
11/14/21, 12:49 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 0 □□□

Maganin warin hamata a saukake shine lemun tsami, ka yanka shi gida biyu ka gurza a hamatarka kafin ka shiga wanka, kana shiga ka wanke kamar yadda ka sana wanka shine maganin warin hamata da dukan wani lungu idan kana so, sannan bashi da wani aibu, kuma ba dole kulun sai ka yi ba yana iya yi maka kwana hudu bai dawo maka da bugawar hamata ba domin wani sa'in da turaran da komai aman idan aka sha rana akan hadu da bugawar hamata har kai da kanka ka ringa jin sai a hankali jikin naka, to ba wuni a rana ba ko a ina ka wuni idan ka yi haka ba zaka yi warin hamata ba komai zufar da zaka yi
Bale mu mata, mu sani turarukan nan na hamata akoy masu mugun karfin da suke balo ciwon nono boyaye, na gani da idona matar da daga fesa turaran fesawa na hamata hamatar ta dan kaikaita mata sai zuwa nono daga nan kafin dare nono ya sundume nata ashe tana da kansar nono bata bayana ba, wannan turaran ya bayanar da ita da karfin gaske, danma hannu da shuni aka fita da wuri karshe dai sai cire shi aka yi .....wannan ciwo ne kuma haka Allah ya kadaro mata ....aman akoy musababi, turare a hamata bashi da kyau bale irin na kantin nan na fesawa.....mu bincika dan tabarwa.....na gode □□□□□□□□□□□□□□□

Sun dauki lokaci a hanya kafin suke karasawa wajen aikin

Kasancewar waje ne da hanyar ma'aikatan wajen daban da ta passinger sai bata gane ta kofar da suka shiga ba, abinda dai a yau ta samu kanta da yi shine admirern abinda idannuwanta ke ganni domin a yau tar take gannin wannan duniya tasu da idon basira, a yau da hankalinta yake jikinta ya kasance wannan doguwar tafia da suka yi sam bata kula ba dan idannuwanta na nuna mata duba irin na mamaki

Yan karafunnan dake bakin hanya idan suka karaso sai direban ya rage gudun motarsa sosai sai karfen ya yi kasa kafin su bi su wuce, haka idan suka tunkaro wajen duwatsu masu tsini summa sai su kauce kafin su wuce kafin su fara isowa wajen camerar da du idan sun tsaya sai ya zuge gilas din gefen da take camerar ta dauketa da kyau kafin ta nuna wata blue din wuta sannan suke sammun shigewa idan ta nuna ja kuwa baka isa ka taka gaba ko kace zaka yi baya ba domin idan bayan ka ce zaka yi da gudu wadinnan abubuwan da ka wuce ba zasu kau a hanyarka ba dan daga cen za'a hanna hakan kafin sojoji su tarboka da bindigunsu .....wannan abubuwan na cikin tsare tsaren bada kariya wa ma'aikatan wannan ma'aikata wanda ba wai dan kawai muneerath na sanye da suturar Hostess dinsu bane ya saka suka samu shigewa ba, no dan akoy hotonta da computer ke ajiye da shi sannan sunna da sannin cewa yau zata fara aikinta

A haka har suka karasa wawakekiyar rumfar ajiye motocin da ta ga motoci sun fi a kirga a kimtse wula wula da su hakan ya sakata karra yin sharan da baki tana kallo har sai da ta ji an bude mata bangaren fitowarta kafin ta daga kai ta kalli sojan da ya bude mata yana jira ta fito daga motar

Irin shigarsa take karewa kallo tun daga irin hular dake kansa da kuma farar wukar dake hannunsa wace ta tabata ita ce makamin dake tare da shi kadai , shigar kakin jikin sojojin oalas din ba iri daya bane da na sojan cikin gari, hakama hulunnansu ba iri daya bane sannan su ba kowane ne ke rike da bindiga ba, wa'inda ke rike da bindigogi iya wa'inda ke yawa da Hanja da ko da Sarki ne, suma gugunsu da yawansu bamgarensu daban , salarrynsu daban domin ko formation din da ake basu ba iri daya bane da wadinnan
Dan murmushi ta yi a lokacin da ta ga wani dan hancinsa zuwait da shi a bayane ta ce" Allah daya gari bamban, su kiwa ga irin nasu dogarin "

Shi dai a yadda ya kame mata bai ajiye ba sai da ta fito kafin ya rufe ya kuma shiga bin bayanta tamkar jela fuskar nan tasa a hade kirin da ita

Da mamaki ta ja tana kallonsa kafin ta ce" Kaini zaka yi wajen? Ka ga kuwa ban san inda zan bi ba"

Da yannayinsa na bata girma ya ce" eh aikina shine na nuna maki hanya sannan na baki kariya a du inda zaki je "

Ido ta ruko tana kallonsa a zuciyarta tana maimaita kalmar kariya? Gannin ya nufi wata kofa ya dana wasu butom kofar ta bude ya saka ta biyo bayansa ta shiga kafin shima ya shigo da sauri ta dora hannunta ta rike dan karfen ailbar dake jiki dan ra kula irin na Palas ne mai yin sama ko kasa da bawa ya tsilira shi a yan sekwani, kai ita dai tana gannin garajen dan adam yanzun idan ya makale da kai kuma yaya zaka yi? Shikenan ka mace ko akoy yadda ake yi?

Sanyin kamshi da ya buso ta da haske ne ya sakata tsayar da tunaninta a lokacin da suka bayana a cen sama wajen baban filin taron ma'aikatan

A hankali ta sako kafarta waje tana kiftawa tana kallon yadda mutane ke kai kawo, gaba daya wajen sai ya so sakata juyawar kai domin waje ne mai girman gaske ga

kuma mutane maza da mata sanye da suturu yawancinsu sanye ne da irin suturar dake jikinta ko kuwa dan bingilalen sket ko dogon wando irin dai kayan sweet na maza aman kowace ka kala kayanta kamar sabo dal domin ba alamu na yamutsa ko na dati a jiki bata dai san kuma bangaren wari ba, sai dayan abin takaicin ita dai bata ga daya mai kai a rufe ba, gaba dayansu kawunnansu a bude suke haka kuma irin yadda suturun suka matse su kamar da sun yi wani wawan motsi zai yage

Mazan kuwa sanye suke da nasu kalas costume din watau swt baki dayansu ba mai jalabiya ko mai riga da wando na dinkin yadi ko shada, bambancin suturarsu daga color ne sai ko tsada aman baki dayansu sun sha karanpasan swtt dinsu gasu farare har idannuwanta sunna neman mata ciwo kafin take hango yan tsirakun kalarta a cikinsu, haka kuma yannayin mazan su sai ya fara sakata a tunanin to ko dai baki daya mazan su kyankyasar inji ne? Dirka dirka da su malan sai dai a yannayin baban jikin akoy mai kyau akoy kuma wanda zaka ga kawai ya yi wani sandandam, wani kuwa da katon tumbi irin an ci an tada kai a kasar nasaruma □□

Sai da ta gama kauyancinta ta kula ba wanda ya damu da ita kafin ta juyo ta kale shi yana tsaye ita dai yake jira ya ce" An ce na kai ki asibitinsu sai an gama maki binciken lafiyarki sannan ku tashi kunna da tafia nan da awa uku da minti goma sha bakwai"

Ajiyar zuciya ta sauke ta bi bayansa suka nufi cen ciki
Sun dan yi tafia kafin su karaso wajen, daga sama an rubuta sunnan dake nuni da wajen likitoci ne da inglish , nan ya ja ya tsaya ya yi mata nuni da tana iya shiga

Sai da ra waiga kafin ta yi adu'a ta saka kanta

Dan ja ta yi ta tsaya tana karanta waje waje dake rubuce har ta kawo kan wajen dake bayanin nan ake gannin hostess hakan ya sa ta yi murmushi ta karasa ta dan kwankwasa ta tsaya har aka bata damar shiga bayan an dauki lokaci sannan ta dafa abin ta bude ta shiga a hankali

Sama sama muryarsa ce ke bada dadadan amo cikin yannayi na yana yin fada fada , bayansa ne ya ba kofar hakan ya saka ya miko hannunsa ba tare da ya juyo ba ya ce" John bani "

Tsuru ta yiwa hannun nasa da kuma idannuwan da suka sauka a saman kanta na tsararun yan matan dake laye au biyar , sai uwa uba SIR da ta gani yana tsaye cen gefe shima cikin yannayin nan nasa da yakan yi masu a Nijer idan yana cikin aiki

Zuciyarta ne ke dukan tara tara , tarin tsoro ya darsun mata a kasan zuciyarta na abinda ka je ya zo duda ba fuskarsa ta gani ba aman ba zata manta yannayin gashin kansa da irin tsarin kirarsa ba
A hankali ta lumshe idannuwanta nan da nan ta kamo abinda ta tabata ba dai mutun ba sai dai idan Allahn ne ya kadaro mata samun matsala da wani a nan ta shiga yi shine adu'ar neman tsari ga dukan abinda zai iya cuta mata

Da karfi ya juyo dan jin shiru bayan ya mikowa John hannu kan ya bashi takardar da ya saka shi daukowa dan yana so ne a masa bincike na kirki a kan su domin tafiar da aka yo da jirgin ghana an tafi da biyu a yannayi na maye, hakan ya sa ransa baci yau tunda ya shigo yake balbale au da masifa wadincen din ya kore su ya saka kuma an kaisu centre dan a yi traitment dinsu, hakan ya sa ya shigo yau komai a gabansa za'a yi bayan wannan aiki da ake masu mai yawa ne ga takale takale sai a hankali dai

A kan fuskarta da ta bayanar da yannayi na tsoro ya sauke fuskarsa

Da sauri ya cire da dubansa sakamakon bugawar da tasa zuciyar ta yi , sai dai cirewar ko second biyu bai bari ya yi ba ya maida saman kan fuskarta
Maganar da yake yi ne take kai kawo a makogwaronsa , lokaci daya ya ji hankalinsa na neman tashi dan ba komai ya saka a ransa ya buga masa da zuciya dan ya kalli fuskar wannan rusheshiyar ba sai dan tana muguwa lale lale tana tare da wata mugunta ne, hakan ya sa ya maido dubansa cikin nata tar kafin ya ya iya jimke hannunsa da yake wuwurgawa yana fadan ya lumshe idannuwansa ya bude ya sauke a kan John da ya shigo dalilin gannin kofar bata rufe da kyau ba

Hannunsa ya mike ta gefenta, sai dai ya yi daf da ita sosai ya amshi takardar ya juya da yannayin takun nan nasa ya kai saman teburin likitar sannan ya hau kan kujerar dake kusa da ta likitar ya zauna

Da sauri ta lumshe nata idannuwan itama tana jin bugun zuciyarta na ta tsananta har sai da Sir ya karaso kusa da ita muryarsa kasa kasa ya ce" Ki je ki tsaya kusa da su har a zo kanki, dukan tambayar da aka maki ki yi kokarin bada amsa a kan tsari idan har kina so a yi tafiar nan da ke yau"

Sai a lokacin ta sauke ajiyar zuciya ta gyada kanta kafin ta karasa kusa da yan matan ta tsaya, Sir ya bita da kallo cike da mamakin yadda ta sauya sosai kamar ba ita ba, fatar jikinta, wannan kiba tata da tumbinta du babu, sai abin kwalin da ya nuna masa harta da idannuwanta aun kara fari masha Allah, bama a maganar abubuwan da suka fi saka shi shagala da tunaninta wanda yake gannin ai normal ne idan dai namiji na iya zayane abinda yake so da mace dan ya yi tunanin nan ba matsala bane tunda dai ba tabawa ya yi ba

A nutse take bin dukkan yannayin tambayoyin da ake masu da irin amsar da suke badawa cikin ladabi da kallo harta da comportement dinsu

Yawu ta hadiye a lokacin da ta kusanta ta je ta zauna itama bayan an bata damar hakan tana kallo aka tsikara mata allura itama aka dauki jikkinta , aka kuma auna idannuwanta da hawan jinni akai mata tambayoyin nan kafin a umarceta kam ta je ta yi fitsari ta bada dan a tantance mahaifarta idan bata dauke da ciki

Ba yadda zata yi ta iya hanna kanta barin jiki
Ba yadda zata yi ta iya hanna kanta jin tsoro
Babu yadda zata yi ta iya hanna kanta kallonsa domin shine dodonta, shine abinda yake bata tsoro, shine wanda ta ganni yana wasa da zakanya hankali kwonce, shin idan aka ce ya yi wasa da mutun fa yaya zai gabatar da wasan? Zai cire kan bawan Allah daga gangar jikinsa ne ya wurgar, zai kama ya raba mutun biyu ba tare da ya saka wuka ba, hakan ya sa du takunta ke saka jinninta hawa wanda ta tabata ana aunawa za'a ce ta koma gida ba zata iya tafiar nan ba

Zama ta yi ta sauke dubanta a kan farar takardar dake ajiye dan idan ta dago idannuwanta a cikin nasa take saukewa wa'inda suke mata kama da zaki, domin ja ne da su sosai kamar ya sha abin maye

Likitar ce ta gama daukan jinnin da yannayin bp dinta ta mikawa wace ke tafia dakin gwaje gwajen da shi sannan ta koma ta zauna ta shiga yi mata tambayoyin kamar haka

Yaya sunnanki ke haifafiyar ina ce? Shekarunki nawa?

Muneerath ta gyara zamanta a hankali ta ce" sunna na Muneerath M , ni haifafiyar kasar Nijer ce, shekaruna ashirin yanzun "

Da mamaki ta kalli HANJA da yake kallon Muneerath dan shima maganar shekarunta yanzun ya ji, sai dai ba damar ta masa tambayar yaya aka yi ya ce yar mamansa ce da kuma karancin shekarunta,
Sai kawai ta yi shiru ta ci gaba da tambayoyin kamar haka" Muneerath ke musulma ce ko christa?, Kina da aure ko baki da? "

Muneerath ta bada amsar ita musulma ce, sannan bata da aure zuciyar fal tunanin ya aka yi sauran ba'a masu irin tambayar nan ba, bata san cewa dole bakuwa take sai an bi hawa hawa kafin a bata damar shiga

Likitar ta ce" kin taba haihuwa ne ko kim taba samun ciki baki haife shi ba? Idan kin taba sau nawa? Da rai ko babu? "

Da mamaki Muneerath ta waiga wajen Sir sai ta ga yana tsayen dai aman kasa yake kallo dan haka ta maido dubanta ta ce" Cewa fa na yi ban taba aure ba"

HANJA dake dan kada kafarsa ya wurga mata wata irin harara dake nuni da ki bada amsar da aka tambaye ki a kai

Sir ya matso da sauri domin dama yana wajen ne dan shine responsable din Hostesss ya kalli Muneerath ya ce" Amsa zaki bada daidai da tambayar da ta maki "

Muneerath ta lumshe idannuwanta a hankali ta cike lalausan fizgegen pink lebenta da tsararun hakoranta na kasa sannan ta bude ta dora dubanta tar a kansu ta ce" Ban taba haihuwa ba, ban taba zubar da ciki ba, cikinma ban taba samu ba"

Sukan amsoshinta tana rubutawa ne har ta gama ta dora da fadin" Saurayi nawa kika taba yi, da nawa kika kwonta ?"
Tambayoyi ne da ake yiwa kowace bakuwar Hostess kafin ta fara aiki, tambayoyi ne da ba'a dauke au a bakin komai ba domin ana so aikin da za'a fara da kai a san waye kai a bayane a kuma gamsu da bayananka , sai dai gaba daya wadinnan tambayoyi suka zubawa Muneerath matsanciyar kunya da jin haushin masu yi mata itan , ita kuwa likitar tana cikin mamakin amsoshin Muneerath inda Hanja kwata kwata baya yarda da amsar shi bai wani yarda ba yan matan nan na yanzu ai sai su

Muneerath a sanyaye ta ce" Bani da saurayi "

A kufule HANJA ya daka tsawar da ta saka Muneerath rintse idannuwanta ya ce" Amsar tambayar da aka maki ake so ki bada ba raina mana hankali ba , a nan babu wanda ya damu da ke bale ki yi kokarin birge shi!"

A rikice ta dago ta zubawa fuskarsa ido kafin ta bude bakinta lebenta na rawa ta ce" Na ce bani da shi, ban taba yi ba ban sanshi na, ni ba yar iska bace ta yaya kuke so na ce maku ni yar iska ce, bai ce yana so na din ba tukunnan sai na koma ko!".....sai kawai ta fashe da kuka tun karfinta ta kifa kanta saman table din gaba daya jikinta na rawa dan ita bata ga a wani dalili za'a ringa mata wannan wulakancin ba, a karuwa suke daukanta hala ko me?

Hanja , chok, Hanja bakon lamari, HANJA madaukakin rainin hankalin yarinyar ya saka shi ruko ido da sauri ya kai hannunsa wajen bakinsa da mamakin da ya saka shi bude baki na irin ihun da ta yi a lokacin da shi Prince HANJA kuma shugabanta a wajen aikinta ya yi magana ta masa ihu da magangannun da ihunta suka dauka da kuma kukan da ta fashe da shi ta kifa kanta a yau ranarta ta farko a wannan waje ya

saka shi jin wata juwa na son kwada shi da kasa.....ya Rab MAH da wa kika hada ni kuma?

Likitar da ta ruruko ido itama ta mike tsaye tana kallon ikon Allah da sabon al'amarin yarinyar da kukan duka ta gama sakawa ranta shikenan yarinyar nan zata ja a koreta ko aikin bata fara bane ta kalli Hanja dan so take ta dan bashi hakuri kar ya yi gagawar furta kora a bakinsa dan ba zai dawo baya ba ta ji muryarsa a dan sanyaye na irin takaici ya kume kan nan ya ce"

.

.

.

..... Alhmd
11/14/21, 12:49 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 1 □□□

Ya ce" ta tashi ta tafi"

Da sauri likitar ta ce" ur excellency ka yi hakuri kar k koreta da alama bata san kan aikin bane gata bakuwa sannan ba haifafiyar nan ba"

HANJA da kukan ke neman hadasa masa juwa ya ce" Cewa na yi zan koreta? Ta je ta hadu da sauran a shirya su mu tafi"

Wannan karron ba likitar ba, Sir kansa a mamakance ya kallo shi sai dai irin yadda ya hade rai ya juya yana mai dafe gaban goshinsa ya saka cikin gagawa likitar ta mikar da ita tana kukanta tana bata hakuri suka yi gaba da Sir suka nufi wajen da sauran suke

A nutse likitar ta tsaya kusa da shi kadan ta ce" Sir "

Kansa dake sade ya dago ya juyo yana fuskantarta bai amsata ba
Abin aune aunen ta nuna masa a ladabce ta ce" zuwanka ne "

Hanja da kansa ya dau ciwo na ihun kukan ya cije hakoransa ya zagaya ya je saman doguwar kujerar ya zauna yana mai tube rigar jikinsa ya ajiye hannayensa ya lumshe idannuwansa ana sauraronta ta shiga auna shi cikin nutsuwa da kayan aikinta tana rubutawa ta dago tana kallon wajen fuskarsa ta ce" Lafiar jikinka ingantaciya ce, abinda na ga yana kokarin damunka biyu ne, kanka da ya dauki ciwo sai kuma yannayin bukatuwarka wanda su dukansu yanzun za'a magance su"

Idannuwansa dai a lumshe suke har ta dawo da magani cikin kofi ta zauna saman kujerar ta bashi ya amsa ya sha ya kuma lumshe idannuwansa na kusan minti goma bata yi magana ba sai dai tana rike da tap a hannunta mai kirar aple tana jiran ya motsa

A hankali ta ce" Sir ciwon kan ya sauka? "

HANJA da ransa ke bace yana ta tunanin ta inda zai samu mafitar da zai yakice yarinyar nan daga cikin ahalinsa ya dan motsa mata kansa bai amsata ba

Ajiyar zuciya ta sauke cike da tunanin to wai ko dai da gaske yar maman nasa ce? To a afrika ta samu cikinta ko menene? Ita ta kasa gane yaya aka yi haka, sai dai ta yarda koma me dinsa ce tana da kusanci da shi mai karfi wanda ya zarce na maganar soyaya, hakan ya sa bata yi gigin yi masa wata tambaya a kan Muneerath ba

Screen din tap din ta juyo masa bayan ta tsaya,
Hotunna ne na wasu tsala tsalan yan mata na grup VIP na kasar baki daya wanda kampaninsu ya samu shiga dan samawa zaratan mazan abin bukatarsu a ringa cirewa a cikinsalarry dinsu wanda a haka kampanin ke kara wawusarsu.....hakan kuma nrmal ne nema ne

A hankali take dan matsar da hoton ta sako wani, daga ringeshen da yake yanna kallo tarrr a idannuwansa ana ta wuce su yan mata ne masu fata mai sheki da tsayayu mama da dan kugu sunna cikin shiga ta tairaici sun yi kwonci irin na yan duniya ko a tsaye an wani wara kafa, ko a zaune an saka pom a baki an datsa masa

hakori.....yannayiyika dai na talar abin cikin pant har sai da ya gaji da bi da kallo kafin ya maida kansa ya lumshe idannuwansa

A ladabcenta ta ce" yannayinka na nuni da nan da dan lokaci mararka zata kule, lokacin bai fi yan mintunna ba sir ka fini sannin yaya ciwon mararka yake gashi zaka yi tukin awa hudu, idan kuwa ka fi so na je da gagawa na kawo maka wace ta yi sai na je yanzu yanzu na kawo "

A gaskiya shi da kansa ya san a bukacen yake, sai dai wani lamarin wannan bacin rai da aka hadasa masa na yanzu ya kular da shi sosai, walahi da ace wannan yarinyar bata da daurin gindin gidansu da sai ya wanka mata mari kafin ya koreta, wannan yarinyar nan da wata uku ta saka shi hawan jinni fiye da nrml bp dinsa shi ya sani, dan dai mai hakuri ne shi ya sa yake sauka da wuri, haka kawai katuwar YA ki saka mu a gaba ki rushe mana da kuka? A kanta aka fara tambayoyin nan ko a tunaninta ita ta daban ce da za'a tsara nata? Ko tunani take sai an bi ta nan za'a iya korarta?, Dan bakin raini ta furta masu bata taba yin saurayi ba dan kawai ta basu aikin bincike na banza da wofi! Kai ba za'a yi binciken a kan nata ba dan shi yana ji a jikinsa verry soon zai tatara ya nata ya nata ya kara mata gudu, ina dalili tun bai fara haihuwar ba wata gandareriyar bak'ar y'a zata zo ta dame shi!

Mikewa ya yi zaune ya shiga maida kayansa bai bata amsa ba har sai da ya gama sannan ya ce" No barshi, bana cikin mood din hakan zan sha magani ai tafiar ta yau ce kadai in sha Allah "

Yana maganar ne yana tafia ya fice a office din gaba daya

Ajiyar zuciya ta sauke, bata dan me zai saka ya ce bashi da ra'ayin hakan ba bayan ga yadda jikinsa ya nuna, kai su fa basa son abinda zai taba shi dan shi din adali ne a gare su, mutun ne mai kyautata masu hakan ya sa suke maraba da dukan ranar da zai shigo wajen su, irin yadda ya tsaya tsayin daka kan ma'aikatansu kuwa ya sa suke aiki da kuzarinsu domin da ace Sir HANJA ya kasance mai yin yan mata a wajen aikin nan da sun shiga uku, sai Allah ya taimake su ba ruwansa da y'a a wajen aikinsa ko yar waye, ko wata irin halita gareta, kai ko a wajen sai dai ya sayi wace ta baza hakan ya sa a irin halayan mutan garin ake respcting dinsa sosai

Sir ne ya fito yana tambayar idan result dinsu sun fito

Nan ta mike suka tafi dakin amsar result din suka amso suka dawo suka zauna sunna wawarewa

Likitar ce ta kale shi ta ce" Ita ba'ai mata na gwajin cikin ba kar kuma ya kama ni da laifin hakan"

Murmushi ya yi ya ce" a barta haka, za'ai mata zuwa gaba idan ta gama fahimtar a kan aikin ne ake mata tambayoyin ba dan ta yi wani laifi ba ko dan ana zarginta ba, kin san bata taba fuskantar haka ba shi yada ta ji tsoro"

Kai ta gyada ta harhada mada komai ya juya ya tafi dan ya kai a dora a kan takardar kowace ya amso baje dinsu kafin su fito daga wajen likitar

Tunda ta shigo wajen ta daina kukan tun karfi aman kuma hawayenta na dan zuba haka kuma tana ta sauke ajiyar zuciya

Yan matan dake dan kara shishiryawa ne suka nufota, dama tunda ta fashe da kuka suke jiran gannin shigowa zata yi ko ita takardunta sun samu cika

Wace ta fi rama a cikinsu ce tana kallonta ta ce" Korarki ya yi? "

Muneerath dake kallonsu daya bayan daya ta girgiza mata kai

Da mamaki dayar ta ce" ko dai kallonsa kike ta yi har ya kama ki da hakan? "

Itama da mamakin ta kuma girgiza masu kai

Sai suka samu kansu da kallon junnansu kafin daya ta ce" to kukan me kike? "

Muneerath ta ja hanci ta ce" Gani na yi ana ta min tambayoyi kamar wata karuwa, dan Allah ina gamina da haihuwa ko ciki a yanzun ni da ko rana ba'a saka min ba kai ko saurayin bani fa shi ba'ai min auren ba za'ana cewa wai wani na tara da namiji to na cewa namiji me ya ce min me? Dama sai da Mah ta ce akoy yan iska a wajen nan na bi a hankali"

A gaskiya, kwata kwata basu gane wai tana kuka dan an tambayeta idan ta tara da namiji ne bayan bata da aure, kai su sai suke son gane kawai haihuwar ce bata so dan an hadata da haihuwa take kuka, hakan ya sa suka nemi kwatanta mata cewar ba wani abu bane wannan ai
Wace du ta girme su ce ta ce" Mun zata korarki ya yi kike wannan kukan, ki tashi ki share hawayenki mu idada kimtsawa mu tafi, kin san sai mun yi binciken kayan mutane bayan sun zauna dan an fara shiga da miyagun kwayoyi malesia yanzun ana cikin yin taka tsantsan ne

Ita dai nan ta ringa binsu har ya dawo ya masu ja gaba baki dayansu suka tafi dakin da zasu layu ya kuma masu wani gargadin

Kamar yadda Sir ya saba haka ya fada masu dukan abubuwan da ya dace su kula, su kiyaye, su yi taka tsantsan a tafia da PRINCE idan har sunna son aikinsu

Sai da ya rage yan mintunna kafin ya shigo, ya cenza kayan jikinsa yanzun suturarsu ce ra matuka jirgi a jikinsa
HANJA yana da sirrin kyau da kyan kallo, sai dai idan ka yarda ka kure mada kallon kana iya janyowa kanka abinda ba shikenan ba, hakan ya sa sauran yan matan da suka kwana da sannin tafiar da waye suka dukar da dubansu , banda Muneerath dake kallonsa tana hankalce da takun tafiyarsa dan bata so kwata kwata ya nufo wajenta dan a shirye take ta dankara da gudu idan ya nufota wollah, a cen kasan zuciyarta kuwa tana tana mamakin wai yanzu ace wannan mai jiran gado ne ba rawani, hm wani abin sai sarakan ingila

Kamar yadda ya saba haka ya tsaya a gabansu ya gindaya masu cewar Aiki suka zo yi su nutsu su yi aikinsu idan ya kama su da wani laifin ba zai iya kyale su ba, sannan ya fara yin gaba, sir ya bi bayansa sannan suma suka bi bayansu

A yaune zata yi shiga ta biyu,a yau ne take cikin hankalinta hakan ya sa tunda suka tunkaro shi ta daga kanta tana kare masa kallo
Girmansa, girman tayoyinsa, girman fukafukansa biyu, gaban goshinsa da ya yi tsini, tsakiyarsa da kuma bayansa, matatakalar dake bude da sojoji da ma'aikatan dake kusa da shi gaba daya sai ta samu kanta da jinta tamkar a wata duniya daban,
Wata irin connexion take ji da zuciyarta da tafkeken jirgin
A hankali wani irin shauki da soyayar Jirgin ke ratsa gaban jikinta

Tana taka matatakala tana hawa ne zuciyarta na kwadaita mata son gannin yaya cikin yake har kasan zuciyarta
A lokacin da ta tsinci kanta a ciki bayan sir ya rabawa kowa irin aikin da yake so ya gabatar ya nemi fa ta biyo shi ita da take bakuwa ya shiga cen ainahin wajen da pasinger zasu zauna sunna tafe yana mata bayanin komai har sai da suka raba tafiar suka isa tsakiya sosai sannan ya juyo yana fuskantarta

Murmushi ya dakar mata mai daraja kafin ya ce" kin daina kukan?"

Muneerath ta daka fuska ita a dole haushinsa take ji domin yana kallo aka ringa wala gigi da ita ana mata tambayoyin mararsa da'a bai tsawatar ba, bama wannan ba tunda ta sanar masa tana Palas rabonsu da su yi wani zance sai fai su gaisa sama sama ya shaida mata a Palas komai na fara bi ta wajen dakin computern da ake binciken mesg ko call din du wanda ke cikin gidan more spcialy na kusa da sarkin, hakan ya sa ya daina dogon surutu da ita dan kar magana ta kai kunnen Hanja ya ce meye tsakaninsa da dalibarsa?

A sanyaye ya ce" Fushi kike da ni? "

Muneerath ta kawar da kanta gefe bata bashi amsa ba hakan ya sa ya ce" Yanzu kin iya girki? "
. Muneerath ta juyo da dan sauri tana murmushi kafin ta gyada kanta ta ce" Yanzun ni nake dafawa Mah shayinta ta sha ta more"

Murmushi ya mata yana gannin bai taba gannin mutun mai chance irin nata ba, kwarai yarinyar da Allah dogara Allahn kuwa sai yake dafa mata a dukkan lamuranta

A nutse ya ce" Mutun ne da ya dauki aikinsa da daraja, yana daya daga cikin wa'inda suka malaki jirgin kansu a kasar nan da basu fi su uku ba, yana da arziki mai yawa, ya fara tuka jirgin fa ya kera da hannunsa na wasa kamar da wasa, a harkar da ta shafi jirgi harta yadda za'a ba pasinger kulawa ya karanta, son abin yake a zuciyarsa ba wai haye ne ya yi dan ya yi arziki ba, aikin nan ba aikinsa bane ya saka kansa ne dan yana so, ina girmama mutumen nan domin idan kika ga ya yi fada da dalili , kar ki dauki tambayoyin cen da wata manufa dukkan bakuwa haka ake yi mata wannan din ba wani abu bane dan a san irin aikin da ya dace da mace ne, domin idan kina da yaro a san irin doguwar tafiyar da ta dace da ke, idan kina da aure haka, idan da saurayinki kike rayuwa haka, Muneerath daga bakin wannan lokacin kin zama karkashin kulawar kampanin nan, idan baki da lafia sune, idan wani abu kike so sune, cin ki, shan ki, suturunki, bukatunki, wajen kwonciyarki baki daya a wuyan kampanin nan ne, basu maki dan wata manufa ba.....ana yin tambayiyin nan ne dan a tantance waye kai da irin aikin da ya dace da kai kin fahimta?"

Sai a wannan lokacin Muneerath ta samu wani nutsuwa a zuciyarta, sai a yanzu ta ji hankalinta ya kwonta harma ta ji kunya na son lulube mata zuciyarta domin sai a yanzu ta ga rashin dacewar kukanta hakan ya sa ta rufe fuska tana murmushi ta ce" Tambayoyin ne sukai min kama da wada ake tuhuma da aikata hakan"

Murmushi sir ya yi yana girgiza kansa ya ce" ba maganar tuhuma, bama wannan ba har yanzu dogarin ake jira?"

Muneerath ta ji batu an tabo mata zushiya sai ta murmusa ta langwabar da kai ta ce" Uhum, ka ga dai sai tsofewa nake bai motsa ba, aman na san da na koma niger zai yi bayani ne na tabata sai ya rikice a yanzun dan na iya saka kwali..." Ta fada tana murmushin tuna aminiyarta amina dake fadan ko kwali bata iya sakawa ba

wani namiji take so yace yana sonta wadinnan mazan na yanzu da kyalekyali ke wartarsu

A kadan zuciyarsa yake ayana' inama za'a bani ke, da na dauke ki mun ringa yawon kasashe, ni kam bana sonki da kwalin a haka kin fi min kyau, aman na san zaki amsani idan na fada wata rana'

Kawar da tunanin nan ya yi gannin lokaci ya yi yanzu an fara kiran mutane su shigo ya ringa nununa mata wajen da mutane ke iya boye miyagun kwayoyi suka zarce har bayi ya nuna mata da irin mu'amalar da ta dace tsakaninta da pasinger kafin su koma su yi jiran jirgi ya gama cika , aka bata abin aunawarta tana tsaye abinta zuciyarta fesss da farin cikin wannan rana

_____&_____

Kafin ka yi tafia ne kake da ita, idan ka yita ita take da kai, a wannan tafiar tasu sun sauka lafia a kasar malesia inda suka yi hotel din dake jikin a □roport din dan samun hutu na dan lokaci kafin su daga zuwa gida, sai dai basu kai ga hutawar ba aka shaida masu tafiarsu zata dauki hanyar HAWA □

Sakalau ta yi tana kallon yadda suke murnar zasu sauka a Hawa □, ita dai bata san ina ne haka ba, abinda ya fi birgeta shine rabata da kwonciyar nan da aka yi, domin ita fa bata gaji da aikin ba, abin kasheta yake gata itane take wannan aiki, kai yaya Oga zai ji idan ya ganta a haka? Mamansu fa da tace bata da hankali idan ta ga yau gata tana wannan aiki?

A yanzunma shine ya tuka su, ba su su sauka a kasar ba sai da sanyin safia gashi su basu rintsa ba
Hakan ya sa sunna sauka wajen kwonciya aka fara gabatar masu domin basa tare da yinwa

Dakuna ne a laye, daga su har ogan nasu du aka umarci yan matan da su shiga su huta

Da ido ta raka bayansa da kallo a lokacin da yake tsaye a kan dokin kofar dakinsa da waya a hannunsa dayan hannun nasa kuwa yana dafe da cikinsa wanda ita bata gane cewar mararsa yake rike da ita ba, ga kansa tamkar zai tsage biyu

A hankaki ta fara nufar infa yake tsaye, so take ta ari wayarsa ta yi kiran Mah ta shaida mata ga inda suke domin ta fada mata da ta samu sarari ta ringa sanar mata inda suke domin ta bata katin numberta ta gida wace ake samunta direct

A hankali ta tsaya dan nesa da shi kadan ta budi bakinta a sanyaye zuciyarta na dokawa da tsoron kar a je ya mata wani ihun ta ce
11/14/21, 12:50 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 2 □□□

"Assalamu alaika " ta fada a sanyaye sannnan a irin ciki ciki dinnan

Sai da ya yi tsam dan tabatar da a bayansa ne aka yi salamar kafin ya juyo a hankali yana mai cire hannunsa daga wajen da ya dora Watau saman mararsa

Yana juyowar idannuwansa suka sauka a kan pankamemen kugunta, da sauri ya yi sama da dubansa ya kai saman fuskarta,,
mamaki ne ya kama shi lokacin yaga itace tdaye firit a gabansa, a cikin zuciyar sa ya amsa sallamar tata kallonta yake yana jiran yaji dame kuma tazo shifa ya fara tunanin ko gamo yayi agarin kwashe kwashen shi na mata

Bai dawo daga duniyar tunanin ba ya tsinkayi muryarta mai sanyi da dadin sauraro tana cewa" Dan waya nakeson ka aramin zan kira mah "

Mamaki ne ya kara kashe shi wai shi take cewa ya bata wayan shi? ikon Allah, ikon Allah, shin wai ba ita ce ya damki wuyanta ba? Ba itace ta masa fitsari a mota ba? Ko ba ita bace yanzun ta gama sheka kuka?

hannunshi ya kalla wanda wayar tasa ke ciki kafin ya kalle ta,
kai shikam wllh badan m
Mah ba da ya batar da yarinyar nan a garin kawai kowa ma ya huta
Tsintar kansa ya yi da mika mata wayar batare da yace mata komai ba yana kallon ikon Allah, hakama Sir da ya taho da servic din da suke kawo pizza da samari uku a bayansa ririke da katan katan din pizzar ya samu kansa da rage saurin da yake ya zubawa bayanta ido da kuma tsayin HANJA da ya kereta yana jingine da jikin garu gashin kansa ya yo gaba ya kurawa Muneerath din ido hannunsa kuwa ya miko mata abinda shi dai bai san ko menene ba, haka kawai ya tsinci kansa da faduwar gaba har ya ji kamar ya kasa idasawa kofar dakunnan nasu

Ita ko muneerath kanta tsaye ta karbi wayar ta juya cikin takunta mai birgewa wanda idan mutum bai santa ba zai yi tunanin cewar da gangan take karkada bombom dinta , ita kuwa baiwar Allah abin ne ya mata pantsam a bayanta kuma ba hadaden nan bane yana juyinsa ne da an bashi damar hakan watau da an motsa da shi

Sam ba da gangan ya yi jiran ta juya ya bita da kallo , hasalima da ya san idan ta juya iya shegen da zata yi kennan wanda shi ya dauka kan da gangan ne ta yi haka da bai tsaya mamakin ta amshi wayar tasa ya nemi bita da kallo ba

Mutuwar tsaye ya yi yana kallonta tuni zuciyar shi ta ringa bugawa da sauri da sauri, mararshi ta amsa lokaci guda ya runtse idanuwan shi da sukayi ja dan azabar ciwon kai da jarabar da ta sako shi a gaba

baiyi auni ba tsabar ya lula duniyar tunani bai ma san mintuna nawa ta dauka tana wayar ba sai jin sassanyar muryar muneerath din tana yi masa godiya tare da miko masa wayar

Idannuwansa dake rintse ya bude da yannayin magagi magagi ya kai hannunsa dan amsar wayar shi, a rashin sani carab ya hade da hannunta,
Munnerath a birkice ta daga idonta ta kalle shi gabanta ne yayi mummunar faduwa lokacin da taga cikin idanuwan shi ,
'innalillahi wa innah ilaihirraji' un' abinda ta ke furtawa kenan a kasan zuciyarta nan da nan jikin ta ya hau bari dan walahi idannuwansa kadai ita ta gani aman sun mugun tsoratata dan ita bata san idon mutun na yin duhu dan ja ba sai yau

kamar wanda aka tsikara ya saki hannun nata da sauri ya juya ya fada dakinshi
muneerath kuwa juyawa tayi kamar wanda kwai ya fashewa a ciki cike da tunanin shi kuwa ciwon ido ne ke damunsa haka har haka?
Dakinta ta shige tana mai kai duwawunta saman bed ta zauna tayi tagumi da hannunta ta shiga tunanin to ko ta fadawa Sir Hanja ciwon ido yake? ,
Sai kuma ta shiga tunanin shin a ina zata ga Sir din kamar dazun ta ganshi kuma sai ta ga wayam baya nan

.....a hankali ta zubawa hannun nata da hanja ya rike ido batasan lokacin da hawaye suka fara xuba a idanunta ba , a hankali ta fara fadin" Na shiga uku na lalace aka, Mah ta ce ciki na shiga da namiji ya tabaka....."

Mai yasa ya rike mata hannu mai kuma ta kara yi masa?, Itadai tasan wayar shi kawai ta mika mishi kuma banda kalmar godiya ba abinda tace to ko dai kalmar godiyan ma laifi ne tayi bata sani ba oh ita yar oga ta kawo kanta wata rayuwa mai cike da abin mamaki, yanzun tabatan da ya yi yaya yake so ta yi da ranta?
to shi wai wane irin mutum ne haka da komai laifi ne a gurinshi?

Turo dan bakinta tayi gaba ta kuma lumshe manyan idannuwanta da suka mata nauyi sabida gajiyar hanya da suka sha haryanxu bata samu ta warware ba

Kwanciya tayi tana tuna idanun hanja da ta gani da irin jan da sukayi ko mai yake damunshi to kodai baida lafia ne a zuciyarta take kara wannan tunanin juya wa tayi irin to ita meyema ruwanta dashi har da xata tsaya tunani akan shi kara tsuke bakinta tayi ta gyara kwanciyarta da tufafinta ba tare da ta yi tunanin wani cenzawa ba, nan ta fara dan gyadi gyadi, sai dai bai yi nisa ba ta jiyo ana kwonkwasa mata kofar

Da sauri ta zabura ta mike tana zarar ido cike da tunanin waye kuma?
Karasawa ta yi ta bude kofar idannuwanta suka sauka a kan Sir wanda du yadda ya so dan boye yannayi na bacin ran da yake ciki ya gagara boyewa a fuskarsa hakan ya sa fuskar tasa sam ba walwala a tatare da ita

Kwalin mai dauke da pizzar ya miko mata yana mai tsatsareta da ido
Ita kuwa da murnarta ta ce" Wo sir ka ga irin aikin da na yi yau kuwa? Yanzun na gama fadawa Mah tana ta daria Allah allah nake mu je Niger idona idon Oga na ga irin murnar da zai yi, menene a cikin kwalin nan?"

Gaba daya magangannunta na innocent girl da shirmenta ya zubawa ido kafin ya ji kamar zai yi kuka a hankali ya rabata ya shige yana tunanin ita batama san ransa a bace ba kau?

Yana shiga ya zauna saman kujerar dake dakin yana kallonta ya nuna mata wajen zama

Baya ta waiga ta ga su kadai ne fa, a haka yake so ta zauna da wando tikaka a gabansa?

A hankali ta ce" a islamiya an hane mu kadaicewa da namijin da ba muharaminmu ba, malama Shamsiya ta ce a wannan zamanin ko muharaman namu ya kasance muna suturce jikinmu idan zamu kadaice da su komai kankantar lokaci, domin mun shigo zamani mai wuyar fasara wanda shedan yake kara samun galaba a kan bayin Allah, na saka kayan nan ne dan ba yadda zan yi, na sakankance ne dan na ga ba ni kadai bace da mata sosai, kuma na kiyaye da dukan karfina, dan Allah ka ga bani da sutura a nan ko sallah ban san da me zan yi ba, ka yi hakuri mu je dakin daya daga cikinsu sai mu tatauna"

Ajiyar zuciya ce ta kwace masa ta farin ciki, wai dama akoy sauuran yan mata haka? Ba abinda yake tunani bane dai kennan ya kaita wajen HANJA, shima ba cln yake ba domin shima ya sha ratsa gonar da ba tasa ba, a cikin wa'inda ya samu mu'amala harda wace bai taba tunanin zata bude masa sket ba, aman shima yana rike dautuncinsa wa yaran da yake horawa, dan murmushi ya ji ya kwace masa da tace wai su je dakin daya, to ita bata san idan har lalatar ce a gaban dayarma sai su yi ba abinda ya sha mata kai? Lale Munnerath na dauke da tarbiyar Allah , sam bata san irin rikicewar da duniya ta yi ba, kuma yana godewa Allah,
Yana gannin mutuncin yarinyar nan har yanaiwa kansa fatan wayar gari ya malaketa ta zamo uwar y'ayansa , ba dan komai ba sai dan nutsuwarta da kamun kanta, walahi a da bashi da damuwar auren wace bata watsa kanta ba ko wace ta watsa, haka kawai a shigowarta rayuwarsu ya san girmama darajarta, a shigowarta duniyarsa ya iya bambance muradinsa, da ace zai samu da sai ya fi kowa farin ciki (Yan matanmu, zamani ya zo wajen da mazan na lalata da mu ne dan biyar bukatunsu, aman kuma idan ta kama namijin nan ya kilace walahi talahi bilahilazi idan kika ga ke abokiyar watsewarsa ya aure ki karfin rabo ne da Allah ya saka a tsakaninku,kina ji kuma kina ganni zai je ya dauko wata kamilaliyar da kika fita a komai ya aura ya kilace abinsa, a haka zaki ji ana fadin du irin jiransa da wance ta yi? Bayan ke wancen din nan ke kika gama wulakanta kanki kika bashi dan so da kauna baki san cewa shi lalatacen ya fi son kamilaliya ba? Ai ko yann iskan mazan sun fi so su kilace kamilalu, haba yar uwa dan Allah yaya kike so namijin da yana gani kike cin amanar iyayenki kina fitowa kina tarda shi kuna badalarku ya yarda cewar idan ya aure ki dan soyaya ba zaki masa haka ki tarda waninsa ba? Soyayarsa ta fi ta iyayanki ne ko ta kai ta mahalincinki? Ko bakya jin tsoron Allah ne?, Dan girman Allah mu yiwa kanmu da kyau, idan kina yi ki tuba ki kilace kanki ki kiyayi maza, namiji na iya kashe ki ya kashe dubunki ya karar da dukan alkhairinki, namiji na iya binki ya bi kawarki shi bashi da faduwa.....nasiha ce garemu baki daya Allah ya shirye mu)

Yana karasowa dan kusa da ita kadan ya tsaya yana kallonta a sanyaye ya ce" Muneerath, na san ba zai fara a kanki ba, aman ban san ko zai iya rike kansa a kanki ba, Munee ki sani ke diamant ce kuma burin kowani namiji, kar ki saka ni hawaye dan Allah, domin kin ga walahi ba wanda zai iya ja da shi sai dai Allah ya kama shi, ke kece ya fi dacewa da ki kame kanki kin ji?"

Tsakani da Allah bata gane me yake nufi ba, sam batagane inda ya dosa ba, hakan ya sa take binsa da madaukakin kallo sanann Allah ya haneta cewa me yake nufi har ya fita ya rufe mata dakin

Dan tsuru ta yi kafin ta yi murmushi , ita dai bata san da wa yake nufi ba, abinda ta sani shine ya mata nasiha ne kuma ko yaya yake nufi ta ji ta dauka in sha Allah koma waye ba zai cin mata ba

Hanja na shiga dakinsa ya kira likitarshi wace ya kasance du garin da suka dira akoy likitocin da suke basu kula

 Ba bata lokaci ta taho tana isa kofar dakin ta kwankwasa kofar ta dan dakata har ya bata ixinin shigowa

Tana shiga a ladabce ta karasa gunshi farawa tayi da auna bp dinshi ya dan hau kadan shine ma ya haddasa karuwar ciwon kan nashi sai kuma ciwon jarabar tashi da bata rabuwa dashi dagowa tayi ta dube shi xatayi magana ya daga mata hannu nuni ya yi mata da tayi aikin ta kawai ta tashi ta bashi guri dan yana bukatar hutawa kan lokacin tafiyarsu ya kusa

nan da nan ko likitar ta shiga ta kama aikin ta ta farane da daidaita bp din nashi sannan tayi kokarin ganin ciwon kan ma ya ragu sai yanayin jikin shi ne da bai sauya ba har yanzu
to shima dai ta bashi magani sannan ta mishi sallama ta fita tana ta tunanin sauyawar ogan nasu, da da ne zai ce ta zo da su ne ta dauko masa kuwa tsala tsala ya hau kai, bata san ko bashi da karfin hakan bane oho

Bangaren yan matan hottest kuwa kowace tana dakinta cikin farin ciki sun san indai suka zo hawai to oga hanja yana basu dama sosai sukanje gurare daban daban na shakatawa da sauransu shiyasa suke matukar jin dadin kasancewar su a karkashin wannan kamfanin sabida ogansu yana bawa kowa hakkin shi shidin mai alkhairi ne, sosai yasan darajar mutum

Suna tsaka da wannan ne sukaji sanarwar kowacce taxama cikin shiri dan nan da yan mintunan zasu juya kuma nan da nan farin cikinsu ya gushe domin basu so haka ba ,
amma yaya zasu yi ?

tuni suka hau shiri murnar ta koma ciki ita dai muneerath dataji ma murna tayi zata koma gun mah dan nan duk a takure take ta bude pizza ta zuba mata ido cike da jin haushinta, ita bata san a kan me suke son abin nan ba, ita yaukima take mata a bakinta , gashi a cikin jirginma abinda suka ci du na cikin leda ne ba zazafawa ba komai malan ita fa kar a rikita mata ciki salon ta samu gudawa a samu na fada!

Ta ga haza, aikinsu ashe ba na hutawa bane? Sai da suka kuma daukan doguwar hanya doguwar tafia sunna tsaye kan kafafuwansu , tun tana gane rabon kayan da kulawa da bukatar Hostess da sun nemi hakan da kwari kwari irin abin nan na farkon shiga har ta dawo yi da salo salo ga tarin gajiya na ciciyarta

Sun samu kusan wuni kafin suke sauka, wannan karronma sai da akai masu su test na cutar nan Corona kafin a barsu su fito

Cike da mamaki take kallon dogarinta kafin ta tafa hannu ta ce" Wai dan girman Allah zuwa ka yi ka dawo ko dama kana nan?"

Shi dai kikam ya kasa bata amsa, to shi me zai ce mata dan Allah su da ba magana suke da iyayen gidansu ba ita kuma sai ta ringa masa tambayoyi dab Allah bayan ana sauraronsu kuma ana kallonsu ta camerar dake jikin rigarsa daga cen Palas ?
Bude mata motar ya yi ta shiga tana sinsina hamatarta ta yi murmushi a bayane ta ce" ashe warima dan zahi ya mana yawa muke yi, ka ga na wuni na kwana a hanya da kaya daya kwalin kwal ban cenza ba , ban yi wanka ba aman kuma kanshin turaran da Mah ta fesa min bai fita ba ka ganshi yana nan, koda yake na san turaran ya sayi tanadin oga aman kuma ai ya ci ace na yi dan tsami tsami kadanma kau?

Wannan karron ya so ya juyo ya kali wannan budurwa, aman tsoro ya hanna shi sai ya dake yana kallon titi shi kuwa direban yana tuka su shima tamkar wani status aikinsa kawai yake.....(Sauka lafia yar Mah)

Idannuwansa har nema suke su rufe dan abinda yake damunsa, a wannan lokacin ya manta jawaban mamansa da na abansa, a irin wannan lokacin ya manta komai da kowa domin da sauri magannin nan ya sake shi hakan ya sa tun yana hanya ya bada damar a turo masa mace biyu wa'inda zasu iya daukan lalurarsa kafin yake shiga motar da ta je daukansa ya bada umarnin a kaishi gidansa

A haka suka nufi gidansa duda Mah ta bada umarnin a kawo mata shi gida ne,

Da kyar ya iya bude idannuwansa yana mai bale botiran rigarsa tun daga cikin motar kafin ya sako kafarsa waje ya fito yana dan son bude idannuwan nasa ya hango su tsaye dan sunna gannin shigowar motocinsa suka fito daga cikin motar da ta kawo su itama wuleliya da ita cikin shiga ta dogayen wandunna dan ya hanna dan za'a kawo masa abin cikin pant a kawo masa shi a bude, fita yake a ransa.....

A hankali yake takawa bai yiwa kowa magana ba ya nufi .....
11/14/21, 12:50 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 2 □□□

"Assalamu alaika " ta fada a sanyaye sannnan a irin ciki ciki dinnan

Sai da ya yi tsam dan tabatar da a bayansa ne aka yi salamar kafin ya juyo a hankali yana mai cire hannunsa daga wajen da ya dora Watau saman mararsa

Yana juyowar idannuwansa suka sauka a kan pankamemen kugunta, da sauri ya yi sama da dubansa ya kai saman fuskarta,,
mamaki ne ya kama shi lokacin yaga itace tdaye firit a gabansa, a cikin zuciyar sa ya amsa sallamar tata kallonta yake yana jiran yaji dame kuma tazo shifa ya fara tunanin ko gamo yayi agarin kwashe kwashen shi na mata

Bai dawo daga duniyar tunanin ba ya tsinkayi muryarta mai sanyi da dadin sauraro tana cewa" Dan waya nakeson ka aramin zan kira mah "

Mamaki ne ya kara kashe shi wai shi take cewa ya bata wayan shi? ikon Allah, ikon Allah, shin wai ba ita ce ya damki wuyanta ba? Ba itace ta masa fitsari a mota ba? Ko ba ita bace yanzun ta gama sheka kuka?

hannunshi ya kalla wanda wayar tasa ke ciki kafin ya kalle ta,
kai shikam wllh badan m
Mah ba da ya batar da yarinyar nan a garin kawai kowa ma ya huta
Tsintar kansa ya yi da mika mata wayar batare da yace mata komai ba yana kallon ikon Allah, hakama Sir da ya taho da servic din da suke kawo pizza da samari uku a bayansa ririke da katan katan din pizzar ya samu kansa da rage saurin da yake ya zubawa bayanta ido da kuma tsayin HANJA da ya kereta yana jingine da jikin garu gashin kansa ya yo gaba ya kurawa Muneerath din ido hannunsa kuwa ya miko mata abinda shi dai bai san ko menene ba, haka kawai ya tsinci kansa da faduwar gaba har ya ji kamar ya kasa idasawa kofar dakunnan nasu

Ita ko muneerath kanta tsaye ta karbi wayar ta juya cikin takunta mai birgewa wanda idan mutum bai santa ba zai yi tunanin cewar da gangan take karkada bombom dinta , ita kuwa baiwar Allah abin ne ya mata pantsam a bayanta kuma ba hadaden nan bane yana juyinsa ne da an bashi damar hakan watau da an motsa da shi

Sam ba da gangan ya yi jiran ta juya ya bita da kallo , hasalima da ya san idan ta juya iya shegen da zata yi kennan wanda shi ya dauka kan da gangan ne ta yi haka da bai tsaya mamakin ta amshi wayar tasa ya nemi bita da kallo ba

Mutuwar tsaye ya yi yana kallonta tuni zuciyar shi ta ringa bugawa da sauri da sauri, mararshi ta amsa lokaci guda ya runtse idanuwan shi da sukayi ja dan azabar ciwon kai da jarabar da ta sako shi a gaba

baiyi auni ba tsabar ya lula duniyar tunani bai ma san mintuna nawa ta dauka tana wayar ba sai jin sassanyar muryar muneerath din tana yi masa godiya tare da miko masa wayar

Idannuwansa dake rintse ya bude da yannayin magagi magagi ya kai hannunsa dan amsar wayar shi, a rashin sani carab ya hade da hannunta,
Munnerath a birkice ta daga idonta ta kalle shi gabanta ne yayi mummunar faduwa lokacin da taga cikin idanuwan shi ,
'innalillahi wa innah ilaihirraji' un' abinda ta ke furtawa kenan a kasan zuciyarta nan da nan jikin ta ya hau bari dan walahi idannuwansa kadai ita ta gani aman sun mugun tsoratata dan ita bata san idon mutun na yin duhu dan ja ba sai yau

kamar wanda aka tsikara ya saki hannun nata da sauri ya juya ya fada dakinshi
muneerath kuwa juyawa tayi kamar wanda kwai ya fashewa a ciki cike da tunanin shi kuwa ciwon ido ne ke damunsa haka har haka?
Dakinta ta shige tana mai kai duwawunta saman bed ta zauna tayi tagumi da hannunta ta shiga tunanin to ko ta fadawa Sir Hanja ciwon ido yake? ,
Sai kuma ta shiga tunanin shin a ina zata ga Sir din kamar dazun ta ganshi kuma sai ta ga wayam baya nan

.....a hankali ta zubawa hannun nata da hanja ya rike ido batasan lokacin da hawaye suka fara xuba a idanunta ba , a hankali ta fara fadin" Na shiga uku na lalace aka, Mah ta ce ciki na shiga da namiji ya tabaka....."

Mai yasa ya rike mata hannu mai kuma ta kara yi masa?, Itadai tasan wayar shi kawai ta mika mishi kuma banda kalmar godiya ba abinda tace to ko dai kalmar godiyan ma laifi ne tayi bata sani ba oh ita yar oga ta kawo kanta wata rayuwa mai cike da abin mamaki, yanzun tabatan da ya yi yaya yake so ta yi da ranta?
to shi wai wane irin mutum ne haka da komai laifi ne a gurinshi?

Turo dan bakinta tayi gaba ta kuma lumshe manyan idannuwanta da suka mata nauyi sabida gajiyar hanya da suka sha haryanxu bata samu ta warware ba

Kwanciya tayi tana tuna idanun hanja da ta gani da irin jan da sukayi ko mai yake damunshi to kodai baida lafia ne a zuciyarta take kara wannan tunanin juya wa tayi irin to ita meyema ruwanta dashi har da xata tsaya tunani akan shi kara tsuke bakinta tayi ta gyara kwanciyarta da tufafinta ba tare da ta yi tunanin wani cenzawa ba, nan ta fara dan gyadi gyadi, sai dai bai yi nisa ba ta jiyo ana kwonkwasa mata kofar

Da sauri ta zabura ta mike tana zarar ido cike da tunanin waye kuma?
Karasawa ta yi ta bude kofar idannuwanta suka sauka a kan Sir wanda du yadda ya so dan boye yannayi na bacin ran da yake ciki ya gagara boyewa a fuskarsa hakan ya sa fuskar tasa sam ba walwala a tatare da ita

Kwalin mai dauke da pizzar ya miko mata yana mai tsatsareta da ido
Ita kuwa da murnarta ta ce" Wo sir ka ga irin aikin da na yi yau kuwa? Yanzun na gama fadawa Mah tana ta daria Allah allah nake mu je Niger idona idon Oga na ga irin murnar da zai yi, menene a cikin kwalin nan?"

Gaba daya magangannunta na innocent girl da shirmenta ya zubawa ido kafin ya ji kamar zai yi kuka a hankali ya rabata ya shige yana tunanin ita batama san ransa a bace ba kau?

Yana shiga ya zauna saman kujerar dake dakin yana kallonta ya nuna mata wajen zama

Baya ta waiga ta ga su kadai ne fa, a haka yake so ta zauna da wando tikaka a gabansa?

A hankali ta ce" a islamiya an hane mu kadaicewa da namijin da ba muharaminmu ba, malama Shamsiya ta ce a wannan zamanin ko muharaman namu ya kasance muna suturce jikinmu idan zamu kadaice da su komai kankantar lokaci, domin mun shigo zamani mai wuyar fasara wanda shedan yake kara samun galaba a kan bayin Allah, na saka kayan nan ne dan ba yadda zan yi, na sakankance ne dan na ga ba ni kadai bace da mata sosai, kuma na kiyaye da dukan karfina, dan Allah ka ga bani da sutura a nan ko sallah ban san da me zan yi ba, ka yi hakuri mu je dakin daya daga cikinsu sai mu tatauna"

Ajiyar zuciya ce ta kwace masa ta farin ciki, wai dama akoy sauuran yan mata haka? Ba abinda yake tunani bane dai kennan ya kaita wajen HANJA, shima ba cln yake ba domin shima ya sha ratsa gonar da ba tasa ba, a cikin wa'inda ya samu mu'amala harda wace bai taba tunanin zata bude masa sket ba, aman shima yana rike dautuncinsa wa yaran da yake horawa, dan murmushi ya ji ya kwace masa da tace wai su je dakin daya, to ita bata san idan har lalatar ce a gaban dayarma sai su yi ba abinda ya sha mata kai? Lale Munnerath na dauke da tarbiyar Allah , sam bata san irin rikicewar da duniya ta yi ba, kuma yana godewa Allah,
Yana gannin mutuncin yarinyar nan har yanaiwa kansa fatan wayar gari ya malaketa ta zamo uwar y'ayansa , ba dan komai ba sai dan nutsuwarta da kamun kanta, walahi a da bashi da damuwar auren wace bata watsa kanta ba ko wace ta watsa, haka kawai a shigowarta rayuwarsu ya san girmama darajarta, a shigowarta duniyarsa ya iya bambance muradinsa, da ace zai samu da sai ya fi kowa farin ciki (Yan matanmu, zamani ya zo wajen da mazan na lalata da mu ne dan biyar bukatunsu, aman kuma idan ta kama namijin nan ya kilace walahi talahi bilahilazi idan kika ga ke abokiyar watsewarsa ya aure ki karfin rabo ne da Allah ya saka a tsakaninku,kina ji kuma kina ganni zai je ya dauko wata kamilaliyar da kika fita a komai ya aura ya kilace abinsa, a haka zaki ji ana fadin du irin jiransa da wance ta yi? Bayan ke wancen din nan ke kika gama wulakanta kanki kika bashi dan so da kauna baki san cewa shi lalatacen ya fi son kamilaliya ba? Ai ko yann iskan mazan sun fi so su kilace kamilalu, haba yar uwa dan Allah yaya kike so namijin da yana gani kike cin amanar iyayenki kina fitowa kina tarda shi kuna badalarku ya yarda cewar idan ya aure ki dan soyaya ba zaki masa haka ki tarda waninsa ba? Soyayarsa ta fi ta iyayanki ne ko ta kai ta mahalincinki? Ko bakya jin tsoron Allah ne?, Dan girman Allah mu yiwa kanmu da kyau, idan kina yi ki tuba ki kilace kanki ki kiyayi maza, namiji na iya kashe ki ya kashe dubunki ya karar da dukan alkhairinki, namiji na iya binki ya bi kawarki shi bashi da faduwa.....nasiha ce garemu baki daya Allah ya shirye mu)

Yana karasowa dan kusa da ita kadan ya tsaya yana kallonta a sanyaye ya ce" Muneerath, na san ba zai fara a kanki ba, aman ban san ko zai iya rike kansa a kanki ba, Munee ki sani ke diamant ce kuma burin kowani namiji, kar ki saka ni hawaye dan Allah, domin kin ga walahi ba wanda zai iya ja da shi sai dai Allah ya kama shi, ke kece ya fi dacewa da ki kame kanki kin ji?"

Tsakani da Allah bata gane me yake nufi ba, sam batagane inda ya dosa ba, hakan ya sa take binsa da madaukakin kallo sanann Allah ya haneta cewa me yake nufi har ya fita ya rufe mata dakin

Dan tsuru ta yi kafin ta yi murmushi , ita dai bata san da wa yake nufi ba, abinda ta sani shine ya mata nasiha ne kuma ko yaya yake nufi ta ji ta dauka in sha Allah koma waye ba zai cin mata ba

Hanja na shiga dakinsa ya kira likitarshi wace ya kasance du garin da suka dira akoy likitocin da suke basu kula

Ba bata lokaci ta taho tana isa kofar dakin ta kwankwasa kofar ta dan dakata har ya bata ixinin shigowa

Tana shiga a ladabce ta karasa gunshi farawa tayi da auna bp dinshi ya dan hau kadan shine ma ya haddasa karuwar ciwon kan nashi sai kuma ciwon jarabar tashi da bata rabuwa dashi dagowa tayi ta dube shi xatayi magana ya daga mata hannu nuni ya yi mata da tayi aikin ta kawai ta tashi ta bashi guri dan yana bukatar hutawa kan lokacin tafiyarsu ya kusa

nan da nan ko likitar ta shiga ta kama aikin ta ta farane da daidaita bp din nashi sannan tayi kokarin ganin ciwon kan ma ya ragu sai yanayin jikin shi ne da bai sauya ba har yanzu
to shima dai ta bashi magani sannan ta mishi sallama ta fita tana ta tunanin sauyawar ogan nasu, da da ne zai ce ta zo da su ne ta dauko masa kuwa tsala tsala ya hau kai, bata san ko bashi da karfin hakan bane oho

Bangaren yan matan hottest kuwa kowace tana dakinta cikin farin ciki sun san indai suka zo hawai to oga hanja yana basu dama sosai sukanje gurare daban daban na shakatawa da sauransu shiyasa suke matukar jin dadin kasancewar su a karkashin wannan kamfanin sabida ogansu yana bawa kowa hakkin shi shidin mai alkhairi ne, sosai yasan darajar mutum

Suna tsaka da wannan ne sukaji sanarwar kowacce taxama cikin shiri dan nan da yan mintunan zasu juya kuma nan da nan farin cikinsu ya gushe domin basu so haka ba ,
amma yaya zasu yi ?

tuni suka hau shiri murnar ta koma ciki ita dai muneerath dataji ma murna tayi zata koma gun mah dan nan duk a takure take ta bude pizza ta zuba mata ido cike da jin haushinta, ita bata san a kan me suke son abin nan ba, ita yaukima take mata a bakinta , gashi a cikin jirginma abinda suka ci du na cikin leda ne ba zazafawa ba komai malan ita fa kar a rikita mata ciki salon ta samu gudawa a samu na fada!

Ta ga haza, aikinsu ashe ba na hutawa bane? Sai da suka kuma daukan doguwar hanya doguwar tafia sunna tsaye kan kafafuwansu , tun tana gane rabon kayan da kulawa da bukatar Hostess da sun nemi hakan da kwari kwari irin abin nan na farkon shiga har ta dawo yi da salo salo ga tarin gajiya na ciciyarta

Sun samu kusan wuni kafin suke sauka, wannan karronma sai da akai masu su test na cutar nan Corona kafin a barsu su fito

Cike da mamaki take kallon dogarinta kafin ta tafa hannu ta ce" Wai dan girman Allah zuwa ka yi ka dawo ko dama kana nan?"

Shi dai kikam ya kasa bata amsa, to shi me zai ce mata dan Allah su da ba magana suke da iyayen gidansu ba ita kuma sai ta ringa masa tambayoyi dab Allah bayan ana sauraronsu kuma ana kallonsu ta camerar dake jikin rigarsa daga cen Palas ?

Bude mata motar ya yi ta shiga tana sinsina hamatarta ta yi murmushi a bayane ta ce" ashe warima dan zahi ya mana yawa muke yi, ka ga na wuni na kwana a hanya da kaya daya kwalin kwal ban cenza ba , ban yi wanka ba aman kuma kanshin turaran da Mah ta fesa min bai fita ba ka ganshi yana nan, koda yake na san turaran ya sayi tanadin oga aman kuma ai ya ci ace na yi dan tsami tsami kadanma kau?

Wannan karron ya so ya juyo ya kali wannan budurwa, aman tsoro ya hanna shi sai ya dake yana kallon titi shi kuwa direban yana tuka su shima tamkar wani status aikinsa kawai yake.....(Sauka lafia yar Mah)

Idannuwansa har nema suke su rufe dan abinda yake damunsa, a wannan lokacin ya manta jawaban mamansa da na abansa, a irin wannan lokacin ya manta komai da kowa domin da sauri magannin nan ya sake shi hakan ya sa tun yana hanya ya bada damar a turo masa mace biyu wa'inda zasu iya daukan lalurarsa kafin yake shiga motar da ta je daukansa ya bada umarnin a kaishi gidansa

A haka suka nufi gidansa duda Mah ta bada umarnin a kawo mata shi gida ne,

Da kyar ya iya bude idannuwansa yana mai bale botiran rigarsa tun daga cikin motar kafin ya sako kafarsa waje ya fito yana dan son bude idannuwan nasa ya hango su tsaye dan sunna gannin shigowar motocinsa suka fito daga cikin motar da ta kawo su itama wuleliya da ita cikin shiga ta dogayen wandunna dan ya hanna dan za'a kawo masa abin cikin pant a kawo masa shi a bude, fita yake a ransa.....

A hankali yake takawa bai yiwa kowa magana ba ya nufi .....
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 3 □□□

ADU'A

Alhamdulilahi lazi ahyana ba'adama amatana wa ilaika nushur
asbahnaa wa 'asbahal-mulkulillahi walhamdu lillahi, laailaha 'illallahu wahdahu laa shareka lahu, lahul-mulku wa lahul-humdu wa huwa 'alaa kulli shay'in qadeer. Rabbi 'as'aluka khayra maa fee haazal-yawmi wa khayra maa ba'dahu wa'a'oozu bika min sharri maa fee haazal-yawmi wa sharri maa ba'dahu, Rabbi 'a'oozu bika-minal kasali, wa soo'il kibari,Rabbi 'a'oozu bika min 'aazabi fin naari wa 'azaabin fil qabri.

Wannann itace addu ar tanada muhimmanci sosai da sosai dumin kuwa kanemi alkhairin dake cikin yau dama kuma gaba sannan kanemi kariya da sharrin dake cikinta dama kuma gaba kanemi tsari daga azabar wuta sannan kuma daga axabar kabri kasani duk wanda ya karanta wannan addu ar yayin da ya tashi daga bacci to tabbas baxai wuni cikin kasala ba xakaga da akwai dayawanmu da idan muntashi daga bacci da zarar munyi sallahr asuba sai mukoma bacci wannan ba daidai bane dan yin hakan yakan haifarwa da mutum ciwon kai da kuma ya danga jin laziness ma ana kasala a jikin sa adukkan wuni ranar wasu ma xaku dinga jin suna cewa duniyar yau ta dai na yimusu dadi dama makamanta su to wannan duk aikin shaidan ne to amma in mutum ya lixamci yin wannan addu ar a kuma ya dage da yinta kullum to tabbas xai rage jin dukkan wani kalasa da yake yawanji kullum sannan Allah xai kare shi da dukkan sharrin dake cikin wannna ranar.....TUNATARWA CE YAN Uwa

Tabas abin nasa ciwo ne, baban balaki ne , ko nace abu ne da ya ba gaskiya
Watau Hanja haka ya sadaki yan matan nan daya bayan daya aman ba a tare ba , kafin yake mikewa kan kafafuwansa ya daina jin juwa
Lale sun zo sun sadu da baban gayen da ya zamo burin yan matan garin matasa da manya, sun caji kudi na mamaki, aman kuma sun sha bakar wahalar da ta basu mugun mamaki harma suke tunanin kai du infa Princ dinsu yake yana hadiyar magannin karfi, sun yarda da karfin nada sun kuma yi saranda , danma harka ce ta aikinsu da ba zasu kuma yin fatan haduwa da irin wannan soldier din

Hanja kam bayan tafiyarsu wanka ya yi ya tsaftace jikinsa , abinda yake bashi haushi da zina yana yinta gabansa na faduwa, a cikin tarawa da mata da yake yi abu daya ne yake cin ribarsa shine rage nauyin mara
Haushin kansa yake ji idan yana yi iyayensa na fado masa a ransa
Gaba daya a yanzun da ya gama eh lale ya ji ya daku da mugun ciwon dake damunsa na tsayin kwanaki , aman kuma zuciyarsa ta cinkushe

Da sauri sauri ya fito ya koma dayan dakin nasa ya dauko wayar dake saman table dinsa warau telephone ya zauna ya shiga bugawa bangaren mahaifinsa domin ya tabata du inda take yanzun tana tare da Abih dinsa, so yake ya ji muryarsu , so yake kawai su daga ya ji koda iya salamar tsaftatacen bakinsu ne

Ta yi ringin har ta gama ba'a dafa ba, hakan ya saka shi yin tsai da ransa tare da tunanin yanda zai yi

Mah dake zaune saman bed kusa da Pah bayan an yi kira daga dakin tatar kiran dake shigo masu an shaida mata Hanja ne ke kira sai ta kife kiran ta koma kusa da Pah ta tsura mada ido

Pah ya yi murmushi yana dan girgiza kansa ya ce" Bana so kina saka damuwar nan a Ranki, to wai meye shaidarki cewar ga abinda zai je ya yi a gidan?"

Mah ta sada kanta a hankali hawaye ya tarun mata a cikin idannuwanta kafin ta ce" Na san a yanzu ta rigaya ta zama gama gari, ba garin musulmai ba na kafurai, a kasashen musulmai nema ake dan boyewa aman a kasar nan da ya zamana wa'inda ba musulman ba sun fi yawa gashi a bayane ake aikata ta, da zarar yarinya ta kai shekara goma sha takwas ta samu yancin da zata tsarawa kanta irin rayuwar da zata yi , wa'inda babu daya da zaka gani ace maka wai ba zaune take da saurayinta ba, domin tun a kananun shekarun nan suke raba gida da iyayen nasu, da yawa su tare da saurayin nasu.....kuma wannan nrml ne? Habiby kaina ke daukan zafi idan na tuna tsayuwa bayan dogon kwoncin kabari a gaban Allah, Habiby ta yaya kake so hankali ya kwonta da wannan lamari na yarona? Na san a wajenku wannan din ba wani baban matsala bane, namiji ne shi ya yi bukatar hakan ya sauke..... Aman kuma idan ba ga musulmai kuke fa sai abin ya zo min wani kala, Habiby dan Allah fada min a haka kake so na kwontar da hankalina? Ya ki ya yi auren kwata kwata, kuma ka ga yanzun kiran da yake ko na meye? Na tabata ya gama ne yana so ya ji ko na gane!"

Murmushi ya kuma yi mai daci yana girgiza kansa ya ce" Bama kamar auren nan, Gamu a kasa ta daurin aure gaban alkali, shin idan na daura masa na nan cikin gida ta yaya zan tisa keyarsa ya sakawa matar zobe?, ... Yaron nan sai ya laluba ta ji bana nan na san zai yi hankali!"

Shiru ta yi na dan lokaci jin abinda ya fada kafin ta girgiza kanta ta juyar da kan nata gefe , sai kuma ta juyo da dan sauri tana kallon kansa

Da sauri ta mike ta kara matsawa kusa da shi sosai ta zauna a bayansa ta dira hannayenta tana kallon kan nasa da kyau kafin da mamaki ta ce" Habiby gashi ne ke fitowa a kanka?"

Idannuwansa ya lumshe jin tana shafa kan nasa ya yi murmushi a hankali ya ce" haka nake ji idan na zo shafa ruwan alwallah, aman ban duba ba na san kalar jan nan ne marar kyau ko?"

Da sauri ta sauko kasa ta je ta dauko madubi karami ta zo tana ta kokarin daidaita masa ya ga kansa, dan shi fa ya daina kallon madubi kwata kwata tana fadin" Kalli, bakin gashi ne mai laushi, aman doctern nan ba cewa ya yi ba zaka kuma samun gashin kai ba da zarar ya fara zubewa da kansa shikenan ? Yaya aka yi yanzun yake fitowa?"

Fuskarta ya tsurawa ido yanda take neman amsa ido rufe kafin ya saka hannunsa ya janyota jikinsa gaba dayanta ya rungumeta yana shafa bayanta a hankali ya ce" Baki da wani aikin da ya fi wannan mahinmanci ne?"

Kanta ta dago a hankali tana kallonsa, idan har da gaske abinda take kokarin ganewa kamar yannayi ne na bukatuwa ke nuna kansa a kan mijinta,wani irin farin cikin da ta jima bata nuna irinsa bane ke daukaka a kyakyawar fuskarta
Tabas tana gannin cenji, rabonsa da ya samu bukata irin ta kowani namiji har ta manta, yakan yi kokari dan karantawa sai dai ya sada kansa cike da dacin zuciya ya furta cewa kamar yadda dukan kwayoyin jikinsa masu karfi suka mutu hakama wannan lamarii

A hankali ta ringa dadage har ta hade bakinta da nasa, wanda ya amsheta da hannu bibiyu kafin cikin raunin zuciya ya shiga furta mata" So kike a maimaita

abinda ake yi?" Yana nufin so take sai ta kai wajen da take da bukatarsa shi kuwa ya gaza?, Ko ba komai shekarunsa sun ja, itanema da dan sauranta domin bata cike hamsin ba arba'in da kai ne, shi yasa yake cike da tausayinta, ya yi yinkurin sama mata mafita sau uku tana yi masa hauka tuburan da ihun ita zai ce ya salamawa wani dan sex?, Yakan ji kunyarta ya nuna mata akoy shiga haki mace take mai rai da lafia, bata da matsakar dake hanna mata jin bukatar namiji, ba zai so ta gajiya ba.....sai da ta masa fushi na mamaki domin bai san fitarta ba sai dai jin labarinta a saudiya ya rikita masa lisafi ya so ya ringa barin zance da tsufansa da kyar Hanja ya dawo da ita ya saka su gaba ya masu fada tas kamar shine aban su kuwa y'ayan

A takaice, lamari na samun sauki ya bayana kansa a wannan rana, hakan ya saka Mah zubar da hawaye tana rike da mijinta,
Shima hawayen yake a kasan zuciyarsa ya ajiye hakan a matsayin sauki ne Allah ya bashi na lokacin da ya rage masa dan ya samu ya mora rayuwa da iyalinsa cikin farin ciki, hakan ya saka shi godewa Allah a kasan zuciyarsa bai yi a bayane ba dan kar ta hau kukan nata, shi kam yana gannin shagwaba a wajen maman Hanja kamar ba ita ce mamansa ba idan tana gabansa zata ringa zuba shagwabarta ne

.....

Barci mai rai da lafia ta yi, tana farkawa kuwa ta kimtsa kanta ta saka warta jar riga mai dan kwali fari domin tana da wani sharrr fari kal har kasa

Dan yana dan kwalin ta yi kafin ta dauko wayarta da Mah ta bata ta fito ta rufe dakin nata tana baza sansanyan kanshin nan ta nufi wajen accenceur dan ta sada kanta da bangaren wajen Mah domin ta san Iman na cen

Gannin kamar mutun ne ya shiga zai rufe da gudu ta karasa ta saka hannunta ta rike hakan ya sa ya kara budewa abin

Gabanta ne ya tsinke ya fadi haka shima a lokacin da sukai ido hudu

A hankali take kara takawa dan shiga domin ta rigaya ra rike ba zafa juya ba, shi kuwa a haka ta samu kansa da dan jimke hannunsa na hagu ya cire dubansa a kanta ya matsa gefe yana jira ya ga iya shege irin na yar nan

A gabansa ra rsata tana tura bakinta, sosai ta samu zuciyarta da aiko mata da tambayoyin da suke iya sakata daria, irin tambayar nan da kai zaka yiwa kanka a kasan zuciyarka ka ji wata mahaukaciyar daria na son kubce maka a lokacin da baka shirya ba

A hankali ta samu marar jin kanta na karkatawa dan kallon hannun nasa,
Kwal uba to wai shi hala ba jijiyoyi ne irin na mutanr a jikinsa ba, mesa ce a jikinsa? .....hoton wani wada ne ya fado mata a rai wanda suke wajen babar kasuwa, yaron dan nasu ne yake daga karfe dan rasin jin magana dama gashi gajere bashi da tsayi ga kuma daga karfe sai hannayensa suka yi wani irin jijiyoyi a tsaitsaye
Tashin hankali irin na dan adam da baya gudun ta kife gaba daya sai Muneerath ta juyo ta sauke dubanta a kan fuskarsa dan baban abinda tas tantancewa shine idan bayan kansu iri daya ne da wadan gashi ne ke rufa masa asiri ko me,a daidai lokacin ne kuma abin ya tsaya ya bude .....a lokacin ne kuma ta sauke dubanta a kan sajensa da lebensa mai ja sosai.....haka kawai shari irin na zuciya sai ta kawo

mata magana kama haka 'ji leben uwa na bakuwar karuwa'..... Daria ce ta kubce mata marar sauti aman kuma wace take daria domin dai du wanda ya kale ta dole zai ga daria ne take kafin lokaci daya ta gumtse dariar da take yi ta juya da sauri da nufin tafiarta kafin ya ci yan garinsu

Bata san ta yaya ba, du irin saurin da ta kwasa sai ji ra yi ya damki hannunta a karrona biyu kennan ya juyata a lokacin da bata shiryawa hakan ba ya hade bayanta da jikin garun kofar dakin Mah kafin ya matsota matsewa irin ta gak da gak din nan yana mai bin color din dake cikin idonta dake yawo dan tsoro da firgici ya kasa tsayawa waje daya sai wulwulwul take kafin ta zarro ido sakamakon hannun nata da ya riko ya dago shi sama ya jinginar da shi a jikin kirjinta.....watau yau ita Muneerath yar gidan oga ce hannunta cikin na kato sannan a jingine a saman kirjinta wajen da mamanta suke, harma rabin hannun nasa na gigar cikinta.....'Ta faru ta kare.....' a yanzu ta san babu mai rabata da abin kunya sai Allah, firgicin wannan ya sakata takarkarewa ta kwala ihun da ya saka Mah zabura ita da Iman suka yo waje domin ta dawo tana dakinta tare da Iman so take ta shiryasu tafi wajen likita duda Pah yace shi ba zai je ba

Sunna fitowa basu ganta ba sai da Mah da sauri ta leka ta ganta kafin ta ga bayan Hanja , Muneerath a haukace take fadin" Wayo na shiga uku na lalace dama a hawai ya taba min hannu yanzu kuma ya rike min hannu a kusa da abin nan nawa Mah walahi shine, kur'ani shine innalilahi wa ina ilaihi raj'une dama idan ka ce kai zuwa zaka yi ka yi gaban kanka sai ka hadu da ikon Allah, yanzun idan oga ya gannni da katon ciki ina zan shiga da raina da gorinsu? Wayo Mah ki raba mu walahi daria ce ta kubce mini dan hannun nasa kamar ba na mutun ba shine ya ji haushi ya murde min hannuna haka ya shake ni a makarantarmu kuma ya shuna min zaki"

.....Ikon Allah,walahi tunda mamansa ta haife shi kukan jirgi kawai ke masa ihu a kai kafin a saka yannayi na rashin ihu sai wannan yarinyar mai kama da mahaukata, Yanzu in ba rashin hankali ba shi zata kalla ta dare? To uban me ta gani a jikinsa?, Wai ta ganshi a accenseur ta shiga bata ko dar dar da shi? Kuma shine ta juyo ta fashe masa da daria, yanzun kuma tana cewa shine shine ya yi me? Shi fa yana ta kira kamar da wasa Mah ta ki daga masa waya ya saka shi zuwa gidan nan yau, idan ba dan wannan ba shi da ba wanda zai ganshi walahi shine wannan Bukekiyar ke neman haukata masa dodon kunne?

Mah ta dora hannunta saman damtsen hannunsa zuciyarta cike da adu'ar Allah ya sa ra iya sasauta fushinsa dan har wata jijiya ta tsaya masa a gaban goshi a sanyaye ta ce" Khalb menene haka zaka ji mata ciwo fa kanwarka ce"

Da sauri ya cika jikinta ransa a bace ya ce" Mah du kece,, du kece kika sa muka zo da ita gashi tana so ta hana min kwonciyar hankali, ni ban taba kai hannuna kan mace da nufin haka ba sai a kan yarinyar nan,ta bi ta adabeni sai da zuba min ido.....maida ita zan yi, ba zan iya ba idan ba haka ba kuwa karya mata wuya zan yi!"

A tsorace ta yi bayan Mah gabanta na dukan tara tara a kasan zuciyarta tana alkawarin gabanan ba ita ba shi ko gaisuwa ba zasu kuma yi ba!

Yana gama fada rai bace ya yi dakin Mah

Daga Mah har Iman wani irin mamaki ne ke neman kashe su, kai ikon Allah bama iman da ta yi mutuwar tsaye cike da mamakin wannan lamarin, wai HANJA ne ke

wannan fadan da haki dan wannan yar yarinyar ta tsankwale shi? Wai dama yana doguwar magana haka da rikicewa? Wai dama Hanja din da ta sani yana irin haka?

Mah, Mah, Mah tama rasa me zara yi tunani, a hankali ta janyo hannun Muneerath tana kallonta da wani irin yannayi a hankali ta shafa gefen fuskarta a sanyaye ta ce" Ke tarihi ce, baba, Muneerath.....ni na san ba banza ba kika shigo duniyata, Muneerath fada mini ta yaya hannunsa ya kai kan naki na farko da kuma na yanzu? Dan Allah daughterna ki fada min a nutse ta yadda zan gane komai kin ji?"

Fiki fiki take da ido cike da tsoro tana kallon Mah da Iman kafin ta janye dan kwalinta daga kanta dan ji rake wani kaikayin eahala kamar mai kwarkwata ta shiga fadin "

.....

Baban abin takaicin wasu gigitatun mazan shine .....basa son masu rarashinsu.....su fa mataye masu haye masu ke kashe su, watau wasu mazan infa suke shan wahala a nan wahalarsu ke taruwa ta tsaya, da yawan wasu mazan sun fi so ki ja su a kada, ku kada aljihunsu, ki hauda masu hawan jinninsu, domin gani suke idan ba haka ba kikai masu gaskiya yawa ne, a tunaninsu a gaskiya mace bata mace sai idan ta ja su a kasa.....a nan suke yarda cewar yes ke din wata hamshakiyarsu ce, giyarsu ce, lalumin zuciyarsu ce

.....
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 4 □□□

Muneerath ta ce" Mah kin ga daga Allah ba wani ni ban ce ya taban hannu ba, daga maida masa wayarsa da ya ara min na yi kiranki shine ina mika masa na ga ya taban hannu kuma ina gannima na warce hannuna...."

Da sauri iman ta matso ta ce" Wayarsa ya ara maki?"

Muneerath ta dan kaleta sakalau gannin yau ta mata magana da kanta ta kebe baki ta ce" to da da wata waya kike so na kiri Mah ni da na bar wayar a daki?"

Wata irin ajiyar zuciya ta sauke tana gyada kai cike da mamaki Muneerath ta dora da fadin" tun a nan na shiga tunanin kin ce min idan na ga ko hannuna za'a taba na kiya dan ta haka suke fin karfin mutun har ya samu ciki sai na shiga tunani, kuma sai na yanzun da ya min walahi daga shi babu wani taba min hannun kuma"

Mah kawai kallonta take , daga bisani ta ce" Muneerath, je ki ci abinci kin ji, ga imanma yanxun take ce min yinwa take ji ku tafi ku ci abinci"

Iman ce ta girgiza kanta da sauri ta juya ta shige accenseur tana fadin" Aa na koshi" ta dana hankalinta tashe cike da rudani, tabas fada ta ga sunna yi, aman darajar yarinyar nan da suka dauko a wannan garin har ya kai ya yi fada da ita? Aman a kan me ya ara mata wayarsa? Ya salam, ya salam.....

Muneerath kuwa kai ta kada abinta itama ta nufi kicin domin so take ta je a mata wainar kai yauma ta gwada soyawa da kanta ko za'a dace

Mah a hankali ta idasa shiga da salama a bakinta

Wajen da yake zaune ya rike kansa da hannunsa ta nufa watau saman wani kujera kamar na lybi din nan masu laushin gaske

Zama ta yi ta tsura mada ido a sanyaye ta kuma furta" Asalamu alaika "

A Hankali ya dago jajayen idannuwansa a saman lebensa ya furta" Amen wa alaiki sakam "

Mah ta mika hannunta wajen dafe kumatunsa da ya yi muryarta a nutse ta ce" Me yake damunka? Me ya hadasa maka tagumi? "

Hanja ya cire dubansa a kanta na dan lokaci kafin ya juyo a sanyaye ya ce" Mah, me yasa ina kiran waya bakya dagawa hakama Pah ?"

Ajiyar zuciya ta sauke tana dan hade fuskarta ta ce" Dan na fara jin haushin amsa maganarka komai kankantarta "

Ido ya tsura mata a kasan zuciyarsa kuwa mamakinta ke son kashe shi, lale ya yarda cewa Mah haihuwarsa ne kawai bata yi ba aman irin yadda take karantar dukan motsinsa sai abin ya ringa bashi mamaki.....wani lamarin sai uwa

A hankali ya sauko ya dora kansa saman cinyarta muryarsa a sanyaye ya ce" Inafa neman auren, ko dazun sai da na so kallon wata a Hawai....to kawai sai na ga tana ta kalona .....sai na ji haushin hakan wai me yasa da sun ganni suke fara son nuna min sunna so na? Waye ni? Me na fi wani? Ni ina so na ga wace ban dameta ba, ina so na ga wace zata wahalar da ni ba kawai dan kina mai zaman jira ba daga kin ganni ki nunan so, Mah sam ban yarda cewa ni din take so ba sai na ga akoy dai abinda take so..... Dan Allah kar ki yi fushi da ni, rabona da mace tun da zamu yi tafiar nan sai yau"

A hankali Mah ke shafa gashin kansa tana jin yadda yake sauke ajiyar zuciya wai shi a nan magana ce ya yi mai tsayi

A sanyayenta ta ce" Anya kuwa za'a samu? Wace zaka nuna mata so ta nuna maka aa? Wacece zata ga yarona a tsaye a gabanta komai kyanta ta girgiza maka kai ? Anya son kana so ka yi auren nan kuwa ? "

Hannunsa ya dago ya dora saman nata da take sosa masa ya dan dago ya kali fuskarta kafin ya maida kan nasa a hankali ya ce" Ni na san akoyta Mah, akoy wace ba kuduni, kyauna, ko mulkina ke gabanta ba,,ni na san akoy tawa a kilace a wani wajen duda zuciyata na cike da zulumin wacece ita?, Abinda na sani koma wacece ita din ba zata amsani a zuwan farko ba, ba kuma zan sha wahala dan tankwasata ba fa.....no ina dai so ra nunan ban mata ba ni kuwa zan saka a dauko min ita na aureta"

Mah ta yi murmushi dan walahi irin yadda ya yi maganar sai ya bata daria domin ya wani takwakwabe fuska dan kawai ya sa ta manta fushin da take masa

A hankali ta shafa gefen fuskarsa ta ce" wace uwa ce zata so yin fushi da yaronta?, Wace uwa ce zata kulaci yaronta? Idan ha uwa takai ga yin haka tana cike da tsoro ne, shin yaushe zaka daina? Bana so ka dauka cewar ai kai naka zunubin karami ne, a zunubi babu karami bale idan mutun na yinsa kai tsaye, kai musulmi ne, zina ta haramta a gareka Khalb"

Hannun nata ya rike a hankali ya lumshe idannuwansa ya ce" Mah?, Zan daina ina ji a jikina zan daina"

Mah ta ce" ka ce min ka daina, ka yi min alkawarin ka daina"

Ajiyar zuciya ya sauke a hankali ya ce" Zan je nemo maki sarakuwar ki, zan kawo maki ita ki rungumeta.....zan aurota .....zan samo wace zata zauna da ni, zafa iya rayuwa da ni....Mah bani da ra'ayin mace sama da daya shi yasa wani sa'in sai na shiga tunanin ko sakawa nake a kawo min yan barikin na zaba?, Ni kam a halin tunani nake"

Kanta ta girgiza a hankali ta ce" Idanma yar barikin ka aura da niyar cetota daga aikata aikin nan....ceto ne, aman ka sani zan fi farin cikin ka samawa y'ayanka uwa ta gari"

Murmushi ya yi a hankali ya kara dora kansa saman cinyar Mah din a kasan zuciyarsa kuwa yana aiyana' tarbiyar uwa a yanzu ta fi ta ringa nunawa yaro soyaya, ba ruwanta da inda zai shiga su waye abokanansa , idan kana son gane ita ta haifa a taba shi yanzu zata fito a shiga dibar albarka da ita, Mah a tunaninki akoy iyaye irinki kuwa ?, ni ko na yi aure zan ringa zuba mata ne tana haifowa ina tarbiyantar da kayana ko na kawo maki da an haifa ki bashi tarbiya dan ni ba zan ba mace ta lalata min yaro ba!'

A batane kuwa sai ya ce" i miss u"

Mah ta yi murmushi a hankali ta ce" Gashi yake fitowa a kansa, gashin kuma mai duhu.....kuma, kuma...." Sai wata irin kunya ta hanata karasawa , saima ta rasa ta yaya zata fada masa kuma din

Idannuwansa ya rintse yana jin yadda bugun zuciyarta ke cenzawa irin abin na taba mata zuciya a hankali ya ce" Kina so ya warke ko?"

Mah ta gyada kai da sauri tana kallonsa

Murmushi ya yi mata ya tashi ya zauna a kusa da ita yana rike da hannunta a hankali ya ce" Yanzun zamu je mu kaishi wajen likita, kuma sai ya je"

Yar daria ta yi tana kallon yadda yake harhade girar gishinsa irin zasu raba hali kennan

Mikewa ya yi yana fadin" mu tafi"

Ai kam Mah mikewa ta yi ita dinma cike da farin ciki domin dama ta fi son su je din dan a cen akoy kayan aiki komai da komai idan kuwa zuwa ne zai yi daga shi sai yan kayan aune aunensa

Da sauri ta nufi wajen nikaf dinta ta dauko ta cire mayafin dake kanta ta daura sanann ta kara yafa mayafin sosai a jikinta

Shigar nata ya kurawa ido, kulun Mah cikin shigar abaya take koda kalar ba baka bace aman abaya ce kuma kowace kala zata saka da nikaf dinta,
Haka kawai a ransa yake jin sha'awar irin shigar nan nata, ji yake idan aka ce yau zata fita ba shigar nan ba zai yarda ba, yana wani irin jin shigar a ransa
Murmushi ya mata ya juya ya nufi waje

Ita kuwa ta bi ta dayar hanyar dan fitar da Pah cikin dabara

Tunda ya nufo falon yake jin dariyarta
Haka kawai ya samu kafafuwansa da rage saurin da yake dan gannin ita kuwa mahaukaciyar yar nan da wa take daria? .....ntd Hanja din da ba abinda ya shafe shi da abinda wani yake yi?

Yan mata biyu ne suma a tsaitsaye da plat plat a hannayensu masu aikin gidan ne sunna sanye da dogayen sket da rigar kicin kawunnansu da hulunna itin na chef, itama ta daura hular ta chef a kanta ta cire dan kwalin hakan ya sa gashin kanta bayana har gadon bayanta sannan ta daura abin daurawar nan da ake daurawa idan za'a yi girki
Muneerath ta ce" ku tsaya ku tsaya ku tsaya na irga uku sai a taba a tare, kun ga du wace ta ce wainar kwon nan bata yi ba dadi na san dan kawai mu yi fada ne, kun ga dan ta yi duhu ai ba matsala bane magi ne ya isheta sosai"

Wata dariar ta kusanta ta saka ta ce" Madame, wannan kwon konewa ne fa ya yi"

Muneerath ta ce" lalala, tabas baki san shi kwai sai an masa haka vitamine dinsa ke fitowa ba?, Ai idan dai kwai ne ya soyu da kyau shine darajarsa yanzun dai ku tsaya wollah ku ce ya yi dadi dan in fadawa Mah ta yi murna kun ji?"

Dayar zata yi magana idannuwanta suka sauka a kan Hanja, da sauri ta ajiye plat din dake hannunta jikinta ya dauki rawa , likaci daya ta tabo yar uwarta itama ta ajiye din suka duka kasa kawunnansu a kasa dan sam basu san cewa yana gidan ba da basuma shigo a warhaka din nan falon kasan ba, ba wai dan basa shiga ba domin su suke jera abincin sai dai daga wanann basa rabarbajewa har haka, yanzu haka sai da suka kiya ta tirsasa su kan a nan zasu taba konaniyar wainar kwonta

Da mamaki take kallonsu jin gaisuwar da suke fada ta juya da sauri dan gannin ko waye

Ido hudu suka yi da shi ya ja ya tsata yanzunma rigar dai ce singileti fara a jikinsa bai dora Wata ba ya rufe hannayen nan nasa, a kasan zuciyarta ta shiga fadin' Kai ban taba gannin sarkacecen kato marar kunyar nuna suturarsa irin kyankyasar injin nan, yana yawo tsirara salon a yi daria ya shake mutun kai dai ka shiga uku ba komai a ranka alamu sai iskanci ni kam ai na fada ba ni ba kai mafadacin banza mafadacin wofi, sarautar takuma da ba rawani ake maka ba fuska a bude kowani banza yana kalkonka in zaka fita....' daidai accenseur din yabude su Mah suka fito Mah na fadin cewa a rufe hanyar kasa zasu fita da PAH

Idannuwansune suka sauka a kan Hanja da ya zubawa Muneerath ido yana jira itama ta kwashi rawar jikin ta sada kanta kamar yadda Iman ke yi, sauran ke yi, ga kuma Muneerath vry cute.....so muah yarinyar ta keru rigar kuma ta karbeta, da sauri Mah ta riko hannun mijinta da ido ta nuna masa sannan ta masa alamun ya yi shiru

bata kula da su ba ita domin ya kare su da wannan kirjin nasa ya wani tsaya yana hararar mata kawaye, idan takamarsa gidansu ne ai mamansa ta kawota bale ya koreta kau? Dama irin wadinnan sai girman ba wayau

Dan bakinta ta murguda ta juyo da dan fada fada ta ce" Kai dillah ku tashi mu yi wasanmu ku kuma"

Wayo yaya zan yi da muni ni kwate □□□□

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 5 □□□

Wani irin luuuuuuuu ya yi da idannuwansa a tsayen da yake da sauri ya kara dora dubansa a kanta

Kan iyayensa ya juyo da fuskarsa domin zuwa lokacin ya kula da sun sauko
Irin yadda fuskarsa ta fara zama ja ransa ya nuna bacin rai karara kafin ya juya da waji irin sauri ya fice a falon ya saka mahaifinsa kallon Mah

Murmushi ta sakar masa a sanyaye ta ce" Mu je mu dawo"

Sai a sannan Muneerath ta ankara da su

Ajiye nata plat din ta yi itama ta nufo su tana dan murmushi a nutse ta ce" Pah barka da warhaka, Mah kun sauko ne?"

Mah dake kallonta tana sauraron Pah na amsa mata lokaci daya wani tunani ya ringa darsun mata a zuciyarta
Murmushi ta yi a hankali ta shafi gefen fuskar Muneerath ta ce" Muna dawowa ku shiga kicin ku yi girki "

Tana gama fada ta bi bayan Pah da yayi gaba tuni

Tafia ce suka yi tamkar kurame, tafia ce ta sirri domin mota hudu kawai ta masu rakiya sai tasu ta tsakiya ta biyar
Gari bai san da fitowarsu ba,hanyar kasa aka tsare su kadai suka bi har suka sada kansu da makeken asibitin inda likitan ya tarbe su ya gama aune aunensa
Kwarai shima ya yi mamakin fitowar gashin, ya saka shi a injin yin scan ya gama daukan komai zai samu manyan likitoci a yau su duba result din a tare dan gannin me ya faru me yake shirin faruwa da shi
Ya tabatar masu cewa bai taba gannin cas din da aka kai wannan matakin gashi ya fito ba,sannan bai taba gannin wanda ya kai wannan matsayin ya samu lafia ba, dan haka yana tsaka tsaki amsar da zai basu ma kan takardun dake hannunsa zai dawo da kansa da dare

A haka suka fito a cikinsu Mah ce kawai bata wani karaya ba da maganar bayahuden, abinda ta sakama ranta harma take kara rikewa da karfinta shine Allah ya yi magana, sai da ya saukar da maganin cuta ko wata iri ce, ta tabata idan zai tashi zai tashi, kuma wannan alamu da suka gani ta tabata ba na banza bane dan haka baa cinkushe zuciyarta ba

Mahaifin Hanja kuwa tarin tausayinta,da na yaronsa, da na al'umar kasarsa ke cinkushe a kasan zuciyarsa

A lokacin da suka fito da ido yake bin du wa'inda aka tsare yana kallo , yakan nema masu sauki har kasan zuciyarsa kafin su shige su kamo hanya

Hanja kam kansa a jikin madubi ya lumshe rinanun idannuwansa
Gaba daya wani lokacin sai ya ji zuciyarsa banda kunna babu abinda take yi

Kamar irin wannan lokacin na yanzu, ya rasa a wani mataki zai ajiye halin da yake ciki da tunaninsa da zuciyarsa baki daya, hakan sai ya hadasa masa tashin hankali mai tsananin gaske
Idan ya kalli mahaifinsa sai ya ji dama yana iya gannin ciwon nan?, Idan ya kalli fuskar mamansa sai ya ji shi din ba kowa bane ba kuma komai bane tunda har gashi a tsaye a gabansu sunna cikin hali na rashinu walwalar zuciya aman ya kasa kawo masu mafita sai dai ya kale su
Abinda ya fi sakawa a ransa shine zai ci gaba da kamanta faranta masu har karshen numfashin shi yana mai musu addu ar dawwama cikin farin ciki tare da kwanciyar hankali mai daurewa

har suka iso gida hanja bai sani ba tsabar ya tafi duniyar tunani sai jiyayi mah na taba shi firgigit ya dago tare da fita a cikin motar ya shiga bin bayan su mah da tuni sun isa cikin kayataccen parlon su

ciki ya shiga kamar marar laka a jikinsa ya samu daya daga cikin kujerun dake zagaye da parlon
zaunawa yayi batare da ya ce musu komai ba

Mah ce ta taso daga inda take ta iso gareshi da sauri ta zauna kusa dashi
Dafa kafadun shi tayi cike da damauwar yannayinsa tace" son lafia kake kuwa gaba daya yau bana ganin ka daidai daga zuwan mu hospital har zuwa dawowar mu , shin mai yake faruwa dakai ne son pls tell me " ta karashe tana shafa gefen wuyansa
Daidai lokacin aka gama gabatar masu da drinks dan su sha dan huce kishirwar hanya

zabura yayi kamar wanda aka tsikara ya mike tsaye magana yake cikin fada yana cewa " Mah ba zai yuwu ba wllh, wannan yarinyar terrorist ce ni nasan kashemin ku take son yi !"
Da sauri ya dora hannunsa a gefen kirjin shi da ya mishi mugun nauyi yace" Washhhhhhhhhhhhhhhh"
dadai lokacin da ya hada ido da muneerath suna karasuwa ita da iman dan yiwa su mah barka da dawowa basu lura da yanayin da hanja ke ciki ba sannu da dawowa sukawa su mah suka shige abinsu

karasawa yayi gaban pah ya hade hannayen shi duka biyu yana rokon pah akan su masa rai su ni san tata da shi wllh shi bai taba ganin fitsararriyar dake kallon sa ido cikin ido tai masa fitsara irin yarinyar nan ba,
Muryarsa a raunane ya ci gaba da fadin" pah baku ba har dani yarinyar nan take son halakawa sabida jiki na yana bani a duk lokacin da muka hada ido da ita inba terrorist bace ba zan ringa jiin hakan ba pah tabbasa akwai wata kulleliya da take shiryawa akanmu dan ra tsaka ta kona mu!"

Ya kuma kallon Mah da ta tsare shi da ido tana karantasa cike da mamakin yannayinsa a hankali ya ce" Pah idan ka hada ido da ita baka ji gabanka ya fadi?"

A sanyaye pah ya girgiza kansa shima cike da mamaki n wai me yarinyar ta tsare masa har haka? Hanja da ba abinda ya dame shi da lamarin wani shine du ya fitini kansa a kan yarinyar da bata tsare shi da komai ba?

Idonsa cikin idon Pah ya ce" Ko daya baka jin haushinta a ranka?"

Pah ya rike hannunsa yana kallonsa ya ce" Son me yake damunka ne? Me ta yi maka ne? Idan wani abin ne yake faruwa ka gabatar min da shi sai na nisantata da kai da mu baki daya, aman idan baka da huja ka barmu mu idasa ladanmu mana"

Kalon mahaifinnasa yake a kasan zuciyarsa yana tunanin wace huja suke so da ta fi wada yake fada madu a yanzu? Wace suke so ne?
tashi yayi cikin fushi ya bar parlon tamkar zai tashi sama inda Mah ta raka shi da kallo tana murmushi tana girgiza kai a hankali, Pah kuwa ya raka shi da kallon tashin hankalin yannayinsa

mah ce ta karaso kusa da pah hannun shi ta kama ta zauna a kusa da shi sosai a hankali tana shafa gefen fuskarsa tace " mai ka fahimta gami da son ?"

tagumi pah ya rafka yace" nikam da za abarni sai ince na fahimci wani abu"

da sauri tace "kamar me?"

Pah ya dan watsa hannayensa ya ce" Ba zan ce ga takamaimai ba, ban san me ta tsare masa ba, ba itace mutun ta farko da muka dauka ba, ba itace kalar bak'ar fata ta farko da muka dauka a cikin duniya ba, sai dai ita kadai ce ta africa, sannan kwarai haka ne ita kadai ce mai kallonsa cikin ido harma ta juya kai tsaye ta ci gaba da magana bayan yana wajen a tsaye tamkar kowani mutun ba abinda ya dameta, tabas itace ta farkon da na ga ta aikata haka ya yi diri diri ya wuce bai dora hukunci a kanta kai tsaye ba, na yi mamakin da yake nan shawarar barinta zai yi ko korata zai yi.....hakan sai ya sakani tunanin a cikin rudani yake cikin biyu watau barinta ko koratan, kin ga ya dora mata sunna wai terorist.....ko wa ta tada a gabansa?, Kin ga Prince yana fada akan mace? Sai na ji ina son zama na ringa kallonsu, sai na ji ina so mu yi cij abinci a tatare da su a table daya a lokaci daya ina kallon su, sai na ji haka kawai ina son na zauna a daidai lokacin da zasu yi fada.....haka kawai nake jin koma meye na yarinyar nan alkhairi ce ga rayuwar son, tabbas na gano tanada matukar tasiri a cikin rayuwar sa ta halin fada ko jituwa....."

murmushi mah tayi tace" isha Allahu lokaci zai nuna mana Allah yasa hasashen dana ke ya tabbata akan son da muneerath"

fuskanta ya shafa ya kashe mata ido daya ya ce" ameen ya Allah kalb"

Sunkuyar da kanta tayi tanajin kunyar pah saboda abubuwan yanzu da yake mata na soyayya tunda shekaran jiya zuwa yau kuma ba wasa yanzu ita har mamaki take yadda jarumtar shi ta dawo kamar ba shi ba, ba zara taba manta yau din nan ba, bata tunanin zata kuma samun ranar sai gashi ta sameta ido bude, ita kam me zata ce da wanda ya haliceta bayan ta kara ninka ibadunta? .....a kasan zuciyarta ta furta'Alhamdulilah'

kama hannun shi tayi tace" muje kayi wanka ka huta lokacin shan maganin ka ma yayi"
a tare suka mike pah yana dan bata rai sabida takura shi da take na shan maganin nan

....

Su muneerath kuwa suna komawa daki ita da iman wace ta biyota dakinta , haka kawai tunanin yadda aka yi ya bata wayarsa take hakan ya sa ta mugun sake da ita dan so take ta fada mata wai ta yaya hakan ta faru?
toilet ta fada dan yin wanka saboda wainar kwan nan da ta soya wai ita a ganninta tayi wani babban aiki ne

Iman ko guri ta samu a bakin gado ta zauna tunani ta fara na yadda zata bulluwa muneerath tabbas jikin ta zata shiga sabida a dan zamansu ta gane muneerath din ba wani wayo ne da ita ba sabida haka ta samu makamar da zata na cusa mata kiyayyar ko wane irin namiji kawai ta tsaya ga dogarin ta ya fi mata domin itafa ta hasasu kamar ta fara samun matsayi a gurin hanja so ya kamata tayi wani abu akai duda bata tunanin wai Hanja zai iya kula wannan yarinyar,aman fadan sun nan ya tsaye mata a rai

Muneerath ce ta fito daga wanka daure da towel a kugunta gaban madubi taje dan daukar mataji ta taje kanta da ta wanke tare da abun busar da kai

dagowa iman tayi dan jin mutsin muneerath din ta zubawa faffada kugunta ido ko keftawa batayi cewa take chab din gaskiya dole ma inyi wani abu akan yarinyar nan tun bata tafi da abinda na dade ina muradi a rayuwata ba oh ji yarinyar karama da kira kamar ita tayi kanta cab da sake wllh

tasowa tayi ta matso kusa da muneerath din da take ta kokarin shafawa kanta data gama busarwa mai

Da nata salon son kusanta kanta da Muneerath din ta ce" dan kawo na taya ki mana?"

Muneerath ta dan kaleta a ranta tana ayana 'su yan gidan nan mamaki suke bani, sai su ringa shiga harkar mutun da sanyin rai bayan mu a namu gidan eh yane ne, kana kallon wanima zai dura maka ashar ya ce kallon fa? Ni du sai na ga wani salon munafirci ne sun kama yaro sun dura masa vitamine ya zama gabjeje yana yawo da yar riga a cikin mutane yana langwui.....' dan murmushi ta yi tana girgiza kanta tuno tambayar da ta yiwa sir cewar wai dan Allah shi zai tuka mu? Sir ya mutu da mamakin jin dalilin tambayar nata dan cewa ta yi ita walahi du kallon wani dan baba da rai take masa, a anguwarsu kuwa idan aka matsawa mutun da sunnan dan baba da rai irin yayan nan ne da ake sangartawa basu iya komai ba sai sangarta da fada da shirme,
Kumewa kawai ya yi a ransa yana ayana lalle duniya mai ba dan adam dama, lamarin rayuwar Munnerath na saka shi kallon duniya a yar mitsitsiya mai cike da abin al'ajab .....watau mai dauke da al'uma masu abin mamaki,

A hankali Ta ringa taimaka mata tana dan janta da hira haka kadan kadan tana nuna mata yadda zata yi kwalliya da sauransu dake iman din yar gaye ce kwararriya ce kuma wajen iya kwalliya tuni muneerath taji dadin yadda iman din ta koya mata simple mak up wanda ya yu mata kyau ko ya zauna das a kyayyawar fuskarta

Komawa bakin gado sukayi iman ta dago kanta ta kalli muneerath tace" niko in tambaye ki man ?"

Muneerath ta dubeta tace "inajinki"

iman tace" daman gami da dogarinki ne ni ban taba jinki kuna waya dashi ba ko irin ya kawo miki visit dinnan a bazatan nan duba da irin yadda na sha ji kina maganar dogari"

Muneerath ta dago ta kalli iman irin a rikice dinnan ta turo dan bakinta tace" to ai ni dogarin ma bamu taba haduwa dashi ba sau daya ne ma wataran nazo wucewa ta kofar fadar garinmu na hange giftawar shi sa ilin da zai shige cikin fada, sai kuma a hanya idan zai wuce , sai kuma ranar da zaku sato ni, sai na nan na wasan karam da kuke cewa dogari, yo Allahna tuba dogari fa dan uwan sarki ne, shima fa rawani yake sakawa, kafar sarki kafarsa, Mamanmu ta ce idan na samu dogari na caba, jira dai nake na koma gida idan ba dogari bana tunanin zan iya aure ni kam"
Da mamakin hirarta iman ke kallonta, abin mamaki, idan ta kula yainyar nan batama fara soyaya dogarin nan ba?, Da sauri ta mike ta dauko computer Muneerath din wace bata anfani da shi sam dan ita batama san aikinsa ba gaskiya, ta zauna ta shiga opperath a nutse ta hada connxion bayan ta saka cod din masarautar sannan ta kuma hada layinta ta hau google
A nutse ta dora harafin sunnan Dogari tare da danawa kan africa ta shiga kallo
A hankali take kallon hotonsu da irin shigarsu da matsayinsu a fadar sarki

Da mamaki ra juyo tana kallon muneerath da yanxun yar riga ce a jikinta daidai gwuiwarta kanta a hade waje guda , dan mak up din da ta yi mata ya fitar da tsarin kyanta, yarinyar ta bada kala irin ta manyan hannu ce aman ta mace a son irin wannan? Sai ta samu kanta da bushewa da dariya tace "yanzu daman muneerath baki taba haduwa da dogarin ki ba, aman kike maganar mijinki dogari meye meye ki ishemu da zancen dogari ? Ta karashe tana wata dariyar ..... muneerath ko ta cika fam sabida dariyar da iman din ke mata

A hankali Muneerath ta cire kanta, seriusly itama abin na damunta, a hankali ta juyo gannin Iman ta dawo gefenta tana kallonta

Iman ta dafa hannunta ta ce" Ina iya taimaka maki har ki samu soyayar dogari mai kyau mai tsari wa ke kadai"

Muneerath ta ji zuciyarta na dan bugawa tana kallon iman ta ce" Allah zaki min haka?, Aman ta yaya ke zaki iya min haka ke da kike nan?"

Iman ta yi murmushi ta janyo computer ta ajiye ta cire wayarta kirar iphone ta gyara zamanta ta shiga Facebook tana kallonta ta ce" Baki san yanzun duniya ta yi ci gaba na mamaki ba?, Daga nan da kike zaune kina iya malakar zuciyar dogari harma ya haukace sai ke ba? Kin ga ta facebook yanzu har aure yake haduwa a kuwa sha shagalin biki a tare, kin ga abu mafi sauki kennan a yau yau ki fara hira da dogari, a hankali ki tura masa hotunnanki ki mike a haka ki karkato bombom din nan naki na maii hotuna masu masifar kyau ki karkato mamanki ki rike su ki bankaro su sosai ki yi yannayi na yarinya mai fuzga wace zata tada sha'awar namiji daga ya kaleta irin haka...." Iman ta mike ta rike mamanta ta wani gantsare ta turo lebunnanta ta cije daya ta wara kafafuwanta takashe ido daya inda Munnerath gaba daya baki da hanci bude tamkar sabon kamui take kallon iman har ta gama ta zauna ta dora da fadin" mu dora shi saman dp dinki na facebook mu ringa matsa masa har ya amshi invitation dinki daga nan mu ringa masa hira kala kala idan yana son sannin wacece ke mu fada masa ki fada masa irin son da kike masa, na tabatar maki cewa nan da yan kwanaki zai haukace maki sai kin ga dogari a kasar nan koda a kafa ne"

Gaba daya Muneerath sai ta ji kanta na sara mata, wani irin takaicin iman ne ta ji na shiga zuciyarta, muryarta a shake ta ce" Ki ce karuwanci zaki koya min?"

Iman ta tsaya da maganarta tana kallonta da mamakin jin furucinta domin ita dai a nan bata ga meye ya kawo kalmar nan ba

Muneerath ta girgiza kanta gwuiwarta a sage ta ce" Yaushe mata suka yi arha har haka? Yaushe muka yi zubewa har haka? Yaushe musulunci ya zama abin wasa har haka? Yaushe rashin sannin ciwon kai ya cika matan duniya har haka? Anya kuwa maganar ta al'adu ne ba iskanci bane duba da koyarwar litafin daya ne?? Anya kuwa mace na anfani da karancin shekaru irin nata kuwa? Dole a ambaci mazinaciya kafin a ambaci mazinaci domin du iskancin namiji malamarmu ta pc ta ce da mu ba zai kai hannunsa kan mace ba sai ya kula cewar itama lalataciyar ce! Yanzu iman ni da ke Mah ta ce da mu ko tabamu namiji ya yi zamu dauki ciki, a nan ta ce da mu koda kowa na yawo kansa bude mu mu kasance masu lulubewa domin suturar mace mutuncinta.... aman shine kike irin wannan abin? Anya ba tambayar mah zan yi ba kuwa ke ba yar iska bace?"

Iman showwwwwwwwwwwwwwwwww
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 6 □□□

Iman ta zaro ido da sauri tana kallonta ta ce" ke wai me kike fadi haka, ba ke kike haukan sonsa ba ni kuma me ya hadani da iskanci wannan ai ba iskanci banr!"

Muneerath ta mike rai bace ta ce" Walahi ke yar iska ce kuma sai na jadadawa mah kar ki yi cikinki ki goga min! Nan nan ake yiwa yar gidan idi gorin ta yi cikin shege nan da nan babanta ya koreta , dan na ce maki ina sonsa ai Ogama ya sani kuma shima ya ce ya san ba dogari ba ko baban dogari ne zai so ni shine ke kike cewa ni Muneerath na tarbi namiji nace ina sonsa? To bari ki ji, walahi dogari idan ya ga dama ya ce yana sona zan fadawa aminiyata amina mu ja masa rai na kwana biyu kafin na bashi amsar eh ina sonsa, idan kuea bai ce ba ya jima bai so nin ba sai me? Sarki ne dai ko? Yau ina hostess dolema zai zama dan uwana dan ina komawa zan kai gaisuwa kai tsaye gaban mai Damagaram, ko sarkin maradi!"

Tana gama fada ta juya cike da bacin rai tana kallon iman da mamakinta ta fita da wayarta tana girgiza kai a ranta tana ayana 'dama ai da ganninku kwartaye ne ku, ni dai ba kwartuwa bace!'

Iman mamaki, kunya, dana sani suka kusan sumar da ita, bata taba tunanin zata zile mata haka ba, yanzu du irin bata lokacin nan da ta yi tana mata surutu ya tashi a banza? .....mamakin furucin yarinyar kuwa ya tsaye mata a rai, bata gane ba, meye a ciki dan ta nunawa namiji tana sonsa? Tsaki ta yi tana girgiza kanta a bayane ta ce" Bagidajiya kawai, tunda dai ba zaki furtawa namiji kina sonsa ba bani da damuwa da ke dan na san ko ya yar gwal ce ba fai MY PRINCE ya fara nuna so a kanta ba, baka kirin mai katon bombom!"

Bayan salar isha'i

Hanja ne ya shigo da dan hanzari kamar yadda tafiyarsa ta kasance , idan ka gansa yana tafe da lako lako to bashi da lafia ne

cikin parlon mah ya shiga da salama a bakinsa cen kasa kasa

Mah na zaune tana dan nazari ya karasa kusa da ita sosai ya zauna dauran kanshi yayi a kafadun ta a hankali yake sauke wata irin ajiyar zuciya mai zafi yana yi yana fan lumshe idannuwansa

Kallon fuskar shi tayi a hankali ta jimke hannunsa dan tana jin yadda zuciyarsa ke bugawa, a sanyaye ta ce" Me ke damun zuciyana?"

Idannuwansa ya lumshe yana jin zafi a kasan zuciyarsa a hankali ya ce" Ina jina ba karfi a gabanku, ina so na kasance mai faranta maku, ina so na cire maku damuwarku"

Idannuwanta ta lumshe tana murmushi a sanyaye ta ce" Bamu da damuwa khalb bayan wace bawa baya iya cirema kansa sai yadda Allah ya yi da shi, you see farin cikinmu kuwa na tare da mu tunda kana gefenmu, yanzun yaya maganar dawowar naka? Ina so ka dawo kusa da mu"

Dan murmushi ya yi a hankali ya ce" Tigre fa?"

Mah ta dago tana dungurar kansa ta ce" Ka kaita gidan zoo mana?"

Ido ya kwalalo ya ce" Sai na mutu za'a kaita mah, idan na mutunma a barta ta ci gadona in ban haihu ba, in kuwa na haihu na tabata my Princ zai rike min ita"

Mah ta dan shafi gefen fuskarsa a hankali ta ce" ka zo da ita, ka sakata a dakinta na nan, aman gaskiya karta ringa zuwa gaishe ni na yafe"

Yar dariyar da bai shirya ba ya yi yana kallonta kafin ya saka hannunsa ya buda alkur'anin dake ajiye a gefenta ya budo wajen bakara ya gyara zamansa ya tankwashe kafafuwansa a hankali ya buda muryarsa ya yi bismillah ya fara karanta mata ita a sanyaye wanda take gane dukan kalaman ciki idannuwanta lumshe tana idasawa a kan lebenta shauki na dibanta tana cike da farin cikin yannayin

Na su su tashi ba sai da dare ya yi sosai Hanja ya yi mata salama shima zuciyarsa sakai nauyin ya sauka hakama bacin ran da yake ciki ya age sosai ya nufi bangarensa inda itama ta shige dan yin wanka ta tarda nata mai gidan

_____

Karfe takwas da rabi ta gota
A hankali take tafia tana bin matatakalar gidan cike da dana sannin biyowa ta matatakalar sai dai haka kawai ta ji ra'ayin saukowar ta nan yau dan ta irga ko hawa nawa ne, sai dai abinda bata sani ba mugun wahalar da kanta ne ta shiga yi ta sauka a hawa na hudu bayan ta gama hada zufa ta duka ta cire takalmin dake kafarta cike da dana sani ta daga kanta ta kalli saman da ta baro tana tunanin ko dai komawa take ta biyo ta lft din?

Cijewa ta yi a hankali ta ci gaba da saukowa a bayane ta ja tsaki ta ce" Mutun shi ke kashe kansa dan neman fitina irin tasa! Yanzu da suka yi wannan hawan dan a ce masu me? Yanzun tsakani da Allah waye zai iya hawan nan a cikin gidan nan? Kawai kwaliya da barnar sumunti? Wannan ai almubazaranci ne na tabata wannan bulon zai iya yin wani gidan aman aka ajiye shi a matsayin na hawa a taka kawai....."

Tana mitarta ta idasa saukowa kasa ta daga kanta tana ajiyar zuciya a hankali ta ce" ni da matakalar nan sai a kiyama idan na je aljana na tarar da matakala mai sunna matakalaba wannan ba!"

A hankali ta idasa shigowa pankamemen Falon bakinsa sake gannin an cenza labulayen dake ciki an saka farare kal kal masu girman gaske da daukan ido

A hankali ta daga kanta tana bin dakin da kallo yana fitar da kanshin turaran wuta mai sanyin kanshi , ga sanyi yana ratsa ko'ina na falon kafin ta sauke kanta a kan sababin kujerun da aka zuba a tsakiyar falon suma farare kal kal kal, da irin yadda aka ajiye wasu dima diman po da flower a cikinsu jifa jifa su dinma kalar fari ya fi yawa a tare da su sai dan ratsin kalar blue mai duhu

A hankali ta dora kafarta saman kafet din da yake tsakiya wanda yake da girma sosai tana kallonsa mai wasu abubuwa a sama masu shige da kwai harma idan ta zo takawa sai ta kauce kafarta kar a je kwon ne aka jejera ta taka ta fasa dan yanzun ita ta dawo daga rakiyar masu kudi da yan gayu , ta gane cewa ba abinda ya gagare su, da kudinsu suke shagalinsu, barikinsu kuwa aljihunsu

A hankali ta juya wajen katon madubin dake ajiye
Idannuwanta ta lumshe a hankali ta dora hannunta a gefen fuskarta tana kallon kanta tamkar ita dince a ciki

Wajen idannuwanta ta tsurawa ido itama tana mamakin kalar idannuwanta, a cikin yam gidansu du haka idannuwansu suke tamkar na mage, na wasun su kuwa tamkar na aljanu domin ya saka ja mai haske kamar na mayu

Rigar dake jikinta ta bi da kallo, a hankali take sauke ajiyar zuciya ta kai hannunta ta shafa shafafen cikinta da yanzun yake bata mamaki a shafe tamkar bai tana tasawa ba, sai irin kirarta da sanadiyar shafewar cikin ta karra bayanar da kanta tamkar wata niki minaj ta bayan, blue din riga mai duhu sosai ce a jikinta , bata da kwaliya ko kadan sai dai budadan wuya ne da ita sanann hannayenta a dan bude suke kuma har kusa fa tsintsiyar hannunta, rigar ta bi lafiyar jikinta sosai ta kwonta mata har kasa sai yar tsagar da ta bata haushi ta ringa mitar du yadda ka yi da nasara sai ya nuna maka shi dan iska ne, sai da ya miko da dinkin zarensa ya kare?
Sai hular da ta saka mai haske a kanta wace ta haska kalar fatarta
Bata yi wani dogon kwaliya ba, dan lips kadai ta shafa a kan lips dinta sai kwalin da ta furta da kyar tana share kwallah da ta tarun mata, sai turaren da ta shafa sosai a jikinta wanda ya ratsata sosai

A hankali ta kai hannunta ta jikin madubin zata dora dan ta shafa madubin da yake birgeta sosai , a lokacin ta jiyo muryar Iman da Mah ta turo ta kirayeta ta ce" Munee aka ce ki zo deening"

Muneerath ta juyo da sauri gannin har tara ta yi su kuwa da suke kari tun takwas a tunaninta har sun gama sun haye sama shi yasa ta tsaya shiririta

Da dan sauri ta zagaya ta nufi deening din ,
Dan saurin da take ya saka lamarin bada kala sai ya zamana kafarta na motsawa wajen na yin hanyar da Kafar ta nufa, sai kaeai ta ringa aikata sitin saba'in ba tare dama ta san tana yi ba

A hankali ta dan rage tafiarta gannin Pah zaune, gefensa na dama HANJA, sai Mah sai iman

A dan sanyaye ta yi masu gaisuwar jimula bayan ta kara binsu da kallo a ranta tana ayana' yanzu Mah ta saka ni gaisuwar rungume rungumen nan ni kuwa walahi kunya nake ji'

Har zata zauna Mah ta ce" Hi girl, baki gaishe mu ba fa?"

Muneerath ta hadiyi yawu a hankali ta karasa kusa da Iman da ta fi kusa da ita ta dan rage tsayinta ta mana mata kiss a kuncinta tana yatsina fuska a ranta tana ta aibata gaisuwar nan ta zagaya ta yiwa Mah, lokacin ne kuma Hanja ya rike cokalin dake hannunsa da wani yannayi yana jin hankalinsa na tashi dan sam baya so ta masa wannan gaisuwar shima haka kawai baya so!

Sai dai ga mamakinsa ko Pah bata yiwa ba ta koma ta zauna da yaren hausa tana dan murmushi ta ce" Ai dai banda gardawa"

Mah dake kallonta ta yi dan murmushi dan bata san me tace ba aman da bata yiwa hanja haka ba ta ji dadi ainun har cikin ranta

Pah da ya gama ne ya fara mikewa yana fadin cewa meeting ne da shi tare da ministocin kasar , dama a shiryensa yake cikin suit dinsa ruwan ash mai duhu

Mah ta mike da dan sauri cikin shigarta na abaya ta fita a kujerar ta mayar da kujerar ta rufe ta bi bayansa da dan sauri, sai ya yi sauran Hanja dake zaine

fuskarsa a hade da Iman da ta kasa tashi duda ta kare, sai Muneerath da ta gama hada dan abinda zata taba ta zauna abinta ta saka cokalinta tana dan ci, ...sai dai irin cin nan ne mai bayar da haushi domin tana ci ne tana dan buga cokalin a farantin hakan yake bada sauti

Da dan sauri Iman ta kureta da ido tana mata alamun ta bari, domin idan ana saman table ba kasafai ake surutu idan yana waje ba, uwa uba irin cin abincin nan na bashi haushi domin ya tsani idan kana cin abinci cokali na yawo a cikin plat dinka kwata kwatama cin abincin na dan lokaci ne da yake gannin babu fa'ida bata lokaci ana yi, shi da kansa dan shayin da yake surfing ne ya zaunar da shi

Muneerath da gaba daya take sha'aninta a ranta fadi take" Wannan mutun ba dai fari ba, kuma sai yana saka kaya baki , yanzu jalabiyar nan dama nasaruma na sakawa?"

Idannuwansa ya rintse dan tunda ta zo shi dai bai kaleta ba, ta kara bashi haushi da bata kawo gaisuwarta ba, da bata masa gaisuwa irin yadda ta yiwa su ba da farko yaji dadi aman daga baya sai ya shiga mamakin yaya aka yi bata yi gagawar yi ba bayan a kulun har haushin iman yake ji kamar mai jira safiya ta yi idan yana gidan ta rukunkume shi ba, sai kuma yanzu abin nan da take yi da cokali har tsakiyar kansa yake hawa kamar ya buga kanta da table din nan ta suma ya huta

Mah da ta dawo ne tana kallonta ta ce" Muneerath daina wasa da abinci ki ci ki gama, yayanku baya son ana hada cokali da plat kukan hakan na tayar masa da hankali"

Da mamaki muneerath ta dakata tana kakkon mah, kai, ya ilahi ta fada a kasan zuciyarta, dama maza na aljanu hala? Domin a gidansu akoy yayarta da ba'a wasa wuka idan tana wajen, ba'a gurza galan a kasa kuma ba'a gurza kwano a kasa, sannan ba'a cakal cakal da cokali a kwano idan dai ka mata haka yanzu zata fadi ta shigo bori irin na masu aljannu ta sume idan aka yi wasa a wajen

A hankali ta dubi Mah da yaren turanci ta ce" MAH HALA ALJANU NE DA SHI?"

A tare Iman da HANJA suka dago suka sauke dubansu a kanta

Kallon da Hanja bai mata ba na yana hanna kansa ya samu idannuwansa tsumu tsumu a cikin nata a lokacin da ta dubi tsabar idannuwansa take tambayar shi hanja Aljannu ne da shi?

"Innalilahi ya salam ya rab" shine abinda ya fito daga bakin Mah tana mai kai duwawunta saman kujera tana kallon Muneerath kafin da sauri ta kai dubanta wajen Hanja da ya mike rai bace ya.....

Sai fa ta haukata ka
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar:
DUTSE

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)

[T.M.N.A]

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 7

Da sauri Mah ta mije tsaye gannin wajen ne yake nufowa ta juya gaba dayanta ta dora hannayenta saman kirjinsa ta tare da dukan karfinta tana kallon fuskarsa ta ce" Khalb me zaka yi?"

Hanja da zuciyarsa ke kunna yana kallon Mah ya datse lebensa na kasa yana tsaye kikam ya ga Yadda Muneerath ta zabura ta mike tana wuki wuki da idannuwa rai bace ya ce" Mah dan Allah ki miko min ita "

Muneerath ta zarro ido da sauri ta labe a bayan ta ki ta fito gaba dayanta duda labiyar ba wai ba'a ganninta bane domin Mah bata da baban jikin da zata iya boye na Munnerath a hankali ta ce" A miko masa ni kuma? Yo me na maka?"

Da sauri Mah ta kama hannunta ta bayanta ta dan matsa dan ta mata alamun ta daina magana idan yana yi, Muneerath ta dan saka kara tana kallon hannunta tana kallon yadda ya wani irin zuba mata idannuwan san nan ta turo baki tana kunkuni a kasa kasa

Mah ta kama hannayensa a hankali ta zaunar da shi saman kujera ya kasance sun sakata tsakiya shi da Muneerath din da sai da ta ga ya zauna kafin take maida duwawunta saman kujerar tana sauke ajiyar zuciya cike da tunanin to shi kawai haka yake? Ta kula kiris yake jira ya ringa hararanta ko dai haka kallonsa yake? Yanzun daga tambaya ai in ba haka bane sai kawai ya ce mata ba haka bane kau? Mtsssssss halaya sak irin na marar wayau!

Mah dake maida numfashi a hankaki ta karra dora hannunta saman hannun Hanja dake ajiye saman table din nan a sanyaye ta ce" Me yasa kake saurin hawa a kanta? Me yada maganarta kadan ke hasalaka??"

Hanja ya lumshe idannuwansa a hankali bai bata amsa ba , shi da kansa tambayar kan nasa ne yake a kan lamarin yarinyar nan, shi dai ya san a ba sa'arsa bace , nesa ba kusa ba,
Abinda yake bashi mamaki da yainyar nan ba wani dogon karatun da ya kamo nasa tayi ba na farko, na biyu ba wata mai shekaru ba, na uku ita ba wani irin yan matan nan masu tsaida numfashi ba bale ta ce dan kyanta take masa iya shege da shiga hanci da dukunkune, haka kawai ya sauka a kungurmin jeji ya kwasota ta zo ta hanna masa zaman lafia? Ya kula ko kallo bai isheta ba kamar wata tsiya! Shi kam ya shiga uku yana zaman zamansa sun dauko mahaikaciya

Muneerath dake dan bubuga yatsanta a hankali ta dago ta kale shi da kuma mah Bakinta ta tabe ta kuma maida kanta kasa

Iman dake zarro ido cike da mamaki tana kallonsu gaba daya ce ta kai hannunta ta dafe kuncinta tana mai ci gaba da kallon nasu

Hanja ya kai hannunsa wajen gashin kansa a hankali ya ce" Yau za'a kawo tgr"

Mah harda su ajiyar zuciya kafin ta gyada kanta ta kuma sauke dubanta a kansa a hankali ta ce" Na mikk maka tea din ka gama sha ne?"

Bai kai ha bata amsa ba Muneerath ta mike abinta tana ayana bara dai ta shiga kicin ta da kokoya hakananma dan ta ga su a nan ba fadan ta bata suke yi mata ba

Kasa kasa ya bita da kallo har ta juya ta nufi hanyar kicin din sai kuma ta ja ta juyo da dan sauri tana kallonsa ta juyo ta taho da dan sauri hakan ya saka shi jin gabansa ya yanke ya fadi

Tana zuwa facing din Mah ta ce" Mah na manta ban fada maki ba, walahi ki binciki wannan yarinyar yar iska ce"

Ba Mah ba , shi da kansa da ya lumshe ido sai ya samu kansa da budewa tar yana kallonta

Iman kuwa cikinta ne ya bata wani irin kululu da sauri ta kalli Muneerath gabanta na dukan tara tara

Mah yannayin hankalinta ya nuna hankalinta a tashe yake tana kallon Muneerath ta ce" Daughter me yada kika ce haka? Wani irin iskanci kuma?"

Iman da sauri ta zabura ta mike tana kallon Muneerath ta ce" Mah walahi karya take min wannan yarinyar fa inaga bata da hankali fa Mah"

Wata uwar Harara da Hanja ya sauke a kanta ta yi gagawar zama hannayenta na bari hakama jikinta cike da tsoro da tashin hankalin ashe yana zaune ta yi magana muryarta sama sama har haka, da kuma tsoron abinda Muneerath din ta fada da yannayin da fuskar Mah ya nuna

Muneerath ta tafa hannu ta ce" Kai mutane, yanzun nice mahaukaciyar? Kin ga ban so nuna mata abinda kika ce na yi ba aman tunda ke ba yar kirki bace zan nuna mata ba sai kin kwaso cikinki ba ta kare a kaina ina daki....."
Cike da shiririta irin abinda ya sha kanta kaeai take son isarwa ta bar wajen ta juyo wajen Mah a sangarce ta ce" Mah, daga ce mata ga wanda nake sa ran ya zamo mijina muna magana ni da ita watau Dogarina ta ce meye Dogari? Ni dai na ki fada mata sai ta dauko computer ta tambayeta, computer ta fada mata sai cewa ta yi xata

taimake ni, ni dai ina kallonta du ban gane ba Mah ba sai ta shiga wani abu irin na kwartaye ba?"

Mah da hankalinta ya tashi da yannayin da Iman cike da tsoron kar a je yarinyar wani mugun abu take aikatawa da bata sani ba, cike da tsoron kar a je ta dauko yar mutane tarbiyarta ta kakace bata sani ba a sanyaye ta ce" Wani abin take yi Muneerath ?"

Muneerath ta gyara tsayuwarta ta ce" Cewa ta yi wai na bude facebook a yi hotona na turo sama da kasa a dauka a turawa dogari"

Mah dake kallonta a hankali ta ce" Meye sama da kasa?"

Cike da jin kunyar Mah din Muneerath ta sosa gaban goshinta idannuwanta suka sauka a kan fuskar Hanja da gaba daya ya zuba mata ido da kallon hararan da bata san me ta masa ba

A hankali ta ce" To kuma mah dan Allah kema ki gane mana, cen da cen fa"

Mah ta dafe kuncinta a hankali ta ce" Muneerath wani mugun abin take yi ne iman din? Ki fada min kin ji yarinyata?"

Hanja ya kalli yadda mah jikinta ya yi sanyi ya kuma maida dubansa kan Muneerath kafin ya girgiza kai ya mike ya juya rai bace ya sauka daga wajen cin abincin ya koma falo ua dauki wayarsa ya shiga kiran wanda zai kawo masa zakayarsa wace yau ya farka da wuri dan a kawota ya sakata a dakinta kafin suke hakura ya koma gidansa da abinsa

A hankali ya dago dubansa daga inda yake zaune jin ana bubuga table din sannan maganarta na tashi sama sama ya sauke dubansa a kanta
Gabansa ne ya yanke ya fadi daidai lokacin da ya ga Iman na tsaye tana ta rantse rantsen bata yi komai ba, a daidai lokacin ne Muneerath ta cire hular kanta ta ajiye a zafafe ta ce" Bara ki ga abinda take yi din an gaya maki tsoronaki nake da ba zan fadi ba ko kuma an saurayi muka hada da zan maki shari? Kin ga fa...." Lokaci daya ta shiga bankarewa gaba dayanta tana dan juya jikinta kafin ta daga hannunta ta cusa cikin gashin kanta baki mai kyan gaske ta lumshe idannuwanta ta turo kirjinta , lokaci daya ta bude ta daidaita tsayuwarta tana haki ta ce" kai Mah wani abin ba zan iya nunawa ba dan gaskiya ni ba yar iska bace, wai wani na yi haka ta dora saman dp a turawa dogari, tsakani da Allah soyaya ko iskanci?"

Mah ta rafka tagumi a hankali ta ce" Iman?"

Iman ta sada kanta hankalinta tashe ta fara magana da kuka kuka ta ce" Mah, ni fa ba haka nake yi da maza ba dan in taimaketa ne na ga ko sannin zamanta bai yi wanda take so din"

Munnerath ta girgixa kanta ta ce" kuma a haka ne zai so nin? Baki san mu a garinmu sarkin garinmu na kirki bane? Su fa sarakan garinmu basa son yan mata yan iska, haka kawai in ya ganni ba sutura ai sarki ba zai sakama aurenmu albarka ba ko?"

Iman zata bata amsa Mah a sanyaye ta dago hannayenta ta ce" ku taho, ku zo gareni ku zo kun ji?"

Kallon junna suka yi Iman da Muneerath , Muneerath ta sakar mata harara da dara daran idannuwanta ta dan kebe bakinta irin ta murguda mata shi din nan , iman kuwa ta lumshe idannuwanta hawaye suka zubo mata a hankali ta sauke dubanta a bayan Hanja da ya gama kallonsu ya mike wannan karron ba a zafafe ba ya juya jikinsa a wani irin mace ya juya tamkar wanda bashi da laka ya fice a falon gaba daya

A hankali take saukowa da hannayensu a cikin nata har sai da suka gama saukowa suka karasa kusa da kujerun
Maimakun ta hau kan kujerun da su sai suka zame saman kafet ta tankwashe kafafuwanta ta saka su gaba su biyun

Iman , yar budurwa kyakyawa mai shekara ashirin da bakwai, mai karamin jiki irin nasu mai ilimin boko da na islama, mai dama da yawa a gabanta
Sai Muneerath kyakyawar yarinya karama yar africa, mai ilimin boko daidai gwargwado da na islamiya, yarinya mai tatare da abubuwan mamaki, wace du wanda ya karewa rayuwarta kallo zai yi imanin rayuwarta na tafe ne bisa tsarin ubangiji, tana matakin da take a yau ne dan Allah ya tsaya mata

A sanyaye ta ce" Kun kuwa san Mecece mace?,iman da Muneerath ku bani amsa idan an ce ku fadi wacece mace wacece ita?"

Kallon junna suka yi, Iman ta sada kanta a hankali ta ce" Mace na nufin halitar da Allah ya halita mafi daraja a cikin halitunsa na dan adam aman macenta "

Mah ta tsura mata ido kafin ta kalli Muneerath ta ce" Muneerath ?"

Muneerath ta sauke ajiyar zuciya , cen kasan zuciyarta sai tana gannin wani bambarakwai, yanzun a cema mah ga laifin da iman ta yi maimakun ta kama yi mata ihu ta zazageta ta mata rantsuwar idan ta dauko mata magana cen ita ta sani ta karata da abinta sai ta wani zaunar da su kamar wa'inda suka yi abin kirki tana masu tambaya a hankali? Ita rayuwar mutanen nan har yanxu mamaki take bata, rayuwar wancen rusheshen ce kawai take dan shige da ta yan jagaliya irin ta gidansu sak, dan ta kula shi daga an taba shi so yake ya warci mutun ya buga, ita kuwa Allah ta tuba me zai sa ta zauna wannan mai hannayen murda murda ya cin mata? Haka kawai ya karyata ya barta da dingishi?

A hankali ta ce" To mah mace ana nufin uwa ko? Mu a cen in aka cema wada ba'ai mata aure ba mace sai a ce yaro wawa ne, a nan dai ke kadai ce mace mu nan du yan mata sunnanmu, ko me yasa suke cewa haka?"

Mah ta sauke ajiyar zuciya tana murmushi a hankali ta ce" Mace, Mace itace uwar al'uma....., Kun ga mace ita ke daukan ciki, ta raine shi a cikinta, cikin ikon Allah ta haife shi, bayan ta haihu ta shayar, ta bada tarbiya.....wannan itace mace, Daughter Mace ya dace ta kasance mai nutsuwa, mai sanyi, mai mutunci, mace ya dace ta kasance mai kare suturarta.....idan aka samu uwa marar tarbiya yaya kuke gannin yayanta zasu kasance ?"

Bata tsaya sun bata amsa ba ta kara riko hannayensa da suka kasance fari tas da kuma baki mai haske tana kallonsu ta ce" ina jin farin ciki idan na ga mace ta kama mutuncin kanta, idan kuma na ga akasin hakan hankalina na tashi sosai, du sai wasu tunani su shigo cikin kwakwaluwana, shin kun san kuwa Mace na iya cenza akalar mugun nufin namiji ya dawo kyakyawa kamar yadda idan da kyakyawan nufi ya nufota tana iya ja ya lalata mata rayuwa?, Mace na iya hadasa haka idan ta kasance

mai watsa kanta, kece kika nuna masa ke da kanki baki sandarajar kanki ba dan Allah ta yaya zai san naki?"

Wata ajiyar zuciyar ta sauke ta dauko wayarta ta ajiye a tsakaninsu a hankali ta ce" Wannan abar, wannan abar lalacin dake tare da ita ya fi rinjayar dan adam fiye da alkhairinta....., Ta dalilinta dubu sun lalace, ta dalilinta dubu sun afka muguwar rayuwa a likacin da basu ankara ba, itace ke shagaltar da musulmi wa zuba sallah a kan lokaci, ita ke shagaltar da mace a cikin gidan mijinta wa aikata aikace aikacen da zata samu lada, wannan da kuke ganni har hanna yaro zuwa aiken iyayensa take, a haka take jan yan matanmu suke daukan hoto su ba karuwai ba, su ba kilatatu ba su watsa ta yanar gizon da basu san ina da ina zai zaga ba, wa da wa zai gani? Idan a tunaninsu sun goge da suka goge din ina ya je ya zubu? Ya salam wasun sai a lokacin da za'a tara masu kasa komai zai fito.....Iman, Muneerath shin me ya dace mace ta yi?

Muneerath ta saka hannayenta ta dafe kuncinta a sanyaye ta ce" Wollah mah ko? Watarana sai na ji ko karatun bokon nan kamar iskanci ne fa?"

Mah ta kaleta tana kara karantarta

Muneerath ta ce" to Mah du abinda nasarun nan suka kawo kana shagalta kake dawowa dan iska"

Iman rai bace ta ce"

□□□□□□□□ Ba dai ni ba kau? Ni kuka hanama nvl □□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

Iman rai bace ta ce" Sai ki ringa cewa dan iska dan iska, yanzun da kika fadi haka a gaban prnc me kike so ya dauke ni? Da kike cewa yar iska ce ni da wa na yi iskanci?"

Muneerath ta tsareta da ido kafin ta tabe baki kasa kasa ta ce" Ai shi dan iska ba boyuwa yake ba, kuma ni ina ruwana dan yayanki ya sani ai gwarama ya sannin ko zai iya maii fada in kina jin tsoronsa malama ki daina min fada wollah kin ga dai ba tsoronki nake ji ba"

Iman dake share kwallah tana hararanta ta ce" Ni din tsoronkin nake ne? Duba ki ga fa fada ne kike tankwalar Yaya Hanja fa, salon ya hada mu daga ni har ke?"

Muneerath ta zaro ido tana dafe habarta ta ce" Kuma ya mana me yo?"

Mah ta saki murmushi tana kallonsu idan wannan ta dauki magana ta ajiye wannan ta dauka, gaba daya wani irin nishadi y'ayan ke sakata, sai take gannin y'ayan da bata samu bane a gabanta suke rigima irin ta yaya da kanwa, duda na Iman na mata nuni da wani lamari irin na kishi, na Munnerath kuwa tsabagen yarinta da magana kai tsayenta ke birgeta

Gannin sai yi suke a sanyayenta ta ce" Ku saurara "

Kallonta suka tsaya yi su dukansu
Mah ta ce" Dan Allah ku kasance masu rufe suturarku , ina rokarku kan ku kasance masu anfanuwa da abin anfanar dake tare da waya, kar ku yarda dan ya zama sabo ga yan mata da mata da samarin da wasu manyan mazajen da basu san me suke ciki ba suka mayar da waya filin baja kilinsu kuma kuce haka zakuna yi da taku rayuwar....idan zaka yi abu ka fara tuna ubangijinka, ka tuna mutuncinka, ka tuna na ahalinka, ka tunana y'ayan da zaka samu idan Allah ya hukunta maka haka"

Cikin lumana, a sanyayenta ba tare da hargagi ko iface iface ba, cikin ilimi da tarin nutsuwa ta yi ta yiwa yaren nasiha daga karshema sai suka haye sama suka tare a bangarenta suka shige kicin din falonta suka shiga yin cake wanda Muneerath ta bada hankalinta cike da farin ciki tana kallon yadda Mah ta gama kwabawa ta zuba a abubuwan gashi masu kala daban daban, duka tana kallo aka saka a cikin abin gashi aka daidaita lokacin gasuwarsa sannan suka dawo wajen hada cream na shafawa a sama wato d coration

Wani ikon Allah, yau ta fara gannin yadda aka yi haddin cake , yau abin ya shiga cikin kwakwaluwarta ya zauna mata wanda take tunnanin idan tace zata gwada tabas zata iya yi domin idan ana koya mata girki sam ganewama nema bata yi bale har ta rike wani abin, aman a wannan itace harda su tambayar kowani kalar cake haka ake daidaita masa lokacin gashinsa? , Hakama a lokacin da za'a yi crm din sosai ta samu kanta da bada hankalinta da rike abin a ranta sosai, nan Mah ta zuwa clr yelow mai haske ba carrr ba ta yi decoration ma mai heart din ta dora wlcm Pah

Sosai suka cika dare da yan matan, bini bini Muneerath na hankalce da irin yadda Mah ke zuwa ta yi kiran Pah ta dawo, hakama da akai kiran sallah ki second daya bata kara ba ta kora su yin alwallah suka saka rufafen sutura suka gabatar da sallarsu cikin nutsuwa

Sai da dare kowace ta nufi dakinta

Muneerath na kwonciya bayan ta yi wanka ta saka yar rigar barcinta ta kwonta ta zubawa clng ido

A hankali ta lumshe idannuwanta a bayane ta ce" Shin haka dama wasu gidajen suke? Dama akoy iyayen dake daukan y'ayan wasu tamkar nasu? Dama akoy iyayen dake yiwa y'ayansu nasiha?, Dama akoy gidan da ake wuni a kwana ba'a dankara ashar mai zafi ba?, dama akoy iyayen da zasu ji y'arsu na kokarin son kauce hanya su zaunar da ita a dabara su mata nasiha?, A gidansu da aka ce tana fita yawon iskanci ne Mamanta mahaifiya cewa ta yi Muneerath matsalarki ce, in dan maza ne kuma wasu ba'a haife su bama, sai sun cinyeki ya babunki su yarda banza!
Mahaifinta kuwa cewa ya yi: lale yar oga yanzun kema iskancin zaki fara ko meye? To dahuwar mutun mai kosai.....!,

A hankali ta juya tana lumshe idannuwanta tana tunano magangannun mah
Inda take masu nuni da idan sun kare mutuncin kansu sun rufawa har ita marikiyarsu asiri ne, sun cireta a kunya
A hankali ta dora hannunsa saman yar fulawar da Mah ta ajiye mata mai kanshi tana shafawa tana lumshe ido dan barci ke fuzgarta ta kuma duba tsarin rayuwa irin tasu.....
Ba zasu taba daina bata mamaki ba

Dan murmushi ta yi a saman lebenta kasa kasa ta furta" Inama ku farga ku gane mecece duniyar? Inama ku jawo mu a yanzun da lokaci bai kure maku ba? Inama ranar da zan dawo gare ku na tarda kabarin kun neme ni har kun yi kuka? Dama ina dawowa na tarda a gidanmu an fara bambance yaya da kani? "

Kanta ta dan girgiza tana ta hangi badakala irin ta gidansu
Ba ruwan kowa da kowa
Ba abinda ya dami wani dan wani na cikin hali na mugun yannayi
Ba ruwan kani da jin kunyar yayansa ko kuyaye wulakanta yayansa
Sai a dambatu uwa ta shigarwa yayanta fada a daki dan mijinta dan abokiyar zamanta dan son kai irin nata koda kuwa yaron nata ne baida gaskiya

Cike da tunani irin haka ta samu barci mai nauyi ya yi gaba da ita aman wayarta ta ma'aikata a kune kuma da sabis koda kuwa kira zai iya shigo mata a kowani lokaci dan a shaida mata idan tana da tafia

Ragaitacen barci ta yi a washe gari, ba ita ta fito daga bed dinta ba sai da Mah ta yi shiga ta hudu tana dubata domin ko kari ta ki ta fito ta yi tana sheka barcinta a nutse

Gaban mirror take tana dan masaging din wuyanta da take ji ya rike mata kadan

A hankali ta dauki abin jan baki ta dan gogama lebenta mai ruwan ja

Kurawa fuskar nata ido ta yi yadda takr sheki, a hankali ta shafa gefen fuskar nata tana bin jar rigar dake jikinta da kallo, rigar sakakiya ce sosai kuma doguwa ce har kasa

Jan bakin da ta saka ta sa hannunta tana gogewa , sai dai ba mai fita kwata kwara bane domin ya bara mata sawunsa kadan ana ganni

Turaren ruwan dake ajiye ta dauko a hankaki tana dan fesawa a wuyanta da jikinta

Lumshe ido ta yi dan turaran wani irin sanyin kamshi ne da shi , kafin ta bude idannuwanta tana kara kallon yadda idannuwanta suka karra kyau masha Allah

Cikinta da ta tabata yinwa ta gama cinsa ta shafa a hankaki ta mika hannu ta dauki mayafin rigar fari ta yafa a saman kanta kafin ta juya a nutse ta saka silifas irin tada biredin nan mai ruwan ja ta saka ta bude dakin a hankali ta rufe tana tafe tana dan danna wayarta tana kuma kallon gabanta

Accenceur din ta dana ya bude ta shiga a hankali tana kara lumshe idannuwanta kafin ta dana kiran sir da ta tarar ya yi mata kusan kira shida

Bayan ya daga a hankali tana tafe sunna magana Sir ya ce" Muneerath yar gata, plz ina son gannin ki yaya za'a yi?"

Muneerath ta yi murmushi ta ce" In ba sir ba yau kwana uku kadai fa da muka rabu, wai ko dai an koreni a aikin ne na ga ba'a kirayeni ba har yanzu"

Daria ta bashi dan haka ya dara yana gyara zamansa a gaban ruwan da ya gama iyo ya ce" Muneerath, kin fi karfin a kore ki a duniyar jirgi"

Muneerath ta yi murmushi itama a hankali ta ce" To ka zo mana"

Ido ya dan zarro yana gyara zamansa a sanyaye ya ce" Ni banma kai cen ba, na gankima ko ta vidio call be ya wadatar, an fada maki shigowa gidan na yiwa kowa sauki ne kamar naki?"

A hankali ta fito ta nufo falon a sanyayenta ta ce" A shigowa nan ne da wahala? Gidan da ko dogarai masu tsaron kofa babu sai wasu dirka dirkan mutane rike da wukar wasa?"

Yar daria ya yi a hankali ya ce" Plz, ki barni na ganki ta vidio call, nine fa freind dinki?"

Ajiyar zuciya ta sauke a hankali ta dago dubanta ta sauke a kan Babar kujerar da ta kyautata zaton akoy mutun a zaune kuma ga dukan alamu ita ya kure da duba domin a jikinta take jin idannuwansa,

Ido cikin ido suka kalli junna na kamar second goma kafin ya cire dubansa daga kanta yana kara hade fuskarsa tamkar zai kurma ihu dan bacin rai

A hankali ta hadiyi yawu kafin ta murguna bakinta itama ta cire dubanta hankali kwonce ta nufi ratsawa dan zuwa saman table ta ci abinci a sanyayenta ta ce" freind, ka bani number oga mana dan Allah, da shi nake kwana nake tashi, a kasan zuciyata yake"

A hankali ta dora kafarta daya ta fara hawa,
Hanja ya dago dubansa daga cirewar da ya yi ya sauke a saman kanta cike da wani mamakin waya take a gabansa bata ajiye ba, bata gaishe shi ba, idonsa idonta sun kalli junna ba bata ganshi ba

Idannuwanta ne suka sauka a kan Tgr dake kwonce a saman matatakalar tana kada wutsiyarta kanta a kwonce ta dan turo kafafuwanta gaba kadan irin dai yannayin da take kasancewa a ciki yawancin lokuta da dama idan tana zaune a kusa da uban gidanta, watau ta fi sakewa ta ringa kai kawo tana kada bindi tana kwonciya tana tashi tana juyi abinta hankali kwonce

Wayar dake hannunta ta saki lokaci daya cikinta da ba komai ya juya a bayane ta furta" Muhamadu rasululahi salalahu alaihi wa salam, innalilahi wa ina ilaihi raj'une wayo na mutu na lalace"

Daidai lokacin kuma tgr ta kula da mutun ce a gabanta
Irin mikewar da ta saba ta yi hakan ya kara fitar da dukan girmanta da takamarta lokaci daya ta girgiza ta girgije ta juyo da nufin nufo Muneerath dan ta sinsinata ta ga ko ta santa ne ? Idan bata santa ba kuma ta dan tsakura a jikin nan nata

Wani ihu Muneerath ta saka ta yi fatali da dan kwalin, da takalman a guje ta juyo wajen da Hanja ta harde kafafuwansa yana kallonsu ita da Tgr yana jira har sai tgr ta dan zagayata kamar sau uku kafin ya dakatar da tgr din domin idan ta gane bata sanka ba far maka take, a gidan ta san kamshin Mah, na Pah, na iman, na dukan wani da ya dace ta sani, sosai ya so ya ga yaya zasu wanye, sai dai bai yi aune ba, bai taba kawowa ransa ba, bai taba hasaso zata iya daga kafarta daga gaban tgr din ba, baima shirya tarbota haka a kwana kusa a jikinsa ba, sai jinta kuka ganninta ya yi ta yi wata uwar sufa ta dane jikinsa tana kwala ihu idannuwanta sun firfito gaba dayan Muneerath dare dare a saman cinyarsa zuwa yanzun ba salati da salalamin take yi ba ihu ne take yi bilhaki ta rike wuyansa da dukan karfinta ta ce" Zaki ne, zaki ne, ka ganshi kuwa zaki ne....." Da wani uban karfi ta kara shigewa jikinsa gaba daya jikinta na wani irin uban bari tamkar zata side a lokacin da ta waiga ta ga Tgr din a jikinta domin tana kasowa da gudun biyota ta yi da wani irin gudu, sannan da ta ga ta dare uabn gidanta gaba daya yannayin masifa ne ya taso mata ta harzuko da niyar dafkarta ta saka shi yin abinda bai shirya ba domin hannunsa ya saka da sauri ya yi mata nunin da yake mata idan yana son hannata aikata wani aikin da baya so hakan ya sa ta ja birki kafin a hankali ta karaso ta shiga sinsinar Muneerath tana shafa kanta a jikin cinyarta da ta bayana dan dirka kokowar da take tana ihun za'a kasheta

Wannan juyowar da Muneerath ta yi ta ga ga kan zakanyar nan ga cinyarta ya sakata nutsa kanta a kirjinsa kafin ta sauke wani dogon numfashin da daga shi ya ji dif gaba daya jikinta ya saki

A hankali ya dago hannunsa da ya masa wani irin mugun nauyi ya nufo shi kusan gashin kanta da ya bazu a jikinsa , lokaci daya kuma jikinsa ya dauki bari hakan ya sa zabure ya.....
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

3 □□□ 9 □□□

Ba san da wani baki zan gode maku ba □□□□□□□□□□, ban cika azarbabin magana ko kurantawa ba, aman wollah idan ina tare da ku ko parrot zai ganni nan ya barni nan

Allah ya saka maku da alkhairi baki dayanku,
Kunna da yaea sosai walahi
Kuma alkhairi ne ya hada mu
Gaisuwa zuwa a gare ku yan uwa al'umar gidan DUTSE, tabas kuna saka ni nishadi duda kasancewata karama a cikin marubuta mai tatata sai kunna sakani jina wata gingirmemiya, ba zan ce komai ba sai fatan alkhairi
Allahu ya datar da mu baki daya

Hakkun *DUTSE AJIYAR ALLAH NE, DUTSE YA GAGARI GARA □□.....DUTSE YAKE SHI HANJA*

Lokaci daya kuma jikinsa ya dauki bari , ya zabura da ita a jikinsa ya mike tsaye da ita din a jikinsa kafin ya juyo wajen kujerar gaba daya hannayensa na masa raea ya shinfideta saman kujerar

A hankaki ya idasa mike tsayinsa tsaye zurbat kafin ya shiga bin hannayensa da suka tada gashin hannu da kallo watau tsigar jikinsa da ta mike gaba daya lokaci daya kuma ya kara sauke dubansa a kanta wace take kwonce rigar nan ta yi sama sosai wajen cinyoyinta a fili haka kuma wajen kafada guda ya yi kasa sosai hakan ya ba dan saman kumburaren mamanta ya dan bayana kadan

Gashin kanta da ya yi lumbuk ya kuma tsura mata ido yana kallo da gashin girarta har zuwa wajen kanta

A hankali ya waiga ya kuma waigowa gannin ba kowaa falon ashe sai shi kadai, gaba daya tunda ya fitar da tgr Mah ta gudu, dama iman idan yana zaune ba wajen take zuwa ba hakama masu aiki kowane yana wajensa a labe ba wanda ke dan kai kawo koda dan su yi kakabe kakabe ne

Ajiyar zuciya ya sauke a hankali yake dan baya baya Tgr kuwa na kusa da Muneerath din tana kara sinsinarta

Wajen wayar tafi da gidanka ya je yana dan murza gaban goshinsa ya daga a hankali ya dora number bangaren Mah

Dagawa ta yi tana salama aman kuma ya kasa buda bakinsa ya bata amsa hakan ya sa take ta hello? Hello? Aman shiru ba amsa ba alamun za'a amsa

Ajiyar zuciyar da yake saukewa idannuwansa rintse yana son yin magana ya kasa ne ya saka Mah jin gabanta ya fadi

A tsorace ta kalli wayar , abu daya ya fara diro mata a rai shine bashi da lafia, gashi kuma zaune kusa da zakin nan .....gabanta ne ya kara tsinkewa ya fadi da gudu gudu sauri sauri ta warci wayarta ta yi kiran dakin s curit dinsu tana fadin" Maza maza a leko wajen da prnc yake me yake yi?" Domin gaba daya wani banzan tunani ne ya darsun mata kar a je tgr din ta haukace ta cinye mata d'a

Da wani gudu ta idasa shiga cikin accenseur din ta dana ta lumshe idannuwanta tana ta adu'a a kasan zuciyarta jikinta kuwa na bari

Daidai ta bude ta sako kanta cike da tsoron halin da zata tarda yaron nata, kwata kwata ta kawar da tsoron tgr din zata shigo wajen ne ko wace wace ta dano kai da dan sauri tana karasawa falon

Shi ta fara ganni a zaune dangalgal saman cafet din falon, kafarsa daya a mike dayar a tankwashe, tgr a jikinsa ya rungumeta yana shafa gashinta yana kuma kallon Mah da ta taho

Ja Mah ta yi ta tsaya tana kallonsa,a sanyaye ta ce" Khalb, me yake faruwa ne?"

Idannuwansa da sukai masa mugun ja ya rintse a hankali kafin ya bude ya juyar da dubansa ya dora kan Muneerath dake kwonce

Itama duban nata ta kai wajen, lokaci daya kuma ta zabura tana salalami ta karasa da mugun sauri tana kokarin dago Muneerath tana fadin" Me ya sameta? Meye meye haka? Bata motsi fa innalilahi wa ina ilaihi raj'une, son kama min"

A hankali ya girgiza kansa daidai mutanen cen sunna neman izinin shigowa

Da gudu gudu suka shigo sun kai soja goma aman da shiga ta suit a jikinsa kowane kuma da dan abin kunne a sakale a kunnensa haka kuma da bindigoginsu , kosasu ne, masu tsafta ne, dakarun Hanja kennan

Du tsayawa suka yi daga nesa sunna masu tambayar halin da ake ciki me yake faruwa

Mah da sauri ta dago ta ce" Ku kira min likita bata da lafia ne "

Da sauri babansu ya basu umarnin du su fice kafin ya yi gagawar tabo lititan gidan

Kafin kace meye wannan har sun karasa shigowa

Sunna idasa shigowa su dukansu fara ja suka yi suka tsaya domin da Hanja suka fara yin tozali kafin ifannuwansu ya sauka a kan Tgr dinsu

Gaisuwa suke kai masa a ladafce domin kuea kaf dinsu basu da karfin kokowa da yannayinsa sai dai su ja su dan tsaya

A hankali ya sauke dubansa a saman kansu kafin ya dauke kansa daga kansu ya kuma maidawa wajen Mah dinsa
A kasan zuciyarsa ya rasa tunanin meyake yi?? Meye ya tsayar da maganarsa me ya hanna harshensa sarafuwa ne? Me ya hanna masa kalaman da zai fada ne? Ta yaya zai iya buda bakinsa ya nunawa Mah irin bacin ran da yake ciki, ta yaya zai fada

mata yarinyar nan a dumbin tarin raahin kunyarta itace yau harda hawan masa jiki dan kawai Tgr ta nufota? Ba zai dauki komai ba, bama zai gane komai ba,

Rai bace ya cire dubansa a karro na ba adadi yana kara rike Tgr dake jikinsa tana hawansa sai dai bata nufi kowa ba dan tunda ya mata hannin nan ta hannun kennan fa

Likitan ne.....
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 0 □□□

Likita ne namiji docter ne da yake ja gaban likitocin palace din,
Da sauri mutun uku ke biye da shi dadauke da yan abubuwan kawo agaji na kusa kusa

Sai da chef din s □ curit □ din nan ya caje su kafin su karasa wajen da Mah ke zaune rungume da Muneerath hankalinta tashe tana dan share hawaye gefe da gefen idannuwanta

Dayar ce ra kama Mah dan ta taimaka mata ta dan matsa su duba Muneerath din

Kwontar da ita suka yi saman kujerar suka aaunata
Da sauri ya bukaci da a kawo masa oxyg □ ne domin ifan mutun ya suma wannan shine dama mafi sauki da ake yiwa mutun dan ya dawo da hankalinsa idan bai samu numfashi bane ake zuwa ga allurar karin ruwa wace ke dawo da mutun ana kiran da abubuwan nan R □ animation, idan ya ja dama ne ake kara daukaka bincike dan gannin abinda ya hannaka dawowa a hayacinka

Wannan karonma basu dauki lokaci sosai ba sai gasu nan tafe da dukan abubuwan da ya bukata

Mah na zaune gefen HANJA ko nace dan face da shi tana kallonsa

Gaba daya a zaunen nan da yake zakin nan a jikinsa yake , kansa a saman kirjinsa, shi kuwa yana shafa bayansa ne aman kuma tsuru idannuwansa a wajen inda likitocin nan suke tsaye cikin nutsuwa sunna aikinsu, a hankali ta maida dubanta wajen likitocin ta ga irin yadda dukansu babu mai kwakwaran motsi sai da dalili du kuwa dan yana wajen ne kafin ta kara maido dubanta kansa a hankali ta sauke ajiyar zuciya tana kara kureshi da duba dan burinta so take ta karanci abinda ya samu yarinyar nan dan ta kula dikim din ya tashi

Irin yadda mutun ke farkawa a tsorace yawancin lokutan summa hakan ne ta faru da Muneerath wace dama a tsoracen ta summa sai kawai ta dawo a firgice bayan ta kwala ihu ta nemi rarumar wanda a tunaninta har yanzun a jikinsa take hakan ya sa da sauti likitan nan ya kama damatsunnan hannayenta cikin yaren turanci da rarashi ana taimaka masa dan kar ta cire abin numfashin da aka saka mata ya kara kusanta jikinsa da nata sosai a cikin aikinsa ba da wani abin ba yana kara dan matsar da ita kan kujerar yana fadin" Shuiiiiiiiiit, is ok, ya isa haka ba wani abin da zai kama ki, ki nutsu kar ki cire abin hancinki"

A hankali ya bi hannayen likitan da cinyoyinsa dake kusa gak da gak da nata,
Idannuwansa ya yi gagawar rintsewa jin irin dukan da zuciyarsa ta masa da bai san ko na wani daukar maganar bane

Cire dubansa ya yi daga bangarensu ya juyo kann Mah dinsa
Idannuwanssa ya lumshe a lokacin da suka yi ido hudu da Mah wace ta wara nata duban tana kallon yadda idannuwansa ke nuni da ransa a matukar bace yake

A hankali ya mike tsaye daga zaunen da yake hakan ya sa Tgr ta ringa zagayarsa tana kada bindinta hankalinta kwonce domin ita kam nata bukatar a cike yake tunda gata ga uban gidanta

Wajen agogo ya kai dubansa kafin ya juyo yana kallon Mah a hankali kuma ya juya ya nufi bangarensa inda Tgr ke biye da shi yana tafe a hankali kamar yadda jiya ya fita a hankali jikinsa tamkar ba lakkah ko daya

Da ido ta idasa raka shi kafin ta sauke ajiyar zuciya ta koma kusa da Muneerath sosai tana kallonta ta rike hannunta tana shafa gashin kanta a hankali ta ce" Ki yi hakuri yar albarkana, ki daina zaburar nan"

Muneerath ta lumshe idannuwanta tana kallon Mah kasa kasa muryarta ta ce" Mah?, Zaki ne ya biyo ni"

Mah ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Ba fa zai cije ki ba, kin ga ai Hanja na nan ba zai bari ya cije ki ba"

Sai a lokacin nan hoton wanda ta rukunkume ya shigo idannuwanta, cike da takaicin kanta ta jimke hannun Mah ta rintse idannuwanta da karfi hankalinta tashe tana jin haushin kanta

Zuwa lokacin ne wayarta ta dauki tsuwa,

Mah ce ta mike ta dauko mata ita cen yashe domin likitocin sun tafi, tana jujuya wayar tana kallon yadda ta ratatake da kyar ta iya daga mata ta saka mata ita a handsfr ta miko mata kafin ta kuma zama a hankali ta dagota tana mata apkin sannu ita kuma sai kara langwabewa take tamkar zata fasa kuka bayan ba abinda take ji a yanzun, da gaske ne a dan rikice take ta ji tsoro dazun sosai aman yanzu da ta ga Mah a kusa da ita sai take jinta cikin nutsuwa dan haka kawai take ji babu abinda zai kuma tabata a gaban Mah ciki harda danta, langwabewar nan kuwa da take gani ta yi kamar da wasa dan bata da lafia ne ake tatarotan nan to ai kuwa Mah ta shiga uku domin ita dai zata yi ta kwonci ne tana zuba iya shege, aman gabanan kafarta kafar Mah dan ta kula dan Nan na Mah bashi da lafia, sam ita ko wa zai ce mata yana da lafia ba zata yarda ba, yaya mutun mai hankali zai yarda ya ringa wasa da ransa? Haba dai walahi ita dai da ranta da hankalinta ba zata yi kawance da zaki ba!

A hankali ta amsa muryarta a sanyaye

Daga dayan bangaren aka shaida mata cewar tana da tashi karfe biyu na dare

Da sauri Mah ta amshi wayar ta datse tana fadin" Ba zaki tafi ba yau kam, ke da baki da lafia?"

Wani irin mikewa Muneerath ta yi tana kallon Mah ta dan girgiza kanta a hankali ta ce" Haba mahna, wollah nu kalau nake kin ga? Kalau nake Mah, zan iya barama na je na dan rintsa kadan kafin karfe goma dan Allah mahna ki tasheni wollah dan suma ne mu a garinmu da za'a maka dukan mutuwa kuma a sakaka aiki ka yin kuwa bale suma a kwonce cikin nutsuwa ? Wama ya san ko Niger zamu sauka na ga Oga? Mah plz ga wayata dan rike min bari na je na huta"

Da gudu ta yi wajen accenceur, Mah ta rakata da kallo baki bude

Dan murmushi ta samu kanta da saki tana girgiza kai da mamakin kokarin Muneerath din, sai ta ajiye haka a matsayin yarinta ne , dan yarinya ce ya sa da ace wata baba ce ta suma yanzu ai ba inda zata iya zuwa, kai bama zata iya aikata komai ba sai dai a ringa mata sannu

Mikewa ta yi a hankali ta kurawa hanyar da zai sadata da bangaren yaronta
So take ta san me ya faru? Yaya aka yi Muneerath ta suma a kan kujerar da yake zaune? Me ya kawota inda yake zaune?
Ba dan komai take son sani ba sai dan tabatar da tsaro a tsakanin yan matan nata da yaron nata, sam bata zarginsa da komai suma haka, aman zata kasance mai taka tsantsan a tsakaninsu dan gudun tasiri irin na shedan ya yi karfi a tsakaninsu

Komawa ta yi wajen accenceur da yar karamar wayarta da kuma ta Muneerath a dayan hannunta ta dana ta yi kiran matar dake kula da Camerar gidan

Cikin nutsuwa ta shaida mata tana son vidion da ya wakana nan da awa biyu, sannan ta nemi da a kawo sabon phone
.....

.....wannan kennan.....

Ruwa ke zuba a jikinsa, idannuwansa a bude suke ruwan na ratsa masa idannuwan aman baya rintsewa kuma baya kiftawa har sai ya dauki dan lokaci kafin ya kifta din

A hankali ya karadaga hannunsa dan so yake kwata kwata ya daina yi masa dan barin da yake masa
Gannin ya daina kwata kwata ya jimke hannun nasa ya sada kansa yana hararan jikinsa cike da jin haushin wannan rashin kunyar, mema aka yi da har zai nuna kansa?

Gannin zai bata lokaci sosai gashi zasu yi tafiar kwana biyu cif ya saka shi daura alwallah ya fice a bayin

Sallah ya fara gabatarwa ta la'asar a dakinsa domin lokaci ya shige bai yi ba kafin yake karasawa wajen kayansa da yar wayarsa a hannunsa ya rubuta message ya tura a VIP na matan da yake dauka ya tura

Tsai ya yi da ifannuwansa yana tuna magangannunta

A hankali ya lumshe idannuwansa yana jin kansa ya fara daukan zafi....."BAKA JIN KUNYAR MAHALINCINKA? KA YI AURE, KA YI AURE" maganar da mah taje yawaita fada masa

"IDA AKA CE DA KAI MEYE HUJARKA ME ZAKA GABATAR? RASHIN MUHALIN AJIYEWA NE, RASHIN KUDIN SADAKI NE? KO RASHIN LOKACIN BATA NE? KA JI TSORON ALLAH KA YI AURE".....

Idonsa rintse ya daki madubin jikin wrdrb din da karfin da ya saka madubin zubowa gaba dayansa kasa
Bai kula da hannunsa ba ya dauki wayar a takaice ya rubuta sako kamar haka "A BARI!" Ya tura kafin ya juya a hankali ya nufi wajen bed dinsa
Kwata kwatama sai ya fasa tafiar ya nemi wajen kwonciya inda tgr ta haye saman itama tana gyarawa ta kwonta kusa da kafafuwansa ya yi adu'a ya fara neman barci karfi da yaji cike dajin haushin abinda shi kansa bai san dalili ba.....ya fi ajiye hakan a gurbin rainin da wannan yar african ta masa, ta rasa wajen hawa sai jikinsa ? Ta rasa wa zara ringa cirewa kai sai shi? Lalema!

Dukan abinda ya dace a yi an yi sun kama hanya tafia ta cikin dare ce wace bata da nisa sosai domin duka duka awa hudu ce ta sauke su a kasar da zasu je

Wannan karronma dakunnansu suka shige suke hutar da gajiyarsu , sun samu isashen barci domin a garin ne zasu yi kwana har biyu kafin su juya dan akiy jirgin da zai duba wanda ya kakare a cikin garin ya ki tashi yana kampanin gyaransa , kasancewar jirgi ne da kampaninsu ya kera sai aka nemi da ya zo ya ga meye matsalar idan ba sai an kai jirgin Ingila ba sai kawai a fadi matsalar a kawo kayan gyaransa, idan kuwa sai an kai shi dole a ga ta wace hanya ya dace a kai shin

Shi dinma wani barcin ya nema dan zuciyarsa a cinkushe take duda ya samu sun yi hira da Mah ta masu rakiya da wannan bakar har a roport dan ta ga yaya jikin

yarinyar yake wai ita bata yarda ta yi tafia bata da lafia ba kamar wata yar goye har sai da ta ga tana tsalanta ta bi yan matan da zasu je tare hankali kwonce kafin tabara masa amanarta ta koma gida, aman haka kawai ransa ke bace har yanzu

Ya sha barcinsa sosai, ko da ya farkama sai ya zame dakin motsa jiki dan kuwa sanyin safia ne

Sai da ya gama motsa jikinsa kafin ya dawo dakinsa

Zuwa wannan lokacin mararsa ta masa wani irin nauyi sosai, hakama jikinsa du a mace yake, babar bukatarsa ya sauke jarabar dake tare da shi

Wani wankan ya sake sai ya dauki tufafinsa ya saka, watau jalabiya fara kal sannan ya dauki hirami ya dora a kansa domin kasa ce ta larabawa duda ba kowa ke irin shigar hakan ba, aman du wani musulmi shigarsa kennan, shi kuwa dama yana son shigar nan ba wai baya sonta ba

Caf□t□ria ya nufa da kansa dan so yake ya je ya hada hadin lemun tsami ya sha ko zai dan samu rlif, idan kuwa ba hali to ya sada kansa da asibiti ya amshi na hadiya dan kuea ya rantse bafa zai yi ba wannan karron , to yama ce wa ya motsa shi? Aikin banza aikin wofi kawai!

A lokacin da ya tura gilas din wajrn ya sanyo kansa, kamshi ne irin na kalolin abinci duda ba a nan bude ake dafawa ba aman kasancewar waje ne mai daukan jama'a koda yaushe, wasun har an kawo masu nasu abincin shi yasa dakin cin abincin baya rabo da dan kanshin abinci duda ana yawan kula da hakan
Sai sanyin Ac karara da ya dake shi, sai ko idannuwansa da suka sauka a kan mutanen dake ciji yawanci table mai dauke da mutun biyu ne, sai mai dauke da mutun daya, sai daidaiku masu dauke da mutane kamar uku, ko hudu haka irin dai abokai sun zo, ko familly haka

Komai na wajen kalar fari kal ne, da idonka zaka ha tsafta ke jan ragamar wahen hakan ya sa bai juya ba ya dan fara tafia a hankali har ya karasa wajen zaman mutun daya ya tsaya yana kallon kujerar kafin ya ja a hankali yana mai yin bisimillah ya zauna saman kujerar

A hankali idannuwansa suka dago dan son gannin wa'inda ke gabansann nann da yake jin sunna ta kyakyata daria sunna hira kamar su kadai ne a wajen,gashi kuma muryar mata biyu ne da namiji guda

Gabansa ne ya kwonci kwonci ya fadi a lokacin da ya yi arba da Muneerath d take facing dinsa, sanye da bak'ar Abaya ta yane kanta da bakin dan kwali, ta saka dan kwalinta sai ko dan lip a bakinta tana kallon namijin da bai san ko waye ba sai bayansa ne kawai ya gani yana maganar da ta saka wace ke kusa da namijin bushewa da daria ita kuma tana sanye da wando da riga wace sam bai gane cewar a cikin Hostess din take ba

Lokaci daya ya ringa jin tamkar mai ciwon huka wani abu na masa yawo a gaban kirjinsa, idannuwansa na yin wani farfarfar kamar sunna son kaishi duniyar summa

Ransa ne ya ji yana tafasa a lokacin da ya tuna cewar Mah fa amanar yarinyar nan ta bashi shine dan ta raina mutane daga saukarta a garin da ba nata ba ta dage take irin wannan abin da kartin maza? Ina wannan ba irin rikon Mah dinsa bace, ta kuwa

san wacece Mah? Yarinyar nan ta san wani irin tarbiya Mah ke badawa? Dama shi ya san yarinyar nan munafurcin dake tare da ita ya fi zama saliharta yawa, gatanan dai gaban kato tana ta sakin murmushi to me take nufi ne? Me take nufi ne?
Sunnan gidansu zata bata bayan da sunnaN Pah a saman takardarta ta aiki hakan ya sa aka sakata a dukan tafiar da shi zai yi?

Kansa ya cire daga kansu a hankali yana sauraron ma'aikaciyar wajen tana tambayar command dinsa

Wani balarabe da yake ta kallonsa dan yana son gabe wai shine ko ba shi bane ya taso ya karaso a nutse ya yi masa salama tare da miko masa hannu a bayane ya ce" Prince tun dazu nake son gane wai prince HANJA ne a wajen nan ko ba kai bane, ashe kai din ne?"

Da sauri Hanja ke dan masa alamu na kar ya tona shi dan gudun masu son daukarsa hoto da masu son yi masa magana yana yi yana kara girgiza kansa dan ya gane , sai dai ya makaro, domin mutanen da yake kallo da mamakin su waye tare da ita sune suka fara juyowa cikinsu na juyawa a hautsine balema Sir da bai ga shigowarsa ba ya shagala da kallon halitar da yake bege ba dare ba rana yana shan dariyar hirarsu shima yana basu daria ya ji cewar uban gidansa ne a wajen
Sai ko Muneerath dake zaunenta aman itama dubanta ya kai inda yake zaune
Kafin kace menene wannan kamar yadda a kasasen waje kasasen turawa da larabawa ake yiwa manyan cele da kuma manyan masu kudi, balema masu mulki ko sarakai taruwa a kai idan aka gansy a wajen public ba dan a masu maula ba sai kawai dan a samu saka hannunsu ko a samu hoto da su, idanma aka yi rashin sa'a da yan jarida a kusa yanzun zasu yayameka kuma sai yadda Allah ya yi da kai ne idannuwanta suke kallon abin mamaki gannin nan da nan ana ta son a samu yi masa magana aman Sir da mutumen nan sun hakikance sunna tarewa tare da kakarewa dan shi dai ba yawo yake da gardawansa ba tsere masuma yake dan baya son takurar nan, ya yi fitowar nan ne dan ya samu ya huta shi kadai da ransa

Kai Hanja ya girgiza yana sauke ajiyar zuciya a hankali ya mike yana dan tafia ta inda suke ta kokarin gannin sun kare shi

A hankali take kallon yadda yake matsowa inda take zaunenta ita daya abinta bata tashi ba, haka kawai ta ji gaba daya yana neman cika mata ido dubansa na neman gagararta domin idannuwanta ne ta ji sun fara rawa rawa take jin kamar ya fi karfin kallonta kai tsaye

A hankali ta cire dubanta a kansa, sai dai bata sada kan ba sai ta mayar da duban nata gefe

A yan sekwani ta ji lalausan hannu fari kal mai dauke da birda birdan jijiyar da bata san haka hannun yake ko yanzu ne suka tashi ba sannan wanda ya fi girman nata nesa ba kusa ba ta ji ya kama tsintsiyar hannunta ya.....
11/14/21, 12:51 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 1 □□□

Hannun nata ya warta a lokacin da ta afka a duniyar tunani ba tare da ta ankara ba ya damka ya kuma mikar da ita

Ido ta kwalalo domin da dayan hannunsa ya saka a wajen kugunta ya karra mikar da ita sosai ya matso da ita dan daf da shi kafin kansa a gefe ya shiga tafia da ita da dan hanzarin da ya saka ta saka katabus sai tafiar da yake yi kawai da ita har ya fice a cafetariar baki daya kafin ya bude motar da ya zo da ita ya turata ya zagaya da dan sauri ya bude ya shiga ya tayar ya harba kan titi

Idannuwanta a waje suke, gana daya numfashinta sama yake yana kasa da wani irin sauri tana wuki wuki sannan ta kasa zama waje daya sai ta yi kamar zata kama ta bude sai kuma ta ji hannayen nata sun kwashi wani irin bari tamkar ba zasu iya dannawa su bude mata ba

Haka tana ji tana ganni ana watsa masu hotunna Sir na tsate yana binta da kallo hakama Kawarta Hanja ya ja motar nan ya yi gaba fa ita

Wani masaukin ya nufa da ita, wanda yana tsayawa ya bude motar stil bai tsaya ya yi jiran ta fito ba ya kuma damko hannunta ya nufi ciki da ita

Wajen dauke yake da dan fili daya kwal zagaye da gilas da alamu shine zagayen gidan wanda baya hanna a ga mutun dan yana ciki haka kuma wajen kamar shi kadai ne kwalin kwal a ajiye

Ciki ya nufa da ita ya saka hannunsa ya danna cod din wajen kafin ta tura ya bude ya shige da dan sauri da hannunta wanda take ji zuwa yanzu tana ga ta karye nema

Da dan karfi ya hankadota da hannun nata da ya riko, hakan ya da ta yi gaba tagal tagal ta je ta kifu a kan kujerar dake falon kafin ta dago a firgice tana kallon irin hararan da yake binta da shi

Makwar ta hadiye yawun wahala tana jin kamar zata hira ta gudu dan tsoro ne fal a kasan zuciyarta na yannayin wannan mutun

Kai kawo Hanja yake da wayar a hannunsa android yana ta tunanin yadda zai yi da ita

A hargitse ya juyo kanta a lokacin ne kuma kira da message kala daban daban ke shigoea wayarsa

Kiran ya fara dagawa domin na lauyan gidansu ne

Shiru kawai ya yi yana sauraron abinda lauyan ke fadi cewar ya ga hotonsa yanzu yanzu an dora da wata wai matarsa ko budurwarsa duniya na son karin bayani, shi da baya yarda a dora hotonsa irin haka da mata menene kuma ya hada shi da aikata hakakodai budurwar tasa ce da gaske?

Hannunsa ya daga ya kai wajen goshinsa ya dafe cike da takaici ya ce" AA "

Lauyan nasa ya ce" Ok ina zuwa bara na dakilar da yade yaden sannan na ba yan jarida amsa, domin sunna ta tambaya ne dama kana fita waje ne ka yi yawo da mace a sake baka yi a kasarka? "

Kit Hanja ya fara kashewa da sauri ya shiga yanar gizo dan tabatarwa kansa

Hotunna kaloli ne aka yayada a wannan dan mintunnan har ya zaga ya kai wajen manyansa
A hotunnan wa'inda suka fi bashi haushi sai wa'inda aka nuno karara ya riko kugunta da kuma dayan hannunta kam sannan ya janyota jikinsa sosai kafin ya fara tafia da ita

Tabas du wanda bai san ba wani abu tsakaninsa da wannan yarinyar ba dile zai ce wata dinsa ce

Da takaici ya ajiye hoton a gabanta ya zauna ya rafka tagumi yana kallon yadda take binsa da kallo a zaune dangalgal kafafuwanta a hade waje daya gaba daya jikinta na bari bari tana kallonsa a mugun tsorace, gashin kanta a fili dan dan kwalin ya zame, zufa ta jika gaban goshinta hakan ya sa gashin nata ya liliku a gaban ganta , sai idannuwanta dake yawo a fuskarsa da dakin , wannan kwayar idon ta kara girma tana ta yawo a jikinsa

Hannayensa biyu ya rafka tagumin da su a lokacin da shi kansa bai san tagumin ya yi ba yana binta da kallon haushi da tunanin yaya zai yi da ita

Ransa bace, sai dai muryarsa da sanyi ya ce"me ya kawo ki rayuwata? Wani ya aiko ki ne ki hada min ciwon kai?"

Muneerath ta yi gagawar girgiza kanta tana kallonsa ta hade hannayenta ta ce" Walahi ka ji na rantse maka ni ba wanda ya turo ni, ka manta kaine da kanka ka dauko ni a garinmu?"

Hanja sai kawai yake bin yannayin da take maganar da kallo
Lebensa na kasa ya cije da tarin haushi ya ce" Dubi haukan da ake dorawa wai ni Hanja wai ke budurwata ce ko matata? Sai nake ji kamar na yankaki na birne a wajen nan na huta"

Jikin Muneerath ne ya kuma daukan bari da sauri ta dauki wayar tana dubawa kafin ta ahiga girgiza kai ta kuma hade hannayenta ta ce" Kayya, kayya, aman wanda ya yi wannan munafuki ne kuma ba zan yafe masa ba koda kabarinsa zai kama da wuta balbal, dan Allah kai ai ka san ba wannan tsakanina da kai, maganama ni da bana maka tun ranar da ka shakeni ina zaman zamana? Ka min rai kar ka kasheni Oga bai ganni ba, ka yafe min wannan gangancin da aka ce wai ni din nan budurwarka, ka ga fa da saurayina walahi nima ba zan taba yarda da wannan maganar ba wa'indama suka dora basu da hankali ne, aman dan Allah kar ka yi maganar kasheni

a kasar nan ka maida ni kasarmu na tarda iyayena na rayu da su, ko yau na bar aikin Hostess na ci riba domin zan fada cewar aikin nan na taba dandanawa "

Tana magana ne tana dan kusanto shi da daga yan yatsotsinta masu dauke da faratuna farare tas ba digon abinda yan matan kasarsu ke sakawa farce musulman da kafuran, hakama hannun nata baya dauke da dogayen faratuna, sanann sai ta hade hannayen nata ta kuma rungume a kirjinta
Fuskarta da furucinta gaba daya sai suke masa nuni da yarinyar is innocent, tamkar yarinyar da bata san komai ba

Idasa zama ya yi a saman cafet din wanda shi da kansa bai san ya yi hakan ba

A sanyayen da bai sanuryarsa har ta kai haka sanyi ba ya ce" Kin tabata idan nace zan maida ke kasarki daga nan zaki yarda? Na saka ki a wani jirgi ya kaiki?"

Muneerath ta koma dan nesa da shi ta zauna tana ta ahiyar zuciya a hankali ta gyada kanta kuma tana kallonsa ta ce" Wanda zai tashi idan ya taka biredi ai ya rage, bale har ya samu hawa bene? Walahi ko a yanxu aikina ya tsaya alhmd zan koma na cewa mamanmu mafarkina ya tabata, na samu biyan bukatana, zan cewa kishiyar mamanmu nice na taka kasashe hudu na duniya ina aikin da ya zamo burina, sannan zan nunawa oga da ya ce ya san ni ba mahaukaciya bace kuma yana tunanin idan na yi kokari ina iya zama wani abu a yayansa cewar lale na je na taka jirgi kuma na yi aiki, ka ga sai na dauko takarduna na ci gaba da karatuna a university"

Lebenta da take hadawa tana dan warewa idan tana maganar yake kallo , sannan yana dora kowani furucinta a kan ma'auni yana aunawa

A hankali ya cire dubansa a kanta cike da mamakin kansa

So yake ya hanna kansa ci gaba da yi mata magana dan yana so karfi da yaji ya karyata cewa yana jin dadin yin hira da ita a wannan lokacin harma yana son sannin dukan amsoshin tambayoyinsa dan a ganninsa a kan meye zai ci gaba da magana da parfait inknow haka ba gaira babu dalili, sannan yarinyar da a tunaninsa du dunia babu wanda ya raina shi irinta, yanzu haka ya tabata dan ta ga daga ita sai shi ne yana iya karya mata wuya har take mada magana, da ace a kusa da Mah ne da bai san yaya zasu kwashe ba

A hankaki ya juyo ya ga kamar zata dauke shi da ido, duba ne na tana son karantar a wace suke ciki, zai mata ilan ne ko zai sasauta mata

A hankali ya cire dubansa yana fadin" Ki daina tsareni da ido "

Da sauri ta cire idannuwanta a kansa, a kasan zuciyar Muneerath adu'a take tun karfinta kan Allah ubangiji ya rufa mata asiri ya rabata lafia da mutumen nan, ita dai ta san bata taka masa ba, bata karya masa ba, aman ya tsaneta kamar wace ta masa wani mugun abu,
A hankali ta kara juyowa zata kuma kallonsa ta ga ita yake kallo hakan ya sa gabanta ya fadi ta juyar da kanta

Walahi ba zata taba mantawa da wata bugawa da yayarta ta mata wani lokaci da aljannunta suka tashi, watau tsayuwa ta yi sunna fada sai ta ga ta kureta da kallo ashe ashe abu na kusa tana kyarara ihu sai ta warci Muneerath din ta doka da kas....kafin dai ta ankara ta gudu ta kara balata, wannan shi ya sa a yanzu ta ji gabanta na dukan dari dari

Idannuwansa sun yi ja kamar ba nasa ba, hakan na mata nuni da abin na kusa
Inahu sulaimana wa inahu bismilahi rahamanin rahim, Allahu la'ila ha ilahu, alhayul kyayum.....

"haka mamanki ke cewa baki da hankaki dan kina son zama Hostess?".....maganar da ya ji yana fada kennan, wanda itama ya sakata daina adu'ar da take a kasan zuciyarta da sauri tana kallonsa

Kanta ta sada lokaci daya tana tunano iyayenta

A hankali ta dago tana murmushi ta dan matso kusa da shi sannan ta juya tana kallon inda yake kallo a hankali ta ce" Ko kaine sai kace bani da hankali, ka ga ni ban iya girki ba, ban iya ruwa ba a lokacin, ban iya komai ba fa....bani da hanyar shiga makarantar nan dan kudin da ake biya Oga ba zai biya min ba, a haka kuma nake ikirarin ni Hostess ce"

HANJA ya juyo gaba dayansa wannan karron yana kallonta, a yanzunma a tsanake ya kuma cewa" Yaya aka yi kika samu kanki a ciki?"

Muneerath ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Abinda na fara rikewa shine Allah, na san cewa shi kadai ya isa ya tsaya min, na san da cewa ikonsa na kan kowa, kuma yana iya yi min a lokacin da ban aune ba, shi yada kawai na dukufa ba dare ba rana ina fada masa....Ya Allah ka bani DOGARI sannan ka bani damar zama Hostess"

Dan dakatawa ta yi tana kallonsa kafin ta kara sada kanta tana wasa da hannunta ta dora da fada masa irin yadda aka yi ta koyi ruwa, irin yadda ta fara koyan girki aman kulun abin na gagararta, kamar an kunna redio tas ta kwashe masa yadda ta tsinci kanta a wajen horon Hostess
Ta idasa da dafe habarta tana yarfe hannunta ta ce" Wannan labari nawa akoy abin mamaki ko baka gane ba kai?"

HANJA bai taba gannin mutumen da yake hira a sake a gabansa irin yarinyar nan ba , ciki kuwa harda Mah dinsa, domin Mah tana magana da shi ne da sigar rarashi da yannayi na son ta lalaba shi, aman yarinyar nan hira ne take da shi kamar na sako da sako, kanta tsaye hankalinta kwonce ta gama bashi labari da sunnayen mutane kala daban daban da a ciki bai san meye Oga, meye hajia baba watau hostess dinsu baba, sunnaye dai kala daban daban da ta ambata da hausa ba da turanci ba ta krashe da koda labarinta irin abin dai a ranta yake
Sannan bai taba gannin yarinyar dake magana zuuuuuuuuuuuuuuu kamar wata redio abinta daki daki har sai a ta dasa aya ba sai wannan yarinyar

Kansa ya cire a kanta a hankali yana jin kamar zai saki murmushi a bayane sai dai ya hanna kansa hakan

Muneerath ta kuma rafka tagumi ta ce" Yanzu ko yaya makomata take? A islamiya ake cewa karmace ta yarda da namiji ya zo mata idan ba mijinta ba, idan ta yarda da haka har namiji ya tabata to fa ta aikata zina..... hakama Mah ke cewa namiji na taba mu muna iya daukan ciki,shikenan mutuncinmu ya zube idan har muka yi wasa da suturarmu.....Dan girman Allah yanzun hannuna ka riko ka kuma riken jikina fa?

Da wani irin mamaki yake kallonta, kai shi kwata kwatama sai ya ji ya rasa me zai yi tunani da yarinyar nan, gashi dai yanzu sunna maganar fahimta kuma tana son fara

sako masa rainin wayon, ko me yasa take irin haka? Ko a tunaninta shi HANJA zai iya wata mu'amala da ita ne?
Bata san cewa a cikin tsarinsa shi yana da haram bane? Bata san cewa baya zuwarma macen da bata fito ta nuna sana'arta bane? Bayan wannan bata san cewa baya haikewa yan shila bane? Dan tana ganninta bukekiya ai girman jiki ne ko a tunaninta shi zai iya wani abu da abinda bai nuna ba?

Kansa ta cire yana dan girgizawa kafin ya mike tsaye ya ce" Kin ga magana nake so na maki ina so ki fahimce ni kin gane?"

Muneerath ta yi gagawar gyada kanta tana binsa da kallo, willah kamar wani balarabe Allah, kawai shi kuma haka farinsa yake fas? Kamar mai shafe shafe ita mamakin laushin fatarsa take, yanzun dai dan tana tsoron a wajen nan ya hada mata jinni da kwakwaluwa ya sa bata kireshi da sunnan da ya dace da shi ba, kai tsaye ya ringa tabata dan yana dan.....

"kin ga, a gabanki ta ce wai ga amana nan na rike mata yarta, ban san yaushe ta min kishiya take kiranki kai tsaye yarta ba, abinda na sani ita din mutun ce mai kafa kafa da mutuncinta, kin ga idan halinki ne kuka kowani namiji ki bari idan kika fita daga gaban Mah sai ki dora daga inda kika tsaya, aman a yanzun ki kula, ki kiyaye, ki ajiye komai ki yi hakuri da komai, Bani da damuwa da MU'AMALARKI da MAZA, domin ba hurumina bane, aman inada da damuwa da damuwar mamana.....Shin zaki kiyaye harkar maza a zamantakewarki a kusa da ita kafin ta bani damar na mayar da ke gaban iyayenki?". Ya fada da yannayi na serius, ya fada yana kallonta tare da tsatsareta da idannuwansa yana jiran amsarta a kusa dan ya kara gaba

Cike da mamaki Muneerath da ta fara jin haushin maganarsa tana tunanin to a mema ya dauketa ne kwata kwata tunanin kar ya ilatata ya shige mata ta turo baki ta dan saki harare ta ce" To tsakani da Allah a mema ka dauke ni? Hala ni yar iska ce? Inace kai ka rike min hannu da nan dina kau?".....ta karashe tana mai nuna kugunta cike da jin haushin furucinsa

"Ikon Allah" shine abinda ya kubce daga bakinsa yana kallonta

Fara tatare naman gaban goshinsa ya yi yana hada rai dan fa ya kuka yar nan ba'a zaman kalau da ita sai ana rashin mutunci da ita, yanzun ko dan wannan dogon sharhin da ya mata ba dan yana tsoronta ba ai ya ci ta masa biyaya, maimakun ta amsa shi sai ta shiga fadin wannan kalma tata ta rainin wayo?

Wata tsawa ce ya sakar mata wace ta sakata zabura tana kiki fiki da ido tana kallon ,yama karra hade fuska ya ce"

(*AKOY SU, WALAHI AKOY SU, YAN MATAN DA SUKE TAFIA ISLAMIYAR SUKE KUMA TAFIA BOKO DIN AMAN BASU SAN AINAHIN ME HAKAN YAKE NUFI BA KUMA BASU GANE MEYE AINAHIN MANUFAR ABIN BA, A WAJEN MUTANEN DA YA DACE TA SANI SUNE KAWAYENTA, IRIN KAWAYEN NAN NA ZAMANI MASU ABIN TSORO WA'INDA IDANNUWANSU KE BUDE TARRR SUN SAN KOMAI, TO IDAN NATA KAWARMA NA HAKAN TA SANI BA SAI A KARE A TUTAR BABU, YA KASANCE A ANGUWA TAKAN JI AN CE WANCE TA YI CIKIN SHEGE, WAYE YA YI MATA? WANE NE YA LALATA TA.....IDAN BA HADUWA TA YI DA LALATACIYAR

DA TA FEDEMATA BIRI DA ABAWA CEWAR GA NUFIN LALATAR BA ZATA GANE BA, ABINDA DAI ZATA GINU A KANSA SHINE TSORON KAR A MATA CIKIN SHEGEN, SAI NA GABA TANA IYA KASANCEWA IRIN HALITUN NAN DA U MAGANA IDAN BA KARARA AKA FITO MASU DA ITA BA, BA GANEWA SUKE YI BA SHI YASA TAKE TAFE A BAIBAI KUMA KOMA ME AKA CE MATA TAKR YARDA, IDAN KUN KULA TANA RAYUWA NE A TSAKANIN GIDA BIYU, GIDAN SU KAWARTA DA TAKE MANGARIN RAYUWARSU HAR TAKE FATAN ITAMA TA ZAMA IRIN HAKA BALEMA IDAN SUNNA MAGANA DA ITA DA KAWAR TATA TANA FADA MATA MAMANTA TA HANNA SU ZAGI A GIDANSU, SAI ABIN YANA BATA MAMAKI DUBA DA NASU GIDAN ASHAR BA KOMAI BANE! SAI UWA UBA KARIYA IRIN TA UBANGIJI, ALLAH SHI KE KAREWA .....SAI KA RAYU A ANGUWA TA BADALA AMAN IDAN ALLAH YA TSAREKA BA ABINDA ZAI FARU DA KAI HAR KA YI KA GAMA RAYUWARKA A TARE DA SU.....abinda baya kasancewa cen dama ba kasamracen bane watau baya cikin rubutacen al'amari*)
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 2 □□□

Sorry ba eddtng

Ya hade fuska ya ce" Look, abinda nake so da ke daga nan har mu koma kar na kuma gannin shirmen biye biyen nan! Wannan din Umarni ne na baki ba shawara ba, idan kuma kika ki bi zan bi da ke !"

Yana gama fada ya kama hanya ya dadana numbobi a wajen wani allon waya kamar lap sannan kofar ta bude ya wuce ya fita kwata kwata a dakin

Da gudu Muneerath ta mike dan bin bayansa sai dai gannin ya rufo kuma ya yi cikin motarsa ya sakata fara yin dan baya baya kafin ta hantsila gaba dayanta

Ihu ta saka mai hade da kuka tana rinrintse ido dan du a tunaninta wani abu ne ya fito zai kamata

A haukace ta buda idannuwanta a rikice tana ta waiwaiga cikin dakin idannuwanta suka sauka a kan wani makeken zaki kansa na kallon sama kadan kamar yanna son kallon jaririn zakin dake saman wuyansa

Zakin irin na felush ne, an mahaukacin bata lokaci dan yinsa kama daga kalarsa har gashin jijinsa da irin tsayuwarsa da komai

A guje ta yi bayan kujerar dake falon ta tsuguna tana mai saka hannayenta ta toshe bakinta danma kar ya jita ya halakata , lokaci daya kuma cikin nata na juyawa dan azabar tsoro

Gaba daya gumi take, haka kuma jikinta rawa yake, ta daina ihun kukan sai zuru zuru da take da kwayar idannuwanta masu shegen kyau cike da ruwan hawayen dake sauka a saman hannayenta da ta rufe bakin nata da shi

Shikennan, shikenan, tata ta kare, dama wannan mutumen dake biye fa rayuwarta shine ajalinta domin du hafuwarsu da harare suke rabuwa ita da shi
Gaba daya ta gama hautsinewa , ta kuma dauki lokaci mai tsayi ba tare da ta dani ba, kwakwaran motsi ta kasa yi haka kuma gwuiwoyinta sun sage sun yi tsami ,
Zuwa yanzu kanta a hade yake da bayan kujerar tana ta sauke ajiyar zuciya mai zafi baki daya ta gama sarewa ta saka a kasan zuciyarta cewa jira zakin nan yake ta yi wani motsi ya ankara da ita ya cinyeta hakan ya sa baiwar Allah ko cikinta ya yi irin murdawar nan sai ta rintse ido dan kar kukansa ya ankarar da zakin cewa da mutun

A haukace ta juyo jin an taba kafadarta, a zabure da niyar kwala ihu da wani kukan har kamar zata sike, sai dai mikewar da ta yi tsaye idannuwanta suka sauka a kan fuskarsa yana kallonta cike da mamakin yannayinta

A haukace ta fada kirjinsa tana mai fashewa da kuka jikinta kuma na rawa, rukunkumeshi ta yi tana jan numfashi da kyar hakan ya sa gaba daya ya yi kasakai cike da mamakin yannayinta a hankali ya shiga fadin" Hey, menene haka? Meye? Me kika gani haka?". Domin ba zai manta a jiya ne ta sume masa a kirji bayan ta masa irin rikon nan dan kawai ta ga tgr

Muryarta cen ciki tana kukan ta shiga fadin" Zaki ne, zaki ne, shine ka kawo ni wajen zaki? Dan Allah me yasa kake son kashe ni? Me na maka? Inace yanzu muka shirya? Dan Allah ka daina hadani da zaki haka ka ji?"

A hankali ya dan juya da ita gefen da felush din nan take a hankali ya kurawa Felush din ido yana jin wani abu daba dangane da felush din wanda ya kasa bambance tausayinta ne na ta tsorata da tgr ya sa ta ji tsoron wannan abin ko menene?

A hankali ya shiga tafisa da ita inda ta kara rukunkumeshi tana girgiza kai hawayenta bai tsaya ba har idannuwanta na mata zafi ga muryarta har neman disashewa take tsabar ihun da take ta ce" Kar ka kaini mana, kai kuwa kar ka kaini dan Allah, ka min rai kar ka kaini na tuba "

Saman kujerar nan ya fara zama kafin ya rintse idannuwansa sakamakon irin yadda ta biyo shi gaba dayanta idannuwanta rintse ga gumi na karra tsatsafo mata du da irin sanyin garin domin ko AC babu a wannan wahe dan gari ne mai sanyin gaske wanda idan ka fito daga kasa mai rana zaka wahala sosai da saka kayan sanyi domin har kankara ke zuba watau neige a garin, gashi bata da rana hakan ya sa a kasar suke fama da saka kayan sanyi da kuma anfani da abin dumama dakunnansu idan sunna ciki

A hankali ya dora hannunsa saman kanta ya dan shafa kadan muryarsa cen ciki ya ce" Ki daina kuka da ihu, kaina zai rabe biyu!"

Muneerath ta kara kankame shi ta ce" To to, kukanma sai na daina aman idan ka fitar da ni dan Allah ka fitar da ni ka ji?"

Ajiyar zuciya ya sauke domin a yanzun ba da ihun ta yi maganar ba da rada rada ta yita a saman kirjinsa kafin take barkewa da kuka tana karra rike shi

A hankali ya kuma kallon zakin, walahi so yake ya ce da ita cikin mahaukaciyar tsawar da zata firgitata cewar KE tada ni , ba zaki bane kin wani haye min jikina kin rikeni kina giga min hawaye da majina a jiki!

Aman haka kawai sai ya ringa jin idan ya yi haka zai iya firgitata bayan bata da laifi a tunaninta har yanzun zakin da ya tsoratata ne, sannan haka kaeai yake ji a ransa baya so ta kuma sume masa duda koda sumar ta yi yana iya bata taimakon gagawar da suke koyar da ma'aikatansu saboda halin tafia a cikin jirgi babu abinda ba'a haduwa da shi

A hankali ya ce" To ki daina rike ni mana, kin ce ba kyai taba mutun fa"

Muneerath ta karra rike shi tana girgiza kai tana ta sauke ajiyar zuciya jikinta har ya dauki zafi

Sai da ya ga dama dan kansa kamar an kwato maganar daga bakinsa ya ce" ke Felush ne, bafa mai rai bane"

Dif ta yi na dan sakwani kafi ta dn dago da fuskarta wajen sagensa da tsinin karran hancinsa da jajayen lebunnansa a hankali tana kallonsa tana kuma hangen zara zaran gashin idannuwansa muryarta cikin rada aman dumin furucinta na dukan habarsa hakan ya sa a hankali ya samu kansa da rintse idannuwansa ta ce" Kana nufin wancen abin ba na gaske bane aman har yake da faratunna da fatar kafa irin na mai rai?"

A hankaki ya bude idannuwansa da suke da yannayi irin nasu yannayi kamar mai dan kurba eh yane ya dan duko da duban nasa a saman fuskarta hakan ya sa lebunnansa suka dan zarto kusa da hancinta, hancinsa na gugan gashin idannuwanta idannuwansa na kallon goshinta ya yi mata shiru ba tare da ya bata amsa ba kawai ya kura mata ido irin kallon nan na rashin kunya wanda ka ga ana kallon kana kallon mutun aman ba zaka daina kallon nasa ba dan ba tsoronsa kake ji ba

Hancinta dake shakar kamshinsa ya fara ankarar da ita irin zaman da ta yi dare dare a saman kan kato ta hanyar shaka mata kanshin jikinsa sosai a jikinta har ya kasance kwakwaluwarta a yanzun ta faa kai mata sakon halin da take ciki

Wani irin hantsilawa ta yi baya jikinta na rawa tana zarro ido ta mike tsaye da sauri tana kallonsa cike da mamaki da tsoron abinda ta aikaa wanda a yanzun ta gama gane ita Muneerath yar oga itace ta ara rungume jikin kato
Da sauri ta dora hannunta na dama a saman bakinta ta zarro ido kafin ta saki hannun nata ta tafa tana girgiza kai a hankali ta ce" Ashe nima yar iska ce? Yanzun shikenan nice na yi wannan abin shi kuma ya kyale ni har ya zauna da ni a samansa? Yanzun wannan gabjejen katon sau hudu kennan yana zuwar min? Innalilahi wa ilaihi raj'une"

A hankali ta karasa kasa ta zauna ta rafka tagumi tana kallonsa.
Sai ta ga kamar barcima yake, sai ta ga kamar ko a ka bai dami da abinda suke ciki ba, yanzun ina zata dosa? Ina zata kai wannan abin? Iman bata yi ba ita ta yi? Walahi ba laifinta bane! To ai zakin nasa ne kuma a cen gidanma jiya zakinsa ne, a nanma kuma zakinsa ne, sannan kafin zakin ai shi ya fara rikota ya zo nan da ita

Wayarsa dake ajiye kuda da kalin Pizza ce ta fara ringin, ringin take ta hanyar kida irin na Iphne

Da sauri ta rarafa dan daukowa hakan ya sa Hanja dake a zaunen nan kuma rakata da lumsasun idannuwansa dan gannin meye kuma zata aikata da zai idasa halaka shi a zaunen nan da yake , gaba daya sai ya ringa tunanin yarinyar nan ba abinda bata sani ba rainin hankali ne irin nata da salon nata a haka,
Abin haushin maimakun ya yiwa rainin hankalin nata kwakwaran hukuncin da zata kama kanta ta kula ta daina neman haike masa sai kawai yake son karasa fahimtar irin nata rainin wayon

Juyowa ta yi ta karaso ta mika masa wayar saman cinyarsa ta koma ta zauna ta rafka tagumi tana tunanin tata wayar a dakin cen da aka sauketa ta saka a caji sabuwar wayarta dal da Mah ta bata a jiya kafin su taso, sun yi whatsup da Mah cewar sun sauka rabonta da ita tun da safe har gashi yama na kokarin sanyo kai, ga wata yinwa dake kwakularta har ta fara shedata dan ta fara sakata juwa

Wayar yake bi da kallo gannin sunnan Mah na yawo kwado kwado aman ya kasa daga hannunsa ya dauka har ta tsinke, sai dai tana tsinkewar aka kuma bugowa hakan ya sa ransa yake ayana' Aya sai yanzun hoton ya kai inda kike Mah?'

Muneerath ta ce" Hanja ka daga mana ana kiranka"

Da sauri ya wara idannuwansa a kanta yana kallonta gannin ta mike tana kakabe kakabe bayan ba kurar komai a jikinta aman sai dube dube take kamar ba ita bace ta gama haukan ihu da kuka yanzu yanzun nan kafin ta karasa kusa da dan kwalinta ta duka ta dauka tana kadewa ta zabgawa zakin nan harara a bayane ta ce" Asarare kawai! "
Ta dawo ta zauna tana kale kale a dakin

A hankali ya daga kiran , blootoof din dake kunnansa yana ta haska wuta blue hakan na nufin magana ake a ciki

A hankali ya kai dubansa kanta kafin ya cire muryarsa kuma cen ciki ya ce" Lafiyarta kalau "

.... .
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 3 □□□

Ci gaba da magana Mah ta yi wanda shi kuma ya yi shiru yana sauraronta gaba daya bakinsa ya masa nauyi yana tunanin anya zai iya dogon bayanin a yanzu kuwa?

Muneerath kam idannuwanta a kan kwalin Pizzar nan da ta kula biyu ne da kuma kwalba dake dauke da jus irin na yan gayun nan

A hankali ta kuma satar kallonsa, ta riga ta gama tsara cewar tana zuwa gida zata fadawa Mah abubuwan da suka faru a nan, idan ya so sai a san abin yi domin bata so ko daya a ga laifinta, sannan a gaskiya tana komawa zata nemi da a maida ita gida wajen nata iyayen ya isa hakanan yawon taburadar!

A hankaki ta mike ta karasa kusa da kwalin
Sai da ta kuma satar kallonsa kafin kasa kasa ta ce" Kai yinwa nake ji, shi kuma sai waya yake kamar tsohuwar karuwa yana lumshe ido, gaskiya ci zan yi ina dalili mun fito dan mu yi ciye ciyenmu ka kawoni nan kuma ka manta cewar mutun ce ni"

Kwali daya ta dauka tana ta adu'ar Allah ya sa ta kaza ce, ba ta alade ba!

Ai kam sai da ta idasa dubawa ta gane ta kaza ce sannan tana fara dandanawa ta ji dandanon kaza sai ta saki murmushi ta dauko ta zauna ta shiga ci tana tunanin ta wannan kampanin ba dai dadi ba

Da idannuwansa yake binta da kallo, baya jin abinda take fadi idan ta yi hausarta a nan, a gida ne du ya saka abinda zai kai masa sakon kalamanta ya fasarce masa a lokacin da yake mata kallon terrorist, wanda ya yi niyar sunna komawa zai cicire dan a yanzun ya gane cewar ba terrorist bace, haka kuma ba ta makale masu bane dan ta ci dukiya ko wani abin ba, ya gane cewa hukunci ne na ubangiji kasancewarta tare da su a irin wannan lokaci, sai dai kuma dayan abin yana da tantama a kan kwakwaluwarta

Irin yadda take kara gyara zamanta tana daukowa tana ci ya sak shi shagala da kallonta, kafin a hankali ya ce" I'm seek Mah "

Mah dake ta jero tambayoyi kan ina yarinyar mutane, me ya sameta, menene wannan hotunnan da yanzu Iman ta kawo mata tana kuka? Me ya kai hannunsa nan dinta a waje public ? Me ya sameta? Tana ina? Ta ji amsarsa cewar bashi da lafia sai

ta samu kanta da sasauta muryarta a hankali ta ce" Kana clinik ne? Me yake damunka son?"

HANJA ya sauke ajiyar zuciya a hankaki ya ce" ina gidana, kuma gatanan"

Mah ta kai zaune saman kujera a sanyayenta ta ce" Kana nufin kana tare da Muneerath ? Dan bani ita mana dan Allah?"

Idannuwansa ya kuma saukewa a kan Muneerath , a hankali ya nuno mata wayar kafin idannuwansa cikin nata ya yi gyaran murya a lokacin da ta dago dubanta tana kallonsa a saman lebunnansa ya ce" Mah "

Muneerath ta taso da sauri tana kallon bakin nasa a ranta tana ayanna 'To ko dai wani ya dakar masa leben ne?'

Amsa kiran ta yi da sauri a tsaye a kansa kafin kuma lokaci daya ta shiga kai kawo , sai kuma ta ja ta tsaya tanarike da kugu da hannunta daya idan Mah na magana daga Mah ta yi shiru sai ta ciro hannun nata ta shiga bata amsa tana kai kawo tana nunawa da hannunta yadda ka san tana gabatar da wani shiri hankalinta kwonce tana kara nunuwana da hannayanta shi kuma yana biye da ita da ido yana hasko dukan abinda take fadi da irin yadda ya faru da irin nunin da take kamar Mah din na kusa da ita kafin ta kare maganarta da fadin". A gaskiya ni dai ban san ko me yake damunsa ba, idannuwansa dai kamar ya sha kuka , aman kuma bakinsa kamar yana masa ciwo dan dazun dai yana dan magana yanzu kuma ta dauke dif, sai kuma kamar ransa a bace yake, to dai abin nasa ni dai Allah ya sa kar ya motsa ina kusa, a yanzun dai da dama fushin ne ke dan nuna kansa aman Mah abinda na fada maki kaf iya gaskiyar kennan na jiyan nan kadai na san na tsero wajensa kuma ashema ba samansa na fada ba dan na farka na ganni saman kujera, na yau din nan ne kawai na kula cewar kamar bayan ya taban gefen kafada sai ni kuma na rike shi dan ya ceceni daga zakin ashema zakin na wasa ne?"

Mah ta ringa sauke ajiyar zuciya tana ta adu'a a kasan zuciyarta kafin ta ce" Yarinyata kina ji?, Ki kula kin ji ko? Ki karra rike mutuncin kanki, idan ya kara tabaki ne abin zai iya tabatuwa kin ji ko? Dan Allah ki kiyaye sallah a kan lokaci, sannandaga an yi ki fada masa ya yin shima kin ji? Kuma yanzu ki sa ya nemi likita dan bashi da lafia kin ji?"

Muneerath ta amsata kafin ta maida masa wayarsa ta kuma tsaya tana jira ya kare

Sai da Mah ta idasa maganarta yana sauraronta a hankali ya amsa mata kafin ya kashe kiran ya daga dubansa a kan Mubeerath da ta ce" Yauwa Mah ta ce ka ga likita baka da kafia, kuma dai ka tashi ka yi sallah nima bara na gama cin nawa abincin sai ka nunan bayi "

Zuwa yanzu lamarinta ya daina bashi mamaki, sai dai dam baya tunanin zai daina binta da kallo dan ya gane ita din wace irin halita ce?

Yana nan zaune ta gama, ta miko masa jus din ta ja ta tsaya ya bude ya mika mata yana kallonta ta koma gefe ta saka bakin dan kwalinta wai kar ta hada baki ta sha iya shanta domin bashi da gaz haka kuma bashi da karfi sai ta ji dadinsa a bakinta sannan ta ajiye masa a kusa da shi tana fadin" ga naka "

Shi da da ido ya kuma rakata har ta nufi bayi sannan ya mike yana tafe a hankali ya nufi wajen da wrdrb dinsa yake ya buda yana bin kayan da kallo dan ya dan jima rabonsa da garin

Sai da ya yi adu'a sannan ya dauko wasu tufafin ya ja ya tsaya har sai da ta gama ta fito

Bai kulata ba , aman kuma ya ajiye mata abin sallah ya nufi bayin

Da ido ta bishi kafin ta gyara ta tada sallarta

Tana saman salaya kanta sade ta gama sallar aman kuma tana ta istigfari ya fito ya fita a falon
daa sauri ta bishi da kallo ta waiwaiga cikin dakin kafin ta sauke ajiyar zuciya ta ci gaba da adu'arta

A fitar Hanja wajen motarsa ya nufa ya ciro salaya
Sai da ya gabatar da sallarsa cikin nutsuwa kafin ya ninke salayar ya shige motar ya nufi kampanin da jirgin nan yake

A lokacin da ya karasa aiki ya hau tukuru sannan a tsanake , hakan ya sakashi cire du wani tunanin dake damunsa, ba shi ya gama ba sai cen kusan jarfe biyun dare

Daga nanma hotel din nan ya wuce ya je ya dauko abubuwansa da basu da yawa sannan ya bude nata dakin

Bin dakin yake da kallo a nan dai ya dan bata lokaci domin sai da ya shiga bayi ya ga kayanta na uniform da ta wanke ta shanya a bayin, ya hado brush dinta da soson wankanta kafin ya fito ya dauki jakarta ta baya ya shiga ninke kayan yana sakawa a cikin jakar har ya zo kan pant dinta
Da sauri ya dan zarro ido sai kuma ya girgiza kansa yana yatsine fuska tamkar ya ga abin kyankyami ya cusa mata shi a jakar ya zuge zif din sannan ya cire wayarta da cazarta ya nufi kofa yana dadana wayarsa ya tura kira a lokacin da ya zauna cikin motarsa

A kausashe ya furta kalmomi kamar haka" tashin safe zamu yi"

Daga haka ya kashe wayarsa baima gama jin ok sir din Sir baya tada motar ya nufi gidan a ransa yana fadin'Na san yanzun ta yi summa goma, yarinyar sam ba hankali a tare da ita'

A lokacin da ya karaso har karfe uku ta gota

A hankaki ya idasa shiga falon da yake ciki daya ne kwal sai bayi sai wajen tufafi, akoy gado aman idan ba sani ka yi ba ba zata taba sannin akoyshi ba domin a cikin bangon yake

A hankaki yake takawa ba tare da ya cire takalminsa ba har ya idasa kusa da cafet din dake ahinfide fari kal

Ido ya tsura mata, irin kwonciyar da ta yi da dan nadewar da ta yi

A yanzu dan kwalin baya jikinta haka kuma gashin kanta ta cire ribom din jiki, a kusa da ita kuma dayar pizzar ce ta bude ta ci iya cinta ta bar sauran a nan, sai jus din da ta kara ta ajiye sauran

A hankali ya duka kusa da ita ya kai hannunsa gefen wuyanta ya taba

Hannun nasa ya dago yana mai karra binta da kallo, abu daya ke masa yawo a ransa.....shin bata da lafia ne? Me yasa du sanyin garuruwan nan ita kulun jikinta da dumi? Bata da lafia ne?

Aman idan bata da lafia hakan na nufin tun ba yau ba fa? An samu circonstanc da yawa da hannunsa ya kai kan nata ko wani waje na jikinta ya ji dumi a jikin nata

Jakarta ya ajiye mata ya karasa ya dana wajen bed dinsa

Bed din ya fito mai dauke da yan gida gida a jikinsa
Budewa ya yi ya ciciro zanin gado ya nufi wajen Muneerath dake kwonce

A hankaki ya samu kansa da warware guda ya rufa mata shi kafin yake kara zubawa fuskarta ido sai kuma ya mike a dan zabure ya yi wajen bed din

Bai cire kayansa ba ya haye saman gadon yana shafa mararsa tare da dan rintse idannuwansa ya juya bayansa ya shiga adu'ar baci kafin ya ringa bitar karatu a kasan ransa ko zai samu barcin ya dauke shi

Shi ya kwonta ba da wuri ba, kuma shi ya rigayeta tashi domin motsinsa ya farkar da ita

A hankali take kara wara dubanta a kansa yana zaune yana opprat din laptop a saman kujerar da bata san a ina ya daukota ba
Kayan dake jikinsa a yau farare ne kar kar masu shegen kyau irin na Pilot
Sun karra haska fatarsa sun masa wani irin kyan da ya birgeta har ta samu kanta da sakin murmushi tana kallonsa tare da dafe kuncinta a bayane ta ce" Kai kamar mutanen da ake nunowa a TV wollah, kai kam ka ringa shan maganin baki kar a cinyeka"

Sai kuma ta kai dubanta da sauri wajen kofar da sauri ta zabura ta mike tsaye tare da nufar bayi da dan gudu gudu ta shige ta rufe bayin Hakan ya saka shi bin bayanta da kallo kafin ya dan girgiza kai

Yana ta aikin nan ta fito ta dauki kayanta dake cikin jakarta dan tana farkawa ta fara gannin jakar ta kuma komawa da wayarta tana karanta cewar nan da minti talatin zasu tashi ta kuma duba lokaci ta ga har tara ta wuce da sauri sauri ta saka suturarta sannan ta ciro hijab dinta na sallah ta tayar da sallar bayan ta gama gungunnin yana kallonta ana kiran sallah bai tasheta ba

Sai da ta gama sallar sannan ta kuma daukan wayarta, nan ta ringa gannin message din Mah tana ta afkin tambayoyin nata kafin ta fada mata yau Birthday dinsa ne sun shirya masa dan karya karya surprise kar ta sanar masa

Dan bakinta ta tabe a kasan zuciyarta tana ayana'Ku yi shagalinku kudi ke maku kaikayi'

Tana nan zaune ya mike yana rufe Laptop din ya dauke shi a hannunsa dama ba jona shi ya yi ba ya dan kaleta ya sakar mata harara gannin kale kalenta take hankali kwonce ko yar gaisuwar nan bata yi masa ba ya cira kansa ya shiga tafia

Da sauri ta mike gannin a shirye yake, sannan ta ga an saka lokacin tafiyarsu tana biye da shi tana hararar keyarsa idan ta daga kanta a ranta tana ayana' Bakin hali ba zaka min magana ba bayan ba gaba ba muke, sai me karma ka min wollah nima ai ba yi makan zan ba malan mu dai je garin namu a maida ni kasata ya isa hakanan a zamana da kai ba abinda baka nuna min ba, bindiga ce, shaka ce, hankada ce, ka kunto min zaki, ka ajiye min zaki duka kaf dan ka halakani Allah ne ya tsaya min kuma na san zai kare ni'

Sun yi tafia cikin nutsuwa da kwonciyar hankali kamar yadda suka zo
Pilot din su biyu ne , dayanma fararan kaya ne jikinsa , kuma bakin fata ne mai fara'a, yana tafe ne da nufin ya karra gogewa a harkar tafia, sai kawayenta da Sir wanda tuna suka dawo ido kawai yake binta da shi, yana jiran su kadaice ya isar mata da sakon zuciyarsa, shi kam wannan lamari na bashi tsoro da ba dan ya ga abinda aka rubuta a shafin masarautar cewa ba matarsa bace ba budurwarsa bace bama kawarsa bace yarinya ce da mamansa ta dauko Hostess ce bayan wannan ba komai a tsakaninsu ya dan samu nutsuwa ba da shima gaba daya hankakinsa ya tashi da lamarin

A baban dakin da suke haduwa ya yi maganarsa ta karshe kan kowa ya rike wayarsa a hannunsa suka shiga gaba dayansu inda Muneerath ta kebe baki ta dan karkace gannin da duhu a dakin duda basu saba gannin haka ba ta hade fuska tana rike da hannun Saudat ta ce" Bara ki ga yadda zai yi daga ya shigo"

Ta dan yi gaba ta dawo ta ce" fuska kamar kunnun safe zai kalle mu ya ce" Kun dawo daga aiki,aiki kuka rafi yi, kun yi kun sauka hakan baya nufin ba zaku samu kira a kowani lokaci ba, idan kira ya same ku ku amsa ko ku samu takardar kora". Ta karashe tana kebe bakinta ta ce" kamar wani aikin shiga aljannah"

Saudat dake daria kasa kasa zata yi magana tare da mamakin duhun wajen ta yi gagawar ja ta tsaya gannin gaba daya wajen ya dauki wani irin haske da walwali yana walwalwalwalwal

Da sauri suka karta wara dubansu sunna kallon lokacin da HANJA ya shigo tare da wasu ma'aikatan gidan lokaci daya dakin ya dauki dan sanyayan kida irin nasu na taken sarakan garinsu mai hade da wakar Happy birthday, sai kuma yan matan da suka shiga rawa su shida rawar iri daya ne da alamu cholegrafi suka shirya suka hardace abinsu

Yan matan masu kyan gaske farare kal kal kal sunna takunsu cikin tsari sunna juyi hakan ya sa sauran suka kama tafi duka ana dan taya rawar ana taya wakar ta hapoy birthday din w HANJA wanda ya ja ya tsaya tunda ya shigo yana kalonsu baki daya fuskarsa bata bayana me yake ji game da da abinda ake yi ba, aman ga dukan alamu ya ji dadin hakan domin da bai birge shi ba da ya yi tafiyarsa

A hankaki Muneerath ta fara gyada kai, dan lokaci daya ta ringa jin wakar na shigarta sai kuma ta ga rawar da suke sam ba haka ya dace su yita ba, rawar da ya dace su kada su juya su rakarkashe su kai dan idi idi su kara a gaban makadi sai wani jimke hannu suke maimakun su bada kala su saki jiki su tafki rawa ba

A hankali ta janye hannunta daga cikin na saudat dake murmushi

Ita kanta bata san abin ya debeta har ya karasa da ita tsaka tsakan rawar ba sai da ta yi kamar juyi hudu ta kula da ana tafa mata kamar yadda du wace ta yi abin

bajinta ake tafa mata ana shan dariya da morewa ba sai da idannuwanta suka sauka a kan fuskarsa ne gabanta ya fadi lokaci daya kuma ta nemi tsayar da kanta rawar ta kasa a lokacin ne aka shiga turo katon cake din da aka yi masa mai yannayi da jirgi masu rawar na tikar rawarsu masu tafa gannin cake din na tafawa har aka kusan turowa gabansa inda yake tsaye kikam tamkar idan ya budi baki aman wuta zai yi na bacin rai da kuma jin haushin shirmen yarinyar nan da ya gama yiwa jawabin ta kama mutuncin Mah dinsa itace ta cire da rawa a cikin mutanen nan

A hankali ya daga kafarsa zai karasa inda take, daidai wani lalausan hannu ya shiga cikin nasa , hannun mai dauke da sanyi da kuma laushi sai kamshin turaran da ya dakeshi hakan ya saka ya juyo da dan sauri dan gannin ko waye lokaci daya idannuwansa suka sauka a kanta,
A hankali ya lumshe idannuwansa ya kuma budewa ya kai dubansa kan hannun kafin ya dagoda wani yannayin na ya shaka ya budi bakinsa ya ce"
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 4 □□□

Ba edditing.....

Kasa kasa ya furta" Sake min hannu "

Hannun nasu itama budurwar ta bi da kallo kafin ta saki a hankali ta sanyayar da muryarta sosai ta ce" Me ya hadasa maka bacin rai a rana irin ta yau? Ranar birthday dinka my prnc?"

A hankali yake binsu da kallo sunna yin duku duku suka fice ita da saudat

Kafin ya kuma bin Sir da kallo wanda shima ya silibe ya fice da dan sauri ya yi gagawar maido dubansa jin PDG na yi masa happy birthday tare da gayatarsa ya

karasa ya yanka cake din da ma'aikatar ta yi masa dan su yi surprsd dinsa abinda da yadda nasara ya ba cikon shekara mahinmanci , irin yadda du wani baba a wannan kampani harma da wahen kampanin suka gayato ya kuma amsa gayyar, irin yadda suka kayata wajen ya kayatu yake walwali

A hankali ya daga kafarsa ya nufi wajen cake din bayan ya yi iya yinsa ya tataro du wata jarumta ya yabawa fuskarsa tare da sakin lalaisan murmushin da bakinsa lebensa a likacin da baban sojan dake kula da lafiyarsa da kuma yannayinsa yake dan fada masa cewar ya saki fuskarsa dan hotunnan mdia ya dan lumshe idannuwansa zuciyarsa cike da jin haushin lamari irin wannan da yawancin abu za'a saka ka yi ba dan radin kanka ba sai dan kawai ka birge wani , kuma ya zame maka wajibi ka yi duba da irin yadda mahaifinsa ya kawo sunnansa ya dora kan wanda zai gaji kasarsa
A hankaki ya taka ya tsaya gaban cake din, masu dauka na dauka, manya manyan ma'aikatan suka saka shi a tsakiya a hankaki ya dora yar siririyar wukar da aka bashi ya dago dubansa ya kai wajen da take dirka rawa kafin a hankali ya kai hanyar da suka bi wace bai san waje zata fitar da su ko sunna ciki ne tare da wannan katon da kuma kawar nan tata da aka fito yau ta fara aiki tare da su

A hankali ya maida kan cake din ya dan saki wani murmushin kafin ya yanka cake din inda aka shiga tafawa

"Freind, " ta fada muryarta a sanyaye a lokacin da suka durfafo palace din aman suka ja suka tsayar da motar ya juyo da dubansa muryarsa a sanyaye ya ce " Muneerath, plz.....saudat ki saka baki ban san me yasa take damuna da maganar Dogari ba"

Muneerath ta kuma kallonsa ta juya ta kalli Saudat wace ta sada kanta tana dan murmushi, dama ta san a rina, walahi ta gane son Muneerath yake ba yau ba, aman ta yi mamakin da bai fadi ba sai yanzun

A hankali Muneerath ta ce" Dogari, Freind me yasa kake so na bar maganar dogari a rayuwata ?, Ka kuwa san tun ina yar karamata nake dakon wannan buri?"

Da dan sauri ya ce" Buri ne ba bukatar zuciyarki ba My Muneerath, shin zama zaki yi ta yi kina jiran kila wa kala? Ko kina tunanin kina iya ba wani dake sonki damar ku yi soyaya?"

Muneerath ta kuma satar kallon Saudat, haka kawai take jin bata son maganar ta yi nisa sosai , aman ya ta iya su da suka kasance a mota daya a nan bata tunanin zata waske

A hankali ta ce" Buri na ne"

Sir ya kara kureta da ido kafin ya ce" Ni kuma kece burinahhhhhhhhhhh my Munee"

Sai da gabanta ya fadi, da sauri ta kura masa ido da wani irin duba tana jin zuciyarta na bugawa a hankali a hankali kafin ta cire dubanta tana kallon waje

Ta kasa gane a wani hali take,
Ta kasa gaskata kunnayenta

Ta kasa gane a yanzu a wani yannayi zata ajiye wannan rana
Wai ita? Ita Muneerath yar kuryar dakin kauyen anguwarsu, itace ta hadu da daukakar ubangiji a yau har ta samu furucin so daga bakin mutun mai daraja irin sir? Sir ATTAHIR musulmi ne, mutun ne mai tausayi da taimako, mutun ne mai girmama mutane mai girmama talaka, ya kasance mai bata talafi a kowani yannayi take ciki

"Dan Allah, bana so ki bani amsa haka kai tsaye, bana so ki so ni dan wani dalili daban, ni ina son ki, kuma ni gani a gabanki bana so ki daidaita ni da mafarkinki, Muneerath ni realty ne, Muneerath ina son ki.....idan dai ba wani ya rigaya ya fito wanda ya fi karfina ba.....bana tunanin zan iya barinki a kan tsumayi da kike, My munee idanma so kike na je na saka rigar dogari zan saka na rike sanda irin na dogari dan na amsa sunnan miji a gareki" ya karashe yana kara sanyayar da muryarsa yana kallonta

Wani irin yuyu take ji a kunnenta,wani irin lamari mai wuya fasara ya kara ziyartarta

Meye aibun SIR?
Meye zai saka ta kasa aminta da shi ?
Ahi din baban mutun dinta ne
Shi din mai tausayi ne
A hankali ta ja hancinta dan ji take kamar iskar ta mata kadan
A sanyaye ta ce" Haba sir"

Sir ya karra tsatsareta da duba kafin ya kuma cire idamnuwansa a kanta yana kallon Saudat ya ce" Ko dai ta kamu da sin wanina ne?"

Saudat da ta ji wani shaukinsu na dibanta ta ringa murmushi a hankali ta ce" Ka bamu lokaci da kawara na san zamu bada amsa mai kyau, ka karasa da mu gidan sai mu nemo amsa kwana kusa"

Ajiyar zuciya ya sauke ya kuma kura mata ido ya ga sai dantse hakorinta take, a hankali ya tada wuleliyar motarsa ya fara tafia motocin Hanja suka wuce da wani irin gudu gaba dayansu suka nufi eriyar palace din

A lokacin da suka karaso sai da ta fito ta nuna cd dinta kafin ake basu shiga damar shiga daga ita sai saudat bayan Bodyguard dinta sun karaso da sauri sunna fadin a cen suke basu ganta ba suka biyo tawagar Sir tuna ya ce su dawo tare

Ita dai bata da karfi, a hankali ta juya ta bi motar Sor da kallo kafin ta saki dan murmushi sunna shiga ta saka ihu harda dira ta riko hannun Saudat ta ce" Wayo na shiga uku, Saudat Freind fa? Freind ya ce yana sona?"

Saudat dake murmushi tana ta bin tsarin Palas din da kallo cike da kauyanci duba da yaune rana ta farko da ta sako kafarta albarkacin albarkaci duda irin yadda kafafuwanta suka taka kasashe daban daban ta kuma kai ziyara da mahifinta da yake baban mai kudi a wazaje daban daban sai nan din ya zame mata abin kallo harma ta kasa boye kauyencinta take ta juyi tamkar zata kifa

Muneerath ta tabata tana girgizata ta ce" Kina tare da ni kuwa? "

A dan firgice ta rike hannun Muneerath ta ce" Munnee mu gudu, kalli yadda sojawa suke baje a gidan nan, kina gannin da makamansu da wadinnan kannanun jiragen droon din dake yaeo san kanmu sunna iya rufemu da harbi fa a kowani lokaci aka bukaci da su yi hakan"

Muneerath da bata san asalin aikin dronn ba , ita dai a tunaninta du isa ce ta mai kudi ya saka suka zuba kannanun jirage sunna masu yawo a cikin gifa ta ce" Ke wadinnan sojojin bafa bindiga bace a hannayensu yar wukar roba ce, kuma wadinnan jiragen na wasa ne ai"

Ido saudat ta zarro zata yi mata magana ta yi gagawar hadiyewa sakamakon sojan da ya nufo su furkarsa hade ya ja ya tsaya a gabansu fuskarsa hade ya shiga tambayar da wa take tare, yaushe ta dauki rdv din shigowa gidan nan? A wajen wa ta samu damar hakan?

Da mamaki Muneerath ta budi bakinta ta ce" Aman giya ka sha yauma kau? Yanzun dan zan shigo da kawata sai ta bi layi kamar wace ta zo maula ko wani abin?....."

Yana niyar mayar da kawar tata baya akai masa magana a blootoof din dake kunnensa hakan ya sa da sauri ya dakata kafin ya juya ya basu hanya inda Muneerath ta girgiza kai ta ja hannun Saudat da jikinta ke rawa na tsoron wannan drnnn din dake saman kansu sunna biye da su

MAH dake tsaye cike da mamakin yannayinsa ga irin tarbar da sukai masa sam bai basu damar gabatar masa da murnar taya shi cikar shekararsa ba ya shigo a wannan hargitsen falon gaba daya, tunda ya shigo kuma ya aniya surfa masifa yana nuna mata waje cewar bashi da damuwa aman kar ta kuma bashi amanar yarinya marar hankali du ta hada masa ciwon kai, ta yi meye, ta yi meye, itace harda shigewa cikin maraya hostesss tana tikar rawa bata gannin irin jikinta ta wani silale ta bi Attahir shine ya kawo su har gidan nan, toh lale zai kori Attahir din idan har shi aikinsa ya lalata y'ayan mutane ne ko kunya baya ji yace yana me da dalibarsa? Bayan ya san abinda ya fi tsana kennan shine yake masa a kampanin kasarsa? Tare da wata cen da ta raina mutane?.....da karaji ya karashe wanda maimakun ya tayarwa da Pah Hankali sai kawai ya zauna saman kujera ya dora kafa daya kan daya yana kadawa yana ta sakin murmushi, inda Iman dake tsaye rike da wani Plate da Mah ta yi zanen Happy birthday da wani walkiyar abu da hotonsa a jikin plate din ta yi kasakai jikinta na rawa coke da tsoron fadan da yake yi

Mah a sanyaye ta ce" Son, menene ya daga maka hankali har haka.....son me yasa abin ke taba maka har kasan zuciyarka?"

HANJA da a tsayen nan yake ji kamar zai yi fifike da bacin rai ya shiga fadin" Me ya batan rai? Ni sa'anta ne da zata gudu ta barni a cen ta tafi bayan ke kila ce amana na kular maki da ita?, Salon wani abin ya tsoratata ta rukunkume Attahir ta suma? Haka fa take yo fa rukunkume mutumen dake kusa da ita take yi fa! MAH na gaji! Na gaji!"

Pah ya yi gagawar cije lebensa na kasa yana dan rauda kansa yana danne dariyar dake cinsa

Mah kam hankalinta ba a kwonce ba, tsakani da Allah baya fada haka, baya tada jijiyoyin wuya haka ya ringa bambami bale a irin wannan ranar da suke fita gaba dayansu su wuni sunna farin ciki tare? Hakan ya sa a hankali ta mika hannunta ta riko nasa ta ce" Idan mutun ya tsorata ai dole ya kama wanda ya fi kusa da shi kau? Laifi ne a cikin hakan?, Son ko rike ATTAHIR din ne damuwar?"

Rai bace zai yi wata maganar lift din da ya ajiye au suka fito Muneerath ta bude kofar falon tana kyakyata daria da hausa ta ce" Wai ni yar bakar gidan Oga? Allah zaki yi ki gama ni na san ba wani sona yake yi ba yanzun yace min wasa ne , tsakani da Allah ina ni ina kai kaina inda Allah bai kaini ba?????????"

Turus ta yi gannin mutumen na halin, ana ta wani riko masa hannu gabjeje da shi yana bautsewa ko wa kuma ya taba shi oho □□□□□□, , ta dan yatsina dubanta a lokacin da suka yi ido hudu ta ga kamar wanda ya harareta kamar mai jin haushinta, a kasan zuciyarta ta ayana' to shi dai idan ba kasheni ya yi ba , ba zai daina min hararen makiyiyarsa ba!'

ta kamo hannun saudat da ta tirje cike da jin tsoron gannin Sor HANJA na wajen ashe, da kuma matsanancin mamakin yau itane a tsaye a falon sarkin kasar nan da matarsa harma da baban dansu kwalin kwal jal , ta janyota da sauri suka nufo su ta budi baki kasa kasa ta ce"
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□ *[T.M.N.A]* □ □□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 5 □□□

Kasa kasa ta ce" Ke dillah ki saki jikinki kin wani kankame mu je mu runringume sun, wai a nan fa sai ka rungume mutun, aman walahi kar ki rungumi maza ni dai ba ruwana sai mu je dakina na fada maki abinda Mah ta ce da lamarin maza"

Ita dai Saudat, kiri kiri take kallon ikon Allah, a lokacin da tana tsate Muneerath ta idasa jikin Mah da farin ciki ta rungumeta a cikin jikinta ta bata peck tana mai farin ciki da fada mata ta yi kewarta kafin ta zana mata irin salar da aka yiwa HANJA a cen, ta karashe da fadin ita kam yanzun kuma bata san wa ya bata masa rai yake fada ba

Tana nan tsaye ta ga irin bahagumen rungumar da ta ba Iman ta rada mata cewar fatan dai yanzun an daina iskanci?

Sannan ta karasa ta duka har kasa ta gaishe da Pah wanda abin mamakin ya dafa kanta ya saka mata albarka yana ta sakin murmushin da ta rasa ko na meye kafin ta tashi tana kallon hannun Iman da ta yi kici kicin gaba daya yannayi na bacin rai da tashin hankali sun tataru sun nuna kansu a tare da ita ta tabe baki ta ce da Maj zasu ke da kawarta aminiyarta ce tun niger sai yau Allah ya sada su ta fito itama yanzun Hostess ce, inda Mah ta gyada mata kai domin gaba daya hankalinta a kan rigimamenta da ya zama kamar status kawai bin Muneerath din yake da kallo har abin na bata tausayi

Har sun fara tafia Muneerath ta daka birki ta dawo tana murmushi ta kalli wannan ta kalli wancen, a hankali ta kara kunnenta a kusa da Mah wadda ta yi tsai dan sauraronta , sai dai dama Muneerath ko rage murya ta yi ba wai iya rada ta yi ba domin bata iya yinta cen kasa ba ta ce" Mah wayo Allahna, Mah sir dinmu wannan freind din nawa da na fada maki shi kadai ne abokina namiji a duniya wai yace wai wai....."

Sai ta rufe fuska tana ta murmushi kafin ta juya da gudu ta ja hannun Saudat ta nufi lft da ita ta danna suka shige inda Mah ta saki dan murmushi bayan ta raka su Muneerath da kallo cike da sha'awar sakalcinta da yarintarta har suka gushewa ganninta kafin a hankali ta maido dubanta kan HANJA

Sai da gabanta ya fadi,
Gaba daya fuskarsa ta gama hadewa tsaf haka kuma fuskar ta yi wani irin ja
Huci yake fitarwa wanda yake nuni har gaban kirjinsa

A hankali ta kara mika hannunta ta matso shi sosai ta roke hannunsa da hannunta guda kafin ta kai dayan hannun nata wajen kirjinsa cike da tausayawa ta ce" Son, kalle ni, plz ka kalle ni, dan Allah ka sasautawa kanka fushin nan, Son so kake a maidata ne? Idan har a kasan zuciyarka so kake ta fita daga nan zan yi hakuri son, zan yi, dama bana so ace bata rigaya ta idasa cika burinta na son zama Hostess mun barota a cen an koreta ne, domin D'a na kowa ne, aman idan har yanzun so kake ta tafi shikenan ka shirya mata tafiyar sai na yi mata rakiya in sha Allah, dan Allah ka bari haka ka ji? Yau fa birthday dinka ne, ranar da take baba a wajenka da mu baki daya, ka ga kuwa cake dinka? Na maka girki da kaina..... plz ka dube ni Son?". .....ta katashe tana kara sado dubansa kanta domin idannuwan nasa a kan hanyar da suka shige

A hankali ya lumshe idannuwansa , hannunta dake cikin nasa ya kawo wajen kirjin nasa a hankali ya danna kafin ya rintse idannuwansa

Muryarsa wannan karron ba da babatun ihun da ya shigo da farko ba, ba da fadan da ya shigo ba, a hankali sannan a sanyaye lafuzan wani na korar wani a hankali ya ce" Mah i'm seek "

Gabanta ne ya fadi da yannayinsa, da kuma furucinsa,
Haka ya fada a jiyama a cikin waya kuma daga baya ya ce wai ya warke
Aman a yanzun itama irin bugun zuciyarsa da irin yadda idannuwansa suka rikide sai ta tsorata, dan haka da sauri ta umarci Iman kan ta kira mata docter kafin su yi ciki tana rike da hannunsa gaba daya hankalinta ba a kwonce ba ta tsaya kisa da Pah tana gannin yadda hankalinsa kwonce shi ko a ka bai wani nuna damuwa da yannayin Hanja dinba sai ta ji haushin hakan ta idasa jan hannun yaronta da nufin kaishi bangarensa sai kuma suka dawo domin tunawar da ta yi akoy tgr ta taimaka masa ya kwonta saman kujera ta shiga cire masa takalmansa da safa da komai kafin

ta zauna tana rike da hannunsa tana cika tana batsewa da yannayin Pah, kuma har kasan zuciyarta a yanzun kam ta hakura da rike Muneerath din tunda dai haka zaman Muneerath din ke rikita shi, ta hakura, Allah yana ganni dama yarinyar ce ta shiga zuciyarta , irin hakurin yarinyar da courage dinta kuma ya sakata sakawa ranta abubuwa da yawa

Jinninsa aka diba, bayan aune aune likitan ya tafi da sauri da kayan dan dubawa

A hankali ta talabe shi da dan jus din da ta zuba a dan kofi ta kafa masa a bakinsa ya dan surba ta maida kan nasa tana shafawa ta kalli Pah dake dadana Computer yannayin fuskarta na nuni da fushi take ta ce" Aman me yasa zaka yi zamanka kana kallon halin da son yake ciki ko magana ba zaka matso ka masa na ji dadi ba?"

Pah ya dakata ya dago ya zubawa HANJA ido, irin kwoncin da ya yi fuskar nan tasa a hade tamkar wanda aka watsawa kashi, ya yi wani irin kwonci gaba daya ya yi ja hakan na nuni da abinda ke damunsa na nukurkusarsa daga cen kasan zuciyarsa ne
Abin tausayin shine shi kansa bai gama gane me yake ciki ba, ko kuma baban girman kan dake damunsa ya hanna masa ganewar
Ya kasa gane cewar yana cikin bacin ran tunanin ta yi magana da waninsa ne? Ya kasa gane cewar dariyar da take saka shi bai shirya ba a cikin tsarin abinda ya rike masa wuya ne
Uwa uba ya kasa gane cewar babu halitar da aka halita ba kishi a jinsin dan adam ko wani iri ne sai dai idan bai hadu da ainahin abinda zai yiwa kishin ba.....ko kuma ya gane baya so a gane ya afka dan gudun kar a masa dariar shi mai fadin bai san KISHI ba?
Ko kuma yaron nasa na cikin duhu ne? Idan kuwa yanna cikin duhu har haka lalle yana tsoron yaron nasa ya fada a mugun halin da ba zai iya ciro shi ba

A hankali ya sauke ajiyar zuciya ya ce" Hurul ayn, yaya kike so na masa ne? Ni da na yi nawa wa ya kama min?"

Tsatsareshi ta yi da ido kamar zata dauke shi da su , a hankali ta cire dubanta tana ta kokarin fasara maganarsa, rashin lafiar da yake ciki ko me yake nufi?

Mikewa ta je yi dan ta karasa kusa da shi ta samu gamsashiyar amsar da take son sani ta ji an rike mata hannu

A hankali ta juyo tana kallon HANJA kafin ta duka kadan tana kallonsa a hankali ta ce" Son, yanzu za'a kawo maka magani ka ji? Ko na kira wajen aikinku ne na sanar masu?"

Idannuwansa ya rintse da abinfa yake kasan ransa wanda ya ki gushewa, a rarabe ya iya budar bakinsa ya ce" Me ya ce mata?"

Ita har ga Allah ta manta cewar Muneerath ta mata maganar cewa Sir ya ce mata wani abin aman bata idasa fada masu ba, hakan ya sa ta rasa me aka cema wa?

Da sauri ta kara kai hannunta tana taba jikinsa hankalinta tashe ta ce" Khalb, dan Allah ka duba bashi da lafia fa?"

Pah ya dafe gaban goshinsa yana kallonta kamar wata yar baby du ta rikice ta kasa gane cutar dan nata ba wani abu bane sai na kokowar watsar da abinda ke damunsa da yake yi tun karfinsa ya girgiza kai ya rufe computer ya mike ya karaso inda suke

A hankali ya kai hannunsa jikin Hanja ya taba kafin ya kaleta
Dan murmushi ya sakar mata a hankali ya kalli Hanja da ya lumshe idannuwansa tamkar mai yin barci bayan idannuwansa biyu kawai abu ne ke nukurkusarsa ya ce" Cewa ya yi yana sonta "

Hanja da idannuwansa ke rintse bai san lokacin da ya bude su a kan Pah ba
Dama tunda ya zo ya fara fada ya kula Pah sai wani murmushi yake yana kada kai, bai san yaushe Pah ya fara fifita yarinyar nan akansa ba, gashi dai yanzu kuma yana fadin haka?

A hankali ya nemi tashi zaune hakan ya sa Mah da sauri ta so taimaka masa sai dai Pah ya rikota a jikinsa yana tatare mata goshinsa da yannayin kamar zai yi fada sai kuma ya kane mata ido daya yana mata murmushin da ya kara dulmiyar da ita a duhu

Hanja ya idasa zama da kyau a hankali ya ce" So kuma? "

Pah ya gyada kai da sauri yana dan daga kafadunsa kafin ya saki murmushi ya ce" Kuma da alama itama tana sin nasa dan ka ga kunya ta ji ta fada, ashe dai ka kusa zama yayan ango ka daura mata aure abinta"

HANJA har wani duhu duhu yake ganni na bacin rai, abu ne da bai saba ba, abu ne da bai taba tsintar kansa a ciki ba, ransa bace ya ce" A kan me zan daura mata aure ni kuma? Bama za'a yi mata ba walahi ba wanda za'a aurama ita!"

Pah ya ce" a kan wani dalili fa?"

Hanja ya kalli Mah dake kallonsa ya kuma kalli Pah, sasautowa ya yi daga saman kujerar ya hade hannayensa ya furzo da wata iska daga bakinsa ya ce" Aman ai amanarta muka dauko ko?"

Da wani irin mamakin jin a yau ya ce da shi a dauko amanar Muneerath Mah ta kara tsatsareshi da ido

A hankali ta samu kanta da fadin" Son, kishi nake gani a tatare da kai?, Son kishin Muneerath ne nake gani? Son ka fada soyaya? "

Lalala kamar wanda yake jira hakan ya fito daga bakinsu, nan fa hali ya motsa kamar ba shine yanzun take kamawa tana kwontarwa tana lalasa kamar wani dan goye yanzun ya firfito ido cike da mamakin furucinta a birkice ya ce" Mah so? Soyayar yau na fara? Wani irin kishi? Ni? Kishi? Ni ban san kishi ba! Ke fa kike cewa yar amana ce kuma ta kiyaye du wani hulfa da wani, kuma ni fada ne nake mata in na ga na hanna ta tana yi, barama na tarda ita sai ta fada min abinda wannan sakaran ya fada mata kuma shi sai na kai shi conseil kafin na kore shi dan na kula yana cikin masu lalata mana ma'aikatanmu!""""""""""""""

Fuuuuuuuuu ya mike kamar ba shi aka gama rikewa bashi da lafia ba ya nufi lft

Da sauri Mah ta mike tana kiran sunnansa

Pah ya tiko hannunta yana daria a bayane yana girgiza kansa ya dawo da ita saman kujera sunna facing din junna

Irin yadda hankalinta yake tashe ya saka shi kara yin dariar da ta jima bata gani ba

Har dafe kansa yake a hankali ya ce" Alhamdulilah"

Mah a sanyaye ta ce" Du sai na ga kamar ba kai na, du sai na ga kamar baka damu da damuwarmu ba, duba fa ka ga halin da yake ciki, kuma duba ka ga ya bi bayanta kar ya daketa"

Pah dake daria a hankali ya ce" Ba zai iya dukanta ba"

Mah da bata gamsu da maganarsa ba ta ce" Ka fa san zafin ran son idan ransa ya baci, abu kalilan yake zartarwar da hukunci mai tsanani, bana so ya taba lafiyar yar mutane kafin na maida ita wa ahalinta"

Pah ya karra yin daria domin shi rabonsa da gannin nishadi irin wannan har ya manta, wai shine yau da idannuwansa da ransa da lafiyarsa ya gama gannin sc□ne din kishin yaronsa? Ya ce" Ya yiwa wa duka? Ni sai kawai na ga idan abu ya shafi yaronki ne sai ki rikice ki kasa gannin komai, ai Muneerath ta fi karfin dukansa sai dai ta dake shi! Kuma idan kika yi gigin mayar da ita wa iyayenta a yanzun a awani kusa zaki zama wada zai yiwa kallon mai son raba shi da numfashinsa.....yaronki ya yi wasa ya zurma da yawa, ya yi sake ya zurma a duniyar da bata damu da shi ba, ina mai taya ku da adu'ar kar ku yi wani wasan da zaku haukace ku rikice ku rasa gane yarenku!, Kin ga barni na gama bincikena a kan lamarin Muneerath"

Jikin Mah a mace, cike da rashin karfin jiki ta dora kanta a gefen kafadar Pah a sanyaye ta ce" Ya Allah ka kama masa, yarona karami ne, bai iya kokowa a kan abu ba, Allah ka bashi , ka sasauta masa ya rab, ka sa wannan rigimar ta zama mai sauki a tare da shi, ka sa yarinyar nan yi masa kallo irin wanda yake mata...."

Murmushi kawai Pah yake ya kurawa hanyar da ya bi yana jiran gannin saukowarsa a haukace□□

Hauka suke zubawa tuburan
Gaba daya Saudat ta kasa yarda cewar wai da gaske dakin nan na Munnerath ne
Ihu suke na arziki sunna bude bude da ciro dogayen rigunna
Kida na wakar hausa suka saka sunna casu abinsu tare da kyakyata dariar shirmensu

Saudat ta ce" Muneerath, girman ubangiji ya fi gaban tunanin bawa, wai da gaske baki da shamaki a palace din nan? Muneerath kina kallo Sir HANJA gamu ga shi a gidansu yana kallonmu? Munnee wai kuma baya maku fada a nan?"

Muneerath ta zauna saman gadon da yar rigar dake jikinta sai dogon wando ta talabe habarta ta ce" ke sangarta ce fa irin ta yan baci, wollah a nanma bini bini yana fada, bini bini mamansa na rarashi har mamaki nake, yo da gidanmu ne oga da matansa ba sai dai su idasa haukata zuciyarka ba dan ka kasance mai fushi wollah matsalarka!, Aman a nan kin ga idan ya shigo an kama kamo shi, ana wani shafar kansa, ana wani zabura ana kawo masa abin tabawa, kai kudi jaraba ne, kamar wani sarki saima kinnga yadda wannan yar uwar tasa take masa haukan so? Sonsa take kamar ta mutu"

Saudat ta zarro ido ta ce" Tap, aman ta dauko ruwan dafa kanta, baki ga wata rantsatsiyar budurwa da ta shigo da bakar riga a jikinta ba? Wannan budurwar ni nan ni nake kallonta ina karawa baki ga kyau ba, luwai luwai da ita, yar wannan mahaukacin mai kudin ce kuma ita kadai ya malaka a duniya, ke itace fa budurwarsa ita ta bada makudan kudade wa kampanin aka shiga shirya masa karya

karyar nan, daga baya da kampani ya nuna na zai amshi kudinta ba ta nuna wannan kadan ne ta shirya masa wata salar ta birthday dinsa a wani wajen wannan tana so ne ta ga yaya zai dauki lamarin, ke kin ga abin wai? To Allah sai ta yankata a kan Hanja, kuma da kike cewa kamar sarki an fada maki ba sarki bane? Shi fa zai gaji abansa"

Muneerath ta yatsina baki tana girgiza kai ta ce" lale, to ita tsakani da Allah kashe kashen kudin na menene? Ni mamaki suke bani da suke nunawa kato so, yo Allah na tuba ka ja zarenkama yaya ka kare da namiji bale ka nuna zakewa? Da hakuri ta yi har ya nuna yana sonta sai ta yarda, kuma ni du in kika ce sarki daria kike bani kali fa kin taba gannin sarkin garinmu fuskarsa a bude? Ji fa shi wannan fuskar tasa kulun a bude take gashi dan kyakyawa da shi sai fada kulun kulun"

Saudat ta yi daria tana bude computern Muneerath ta zauna gefen bed din ta ce" Ba zaki gane ba, bara na shigar maki tarihin masarautar kasar nan sai kin haukace

Tankwashe kafafuwansu suka yi inda Saudat ta shiga duniyar yanar gizo dan ta nunawa Muneerath me ake kira da sarauta , ta kuma ganar da ita cewa Allah ne ya tsaya mata ba kowa ba da har ta samu arzikin nan, ta ganar da ita cewa Hanja sarki ne mai mulkar saraki, ta kuma ganar da ita cewa ba wai rawanin bane shedar sarautar domin da rawanin ne da kowama ya naa ya kirayi kansa da sarki

Sunna shirin fara afkawa duniyar saraki aka shiga dukan kofar tamkar za'a karyata, karan da take ke iya nuna maka cewar ba mai karamin karfi ke dukanta ba

A tare suka zabura sunna kallon kofar

Saudat ta ce" Mun shiga uku waye?"

Muneerath ta diro da sauri ta je ta dan buda ya kofar da kake lekawa dan gannin mai bugawa dannita kanta tunda ta zo gidan nan ba'a taba buga mata kofa a haka ba, hakan ya sa ta tsorata da jin dukan kofar na yanxu

Da sauri ta dora hannunta saman kanta ta kallo saudat ta budi baki ta ce" Ubanmu zai ci walahi zaki ne da shi min shiga uku"

Saudat ta fita kidimewa domin ita cen dama tsoronsa take din, duda baa gane waye din ba kalmar ubansu za'a ci ya sakaa rikicewa ta duka tana kokarin fashewa da kuka , sai dai bata yi ba gannin Muneerath ta nufi kofar kuma da nufin budewa a haukace ta ce"
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 6 □□□

A rikice saudat ta ce" Kar ki bude dan Allah kar ki bude kin ce zaki kuma zaki bude?"

Munnerath ta ce" Idan ban bude bane zamu kara laifi, to wai mema na masa daga dawowata? Kin ga walahi idan ban bude ba ya fara ihu a wajen nan abin hauhawa zai yi sai gyaran Allah, na tabata Mah na kusa dan bata bari ya dakeni, kakarinta shaka ce da ya shakeni kuma kafin Mah ta iso wataranan sai na gala masa cizo a hannu wollah"

Tana fada tana murda ky din ne ta bude dakin gaba daya

Irin dukan kofar da yake, irin yadda yake jijiga kofar kai kace daga an bude zai dauke wanda ya bude din da mahaukacin marin da sai ta ga walkiya, Saudat kanta da ta duke ta rufe ido cike da tsoro da gannin gangancin Muneerath a kan wai tunanin da wanda zai amsheta ta bude kofar nan j'ai n shirun ya yi yawa a hankali ta shiga bude idannuwanta dan gannin ko ha ya shaketan ne ya yi waje da ita

Ido ta kura masu kamar yadda ta ga ikon Allah Muneerath ta bude kofar aman kuma ta ja baya kadan ta tsaya da shigarta tana kallonsa

Tun daga kafarta ya dauko kallonta har ya dire saman fuskarta da ta yi wuki wuki tana kallonsa ta kwashashabe fuskar tamkar zata fashe da kuka

A hankali ya mika hannunsa ya damko nata hakan ya sa Muneerath fadin" Innalilahi kuma taba min hannun zaka yi? Dan Allah ka daina min haka ni walahi irin abin nan naka mamaki yake bani bayan mamanka ce da kanta ta hanna kuma kake yi!"

Hanja ya lumshe idannuwansa a lokacin da ya nufi wajen kofar Iman da ita, ba dan komai ba sai dan kar ya yi magana a gaban Saudat wace take kasa da shi ma'aikaciyarsa

Jikin bangon kofar Iman din ya turata kadan hakan ya sa ta hadu da Bangon tana rintse idannuwanta domin har ga Allah ita idan yana cikin halin nan tsoronta daya kar a samu matsala ya dankareta, fada da namiji ba riba gashi namiji mai aljanu idan ya riketa bata san yaya zata yi da ranta ba hakan ya sa a rikice ta yi gagawar rufe ido tana kuma kai hannayenta dan kare fuskar tata

Huci yake tamkar kububuwa
Gaba daya ya gama hargitsa yannayinsa
Fuskar nan tasa a hade take ta yi jajajir kamar wanda aka tsoma a ruwan zafi ya silgeta
Lebensa kuwa sai shan tauna yake dan tsabar balakin dake kan harshensa

A dake ya ce da ita" Me kike so da ni ne? Me yasa ban isa na saka ki ko na hanna ki ba?"

Munnerath jin yana mata tambayoyi a hankali ta buda idannuwanta
Gabanta ne ya fadi sakamakon idannuwansa da ta kalla cikin ido, haka kawai ta ji kirjinta na dokawa kafin ta cire da sauri, sai dai bata idasa cirewar ba ta dawo da duban nata wannan karron a hankali tana mai son rintse idannuwan tana kuma shakar kamshin jikinsa

A sanyaye ta ce" Me na yi kuma?"

Hanja ya lumshe idannuwansa dan a yanzun da ya tsatsareta sai yake jin fushin nasa na yin kasa kasa a hankali
Hajan ya sa amon muryarsa ya sasauta a lokacin da shi kansa bai fahimci haka ba ya ce" Me yasa ku yan africa bakwa bada amsa idan akai maku tambaya sai dai ku mayar da wata tambayar ne?"

A hankali Muneerath ta dora dubanta a kan damtsen hannunsa da ya cika ya tumbatsa a hankali ta dan yi murmushi ta ce" Kai fa yaya Hanja, to kaima yanzun ba tambayar bace ka maido da ita ba? "

Gefen kunnenta mai dauke da dan saje kwontace a kusa da kunnenta wanda bashi da tsayi sosai aman ya kai rabin kunnen nata kuma bakinsa sosai ne gashin nata hakan ya sa kalar fatarta ta fi shi haskawa, ya kurawa ido yama rasa me zai ce mata

Gannin zata juyo dubansa ya saka shi sauke ajiyar zuciya a hankali ya ce" Me ya ce maki?, Dama so yake ya lalata maki tarbiya ko? Ko kuma kema irin mai biye biye kowani shara ne?"
Munnerath ta kwashashabe fuska a hankali ta ce" Wane? "

"Ya Rab" shine abinda ya fada a sanyaye kafin ya ce" Attahir "

Da ba dan ta san waye attahir ba da ba zata iya cenkowa ba, a hankali ta ce" Cewa ya yi yana so na fa, kuma shi din ai ba lalatace bane"

Dole Muneerath ta ringa tunanin ko dai aljannu ne da HANJA, domin yanzun suke magana ta laluma aman daga fadin haka ya shiga fada har yana rintse ido yana hade magana biyu , a fusace ya ce" In ji wa yace ba lalatace bane? Ya rasa wa zai ce yana so sai ke?, To zan kore shi na ga a inda zai ganki! Walahi ki kiyayeni Muneerah bana son shirmen yayume yayumen nan, ki bari idan na maida ke garinku ki kula maza dari ke ta gano ! Aman ba zaki bata mana sunnan gidanmu ba!"

Haushi ne ya shiga turnuketa, idonta ya fara rufewa dan fa ta tsani fa ya ringa nuna wani in ta je garinsu ta bude baja kolin iskanci, hala bai ga yaya tarbiyar nasu garin yake bane ko meye?
Bakinta ta tunzuro ta bi ta kasan hannunsa ta juyo ta ce" wollah ka ji tsoron Allah, wajen cin abincinutun dan ka raba shi da shi ribar me zaka samu? Koma lalatacen ne ina rayuwarsa ce? Kai dai sai dai ka ringa korar mutane kana masu fada ba gaira babu dalili? To ai kaima da Allahn ya baka ba dan ya fi sonka a kan sauran bayinsa bane! Idan ka kore shi ai Allah zai bashi wajen da ya fi wannan, kuma da kake cewa ka maida ni garinmu na yi maza dari ai ni ba yar iska bace ba kuma yan garinmu basa yawo da bingilin sket basa lalata a bayane dai ehe! Kuma Allah na gannin mutun, ni a maidanima na koma gaban Oga !"

Ido da baki da hanci gaba daya ya bude yana kallonta hakama Iman dake tsaye jikin kofarta ta leko ta ya kofar nan ta saki baki da hanci tana saurare

Da ido ya rakata har ta kusa shiga kafin ya zarro ido da ihu ya ce" Muneerath dawo min nan, zo min nan yanzu yanzu!"

Muneerath da ta saka kafarta daya a dakinta ta makale kafadarta tare da turo baki ta shige dakin ta turo kofar tare da murza ky tana fada a bayane cewar" Haka kawai ka ringa wani cewa zaka kori mutun ka kore shin mana, kaima ai sai a kore kan malan!"

Saudat da ta gama saka takalminta a tsorace kar zata fashe da kuka ta ce" Muneerath ni dai ki raka ni na koma dakinmu na hostess na fasa kwanan a nan, yanzu Muneerath bakya tausayin kanki kika yiwa Hanja haka? Zai hada har ni ya kora saboda wannan abin da kika yi, yanzun so kike ya kashe mu ?"

Munnerath ta yi turus tana kallonta, tsakani da Allah saudat kuka take hakan ya sa ta fara tunanin to wai meye na tsoro a jikin Hanja?, Ita walahi hargaginsa da daure fuskarsa du basa ce mata komai, a gidansu meye babu? Akoy mafadatan da asubar fari suke farawa basa dainawa sai duhun dare, akoy kuma wanda idan mutun zaku kashe ba zai kale ku ba dan bakin hali, au dai bambancinsu ba shiga sabgarka zasu yi ba idan suka shiga kuma a fito a caskale ne a ba hamata iska!, Shi kuma sai yana nuna ya mayar da ita kasarta ta je ta aikata abubuwa kamar wata yar iska?

Gwuiwa a sage ta ce" Saudat kali fa, to ba shine ya fara jana ba?"

Daudat ta dafe kunci ta ce" Baki da hankali?, Ko me ya maki ai daidai shine ko?"

Munnerath ta tabe baki ta ce" Ba inda zaki je, idan dan ina gidansu ne za yana wulakantani ai zan samu Mah na ce a maida ni ni na gaji ya ringa min fada dan ya ga kato ne shi !"

Hanja kam abin gaba daya fin karfin tunaninsa ya yi hakan ya sa tana kulewa ganninsa a haukace ya nufi matatakalar gidan da rabonsa da hawa ta nan har ya manta ya shiga tatakawa da gudu gudu yana bale boturan rigarsa domin ji yake kamar ana zuba masa ruwan zafi, gaba daya ji yake kamar zai summa, bai san meye wannan ba, bai san me ke damunsa ba, abinfa dai ya sani shi da Attahir Allah ne kawai zai raba su, baya gannin laifin Muneerath dan ita yarinya ce yana iya koya mata yadda zata wulakanta shi, aman shi malamin shi zai samu ya koyawa hankali, ba zai lamunci wannan haukan ba ba zai iya ba

Nan da na ya sauko daga sama wanda hakan sai da ya tsorata Mah dake zaune rike da result dinsa wanda basu samu komai da ya shafi zazabi ko wani ciwo a cikin jinninsa ba, jira dai sule su auna bp dinsa da matsalar zuciya dan su ga abinda ke saka shi bugun zuciyar nan

Gaba daya suka mika Banda Pah da ya kuma tsura masa ido

Wajen t□l□phone ya karasa ya dafa wayar ya shiga dadana number office din PDG na a□roport

Nan da nan aka daga
Hanja da ya murza gaban goshinsa ransa bace ya ce" Ka duba sunnan Attahir lawan ka ga me kampani ke binsa ko yake bi"

Da sauro mutumen ya shiga dubawa, daidai Pah ya taso ya karaso wajen wayar ana fadawa Hanja

A hankali ya saka hannunsa ya janye wayar ya kanga a kunnensa ya ce"
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 7 □□□

"s ok" kawai ya fada ya ajiye wayar yana mai tsatsare Hanja da kallo

Shi da kansa yanzun kuma sai tausayi da kaunar yaron nasa ke neman hanna masa kwashewa da daria,
Mah har ta fara sharar hawaye dan yannayin nasa baya mata dadi gata dama mai kuka a kusa

A hankali Pah ya ce" Me zaka yi?"

Hanja da ya cije lebensa yana kallin Pah a kan me yasa ya kashe masa kira ya buda bakinsa da kyar ya ce" Korarsa zan yi!"

Pah ya mika hannunsa a hankali ya kami na hanja ya nufi wajen kujera da shi bayan ya yi alamu kan a basu waje hakan ya sa kowa ya yi gagawar kama gabansa

Zama ya yi yana kallonsa a hankali ya ce" Cire rigar"

Hanja ya Kali rigar jikinsa ya ga har zufa ce ta wanke masa rigar fa, a hankali ya cireta yana jin kansa na sara masa ya lumshe idannuwansa a hankali ya kuma sada kansa

Pah ya sauke ajiyar zuciya a sanyaye ya ce" Ba'a yi masu garaje su, baban damuwar idan suka yi niyar rike wuyan mutun komai tsufansa, kudinsa, mulkinsa, takamarsa,

gatansa sai ka ga ya dawo yana walagigi kamar mai shan giya bayan shi din ba dan maye bane, dayar matsalar kuma itace ba kowace mace ihu ke tafia da itaba, ba kowace kyau, kudinka, ko isarka zai sa ta yi flln a soyayarka ba, Watan kamar da wasa sai ka ga kaine sarkin an kuma sai ka mata fadanci, watan ta fi lu'u lu'u daraja , irinsu ne idan ka kilace su ka gama samun nutsuwar duniya ka mutu kuma ka tarda alkhairi domin sune masu kaika ga aikata alkairin da zaka shiga aljana gibe kiyama, matar kwarai itace abar alfahari ga namijin kwarai"

Hanja kallon Pah yake, gaba daya zai iya cewa a baibai yake daukan maganarsa baima gane ina ta dosa ba dan haka yake dan murza hannunsa so yake a gama masa nasihar ya tashi shidu gani yake idan ba balbalin balaki suka yi da yarinyar cen da wancen ciki caka din ba ba wani sauki da zai samu na rainin wayon da take masa

Pah ya ce" da yawa na rasa abinda suke so dan sun kasa gane meye suke ciki da zuciyarsu, da yawa na afkawa da fada da kokawa har su bata rawarsu da tsale, Hanja shin ka kuwa ga abinda kake zama a gabanta? Famanka ka kai mata duka bayan idan ta jigata kaine zaka fara hakacewa, so kake ka mata ihu maganarka ta girmami tata karfi da yaji bayan a ruwan sanyi take soyeka tsaf a tanda, kali fa yarinyar nan jikinta ne ya debeta domin ko kiriniyar masu shekarunta bata da ita dan a milieu din da ta mike bata san haka ba, me yasa kake neman nesa bayan ga amsa a kusa da kai?, Sai an maka ruftawar da kudinka ko mulkinka ba zai hanna ka kwonta a gadon asibiti jinya ba sannan zaka ankara ka farka ka farga?"

Hanja ya sauke ajiyar zuciya a hankali yana kallon hannayensa , sannu sannu ya shiga tariyo abubuwan da yake yi a gaban Muneerath, walahi sai wata kunya ta nemi hanna masa hada ido da pah, sai dai ba zai yi haka ba zai hada ido da shi ko dan ya nuna masa cewar bafa abinda yake tunani bane ba fa, haba meye yake damunsa haka ne? Dole ne iyayensa su yi tuninin da ba shi ba a kansa, yanzun tsakani da Allah meye hadinsa da yar nan da har zasu ringa yi masa irin tunanin nan? , A nutse bayan ya mayar da bacin ransa a lokacin da ya gama gannin a kan mema zai wani damu wai? Ya ce da pah yana kokarin mikewa ya dan dafe gefen cikinsa rike da rigarsa ya ce" Na rasa macen so sai wannan? Ban taba yin facing din fitsarariya irinta shi yasa nake samun kaina a irin wannan yannayin, aman gabanan zai kasance tsakanina da ita relation ce ta yaya da kanwa a cikin gidan nan kamar yadda tsakanina da Iman yake, idan mun fita wajen aiki kuwa zan kasance uban gidanta a abinda ya shafi aikinmu ,ba sai na kawo maku karar ku mata maganar bane har zaku yi wani tunanin a kaina ba? "

Pah ya rakashi da kallo kafin ya yi murmushi a ransa yana ayana 'Allah ya takaita maka wahala a game da makauniyar soyaya, ban san ko zan ga karshen wasanka kai da Muneerath ba? Ko sai dai na gani a gobe kiyama?'.....tunanin mutuwa bai taba barin tunaninsa ba koda kuwa likita ya fada masa da sauki jikinsa da waye waye, ahi ya tabata saukin a wajen Allah yake, kuma idan mutuwar cema saukin *Alhamdulilah* .

Kamar da awa daya tsakani sunna hade a falon Mah gaba daya yan matan inda a zaman hirar ta Muneerath ce kawai sai saudat da bata gama sakin jikinta ba da take yar dariya, sai Iman dake kwonce tace kanta ke ciwo bayan ta gama shan maganin da ba ciwon kan bane sai cinkushewar tunani, sai Mah dake biye da hirar tasu, kira ya shigo t□l□phone din a nan ne ake shaidama Mah likita ce ta zo wai an ce ta zo ta duba jikin Muneerath dake da zafi
Da dan Mamaki Mah ta tambayi bata da lafia ne? Wa ya ce?

Amsar da aka bata ne wani tausayin yaron nata ya karra tsarga mata, shin yaya zata yi da gardamamen yaronta da Halayan Muneerath mai wuyar fasara da abansa da ya nuna ba zai takura yaran ba? Yaya zata yi ta taimaki y'ayan nata?.....bata san yaya suka kare da Pah ba hakan ya sa ta mike dan nufar bangaren Pah domin ta san yanzun ya koma dan ya huta kafin yama su hadu su yi yar kwrya kwryar birthday din yaron nasu wanda du yadda zasu kai da kin son gayatar mutane sai manyan kusoshin kasar sun halarta.....(Biki na manya kennan □□)

A wannan rana sai hakura familly din masarautar suka yi da son yi masa dan clbrt din zagayowar ranar haihuwarsa domin a lokacin da suka kuma waiwayarsa dan yin hajan gaba daya baya gidan

.....
Bangaren Hanja kuwa yana gama abubuwan da zai yi a gidansu ya zauna da computersa a gabansa ya gama latse latsensa duda gaba daya yana yi ne kawai irin basarwar nan dan kar ka afka cikin tunani har kira daga wajen likitan da ya turawa mesage dan irin yadda jikin yarinyar nan koda yaushe da dumi ya same shi cewar lafiyarta kalau haka yannayin jikinta yake sako daga Mah dinsa sai kawai ya kure waje daya da kallo

Cike da takaicin kansa da gannin kamar mema ya kaishi aikata hakan ya saka shi dafe gaban goshinsa yana mai tunanin shin me yake damun tunaninsa ne?

A hankali ya girgiza kai shi kadai yake ba kansa amsar shin so yake Pah da ya gama dora masa abinda ba haka ba ya yarda da hakan harma ya yi convncng din Mah a kan tatsuniyarsu? Yanzu fisabililahi yau yake yin yan mata su yi soyaya? Ana so ace du soyayar da ya yi bai yi ta cikin zuciya ba irin bai yi soyaya ba shirme yake yi sai yanzu ya hadu da abin sonsa tamkar shirin film?, Idan ya kula iyayensa sun hau kan maganar da suka gama yankewa cewar shi Hanja wai yana son yarinyar nan?

Dan murmushi ya yi yana Girgiza kansa cike da takaicin kansa da kansa, shin sun manta waye shi?, Ya rasa ina zai harbi sai afrika kasar Niger?, Ya rasa wace zai kyalo sai Hostess masu rabon abinci da murmushi wa ppsnger?, Ya rasa wa zai so sai wannan mai rainin wayon?, Shin sun manta a irin kasar da suka daukota su da kansu burinsu su mayar da ita lafia?,

Dan kyaci ya yi yana murza hannayensa tare da kuma girgiza kansa, sai ya ba kansa amsa cewar ai koma me za'a yi tunani da kai Hanja kai ka janyowa kanka, duba ka ga yadda kake daga murya da kwonji kana zakalkalewa a kan maganar yarinyar?

Yana cire dogon wandonsa na pilot yana jin yadda ya ba kansa amsa ya girgiza kai tare da hade rai sosai yana mai ayana' tabas laifina ne, dole a min gurguwar fasara, basu san cewar aiki da jirgi bai haukatani ba, ina haka ne dan na kareta daga irin namu mazajen masu dukan du macen da ta wangale kafa su tsalake su manta da ita tamkar sun shiga injin sauke nauyinsu sun sauke sun biya an wuce wajen ne, yana gudun kar a bata tsoron da idan ta yi wata sumar ba zata farfado ba, aman ya yi haka daga yau ba zai taba daga dan yatsansa dan yin wanni abin a kan hakan ba, zai karyata tunanin dukan wani mai tunanin wai wai shi Hanja .....' sai kuma ya danne lebensa na kasa yana girgiza kai da dan alamun abin shi yanzu nema ma yake ya bashi dariya
Sai kawai ya yi wankansa ya saka sasaukan kayansa ya amsa a gagarumar shirin birthday dinsa da yarinyar yar gidan ministern kasar kuma dan kasuwa ta shirya masa duka a kan idasa nufinta na ta ganar da shi cewa baban goro sai magogin

karfe, du wata mai rawar kan son ta nuna kanta a lamarinsa takan motsa dan yatsarta ne ta bata shawarar kaucewa ko ta kawar da ita ta kowace hanya domin ita a ganninta ita ta fi cencenta amsa kiran sunnan matar sarkin garinsu duba da cewar idan kyan ne ta samu, nasaba tana da kyakyawa, dukiyar ta wanke kafa a ciki ta yi asuwaki da kafar kaza, iyayenta sun bata goyon baya to fa bata tunanin akoy wai shamaki da ya dara nasa wanda a kadan a yanzu ta kusa shekara tana kara yada masa manufarta aman cikin ikon Allah tamkar kurma kuma bebe a yarenta, dan ko hannunsa ta rike sai ya bata umarnin saki bayan ta san cewa a yana musulminma su musulman da basa harkar mara shi yana taba abinsa, domin tsaf ta san waye shi kafin ta ji cewar du duniya babu namijin da zai iya da ita face shi

Tabas ya ga shagali, shagali irin na yayan gata irin na yan gayu, shagali wanda ya amsa sunnan shagali , an cushe hanyar yan jarida dan yanuna baya so, haka kuma an lamarin kida domin ya kwatanta idan ya yi karfi kansa na iya ciwo hakan ya sa jarumarsa mai begensa ta soke maganar kida duda ta ci burin taka rawar salsa da shi tare da shi a jikinsa ko dan ta shaki kamshin turaran nan nasa dake haukata tunaninta

Mutanen da aka gayata manya ne, girmansu bai hanna masu shagalta da kallonsa ba
,
Yar budurwar kyakyawa ce, kyawunta bai hanna mata shagalta da kallonsa ba
Shi kuwa a zaune yake yana mai bin mutanen da kallo fuskarsa ba annuri, yakan so ya yi mamakin lamuransu sai dai yana turewa duba da kowa da irin yannayin rayuwarsa

Abinda ya so ya gani a cikin taron duban yan matan wajen nan shine dan tudu kafin a kawo gangare, Ba zaku gane ba, kowani dan adam da irin nasa bukatar wace da ace zai wuni ya kwana yana cikinta ba zai gajiya ba, wani zaka ga a duniya idan ya ga kalolin gidaje yana iya bata dogon lokaci yana aprct koda kuwa ba zai leka ciki ba, wani burinsa ya wayi gari ya ga manyan motoci, wani shi a barshi a bangaren cin abinci, wani kuwa abin sha'awarsa ya gayara kanana na wasa.....hakan ta kasance da HANJA wanda yake da nasa son bukatar.....shima mutun ne tamkar kowa shi yasa yake tsintar kansa da zabi irin na cikin zuciya, sam sam sam ba maganar kawo bakuwar gidansu mai hali irin na yan taure bane, ko da cen a zuciyarsa yakan so ace idan zai yi hayar abin hawan nan ya samu mai kosashen tudu kafin a zo gangare, sai dai abin mamaki sai yake gannin wasu yan tsatso tamjar na saurayin kare mai yinwa, sai da ya sauke dubansa a kan nata tsatson ita mai shirya masa yar kwarya kwaryar birthday din nasa, wace ya gama gane me take nufi da lamuranta cewa soyaya ta aure take masa ba wai ta a yi na dan lokaci a watse ba, a lokacin ya afka wani tunani daban, sosai ya ringa aunawa a ma'auni kafin ya samu kansa da dan girgiza kai yana tunanin duda abin baiwa ne, kuma masana sun ce ramamiyar mace mai dan kwonkwaso ta fi daukan abin du girmansa baya tunanin idan wannan dan tsatson da ya tabata abin nasa ya kai shi girma zai wani iya da shi,
To shi tsakani da Allah me take so ya mora a zamantakewar? Saman tamkar sabon fitowar lemun yami irin kananun nan ba masu girman nan ba,, gashi kuma shekaru sun rigaya da sun ja bale ya yi tunanin yanzu aka fara girma zuwa gaba zasu iya fitowa
Gashi shi da Allah ya haliceshima baya son irin na gyaran docter ya fa fi son na ubangiji,
Bayan ne ya nuna alamun kamar akoy sai dai a yanzu da suka fi kunacewa junna waje a wajen zaman sai ya kula da irin gyara zaman rigar da take, kai da alama wando mai ciko ne a ciki

A gaskiya, yana da burin aure, aure yake nema kamar yadda iyayensa suke so ya yi, zai yi a kwana kusa , sai dai dalilin da ya saka shi zama a wajen nan har ya jima sai

dan ya ga wata mai tafia daidai da nasa ra'ayin, dan ya tabata yan matan garin masu ji da kansu kawayenta ne , kuma zasu halarta, idan ya ga matar aure yar ingila sai a gama komai kawai a shafa fatiha

Dukan wannan lamari yana dan hira da zuciyasa ne
A bayane kuma gashinan zaune ne a saman hakimtaciyar kujerar da aka tanada domin shi sarkin kasarsu ttb, aka kawata da kawatacen cake da manya manyan jus na kasa da kasa, aka gabatar masa da mutanen kasarsa masu fada a ji da y'ayansu
Ya kuwa gimtse ya hade ya ja zarensa na baba ya ki sakin baki dan yi masu daria kamar sabon kamu, ya kuma bada kala ta baban yaron da yake, yana mai hankalce da takun kowa inda dogaren masarautarsa watau Bodyguard sun cika wajen sunna ta kukutsawa a cikin shiga ta bada kama domin suit ne a jikinsu tamkar ba aikin da suka fito yi kennan ba kakarfa da su sunna aikinsu na baiwa uban gidansu tsaro ya manta da yan gidansu da suka shaka karshe dai ska baje tafkeken cake din a tsakar falo inda yan matan sukai masa barin mahaukaciya suka yanka abinsu Mah na daria tana daukan vidio dinsu irin shirmen da suka ringa yi sunna tikar rawa da daria abinsu , da dan fadace fadacensu da shiri a nan take har sai da ta gama vidion inda ta fi daukan Munnerath bisa nata niyar da take yin abinta ita kadai tana gamawa ta zauna ta tura masa tare da mesage din Happy birthday tana dan murmushi a kasan zuciyarta tana ayana 'Son, in ka san wata, baka san wata ba'

,..

Mah □□

.....
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

4 □□□ 8 □□□

Sai da suka gama, suka gaji dan radin kansu sannan sukai mata salama bayan ta kara tunatar da su cewar idan sun shiga su tabatar bayan yin wanka sun daura alwallah, sannan kar hira ta shagaltar da su har su cika dare dan kar su kasa tashi sallar asuba a kan kari, sannan kar su manta da adu'a kafin su yi barci

Har sun kama hanyar tafia Mah ta bukaci kan Muneerath ta bata wayarta zata yi wani abin da ita
Ai kuwa da murnarta ta bata suka yi tafiyarsu ba tare da tunanin komai ba

A wannan daren bayan Mah ta gama kula da mijinta wanda tafiyar gagawa ta taso masa du yadda ya so ya kaucewa tafiyar hakan bai yiwu ba aman sai ya nemi alfarma a wajen matarsa kan ta boyewa Hanja domin ya tabata idan ya sani zai fito kai tsaye ya hanna ne,
Ita din da kanta ta samu kanta da yarje masa ba fan komai ba sai dan tana matukar jin dadin irin yadda yake dan haba haba da jikinsa da lokacinsa bayan a da ya zubar da komai maganar fatar bakinsa daya biyu zancen mutuwarsa ne, duda ta san haka din abu ne mai kyau dukan musulmi ya kasance ya rayu da sannin yana iya mika ran aro a kowani lokaci, a kowani lokaci sai dai kuma mugun zurfafa tunanin mutuwar na iya hadasa cuta, hakan kuma na iya kasancewa cutarwa ga bawa domin da ace hakan ba komai bane da Allah bai boyewa bawa ranar mutuwarsa ba sannan da bai saka hijabi a tsakanin mala'ikan mutuwa da dan halita ba
Dan haka ta bashi dukan kulawa ta yi masa rakiya har wajen motar da zai bi boyayiyar hanya ba tare da media ta san da fitarsa ba sukai kyakyawar salama ta dawo cikin dakinta

Kai kawo ta ringa yi a baban falonta da byro a hannunta tana dan wasa da shi ta hanyar juya shi a hannunta

A hankali ta kai zaune saman bed ta mika hannu ta dauko wayarta cikin nutsuwa tare da ta Muneerath wace ta amsa
Number ta dauka ta kwafa a wayarta ta danna kira tana mai kai dubanta wahen agogo wace ta nuna mata karfe kusan biyu ne na dare, sai dai ta tabata wanda ta kirayan zata same shi koda a karfe nawa ne, kuma bata tunanin zata iya rintsa idannuwanta idan har bata daidaita wannan abin ba

Ba ita ta kwonta ba har sai da ta gama komai kafin ta dauro alwallah ta taho saman bed dinta tana mai adu'aa dukan motsinta ta haye saman gadon

A hankali ta rintse idannuwanta sakamakon murdawar da cikinta ya fara yi mata

Sannu a hankali ta ringa adu'a a irin tsugunin da ta yi a saman gadon tana rike da hannunta tana beman sauki a wajen ubangijinta wanda ta tabata shi kadai ke kawo mata agaji a irin wannan ciwo nata
Ciwon ciki ne da take yi , wanda yake taso mata wani sa'in sai ta kusa shekara biyu bata yi shi ba
Wani irin ciwon ciki ne dake gagabowa tun daga mararta ya yi sama gaba daya ya rikitata ya yi ta juya mata ciki tana birgima du hakurinta da girmanta kuwa, da jyar yake sakar mata amai kafin ta samu zuwa bayi ta zubar da datin dake taruwa wanda yake bata tsoro a dukan lokacin da ta samu yinsa domin shi ba gudawa bane sam, hasalima tauri ne da shi kuma ba tare ba, haka dai take fitar da shi mai mugun warin dake juya mata kai

"Hasbunnalahu wani'imal wakim" shine abinda take maimaitawa tana kallon agogo gannin har hudu ce ta gota ta tabata a yanzu Son baya kusa ita kuwa du abinda zara

tsinci kanta a yanzu ba zata iya kiran mijinta da ya fita dan hidimar kasarsa ta dawo da shi ba, haka kuma ba zata kirayi Iman kururuwar iblis ta tara mata jama'a ba
Hakan ya sa a hankali ta ringa murkususunta tana ambatar sunnan Allah tana karra gyara daurin dan kwalin da ta dora a saman doguwar rigar barcinta fara mai dogayen hannu mai laushi domin sam bata wani lafe mata a jiki ba

Wankin hula ne ya nemi kaita safe, tun Mah na gane yaren ciwonta har ta dawo ta fita a hayacinta, har lokacin salar asuba ya shige bata san inda kanta yake ba bayan ita din mace ce mai bi kofar du wani yaronta da ya kwana ya wuni a gidan ta tashe shi sallar asuba , dan kuwa ko anfani da waya bata yi ta fi gane ta je da kafafuwanta
.....

Jiki mai rike abin sabo ya maimaita shi da karfin gwuiwa, sabawa da ta yi da tashin asubar ne ya sakata tashi a kan lokaci harma ta tashi Saudat suka daura alwallah suka gabatar da sallah bayan sun yi wanka domin tsaftar nan ta Muneerath ita kadai ce abinda bata taba barinta, tsafta akoyta ta jikanta da kuma mugalinta, du inda zata zauna koda na minute daya ne sai ta yarda da tsaftarsa

Bayan sun gama sallar suka gaishe da junna

Shiru Muneerath ta yi tana duban agogo kafin ta kalli Saudat dakr Hamma ta ce" To yanzun ai ya dace mu bashi amsa ko?"

Saudat ta katse hammarta tana dan zarro ido kafin ta yi yar dariya tana talabe kumatunta ta ce" Anya kuwa sir mai sanyin haki zai iya da rigimarki?, Kin san menene idan har bai zama kazar kazar ba ina tsoron ki mayar da shi solofiyon namiji"
. Muneerath ta yi yar dariyar itama tana cire hijab dinta a hankali ta shiga dan motsa wuyanta kafin ta kwonta ta ta shiga dan motsa kafafuwanta tana jim na sasafe da take dan yi dan ci gaban rike lafafen ciki kamar yadda aka koya mata ta yi murmushi a karro na biyu ta ce" kin san menene?, Attahir na nunin shima wani zaki ne, harma ya ce zai iya saka rigar dogari dan na so shi.....wannan wasan da ya buga ya saka ni a tunaninsa.....aman;;;;;;;;;;;;;' ta dan yi shiru tana kikifta ido alamun wani tunani ne ya shigo kwakwaluwarta hakan ya sa saudat tabo hannunta tana fadin" Aman me?"

Muneerath ta yi murmushi ta juyo tana kallonta ta ce" Ni fa bana tunanin idan har namiji laso laso zai iya rayuwa da ni lafia, kin ga meye anfanin namiji idan zai maka magana sai ya sanyayar da murya? Ni fa gani nake to wane ka bara min kennan? Kin ga aka ce mace ita ce yar kwalisa, yar sanyin murya, yar lalashi, yar yar yar yar....., Ki duba ki ga Attahir idan zai yi magana fa fari yake, na taba tambayarsa ko ciwon idannuwa yake ko kuma haka aka haife shi ne? Sa ce min ya yi aa wai akoy abinda ke saka shi cikin shauki irin haka, shi kuma haka Allah ya halice shi bawan Allah"

Wata irin daria ce ta kubcewa Saudat har tana rike ciki a saman salayar tana kwonciya, ya subahannalah wai shin wace iri ce Muneerath ? Yanzun yana mata irin kashe idon nan dan ya saka ta afka a soyayarsa wai ta masa tambayar ciwon ido yake?

Bata karasa wannan ba Muneerath ta girgiza kai tana zama ta mayar da gwuiwar hannayenta baya ta gyara kwinciyarta ta daga kafafuwanta kadan ta tsayar da su tana ta sauke ajiyar zuciyar wahaka dan wannan yana bata wahala duba da

mazaunan nata idan ta yi haka wani bajewa suke abinsu ta yi murmushi ta ce" Allah ya daina baki daria wannan abin, to sai na ga ni me namijin ya bara min dan Allah?, Haba ai ya dace nakiji kawai ya kasance mai kaza kaza,mai balaki da tashin hankali, dan rikici na mamaki, wanda idan na masa zai daga ni sama ya nunawa shirwa ni ya nana da kasa.....a haka zan fi jin tsoronsa, ke ogama cewa ya yi wai akoy kura wai kawai in ya kula ni din wannan an so a yi tabi tabi sai dai aka gyara min aka zari hamsin a dari, wai a haka zai barni ko dan idan ya min aure ya ci daria, dan ya san wai ko a yadda idan namiji ya ce irin wai ina da ko manyan kaya ko me? Nake fada masa in ce masa ya daina dinka min manyan kaya, ke ni dai da abin ya ishe ni sai na koma siyan gwonjo da kudina na kari, yo shi kamar wada ya tsane ni a cikin y'ayansa kulun kulun sai ya sa a min baban dinki, mai dinkin nema munafuki sauran ai dinkin motsa da karfi ka yage yake masu sai ni yake yiwa buhu dan kawai an tsane ni"

"Innalilahi" shine abinda Saudat ta fada tana karra wara dubanta a kan Muneerath, walahi ita bata taba gannin mutun mai faranci irin Muneerath ba, yanzun babanta take cewa an ce tana da manyan kaya? Haba haba dole ya ce an zari hamsin, kuma tsakaninta da Allah ne take maganarta ,
Sai kuma tausayin Muneerath din ya tsargun mata a zuciyarta, shin menene musababin wannan hali da take ciki? Munnerath bata taba zama ta bude mata sirrin cikin gidansu ba, idan ta kamata wani sa'in tana hawaye ko ta zurma a tunani idan ta tambayeta ba'asi tun tana ce mata ba komai har wani lokacin ta fashe da kuka ta dora kanta gefen kafadarta tana fadin Saudat, kin ga fa iyaye ne da ni, da ransu da lafiyarsu, idan na ga asabar ko lahadi ta gabato na ga iyayenku na kawo maku ziyara, wa'inda suke nesa da kasa sai na ji zuciyata ta tsinke, shin wai anya baki daya y'ayan gidanmu su suka haife mu?, Sam basu damu da mu ba, mahaifiyata na raye ina nan bata neme ni ba, shin me yasa ba shakuwa ba soyaya sai kiyaya nake karanta a tare da su?, Idan kina so ki ga ana sonki a gidanmu tabo fada a waje yanzu zasu ringa yiwa kansu kirarin su an gwada masu rashin mutunci? To wannan fa an tabo waje watau zasu nuna maka su din sun iya masifa mai sunna masifa wace bata da hadi, abin bakin cikin ba dan a nuna maka kauna ake maka hakan ba, sai dan a nunawa duniya in masifar take nema ta tardo gidan, shi yasa ni bana kai masu fadana, idan na ga an fi karfinama sai in yi Allah ya isa walahi,.....aman abinda yake bani mamaki Saudat shiru ba Oga ba Mamanmu ba kowa nawa harda shi mai son na yi karatun ko bai san bana gidan bane?

Daga wannan ranar ta ringa yiwa lamarin Muneerath uzuri, daga nan ta ringa fahimtar dukan wani abin na gabonci, irin na mamakin nan idan Muneerath ta aikata daga mahaifiyarta ne, iyaye mata sune masu koyar da y'ayansu lamarin rayuwa, uwa mahaifiya ita ce zata bambancewa yarta komai , ciki kuwa garda karatun da ake basu a rufe a islamiya, yawanci malamanmu ba zasu fito maka a mutun dan su ganar da kai wane ake nufi ba, hakan kuma ya dauko asali ne daga irin yadda y'ayan na yanzu kyar sun san me ake nufi dan an basu magana a rufe to fa tabas sun san ina ta nufa sai dai a kalli junna, aman kuma sunna mance cewa akoy masu hali irin na Muneerath, inda Allah ya taimaketa ita Muneerath din, ya kasance yarinya ce mai masifar tsoron harkar D'a namiji, kai ko fadan fa Muneerath ba wani karfi ne da ita ba, ita dai barta a wajen harkar kin tsoron waje, kai magana fa idan ta yo niyar fitar da ita fitarwa take ko a gaban waye!

Munnerath da ta mike tana juya kugunta shima duka a cikin yannayin dan motsa jikin da take ne ta dakata da sauri ta ce" Ke ban fada maki abinda Mah ta ce ba, ta ce walahi talahi du yarinyar da ta yarda namiji ya zo mata sai ciki kawai, na ce wai wani iri sai Mah ta ce ko hannuna na yarda ya taba, kin ga yaron nan nata ko? Sau biyu yana rukunkume min jiki, dan Allah dan na tsorata na yo wajenka ai sai ka wankan mari na ankara namiji ne kai, sai kawai na duba da kyau sai na ganni a

jikinsa, Allahma ya sa Mah ta ce sau biyu kawai ba abinda zai samu aman ina yarda na uku ya faru an kare"

Zuwa yanzu tsakani da Allah tausayin kawar tata take sosai , duda idan ta dauki wani wajen kasantuwar Muneerath a haka shi ya fi daidai da rayuwarta duba da irin kirar da Allah ya yi mata da ace ita din mai kwaramniya ce da maza sun gama sukuta a kan dokin nan nata sun kara bude shi ta yadda zata zama dokin yan duniya, domin namiji karya kake ka ce zaka iya zagaye shi, idan ka ci riba a kan wani, a kan waninsa ba zaka kai labari ba, sai dai kuma idan ta bi wani bangaren na idan fa akaiwa Muneerath aure aka kaita a haka mijin ya nuna manufarsa da abinda zai kai hannunsa wanda ya zarce runguma za'a kwashi diyan kallo, may be ta sume masa ta yadda ba zai iya anfani da ita a haka ba, ko kuma ta haukace gaba dayama da kuka, ko a zaman gidan horon Hosteesss da suka yi irin tsakaninsu yan mata wani lokacin baka jin kunyar cire rigarka ka saka wata a saman bra dinka, ita bata taba haka ba, saima kowa ya bar dakin take cire nata kayan a labe ta cenza, to ina da namiji ya ce ga abinda zai taba?

Kallonta take tana ta kokowa da tunaninta, shin ta sanar mata abinda yake faruwa asalin meye yake iya faruwa da ita a lokacin da ta auri namiji ko kuma ta barta idan aka ce yau an daura aurenta koda tana nesa ne ta sanar mata? Ko kuma a yanzu take zaunar da ita ta yi mata ainahin karatun fari fari ta yadda zata san me ake nufi da kalmar *YA ZO MIN?*

Tana kallonta ta ce" Muneerath zauna mana mu yi magana?"

Muneerath ta juyo ta ga yadda Saudat ta yi kala irin na serieus tana kallonta watau jira take su yi magana da alamu mai mahinmanci ce

Kokarin zama take aka yi knowkng din kofarta

Da sauri ta juya tana murmushi ta ce" Yau dai Mah ta makara, kin san tun dazu idan na kalli agogon cen mamaki nake har yanzu shiru? Mah ba dai sabko ba yau ta makara zan kuwa yi mata daria na ce Mah na yi sallahta a kan lokaci, ian zuwa Saudat sai mu yi maganar"

Tana fada ne tana karasawa ta bude kofar
Abinda aka fada mata ne ya rikitata, ko dakatwa ta yiwa Saudat magana bata yi ba ta shiga bin Likitar doctern mace suka nufi ainahin asibitin dake Palas din wace take nan domin kula da lafiyarsu
Har gani take sun kasa karasawa duda a mota aka dauketa, gaba daya ta rikice Tambaya take yaushe ? Wa ya kaita asibiti ? Pah ya dawo ne? Kwata kwata Muneerath ta manta shigar dake jikinta ta kayan barci na roba masu bin jiki masu kananan gannaye kanta kuma ba hula a kame a tsakiyar kai sai takalmin dake kusa da bed dinta wanda yake kafarra wanda Mah ta hannata taka tiles din gidan nan ba takalmi, sai farar safar dake kafarta wace yanzun saka safa ya zame mata jiki sam bata zama ba safa a kafarta

Tambayoyi take ma likitar tana bata amsa har suka isa suka fita

Iman ta ganni zaune tana hawaye hancin nan ya yi jajir hakan ya sa gabanta ya yanke ya fadi da gudu ta nufi iman tana tambayarta ina Mah din ne? Ko ta mutu ne take kuka haka?"

Rai bace ta mata nuni da dakin da manyan dakarun sojoji ke tsaye wa'inda ita bata taba kula da su a gidan ba wa'inda har ga Allah sai da ta ji gabanta ya fadi na tsoronsu da ta gansu , aman da yake a yadda iman ta fada mata bata mutu ba da haushi ta ce" Shine kike yiwa mutane kukan iskanci a nan, ki yi mata adu'a mana Allah bata lafia haka kawai ki saka ni faduwar gaba karfe tara na safe ko karyawa ban yi ba?, "

Sai kuma ta sasauta muryarta ta ce" Iman dan Allah raka ni mana na ganta wa'innan na tsayan da alama basa son iskanci, kin gansu kar na he su mareni su kurumtani kin ji?"

Iman ta kauda kanta tana gunguni da tunanin lale Muneerath ta raina mata wayo, Bodyguard din na HANJA na dare ne bata sani ba? Mutanen da idan dare ya yi ko Pah basa bari ya shigo kai tsaye bangaren Hanja sai sun tabatar da Pah din ne ita da take tafia da shi kusa da kusa har sunna fada zata nuna bata sansu ba?

Munnerath gannin dibar akbarkar ta iman ta tashi sai ta kebe bakinta ta mike tana kade gefen cinyarta ta kale su ta yi adu'a ta nufe su dan ta tabata Mah na ciki idan kuwa tana farke ba zata so ace ta zo bata shiga ba, ta ga damar ana sakinta ta kama yi mata nasihar zumunci da kula da kwadaita mata lada a gannin marar lafia

Da ta tsaya a gabansu sai da ta raina tsayinta da kibarta, 'kamar yan tagwayen d'an Mah' haka take fada a zuciyarta

Sai da suka dubata da wani abu a hannun su har fuskarta da kyau kafin su bata hanya ta shiga , dama Iman ce ta bada umarnin a daukota domin itama da ta shiga ta tarda Mah a haka shine fa ta sanar da Hanja kafin ta sanar da likitocin , a yanzu da aka gama treatmen din Mah sai ta saka a kawota dan ta tabata idan Mah ta farka bata ganta a tare da su ba tana iya bata rai

Tunda Muneerath ta sanyo kafarta ya dago kansa daga zaunen da yake dare dare a saman bed din asibitin mai daukan mutun har biyu domin yana da fadi gaskiya ba irin matsatsen bed din nan bane , ya yi irin zaman nan kan Mah a saman cinyarsa hannunta kuma a cikin nasa , kanta sanye da hular mararsa lafiyan mai hade da kayanta, jikinta kuma rufe da bargo sai wajen fuskarta da kanta ne suke bude, ga dukan Alamu barci take yi

Da farko da dan karfi karfin tafiyarta ta shigo wajen, sai dai cikin ikon Allah daga bakin lokacin da ya dago da idannuwansa masu duhun haske ya sauke a saman fuskarta ya tsayar da dubansa kyam a cikin nata idannuwan da fuskarsa da ta yi ja, wace ta kula da zarar hankalinsa ya dan tashi daga fari tas sai ya dawo ja , sai ya zamana tafiar tata na rage sauri, har ta dawo tamkar an zare mata lakhah ne take neman tabulewa ta rufta kasa dan gaba daya sai ta nemi karfin jiki ta rasa kuma dan wani balaki ta ki cire duban nata a cikin idannuwansa har ta idasa kusa da su daf da daf tana mai kai hannunta na dama ta rike abin gadon dan ji take kamar wace ake jijigawa anai mata juwa , yannayi dai kamar na wace ta kurba bayan ita din nan ko goro bata ci

A hankali ta cire nata duban daga nasa dan ta kula HANJA mutun ne mai irin kallon nan da ake cewa ba kyau, watau haramtacen kallon nan da aka hanna a musulunci, irin kallon nan na a kafe mutun har a gano muninsa, kai in ba hanja ba ni kuma munina ai a bayane yake kau? So dai yake ya samu na cewa na masa bayan mamanshi ba lafia, koda yake ai aibun sangarta yaro kennan, sai mutun ya sangarta yaro yanzu haka kuka ne yake dan mamansa bata da lafia da ya ji motsina ya fuske, a banza bayan na gama sannin kai din dan akoke ne a gaban Mah da Pah'

A hankali kuma a lokacin da ta shafa gefen fuskar Mah ta ji ba zafi jikin ta kuma ga yadda take barci, ta kasan ido ta kuma lura da fa ita yake kallo walahi sai ta samu kanta da tunanin me yasa ya cika kallo?, Du abinta ta gane cewar shi din mai yawan kallo ne uwa namijin karuwi!

Dan neman magana irin nata, ba sam take mance shi din mai gigita rayuwarta ne sai ta samu kanta da yin kasa kasa da kuryarta sosai tana dan sata kallonsa ta kasan ido kafin ta dan gyara bakinta a hankali ta ce" Ka san cika kallo bashi da kyau a musulunci, a gayancema ba kyau a kurema mutun ido, ko kuma ka sani take sanin ne zaka yi mr HANJA?".....

Ku mu bata amsa sisters □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Barama ku ji, more cmmnt mr pstng ah tam □□□□

Kumama kumama ba edditing □□□□
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

Sarai kunnayensa sun jiye masa dukan abinda ta fada, sai dai ga mamakinta shiru tamkar ba kowa a dakin, hakan ya sa ta yi tunanin kawai bai jita bane dan haka sai ta kara gyara tsayuwarta sosai tana kara dan shafa gefen fuskar Mah da hannunta na hagu dake kusa da shi, da dayan hannun kuwa na dama tana dan susar gefen duwawunta irin na ka rasa me zaka yin nan kana neman fitinar nan a hankali ta ce" Cewa na yi cika kallo ba halayan mutanen kirki bane, kai kuma sai ka wani tsatsare mutun da ido ko me yasa kake haka? ?"

Wannan karron ma shirun ne hakan ya sa a hankali ta dago zarra zarran eylach dinta ta sauke dubanta a kan fuskarsa dan ta fara tunanin ko dai barci ya yi yana jinta tana magana ya wani shareta bayan ta san ba halinsa bane barin sai ta kwana?

Ga mamakinta kallon nata yake, kuma dai a yadda ta fahimta ba suma ya yi ba domin ai yana numfashi, hakan ya sa ta dan yi gaba kadan ta dawo, ta kuma yi gefe kadan ta dawo, gannin kwayar idannuwansa na binta ya sa ta kuma yarda cewa ba a sume yake ba

A kasan zuciyarta kuma ta ce' Na shiga ukunna , to ni yanzun yaya zan yi da shi kar dai ya fashe min da kuka a wajen nan dan mamansa ba lafia, to wai dama shi Pah yana zuwa yawo ne gashi sun shagwaba yaro sun barshi a gida bata da lafia zai haukace min? In ba mutane ba yanzun du kudin nan na Pah kuma yake neman wasu kamar wada zai shiga kabari da kudi?, Wani lokacin sai na kasa kasa gane son kudi irin na masu kudi walahi' a bayane kuma sai ta yi kalar tausayi tana dan kallonsa aman sai ta cire dubanta daga ta hada ido da shi domin sai kawai ta ji kamar zata kifa masaa kansa, a sanyaye ta ce" Ka yi hakuri ka ji? Ka ga fa cuta ce ai ba mutuwa ba kau?, Nawa suke yi sunna tashi mai lafiyar kuma idan lokacinsa ya yi sai ka ga ya mace murus har lahira ba wanda ya isa ya hanna, ka daina yi mata kuka ka mata adu'a ka ji? Kuka ba magani bane, idanma baka iya ba mu je na kokoya maka ka dawo ka ringa mata dan walahi ni din nan a islamiyarmu har jira ake na fara kira'a, yanzunma sauke mata kanta a samanka kali fa ai sai ta kage baiwar Allah"

Abinda ya gama sani game da wannan yarinya shine ba zata taba daina bashi mamaki ba, ya rab wai irin idan aka ga yaro na rigima na mamansa da ake masa wayo a rarashe shi ne take son masa wai ya bar kuka ko a ina ta ga yana kuka??, Sai dai wani al'amari sai haka din ya rage masa kuncin zuciya, haka kawai ya ji yana son yin abinda ta fada, magangannun nata sai suka samu muhali a cikin kwakwaluwarsa harma ya samu umarni daga kwakwaluwar tasa kan ya sauke kan na Mah kar a je ta kage din ne, dan haka a hankali ya saka hannayensa biyu ya sauke kan Mah ya mike ya karra gyara mata kwoncinta sannan ya mike gaba dayansa hakan ya kasance fuskar Muneerath na daidai kirjinsa ya kuwa tsaya mata kikam a saman kanta, hakan ya sa dan dole ta kauce kadan tana lumshe ido dalilin kamshin nan nasa da ta rasa shin wani irin turare ne mai irin sansayen Kamshi da naci haka a jikinsa

A hankali ta kai zaune a wajen da ya tashi kanta a kasa tana jin yadda hancinta ya karra cika da kamshin turaran nasa

A hankali ta dan dago dan kallonsa, sai ta ga ita yake kallo hakan ya sa ta karra tura bakinta aman kuma ta kasa furta masa komai

Idannuwansa ya lumshe kafin ya juya ya kama hanyar fita

Har ya kusa fitar ya juyo yana kallonta , hannunsa na dama ya dago a lokacin da suka yi ido hudu ya kai wajen lebunnansa
Cikin yannayi na sanyin jiki da iya sarafa karatun kurma ya yi mata alamu na zif wa bakinta, sannan ya nuna mata Mah dake kwonta ya kuma maida hannun wajen bakinsa ya yi mata alamu da kar ta mata hayaniya kafin ya lumshe ido ya kai hannayen biyu gefen fuskarsa ya mata alamun ta barta ta huta, sai kuma ya dan fitar da idannuwansa da yannayi irin na ta fahimta? Kafin ya kai wajen kunnensa ya dan ja sai kuma ya dantse hakorinsa a kan lebensa na kasa wanda Muneerath dake bin dukkan motsinsa a saman lebenta take fasarawa kanta abubuwan da yake nunawa da yarenta watau hausa har ta dire kan' Idan kika ki zan cije maki lebe'
Ido ta dan fitar, a nata fahimtar kennan kafin ta yatsina fuska ta cire kanta shi kuwa ya juya da dan sauri ya fice dan amsa kiran karamar wayar da Pah ke kiransa da ita

Yana tafia ta bi bayan kofar da ya rufo da kallo

Ajiyar zuciya ce ta kwace mata kafin ta mike ta kara dan yaye bargon Mah ta tataba jikinta

Jin jikin ba zafi, ga kuma karrin ruwanta na tafia daidai sai kawai ta yi bismillah a hankali ta haye saman bed din na Mah ta kwonta daga saman bargonta kasancewar lubukeke ne, ta dora kanta a kusan gashin na Mah a hankali ta ce" Kin ga, kece mamana fa, ke ce Ogana a garin nan, kin ga Allah ne gatana kuma ke ce gatana a garin nan, dan Allah ki rufa min asiri ki mike daga cutar nan taku ta yan gayu kar ki sheka yaronki ya sheke ni ya ba zakinsa ya cinye banza ya yarda kasusuwana kin fa fi kowa sannin irin tsanar da ya yi min kau? Ban san me na masa ba ko yanzu nunan ya yi zai cije ni, wai ko dai maye ne shi? Mi ya kawo cizo a lebe?"
Ta dan yi murmushi ita kadai ta ce" Wai shi mai leben nan uwa na jarirai da wasu hakoransa masu laushi yana tunanin zai iya karawa da hakorana ne?, Yo idan na dantsa masa cizo ba sai a asibiti za'a iya bambareni daga jikinsa ba?, Da wasu girarsa kamar na yan gayun yan matan garinmu, namiji da shi yana aske gira"

Sai kuma ta lumshe idannuwanta a bayane aman kuma kasa kasa sosai ta shiga yiwa Mah adu'ar da duka ta zo bakinta tana tofa mata ta bayanta, ta yi dare dare a saman bed dinta sai ga barci ya kwasheta mai dadi irin na safiyar nan gata a saman lalausan bargo abinta

Rike yake da hannun mahaifinsa, sosai yake jinjina soyaya irin ta iyayensa, a yanzu haka sai da ya jajirce ya rintse ido ya tsaya gaban mahaifinsa ya shaida masa bata da lafia ne, cikin ikon Allah ya yi luuu zai zube masa domin juwa ce ta kwashe shi da hanzari ya rike shi a jikinsa yana mai yi masa magana da dan karfin da zai wartsake ya nuna masa cewar rashin lafiyarta ne ciwon cikinta ne, kuma a yanzun baya bukatar su zube masa su biyu, idan suka zube masa yaya suke so ya yi ne?,, Hakan ya saka Pah ya jure ya daure ya ringa sauke ajiyar zuciya har ya samu nutsuwa kafin ya kama hannun HANJA su nufo wajen da aka rike Mah din watau dakin hutunta

A lokacin da suka shigo dakin, abinda ya gani ne ya saka shi yin turus da mahaukacin mamakin da ya saka shi bude baki da ido yana kallonta

Mah da ta buda idannuwanta ta samu kanta da sakin murmushin yannayinsa, a hankali ta mikawa mijinta hannu da ya nufeta da sauri stlll tana murmushin Hanja

din da ya yi mutuwar tsaye a wajen shigowar yana kallon Muneerath dake barci a saman gadon Sarauniyar ingila a bayanta a irin wannan lokacin da take rashin lafiya, ta wani lafe abinta har an luluba mata bargo gashinta dake daure ya karra yin lumbuk a jikinta

Da kallon mamaki yake bin Mah da ta kama hannayen Pah ya taimaka mata a hankali ta sauko kafafuwanta ne masu sanye da dogon sakaken wandon asibitin da kuma safa dinta kafin ta maida hannunta a hankali ta gyara mata rufarta ta juyo tana murmushi ta dora tafin hannunta a gefen fuskar Pah da idannuwansa suka tsumu da kauanar da kuma tausayin matar tasa a sanyaye ta ce" Khalb, yaushe ka dawo?"

Maimakun Pah ya bata amsa sai ya yi gagawar rungumeta a jikinsa tsam idannuwansa a rintse yana jin yadda zuciyarsa ke kadawa

A hankali take dan tapping din bayansa itama nata idannuwan a rintsen a hankali ta ce" na ji sauki fa "

Pah ya dan girgiza kansa a sanyaye sannan muryarsa cen ciki ya ce" sai da na matsa ciwon ya motsa?, Wani irin ciwo ne wannan da ba zai barmin mata ta huta ba? Da ace na ga wannan dan aiken ciwon da na kama shi ban san yaya zamu kaya ba, ALEESA lafia fa na barki"

Murmushi ne ya kwace mata, sai kuma wani irin tausayin kansu ya kamata, a hankali ta ce" haba khalb, idan da karar kwana kuma fa?"

Da sauri ya ringa girgiza mata kai tamkar matashin saurayi yama rasa me zai ce mata, sai da ya nisa kafin ya ce" Kin manta wa aka fadawa sauran kwanakin da suka rage masa a duniya?"

Murmushi kai ciwo ta yi ta ce" Ka manta ba su ke da wannan ikon ba?, Sai wanda ba'a gane masa wani ciwon dake iya kaishi ga kushewar ba ya mace ya bar marar lafiyan"
Hanja dake jingine yana kallonsu dukkan bayanansu a cikin kunnayensa duda a hankali suke yi aman dakin kai amsa amo ne komai kankantar magana kunnayenka na iya ji
So yake ya karasa ya ce da su dan Allah su daina wahalar masa da zuciya, shin me yasa suka dauki maganar mutuwa hira mai dadi a tsakaninsu? , Sai dai haka kawai kafafuwansa sun masa nauyi , jima yake kamar idan ya matsa kusa da gadon cen akoy abinda ke iya kama shi

Daidai lokacin Muneerath ta farka a barcinta,
Murginawa ta yi dan yaye bargon da aka luluba mata tana cuno bakin an hanna mata jin sanyi bayan yanzun ita din nan ta rigaya ta saba da sanyi
Hannayenta ta daga sama ta bankarro kirjinta tana mika tare da adu'ar farkawa a barci

A hankali ya janye dubansa daga kanta yana mai jin gabansa na dukan tara tara daidai lokacin Muneerath da farin cikin gannin Mah ta farka da kuma Pah ya dawo ta ce"

ALHAMDULILAH, ALHAMDULILAH YA RAB
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 0 □□□

Da matukar farin ciki ta dirko ta karasa kusa da su sosai ta ce" Lah Mah da ranki, dama na san zaki tashi ciwon ba wani bane dan jikinki ai ba zafi, Pah yaushe a gari?"

Pah dake murmushin yar shiriritar yar dake nan haukata masa yaro ya dan kama kuncinta ya ce" Ke da kike jinya ce kika yi barci?"

Muneerath ta yi murmushi tana dan jin kunyar an taba mata kunci ta ce" Pah, gwara ni, ka ga Walahi Hanja kuka ya yi ta shekawa da kyar na lalaba shi ya tashi a nan"

Ido ya kwalalo daga inda yake yana mai karra kallonta, da kallon yadda iyayensa ke dariar abinda ta fada
A ba zata, a yannayi na rashin tsamani wani sansanyan murmushi ya wadaci saman lebensa, wanda ya sauka a kan fuskar Mah dake satar kallonsa tana mai jin dadin irin yadda du yada ya so kin kallonta abin ya gagare shi

A hankali ya kuma juyar da kansa yana shafa sajensa kadan kadan kafin ya taka ya karasa har kusa da su sosai

Muryarsa a rage sosai ya ce" Hutu, likita ya ce hutu take da bukata"

Pah ya gyada kansa ya mike yana fadin" Ba zata huta a nan ba sa a turakar mijinta"

Muneerath ta fito daga labewar da ta yi a bayan Pah tunda ta ga ya nufo wajen tana dan murmushi gannin bai kulata ba ta sake abinta ta karasa kusa da gadon ta yayo bargon ta cuimuimuye ta dora a kanta ta yi gaba tana fadin" Sai kun zo Mah bara na je na gyara maki gadon tunda an sake mu"

Gaba dayansu da kallo suka bita cike da sha'awar lamarin yainyar, ko dan a gabansu basu san mutun mai hali irin haka ba?, Irin rayuwarta na matukar saka su nishadi na debe masu kewa na saka su a shauki a koda yaushe, bata da wata damuwa ita sam a rayuwarta, tabas zaku yi mamaki idan har kuka fahimci rayuwa irin ta Muneerath ta zamo abin mangari a wajen sarki na ingila da matarsa, rayuwarta bata fa kowa a saman kanta, bata da kowa a cikin zuciyarta ita din lafiyarta kalau ras take haka take lamarinta ba tare da ta jira wani ba

Tun kafin ta kulewa ganninsu suka cire dubansu a kanta suka dora kan HANJA
Gaba daya hankalinsa da nutsuwarsa sun rakata da kallo ne
Kallo ne mai shige da kamar baya so ta tafi a wajen
Kallo ne kamar wanda zai dawo da ita kar ta yi masa nisa
Yannayin da fuskarsa ta nuna kamar Hanja na son ya dakatar da ita ne

Ba shi ya san halin da yake ciki ba har sai da ta bacewa ganninsa kafin a hankali ya ankara da halin da yake ciki, sai ya samu kansa da kasa juyowa kai tsaye domin bai san yaya iyayen nasa suke ciki ba duba da sun yi shiru ya tabata hankalinsu a kansa ko kuma Pah na taimakawa Mah ta mike

Sai da ya rintse ido yana mai tambayar kansa menene dan Allah ya saka shi bin yarinyar nan da kallo? Me hakan yake nufi? Salon ya janyowa kansa ko?

A hankali ya juyo sai kuwa suka yi ido hudu da Mah wace sunna hada idon ta sakar masa lalausan murmushinta mai sanyaya zukatansu
Sai dai ga mamakinta nan da nan sai ya hade rai yana mai cire kansa ya karasa ya kama dayan hannunta Pah na dayan hannun suka taimaka mata ta idasa mikewa tsaye kamar yadda suke mata kafin su kamo hanya a hankali su nufi kofa fuskar nan tasa a hade shi a dole kar a masa maganar bin yarinyar nan da kallo, koda yake a shiryema yake da basu amsa daidai da tambayarsu, zai fada masu ne haukan yarinyar nan na karra girmama duba fa ta dauki bargo ko me zata yi da shi?

A hankali suke tafia har suka karasa bangaren Mah din
Kasancewar ta ce tana son zuwa ta dauki sako a cen wanda ba wani sako dan dai ta salami yan matanta ne dan ta tabata sunna cen din duba da Muneerath ta dauki bargo ta ce zata je ta gyara mata gado

Ai kam sunna nan din, kuma su suka gyara dakin da kansu wanda Iman da kyar ta iya wani kokari a guaran tana kallon yadda Muneerath ke mika injin shara kasan bed tana son sharo dati bayan ba wani dati ko daya yau dinma abinda ya hanna masu gyarawar dan mai wajen bata nan, idan bata nan kuwa ba shiga suke yi ba

Murmushi Mah ta saki a lokacin da Muneerath ta matso tana mata murmushin itama ta ce" Mah me zamu dafa maki?"

A kasan zuciyarsa sai kawai ya samu kansa da mamakin furucinta, wai me za'a dafa , yar dake kona shayi? Ta kona wainar kwai ta ce ta fi vitamine?,
A hankali Mah ta zauna bakin Bed tana mai godiya wa abubuwan kaunarta watau Pah da kuma Hanja

Pah ya ce" Bara na je falona na dawo dan na saka a kimtsa maki komai"

Yana tafia ya yi sauran su hudu a dakin,
Mah na murmushi tana shaa kan Iman dake gefenta tana jikinta sosai tana sauke ajiyar zuciya, Muneerath kuwa tana tsaye a gabanta tana kallonta, Hanja kuma yana cen kusa da mirror dinta yana duduba turarukan dake ajiye kamar wanda hankalinsa na kan hakan bayan gaba daya hankalinsa ba a wajen yake ba a kan su Mah yake

A sanyaye Mah ta ce" My Munee, wannan kayan na fita ne?, Kin ga yadda wandon nan ya maki a jiki kuwa? Ba hula a kanki fa?"

Muneerath da sauri ta bi jikinta da kallo, lokaci daya ta zarro ido tana fadin" La hauli, tashin hankali da a haka naie yawo ko hula babu? Allahnma da ya sa a gaban Hanja ne da Pah, wollah Mah ni du rikicewa na yi da aka ce baki da lafia kuma ina zuwa na tarda shi yana kuka sai ya karra rikitani"

Wannan karron sai ya kasa rikewa, ya juyo ya karaso wajen yana hararanta a dake ya ce" Ke a ina na yi kuka da zaki ringa yadawa cewar ina kuka?"

Iman dake jikin Mah a hankali ta dago dubanta tana kallonsa tare da mamakinsa da ya ki ya daina kokarin kasheta, wai me yarinyar nan ta fita ne da har ta fita samun alfarmomin nan a game da mutumen da ta rayu da sin gannin sakin fuskarsa a gabanta?

Muneerath ta kama baki ta ce" Lah, Ka rantse da Allah ba sai da na rarasheka ba ka daina kukan, ji fa dan ka ga ta tashi ne zaka karyata ni?"

Wata daria ce ta kubcewa Mah lokaci daya tana dafe cikinta tare da dafe kafadar Iman

Da sauri suka nufeta, lokaci daya suka rufun mata a tare suka kai hannayensu gefen kafadarta da nufin rikota dan talaf mata duba da dan tarin da ta dan fara sakamakon dariyar ba zatan da ta sarketa

A hankali idannuwanta suka sauka a kan fari kal din hannunsa dake saman bayan hannunta mai duhun haske wanda ta ji tamkar an dora mata gashin mage ne mai laushi a bayan hannun nata sannan a hankali aka dan murza bayan hannun hakan ya sa gaba daya ta ji gabanta ya fadi
A hankali ta cire duban nata daga kan hannayen nasu ta dan fara kokarin zarewa cikin dabara tare da dago duban nata ta sauke a kansa dan gannin idan tunaninta na baima san ya taba mata hannu ba haka ne

Ido hudun da suka yi, da idannuwansa masu launin ja wa'inda tun tashin hankalin rashin lafiyar na Mah da suka dauki launin har yanzun bai hadu da abinda zai saka su cenza kala ba suka shiga cikin nata masu hasken gaske da kwayar cikinsu masu kala daban da ta mutane sai ta tsinci kanta da bugawar zuciya a karro na biyu wanda shima abinda ya ziyarce shi kennan harma ya shagala da kallonta har sai da ta cire hannun nata da sauri tana kallon yadda Iman ke mikowa Mah ruwa tana mata sannu ita kuwa tana nuna ba komai fa

Gaba data rasa me zata yi ta yi,baki daya daburcewa ta yi ta rikice hakan ya sa da sauri ta juya tana fadin " Mah bara na dauko hijab "

Hannunsa na hagu ke rike da Mah dinsa, ya rintse idannuwansa yana jin yadda yake fitar da numfashi tamkar mai ciwon huka

A hankali ya bude duban nasa ya kurawa hannunsa ido, wannan tabawa da ya mata itace tabawa ta farko da ya yi mata ba da niyar fada ba
A gaskiya bai san me yake damunsa ba, abinda ya fi ajiyewa a kasan zuciyarsa shine Bashi da lafia

Gaba daya jikinsa sai ya mutu Iman kuwa Muneerath na tafia itama ta bar wajen, dama karfin zamanta dan ta ga Muneerath din ne a yanzu da bata nan bata isa ta yi dogon zama a wajen da yake zaune ba, shi kuwa bai bar wajen ba har sai da Pah ya dawo ya dauki matarsa ya yi bangarensa da abinsa yana ta ririta tamkwar kwai
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 1 □□□

Bayan kwana biyu

Kula ta musaman, jinya mai girman daraja Mah ke gabatarwa a gefen mijinta, hakan ya saka Hanja fita dukkan wasu taro na Pah da kuma jagorar da yawa a cikin Palas a baban dakin taro
Wannan al'amari ya dauki hankalinsa sosai harma ya yi kwanakin nan ba tare da ya saka kafarsa a filin jirgi ba, hakan ya matukar bashi mamaki da tunanin dama akoy abinda zai hanna masa leka tsuntsu marar numfashinsa?
Sai dai wani abin ya fi gaban wani, watau a yanzu da ya tsaya ya fuskanci mecece matsayin gadon da ya tabata ko ba dade ko ba jima idan dai da ransa da lafiyarsa ko da ran mahaifinsa ko babu ya zame masa dole da karfi da yaji ya mulki kasar sai wani dari dari ya kama shi
Shin yaya Pah yake yi yake walwala?, Kai gani yake da shine harta walwala rasawa zai yi, ko dan shi din farin shiga ne?
Yaya Pah yake yana samun time isashen da yake ganninsa zaune a falo?
Yaya Pah yake har yake gane iyalinsa nada matsala ko sunna cikin farin ciki harma ya basu lokacinsa?
Tabas a yanzu ya yarda cewa shi din bako ne kuma yaro ne karami a duniyar nan wanda yake da bukatar a kama hannunsa

Gefe guda ga wannan nataciyar yarinyar da tunda sunnansa ya fara yawo kan Media a matsayin wanda yake gabatar da aikin babansa harma sunnan da ake kiran mahaifin nasa maimakun prnc kamar yarda ya saba ya hau kansa aka fadi dalilin cewa yana cikin hutun kula da lafiyar matarsa ne take aiko da takardar neman izinin samun damar shiga Palas din dan ta ga jikin Mah da ita da iyayenta
Ba dare ba rana sai an sanar masa da nata sakon a cikin sakwani hakan ya sa yau ya yi croi samanta dan ya gama da tata matsalar kafin ya fuskanci yan hutun nan su amshi kasarsu su rufa masa asiri, tsakani da Allah tunanin da kwakwaluwarsa da zuciyarsa take cikima ta fi komai adabarsa a irin lokutan nan

Tunda ya sauko daga matatakalar gidan tare da Tgr dake tafia ta kasaita yake jiyo muryarsu da yar dariyarta

A hankali ya jinginar da bayansa a jikin garu ya samu kansa da saurin lumshe idannuwansa yana mai bin hirar da take yi tana gaurayawa da yarenta da bai iya ba domin a yanzun tana french ne da kuma ainahin hausa tamu gangariyarta abinta sunna labaru irin na tsegumi da kuma hirar dangi ita da aminiyarta a saman table sunna cin ganima sunna kora jus , iman kuwa na kwonce a saman doguwar kujerar Falo tana sanye da earpc a kunne tana sauraron wata tsumamiyar wakar larabawa tana lumshe ido

Sai da ya gaji dan kansa Tgr kuwa tana kai kawo a daidai wajensa kafin ya sauke dubansa a kan Tgr

Haka kawai ya samu kansa da sakin murmushi yana mai son gannin tsererenta idan ta ga Tgr

A hankali ya ci gaba da takawa ya idasa fitowa gaba dayansa direct ya nufi wajen Dinern hankali kwonce

Sansanyan kamshin turaransa ya saka an lumahe idannuwanta kafin ta dago dubanta a hankali, sai dai abinda ta gani ya sakata saurin maida kan nata jikinta na rawa ta yi shiru tamkar gawa danma kar a ji motsinta a wajen har suka wuceta suka fara taka yar matatakalar hawa wajen table din

Yar shewa Muneerath ta saki tana kai hannunta kusa da kafadar Saudat ta ce" Ke dillah ki bari, yanzun dan zai zo zance sai ya shigar da takarda?, Ai yau yau zan saka a kawo shi zance gidan nan ya kuma shigo har falon nan mu zanta mu fafata abinmu, ai dai zaki zauna a kusa da ni ko?"

Saudatma ta yi yar dariyarta ta ce" ai kece fafatawar, kin ga a yadda ya damu kan yana so ya ganki gashi kwana biyu cif tunda muka shigo bamu ga waje ba ya dace mu dan sama masa dan time dinsa , kin ga fa soyaya ciyar da ita ake ba mantawa ake yi da ita ba fa"

Muneerath ta dan talabe habarta ta yi luuuu da idannuwanta a hankali cikin yaren turanci wannan karron ta ce" Ban san zan so wani halitar da ba dogari ba Saudat, wani sa'in sai na ji ina son Sir sosai bale idan kina koda min shi sai na ga ai shima da nasa ikon a inda yake, ya Allah ka yaye min matsalar sarauta dake zuciyata na fuskanci abin sona mu so junna mu yi aure"

Saudat ta girgiza kanta da dan kari kari ta ce" Dogari?, Wai dan girman Allah su rasa ina zasu sauko ki sai nan?, Dogari mutun ne mai daraja aman a kan me zasu sauko maki burinki na son zama sarauniya?, Ai ba'a sacewa bawa gwuiwa komai

kaskancinsa domin ba'a san meye Allah ya boye a tare da shi ba, waye ya san gobe ne?, Kin wani damu dogari dogari kin kuwa gane ainahin aikin dogari? Dogari irin na kasarmu?"

Muneerath ta mike daga zaunen da take, hakan ya sa doguwar rigar dake jikinta fara ta idasa sauka tana rawa a jikinta ta dan watsa hannayenta ta ce" Ba zaki gane ba, ni fa ba wai kudinsa ko wani yannayin rayuwarsa bane damuwata, Saudat buri ne da mafarki da na tashi da shi yake bani wahala, ki duba ki ga irin wh....."

Katsewa maganarta ta yi a lokacin da idannuwanta suka sauka a kan fuskarsa

Sajen fuskarsa mai kyalin baki da lebunnansa zuwa uwa uba fitinanun idannuwansa masu kallon wuce ka'ida da ya zuba mata
Sanye yake da suit ash color masu farar riga a ciki mai duhun haske
Gashin kan nan nasa ya sha mahaukacin gyara sai kyali yake

Da farko a kansa dubanta ya tsaya, ta yi ta yi ta cire ta kasa aiwatar da hakan , hakan ya sa ta samu da kyar ta lumshe idannuwanta tana jin wasu kwala sun cika mata su masu zafin da suka hadasa mata jin ciwon ido kafin kunnayenta su jiyo mata amon muryarsa ba ihu ko kadan cen kasa kasa ya amsa kira a wayar dake hannunsa ya ce" Ka sanyo su baban falo nan da awa guda idan na gama karyawa"

Yana gama wannan ya danna wani kiran wanda yana dagowa ya kuma saukewa a kan furkarta da yannayinta kafin ya saci kallon Saudat da ta mike itama ta sada kai jikinta na dan bari tamkar yadda suke mada a wajen aikin nan, ya kuma maidawa kan Muneerath wace bata taba yin barin nan dan yana waje ba ya karra zuba mata ido, dan siririn dan kwali fari ne a yane a zagayen lakausan dogon gashin kanta mai cika daga gabam goshi sosai, sai yar siririyar agogo fara

A sanyaye ya ce" Ka zo ka dauki Tgr "

Daga haka ya katse kiran yana kallon lokacin da ta kalli Saudat a dan zabure wanda ga dukan alamu a yanzu ta fara gane tare yake da tgr din

A hankali cikin dabara ta ringa kallon kasa kasa har idannuwanta suka sauka a kan Tgr dake zagaye shi tana kada bindi
Wata wawuyar ajiyar zuciya ta sauke a bayane kuma kasa kasa sosai ta ce" Wayo Allahna, ta yau dinma ta kirkin ce, kuma gashi ba Mah ba Pah a kusa, ga yar mutane tana tare da ni , gashi inaga haushina yake ji dan sai hararena yake..... innalilahi Saudat Zaki....."
Ta idasa maganarta da dan daga murya wajen ambatar sunnan Zakin da hausa tana kwalalo ido ta nunawa saudat da idannuwanta.....

Saudat gaba daya ji ta yi tamkar zata suma, haka jikinta ke rawa ta rasa yaya zata yi daga tsayen da take

A hankali ya dagakafarsa ya kara taku daya dan karra kusanta kansa da Muneerath, sai dai abin daria yana yin taku dayagaba tana yin daya baya idannuwan nan kuwa tamkar zata dauke shi da su

Sai da ya gama murmushinsa na yannayinsa a cikin zuciyarsa kafin da hannayensa ya nuna masu wajen zama da yatsarsa daya ya kuma nuna cewar su zauna , ya kuma dan nuna alamun idan ba haka ba.....ya karasa da dantse lebensa, daidai lokacin kuma mai kula da bangaren Mah ta same shi ta waya da tambayar idan har yanzu su

Mah zasu sauko su gaisa da bakin?, Ya shaida mata lokaci kafin ya kara sauke masu kakausan kallo a kansu wanda ya saka a birkice du suka samu matsugunni suka tsuguna duwawunsu

A hankali Muneerath ta saka hannunta tana ture dan kwalinta da hannayenta kuwa tana firfita tana satar kallon yadda Saudat ke share hawaye kanta a sade baiwar Allah

Karasawa ya yi ya ja kujera ya hau ya zauna kafin ya shiga shafa bayan Tgr dake daf da kafarsa yana hankalce da yadda Muneerath ta nade kafafuwanta kawarta kuwa sai hawaye take

Dan gyaran murya ya yi ya nuna mata abincin da idannuwansa sannan ya nuna plat olat din dake ajiye

A sanyaye ta ce" Toh "
Ta mike tana sarar kallon Tgr ta bubude abincin
Bata tsaya tambayarsa ra'ayinsa ba ta zuzuba masa abincin ta ajiye da cokali sannan ta tura masa mg din jus din ta koma ta zauna tana sauke ajiyar zuciya

Da gaya, da neman fitina, da ba bawa wahala ya ringa takalar abincin kadan kadan su kuwa sunna zaune zuciyoyinsu na dukan tara tara inda Muneerath ke bin hannunsa idan ya dauko abincin a kasan zuciyarta tana ta ayanna dama ba Tgr a kusa Allah yau da sai ta kwaba masa abincin nan idan yana so ya yankata!, To dan dai Tgr dai daba ce, daba kuma mai cinye mutun murus wace ita nama shine abincinta danye ba dafafe ba, hakan ya sa ta nutsu ta yi shiru tana sauraro har daidai lokacin da wayarta ta dauki ringin cikin wakar hausa mai taken tatausan lafazi

A hankali ta kai hannunta ta dauki wayar tana duba sunnan dake sama baro baro an rubuta Freind
Dan murmushi ta saki hade da sauke ajiyar zuciya a hankali ta daga idannuwanta a kasa kafin ta dan dago da dubanta ta sauke a gefen da yake
A karro na hudu idannuwansu suka kuma sarkewa da junna, da sauri ta cire dubanta a cikin nasa ta sada kanta tana shafa gefen wuyanta a hankali ta ce" Sir zan tabo ka idan an jima zan yiwa Mah maganar zuwanka abinda tace sai na fada maka"

A hankali ta kashe kiran ta ki kallon wajensa, gaba daya ji take bata iya kallonsa bata san me yake ji a tsatsare mutun da ido ba

A hankali ta ce" HANJA, yaushe zaka mayar da ni gida? "

HANJA da gaba daya ya ji abincin ya tsaye masa a kirjinsa ya cinkushe masa, gaba daya ya ji zaman wajen ya fara isarsa maganarta sai ta diro masa a wani baibai
Me take nufi da yaushe zai maida ita Niger?, Me take nufi da shi?, Shi wai sa'anta ne ko meye?

Mai kula da Tgr dake tsaye yana jira shima a kadan ya yi minti arba'in a tsayen ya kai dubansa kansa, yana shirin masa nuni da ya tafi da shi su Mah suka sauko

Turus Mah ta yi gannin a yan taron harda su Tgr ga kuma y'ayanta da alamu an tsatsare su ne , sai itama ta ki idasawa har sai da ta ga an ja Tgr an tafi da ita kafin ta karaso tana murmushi

Jikinta ya yi sauki sosai, saman kujera ta zauna tana zama ta dan daga murya ta ce" Abinci ake ci ne? Wanda ya gama ya zo na ganshi, Son harda kai a cin abincin?"

Muneerath yanzun ta samu kanta, an tafi da Tgr haka kuma ga Mah a gefe dan haka sai ta dauko dan mayafinta ta kade abinta ta yafa sannan ta mike tsaye da kyau tana gyara rigarta ta kalli Saudat, yar daria ta yi da yannayin na Saudat ta ce" Sai ki taso mu karasa cen yau mun tsira Allah dai ya sa mu rabu da kasar nan lafia, taso kin ji" Tana fada tana kamo hannun Saudat ta mikar da ita hankali kwonce ta jata suka yi wajen Mah

Wata shakar ya yi, harma ya ki ya motsa daga yannayin da yake
Daga inda yake yana ji dan rashin kunya yarinyar nan na fadawa Mah zata kawo kato gidansu, ta karashe da tambayar Mah yaushe za'a maida ita Niger? Tana missing din iyayenta fiye da tunanin dan adam, sai ya ji kawai shi take nema da fitina dan haka ya mike tsam tare da daukan tissu ko ruwa bai tsaya ya sha ba ya juyo ya sauko da sauri sauri ya karaso

Yana tsayawa su Pah na shigowa da baban Minister da matarsa da y'arsu yar kwalisa sai rangaji take abinta
Bai tsaya da niyarsa ba yana zuwa rai bace ya ce" Ke!, An ki ba'a mayar da ke Niger din!, Kuma dakike maganar zaki gayato wani sakaran saurayinki marar aikin yi sai ki gayato shin mu gani tunda ke bakya jin magana sai neman rainawa mutane wayo da batawa mutane rai da kika fi kwarewa a ciki, ba zaki je din ba kuma ba zai zo nan ba!"

Ikon Allah ne kawai gaba daya al'umar dake wajen suka tsaya kallo, ciki kuwa harda Iman da yar gidan Minister wada tunda take bata taba sannin yana doguwar magana haka ba, itama sai kai dubanta kan wace yake yiwa ihun, Iman kuwa da gaba daya kwanakin take dan fuskantar ya cika zakewa a lamarin Muneerath jin ba zai maida ita ba ba kuma zara gayato saurayinta ba sai ta yi mutuwar tsaye tana dane kukan dake son fasowa ya fito daga bakinta

Kallon kallo suke kafin Munnerath tsam ta mike ta koma datan gefen Mah ta shirya tsaf koda ta kwana ta ce" To kuma ni yanzun dan Allah me na maka, kai kawai ka tsane ni?, To a kan me zaka ce ba zai zo ba bayan saurayina ne kuma Mah ta san da zamansa?, Bayan wannan Niger din nan fa ba anguwa ba nake nufi sunnan garinmu ne garin iyayrna inda ka dauko ni, ko zan iya sannin a kan me ba za'a maida ni ba? Ni wollah Mah kin gani haka fa ya hayo cem wajen da zakinsa ya hanna mana cin abinci karshe harda hawaye kawata take na ta gama sarewa cewar mun mutumun lalace, kuma dai ai ni na daina yi masa rashin kunya shine zai ce yanzuma ba zan je Niger ba?, To ni dai sai na je ko a tayar jirgi ne koa kafa!"

Hargowa da rigimar da ta shiryawa din ne kam ya gama hadawa kala kala, fitina tashin hankali fada shine abinda iyayensa suka gama karanta a tatare da shi wanda yake kiris ya fashe da su

Lokaci daya ya daga kafarsa zai zagaya ta dayan Bangaren, hakan ya sa Saudat ta duke jikina bari cike da tsoron yannayinsa ta rufe ido ta dora hannu a kai tana dana sannin zuwanta gidan ta gama sannin cewa tasu ta kare hakama sun gama rasa aikinsu kennan ko wa ya tsaya masu,sam bata san Muneerath rikakiyar mahaukaciya bace sai yanzun da ta baiwa sir Hanja amsa a haka, in ba kasada irin tata ba idan yace ba zata je ba ta yi hakuri a lalaba shi mana sai ya mayar da ita a hankali idan ya yi niya duda bata san dalilinsa na cewar ba zata koma garin iyayenta

ba, haka kuma ita da kanta ta ga gangancinta na cewa zata gayato sir Attahir gidan nan , ita a tunaninta yadda ya zamo waje mai saukin shiga a wajenta hakama kowa ? Gaba daya ta tsorata da jan da fuskarsa ta yi shi yasa ta duke dan ta san har ita yau sai ta dauki duka!

Da gudu Muneerath kuwa ta dafe rigarta ta juya wajen matakalar benen ta fara haurawa da dan ihun neman ceto tana kiran sunnan Mah da Pah

Gogon kuwa ko idannuwansa basa gane masa da bakin fuska a wajen, ko lamarinsa ya yi daukakan da baya iya hakuro har su tafi?, Ya aniya bin bayan nata da nasa kalar salon bi da gudun dan so yake ya damketa ya yi mata shakar mutuwa sai ta fara bambance raini tsakaninsa da banza Attahir din da duk a cikin abin ya fi bashi haushi ba tare da ya san dalili ba

Pah dake yar daria ne ya yi maganar da ta saka jinnin kowa kusan hawa a wajen nan, kama daga iyayen budurwarsa masu neman iri, da shi gogan dake neman kasara yar mutane, da kuma Iman mai fama da nata miki cikin shiru, da Saudat da bata san abinda ake ciki ba, da Mah wace ke kokarin taro shi kar ya aikata haka dan bata san a yaya zasu kare ba ta tabata ba iya tsere masa zata yi ba duda ta fala a guje abinta a lokacin da ya ce" Ts 's my dghter in low "

Shi dai turancin nan ba yarena bane, idan ban yi daidai ba ku daidaita □□
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 2 □□□

"WHAT?" shine kalmar da ta fito daga bakin budurwar da dukan karfinta haka kuma idannuwanta a waje

Iman dake tsaye bata san lokacin da kafafuwanta suka kasa daukanta ba

HANJA da ya ja birki daga niyarsa na son bin bayan Muneerath ya juyo a hankali ya tsaya da wani expression a kan fuskarsa na son sake jin karrin bayani daga mahaifinsa da ya fuske ya maimaitawa Yar gidan minister abinda ya fada

Juwa ce ta kwasheta daga tsayen da take, juwa ba ta karya ko ta gayya ba
Juwa ce ta makata da kasa wanda hakan ya saka du wani dake wajen nufarta banda Iman da ta hade kai da gwuiwa da kuma Saudat da ta mike tsaye tana wuki wuki da idannuwanta , sai kuma ahi gogan da gaba daya ya tsayar da du wani tunani nasa a kan mahaifinsa

Saman doguwar kujera Mahaifinta ua kwontar da ita, Pah ya nufi wajen Wayar tafi da gidanka ya dauka ya shiga buga kira wa likitocin palace din
Mahaifiyarta na shafa gefen fuskarta tana ambatar sunnanta , MAh na gefenta tana afkin yi mara sannu

Karasowa ya yi tsakiyar falon ya zauna saman kujera ya dan ringesa hannunsa na dama ya dora kafa daya kan daya yana dan kadawa yana kallon ikon Allah domin ba suma ta yi ba kuka ne take sai lalabata suke yi ana bata baki da hakuri a haka har likita ya zo ya dubata ya tafi Pah na zaune yana kallon su

Mahaifinta ne ya sauke ajiyar zuciya cike da ladabi ya dan saki dan murmushi ya ce" Honorabl, ka yafe mana wannan hargitsin, maganar nan ce ta rikitata duba da soyayar da take yiwa sir HANJA"

Cike da isa irin na saraki Pah ya kai dubansa kan Hanja dake zaune yana kallon kowa cike da miskilanci kafin ya fyskanci minister da datako iron nasa ya ce" Soyaya suke da yarinyar wajenka? Tun yaushe fa?"

Minister ya kalli yar tasa dake ta hawaye a yanzu ta daina kukan tun karfi ya ce" Hassy ki sanar masa"

Sai da ta ja numfashi sannan ta ce" ya kai shekara biyu "

Mah ta kalli Hanja da sauri tana bukatar karin bayani aman abin haushin ya ki ya furta komai sai tsatsare Hassy din ya yi da ido

To shi gaba dayama gannin ranar nan yake kamar a wani mafarki, Pah ya masa aikin nan ga kuma wata na yi masa wani , to wai a me aka dauke shi dan Allah, idan soyayarma yake yi ya rasa da wa zai yi sai da yarinyar cen kuma ya kasance shi bai sani ba har sai an fada masa?

Pah ya dan dage kafadunsa yana kallon Minister ya ce" Zan waiwayeka a kan maganar".....yana fada ya cire kansa yana basarwa ba tare da ya kalli gefen da Hanja yake zaune ba

Su da suka zo gannin marar lafia sai ya kasance ziyarar tasu ta samu takaituwa harma suka bar gidan da wuri ba tare da sun samu kan yarsu ba hakama wanda yar tasu take haukan a kansa

Bayan tafiyarsu da kamar minti biyar sunna zaune a yadda suke Mah ta umarci Iman da ta koma dakinta cike da tausayinta a kasan zuciyarta, sai dai du yadda ta kai da son iman da tausayinta ba zata hadata soyaya da Hanja ba idan har ba shine ya bukaci hakan ba domin ta san wahala ce zata siyan mata mai dogon zango, dan haka gwara ta kyaleta ta yi ta gama

Sai da ta shige Tare da Saudat Hanja ya fuskanci iyayensa tare da neman karrin bayani a kan furucin Pah

Pah ya dube shi da kulawa ya ce" Me yasa ba zaka ba kanka lafia ka samawa kanka nutsuwa ka hannama kanka faduwar gaba da shiga tashin hankali sakamakon abinda kake so na ambatar maka wani a gabanka?, Dama an yi namijin da zai ringa shiga bakin macen da jinina ke so bayan kana raye ba mutuwa ka yi ba? Girman kai da jiji da kai fa ba wannan bangaren ake yiwa ba, mai ilimi yana nan soyayar mace ta lalami ya saye zuciyarta a lokacin da ita kanta bata shiryawa hakan ba, ko har yanzu kana kan bakanka na kai baka ce kana sonta ba?"

Hanja ya dafe gaban goshinsa kafin ya ciro ya ce" Me ya kawo maganar so a tsakanina da ita ?, Rudani ke iya rudata a kan lamarinta ko meye?, Ba maganar so bace Pah"

Pah ya gyada kansa kafin ya mike ya nufi wajen lft a kasan zuciyarsa yana ayana idan ka san wara baka san wata ba!

Yana bacewa ganninsa sukai ido hudu da Mah, mikewa ya yi da takun gagawa ya bara mata wajen danma karma ta dora masa da wani ciwon kan ya bar gidan gaba daya ya nufi gidansa domin yana son kebe kansa dan ya yi tunani a kan rayuwarsa da sokoncin da yake bazawa a kowani lokaci a gaban wannan yar yarinyar

Sosai ya dauki lokaci a gidansa yana ta auna magangannun iyayensa, inda ta amsa kiran yarinyar gidn minister ya bata lokacinsa yana sauraronta yana auna yannayinsa da dukan wata tafia dake iya sada shi da maganar abinda ke cikin zuciyarsa
Me yasa take masa magana kamar wata marokiya? Kamar wace ke maula a wajensa? Me yasa idan ya mara gardama a abu sai ta shiga wani lalaminsa ko ita ta yi biyaya kai tsaye?

Tsaki ya ja bayan ya kashe wayar ya daura alwallah ya shiga gabatar da nafila domin ya kula idan ba sallar ya yi ba ba zai samu sukuni ba

Cika daren da ya yi shi ya saka shi makara, domin ba shi ya kwonta a jiya ba sai da ya gabatar da sallar asuba ya yi barci a saman salayarsa hakan ya sa sai sha daya na

safe ya farka daga barci kafin yake shiryawa a gurguje ya nufo gidansu dan ya ga a wani hali yake ciki

Baban abinda ya tarar ya saka shi jin juwa na neman maka shi da kasa wace bai san dalilinta ba

Labarin da ya samu a wajen Mah dinsa da ya tarar vry sad ya saka shi juyawa ya nufi bangarensa ba tare da ya furta komai ba

A lokacin da ya zame a bangaren nasa sai ya samu kansa da maimaita sakon mahaifinsa wajen karfe daya na dare ta voice note inda yake shaida masa ya neme shi bai same shi ba gashinnan a a roport ya zo da kansa ya saka an tashi jirgi za'a kai Muneerath Africa dan ta je ta ga iyayenta
Ya kuma shaida masa tafiar harda Mah a yan rakiyar ga Mah dinsa da Muneerath sunna hawaye wai munneee ta ce ta fasa tafiyar wollah sai take ji ba zata iya barin Mah ba

Idannuwansa ya rintse daga zaunen da yake a hankali ya danna Vidio din da ya turo masa wanda yana dannawar ya yi daoloding da gagawa ko dan karfin ntwrk ne

A hankali ya shiga vidio din ya tsurawa abinda ke wakana a ciki ido yana kallo

A hankali ya samu kansa da lumshe idannuwansa kafin ya bude a sanyaye ya dora yan yatsunsa wajen kuncinta da hawaye ke zubar mata ta dage tana rusa kukan rabuwa da MAH

Dan murmushi ne ya kwace masa kafin yake dan kausasa dubansa a sanyaye ya ce" Karya ne, karya kike ko?, Kukan nan na farin cikin zaki yi tafiyarki ne ko? "

Sai kuma ya rintse ido a kasan zuciyarsa ya shiga ba kansa amsa' Hanja ba shikenan ba kaima ka huta?, Ka huta da ihu da take saka ka, ka huta da bata maka rai da take yi, ka huta da tunanin kar aje muguwa ce ta cuci iyayenka da suka yarda da ita, ka huta da faduwar gaba, ka huta da tunanin akoy wata halita dake iya kallonka ido cikin ido ta ce da kai sai an yi, ka huta da tunanin me take yi da wa take yi , ta je din Hanja, ta je din, idanma Pah ya yi haka ne dan ya daga maka hankali ba komai bai yi wng ba'

A kadan ya dauki lokaci mai yawan gaske yana kuma kallon vidion, karahe dai sai ya ajiye a kan vidion ya mike ya shiga kokarin shiryawa dan ya tafi wajen aiki, ya tabata da irin abubuwan nan ke shigar masa cikin tunani sunna hanna masa sukuni

---

Tamkar a mafarki take ganni
Sosai take jin ciwon rabuwa da iyayen goyonta duda an bata takarda da numbobi prvt nasu wa'inda kai tsaye ko wani ta aiko yana iya zuwa ya shige cikin palace da sunnanta bale ita da kanta, sannan Pah ne da kansa ya ja mata gargadin idan kafarta ta taka kasar ingila bata da masauki sai gidansa
Sai dai duda haka wani irin baban gurbi take ji ta baro a ingila
Wannan gurbi kuma ba komai bane face Mah, Mah itace macen da ta fara ganar da ita abubuwa masu mahinmanci na rayuwa

Mah itace ta koya mata cake
Mah itace ta jata a jiki ta koya mata soyaya irin ta d'a da uwa
Bata san irin adadin soyayar da take yiwa baiwar Allahn nan ba, bata san irin adu'o'in da zara bi baiwar Allahn nan da su ba duniya da kiyama, abinda ta fi sani shine ta hadu da mutane masu halaci, kuma zata dawama mai halaci a tare da su

Wayar ma'aikata aka bata da shaidar cewa a koda yaushe tana iya samun kira dan tafia,
Mota ce aka basu kowace da tata sabuwa dal

Gaba daya bata lura da irin yannayin da Saudat ke ciki ba, zumudi da tsoro da son ganninta gaban iyayenta dan ta jero masu tambayoyin dake cikin zuciyarta wa'inda ta yi ta tarawa tsakanin zaman nan nata na dogon zango a nesa da su ya hanna mata gannin irin halin firgici da yawan kallonta da Saudat ke yi har zuwa yanzu da ta bude gaban motarta ta shiga tana kallon motar tana murmushi da jakarta mai dauke da AtM dinta wada ita kanta bata san adadin kudin dake cikin banki na nan niger da sunnanta da kuma wanda aka bude mata na ingila da sunnanta ba

A zabure ta kalli bangaren da Saudat ta bude ta shiga ta rufe kofar da karfi

A dan zabure ta ce" Aushhh saudat ki rufe a hankali mana ji kin rufo da karfi har kaina ya amsa walahi!"

Saudat dake binta da kallon mamaki ta ce" Muneerath me yasa kike kamar baki baki sani ba? Ni zaki boyewa irin wannan abin?"

Kasakai ta yi da mamakin yannayin Saudat din da kuma irin abinda take fada

Da sauri ta karra waigawa bayanta ta ga motoci uku biyu ta sojoji daya ta police kamar wa'inda suke jira ta basu waje su wuce

Da sauri ta kunna motar tana fadin" Tsaya na basu waje su wuce ki fadan me na boye maki ni kuma?"

Saudat ta karra cika da mamakinta ta ce" Su wuce ina bayan su din daga bakin yanzu har ki bar niger zasu kasance da ke masu baki tsaro ne a matsayinki na sarakuwa sarkin Ingila?"

Kamar jinta ne ya dan dauke na dan lokaci kafin ta maimaitawa kanta maganar, hakan ya bata dariya ta kalli Saudat ta ce" Hala a jirgin aba buga maki kai da wani waje kika haukace?"

Itama da takaicin yadda Muneerath ke son raina mata hankali ta ce"
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 3 □□□

Ta ce" Me yasa kike son saka wasa a dukan lamarinki?, Me sarkin garin ingila yake nufi da maganar cewa ke din SARAKUWARSA ce? Meye fasarar karamawa da muka samu irin wannan?, Abinda muka malaka a yanzu ni kaina da sanadiyarki na malaka ko sir da ya yi shekaru a matsayin ma'aikaci baba mai horar da hostess bai malakesu ba duka hakan a kan wani dalili?, Da aka yi maki accct na kasar ingila da takarda ta shaidar da aka baki damar zama na dindindin a kasar ingila wada kike iya shiga ba tare da visa ba kai tsaye ki shiga wajen da ya maki ki kama gidan da ya maki da dukan isa irin ta haifafen kasar me suke nufi? Meye fasarar fadan da kuke yi ke da Princ HANJA?, Me yake hasala shi a kan maganar da ta shafe ki?, Me yasa a ranar nan ya yi maki tambayar me wani namiji ya fada maki , ke kuma kika dubi tsabar idannuwansa kika bashi amsa kai tsaye ba tare da kin ji dar din abinda ka iya zuwa ya zo?, Shin inai maki kallon marar wayo kina mani na shahsasha ne?, Soyaya kuke da magajin kujerar garin ingila ko me?"

A firgice Muneerath ta ce" Dan Allah sasauta da magangannun nan naki Saudat kina neman tarwatsa min kwakwaluwa, me hakan yake Nufi ? Me magangannunki suke nufi dan girman Allah?, Wacece ni? Me ya hada ni da irin wannan kokowar? Koda na kasance mai aiwatar da lamurana kai sake na san wajen wasana, kin ga tunda Allah ya hadani da shi na fahimci ya tsane ni, Saudat mutumen nan da ba dan mamansa na gefe ba da ya karya ni, kina gani fa ba laifin tsaye ba na zaune zai kama hararata, ki duba ki ga sau biyu ina suma a saboda shegen Zakinsa, Saudat ke fa shaida ce dan tsabagen tsana na ce Freind zai zo wajena ya ce ba zai zo ba dan yana gidansu ko?, Kuma sau uku yana zo min dan Mah ta ce idan ya kara ne zan samu ciki na ki ya karan fa, aman dan Allah me hakan yake nufi ke da kanki kin san koda Pah ya fadi haka ya fada ne dan ya kular da shi, baki ga haka yake tsokalarsa ya yi ta cika yana batsewa ba?"

Dafe kai Saudat ta yi cike da tunanin ta inda zata fara kafin ta dago kanta ta ce" Da farko kar ki kuma budar bakinki a gaban kowa ki ce wai namiji ya zo maki, kin kuwa san menene ma'anar an zo maki?, Ciki baya samuwa sai idan mace da namiji sun kwonta sun yi hvng sex , idan na ce maki sex ina nufin sun samu moment a tsakaninsu da basu da shamakin komai babu wani hijabi da ya tarewa daya gannin tsiraicin daya, zasu raya sunna ce mai tsafta da tsayawa a rai, zasu zama abu daya ne , zai kasance sun samu nutsuwa da junnansu ne ta yadda a duniyarsu babu wani abu kuma da ya rage da zai zamo boyaye ko bako a garesu, na biyu ki fito min a mutun ki min maganar tsakaninki da SIR HANJA, na uku daga nan gidanku na nufa

domin nawa iyayen sun yi tafia paris dan visite na rashin lafiyar mahaifina, kafin su dawo ba zan je gidanmu daga ni sai mai aiki ba , ba kuma zan kama h□tel ba"

Muneerath ta dafe gaban goshinta itama cike da rikicin magangannun kawar tata, ita har ga Allah abin daria nema yake bata, kuma dukan abubuwan da ta zayana ta yi masu waje ne ta ajiye su a irin tsabagen kula irin ta Familly din Su Pah

Gaba daya sai ta mata shiru ta tada motar, kai itafa abinda ya fi damunta shine tunanin yadda za'a yi Ta samu waje a gidan Oga ba tare da an kai ruwa rana ba

Cike da shagalta da kallon garin haihuwarta, wajen da ya tara iyayenta kakaninta, danginta take tuki har ta dauko duguwar hanyar da zata sadata da kofar gidansu

Abubuwan da suka cenza a garin basu da yawa sosai, sai gine gine da ta ringa ganni sai gyaran hanyar da aka yi wanda idan za'a hada da kasar da ta fito ne babu mahadi, sai dai abinda yake tsaye a kasan zuciyarta irin farin cikin dake daskare a zuciyarta ya wuce tunanin bawa

A hankali ta yi kwana ta samu ta dakata dan nesa kadan da gidansu tana karra wara dubanta a kan wanda idannuwanta ke ganni

A hankali kafafuwanta suka dan fara yi mata rawa rawa, zuciyarta ta shiga dokawa da dukan karfi, zufa da tsoron da Saudat bata taba ganni ba a tatare da Muneerath ya bayana a tare da ita

Tabas da take ce mata idan tana so ta ga rauninta ta bari idan tana kusa da ahalinta

A hankali ta ce" Muneerath ? "

Muneerath ta juyo da sauri tana kallonta ta kasa amsata

A hankali ta ce" Ina ne gidan? Kin ja kin tsaya jikinki na rawa kin kafe wancen mutumen da kallo?"

Muneerath ta hadiyi yawu a hankali tana karra jimke hannunta dake saman cinyarta a sanyaye ta ce" Oga ne cem tsaye, wannan tsayuwar da Oga ya yi idan aka tabo shi ne, ni kuma bana so na fado daidai ran oga a bace, kin ga tsayuwar cen da ya yi ko dansa ya taba shi zai ga ikon Allah, ga kuma gidan namu a bude ham ban san me yake faruwa ba"

Da mamaki da kuma tausayi ta karra kallon gidan da Muneerath ta fito, a kasan zuciyarta ta ayanna 'Lalle babu mai daukaka bawa sai Allah'

Ajiyar zuciya ta sauke ta ce" To ki tada motar mu karasa mana"

Ido ta zarro ta ce" Wa ni?, Na je gaban oga da motar nan a haka mu yi kaka da shi?, Kin ga mu juya kawai mu koma karma idannuwansa su juwo kaina a haka idan ya bar kofar gidan sai mu dawo"

" KUT Walahi baki isa ba!" Saudat ta ce , da sauri ta kama marfin mota ta bale ta fita kai tsaye ta durfafi wajen da Oga ke tsaye zuwa lokacin ya ga tsayuwar motar duda bai kure su da ido ba aman haka kawai ya ji zuciyarsa na yawan son ya kalli motar

Da sauri Muneerath ta fito tama zarro ido ta ce" Kan balaki, Saudat ki fa bar balaki ya yi barci , karfa ki yi garaje fa"

Wani marfin langa da aka jefo daga anyar kofar ya saka Saudat ja da mugun sauri tana kallon wajen da kuma hayaniyar dake fitowa sama sama

Kafin ta idasa fahimtar komai wani uban dutse ya biyo baya ya sauka a kusa da kafarta harma ya shafi yar karamar yatsarta

Da sauri Muneerath ta ja hannunta gefe ta nemi nausuwa cikin gidan ranta bace, sai dai kafin take idasa saka kafarta aka yi baya da ita

Wani wawan mari dayar ta kifawa daya, da gudu suka karra kurmiyar junna sunna dukkan junna da kokowa

Oga dake tsaye dadage yake dan gannin wai da gaske abinda idannuwansa ke gane masa ne? Gannin ta shige cikin al'umar gidansa ya saka shi nufar Saudat da ta yi mutuwar tsaye tana kallon ikon Allah

Da sauri Saudat ta rufe fuskarta dan tsoro ne ya shigeta kar a je Oga ya wanka mata mari

Oga ya kare mata kallo ya ce" Ke dillah bude idannuwanki ki fada min wannan yar wacece?, Kamar kamar y'ar oga sai dai abin mamakin kalar fatar wannan ba ta africa bace sam sam"

A hankali ta bude idannuwanta tana kallonsa da tsoro, ta kuma hangi Muneerath ta hakikance a cikin yan uwanta ba mai ba yar uwarta hakuri domin a fadan harda kanwarta ana ta dakuwa

A dan tsorace ta ce" Eh Muneerath ce"

Sai da ya kwalalo ido kafin da sauri ya nufe su

Da wani yannayi irin na yan daba ya ringa eartarsu da daidaya yana kifa masu mari yana maida su gefe da gefe kafin a haukace ya ce" Zaku nutsu ko sai na kira police ya kwashe min ku baki daya na huta da jaraba?!"

Du wajen ne ya dauki shiru sunna kallonsa koea na huci tamkar kububuwa

A dake ya ce" Yar oga? "

Muneerath dake tsate rike da kanwarta gaba daya sun kara tara mata gajiya sai da gabanta ya fadi da sauri ta kale shi kafin a raunane ta amsa still tana kallonsa

Du da mamaki suka juyo suma sunna kallon nata lokaci daya ana kare mata kallo tun daga kasa har sama

Daya daga cikin matansa ne ta saki buda tana rike dan karamin hancinta ta ce" Lale bariki ta yi rana, wai dama wannan Muneerath ce? Tabdijan iskanci ga mai daure maka gindi a gidan Oga!"

Muneerath ta budi bakinta zata yi magana idannuwanta suka sauka a kan fuskar mahaifiyarta

Shigar maman nata ta so ta bada mata ko wacece, sai dai irin yannayin da ta tsareta da duba ya sakata karra kallonta da kyau

Oga ya yi juyi ya kuma juyowa cike da mamaki ya ce" Wai yar oga da gaske dama a ingilar kike? Muhamadu rasululahi salalahu alaihi wa salam na shiga uku, wai yanzun ke din nan Hostess ce? Walahi ni du a tunanina kin hadu da wani dan iskan ya gama hore maki kunne irin na yar uwarki, Yar oga yanzun daga ina kike? Na shiga uku dama na san zuciyar nan taki tawa kika gado idan nace sai na yi sai fa na yi, gatanan Babarki da na ganta na nace sai ita na kuwa bi ta inda na bi itama ta haukace sai ni aka aura mata ni iyayenta suka yi fushin zuciya da ita suka salama min na rungumo abina gatanan wai yanzun ta saku ta daina sona aman saboda ke take zaune ta ga ta inda zaki dawo yau gaki Allah ya dawo min da ke shikenan sai ta daina fushin ta fuskanceni mu fuskanci junna"

Da rashin fahimta take kallonsa tana son karrin bayani, sai dai bai bata wannan damar ba ya shiga kora yaren cikin gida

Ruuuuuuuuuu da su da iyayensu suka aniya nufar cikin gidan

Lokaci daya ya dakata ya tsare matan biyu da suka yi saura wa'inda ke dakuwa da junna ya ce" Kai,hala da nace na sake ku a tunaninki wasan yaa nake?, Ke delu dama saki daya ya rafe mana na cikashe maki shi, ke kuma sarai ai biyu na baki a jimulce dan haka ba sauran zama da ni da ku , ku kama gabanku jarabar ta isheni haka, inm lalatace ne ni da saka hannun matan nan, kun mayar da ni kamar dan dambe ni kunlum ina cakuwa da mutane ana abu kamar yam wiwi, ni ban ajiye ba ban ba wani ajiya ba, to ku sani na gaji iya gajiya, y'ayan oga kuma ku barmin su zan iya da fitinarsu, ke Bakuwa shigo mana na raka ki bangaren su Yar ogan"

Da sauri Saudat ta daga kafa ta karasa ya ja hannunta ya turata ciki ya rufe kofar harda saka sakata kafin ya ja ashar da rantsuwar du shegen da ya bude shi da shi ne kafin ya tisa keyar Saudat da ta gama gane cewa lale Muneerath din yar ogan ce, sai kuma ogan ke iya mata

A tsaitsaye suka same su a falon Mamansu

Muneerath na tsaye tana kallon mahaifiyarta cike da mamakin yannayinta

Oga ya yi dan gyaran murya yana dan wani abu kamar wanda yake tsoron shiga kai tsaye ya ce" To ki zauna mana wai tsayuwar ta mecece?"

Muneerath ta juyo tana kallon Oga ta kuma kallon mamanta

Mahaifiyarta ta dube shi a kausashe ta ce" Me kuma kake so Mutari?, Dan Allah ba sai ka shigo nan ba ka tafi kawai na ji da y'ata ta fada min a infa take! Ka koma ka barni da ita idan takamar y'ayanka ana masu taken sun gado rashin mutuncinka yau ta dake ni sai na san na hada jinni da shedan!"

Da sauri Saudat ta juya zata fita a dakin Muneerath ta yi gagawar kamo hannunta ta janyota ciki

A hankali Muneerath ta kalli Mamanta mahaifiya a gareta muryarta a sanyaye ta ce" Sai nake gannin kamar kin damu da son sannin daga inda nake, ko kuma kina son sani ne dan ki wulakantani?, Inace Sir ya shaida min an yi kira na nemi alfarmar a bani ke kin nuna ba sai kin amsa ba kawai na gaishe su?, Shin kin manta burina na

son zama hostess da nake kwana da shi nake tashi wanda kika ce min ni mahaukaciya ce?, Ko kina son ce min a yanzu kin san darajata bayan na rayu da ke cikin rayuwa ta halin ko'in kula wace baki san darajar kowa ba sai oga?"

Idannuwanta dake rintse tana sauraron datata mangangannun yarta ba taunawa ta bude rai bace ta dauke Muneerath da wani gigitacen marin da ya saka Oga yin tsuru tsuru har cikin zuciyarsa ya ji amsa kuwar marin kafin da sauri ya shigo gaba dayansa yana rike Muneerath din da ta buda idannuwanta da har suka fara yi mata ja tana kallon Maman nata

Rai bace mahaifiyarta ta ce" Ki sada dubanki a cikin nawa kafin na saka yan yatsuna na kwakwale maki ido na zubar a wajen nan Muneerath !, Ki tausasa kalamanki a kaina tun kafin na koya maki yadda ake furuci wa mahaifiya!, A yau idanma karuwa ce ni, idan yar shaye shaye ce ni, idan mahaukaciya ce ni , nisawa na yi kika tsago jikina kika fito....kuma a haka da haukan nawa da iskancin nawa na shayar da ke na suturtar da ke!, Idanma kakan tsatson marar mutunci kika tsago kika fito ki kula ki tausasa muryarki a kaina in ba haka ba komai na iya faruwa ciki harda rasa harshenki domin ba zan maki baki ba ni, sai dai na ringa tsinguyar naman jikinki daya bayan daya har na karar maki da su!"

Oga da idannuwansa ke rintse da bacin rai da abubuwan da matar tasa ke yi ya budi baki a sanyaye ya ce" Me zai hanna mu samu kebewa mu tatauna a nutse ta yadda kowa zai fahimci kowa ne?, Kina gani fa daga doguwar tafia take"

Da dan daga murya, da bacin ran da take ciki ta juyo a hasale ta ce" Dillah ka rufe min baki azalumi, maci amana wanda ke raba y'aya da iyaye da kowa nasu dan cikar burinsa!"

Wani marin ne ya sauka a jar fuskar mahaifiyar Muneerath wanda hakannua saka Saudat kaiwa kasa saman gwuiwowinta cike da tsoron al'amarin dake faruwa

Shima yanzun cikin daga murya ya dubeta cikin ido ya ce" Ya isheki haka!, Na ce ya isheki haka kin ji? Na yi, na je na yin!, Me yasa a lokacin da na zo wajen ki da maganar soyaya dan kin ganni a kafa na yi aski irin na gayun zamanina kika tofa min yawu a fuska kika aibata ni kika nuna gidanku da irin motar da kike tukawa ta alfarma kika ce da ni aman mahaukaci ne ni kuma bani da magaya ko?, Kika aibata min iyaye kika aibata min dangi kika nunan ko akuyar gidanku ta fi karfin na yi zaman aure da ita bale ke yar gata mai gata gaba da baya?, A kan me da na zo baki yi min maganar kirki kika rabu da ni ta sigar da ta dace ba sai kika wulakantani mafi munin wulakanci harda watsa min ruwa dan na nemi soyayarki?, Ni bana tare da kuruciya ne ko bani da zuciya a cikin kirjina aka fada maki ?, Walahi walahi ban taba son mace kamar yadda na so ki ba, a kan dole dan na rayu da ke na kuma koya maki hankali na maki asirin da na raba ki da danginki da duniya baki daya ya kasance a duniya idan ba ni ba bakya gane yaren kowa, idan ba soyayata ba bakya fahimtar ta kowa, sai dai halayanki na yawo wajen biki wannan ba ni na dora maki ba, idan kika auna izina ce ta hau kanki Allah ya nuna maki shi ke shiryarwa, kin zageni da dan iska dan kawai na zo a shiri irin na yan gayun da basa jin magana, ke sai gashi da aurenki kike yafa dan gyale kina shagalinki duda na yarda cewa ba maza kike bi ba aman yawon ta zubar din da kike Allah ne ya nuna maki !, Ba zan iya ba, walahi ba zan lamuncewa kowa ya wulakanta yar oga ba, Halina kuma da kike zagi cewar mugun tsatso mugun hali na ji na dauka, ni dai bani da hali irin na izgili!, Idanma a yanzu kike son koyawa y'ata ladabi ki bita a sannu kar ki rikita min ita domin kaf cikin y'ayana zan iya rantse maki ita kadai nake iya shama kur'ani!"

Yana gama fada ya juya har yana gannin duhu duhu a idannuwansa ya fito, nan fa ya ga y'ayan yan mata sun layu sunna saurare hakan ya saka shi tsayawa ya kare masu kallo gannin sun yi tsuru tsuru ya ce" Kowace ta fida mijin aure nan da sati biyu in ba haka ba in ban yi sadaka da ku ba ku ce min shege!"

TABDIJANNNNNNNNNN
11/14/21, 12:52 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 4 □□□

Marin da ya wankawa matar tasa tamkar wanda ya saka mata sakata a bakin nata ya gume mata
Koda yake a kalamansa ta samu yaren shiru ta arawa kanta kafin da sauri ta juya ta nufo dakinta jikinta na bari ta rufo
Zamewa ta yi nan kasa hannayenta na rawa baki daya ta kurawa waje daya ido
Tabas an yi haka, a hankali ta shiga tunano ranakun da take shiryawa ta fita gari idan kucakin namijin da bai amsa sunnan namiji ba ya yi gigin tunkararta ya nuna mata so irin tizga ahin da take yi, ba zata manta ba har kara koyon karatun wulakanta namiji take yi
Ba zata taba mantawa ba ranar da ya nuna yana sonta har ruwan bakinta ta furza masa domin a lokacin har kiransa ta yi da wani muninsa kamar gwogwon biri, ba zata manta tana masa diban albarka yana share zufa yana karra kallonta har ta dire aya ya ce da ita dan tana da kyau kuma tana yar mai kudi ne take masa irin wannan wulakancin ?, Shin shi ba dan adam bane ko ta ga alamun a halitarsa an rage shi da wani abu?, Dan ya zo ya nuna mata so sai ya kwashi kashi irin haka a hannunsa?
Ba zata manta irin hucin da abokinsa ke yi ba yana fadin Oga ka barta a gidan nasu mu nuna mata muma irin namu ikon, aman sai ya ce da su wannan ta haramta wa

irin haka a gare su, wannan din ajiyar oga ce, ta oga ce kuma sai ta haifawa Oga abin alfahari!

Wani kukan ta kuma rushewa da shi na dana sannin mugun halaya irin na yan mata masu jiji da kai da neman fitina da tunanin su sun fi kowa
Ashe ita ta janyowa kanta wannan rayuwa?, Gashi dai sanadiyar rashin lafiyar da ya yi ya karya abinda ya mata da kansa wanda yana da makarin tsayin shekarun nan wanda tamkar wace ta yi barci ta farka ta ganta da shekaru zagaye da ahalin gidan Oga masu wuyar fasara
Hauka jajir ta zuba masa a sume ya kaita gidansu nan ta tarar da sai yayanta daya rak da iyalinsa mahaifinta ne dama ya rage mata shima ya rasu , bayan ta sanar masa komai ya karra yi mata nasiha ya lalabata kan a yanzu gidan mijinta shine kwonciyar hankalinta ta rungumi y'ayan da ta samu da shi ta yi kokarin basu tarbiyar da ita ta yi wasa da ita, koda kuwa Oga ya kasance mai baudaden hali da damansa a kan wani, tunda shi aurenta ya yi ya kilaceta , da wani ne a hakan zai aifata ya kuma murje ido ya mayar da ita dakin ziyararsa, duniya ta yi lalacewar da baka yiwa mutun komai bama yana son ya kasaraka bale ita din ta yi garaje da yawa, dan haka ta kula ta kiyaye ta yi hakuri Oga kansa tana iya mayar da shi yanda take so koda iya cikin gida zai dawo tausasashe wa su a waje kuwa a ogansa yake da kyau, dama shi rayuwarsa ta yan jagaliya ne shi ba barawo bane ba kuma mazinaci bane, da kyau a halayansa akoy na kirki tunda yana sallah ai a yi masa uzuri, shima kuruci ta saka shi aikatawa, duda hali na kuruci zafin sonki ya saka da ya maki hakan bai yarda makarin ba, a yanzu da lokacin ki dawo hayacinki ya yi kib ga ya karya gaki kuma da ranki da lafiyarki ,sai dai a karra yi masa adu'a Allah ya shirye shi, ya ahiryar masa da zuri'arsa

Ta ringa rusa kuka a lokacin tana shaida masa batama san inda Muneerath ta shiga ba, ya ce Wai ta samu aikin Hostess aman bashi da tabas tunda bai je ya gani ba, wai a waya aka fada masa a waya, kuma yake zaune hankali kwonce y'a mace?, Ita kam ba zata iya zama da mutun irin Oga ba, zata koma aman da zarar yarta ta dawo zata kwaso y'ayanta ta dawo gidansu

Shi dai rarashinta ya yi ta yi, a nan ya kwaso mara tsabar dukiyarta da aka raba gado ya jingine da takardun gidaje har kwaya biyar, da kudin dake banki milioyi na gadon da suka gada ita da shi a wajen mahaifinta, ya dora mata da fadin gadon Mahaifiyarsu bai taba zuwa inda suke ba, kasancewar kasa ce ta nasaru shi bama shi da ra'ayin bin kudin nan da dukiyar, wanda yake cikima sun ishe shi

A hankali ta kara rike kanta dake sarra mata tana wani kukan na takaicin rayuwarta, tabas ta yiwa kanta ila, yanzun ta ina zata fara da tarbiyar y'ayanta?, Har yanzu ba wani jituwa suke da namijin ba, matan kuma su uku ne du a wani bambarakwai suke kallon cenjin da ya samu, aman ba komai kamar yadda datijuwar malamar islamiyar da take zuwa take fada mata cewar adu'a, da adu'a zata Wayi gari ta ga abinda yake impossible Allah ya mayar mata da shi possible, Oga kansa halita ne na Allah, akoy masu kashe kashe da suke dawowa su zamo tamkar basu taba yi ba, idan har ta jure kaima Allah kukanta kokowar da ya dace ta dankara a tunaninta tana barci Allah zai yi mata shi ta hanyar shiryar mata da zuri'arta baki daya

Tuna wadinnan abubuwan ya sakata saurin mikewa ta shige bayin dakinta dan ta dauro alwallah ta hau salayarta har a yi kiran sallah

Saudat dake tsaye a tsorace tana kallon Muneerath jira take ta fashe da kuka ta yadda otama zata samu ta fashe da shi na tsabagen tsagwaron tsoron dake cin zuciyarta na wannan hargitsi da aka yi

A hankali ta dora hannunta dake rawa a hannun Muneerath a sanyaye ta ce" Munee kar ki yi kuka kin ji?, Dan Allah mu je idan ta huce sai mu dawo ki bata hakuri kin ga ba'a yima iyaye magana a haka, ki ga mu yan africa ne da mari iyayenmu ke nusar da mu ba da rarashi ba, mu je idan ta huce sai mi dawo ki yi hakuri"

Da mamaki Muneerath ta juyo jin wai karta yi kuka tana kallon Saudat
Me zata yi banda dariya, ai kam ta bushe da daria tana jan hannun Saudat da ta fara kokonton anya ba Allah ne ya hada ta da mahaukaciya kawance ba?

Dakinta ta jata mai dauke da gadonta daya sai sif din kayanta

Sunna shiga ta rufe ta saka hannunta ta kunce yalwatacen gashin kanta ta barbaza shi sosai ta zauna a kasa nan tana kara cusa hannunta cikin gashin kan nata kafin ta dago ta kuma yi yar dariya tana girgiza kanta tana kallon Saudat da ta kasa zama dan a tsorace take ta ce" Kin san me hakan yake nufi?, Kin san me wannan ranar take nufi a wajena?, Wannan ranar tana nufin babar ranar da ban taba riska ba mai dadi da farin ciki, wannan ranar itace ranar da nima zan fara tinkaho da kaina, kin kuwa gane me nake nufi?"

A hankali saudat ta girgiza kai tana kallonta

Muneerath ta nuna mata gefenta tana nufin ta zauna

A hankali ta zauna a gefen na Munnerath din

Muneerath ta kamo hannunta ta ce" Saudat, a da ba tafia ba idan namiji zan kawo a gaban Mamanmu walahil azim zata kare mana kallo ta cire kanta ne ba tare da ta fahimci jinsin namiji na kawo mata ko mace ba, ke bara na kare maki magana idan ana magana aka ce min yar iska sai ta daga kafada ta ce ita ina ruwanta in ina so na zama karuwama matsalata ce!, Saudat idan kin ga na yi doguwar magana da mahaifiyata to fa a kan kudi ne, shima kudin da take nema ido rufe dan kawai ta siyo maganin mata ko me? Ta kawo ta yi ta sha wanda ban san ko na menene ba, ita dai idan kin ga tana kwalkwaltu to fa dan ta gyarawa Oga ne, a kan Oga tana iya batawa da kowa, a kan Oga tana iya kisa, Saudat nakan yi kuka na tsayin wuni guda ina tambayar kaina me yasa ko irin na sauran yan uwana da zaki ga idan abu ne iyayensu sun shigar masu fada ne ko idan aka zagar masu y'aya iyayensu na tarewa ni tawa uwar sai dai ta taya mutanen a zage nin?, A lokacin da na kawo maganar ga wanda nake da burin aure watau sarki da mamana aka wuni ana min daria ana cewa mahaukaciya ce ni, daga karshe suka ce gwara na kama dogari marar galihu idan Allah ya tsaya min ya ji tausayina sai ya aureni, dan kuwa ba wanda zai so kirtitinar bak'a irina!, Saudat a dayan burina da na nuna ina son zama Hostess kishiyar mamana ta ce sai dai na zama karuwar yan gugan gidan jirgi idan na yi daraja, walahi a gaban Mamana ta fada sai kawai maman nawa ta yi daria tana fadin wa ya ga yar baka kirin, gaskiya Oga ya yi haihuwa a nan, a wannan ranar ce da abin ya min ciwo muka kidime da fada a gidan nan da yayuna domin aun samu abinda suke so, oga na zuwa ya raba mu aka fada masa komai ya ce du ubanda ya kara shiga harkata walahi zai iya yin komai, a ranar ne ya dauke ni ya biya min kudin koyon iyo, sannan yake bani yan kudade a kai a kai dan na yi yan bukatocina, ya ce koda ban zama ba na gwada"

Muneerath ta dago da idannuwanta da suka cika da kwallah sosai tana kallon Saudat dake hawaye ta ce" Ashe nima zan ga ranar da mahaifiyata zata daga hannu ta dake ni dan gyarana? Ashe zan ga ranar da Umana zata titsiyeni kan na fada mata daga ina nake?, Ashe zan riski ranar da mamana zata daga dan yatsarta dan ina cikin damuwa?, Saudat a nan ake fada ni da fada mutun fiye da bakwai tana tsaye tana kallo ba zata yi magana ba bale ta shigar min , ashe dai mamana na cikin duhu ne ya sa na ga rayuwa irin wadda na gani.....? Ta karashe maganar da fashewa da kuka mai zafin gaske tana dora kanta a gefen kafadar Saudat har tana jijiga gaba dayanta dan abin daga kasan zuciyarta yake fitowa, daga cen kasan zuciyarta take jin wuyar abinda ke damun nata wanda take jin yana sakinta a hankali a hankali

Karar bude Kofar ya saka su yin tsit da sauri Muneerath ta dago kanta

Ido hudu suka kuma yi da mahaifiyarta dake dauke da wata babar jaka shake da dinkunnan atampopi da ta ringa dinkawa Muneerath din a lokacin da bata nan

Cire dubanta ta yi a kansa ta karasa kuda da gadon Muneerath din ta yaye shinfidar sama domin ta yi dati sosai ta juyo wajensu muryarta a dan dake ta ce" Ku tashi ku yi wanka ku dauro alwallah ku gabatar da sallar la'asar kafin lokacinta ya shige, idan kun gama ku fito dakina ga abinci ku ci, so nake kuna gama cin abinci ku gyara dakin nan sosai ku wanke bayin ku cenza katifar Abdul ya tafi ya siyo sabuwa sai ku cenza wadinnan wandunnan dake jikinku ga atampa nan ku saka maza mu je saloon a maku kitso, kar na dawo na tarar da ku zaune a nan"

Tana gama fada ta juya ta fice inda Muneerath ta bita da kallo cike da wani mamakin da ya kusa kasheta da farin ciki marar musaltuwa har sai da saudat ta ce" Kin ga tashi wollah kar ta dawo ranta ya baci kina zaune uwa sakarai".....

RAYUWA KENNAN

BAYAN KWANA SHIDA

KASAR INGILA

A tsakanin kwanakin nan sun gabatar da rayuwa cikin wani yannayin da basu saba ba sam
Yaronsu dake gefensu ya zama gashi a cikin gidan aman kuma tamkar baya nan
A tsakanin kwanakin nan ya yi tafia sau uku wace yake yin zuwa da dawowa bai kwana ko daya ba
HANJA na acting tamkar ba abinda yake damunsa sakamakon abinda mahaifinsa ya yi masa, sai dai abinda bai sani ba bai taba gabatar da rayuwar nesanta kansa da su ba irin wannan
Mah ta yi nacin bin, ta yi nacin kiran, ta yi fadan da tambayar shin lafiyarsa?, Sai dai a kulun amsar daya ce abubuwa sun sha kansa bashi da time
Yakan kwatanta yin hira da Tgr sai ya samu kansa da mamakin kansa da tunanin to amsa zara bashi ko me?
Sau biyu yana yarda da haduwarsa da yar gidan ministа sai dai abin takaicin yarinyar sam bata da ra'ayi nata na kanta, ko zance suke abinda ya gabatar shine gaskiya koda da gangan ya gwada nuna mata akasin tunaninta takan zubar da nata

tunanin ta dauki nasa, a haka ya nuna mata yana da butakar kwonciya da ita abin mamakin ita ta kama masu waje ta gyara komai sannan ta ringa zumudin irga lokacin da ya rage ya kwonta da ita
Wannan lamarin ya daure masa kai, sai kawai ya girgiza kai yana saka nimbobinta a black list yana jin takaicinta tare da tuna yarinyar da koda wasa ya nemi taba mata hannu ko a cikin malagigin wuya na tsoro take in dai hankalinta na jikinta sai ta bige masa hannunsa tana jaraba
Kai koda da gangan take yi hakan na birge shi, hakan na nufin ba zata iya gagawar yarda da namiji ba koda kuwa saurayinta ne
Aman ita gashi soyayar bai rigaya ya furta mata ba, yana dan kulata ne yana auna magangannun soyayarta da take nuna masa aman a haka ya nuna mata zai kai keyarta kasa ya yi wasan kura a jikinta ta aminta harma take zumudi?
Walahi sai KYANKYAMIN HALAYA IRIN NA MAZINATA ya darsu a zuciyarsa, watau su basa kyamar wutsiyar kowa kuma basa auna da wa zasu kasance da irin lokacin da ya kama a gabatar da abin? Burinsu a taba su kadan su bude sket kowani kazami ya danna kansa a ciki? Su basu da fid□lit□ ? Kowama nasu ne, a kan yan kudade sai su yi, haka kuma a kyauta sai su yi?

A yanzu da yake zaune saman bed dinsa karfe bakwai ne na dare yana kallon waje daya ba tare da ya san wa yake kallo ba

Tunani ya yi masa yawa, ya kasance mai yawan tunanin abinda bai san dalilinsa ba

A hankali ya dauki katuwar wayarsa ya shiga wajen vidio dan ya yi kallo ko zai samu abinda zai dauke masa damuwarsa duda shi din ba mutun bane mai son yawan kalle kalle

Vidio din da ake ta turo masa sunna bude kansu ta whatsup ya shiga bi daya bayan daya wa'inda ba wani mahinmanci sai kawai ya goge

A haka har ya sauka kan vidion birthday dinsa da Mah ta yiwa su Muneerath ta tura masa

A hankali yake kallon abinda suka yi, wani lalausan murmushi ya samu damar sauka a kan lalausan lebensa a lokacin da suke dirkar rawa , inda rawar ta fi yawa a kanta

Wajen da ta kykyace da dariyatana shafawa sauda crem ya samu kansa da maidowa koda ya wuce

A hankali ya ringa murmushin shima yana dafe daidai zuciyarsa
Idannuwansa ya lumshe yana tunanin idan bai ganta suka yi rigima ba ba zai iya rintsawa ba

Zai iya rantsewa bai taba jin missng din mutun irin yadda yake missing din yarinyar nan
Ba shi kadai ba har a wajen aikinsa sunna missing din yarinyar bale a nan gidansu

Da murmushi ya yi a bayane ya ce" kanwar da nake son samu ce ta fito min daga africa, me take yi? A ina take kwonci? Me take ci? Da wa take hira?, Ya zama wajibi na saka a sakata cikin masu tahowa zuwa indonesia"

A hankali ya mike daga zaunen da yake da wayarsa ya fito

Yana saukowa ya hango su zaune saman diner, a kan dole ya nufe su domin sun rigaya sun ganshi

Da kallon kula suke binsa har ya zauna a gefensu

Fuskarsa ba fara'a a yanzunma haka kuma da Mah ta gabatar masa da abinci sai ya nuna a koshe yake

Pah da yannayin taurin kan yaron nasa ke damunsa tamkar wani DUTSE yana jin duka ya ki ya rugurguje ne ya ce" Dazun mun yi vidio call da Muneerath"

Da sauri ya dago da dubansa, cikin gagawar magana ya samu kansa da fadin" yaya take, a ina take, me take, su waye suke tsaronta, tare da su wa take, Attahir dai yana kasar nan shin yana damunta da kira ko?....." Sai kuma ya yi zuru zuru yana kallonsu , sai da ya gama magangannun ya ringa aunawa a ma'auni

Jikinsa a mace, idannuwansa sun dauki launin ja ya samu kansa da furta" NA SHIGA UKU"

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

SAKO ZUWA GAREKU MAKARANTAN DUTSE, IN SHA ALLAH POSTING ZAI DAWO SAU BIYU A SATI, WATAU LITININ DA ALHAMIS SAKAMAKON NOVEL DINA NA KUDI MAI SUNNA WATA KOKOWAR DA ZAN FARA POSTING RANAR LITININ IDAN ALLAH YA AMINCE, NA GODE SOSAI DA KULAWA.....DOMIN SAMUN NAKI KO NAKA KA TUNTUBENI A NUMBER WAYATA KAMAR HAKA +22793811618, A FARASHI MAI SAUKI NAIRA DARI BIYU 200..... IN SHA ALLAH ZAKA SAMU NISHADI DOMIN SALON NA DABAN NE

DAGA YAR MUTAN NIGER sajida □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 5 □□□

Murmushi ne kwonce a kan fuskar Pah, inda damuwa ta bayana a kan fuskar Mah

A hankali ta kamo hannunsa tana kallonsa da kula ta ce" ba fa faduwa bane dan ka yarda cewar kana cikin soyaya, Son ba faduwa bane dan ka yi kokarin gyara soyayarka, sam bana so ka zamo mai wasa da damarka , Son idan ka yi sake da maganar Muneerath bana tunanin in ta juyar da muradinta ta yarda da shi a kan wani in zaka iya karkatota ta dawo gareka, ka ga , ga number mamanta wace na samu tun a daren da na yi rashin lafia da kuma number mahaifinta, numberta ta cen ce a wahen Pah dinka na yi na yi ya bani ya kiya ya ce sai ka nuna kana so da kanka, plz Son kar ka rikita ni , damuwarka na damuna fiye da tunaninka"

Idannuwansa dake lumshe yana jin gaba daya magangannun mamansa na samun matsuguni a cikin zuciyarsa kafin ya kaleta a hankali yana karra karantarta

Kansa ya maida kan mahaifinsa da ya ga shi yake kallo kafin ya dan yi gyaran murya a nutse ya ce" Pah, maganar taron nan naku da Allah ka halarci abinka, ka ga inada tafia a satin nan mai yawa plz"

Hankalinsa ya bashi kacokam duba da magana ce mai mahinmanci wace yake so ya halarta taro ne na manyan sarakai da matansu da zasu halarta a cikin satin nan , tunima sunna kasar shine bai basu lokacin zama da su ba, kuma so yake a yi zaman da Hanja aman yake son kara zile masa kamar yadda ya saba, shi kam bai san dalilin da ya sa HANJA ke zilewa sarauta ba, wannan abin na hadasa masa ciwon kai da zafin kai mai tsanani, Hanja shine kadai gareshi kuma da shi kadai yake takama, shin yaya zai yi ya taro shi ne? Dukkan hanyar da zai bi dan ya ginar da shi ita yake bi, ko ba maganar rashin lafiyarsa dole zai bashi kujera ya hau ya gabatar da nasa zamanin, shi yasa daga ranar da ya ga yarinyar nan ta saka shi magana ya ringa farin ciki
A yanzu haka idan abu ya shafeta irin yadda yake magana fiye da misalin yadda ya saba ke saka shi tunanin tabas wannan itace wace zata budi bakin birkitacen yaronsa ta koya masa magana da kowa , ba halaya na yadda ya ga dama ba bayan ahi din sarki ne wanda dole zai saurari al'uma, a yi mulki a yi isar a kuma tausayawa talakawa
Dan haka yau zai cenza masa ya fara zuwar masa a kaisashe dan ya ga kuma yaya zata bada, dan haka sai ya kure shi da duba a kausashe ya ce" Saurara Hanja, wannan tarron ba shawararka nake na ba, umarni ne na baka kan kai zaka halarce shi! Dole ne kuma kai zaka halarce shi, idan kana so ba a satin nan ba kana iya saka

rana ka halarce shin, fa wayata nan ka cire numbobinsu su hudu ne, idan ka saka rana sai ka sanar masu da wajen da kake ra'ayin ku yi tarron!"

Yana gama fada ya ajiye wayar ya mike fuska a hade ya yi gaba

Da kallo suka bi shi su dukansu kafin Mah ta dubi Hanja

Sai da gabanta ya fadi gannin irin bacin ran dake kwonce a saman fuskarsa

Ta budi baki zata yi magana ya mike a fusace ya juya ya nufi kofa hakan ya sa ta mike tsaye da sauri tana kallonsa har ya bar falon gaba daya

A hankali ta zauna tana dan dafe cikinta dake mugun murda mata kasa kasa sai kuma ya saka tana lumshe idannuwanta
A hankali ta bi hanyar da Pah ya bi da kallo tana mai tunanin Me ya yi haka? Me yasa bai bari ta lalaba shi ba kamar yadda ta fada masa cewar ya barsu ta lalaba abinta zai halarci tarron? Me kuma ya sa ya ce da ita tare zasu gabatar kuma yanzu ya nuna Hanja kadai zai gabatar?

Kanta ta sada tana dan barin jiki na irin murdawar da cikinta ke yi har ya lafa kafin ta mike a sanyaye tana jin yadda jikinta du ya mata wani irin nauyi

Hannunta ta mika ta dauki wayar mijin nata a hankali ta shiga contact dinsa

Sunnan da ya yi svng din number Muneerath ta kuma maimaitawa tana murmushi watau shi har ya ganta a matsayin matar yaron nasa ko? Domin da Wife LION ya saka sunnan

A hankali ta dannawa number kira ta karra a kunnenta
Maimakun ta bi ta lft sai kawai ta bi ta wajen matatakalar tana takawa a hankali har aka daga kiran

Salamar da Munnerath ta yi ya saka Mah dan zarro ido tana murmushi ta ciro wayar daga kunnenta ta kuma maidawa a sanyaye ta dakata ta amsa salamar kafin ta ringa sakin murmushi na irin murnar da ta ji Munnerath na yi tana ta tambayarta yaya gidan me suke yi? Tana missing dinsu, sai dai sam bata ji ta tambayeta mutumen da take so ta fara tambayarta shi kafin ta tambayeta kowa

A sanyaye Mah ta ce" My baby, yaya gida, ina mamanki, ina Abunki da yan uwanki? Ina kowa da komai? Yaya garinku?"

Muneerath dake kallon mamanta tana murmushi wace ta tsaya a kanta da muciya kan walahi idan bata murje miyar yodon da ta kada mata ta kadu da kyau ba sai ta muka mata muciyar nan, inda Saudat ke kwasar dariyar scene din, domin a yau a kicin din mamansu Muneerath din suka kusan wuni a kan girkin tukakiyar shinkafa da miyar yodo, ana yi ana sakewa ta sha dunguri da rankwashi, ta sha wani irin daurin zani sai zufa take tana ihun ta kone maman nata kuwa tana tsaye ta yi murmushi ta sha murrr sunna girkin su uku , sai yan kannenta yan mata biyu da aka saka barar tafarnuwa ne, gyaran daki da wankin bayi

Amsawa take tana cewa mamanta " Mamanmu Mah dina ce "

Murmushi ta saki tana kallonta, domin labarin Mah , da Pah, da Iman, da HANJA har gajiya take da sauraro ba dare ba rana

Wayar ta mika mata sai dai ita bata iya turanci ba, Mah kuwa french din nata ba mai tsayi bane hakan ya sa sai gaisawa kawai suka yi a rarabe kafin Munnerath din ta amsa Mamanta na cike da mamakin wai dama da gasken da sarauniyar ingila suka gaisa? Da gaske sunne suka rike mata yarta haka?

A hankali Muneerath dake daria ta dan fara ragewa tana sauraron Mah

A hankali yannayin tashin hankali ya fara bayana a kan fuskarta a raunane ta ce" Mah, dama Pah bashi da lafia aman na zauna da ku ban taba fahimtar hakan ba?, Mah dama kuma kunna da damuwa bayan kun malaki komai na rayuwa dama kunna iya neman wani farin ciki ku rasa?"

Mah ta yi dan murmushi tana lumshe idannuwanta domin ji take cikin ya fara motsa mata

Sai da ya sasauta mata a hankali ta ce" Muneerath kowani bawa da tasa irin kadarar, You see my baby a haka da muke ciki da za'a ce mu miko komai mu wayi gari Pah ya samu lafia, my boy ya ajiye aikin tukin JIRGI ya dawo ya yi aure ya haifa min yan jikokina da zan iya rantse maki ko baya ba zamu duba ba zamu saki sarautar Ingila"

Da wani mamakin Muneerath ta ce" Mah, dama bakwa So sir na tukin jirgi? Tukin jirgi fa mafarkinsa ne, abu ne da ya fi kwarewa a cikinsa, aiki ne wanda idan yana yinsa yake cikin farin ciki, idan ya bar aikin nan wane kuke so ya kama?, Kuma aure yana da yan mata fa ku masa jan ido ya fitar da mace ko ku masa na dole"

Mah ta yi murmushi a sanyaye ta ce" Baby kin san wanenen HANJA?, Allah ya yi shi mai daraja a cikin bayinsa, domin sarakai sunna da daraja sosai yarinyata, HANJA shine yaro daya kwal da ahalin sarautar babar masarauta ta duniya watau Ingila ta malaka, babu maganar tirsasa Hanja a aikata komai sai dai mu rarashe shi, Hanja yana da dama , yana da mulki mai girma wanda ubangiji ya halice shi a cikinsa, Tuki, aikin karfi ko wani iri ne dan nema ko dan sha'awar hakan ba na HANJA bane, HANJA yana da obligation na al'umar kasarsa, Hanja yana da abubuwan da suka zame masa tilas wa'inda suka daki burinsa, da sha'awarsa suka shigo a duniyar dolensa, My girl HANJA bashi da zabi yana aikin tukin jirgi ne dan mahaifinsa na so ya cakudu da al'uma ya koyi rayuwa da su, Sai dai kashhhh a yanzu haka maganar da nake maki mahaifinsa a yau ya taka da kafarsa ya je ya buga takarda da tambarin masarauta da sunnansa a matsayin wanda ya saka hannu dan dakatar da shi aikinsa, ba zai kuma yin aikin da ba nasa ba, komai sonsa da tuka jirgi ba zai iya fita daga gidan nan ba, baby i'm afrd, ina cike da tsoron abinda ke iya faruwa a yai a cikin gidana, Pah dinku ya dauki zafi sosai ya dadauki matakai masu tsaurin gaske wa'inda na so ya barni na lalashi Son na dora masa nauyin da ba zai iya zubar da mu ba, sai dai bai bani damar ba ya karra dora masa wani hawan jinnin wanda nake cike da tsoron abinda ke iya faruwa, kina gani wai fa ya bada dokar kar a bar Son ya fita daga PALACE"

Muneerath dake saurare kanta ya daure, ta kasa gane me yasa Mah ke mata hira irin wannan ta sirrin gidansu kai tsaye, ta rasa gane me yasa mahaifinsa ke son tirsasa shi, lalle ta ji bashi da lafiya shi yasa yake aon hora ahi zama sarki aman a ganninta a barshi ya yi tukinsa mana?, Lalle yau akoy rigima a gidan nan, ita da kanta ta sani, aman kuma maganar sai ta mata nauyi sosai ta kasa tantance ita me

zata ce a nan? Aman kula da ta yi cewar kamar Mah na mata hirar ne dan ta ji sanyi sai a sanyaye ta ce" Mah, in sha Allah ba zai tada hankalinsa ba"

Mah da ta ci gaba da tafia ta fara zufa sosai na irin murdawar da cikinta ke yi mata a hankali ta ce" Dole zai yi fushi, dama yana cikin bacin rai da rudani na zuciya, Baby he is in love but ya kasa admettre harma ya kai ga abin sonsa"

Haka kawai ta ji jikinta ya karra yin kalau tana kallon yadda mamanta da Saudat ke kallonta domin tun cenzawar yannayinta mamanta ta rage gaz sosai suke kallonta sai kuma irin maganar da ta yi cewar Pah ba lafia ya saka Saudat fahimta ta dan kwatantawa mama a sanyaye shine suke jira ta gama wayar

A hankali Muneerath ta kuma cewa" Mah da me zan iya taimaka maki?, Idan ina yin koma menene dan na taimaka maki ki sanar da ni ba tare da jin wani abu ba, domin a rayuwata kin min rana, Mah kin ga kafin na hadu da ke ban san dadin uwa ba, ban san komai na mahaifiya ba, Mah a kanki na fara sannin kula, da nasiha irin na uwa, Mah a dawowata na tarar da mamana ta dawo hayacinta har yanzu nima wai nice na iya dafa shinkafa na iya abubuwa irin na mata? Mah kin ga....." Sai kuma muryarta ta sarke ta dan fara shashekar kuka ta ce" A dawowana mamana ta ce min Haba Muneerath ki ringa adu'ar samun dace da miji na gari ba wai ki ringa adu'ar Allah karkato da hankalin dogari a kanki, Mah a da fa ita ce ta ce min dama dama dogari ko zai so ni?, Daga ranar nan na san cewa bawa baya yanke rai da rahamar ubangijinsa"

Mah ta lumshe ido tana sakin murmushi da bayanan Muneerath, a hankali ta ce" Ina murna da murnarki my Daughter, ina matukar farin ciki da farin cikinki, plz ki daina kuka kin ji?"

Muneerath ta gyada kai tana ta murmushi a hankali tana jin yadda Mah ke shasheka kamar ta yi gudu ta ce" Mah wai motsa jiki kike?"

Mah ta ja numfashi ta sharce zufa da kyar ta idasa hawa gaba daya ta kara dakatawa tana lumshe ido kafin ta nufi dakin Pah a hankali muryarta ta yi kasa sosai ta ce" Baby, zaki min wata alfarma?, Plz zaki taimakeni ki min wata alfarma?"

Muneerath ta amsata tana sauraron tana dan kwankwasa dakin Pah, sai kuma ta ji shiru da dan mosti kadan

Dan jim kadan sai kuma wani bugawar da karfin gaske ya shiga kunnenta wanda ya sakata saurin cire wayar a kunnenta

Mah da ta juyo a figice ta sauke dubanta a fuskar yaronta ta gansa da wani irin bacin ran da bata taba ganninsa da shi ba kafin ta ankara ya daga hannunsa rai bace ya kuma mugun doka kofar mahaifinsa wanda ya zo zai bude jin bugawar da karfi ya saka shi budewa a hanzarce dan sannin cewa lafia ba wanda zai matsa mugun bugu irin haka

Da sauri ya bude yana bayana gaba dayansa yana sharce ruwan alwallar da ya dauro ya sauke dubansa a kan yaronsa wanda sai da ya ji gabansa ya fadi da yannayin yaron nasa da kuma matarsa dake gefe wada ya kasa fahimtar halin da ita take ciki

Rai Bace HANJA ya dube shi ido cikin ido a kausashe ya ce" A kan wani dalili zaka dauki irin matakin nan da rayuwata?"

DOMIN SAMUN NAKI LABARINA MAI SUNNA WATA KOKOWAR KI TUMTUBENI TA NUMBER WAYATA KAMAR HAKA +22793811618. A KAN FARASHI MAI SAUKI IN SHA ALLAH 200 DARI BIYU TA TRANSFER KO KATIN MTN.....na gode masoyana sai kun zo
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 6 □□□

Da sauri Muneerath ta zarro idannuwanta tana saurare da sauri ta gyara tsayuwarta tana karra nutsuwa

Pah ya fuskance shi a dake ya ce" Dan ni na haifeka, kuma dan na isa da kai, haka kuma dan kai din SARKIN kasata ce ya zama dole ka dauki mulkinka!"

Wani irin duka ya kaiwa kofar dake bude hakan ya sa ta bada wani kara mai karfin gaske muryarsa a kausashen nan ya ce" Kamar dole nake karanta a furucinka PAH! Me maganar da na karanta a page na Facebook din Royal Familly cewar ni HANJA na ajiye tukin jirgi baki daya?"

Pah ya kuma Fuskantarsa shima da nasa jinnin dake gudu a jikinsa da kuma karfin hali da sannin cewa hakan na iya faruwa dama ya shiryawa hakan ya ce" Eh dole ne kake karanta, kuma ya zama dole ka bar bauta wa kasa ta wannan fannin ka kama naka bautar da Allah ya haliceka dominsa!, Lion □□ u'r a king!, Plz ka yi aiki irin na saraki!"

Gaban goshinsa ya dafe ya yi tafia baya kadan ya dawo gaba kadan

Hannayensa ya hade ya jimke yana kallon mahaifinsa, fuskarsa ta yi ja hakama idannuwansa, hannayensa du sun tada jijiyoyi irin na bacin rai hakama gaban goshinsa ya tada wani irin jijiya dake bugawa dal dal dal muryarsa a cinkushe ya ce" Abui, ka sani daraja na mahaifina kake, hakan ba yana nufin zaka ringa min irin haka ba!, Ka dauke min ita dan ka hasala ni, ka nesantata da ni dan ka birkita ni, shin dan Allah ya baka dama a kaina ta uba shine kake son halaka ni?, A yanzu ka saka ni shiga abinda bana ra'ayi, sarauta ka ba dan uwanka mana? Idan yana so ya kona kasar matsalarsa ce muna iya bara masa kasar!, Shine zaka yi magana da sunnana kan cewa ni ne na yi wannan d □ cision din?, Sannan ka saka a rufe min kofa ina ihun a bude min sun labe banma gansu ba bale su bude min?, Plz tell me so kake ka ga na fadi kasa?, Tell me so kake ka halakani?"

Pah ya lumshe idannuwansa shima da suka yi jan ya shiga fadin" Yaya kake magana kamar wanda yake aiki da son zuciya?, Yaya kake aiki da kalamai irin na jarumi bayan ka sako son zuciyarka gaba da komai?, Kana min maganar ya kona kasar watau idan na bara masa kasar ya gyarata ko ya konata baka da damuwa da hakan bayan kai shaida ne konatan shine abu mafi sauki da zai aikata daga bakin lokacin da zai wayi gari ba ni ba bayana?, Yaya kake acting kamar wani mai karfi kamar wani mai juriya bayan ka kasa fuskantar barazanar rayuwarka nutsuwarka duniyarka ka iya janyota ka ganar da ita halin da kake ciki?, Yaya kake son min rashin kunya bayan ni ubanka ne kuma ban baka tarbiya irin ta mai jan kunne ba duda na kasance mai jan kunnen?, HANJA ya zama dole ka hau kujerarka!"

Da karfin Murya HANJA ya budi baki ya ce" Ban zan hau ba!, Abui ba zan hau ba!"

A hankali juwa na kwasarta, cikinta na murda mata ba ji ba ganni da wani irin karfi, numfashinta na dauke mata tana janyo shi da karfi da kyar ta iya karasowa tsakaninsu mayafin abayarta na faduwa daga jikinta, zufa ta wanke mata gaban jiki, jikinta yai mata nauyi sosai da kyar ta iya budar baki cen ciki tana rike rigar Pah da dayan hannunta da dayan tana son kamo hannun Hanja domin a kusa da kusa suke sosai tana fadin" Please, i bg u da sunnan mahalincinmu plz ku saurara min haka, dan Allah ku daina fada a tsakaninku, Khalb nd Habiby ku....." luuuuuuuuuuuuuu ta tafi gaba dayanta ta fadi a kasa domin a tsakanin su biyun ba wanda ya kawowa ransa cewa kokarin shiga tsakaninsu da take ba dan ta raba su kawai bane , a cikinsu ba wanda ya san cewa a yau tun safe tana dan fama da ciwon cikinta
A cikinsu babu wanda ya gane halin da take ciki wanda suke ciki ya fi dauke masu hankali har sai da ta kai kasa kan cikinta da goshinta gaba daya da karfi ta yi wata muguwar faduwa ya saka su juyowa a firgice inda wayar dake hannunta ta silale ta fadi kasa daidai lokacin da Muneerath ta rintse ido sakamakon jin karar faduwar wayar sai jin muryoyin dakarun mazajen da suke fada tamkar zasu ciji junna sun shiga kiran sunnan mace daya kwal dake saka su nishadin rayuwa cikin ihun murya inda daya ya ce" ALEESA!," dayan kuwa ya furta " MAMAH" A DAKE KUMA TA JI

WANI RATS RATS RATS sakamakon saukar kafar daya a cikinsu a kan wayar sai daukewar kiran ya biyo baya wanda ya sakata sakin tata wayar daga tsayen da take ta fadi kasa lokaci daya tana jin wani irin faduwar gaba da ya ziyarceta wanda ta ji wata irin juwa ta kwasheta ta aniya yin luuuuuuu zata kifa da sauri Mahaifiyarta ta tarota tana ambatar sunnan Allah da sunnanta tana girgizata da tambayar meye menene ya faru? Duka a firgice hakama kawarta aminiyarta a rude ta dauki wayarta ta shiga maida kiran aman cikin ikon Allah a swt offf take amsa amo hakan ya karra rikita su domin kuka ne ta saka ta shiga fadin ta tabata wani mugun abu ya faru, kuma a kan Mah ya faru, kar dai a je ciwonta ne? Ko kuma fadansu ya saka ta summa ?
Sosai yamnayin da ta shiga ya ba mahaifiyarta mamaki sannan ta dauki soyayar da yarta ke yiwa matar nan da girma da mahinmanci

A saman kujera suka taimaka mata ta zauna gaba daya jikinta na wani irin rawa na tsoro da firgici,
Gaba daya sai ta ji idan ba ganninta ta yi a Palace ba ba zata iya samun nutsuwa ba, harma ta furta hakan inda mahaifiyarta da mamaki ta ce" Muneerath, Ingila fa kika ce?, Waye zai baki damar zuwa Ingila a yanzunnnan ke kuwa?, Awani ake yi na tafia fa, bayan wannan duda kin ce kina da Visa kuma ke din Hostesss ce ai ba koda yaushe ake da jirgin tafia Ingila ba, sannan ni gaskiya kin ga aikin nan naki har yanzu ba wai na yarda da zan iya barinki komawa bane, kuma ba zan iya barinki tafia Ingila ke kadai ba, me zai hanna ki yi ta yi mata adu'a na tabata koma menene zasu kire ki domin da alama su dinma sun damu da ke tunda har MATAR ta kiraye ki"

Daidai Oga ya shigo kennan daga anguwa da manyan kayansa ya karaso yana kallonta yana son tambayar lafia ita kuma wannan?, Sai ya ji Munnerath din ta riko hannun Mamanta ta ce" Mamanmu, dan Allah ki bani dama na je na gani ko zamu samu jirgin da zai tashin, dan Allah mamanmu ki taimakeni kar zuciyara ta buga, walahi na san yanzu sunna cen wani abin ne ya faru dan Allah ki bani dama mamanmu idan akoy jirgin sai mu tafi tare gaba daya har ke harma Oga idan kina so, akoy kudi a acct dina kuma ina da damar gayatar du wanda nake so domin takardar yar kasa ce da ni, ina da alfarma na masarautar Ingilar, ina iya kai tsaye na sa a min takardar gayata na je da ku"

Saudat dake ta gwada kiran layin ne ta shiga kiran layin sir Attahir

Ringin take ta yi aman bai daga ba hakan ya sa ta dauko wayarta ta shiga kiransa da wayarta domin bata san me ya hada shi da Muneerath ba kwana biyu kennan ba kabarinsa kwata kwata

Ta ci sa'a ya daga, hakan ya sa a dan gagauce ta shiga sanar masa cewa Muneerath ce na waya da Mah ta ji alamun kamar wani abu ya samu Mah din ko Sir Hanja, shine gatannan tana ta kuka wai ko zata samu jirgin da zai tashi to Ingila?, Walahi muma muna jin alamun ba ma dadi bane ka san kuma irin karamcin da sukai mata shine nace bara na tambaya ko akoy damar hakan?"

Sir ATTAHIR ya lumshe idannuwansa cike da jin wani abin da yake ta yaki da shi kwana biyun nan dan ya nisanta kansa da ita , da kyar ya iya hadiye abin yana sauke ajiyar zuciya a hankali ya ce" Subahannalah to ta kirayi number HANJA din mana ba sai ta ji ba idan bata samun Mah din, bayan wannan baki san tana da damar sakawa a tashi da jirgi da ita ba koda kuwa ita daya ce? In dai akoy jirage a kasa ko na wata kasar ne tana da wannan damar ku je a roport din kawai bara na yi kira na daidaita maku komai"

Da sauri Muneerath ta mike jin abinda ya fada, ta kai dubanta kan iyayenta da mamaki ke neman kashe su

Oga ya ce" Wai tsaya Jirgi fa na ji an ce?, Ingila dai ingila ko wani gari ne ake yiwa kiranyen nan?, Shi wannan din da kuka yi maganar da shi waye shi?, Kuma waye Hanja da Mah?"

Maman su Muneerath ta girgiza kanta tana kallon Muneerath din da ta matso da sauri ta rike hannunsa tsakaninta da Allah kuka take tana fada masa cewar su din iyaye ne a wajenta , Hanja kuwa tamkar yaya yake a wajenta

Baki ta tabe ta ce" Ya damu da sannin me hakan yake ciki ko kin ga alamun ya damu da damuwar wani ne a duniya bayan tasa?"

Oga ya ce" idan kuwa kina jin tsoron Allah ba zaki ce ni oga ban damu da kamarin yar oga ba, koda na yi rashin damuwa da rayuwar wani banda ta yar oga, ki ci gaba da min irin wulakancin nan, duniya ce"

Da sauri mamansu ta ce" In sha Allah alkhairin duniya zan tainta na kuma gama da ita lafia tunda ban cuci dan kowa ba!"

Da sauri Muneerath ta fashe masu da kuka ta ce" Dan girman Allah kar ku yi, yau dai kar ku yi fadan nan, ku taimake ni ku raka ni, idan bakwa zuwa ku bani dama na je na gani, walahi ina cen ta yi rashin lafiyar da ta daga hankalin kowa har sai da Hanja ya yi kuka du rashin imaninsa kuwa !"

Mamanta ta hae girar sama da ta kasa tana fadin" Je ki shirya bara na sa yayanku ya kai min y'ayana gidan yayana kar kafin mu dawo na tardo sun bar kasar sun tire!"

Oga ya kankance ido ya ce" Da alamu kin manta ni ne ubanta kuma ke kuwa a karkashina kike, dan haka ba inda zaku"

Muneerath ta riko hannunsa kanta na sarra mata a hankali ta dora kanta a gefen hannunsa tana murzarwa zafin da kanta ya dauka na shiga hannun nasa muryarta a mace tana fadin" Oga dan Allah ka barni ka ji aban Muneerath ?"

Hanci ya ringa bugawa yana hararen gefen Mamansu da ta yi gaba ta shiga kimtsa y'ayanta da hada masu kayansu dharda na islamiyarsu sannan tana neman layin danta dan ya zo da motar da ta siya ta sakar masu ya kai mata y'ayanta cen a kula mata domin ba zata iya iya barin Muneerath ta tafi ita kadai ba walahi, kuma da ace bata ji irin kalaman da suke fadawa junna da irin tada hankalin da yarta ta yi a daidai gabar nan da suke kaunar junna take jin son yarta tamkar ranta da ba zata barta ta wani je ba, sai dai a yanzu suke karra sannin junna dan haka ba zata bar abinta ba gaskiya zata je kafarta kafarta

Sun yi tafia mai nosan gaske, mai daukan lokaci

Sunna sauka Sir Attahir ne da kansa ya saka aka dauke su sannan ya shaida zuwansu Palace din dake rikice wanda gaba daya da kyar ya iya samun damar a barsu su shiga da adadinsu

Gaba daya jikinta karra yin sanyi yake a lokacin da suka durfafi palace din

Bayan sun samu shiga sam ba ta iyayenta da suka rude da kasar da gidan da matakan tsaro take ba
Da gudu gudu ta shige motar palace din ta umarci a kaita asibitin palace din ta bar Oga na kiran sunnanta

A lokacin da ta saka kafarta baban filin idannuwanta suka yi arba da abinda take iya kira baban tashin hankalin da bata taba kawowa ranta ba
Da karfi ta rufe idannuwanta ta kuma budewa a kan gadon da ake son turawa da mutun sama rufe da farin abin rufa wanda Pah dake tsaye a gak da HANJA suka zubawa gadon ido haka kuma Iman dake tsaye gaba daya ta yi jajajir dan birkicewa itama ta bi gadon da ido har aka tura shi aka shige wani dakin dake hanyar coridor din watau daki ne na tiyata ko na meye oho

A hankali take daga kafarta, jikinta sanye da atamfa mai ruwan ja mai dan duhu an yi mata dinkin riga da sket wanda ya mata dasss a jikinta ya kamata sosai a jikin nata ya fitar da dukan wani yannayi na kyau da tsarin halita a jikinta

A hankali ta tsaya a gabansu idannuwansu suka ringa sarkuwa da na junna har ta sauke dubanta a kan HANJA wanda suka tsaida dubansu tsai ido cikin ido sunna kallon junna

A hankali ta motsa lebenta dake naturel baya dauke da ko man lebe tana kallonsa cikin ido ta ce" Me yake faruwa ?"

Idannuwansa da yake ji sun gama kyekuashewa ya lumshe a hankali ya kuma budewa a kanta
Dukan da zuciyarsa ke masa da halin da mamansa ke ciki na rayuwa ko mutuwa da kuma ganninta da ya yi a irin wannan lokacin na ba zata a gabansa sai ya ji zuciyarsa na kakaryewa
Dukan da zuciyarsa ke yi da kuma irin yadda yake neman jin wani sa'ida da ganninta ya saka shi daga kafarsa a hankali ya matso daf da ita daidai lokacin da sojan da doreban da ya rako su Oga suka karaso daidai lokacin HANJA ya aikata aikin da ba wanda ya kawo haka a ransa, domin ita kanta wace ya aikatawa hakan bata taba tunanin haka daga gareshi ba a daidai lokacin da ya mika hannunsa ya damko nata ya janyota da karfi ya bata wata wawar rungumar da ta cuje dan kwalin kanta ta saki yafar da ta yiwa jikinta da mayafinta fari kal ta yi kasa kasa dan firgici da tsoro ta yi baya baya aman duka ya tarota a jikinsa ya kara rukunkumeta da rukunkumewar nan mai neman karya kashin bawa inda su OGA, da MAMA, da IMAN, da PAH , da dukan wani dan adam din dake wajen ya zarro ido kafin da sauro sojojin wajen su aniya neman kare hakan da tare Oga da ya zarro ido a zuciyarsa ya ayana' Kuturu uban meye wannan kuma' yana neman karasawa ya raba wannan garjejen jan mutumen da yarsa, a daidai lokacin da itama take mutsu mutsun son kwatar kanta idannuwanta duka a waje muryarta har tana rawa tana son ambatar sunnansa aman bugun da zuciyarta ke yi ya tsananta ta yadda ta kasa fitar da koda kalma daya ce saima jin lalausan sajensa na gogar gefen fuskarta muryarsa cen ciki sannan yana fuzga haka kuma yana goga mata sajensa ba da wata manufa ba sai dan neman inda zai saka ransa ya ji sanyi ya furta" TSORO NAKE JI, I'M AFRD MUNE..... MUNEERATH .....MU..... MUNEERATH MAH, MAHNA MAH..... "

SAKAMAKON LABARINA NA KUDI MAI TAKEN *WATA KOKOWAR* DUTSE ZAI RINGA ZUWAR MAKU LITININ DA ALHAMIS KADAI IN SHA ALLAH..... .. ....
KI GARZAYO KI YI RGST YA UWA DAN SAMUN NAKI CIKIN AMINCI IN SHA ALLAH.....DAGA ALKALAMIN SAJIDA
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□

Da sauri ta ankara ta dan daga murya tana mutsu mutsu muryarta a dan dage ta ce" Hanja ka saka ni abana zai dakeni menene wannan abin dan Allah"

Pah da ya gama gane a wajen Yan africa fa musulmai ba'a haka , wannan ba wasa bane a wajensu ya samu da kyar yana fama da tasa zuciyar da damuwar ya dafa gefen kafadar yaronsa a sanyaye ya ce" Please ka sakata kar ta rasa numfashi, ko so kake itama a kwontar da ita ne?"

Kwontar da itan da ya ji shi ya tashe shi a duniyar da ya afka, da sauri ya sasauta mata rikon hakan ya bata damar wartar jikinta cike da wata kinyar da bata san ta uban mecece ba da kuma tsoron Hanjan da bata taba ji ba, da wani irin tausayinsa da bata taba ji a zuciyarta ba ta ringa jan mayafinta tana lukube jikinta har kanta

Shi kuwa kallonta yake da irin kallon nan tamkar zaka dauke mutun da ido sam baya so ko ido ya kifta

Bangaren su Pah kuwa yana karasawa suka bashi dama ya isa kisa da su Oga wanda Pah na isowa kusansa sai ya samu kansa da sada kai gaba daya dan walahi wani irin gwarjinin mutumen da yake tunanin ko christane ya dirar masa da shayinsa , hakama Mamansu da ta gama cika da hali da mijin nata ke rabawa tana kallonsa da kuma tsoron rungume mata y'a da ta hango an yi itama ta samu kanta da sada kai a gaban wannan jan mutumen da ya tsaya a gabansu tsayinsa du ya kere su sannan ya kura masu ido

Murmushin karfin Hali Pah ya sakar masu kafin ya mikawa Oga hannu a sanyaye ya furta" Asalamu alaikum "

Sai da oga ya kalli matarsa da Saudat kafin ya iya ba Pah hannu yana mai amsa salamarsa da saurin kuma kallon hannunsa jin wani irin laushin abu ya rika a hannunsa

Pah ya dubi Saudat ya sakar mata murmushin itama ya nemi da ta masu translate kafin a nutse ya shiga yi masu barka da sauka , ya dora da fadin ya san su din iyaye ne kowasu makusantan Muneerath, su yi hakuri sun zo a irin wannan lokacin basu samu sauka mai kyau ba, sunna cikin hali ne na rashin lafiyar matarsa watau Mah wace har sun shiga halin kukan rashinta domin sai da ta yi doguwar suma ta kusan awa biyar kafin take dawowa duniya, yanzu haka dai itace aka shiga da ita dakin tiyatar gagawa wace likita ya ce a tiyatar nan kila wa kala ne, rabon rashin tashinta ya fi rabon tashinta karfi, dan haka dan Allah su yi hakuri da irin halin da suka same au, yanzu shi zai je masalacine ya yi alwallah ya zauna a cen har a fito da ita, yana da bukatar adu'ar su da duk wani makusantansu, su taya shi da adu'a ya san Allah baya barin wani dan wani ya ji dadi , su taya su da adu'a idan lokacinta ne ya yi Allah ya sa ta cika da kalmatu shahada, ta samu kyakyawan karshe sannan mutuwarta ta zamo hutu ce a gareta, suma iyalanta Allah ya basu ikon jure rasa masoyiya abokiyar rayuwa a karro na biyu, domin wannan itace matarsa ta biyu KHADIJA shine sunnanta na kirki anai mata kiranye ne da ALEESA

Gaba daya jikinsu ne ya yi wani irin sanyi, Saudat take fasara masu kuwa sai share hawaye take hakama Mamansu da kyar ta iya rike kukanta tana kallon Pah cike da tausayi

Oga ya sauke ajiyar zuciya ya girgiza kai ya ce" Jikina du ya yi la'asar, kai jama'a mutuwa mutuwa, kawai dai sai ta karar da mu innalilahi wa ina ilaihi raj'une"

Saudat dai bata fasara wannan ba sai da ya kuma budar bakinsa ya ce" Cuta ba mutuwa bace Elhaji, Allah ya bata lafia idan ba laifi mu je masalacin kawai nima ai ba karamin makaranci bane mu je kawai mu yi ta karatu Allah ya bata lafia ka ji?"

Murmushi Pah ya yi yana gyada kansa ya juyo yana kallon yada HANJA ke zaune saman abin zama irin na jikin ginin nan kansa a jingine jikin garu still idannuwansa a kan Muneerath dake face da shi itama a zaune a kusa da Iman ta riko hannun iman din tana dan murzawa kanta a kasa

Ajiyar zuciya ya sauke ya shiga yiwa jami'an tsaron magana kan a barsu su kadai watau su Muneerath da yan tafiyarta da Hanja da Iman, daga nan kar a bar wani ya kuma shigowa domin gari ya dauka du wani makusanci ya garzayo so suke su layu a wajen bayan shi baya so a karra rikita Hanja din

Saudat da mama suka karasa suma suka zauna kusa da Muneerath wace kanta ke kasa gabanta na faduwa tana cike da tsoron abinda zai biyo baya na abinda wannan dan na Mah ya wani mata a gaban iyayenta, ita kam bata san dabi'ar iskanci a me ya dauketa ba walahi

A hankali tana kallon kasa muryarta cen ciki ta ce" Mamanmu, walahi rikicewar da ya yi ne aka yi katari nice a kusa da shi haka ta faru, walahi na rantse maki a zamana a gidansu ba aikinmu kennan ba, kuma yanzu hakan shi kansa daga ya dawo a hankalinsa zai fara hararata kin ce na fada maki, ya ga damar ya ce nicema na rukunkume shi, abinda da muka zauna ma da shi ba wani shiri muke yi b....."

Muryar mamanta a sanyaye ta ce" Muneerath ina so na daura alwallah a nunan alkibla kaina ya kule tunda muka shigo, so nake na rokarwa baiwar Allahn nan sauki na Allah da ita da mu baki daya"

Muneerath ta kaleta da sauri da dan mamakin jin furucinta, shin bata ji me tace bane ko kuma bata ga abinda ya faru bane.....kai da ta ji dadinta da bata gani ba walahi dan ita ta ki jinnin a mata kallon yar iska tunda ita dai ba yar iska bace

Iman ce ta mike bayan Saudat ta fada mata bukatar Mama jikinta ba kwari kamar zata kifa ta ja mama suka nufi cen ciki dan ta bata gyararan wajen da zata yi ibadarta a nutse

Kan Saudat a sade da yaren Hausa ta ce" Muneerath, dan Allah ki dube shi, ya dace ki karasa gefensa ki raashe shi"

Ido Muneerath ta zarro ta dan saci kallonsa a hankali ta ce" Saudat ni gaskiya na gaji da rarashinsa dan Mah bata da lafia, adu'a ya dace ya zauna ya yi aman kina ganni ya rungumeni a gaban Oga , Oga fa ya ganni aman ina ga mamanmu bata gani ba , hakan wancen karron kuka ya sha ni tsoroma yake bani kin ji karfinsa kuwa?"

Saudat ta lumshe idannuwanta cike da tausayin lamarin nan dake cikin duhu , a yanzu idan ta kai dubanta kan Hanja sai ta ji tamkar ta rushe da kuka, gashi zaune tamjar DUTSE, ya kura mata ido tamkar BAKUWAR HALITA, kallonta yake da SO da KAUNA da BEGE , wanda harshensa ya kasa yin FURUCI a gareta

A sanyaye ta ce" Muneerath kin dai san lada irin na wanda ya taimaki mutumen da yake cikin wani hali, bayan wannan a tunanina abinda ya shafi Mah ya shafe ki, ko da kike kiransa yayanki a Niger dan dadin zance ne baki bashi wannan darajar ba?"

Muneerath ta yi tsai tana kallonta

Saudat ta ce" me zai hanna ki je kusa da shi ki bashi baki?"

Muneerath ta zarro ido ta ce" kin fa ji irin fadan da suka yi da mahaifinsa, idan na je ya karyani fa garin shishigi?"

Da sauri Saudat ta ce" Ko ya karya kowa banda ke, ba zai iya koda yi maki mugun magana ba plz my freind ki dube shi, ya gaji da yawa zuciyarsa ta gaji"

Wani iri Muneerath ke ji da kalaman Saudat
Haka kawai take ji a cen kasan zuciyarta dole ne ta je gareshi dole ne ta rarashe shi
Sai take ji wata damuwa irin wace ya dace ta ji idan wani na jinninta ke cikin damuwa a kansa

A hankali ta saka dubanta cikin nasa wanda gaba daya ta ringa jin dukan wani kuzarinta da da karfin jikinta na barinta
Idannuwansa masu launin ja suka ringa yi mata kaikayi a cikin nata duda irin nisa da suke da junna

A hankali ta cire dubanta sakamakon kasa jure kallon da ta yi

Iman ce ta zauna a gefenta tana ta sauke ajiyar zuciya tana amsa waya da harshen larabci wanda da alama danginsu ne na saudiya suka zo aman sun samu cewar ba wanda zai shigo hakan ya sa ta fada masu su je cikin Palace su yi ta adu'a har yanzu shiru ba'a fito da ita ba

A hankali ta mike daga zaunen da take tana jan mayafinta ta nufe shi

Tun kallon da yake tsareta da shi sai yanzu ya iya dan sasauta dubansa a kanta yana mai dan sada idannuwansa daga kanta sakamakon bugawar da zuciyarsa ta karra kaimi tana yi da dukkan karfinta

A hankaki ta zauna daf da shi sosai hakan ya sa ya kuma dagowa a hankali yana kallonta

Idannuwanta ta lumshe kafin ta kuma budewa a hankali ta dago hannunta ta nufi kusan idannuwan nasa a hankali ta ringa karra matsawa har ta isa sosai ta kai yatsar nata tsai har kusa da kwayar idannuwansa kafin yake kiftawa da dan sauri ya kuma budewa da wani saurin yana kallonta har kamar da ruwa ruwa a cikin idannuwan

A hankali ta budi bakinta har iskar bakin nata da bata fitar da wari bale kanshi ta dan daki gefen fuskarsa muryarta cen ciki ta ce" Me yasa kake min kallon nan?"

Idannuwansa ya kuma lumshewa ya karra kureta da duba muryarsa cen ciki ya dora hannunsa saman nata , da sauri ta janye tana dan turo bakinta , a sanyaye ya ce" Dan kin fi mini kowani abin kallo "

Da sauri ta dago tana kallonsa itama, a hankali ta ce" idan Mah na cikin halin rashin lafia sai ka zama wani iri, bana son yannayin nan naka, sai ka ringa fadin maganar da baka sani ba"

Lebensa na kasa ya dan danne da dan karfi yana fitar da wani numfashin ya kalli kofar bloc, ya maida dubansa a kanta a hankali muryarsa na crking ya ce" Bana so ta sha wahala, koma me zai sameta bana so ta wahala"

Muneerath ta dane irin abinda ke taso mata ta rintse idannuwanta, wannan karron ita din ce ta samu kanta da dora hannunta a bayan hannayensa a hankali ta jimke , irin jimkar nan dake fitar da labarin dake zuciya, muryarta a sanyaye ta ce" Mah zata tashi In Sha Allah, u see ta sangartaka da yawa sai ita zata iya lalaba shagwababenta, idan ka ci gaba da wahalar mata da kanka Allah ya tasheta zata bata rai, idan ka ci gaba da wahalar mana da kanka Hanja zamu yi ta shiga dam....."

Shiru ta yi da maganarta sakamakon wani kure mata baki da ya yi da kallo, sai a lokacin ta ringa tariyo abinda ta fada hakan ya sa da sauri ta dan zarro ido tana cire kanta gefe idannuwanta suka sarku da na Iman
Irin kallon da Iman ke yi mata sai da ta ji gabanta ya fadi

Watau wani irin kallo ne da ta kasa fasara shi
Irin kallon nan na idan idannuwan mutun sun yi ja kuma ya hada da kallon kyama ko jin haushi

A hankali ta kai nata idannuwan itama kan inda Iman ta sauke nata duban

Fitowar likitar da ta yi ja gaban tiyatar, babar likitar da ta sauka daga saudiya dan aikin nan ya saka Muneerath saurin mikewa tana kallon yannayinta

A hankali ya juyo kan likitocin da gaba daya suka bayana a irin wannan lokacin,

Irin yannayin da fuskarsu ke nunawa shi ya saka du wani mai rauni fara zubar da hawaye
Wanda yake da juriya kuwa sai ya zamana ba baka sai ido

A hankali ya ahiga daga kaffafuwansa still hannunsa rike da na Munnerath ya.....

Kamar yadda na fada cewar in sha Allah Litinin da alhamis zai ringa zuwa maku sakamakon litafina na kudi da na fara posting dinsa yau Litinin mai sunna WATA KOKOWAR

. Shin kina son sannin me ya kunsa? Sunnansa ya dace da shi?

Ba zaki gane hakannba sai kin karanta yar uwa
Dari biyu ne kacal my hajia ki tuntubeni ta number wayana kamar haka+22793811618
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□

A hankali ya dora hannun nasa a gefen fuskar ya dan shafa, sai kuma ya saka hannayensa ya janyo Hanja din ta hanyar rike kafadunsa gareshi
Da karfi suka rukunkume junnansu idannuwansu rintse wanda har jikinsu rawa yake

A hankali Muneerath ta juya wannan karron ba zata iya gannin abubuwan nan ba
Abinda bai cika damunta bane ya sakota gaba lokaci daya ta ji wani irin kuka na son kubce mata mai karfi bayan ba haka take ba
Bata san me yasa take irin barancin nan ba
A yau ta yi kokarin fashewa da kuka mai ihu fiye da irgen yan yatsunta

Labewa ta yi ta hade kai da gwuiwa ta fashe da matsanancin kuka

Tana kukan ta ji an dafa kanta hakan ya sa ta dago a firgice ta sauke dubanta a kan Oga

Da sauri ta shiga kokarin son gannin ta share hawayenta inda Ogan ya zauna shima a kasa yana kallonta jikinsa a mace ya ce" Ta mutu hala?"

Da sauri ta girgiza kai ta ce" kai innalilahi Oga har gabana ya fadi, ni dai ban sani ba ko da ran ko babu, na dai baro su a cen ne, walahi tausayinsu ne ke neman kasarani "

Kansa ya langwabar gefe ya girgiza kai ya ce" yau na ga dukiya kuma na yarda dukiya bata iya yiwa mutun maganin damuwa, kai subahannalahi na fada maki ni ina takamar makaranci ne izub dina talatin da bakwai irin na yi ja gaba na so na dauki ragamar saukar da zo rarabawa sai na ga iyayena, ke na raina kaina kuma walahi muna komawa makaranta zan shiga, Allah na tuba sarkin garin nan da ya dauki karatu sai na ce ashe ni wawa ne ban sani ba?, Kin ga ma zo a talauce zan koma a Allah koro, ban san fari ba ban san baki na, ga masu rike da kasar ga mulkin sun san zasu tsaya gaban wanda ya halice su , kudinsu da mulkinsu bai hanna su karatu ba, sai mu dan shirme da rashin rabo da hauka irin na talaka wani dan nema ne zai hanna mu cikar buri na karatun islamiya da sannin addininmu da bautawa wanda ya yi mu, Gaskiya idan wuta ta ci naman talaka ya zama dan iska!, Watau ya zo a rakiya zai koma a ala koro"

Muneerath kan kanta ta kuma sadawa tana jin so take ta kara barewa da wani kukan, gaba daya ba koshi ta yi da kukan ba

Oga ya dora da fadin" Na yi mamakin gannin mai jan kune da janyo ayar Allah, ina gannin harda sarkin makkah yau mun gaisa, abinda dai bai min ba da na ga kafuraima sun hade kai sai muimui suke da baki sunna karyar da suka saba, kai gaskiya bai dace ya bar wannan iskancin ba sai dai in raba kafa ya yi"

Muneerath ta turo baki sosai ta ce" Oga dan Allah ni dai ka bari bana so "

Oga ya tsura mata ido, kamar wanda aka tsikara ya ce" Kai, yauwa ke yar oga dan Ubanki me kike a jikin kato? Muneerath yaushe kika zama yar iska ban sani na? A gabana a gaban uban saurayinki a gaban mamanki , uwarsa na kwonce rai a hannun Allah kika yarda aka yi badalar nan da ke? Me kike so ubansa ya yi tunani da tarbiyar da na baki tsakani da Allah ? Wannan ai iskanci ne karara walahi"

Dama a daf take da katon tankin ruwan hawayenta, sai kawai Oga ya idasa hankadata ramin ihun kukan da ya kireta da iskanci bayan ya san ita ba yar iska bace, kai yaya zata yi da zuciyarta dake zafi da son ta koma ta ga halin da yake ciki?

Sai kawai ta bare baki ta mike kafafu ta riko hannun Oga ta fashe masa da kuka tana kallonsa

Ido ya zarro yana waige waige, shi fa yanzun tsoro yake ace ya taba Muneerath walahi, ya kula kamar tana da daurin gindi a garin nan , kar a je kafin a gane shine ubanta sai an harbe shi tukunnan bayan matarsa bata yafe masa ba ya koma ya hadu da walakiri da sandunna, gwara dai ya kyaleta har su shiga kasarsu sai ya mata fadan wannan sabon halin, sam ba halinta bane, bai dace ita da kanta ta fara irin halin nan ba

_____

Muryar Pah da ta shake sosai ya bude a sanyaye ya ce" Son, I'm sorry "

Da sauri Hanja ke girgiza kansa yana karra rike Pah ya ce" Pah i'm sorry, ka yafe min a kan komai, Pah ka yafe min na roke ka, ban san me yake damuna ba, aman dukan abinda ka fada gaskiya ne, ban san ko dan kana saurin dago abinda zuciyata ke ciki bane nake jin haushinka, dan Allah ka yafe min ka ce kar su ce min Uwata ta rasu"

Idannuwansa ya karra lumshewa shima yana tapping din bayansa a hankali kafin ya ce" Ka ga wani abu?, Idan ta tafi ta barmu Son ina so mu yi abinda ma'aiki ya koyar, dan Allah kar ka ruguza ni"

Hanja kam baya tunanin in zai iya, hakan ya sa ya yi shiru har uncle dinsa watau cousint din Pah ya karaso ya shiga basu baki da yaren turanci kafin ya umarce su kan su fuskanci likitocin dake jiransu , a kasan zuciyarsa kuwa Allah Allah yake ya ji me likitocin zasu ce dangane da Mah, ya tabata faduwar matar nan daidai take da faduwar iyalanta, domin sakarar soyayar da suke yiwa junna baya tunanin in daya zai iya babu daya, so yake kawai ya ji an yi mai yiwuwar ya taka rawa!

A nutse likitar ta fara bayani kamar haka" Alhamdulilah, dukan halin da bawa ya samu kansa a ciki ya godewa Allah,
Mun yi aikinmu, mun yi kokarinmu, aikinmu ya tafi daidai sai dai wata matsala da ta bijiro ta harkar jinnin da ya ringa fesowa cikin cikin
A yanzu maganar da nake mak....."

Hanja ne ya dubeta a hankali ya ce" Dan Allah ki sanar mana amsa daya cikin biyu, ta rasu ko tana raye!"

Da sauri ta sada kanta ta ce" Ka yi hakuri, bata rasu ba, aman tana cikin mawuyacin hali tsakanin rayuwa da mutuwa, wanda muke so ku saka hannu a sakata a cikin Coma, domin muna so mu dauke hankalinta baki daya dan mu bata kyakyawar kulawar da ta dace"

Gaban goshinsa ya dafe a rikice ya ce" Coma?"

Pah ya shiga maimaita" Innalilahi wa ina ilaihi raj'une "

Uncle dinsa ne ya share zufa ya ce" Menene pourcentage din tashinta da mutuwarta a halin comar?"

A sanyayenta ta ce" Kamar yadda kowace coma ke ciki haka wannanma, tana iya bude ido ta motsa a gobe, kamar yadda tana iya daukan shekaru inji na bata

numfashi da komai, haka kuma tana iya tafia a kowani lokaci, sai dai abin dadin shine farkawar na iya zuwan mata a kowani lokaci"

Hawaye ne mai dumi ya shiga gangarowa daga gurbin idannuwan Pah, a rikice ya siga fadin" Ta shamace ni, ba haka bane abin zai kasance, nine nake da cancer ita dan ciwon ciki ne ke damunta da bashi da wani hatsari, ita ke ce min dan ciwon ciki ne sama sama da bashi da wata damuwa, me yasa zata min haka me yasa?"

Da sauri ya rike shi yana dan girgiza shi muryarsa a sanyaye ya ce" Haba ya shugaba, ka nutsu ka daina irin maganar nan, kaine fa zaka talafa masa ya samu karfin jure halin da yake ciki, kar ka gaza a gabansa , idan ka yi haka ina zai saka ransa ne?"

Pah ya sada kansa hawayensa na zuba sosai

Uncle Joeil ya ce" Ka yi hakuri, ku yi hakuri kar a jona mata inji a hadata da fama, bamu san halin da take ciki ba, may be mutuwarta ta fi wannan wahalar sauki a gareta, ku mu barta ta tafi, ku mu barta ta huta"

Sai a lokacin Hanja ya dube shi,
Duba ya masa mai tsauri kafin ya cire a kansa yana kallon likitar ya ce" Ku jona mata, idan da chance din Mahna ta tashi koda na 0,1% ce ina so, ku jonna mata komai ku shiga bata kulawar da take da bukata, daga yau daga ni sai Pah zamu ringa shiga wajenta,"

Ya juyo ya fuskance shi da kyau da wata kakausar muryar da ta saka shi jin shayin yaron fiye da da ya ce" Ba zan birne uwata ba har sai babu wani sauran numfashi a jikinta!, Daga yau zan saka hannuna a takardar yarjajeniyar da zarar Ubana ya tashi sauka a kujerar sarautar kasata ni dansa rayaye mai shekaru isasu zan maye gurbinsa!"

Daga haka ya juya ya amshi takardar hannun likitar ya saka hannu sannan ya juya da wani irin saurin da ya saka Pah saurin mikewa yana zarro ido hawayensa suka dauke , kukansa ya tsaya tsit ya bi kakarfan yaronsa da kallo gaba daya tsigar jikinsa na tashi, kafin ya lumshe idannuwansa ya juya a hankali ya nemi son gannin iyalinsa inda ya bar Uncle Joeil tsaye cike da mamakin abinda ya faru da tashin hankalin furucin HANJA cewar zai hau mulki bayan shi ya fi kowa sannin irin tsanar da yaron ya yiwa mulki wanda da wannan damar yake karra sakin karinsa dan ya gama sannin cewa mutuwar Pah a kusa take, yana shekawa shi zai hau abinsa

A birkice ya zo ya wuce HANJA baima kula ba ya fita a asibitin

Ba zai yiwu ba, shi da ya gama sannin lagonsu ba zai yarda su masa sakiyar da ba ruwa ba

Zai taba wajen da zasu rasa sukuninsu, karfinsu, dabararsu ta haka zai shige su ya lalata dukan wani motsi nasu

Turus ya yi yana kallon ikon Allah,
Kukanta take kashirban , Oga ya yi ban bakin ya yi rarashin ya zauna ya zuba mata ido ta rike masa hannu taf sai birgima take da kafafu tana fadin" Ko wani ya ce maka ni yar iska ce ai ka karyata shi bale kai da kanka?, Ina zan kai raina na ji sanyi? Walahi Oga tsoro nake ji Allah"

Idannuwansa ya lumshe ya dan jingina yana ta kallonta da irin abin da take yi

Oga ne ya ankara da shi dan haka ya ce" Yauwa dan girman Allah rabani da ita kar ta jaza min balaki a kasar mai jan kunne, yau na ga ikon Allah yar gidan oga dama yar shari ce ke?, A Allah ba taki ba, a Niger za'a birne ni in sha Allahu !"

Da saurri ta kalli wajen da yake tsaye

Sai da gabanta ya fadi haka kawai, hakan ya sa ta hadiye kukan tabarar da take zubawa tana kallonsa kamar yadda yake mata mayatacen kallon nam masa

A hankali ya shiga takowa inda take

Ido ta dan zarro dan ta gama wanye cewa yanzun bashi da cikakiyar lafiyar kwakwaluwa gaskiya, dan haka gwara ta yi ta kanta

A hankali ta ce" Oga ka boye ni dan Allah "

Tsili tsili ya yi da ido, in ba iskanci irin na Muneerath ba yo in ya boyetan bata kula wannan mutumen ya fi shi girma bane? Tsaf zai maida shi gefe ya kamota walahi, shi kam yau ya ga abu a gabansa ana masa abu da y'a

Abin ai na Allah ne budurwa da jika □□□□□□□□□□ ga wani page din □□□□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

5 □□□ 9 □□□

Tsayuwa suka yi suka saka Oga a tsakiya wanda yake cicira ido zucoyarsa cike da tunanin irin hukuncin da zai yiwa Muneerath idan suka samu kansu a kasar Niger inda ake jin yarensa idan ya furta cewa shi mahaifinta ne , ta yadda za'a taya shi cin ubanta la'ada waje idan aka ji irin dibar albarkar da ta masa a kasar mai jan kunne, wai shi Muneerath ta saka tsakiya da saurayinta tana kukan tabara salon yayi tunanin shi ya daketa ya maka masa hannun nan nasa mai tuwo ya summar da shi

A sanyaye yana kallon irin kamanin da Muneerath ta dauko na mahaifinta wa'inda in ba tsayawa ka yi ka masu kallon tsaf ba wani iya ganewa zaka yi ba ya iya budar bakinsa ya ce" Kukan me kike yi Muneerath ? Kin san da Mah ba zata so ki yi kuka dan bata da lafia ba "

Muneerath ta dan leko tana kallonsa
A hankali ta ji tsoron nasa da take ji na kawarwa daga zuciyarta hakan ya sa ta iya fitowa a bayan Oga wanda ya yi fittt ya tafi yana mai ayana 'Yan iska kawai, gaskiya gwara na ga ubansa idana aure za'a masu a masu ba sai mun tsinci yan amaye amaye da tashin zuciya da barcin rana ba mu ahiga uku, su su sha murnar hakan ni kuma bakin ciki ya kashe ni a banza ba'

Muneerath dake kallonsa a hankali ta ce" Ina Mah?"

Yan kafadunsa ya iya dagawa a hankali ya ce" Tana cen kwonce, za'a sakata a koma "

Ido ta zarro hakan ya sa ya kurawa idannuwan nata ido a hankali ya ce" Fada min, kina tunanin zata tashi kuwa?"

Bata san lokacin da ta ce" Yo ni na sani ne ka ga kar ka fara kukan ka ji?, Gwara ka je gida ka cenza kayanka ka dan nutsu ka ci abinci ko yayane, a yanzun adu'a zamu yi ta yiwa Mah in sha Allah zata tashi"

Ajiyar zuciya ya sauke zai yi magana su Iman da Saudat da masu masu rakiya suka karaso wajen domin Pah ya salami kowa ya ce kowa ya tafi gida ya huta ya mata adu'ar tashi idan da rabon hakan

Iman na zuwa, sakamakon gannin a dazuma ya rike mata hannu sai ta samu kanta da riko hannunsa tana kallonsa tana hawaye a bayane kafin ta fashe masa da dan kuka marar sauti sosai tana kallonsa

A hankali ya janyota jikinsa ya rungumeta dan ya rarasheta, Iman fa itace kanwarsa da yake manta cewa ba wai jinni daya suka fito ita da shi ba
Iman na cikin halin rudu na rashin Lafiyar Mah kamar yadda yake ciki shima
Iman y'a ce a wajen yayun Mah wada suka rasu sakamakon accident din mota

Tun tana karama take hannunta har zuwa yau
Bata san wata uwa sama da Mah ba, idan a yau ta rikice da koke koke kan abubuwan da suke faruwa da ita tabas ta cencenci a dubeta a rarasheta, abin kaunarta na nuna kulawa ga watanta a bayane, sai ko mamanta wace take yiwa kauna irin ta mahaifiya na kwonce a halin rayuwa ko mutuwa? Dole ta so a rungumeta, bale su a wajensu rungumar fa ba laifi bane , sam ba wani abu bane, su da ko a gaisuwa suke rungume junnansu bale a haka?

A hankali Muneerath ta ringa jin wani irin zafi na ziyartar dukan jikinta har zuwa kofofin hancinta

Idannuwanta ta cire a kansu ta sauke kan Saudat wace ta kula kamar murmushi Saudat din ke yi hankali kwonce harda rungume hannaye

A hankali ta ce" Kai Saudat zafi nake ji hancina kamar iska ta masa kadan mu tafi inda a maida mu"

Da yaren hausa ta yi maganar tana yawo da idannuwanta da take aon kauda su daga duban bangaren yan iskan nan!, Sai dai kamar gam aka ringa dawo da dubanta har a kuma duban hannunsa dake saman bayan Iman yana dan dadabawa a hankali
A hankali ta kai dubanta saman fuskarsa, idannuwansu suka sarke da junna

A hankali yannayin fuskarta na innocent girl ya ringa nuna halin da take ciki na bacin ran rike wata a jikinsa , sai dai sam bakinta bai nuna ba hakama aikinta bai nuna ba

A hankali ta cire dubanta ta juya wannan karron ba tare da ta jira Saudat din bama dan ta kula Saudat din na son zaman ta kalli iskanci karara
Sai ta kama hanya a kafarta tana tafia, du kuwa da irin nisan wajen gaba daya sai ta manta take tafiyarta a kafarta inda gaba daya ta samu kanta da tunanin rayuwa irin ta HANJA

Tsaki ta ja a bayane tana fadin" Kai kowama sai ka rungume? Kowama sai ka rikewa hannu, baka da zabi a matan da kake iya rikewa hannu? Baka da zabi a irin macen da zaka nunawa kukanka? Kowace bola da sharama sai ka rungume ka nuna mata kanna cikin wani haki na bacin rai? Wannan ai sallon yada iskanci ne a doron kasa, anya kuwa yaron nan ba ya gama watsa kansa ba kuwa ?"..

Bata shirya jin muryar ba ta ji daga bayanta Saudat da ta gama shan dariyar yannayin Muneerath din , wace tana bada baya HANJA ya saki Iman cikin gagawar maganar da bai san yana da ita ba ya ce da ita" Autan Mah, ki daina kukan nan haka kin ji? Saukin kennan muka samu daga Allah, domin da yanzu gawarta aka turo mana , kuma haka zamu dauka mu je mu birne, mu tafi mu yi mata adu'a ki daina kukan haka ya isa kin ji autan Pah ?"

Yana fada ne ya shafa gefen fuskarta da sauri ya kama hanyar fita, sai dai kafin ya idasa fitan muryar Pah ta dawo da shi
A kan dole ya dawo yana waiwayen kofar kamar ya ce yana zuwa zai bita ne sai dai ba halin hakan domin ya tabata tataunawa ne zasu yi da mahaifin nasa, kuma ya tabata hakan baya wuce a kan maganar da ya yi cewar zai dauki sarauta

Dan dole ya umarce au da su tafi, Har saudat zata wuce ya samu kansa da cewa" Dan Allah Munee ta ci abinci kar ta manta da cikinta "

Wannan ya sa ta ki ahiga motar da Iman ta shiga ta taka a kafa, domin ta gama hardace wacece Muneerath, idan ranta ya baci ta fi kaunar ta tafia a kafa ta dan jajantawa kanta ta dan dudura ashar daidai gwargwado sai ta ji ta huce abinta

A hankali ta ce da ita" Waye ke yada iskanci a doron kasa kawata?"

Da sauri Muneerath ta dajata ta juyo zata bata amsa aka zo aka wuce da Iman
Da ido ta bi motar da iman ke ciki riiiii har ta shige mata kafin ta juyo, zata kuma yin magana aka wuce da mamanta da Oga wanda yake murmushi yana daga mata hannu mamantama ta mata murmushi
Dan murmushi ta masu ta dawo hankakinta kan Saudat ta ce" Wai ni oga yau ya cema ina iskanci, tsakaninki da Allah saudat da muka zauna da ke na taba yarda aka yi rungume rungumen nan da ni a cikin hayacina? Wa'inda suka samu a da ai a rashin sani ne na fada kansa, a yanzu fisabililahi ke ba shaida bace shi ya warto ni? Oga sannin ko waye Hanja ne bai yi ba da bai daukeni a yar iska ba tunda dai ni ai da sauki tun da aka haifeni har zuwa yanzu shi kadai na rikewa hannu , shima dan na hanna shi kuka ne, aman shi fa? Kowace shara rungumowa yake kai tsaye"

Saudat ta dan cije lebe tana gyada kai kai tsaye ta ce" Kika san ko sonta yake?"

Gaban Muneerath sai da ya ruguje ya fadi wanda ta san da babu fatar dake tare da kirjinta da a kasa warwas za'a tataro kirjin nata

Gummm ta yi bata bata amsa ba dan haka kawai ta ji Saudat din tama gama raina mata wayo, Kaf duniya babu wanda ya rainata irin Saudat din, dan Allah ina mahadin Hanja da Iman? Iman laso laso din nan da ta gama talata kirjinta a facebook tana dora hotunna kamar tsirara? Duda shima ta fara tunanin anya ba kwarto bane aman kuma ai sam basu dace da Iman ba, kai iman fa kanwarsa ce fa, yanzu haka rungumetan da ya yi dan ya lalasheta ne, ai Hanja akoy tausayi fa

A hankaki suke takawa suma har suka iso wata kujera inda sojojin gadinsu ke barbaje ta ko'ina haka kuma drnnn na saman kansu yana yawo ba daya ba ba biyu ba

HANJA ya kuma duban hanyar tafia palace , zancen zuci yake a tunaninsa ya ce" Ko a kafa ta tafi ko a sama? Allah dai ya sa ba haushina ta ji ba dan na dan rungume kanwata ina rarashinta"

Pah ya yi murmushi yana jin sanyi har kasan zuciyarsa, dama burinsa ya samu wada zata kasance mai kishin da zata hanna masa kallon matan nan da kwonciya da su, burinsa ya haukacewa wace idan ya kula wata zata iya barinsa, sai gashi ya samu a ruwan sanyi

A hankaki ya kalli fuskar Pah
Sai a lojacin ya gane ya ji shi ne fa, dan haka sai ya samu kansa da sada dubansa yana jimke hannunsa a hankali ya ce" Anya zata so ni?"

Ya dago ya kurawa fuskar Pah ido a sanyaye ya ce" Sai nake gannin kamar bana gabanta "

Pah ya kawar da idonsa shima a sanyayen ya dan dage kafadu ya ce" A gaskiya a yanzu baka gabanta, wanninka yake gabanta"

Idannuwansa ya rintse saboda wani irin abu da ya ji ya sokar masa kahon zuciya, bai san menene ba, bai san me yasa kalaman Pah suka so su bata masa rai ainun, bayan ya san gaskiya Pah ya fada masa iya gaskiya

A hankali ya ce" Aman me ya fi ni da zata fi dubansa?, Me yasama ka ce min wani ke gabanta? Sai nake ji kamar an zageni"

Pah ya yi murmushi yana kauda kansa ya ce" Abinda zaka gane a duniyarsu daidaikun mata ke iya nunawa saurayi sunna sonsa, suma kamar wa'inda suka aikata laifi idan aka ji hakan kamar zubar da kima ne a wajensu, ba kamar wajenmu bane da yin hakan ba wani abu bane nrml ne yadda namiji zai nuna maka so hakama mace, Son koda tana sonka ba zata taba nuna maka ba, idan ka nuna mata fine, idan baka nuna ba sai dai ta auri wani ta barka"

Ido ya zarro ya ce" wannan ai kashe kai ne"

Pah ya yi murmushi a bayane wanda rabonsa da yi tun da Mah ta fadi , a yanzu da ya shiga ya ga Alhamdulilah sai yake jin sa'ida a zuciyarsa, a hankali ya ce" Idan ka yi wasa....kamar da wasa.....zaka ga wasa, Now tell me a kan maganar Tronne"

Ido Hanja ya lumse a sanyayen da yake taintar kansa idan sunna maganar Muneerath ko tsakaninsu ne shi da Mah ya ce da Pah" Haka na yanke hukunci, ina fatan kasantuwar hakan"

Daga haka ya mike tsaye yana nuni da a zo a dauke su

A lokacin da suka shigo falo suka tarar da Iman kwonce idannuwanta lumshe sai Muneerath ta yi turus tana kallonta da kare mata kallo, wollah yarinyar akoy rama ko me yasa ita kuma kamar ta karye?

Saudat kuwa da ta gama shirya shirin shakawa Muneerath ta dan karkace kai ta ce" Aman sun dace, wannan saima ranar auren idan ta sha farar rigar nan tasu da dan magenta a hannu fari tana murmushi ya rikota ya rungumota"

Muneerath ta juyo tana kallonta, sam bata san me Saudat din ke yi ba , aman ta shirya fada mata abinda take yi ba daidai bane, sam ba hali bane, ta yaya zata ringa haka Hanja da Iman? Me yasa take haka ne? Ita bata ji abin na bata haushi ne? Haba dan Allah a ringa yin abinda hankali zai dauka mana, Hanja ai sai dai ya samo mata mai karfin hali in ba haka ba kulun a matsala zayana kasancewa, Iman din da daga an yi mata abin haushi take wuni tana kuka? Har fa kusan haukatata ta yi da ta kula motsi kadan sai ta yi kuka sai take taokanarta ba dare ba rana

Tana kallon saudat din a kausashe ta ce"

Barkarmu da warhaka yan uwa □□□□□□□□□□
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 □□□ 0 □□□

Muryarta a sanyaye tana kallon saudat ta ce" Sai ina jin gaba daya magangannunki basu dace ba, yanzu tsakani da Allah ina hadin wannan tsigigiyar yarinyar da a jikinta hancinta da farinta da idannuwanta sai shagwabarta ne kadai abin so?, Ke kin kuwa taba gannin Hanja da kyau? Kai ina ga baki taba kure masa kallo mai sunnan kallo ba wollah, Saudat Hanja sai da mace daidai shi, gaskiya ni bana son hade haden nan da kike masa"

Saudat ta saki murmushi tana kallonta ta ce" Wace mace? Ke baki san nasarun nan, bale masu kudin nan, na kai maki karshe sarakin nam, masu kyan nan, masu farin nan, masu daukan karfen nan sun fi son mace yar sharshara irin wannan ta kwoncen ba?, Yaya kike maganar basu dace ba bayan a gabanki da ya bata runguma ta shige jikinsa gwannin kyau tamkar indiyawa ba?"

"Ke itace fa ta rungume shi ba shine ya rungumeta ba, ke baki san kanwarsa bace?" Ta fada a dan zazafe dan gaba daya ji take abin na bata haushi har a kasan zuciyarta

Saudat ta kebe bakinta ta nemi ratsawa ta gefen Muneerath din ta shige, sai dai bata bata damar hakan ba ta dakatar da ita da hannayenta tana fadin" ki tsaya ki fada min dan Allah mana, ki tsaya ki yarda da maganata dan kar ki sa hakan a ranki bayan ba haka bane, kin ga fa yarinyar cen kanwarsa ce, shi kuma yayanta ne, kuma a zamantakewarsu Mah ita ce mamansu Pah kuma abansu ko? Ina maganar soyaya a nan in ba shirmen irin naki ba saudat"

Saudat ta ringa danne dariyarta a ranta tana fadin ' walahi sai kin kawo kanki da kanki in dai soyaya ce, idan ta barki kika gama haukan boyen zata falasaki ne, mu dai je zuwa ni da ke ma ga mai taurin kai' a bayane kuma sai ta ce" kin ga inace cewa aka yi du mu je mu yi sallah mu sakata a adu'a ba zaki wani tsayar da mu a nan muna maganar da ba ita ba?, Yo in ba abinki ba Muneerath dan kawai tsakanin ya zamo haka to ko Mah ta haifeta ta zo gidan da ita ai akoy soyaya tsakaninsu bale kin manta yar riko ce ita din? Yo kema Pah din da Mah din ai iyayenki ne, yanzun idan aka ce kece budurwarsa sai ace ba kyau?"

Zuwa yanzu so take kawai su yi balaki da Saudat, Allah ma kuwa haka zuciyarta ke fada mata Saudat ba mai kaunarta bace sam, to me yasa zata ringa neman fada da ita? A kan me zata tsaya gata ga ita tana son rikita mata magangannu? Me yasa ba zata bar maganar a yadda ita ta barta ba?

Tana shirin yin magana ta ga mota bak'a na karasowa sojoji na gudu da kafafuwansu haka droon na yawo a saman kan motar, hakan na shedar Hanja na cikin motar

Gabanta ne ya yanke ya fadin mata a lokacin da suka yi ido hudu da shi ya kureta da duba , duban da ba zata ce na meye ba sam
A hankali ta samu kanta da sakar masa harara mai zafi cike da jin haushinsa, wai shi dama gaba daya a nan ya tile? Soyaya da Iman , lallema
Bakinta ta murguda bata iya tsayawa ta ga fitowarsa ba, hasalima bata kula da Pah suke tare ba, shi kadai idannuwanta suka nuna mata ta juya rai bace ta shige ciki tana hada matatakalar ko kula cewar akoy wasu hakimtatum mataye larabawa a dayan falon na kusa da baban falon gidan bata yi ba ta shige lft ta danna tana ta cika tana batsewa

Oga da matarsa da suke zaune suma a falon gefen matayen nan da sam basa jin wani yare face larabci da turanci shi yasa ake zaman kurame dan kowa na son kauce zargin kar wani ya yi tunanin yine ake yi da shi ya kalli Matarsa a hankali ya ce" Kuma yanzu komawa zamu yi hala? Tunda an ce da sauki ko?"

Kallonsa ta yi, irin kallon nan na tsarewa da ido hakan ya saka shi shima kureta da duba, ba irin duban nan na balaki ba, ba kuma irin duba na raini ba, wani duba ne ya mata wanda duda jan idannuwansa sai da ta ga rauninsu

A hankali ta sada kanta muryarta sanyaye ta ce" Nima ban sani ba, yar ogan ce tunda ta bace mana ban ganta ba sai dazun nan a hanya ita da kawarta, ni kam abin na yar oga ya fara bani tsoro, ban san yaushe ta zama haka ba"

Oga ya karra kallonta yana son gane wai ta kula ko da wa kuwa take magana har ta masa a sanyaye haka? Rabonsa da gannin ta masa magana a sanyaye tunda ta dawo hayacinta

Yana shirin yi mata tambayar wani tafkeken soja ya shigo ya tsaya muryarsa sama sama ya shaida shigowar sarkin da Yaransa hakan ya sa larabawan nan mikewa gaba dayansu du suka daidaita hannayensu suka sada dubansu

A hankali Oga ya ce" Toh fah me hakan ke nufi kuma?"

Mamansu Muneerath da bata gane ba itama ta ga shigowar HANJA

A hankali ta karra kallonsa da kyau cike da mamakin yannayinsa
A yanzu jikinsa sanye ne da wandon suit din kadai sai riga ruwan toka mai duhu wace ta dan rike shi daga sama har zuwa kasa kasa kusa da abdo din da ya ninninke ya nuna kansa wajen cikinsa
Hannayensa dake da kauri wajen damatsunnan da jijiya birde birde da irin yadda kasa kasa wajen jimkaken hannun ya nuna kakarfan jiki irin nasa, har zuwa baki sidik din gashin kansa da yake caje gaba gaba ne kadai ya nuna ya dan fara hargitsewa kadan irin cajewar da akai masa ta fara hadewa kadan , har zuwa idannuwansa da jajayen lebunnansa

Da sauri ta cire dubanta a kansa gannin bayan ya gaba gaisar da larabawan nan da yaren larabci radau a bakinsa kamar wajensu ne ya juyo, gabanta na faduwa cike da tsoron me ya kai Muneerath jikin dan sarkin kasar nan?

Pah da ya gama amsawa mutane masu tambayar jikin matarsa yan uwanta na kusa sosai da suka fantsamo dan gannin jikinta da kulawa ya shigo shima ciki wajen Yayar matarsa, da mahaifiyarta, da kuma dayar matar mahaifinta marigayi sarkin Makkah

Cike da mutuntawa ya gaishe su, kafin a nutse ya basu bayanin komai bayan sun yi gaisuwa irin ta larabawan nan

Oga da yake kallon komai sai ya samu kansa da fadin" Nana, inaga wannan runguma da aka yiwa Muneerath ba komai bace, tunda dai kin ga da farko da shi wannan katon ya rungume mutanen nan jira nake ace su dinma yan matan nasa ne? Dan kuwa kin ga su Idan sunna soyaya ba ruwansu da shekaru, sai kuma ga ubansa ma ya aikata, garin nan so suke au karar min da man kaina kaf, walahi so auke du hargitsa min tunanina ta hanyar nunan idan iskanci nake ji su a rubuce suka shanye shi, kin ga mu yake nunowa uban kardai muma su rungume mun mun shiga uku"

Harare ta so sakar masa, sai dai gannin sun nufo su har matan ya sakata mikewa tsaye tana jan lulubinta da tunane tunanen ta yaya zasu gane yaren junna? Ko dai ba'a zama a nan suka zauna?

A mutunce Pah ya fara magana, ga mamakinta sai ta ji Freinch radau a harshen Hanja a lokacin da Pah ya shiga gabatar da su yana dan murmushi kan cewa iyayen yarinyar da suka dauko ne a africa wace Aleesa ta daukota , tana son yarinyar sosai

Sannan ya gabatar masu da matayen suma yana murmushin inda Mamansu su Muneerath ke kara fasarawa Oga wanda freinch din nasa sama sama ne ba wai ya kware bane

Pah ya yi wani murmushin yana fadin" Yarinyar itace yaronku ya haikace a kanta"

Wannan kam sai Hanja ya samu kansa da kasa fasarcewa su mama dukda ya kula fasarar suke jira sai kawai ya dan sosa keyarsa ya dan juya a hankali ya nufi hanyar ficewa yana ayana' Ai fa na shiga uku tunda na ba Pah amanar haka ne, sai ya kuncen wando a ko'ina'

11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□

inda Muneerath din take wani shasha masu kamshi bayan ba abinda sukai mata tana wani hura hanci abinta ga kuma waya a hannunta tana ta aikawa sir attahir message wanda yake zaune gaban tea yana sha yana cike da kewar muryarta, da kewar fadanta, da kewar komai nata aman ba yadda ya iya, maman Sir bata fito a mutun ta fada masa komai ba aman a irin yadda ta nuna shi ba mahaukaci bane, ya san kokowa ce da ta fi karfinsa, hakan ya sa yake nesa nesa da komai nata dan shi kam ya san abokin kokowar nasa ba sa'ansa bane, da ya hada kansa da ciwok zuciya gwara ya ba kansa hakuri

A hankali ya shiga whatsup din kamar yadda ta bukata yana dan girgiza kansa yana son sannin me take so kuma? Idan aike ne sai ya je yanzu yanzu ya yi

Zuwa lokacin ne ta aika masa da kira ta WhatsApp ta kanga a kunnenta
Yana dagawa ta shiga tambayarsa abinda yake damunsa

A sanyaye ya ce" Wani abu kika gani?"
 A hankali ta ce" Gani na yi yanzun baka min irin kalan nan na soyaya da sauransu"

Dan murmushi ya yi na gannin wannan ai wulakanci ne take son yi masa kafin ya ce" Kin damu da su ne? Ko tunda na fara fada maki su kin taba bani amsar kema kina so na?"

Zuwa lokacin ne aka dan buga kofar nasu a hankali

Idannuwanta ta kai wajen kofar kafin ta cire ta dora kan yan matan
Gannin ba wace ta sanma an bugan ya sakata mikewa a hankali ta nufi hanyar budewar ta kama ta bude tana fadin" Freind, aman ai mun yi maganar nan da kai ko?, Nice da bakina na ce maka zan fada maka irin haka da zarar lokacin ka ji ya matso, ka sani b....."

Idannuwanta ne suka sauka a cikin nasa ya wani kuretan nan da kallo baya ko jin wahalar irin kallon nan
Maganarta ta samu ta katse mata a kan lebenta tana kallonsa

A hankali ya langwabar da kansa yana son cire abinda ke son damunsa na wayar da take yi duda bai san ko da waye ba, a hankali ya samu kansa da furta" Yinwa nake jihhhhhh"

Muneerath ta kurawa lebunnansa idannuwa ta kasa motsin kirki har sai da ta so jin kamar Attahir na magana a hankali ta ce" Zan tabo ka idan na gama , ana kirana"

Daga haka ta katse kiran tana kallon irin yadda ya bi wayar dake hannunta da kallo har ya karanci mai kiranta

A hankali ya tsareta da idannuwansa yana jin wani irin abu na tafarfasa masa zuciya
A irin wannan lokacin? Tsakiyar dare ne fa, shine ya yi kiranta?

Muneerath ta ce" To ni dai ai ka san ba iya girki na yi ba HANJA tsakani da Allah in dai ba cake zamu je na maka ba sai dai in su saudat zan taso su taya ni mu dafa ita da i..... Ita da , ita daya" ta samu kanta da karasawa tana wani hararan gefe guda wanda shi kuma gaba daya a tsayen nan ta inda zai bilo mata ya fi tunani domin sam baya jin dadin zuciyarsa, hakan ya hanna masa gane inda indar da ta yi kafin ta bashi amsa

A hankali ta juya dan kiran saudat din yana nan tsaye

Ta fada mata ta dawo tana rike da hijan dinta da kuma wayarta , Saudat din na bayanta infa Iman ta dago ta raka su da kallo gaba dayansu ta koma ta kwontar da kanta tana sauke ajiyar zuciya, sai kuma ta zabura ta mike tana dan sauri ta biyo bayansu tana ayana ai sai dai a dafa da ita

A lokacin da suka fito su biyun ne yana nan tsaye
Singileti ce a jikinsa fara sai wando da ya zarce gwuiwarsa
Har yanzun yar tsoro tsoro ce tsakaninsa da Saudat hakan ya sa tana gaishe shi ta sada kanta ta yi gaba fa dan sauri
Muneerath ta karasa gefensa tana jin damuwar jin yinwarsa a ranta da tunanin bawan Allah idan da ace Mah din ta mutu shikekan ya shiga uku da rayuwa ta sangarta shi komai ita ke masa

A hankali ta budi baki zata yi masa magana ya rigayeta ta hanyar fadin" Ki rufan asiri ki daina tada min hankali"

Ido ta zuba masa tana son yi masa magana iman ta karaso da kula ta ce" Prince me zaka ci na kama masu mu dafa? Ka san Muneerath cake kadai ta iya"

A hankali Muneerath ta lumshe ido daga kallonsa
Wayar dake hannunta bata san lokacin da ta yi mata nauyi ba ta saketa kasa
Bayan ta fadinma sai ta ga idan ta tsaya dauka ta shiga hakin masoyan, a hankali ta juya jiki a mace da niyar komawa daki, tunda ga babarsa ta biyu ita kuma meye nata na yi masa girki? Ai sai ta koma ta saurara

Hannunta na dama da ta ji ya riko ya sakata ja ta tsaya
A hankali ta nemi juyowa sai dai wata bakuwar jaraba sai take jin idannuwanta sun cika da kwalah, hakan ya sa ta nemi janye hannunta dan ta je ta samu iyayenta ta fada masu yanzun bata san me ke damunta ba, kadan kadan sai ta ji magana na bata mata rai har kamar ta yi kuka

A jinginen da yake jikin garu ya janyo hannun nata ta yada zata juyi gaba dayanta ta taho da wani irin karfi ta fada san fafadan kirjinsa inda ya saka hannunsa a hankali ya dafe bayan nata yana shafawa idannuwansa a lumshe ya kai hancinsa daidai kunnanta wanda gashin kan nata ke ta hanna masa hadewa da kunnen naga, muryarsa cen ciki ya iya budar bakinsa da kyar ya ce" My Munarah....."

Gaba daya mutuwa jikinta ya yi, haka kuma ita da kanta ce ta samu kanta da makale kirjin kato a gaban al'uma
Wara yar shashekar kuka ta ja tana sauraronsa
Muryarsa cen ciki bayan ya dan gogi kunnen nata ya ce" Walahi, kasheni zaki yi.....ba zan iya ba, kar ki saka na yi kisa na tada hankalin iyayena, ...kin ga har na gama hango da irin bindigar da zan dauke kansa na huta, ban san me yasa ba"

"Wayo Oga.....". Ta samu bakinta na son kurma ihu ta kirayi abanta ya talafa ya rabata da yaron nan tun kafin ya kasheta

Wa yake son kashewa?
Me yasa ba zai fada mata gwa da gwa ba sai ya raba hali
Ya Allah, ya Allah me yake damunta ne da yaron nan????????

Oho □□

Sorry 2 days na yi tafia ne

Domin samun labarinki, mai sunna WATA KOKOWAR wanda nake kan rubutawa ki tumtubeni ta number wayana kamar haka +227 93 81 16 18 sai kun zo
11/14/21, 12:53 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 □□□ 2 □□□

A hankali ta kuma dan kokarin kwace kanta tana rintse idannuwanta dan jin yadda gaba faya zuciyarta ke neman biyowa ta bakinta ta fito

"Innalilahi" ta fada tana jin ta kasa wani kwakwaran motsi a rikon da ya mata

A hankali cikin dan fada fada ta ce" Ka sakeni, ka wani rikeni kai dai kowace banza tana iya hawa kirjinka kau? Sakarni kar a shiga min zanen cikin yan iska"

Mamakin dake neman kasarashi a kan yarinyar nan sai irin karfin da take da shi a tatare da shi

Ya jima da wuce bangaren da daga ya kalli mace ya ji halitarsa ta motsa sai da ya farra ganninta

A hankali ya fara tsorata da koda son rike hannunta ne bale kafeta da yake da ido shi kadai ya san me yake son karanta a tare da ita da ta fi sauran matan da yake mu'amala da su

Ya yi tunanin ko kalar fatarta ke birge shi? Ya yi tunanin ko wannan bombom din nata ke haukata shi? A yanzu haka ba wai son sakintan bane baya yi, wollah abinda ya mike masa kamar sanda yake jin kunyar aminiyarta da Iman da sukai masa kurru gani
Hakanma sabo ne a gare shi wai jin kunyar a ga yannayinsa

A hankali ya rage muryarsa ya ce" Me yasa dan na rike wata a jikina yake baki haushi? Munarah kina jin haushin na taba wata ba ke ba , kuma ke na taba ki kina cewa iskanci ne, ni kam meye wai irin naku al'adun da ake yi da wa'inda ba'a yi"

Ajiyar zuciya ta ringa saukewa sakamakon sajensa da kuma hucinsa dake sauka a kuncinta, sajensa kuma sai sosa mata lebe suke

A hankali ta ce" Dan Allah sakeni fitsari nake ji"

Sai da ya ji tamkar jinnin jikinsa zai tsaya, a hankali ya ringa dabarar sakatan dan shima ya fahimci idan ba sakatan ya yi ba komai na iya faruwa

Yana cikata da sauri ya juya har yana jin kamar numfashinsa na gaf da tsayawa ya wuce su da wani irin sauri ya shige Lft ya sauka dan so yake ya yi bangarensa ya zauna ko zai samu nutsuwa

Ido da ido suka kalli Junna da Iman, a hankali ta so cire dubanta a cikin na Iman din, sai dai hakan ta gagara sakamakon mugun kallon da ta kula Iman ta tsareta da shi

Muryarta ba karfi ta ce" Ke kuwa me ya samu idannuwanki?, Na ga kamar hararena kike"

Iman ra hadiye abinda take ji a ranta ta ce" Ba kama bace, ba kama bace Muneerath, na gaji, walahi na gaji, me kike so da ni ne dan Allah? Dukan abinda yake nawa kin karbe, harta kusancina da Mah kin amshe bayan kusancina fa Mah ya fi kusancinta da Hanja din kansa da kike ta budewa da isar naki ne, kin kuwa san irin lokacin da na dauka ina dama da soyayarsa? Kin san irin son da nake masa?"

Muneerath dake kallonta a hankali ta ce" Ni yanzun ina hadina da maganar son da kike masa? Idan soyayarku kuke kin taba gannin na yi magana ne? In dan rike nin nan da ya yi ne ki yi hakuri, ni da kaina abin na damuna, sai ace shi musulmi ne, sai ace shi dan musulmai ne sai kuma ya ringa rike mutun a jikinsa bayan ni ba muharamarsa ba, kin ga soyayata da Mah kuma Allah ne ya hadata, ni dai ba danginta bace aman ta rikeni tamkar yar cikinta, wannan kuma ban san yaya zan yi na hanna ba, Iman me yasa kike nemana da fitina ne? Kin ga ni yanzun zazabi ne ya sauko min har rawa jikina yake, mai yiwuwa mutuwa cema zan yi dan zufa ta karyo min, zuciyata ta kusa fito min ta baki, koma menene ki yafe min Hanja kuma ki dafa ki cinye abinki"

Iman ta ce" Abinki dai, gashi kiri kiri kina son min shigar sauri a wajensa? Abin takaicina kamar makauniya, kamar kurma, kamar mahaukaciya idan kina abu kamar innocent, maganar rungumewa kuma ai Hanja kakansu yake yi, a yau idan ya yi niya

sai ya kwonta da mace biyu su kwana a jikinsa, maganar adini kuma ai inaga ba ke ba ya dame kaf ahalinki ya shanye a fannin harda!"

Muneerath ta lumshe idannuwanta , jikinta ya karra mutuwa, shin me yasa Iman ba zata daina mata abubuwan da take yi mata ba? Me yasa kuma idan ta nuna mata tana cikin halin son kadaice kanta bata ganewa? Bata da lafia Bon sang!, Bata cikin mood da kowace irin magana a yanzu! Gaba daya ji take karshenta ne ya zo , tata ce ta kare, shine zata ringa fada mata maganar cewa Hanja na kwana da mata biyu? Dama haka yake? Dama haka ne halayensa? A dan kaushashe ta ce" Ban ga anfanin tarin sannin nasa da baya anfani da shi, Iman wani irin so kike ikirarin kinaiwa Hanja?, Koma wanene so din nan na tsine masa albarka, Iman , Hanja ba saurayina bane, hauka kike rabawa, shirme kike yi, kuma ina matukar tausaya maki, ke baki da zuciya ne? Namijin da kika san yana aikata irin haka da wasu matan ne har kike yiwa irin so din nan?, Ina zaki je da matsalarsa? Ina zaki je da fama da shi? Ko zaki rayu da shi a hakanma?...."

Ta hadiyi yawu tana kallon yadda Saudat ta dawo ta rike hannunta fuskarta na nuna matsananciyar damuwa , a hankali ta ci gaba da fadin" Ko kema aikin da kike na facebook ba iya nan kika tsaya ba? , Ba'a taraya sai halaya ya zo daya, Iman kema aikinki kennan?, Iman ni da ban hada jinni da shi ba, ban hada soyaya da shi ba, wannan abin da kika fada yana kona min zuciyata fiye da tunaninki, Iman ji nake tamkar na yi ra kuka da dukan karfina har sai muryata ta daina fita, Iman ciwo nake ji jin haka yake, ya fara zama abokina, ya fara zama yayana, na fara fahimtar waye shi, sai ki saka min tsanarsa a raina?, Iman halayan nan nasa har ya kai a bayane kowa ya sani? Me mamansa ta dauka mataki? Me mahaifinsa ya dauka? Ko kallon da nake masu na iyaye masu matukar kaunar y'ayansu, masu matukar tsayawa a lamarin yaronsu soyayar bata kai zuci ba?, Iman.....Im....."

Kuka ne ya ci karfin Muneerath, ur Muneerath mai karfin zuciya, Muneerath dinmu da bata san gabas ba, Muneerath dinmu da karamin abu ko nace abu mai tana zuciya baya gagawar taba tata, Muneerath dinmu da ko kukan da ta yi na faduwar Mah nan da nan ta saku da ta ganta a garin harma ta ga da sauki, itace ta fashe da kukan da bata san me yasa ba
Tun karfi ta dora kanta a saman kirjin Saudat tana rusa kukan da dukan karfinta

Muryarta a cen ciki take fadin" Dan Allah, dan Allah ku taimake ni, walahi na rasa gane kaina, dan Allah ku nisantani da kasar nan, ku kaini nesa, daga garinmu zan iya aikowa da Mah adu'a, daga inda nake zan iya yiwa Mah adu'ar samun lafia, Saudat dan Allah ki kirayi Freind a maida ni gida, ba zan iya ba, walahi zuciyata gaf take da bugawa ban san dalili ba, shi kuma ribar me yake ci da wannan abin? Saudat na tsane shi! Na tsane shi!"

Subahannalah, wannan shine ba sabanba namiji da kwontace

Tabas wannan bacin rai da ya rufe ma Muneerath ido tsabar tsagworon kishin da take fama da shi ne ya sakata irin furucin nan, ba sani ta yi ba, ba taba yi ta yi ba, lalle akoy ciwo ka ji wani da kake gannin darajarsa a irin wannan halin aman ta kasa gane cewar abinda ya sa abin nan ya taba zuciyarta har haka dan ta gama macewa a kogin son dan nasara ba tare da ta shiryawa hakan ba, kamar yadda ya gama haukacewa a sonta

A yanzu matsalarta daya ce, kuma tana gannin idan hakan ya kasance gaba dayansu farin cikin hakan zasu shiga

Taba so Na iya cenza mutun, mai mumunan hali ya dawo mai kyakyawa a lokacin da ba'ai tunanin hakan ba

So take ta yi anfani da wannan damar ta samu ta yiwa Hanja dukan da so zai saka shi daina halayansa, duda tana tunanin da kamar wuya
Aman zata kwatanta, tsoronta daya ne kar a je ya kasa zama waje daya ya kula da lafiyar mahaifiyarsa

A hankali ta ringa janta har suka shige suka sauka

Sunna saukowar bata hannata kukan da take yi ba wanda ya saka Pah mikewa da sauri domin falon yake bai jima da saukowa ba, masalaci ya fito shine ya zauna yana jan carbi yana gannin matarsa na masa gizo ta ko'ina a cikin gidan, yana fama da kewarta mai girman gaske

"Subahannalah, me yake faruwa, bata da lafia ne?"

Ya fada yana nufo su yana kallonsu da wani yannayi na tsoron jin abinda ya sajata kukan

Da sauri Saudat ta ce" Ba komai fa Pah, kawai wani dan abu ne ya sakata kukan nan har take cewa zata mutu a kaita Niger". Ta fada da sauri dan kar ya yi tunanin kukan ko na matarsa ne shi mai majinyaciya a kwonce

Muneerath ta dago tana jan hanci ta karra fashewa da kuka tana fadin" Wannan ne karamin? Ke yanzu dan Allah bakya jin kamar zaki mutu da kika ji maganar nan?"

A hankali Saudat ta girgiza kai tana kawar da kan nata cike da son dane dariyar yannayin na Muneerath
Muneerath ta ce" Baku shaku ba shi yasa, aman ni fa muka shaku dole na ji ciwo a raina, Pah wai Hanja, HANJA"

Sai ta kasa karasawa dan tana tsoron kar a je bai sani ba ta fada masa juma a samu matsala

Pah da kula ya ce" Daughter kukan nan ya isa haka , ki daina sshi ki fadan me Hanja din ya yi ne?"

Hanci ta ja tana kallon Saudat ta ce" Fada masa "

Saudat ta zarro ido tana kallonta, sai dai ba zata iya musawa baa domin a tsaye yake a kana kafafuwansa yana jiran jin dalilin kukan, sai dai gaskiya ta gama cutarta
Cike da jin kunya ta fadi abinda ya farun da dalilin kukan na Muneerath tana ji a ranta Idan suka kasance daga ita sai ita sai ta rama walahi!

Pah ya sauke ajiyar zuciya a sanyaye ya ce" Daughter shine kike yiwa wannan kukan kamar an yi rasuwa?"

Muneerath ta ce" Pah, wannan abin ai ba karamin aabu bane, Pah ba abin wasa bane, shin idan ya mutu a irin halin nan fa? Ni kam dan Allah kaa taimaka a kaini gida cen Niger ba zan iya ba, abubuwaan garin nan yanzun na kula so suke su kasheni"

Da mamaki yake karra kallonta , tausayinta ne ya ji a kasan zuciyarsa, yarinyar ta yi falng a love , tanaa matukar kishin abin soyayar nata, aman bata sani ba
Sosai ya so ya rarasheta ta koma ta kwonta, sai dai wani tunanin shima ya same shi

Ba tare da jan abin baa ya bada damar a tayar da Jirgin Masarauta da yake a A roport din bangaren Sarkin daban wanda yake taronsa da sauransu harda jirginsa a wajen , kan za'a kaita gida

Iyayenta da suka samu dan lokaci nasu na kansu suka fara fuskantar junna Oga ya ji cewar wai wani yar Oga na kukan a maida ita gida
A tunaninsa abin na wasa ne ya ga an kuma tashin Jirgi guda mai shegen kyau da sanyi an zubo au dagaa su sai su bayan sun yi salama sukai kuri a zaune a Hight class sunnaa kallon junna

Aun kusan tafiyar awa daya abin ya tuko shi a hasale ya ce" Ke yar Oga dan ubanki ba kin sa an daukomu an ciro mu bamu shirya ba kuma kukan na uban meye kike ne? Ko salon sojawan cen dake cikin baya su zo su kashemu su ce mu muka saka ki kuka? Ashe sojojin nan dake yawo a anguwarmu masu tsaronki ne? Kai mutane Allah mai iko kai kacari ka haifi sarauniya"

Mamanta taa ce" wai me yasa kai sai zagi dazu fa na ce maka ba mutunci bane zage zagen nan"

Habarsa ya rike ya ce" Yo ni nana abin ne ke karra daure min kai,, kina gannin ikon Allah fa, wai dan ta yi kuka tsakani da Allah sshi jirgin hala da batiri yake anfani ba da esansi ba da za'a ringa tayar da shi saboda kukan yar ogo?"

Muneerath da kanta kamar ya rabe biyu dan ciwo cikin kuka ta ce" Oga ka san me aka yi ne? Oga wai yanzu Hanja ashe mata yake bi? Me zai hanna ni kuka dan Allah?"

Oga ya zarro ido kafin ya tafa hannunsa ya ce" In ban dake ki ba shege nake sai dai su kashe ni, yau na ga iskanci gannin idona, dan ubanki ubanki ne shi da zaki ringa rizgar kuka dan yana bin mata? Yo Allah na tuba yau talaka fitikma ya bi mata bale mai kudi kuma sarki? Ke ina ruwanku tunda dai sonki yake kawai mu daura maku aurenku mu tarkato mu dawo , halinsa kuma ya daina ko kar ya daina idan ya mutu sai su gana da walakiri!"

Ido ta zubaa masa cike da takaici, hakama mamanta, suka rasa abin fada sai kallon kallo, inda Saudat ta mike da sauri ta nufi bayi dan ba zata iya rike wannan dariyar ba kam, kasheta zasu yi ahalin nan walahi.

Yinwar da ya kwasa manta batunta ya yi sakamakon tunani da ya sako shi a gaba

Taa ina zai fara yada mata manufarsa? Dole ya hanzarta dan ya fara tsoron mai kiran nan nata shi kam, baya so su saka shi a ha'u'la'i, au saka shi yawo ba riga
Sai da ya raba dare kafin ya mike ya dauro alwallah dan gabatar da sallah kafin ya zauna ya buda alkur'ani ya shiga karatu a nutse yana lumshe idannuwansa yana tuno fuskar Mah dinsa
Tare da ita suke yi har sunna tsokanar junna idan mutun ya yi wani kuskure a wata gabar

Sosai ya roki Allah a kan abu hudun nan
Na farko gamawa da duniya lafia
Na biyu shiriya
Na uku lafiar Mah dinsa
Na hudu Allah ya bashi sa'a a kan yarinyar nan, dan ya fara tsoron abinda ta yi dan kawai ya dan rungumeta tana cewa shi sai rungume mata, to idan ta san waye shi yaya kennan? Kai ikon Allah bai taba jin tsoron a san yana aikata zina ba sai yau
Da sauri ya nemi da Allah ya rufa masa asiri kar ta ji.....to amaan wai kishinsa take ko menene?

Allah Allah yake safia ta yi, sai ya saka kayan da ya san dolema ya kasheta, sannan ya fada mata cewa" MUNEERATH ina son ki, ki yarda ki zama sarauniyar Ingila taa hanyar zamowa matata"

□□□□□□□□□□□□ Ham, kak, na fada masa ko na bari ya gani?□□
11/14/21, 12:54 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Washe gari
Tun karfe bakwai suka nufi asibiti daga masalaci tare da Pah da Hanja

Sun jima a zaune a kusa da ita sunna tofa mata adu'ar neman sauki a wajen Allah

A hankali Pah ke shafa gababn goshinta da ya yi fes da shi a sanyaye yana mai yi mata dadadan kalamai da nunin cewa ta jure, ta daure, kar ta saka, kar ta manta sunna nan , sunna da bukatarta
Hanja kuwa hannunta yake rike da shi mai jone da wata na'urar shima
A sanyaye ya ce" Mah, ganninki a wannan yannayi na kashe dukan kuzarin jikina, Mah yau zan fuskantace ta, ban san yaya zata dauka ba, da ace kina nan ifannuwanki biyu da rai da lafia da kin tare min ita koda ta zo baude min, plz ki motsa ko yayane ta yada zan samu kwarin gwuiwar fuskantarta ki motsa ki nunan kin san ina nan, ki motsa Mah....."

A hankali Pah ya lumshe idannuwansa cike da tausayin yaron nasa,
Wani tausayinsa ya kara shigarsa na Idan ya ji ta tafi yaya zai dauki abin?
Sai dai baya tunanin karamin rigima zata saka Hanja gane matsala ne bibiyar mata da yake, ba wai a adininsa kadai ba, harta matar da yake so idan mai adini ce zata ji kishinsa
A hankali ya juyar da kansa yana aro dukan jarumtar da yake da ita dan yaki da tausayin yaron nasa da fadawa kansa cewa idan har ya jure ya daure ya kasa falasa kansa a gaban yaron nasa dan taimakon yaron nasa ne ba dan wani abin ba,

A nutsue ya kuma hade lebunnansa da jikin kunnen Mah na dama a sanyaye ya lumshe idannuwansa ya shiga karanta mata surorin alkur'ani dan kara sama mata sukunin zuciya, ya yi imanin idan me take ciki adu'a zata sanyaya mata cutarta

A haka har suka gama ziyartar nata suka fito da zumar sai da rana domin likitocin dake tsaye a kanta sun basu lokutan ganawa da ita idan a ra'ayinsu ne, sai dai kuma ifan sunna son ganninsu wannan kuma ba laifi bane sai su zo su ganta su zauna da ita adadin lokacin da suke so, domin a cewarsu idan ana yiwa mutun magana yana ji a mafarkinsa

A falo Pah ya zauna har lokacin bai ga wulgawar Iman ba, bai san tana wajen mahaifiyarta ta labe cike da tsoron bayanuwar abinda ta aikata wanda ita da kanta ta san cewa fitina ta janyowa kanta da kanta

Kamar yadda ya yi niya, bai iya komawa barci ba , wanka ya dauki lokaci mai tsayi yana yi kafin yake fitowa da wayarsa ya zauna dan shi kam bai san wani irin kaya suka dace ya saka a irin wannan lokacin ba
Abinda bai taba yi bane ya yi ta hanyar tabo number masu shirya su na masarautar ya nemi kan su zame a bangarensa da irin shigar da take iya birge mace mai tsatsauran ra'ayi su taya shi shiryawa

Ai kam hakan ce ta faru, a cikin minti ashirin suka karasa da dukan abubuwan bukatunsu suka zame a bangaren nasa inda ya zauna daga shi sai rigar wanka suka shiga shirya shi ta hanyar sake lumde fatarsa da sinadarensu na shirya mutun, shi kuma ya zauna ya basu hadin kai idannuwansa lumshe yana tunanin ta yaya zai iya da ita ne?

Sun dauki a kadan awa daya a kan shirin Hanja, domin shirin da bai taba tsayawa ya yi bane akai masa, barta da gashin kansa sai da suka caje masa shi suka yi tsaga ta yadda wani ya yi baya kadan ya tsaya sama sama kadan

Suit ruwan baki sidik ne suka gabatar masa , da macheste, da safa fara kal kamar yadda rigar ciki take fara kal, da bakin takalmi kafa ciki, harta da gajeran wando sai da suka hadowa shigar nasa suka hada masa
Nan ya shiga ciki ya saka kayan ya fito , suka hau gyara masa mabalan wuyan rigar da komai cike da yabawa da irin kyan da kayan sukai masa, inda shima da kansa yake yabawar a zuciyarsa

Kampanin Julieta ne suka kawo flowers din da shi da kansa ya bada ordensu aka shigo masa da su rututu dan so yake Pah ya taya shi zabe aka zubewa Pah a gabansa wanda jikinsa ya karra yin sanyi sosai yana kallo cike da tunanin yaya zasu kare da yaron nasa

Kyau kam, Hanja ya yi kyau, ruwan kyau da fuzga ya yi shi, kayan sun amshe shi sosai harma ya yi masu maganar cewa idan har ta amince da maganar daje tafe da shi, lalle zasuna shiryashi kulun

A nan ya bar wayarsa ya sauko yana tambayar idan har darius ya shigo domin shima a yau ya bukaci ganninsa dan ya samu kwarin gwuiwar tunkararta da kalaman da suka dace

Pah ya lumshe idannuwansa bayan kamshin turaran yaron nasa ya fara isowa inda yake yana fatan Allah dora shi kansa kar au raba hali gashi yau mai tsawatar masunma bata nan

A gaban Pah ya ja ya tsaya yana murmushi tare da dan yin alamu irin na ya fada masa ya yi kyau kuwa?

Pah ya saki murmushi yana kallonsa ya furta" Masha Allah, my hero, my son u look lk a □□"

Dan murmushin ya kuma saki yana bada damar Darius ya shigo ya fada masa me yake gani da kalamansa

Pah ya zauna ya karra bada hankalinsa a kansu yana murmushi
Darius cike da farin ciki ya shiga fadin" Duk matan duniya sunna son idan aka tsaya a gabansu a koda kyansu, farinsu, gashinsu, dukiyar da suka malaka da....."

A tausashe Pah yana tatare girarsa na sama ya furta" Plz Darius ka dakatar da abubuwan nan da kake fada domin na tabata idan ya yi kokarin nunawa wadda yake so wannan tabas zata nemi fada da shi ido rufe, bama irin matan da ake sace zuciyarsu ta haka bane, an fada maka kowace mace ce wannan ke rufe mata ido? Wata macen tana sonagana ta gaskiya ne, wata macen du tsakaninta da kai bata so ka yi mata magana irin ra karya"

Hanja ya dubi Pah yana murza agogon hannunsa ya ce" Pah, ban taba jin shakar duban halita na yiwa maganar kamar yadda nake jin na yarinyar nan, me zan ce mata dan ta saurareni?"

Pah ya yi murmushi yana kallonsa ya ce" Ba tsoronta kake yi ba, tsoron amsarta kake ji, bale a irin wannan lokacin ban san yaya zaku kare ba"

Yana kallin Pah ya sauke ajiyar zuciya yana fadin" Nima na kula saboda rashin lafiyar Mah itama sai kuka take bata son damu, ban san yaya zamu karre ba"

Pah ya ari jarumta yana kallonsa da kulawa ya dan watsa hannayensa ya ce" Khadija mama take a wajenta, shi yasa a rikice ta zabi ta koma daga gida ko daga cen adu'arta zata tardo Khadija da bacin ran da ta kwasa, shine abin ya daure min kai irin kukan da take a jiyan nan, anya itama ba sonka take yi ba?"

Darius cike da farin ciki ya ce" Sarkina, ko dai princesses Iman ce mai wannan sa'ar?"

Hanja da yake ta auna maganar Pah a ma'auni da sauri ya ce" Pah, ban gane ba, wace ta tafi ina? Take kuka a kan me?"

Pah ya kuma yardawa kansa jarumta ya ce" Inaga ko a cikin hira ne jiya ta tsinci labarin ka kasance mai yin taraya da wasu yan matan da ba matayen aurenka ba, ni kam ban san meye ya hargitsata har haka ba, baka ga kukan da take tamkar zata mutu, cewa take kirjinta ciwo, ji take kamar lokacinta ne ya yi a taimaka a kaita Niger, gannin abin nata da gaske ne ta kasa nutsuwa da gagawa na umarci kan a kaita gida tare da bada umarnin ATTAHIR AHMAD ya yi jagorar bukatarsu ta cikin jirgin"
11/14/21, 12:54 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 □□□ 4 □□□

A hankali ya dago dubansa da idannuwansa da suka fara dauko maganar Pah din har zuwa inda ya furta sunnan mutumen da yake jin haushinsa har ransa ya sauke a kan Pah
Muryarsa a nutse ya ce" Pah dakata, ban gane komai ba plz, wacece ta tafi dan an yi me? "

Pah ya hadiye yawu yana karra nuni da sam shi bai san me ya sa ba hasalima ya nuna cewar shi taimako ya yi ta hanyar fadin" Da kyar aka iya rike Muneerath tana ihun kuka, inaga ta ji maganar cewa kana mu'amalantar wasu mata tamkar na aurenka bayan ba na aurenka bane, shine take fadin zuciyarta ciwo take yo mata ba

zata iya zama ta kwana ba, na kwatanta rarashinta gannin dare ne a jiyan sai abin ya gagara a dole na saka aka kaisu Niger din domin idan ka ga kukan da take sai ka tsorata kar a je ta suma ko ta kamu da wani ciwon"

Tsayuwar da ya yi a gaban Darius sunna tataunawa ya ji gaba faya kafafuwansa zasu maka shi da kasa ta hanyar daukansa suka nemi zubar fa shi ba tare da ya shirya ba Kansa sai da ya amsa na dan lokaci ya sake kurawa fuskar Pah ido yana kallonsa

Darius hankali tashe da ya riko hannunsa daya da dukan hannayensa da karfinsa dan taimaka masa yana fadin" Kula Sir kar ka fadi mana"

Da karfi ya janye hannunsa da ya fara taurara dan bacin rai yana kallon Pah , muryarsa a kausashe ya ce" Kana nufin Bata cikin gidan nan a yanzu haka?, Ta tafi kasarsu dan ta ji wannan yar maganar? Menene damuwarta da wannan maganar koda ta jitan? Inace wa ubangijina kadai nake da damar bama dalilin aikata hakan ba wani halita ba?"

Pah ya tabe baki yana daga kafadunsa ya zauna tare da sauke ajiyar zuciyar gannin bai zube din ba ya ce" Ka san dama wani lokacin ina fada maka cewa wasu matan da suka san ciwon kansu basa koda magana da masu irin halayan nan, inaga tana cikin matan ne"

Gabansa sai da ya doka da karfi hakan ya sa a birkice ya ce" TaTaTana cikin matan da basa kula namijin da ya kwonta da wata macen da ba ita ba?"

Pah da sauri yana kallonsu gannin su duka abin mamaki yake basu ya ce" Ba haka nake nufi ba, ina nufin musulma ce ita, sannan al'adunsu na tafia da adininsu ne, a kasarsu aikata hakan dati ne, mai aikata hakan kuma dan iska ne, basa ko garajen rike hannun junna tsakanin maza da matayensu, basa rungume junna da garaje, namijin da ya mayar da kansa mai biyan bukatarsa da macen da ba tasa ba su da kansu auke kyamatarsa domin sunai masa kallon wanda baya jin tsoron ubangijinsa"

Da mamaki Darius ya ce" Kai abin mamaki, saurayi dama ana kayade masa irin macen da zai yi mu'amala da ita? Gaskiya adininku akoy takura to ita ta yaya zata ce Prince na ingila zai zauna da mace daya? Lalle tana da rigima"

Pah ya dube shi, a saukake ya ce" Adinina bashi da takura, adinina mai tsafta ne, sannan bai hanna mutun auren mace daidai har hudu ba idan har yana iya kamanta adalci a tsakaninsu, kai naka adinin ai kwaya daya ya halatawa mutun, a haka kuke zaune da sunnan matayenku daya aman yan matayenku dubu wannan shine adalcin?, Darius plz ka barni na gana da yarona"

Dan risinawa ya yi kansa a kasa yana mai neman afuwa idan ya bata masa sannan ya fice da sauri cike da mamakin kai kawon da Hanja yake yi, koda yake ya san ko wacece ta yiwa kanta, ya tabata prince dinsu na iya dauko dubunta Idan yana so, aman har a yiwa prnc maganar mace wace kala ce bai fede ba? Ai sai dai kar a kuma kawai

A nutse Pah ya furta" Hanja ka tsaya waje daya mana"

Da karfi karfi ya ce" Na tsaya waje daya? Na tsaya waje daya? Ina son tsayawar na kasa ne, na kasa tsayawa Pah, Pah me yasa ni? Me na yi nake fuskantar wannan hukuncin? Dan na kwonta da mata? Na san adinina ya hanna, aman nawa al'adun basu wani hanna ba, Pah bani da aure, shikenan sai na tsaya na mutu da ciwo a

cikina shine ta yi tafiyarta? Pah ni na san ba zata taba sona ba, idan kana son mutun komai ya aikata ba zaka guje shi ba, Munarah tana soyaya da Attahir ne ba ni ba, an fada mata shi Attahir din nata bai san harkar mata bane? Shine zata shiga jirgi da shi su koma kasarta ta bar Mah kwonce ni kuma ina yawo kamar dan iska?"

Pah ya sadauta muryarsa ya ce" Calm down son, ba fa abin ihu bane, ka gane ita tana aiki da hannawar Adininta, bata wasa da wannan kuma tana tsanar mai wasa da wannan, dukan musulmin kirki ya dace ya kiyate dokokin adininsa, My son Allah ya halice mu ne dan mu bauta masa fa, shin Idan ka mutu a cikin aikata zina me zaka je ka cewa ubangijin da ya maka rai, ya baka daula, ya baka lafia da hankali da dama na rayuwa? Me zaka ce masa idan ka tsaya a gabansa ya nemi dalilinka na aikata hakan bayan kana da damar ajiye macen sunnarka?"

A hankali ya yi baya ya zauna saman kujerar dake kusa da shi ya saka hannayensa cikin gashin kansa ya jimka da karfi.....magangannun da yake a cikon zuciyarsa sune 'Shikenan na rasa ta?, Shikenan na yiwa kaina ilah? Shikenan na kashe kaina da kaina? Innalilahi wa inna ilaihi raj'une, Astagfrullah, Astagfrullah, ya Allah ka sanyaya min wannan zafi da nake ji a zuciyata'

A hankali Pah ya zauna kusa da shi da damin flowers sunna kamshi ya kamo tafukan hannayensa ya bude ya saka masa gindinsu a nutse ya ce" Ka tashi ka je "

Juyowa ya yi da dadadan kanshin flowers din masu sirki da yelow da fari kal a hannunsa yana kallon Pah tamkar bakon Halita a gare shi

Pah ya ce" Idan ka yi wasa, ina tsoron fuskantarka na baka hakurin rashinta, ka tashi ka je za'a kaika har kofar gidansu , sai dai ka sani Muneerath ba irin yan matan dake lashe didigenka bane, ita da Allah ya halicema bai saka mata tsoronka a ranta ba bale ka yi anfani da wannan damar ka sakata dole, sannan ta san kana da kyau ta kuma yarda da hakan aman bai wani damunta, haka kuma irin sarautar garinmu daria take bata , cewa take mu da bama rawani?, HANJA ban san ta yaya zata dubeka ba, abinfa na sani Idan ka samu kanka a gabanta ka bar zuciyarka ta fadi abinda yake cikin zuciyar taka"

Lebensa na kasa dake rawa rawa ya samu da kyar ya iya furta" Pah, Mahna?"

Pah ya yi murmushi yana dan dukan gefen kafadarsa ya ce" Mah dinka, Mah dinka tana tare da Allah, nima zan koma kwana kusa da ita, my son jira ba zai kaika ga ci ba, ka yi jinkiri da yawa, kasancewarka a nan kuma ba shi zai tashi kafadun Mah dinka ba, you see ka rigaya ka balowa kanka ruwa tunda ka fadi a gaban kanina cewar zaka hau mulki, ina so ka hau shi da darajarka, daga nan garadai zasu maka rakiya, haka kuma a cen Sarkin garin ya fada min cewa ya tara dogarai da dawakan garinsu zasu yi maka jagora, sannan president dinsu ya bani maganar cewa sojawa tuni sunna shiri, Son ka dauko abinda ka je nema plz"

Idannuwansa ya sada yana jin zuciyarsa na dokawa ya kasa kwakwaran motsi har sai da Pah ya yi yar dariya ya ce" Ban taba tunanin gannin tsoronka a bayane ba sai yau, ashe kaima akoy abinda kake tsoro? Mace?"

Da sauri ya kalli Pah yana hade fuska ya ce" Tsoro kuma?"

Pah ya gyada kai yana fadin" Eh mana, dubi fa , kalli hannunka a jimke aman sai rawar lebe kake HANJA Sarkin ingila kake fa"

Ajiyar zuciya ya sauke yana cije lebensa ya mike tsaye yana rintse idannuwansa kafin ya juya da sauri sauri ya fice yana amsa adu'ar mahaifinsa a cikin zuciyarsa ya tarda taron sojawan da aka hado sho da su, sai ya ji har wani nauyi na son kama shi ya kara cin fuska ya wuce tsakiyarsu suka nufi wajen jirgin.

"Wai me take faruwa a garin nan ne Nana nake gannin shiru ya yi yawa kamar an kame mutane an labe?" Oga da yake shigowa yake fada

Kishiyar Maman su Muneerath dake fama da kayan miya ta dago ta masa kallon uku biye da shi da maman Rumaisae dake ta faman hade haden turaran wutarta na siyarwa wanda ta matukar kwarewa a hada shi ta ce" Aman Oga gaskiya ka fara rashin jin tsoron Allah a al'amuranka, wai me yasa komai naka ita ce? Du motsinka ita ce? Ni fa abin nan ya fara isata walahi salon na yi magana a ce bani da hakuri, haka kuka tafi kuka yi kwana biyu a ban ina ba kuka barni da jarababun y'aya uwa haihuwar cikin wuta dafe ni ne kadai basu yi ba a gidan nan kuka dawo kana ta wani budewa kana karawa, kiri kiri sojoji a kofar gidan nan sun hanna yayata shigowa ban san dalili ba oga ko dai a wajen cacar taku ka ciyo mana jaraba bincikarmu ake a kwace gidan da muke karya da shi a kashe mu?"

Oga ya wani irin jan birki yana kallonta har ta gama
Tun dafa kafarta har kanta ya karewa kallo, ita dai irin matan nan ne masu tsayi Masha Allah ga kira mai kyau, sai dai a rayuwarta bata san meye gyara ba, kan nan nata kamar gwuiwa a gwaguye kuma bata daura masa dan kwali, kafar nan faso ta mata kanta sosai sai a hankali, a yannayinta na mace idan ta zo gitaka sai ta bajeka da warin jiki irin na gashin hamata da zaamin gyafto, haka take, haka rayuwarta take

Kawai gani ya yi walahi ba zai iya bata amsa ba gaskiya, shi kam ai yanzun yana da abubuwan tsayawa yi a gidan, bale kamshin nan da nana ke hadawa ai dole ya dan zauna a gefen yar oga da ta haukace ya daki babar rigarsa ta yadda idan ya fita zai karra ba makiya haushi
Baki ya tabe yana fadin" da na zama dan yesu idan da adinin musulunci ya hanna ka yiwa dayar matarka magana dan ba aikinfa bane, kin ga ji ba matsiyaci bane walahi da kudina a aljihuna yo haukanki ki gama"

Juyawa ya yi wajen Muneerath da ta kalli Saudat a sanyaye ta ce" Ki ce dai irin kwatancem zuwarma mutun da kika min shine yake yiwa wasu matan ko? Kai Allah wadaran naka ya lalace!"

Saudat kasa kasa ta ce" Ki yiwa Allah kar ki bari mamanki ta ji wannan maganar walahi ta hada daga ni har ke ta jinyata mu, yau na ga shirme to wai ke ina ruwanki ne?"

Oga ya karra kura mata ido ya ce" Ni kamar da kayan nan Yar Oga ta yi barci kuma sune a jikinta Nana?"

Mama ta tabr baki tana zuba kafin kafin a turarenta ta ce" Kiris nake jira na maka mata muciyar nan Abanta, ka duba ka ga yarinyar nan ta ci abinci ta ki ci tana zaune da wani wando da riga ta saki jiki kamar wata katarpila sai langwabar da kai take irin ka mutun nan ta saka ni a gaba in na yi ciki ta bi ni Idan na dawo ta biyo ni , wata sangartar ai bata da anfani!"

Oga ya wani saki murmushi na jin sabon sunna Aban Muneerath da akai masa ya juya zai nufi wajen Muneerath din matarsa ta fito daga cikin kicin tana ta ruwan hawayen hayakin itace ta rangada buda tana kama baki ta ce" Daga sweet heart an koma azamulumi mai yiwa y'ayan mutane asiri, yau kuma Aban Muneerath aka dira? Ka ga bariki kiri kiri watau mu ba haihuwar y'ayan muka yi ba ko uban Muneerath ne ita kadai?"

Oga ya kuma jan birki ya juyo yana kallon yadda take ta shirnatu abinda dan ta karro wani warin hayaki sai huci take, kai shima akoy jaraba yanzun wannan matarsa ce? Du muninsa ya fita tsari tinda shi wanka yake, a kausashe ya ce" Kin san Allah in ban yi wasan kura da ke a gidan nan ce min shege, ku ji yar bakin ciki ai ci gaba aka samu, a da bata da hankali a gaban kowa ni din nam nine swuit heart dinta, daga baya aka yi walkiya ta ganni a fili na dawo makiyinta, yau kuma ta yafe min ta kireni da sunna mai daraja zaki ji haushi dan ke kina ce min Oga? To ni du ubanda ya kuma ce min Oga ba aban Muneerath ba sai na dauke fuskarsa da mari a gidan nan ka ga iskanci ko?"

Dansa ne ya shigo da sauri yana zarro ido ya ce" Kai Oga anya anguwar nan lafia kuwa ? Dazun mun ga an zagayemu da sojoji bamu damu ba dan dai kowa ya san BAZOUM da bada tsaro a kasarsa, aka dan jima motoci suka karu abin tsoron harda sojoji da gendarmomi, to kuma yanzun laluwa ke kusanto mu Oga aka shigo layinmu abin tsoron na ga ana magana da yan anguwar ana ta mayar da su gida, kar dai a je wani ya aikata laifi a gidan nan ka fa san kaf anguwar nan gidanmu ne yan kwaya"

Dau ya dauke fuskarsa da mari yana kallonsa ya ce" Dan ubanka yanzu na dora dokar kirana da Oga sunnana Aban Muneerath, sannan ban gane ba har yanzu kana siyar da kwayar ne? Na shiga uku kar dai a je kun janyo min jaraba ina zaune ban sani ba?"

Da sauri ya juya ya fita hakan ya sa hankalin matayen da y'ayan gidan gaba daya tashi, mai iya dauko mayafi ko hijab ta warto da gudu, wada bata iyawa kuwa a haka dinta ta nufi kofa da sauri dan gannin abinda yake faruwa ciki kuwa harda Muneerath dake sanye da wandon barci wanda da kadan ya dara gwuiwarta sai rigarsa fara kal mai siraran hannaye

Tsoro ne ya darsu a zuciyoyinsu
Mita daya tak ce a tsakiyar anguwar wace ta fi kusanci da kofar au Muneerath, sai ko tarin iko watau sojoji da gendarmomi da dogarai manya manya amintatun sarki cikin sababin shiga irin tasu masu digiri da digirgir watau ko a cikin dogaran masu tsafta ne, wa'inda suke da damar zartar da hukunci idan ka yi batanci ga sarautar kasarmu, sun sha rawaninsu manya manya sababi dal, cikin shigarsu irin ta dogarai sun rike sandunna irin nasu kowane a shirye yake sun layu gefen hagu da dama gaba dayansu hakan ya sa suka yi caaa kuma suka cika ido sosai

Oga ne ya fara yin saranda a tsayen da yake inda gaba daya iyalansa suke bayansa irin sun labe a bayan wada ya fi kunar nan, watau kauran nasu

Zufar dake goshinsa ya samu da kyar ya share a sanyaye ya ce" Inaga motar cen bom ce a ciki za'a seto mu ne a kashe mu gaba daya, oh haihuwa, haihuwa? Na haifo wanda ya je ya zagi shugaban kasa ina ga an zo a kashe ubansa da danginsa, Innalilahi wa inna ilaihi raj'une"

Da sauri maman su Muneerath ta riko hannunsa tana kallonsa ta ce" Aban Muneerath dan Allah ka je mana, ka je ka ji menene ka ga fa inaga mune muka yi laifin dan na kula kaf mu ake kallo"

Hannunsa ya janye yana kallonta ya ce" Kaya, kaya Nana, ba zaki gane ba, dole a kalle mi, anguwar nan waye marar ji irinmu? Dan Allah ki yafe min kar na mutu da fushinki kin ji matar aljanata?"

Muneerath dake bin dogarai da kallo cike da mamakin Dogarai ne birjik haka a kofar gidansu ta samu da kyar ta fito daga cikin yan uwanta ta matso gaba sosai tana karra kallonsu, da sojawan da suke tsaitsaye fuska a hade kamar masu jira a yi motsin da bai masu ba su harbe mutun

Daidai lokacin da Hanja dake tura mesage a wayar Pah rai bace kamar haka" Baka ce min da dogarai a tafiata ba, wadinnan sunne fa Muneerath ke haukan so, idan fa ta kore ni saboda su? Kuma baka ce min Attahir ne zai kawo ni gidan su Muneerath ba, me yasa kake min haka be?...." A hankali ya ji dukan da zuciyarsa ta masa ya yi tsanani da yawa hakan ya sa ya dakata yana dafe gaban zuciyarsa kafin ya dago da dubansa a hankali ya sauke a gaban motar

Makoloton makogwaronsa ne ya motsa ya yi sama ya kuma yi kasa lokaci daya sakamakon ganninta da ya yi tsaye tana karewa mutane kallo bata motsa ba daga inda take
A hankali ya juyo bangaren Attahir ya ga sam ba wajenta yake kallo ba, sannan ya sake maidawa wajenta

Idannuwansa ya rintse sakamakon jin takaicin shigarta da kuma mamakin kansa, wace irin shiga ce budurwa bata yi su fita da ita a matsayin budurwarsa bai taba damuwa ba sai yanzu wannan shigar ta Muneerath da take rufafiya a kan shigar yan matan garinsu, sai ya ji wani irin abu na dukan kirjinsa mai zafi da sana sannin kwaso mutanen nann, kai saima ya ji dama shi daya ya zo aka harbe shin da mazan nan su kare mata kallo

A hankali Attahir ya kara sada kansa ya ce" She love u, ta fada tarkon sonka a lokacin da ita kanta bata shirya ba, ya dace ka rike abinka domin ita din mai aiki da fadin rai ce, ta ga damar saboda fadin rai ta yarda da waninka"

Kallonsa ya yi a karro na biyu kafin ya kuma kallonta

Da sauri ya zarro ido ya samu kansa da bale murfin motar da saura yaana mika hannayensa baya ya dauko flowers din da ya zo da su sakamakon gannin ta nufi wajen dogaran nan har kamar zai bar kafar daya a cikin motar dan sauri

Da gagawa Oga ya daga hannayensa sama yana fadin" Ta zo, mutuwar ta zo "

"MUNARAH" Ya fada a hankali yana kallonta

Da sauri ta ja daga niyarta na son karasawa wajen dogaran nan ta masu tambayar shin me suka yi ne?

Juyowa ta yi a hankali ta sauke idannuwanta a kan fuskarsa

Wani irin tsale zuciyarta ta yi ta doka , a hankali ta nemi zubewa kada sai dai hakan bai faru ba saboda tangal tangal ta yi kafin ta yi gagawar kauce hannunsa da ya miko da nufin son tarota kar ta zube

Baban dogarin Fada ne ya daga murya yana fadin" Ku sada dubanku a gaban sarauniyar Ingila, Allah ya ja da zamaninki mai farin jini, tabas ke din halita ce ta Allah wace ya hada da madaukakiyar baiwa, ku sada kawunanku a duba ga cikin duban abin duban sarkin Ingila Umarni ne daga mai girma mai martaba sarkin garinmu"

Ai kam daga sojojin dake kallon mamakin dama wannan yar bak'ar ce, har zuwa dogaran da sauri suka sada dubansu, ita kuma da mamaki take kallon wanda ya yi maganar tana bukatar karin bayani

A sanyaye ya kuma furta "Munarah, plz ki kale ni"

Tsoron kallonsa take ji, wayo tsoro take ji ta juyo gare shi, hakan ya sa ta ki juyowar sai kallon gefe da take cike da tsoron abinfa ke iya faruwa idan ta kale shin

Rigar dake sama ta suit dinsa ya cire a hankali ya kara son matse mata waje
Kanshinsa da ya karra kusantota ya sa da sauri ta dube shi a haukacr ta ce" Walahi kar ka taba ni, wayo na shiga uku zai taba ni Oga, mama ku taimaka min"

Kasancewar da hausa take maganar sai ya dan ja yana kallonta domin ko yaya maganar nan dai ba mai dadi bace, hakan ya da yake kallonta har ta gama ihun

A hankali ya mika mata rigar tasa yana kallonta

Rigar ta harara sannan ta kale shi tana jan hanci ta ce" Meye hakan kuma?"

HANJA ya lumshe idannuwansa a sanyaye ya ce" Plz, ki rufe jikinki, ki rufe bana so sunna kallo"

Jikin nata ta kalla sannan ta kale shi tana karra turo baki ta ki amsa

Saudat da ta fito da gudu da hijab ta karaso a hannunta tana mika mata cike da wani irin farin ciki marar misaltuwa

Muneerath ta amsa ta bude ta saka tana riko hannun saudat kasa kasa ta ce" Tafi da ni, me ya kawo shi garinmu? Saudat tafi da ji ina jin ciwon nawa na neman tashi zuciyata ta fara kusanto bakina kaini fakina dan Allah na sha magani kin ji?"

A hankali ya kara matsawa yana nuno mata Flowers din hannunsa da suka dan fara langwabewa saboda zafin garin yana kallonta a gabanta

Flower din ta kalla ta kale shi, a sanyaye ta ce" Hanja shukar nan fa ta menene? Ni kamar baka da lafia dan Allah meye ne? Wayo Ogana zuciyata zata ballo dan Allah mu je ciki kin ji Saudat?"

Saudat ta girgiza mata kai tana kallonta ta ce" Muneerath ba inda zamu je, ki saurare shi dan Allah"

Muneerath ta warce hannunta cikin fada fada ta ce" Ba zan saurare shin ba, na ki na saurare shin na ce! Na tsane shi, na tsani halayansa, me yasa zan saurari mutumen da bashi da aiki sai aikata zina? Watau du matan da yake zuwarma ya auna masu ciki ko? Ba abinda zan saurara da mai hali irin nasa, gashi daga jiya zuwa yau ji nake kamar kiris ya rage na babale na mutu ba"

Juyawa ta yi da niyar tafia da sauri ya damko hannunta ya juyota da karfi gabansa hakan ya sa Oga zarro ido ya shiga nufo su da gagawa yana fadin" Mun shiga uku za'a maimaita a anguwa a samu na gorantawa y'ata na ci uban mutun, ke , ke Yar oga dan ubanki ba ya biyo ki ba, meye kuma kin yafe a wuce wajen mu je na bashi duniya da kiyama a daura ku tafi ni bana son bidi'ar komai, shima dama mamansa a kwonce kawai a daura mu je ciki mu je ba sai ya rungumeki a nan ba, shin kina ga yan leke ta katanga kuwa ?"

Damatsunnnan hannayenta ya rike gaba daya ya jijigata da dan karfi yana kallonta muryarsa a rikice ya ce" Kirani da dan iska, ki kireni da komai kike so, ban ki ba na aikata, kuma na yi dana sani!, Aman ba zan iya da nauyin DUTSE irin na soyaya ba, lalle soyaya itace DUTSE, bata jin rarashi, bata jin ban baki, bata jin kunya bata da kawaici sai ta halakani zata huta? Munarah I LOVE YOU.....I LOVE YOU MUNARAH"

Lebunnansa take kallo, furucinsa na sauka a cikin kirjinta
A hankali ta shiga neman numfashinta aman yana neman gagararta,
Gaba dayanta ta ringa son kwatar ganninta dan ta karra kallon fuskarsa da jin kanshin turarensa a hancinta
Lokaci daya jikinta ya saki dubanta ya rufe komai nata ya tsaya cak ya kasance ta yo gaba ta fada a jikin kirjin HANJA, watau sun aikata abinda Oga yake gudu rungume a tsakiyar titin garin malan bahaushe
Sumewa ta yi
Muneerath ta sume

Yar oga ta tafi□□

Yaya kuka gani??????
I'm sorry wani sa'in gaskiya na kudin kan daukan hankalina □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

Domin samun naki ki tumtubeni ta number wayana kamar haka +22793811618 a kan farashi mai sauki in sha Allah
11/14/21, 12:54 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 □□□ 5 □□□
TALLAH.....TALLAH.....TALLAH

Duk wacce batayi anfani da sabulunnan ba anbarta abaya acan karshen bayama kuwa duk Mai tantama akan sabulai nagyaranjiki cewa basa Aiki toh yacire mg's domin kankat ne insha Allah babu Wanda yayi anfani dasabulunmu yace baiyi ba koyaushe mg's sai sanbarka amare da uwargidaye hardama yanmata kuhanzarta kusamu naku ba karya domin bama cika Baki kugwada kubada labari da bakunanku sabulu daya tamkar dubu wadandama basasan using cream sabulun mg's herbal whitening black soap yawadacemuku jikinku zaiyi kyau koyaushe kukasance clean cikin kamshi Kuna glowing koda bakusa turare ba □□

Kayanmu bana bleaching bn organic ne sunagyarajiki fiye da tsammaninku zaifiddomuku da ainihin natural beauty dinkine Wanda yagwada shi zaitabbar amare kuyi kokari kumallaki mg's domin baruwanku da zuwa adirjemuku jiki zakuga yanda fatarku zata dinga walwali
Ina masu pimples
Tabo(spot)
Sunburn dama dukwani matsalar fata kuyi kokari kunemi soap dinnan before 2weeks zaisharemuku hawaye kuzama abun kwatance
Sister's masu nankarwa kuma kunemi soap dinnan Yana rage nankarwa sosai □□□□□□ □□□ uk me shakku tayi kokari tagwada mg's insha Allah bazakiso rabuwa dashi ba

Akwai maisa haske Amma kayanmu nafada bana bleaching bn zaifiddomiki d ainihin halittarkine yagoge dukkan dattin jiki

Akwai Kuma Wanda zaimiki maintaining skin dinki yasaki fresh fatanki tazama kalar hutu
Sannan munada beauty kit □□ duk me bukatan (flawless skin/perfect glow) toh yy kokari yamallaki set dinnan wn zncn baa mgn □□□□□□□□□ uz duk inda kayi se ankalleka □□
Buh gsky wnd besan yy haske karyayi using set din cuz gsky yn sa haske buh bn bleaching ne b zaidai murje fatane nd bring out that hidden beauty in you □□

Pls bamacika Baki you HV to try it and see for yourself
100%tested nd trusted
Beauty kit:11k

Soap price:3k
Location:kaduna buh munaturawa ko Ina Amma delivery is not free

Maiso kindly message 08062991549
Call 08064532391

Note:Babu inda zakusami mg's herbal whitening black soap sai a number dinnan bairiga yakai market b inyakai we will let you know buh as for now wnn numbern ne kawai □□

Maiso yahanzarta before yaji sold out akwaisu available now insunkare you HV to wait akawo so maiso yahanzarta □□ adade anayi sai gsky □□□□

Mg's skincare

Ba EDDITING

Da wani irin wawan karfi ya rukunkumeta a jikinsa yana rintse idannuwansa

Hanneye biyu Oga ya dora a kai yana zuwa maimakun ya tsaya ya kula su sai ya zarce ya karasa kusa da baban dogarin nan ya ce" Salihu hala sarki ya daura masu auren ne ?"

Shashakai Salihun ya kale shi ya kasa magana ya sake maida kansa kasa dan sam bai san yarinyar yar gidab abokinsa oga bace, abokin shashancinsa kennan

Oga ya ce" Kai wai ba da kai nake ba? Muneerath ce fa yar gidan nana ka ga ya rungumeta a gaban al'uma Idan sarki ya daura ne wage muryar nan taka ka shela uban kowa ya sani ka fa san bana so a taba mutuncin yaringar nan haka kawai Allah ya saka min kaunarta a raina "

Salihu kasa kasa ya ce" Ka yiwa Allah Oga daina min magana baka ga wai umarnin sarki muke bi kawunnanmu a kasa ba, ka ja su ku shige ciki ta yaya sarki zai daurawa y'arka aure baka sani ba sai kace garin maguzawa, hala kwacen yar za'a maka?"

Oga ya ce" Na sani ne, ni kam dan Allah mu je gidan sarkin na fada masa idan da hali a daura auren nan, na rantse maka da Allah muna kwonce a wani irin gado mai laushin balaki yar oga ta saka aka daukomu a jirgi daga mu sai ranmu tana rusa kuka kamar an ce da ita Oga ya mutun nan aka kawo mu kasar nan aka zube kamar yan iska, ahine yanzu ya biyota dan bakin hali ta ki ta yafe masa ka ga ya rukunkumeta a jikinsa a gaban su Ladi? Kana hangen wata inuwar ciyayi ta jikin garun cen? Kan ladi mai kanwa ne fa komai a kunnayenta kuma a idannuwanta, kar ya cutar min y'a ya tafi ya barta na rasa mai aurenta ka ga Nana ta dawo hayacinta komai na iya faruwa, ni kuma idan Nana ta barni ai ra kare min Salihu"

Muryar Hanja da ya bude da karfintan nan kamar zai fasa wajen yana mai fadin Attahir ya matso da mota ta suma ne ya saka su kallonsa
Da turanci yake magana, a cikinsu babu wanda ya san takamaiman me ya fada sun dai ga kamar kuka yake rusawa ga shegiya yar Oga a kirjinsa luf har zuwa lokacin

Kai ya girgiza ya ce" Allah mai iko, da ace wata yar gagarumin malami ce ni nan zan ce asiri ne, ka ga y'arka ce kuma ake haukanta haka, kuka ne fa yake ko?"

Oga ya ce" Allah wadaran naka ya lalace Salihu da ka ga kukan da yar ogan ke yi itama sai ka yi mamaki, na zata yar nan ba zara yi hankali ba sai gashi ta yi shi tsaf abinta, ka ga mu je wajen sarkin in dai za'a barni na ganshi kawai walahi ni dai yau a yita ta kare gaskiya na gaji da iskancin yar oga da saurayinta"

Salihu dake kallon yadda ya talabeta ya shigar da ita motar sannan ya yiwa Saudat maganar da ta sakata juyawa da sauri ta nufi wajen mama dan ita har ga Allah bata san ina Oga ya nufa ba ya ce da Oga" ai ko ni nan kai tsaye yau na yi magana da sarki bale kai, kai fa inaga daga yau ka zama aminin sarki ni kuma amininka matsayi ya karru, kai idan kana so har ba sai an maka sarautar ba, Sarkin ingila ne fa, mu je kawai mu je na raka ka"

Ai kam ratsewa suka yi ta baya, suka fice a kafarsu dan kam Oga ya kai makura mafita yake so gaskiya

Saudat na zuwa bakinta na rawa ta fadawa mama abinda yake faruwa

Kafin mama ta yi magama kishiyarta ta dira ta ce" Suma? Suma ko munafurci, yanzu dama Muneerath aikin da take yi kennan?"

Mama ta rintse idannuwanta cike da tsoro, da firgicin lamarin ga kuma baki irin na yan uba ya fara shiga ciki

Saudat ta hade hannayenta a sanyaye ta ce" Mama, Muneerath na bukatarki, mama Muneerath innocent ce, bata san komai ba mama, dan Allah ki je wajen y'arki ki kula da ita sunna jira"

Mama ta sauke ajiyar zuciya muryarta a sanyaye ta ce" Saudatu ai ba motar tasu zan shiga ba ko?, Su yi gaba bara na dauko cenjina mu shiga sahu kin ga yayanku baya nan bale ya kaini a tawa motar"

Murmushi Saudat ta yi ta juya da sauri ta karaso daidai lokacin da Attahir ke kallonta ya ce da Hanja" Sir kar ka yi mata baki da bakin nan dan bata iska, ka yi hakuri mu a nan ba'a haka , ka bari ga Saudat din nan ta dawo mu karasa asibiti akoy a nan kusa in sha Allah"

Da mamaki ya dakata da niyar bata iska ta bakinta dan ya dawo da ita daga duniyar sumar da ta tafi yana kallonsa, mamaki yake na irin tsaurin al'adunsu, a halin na rashin lafiarma sunna da wani zabi da yannayin al'adunsu? Yana mamakin idan ana tunanin wai jikin Muneerath yake so, zai yi matukar mamakin idan aka yi tunanin jikinta yake so

Abinda Saudat ta fada ya saka shi rufe motar Attahir ya ja su suka nufi asibitin da ta fi kusa da gidan su Muneerath din, inda duka masu biye da su suka kuma kwasar ragamar taronsu suka bi bayansu

Yayar Muneerath ce ta fara kwala ihu tana zarro idannuwanta ta ce" Shiri ne ko? Wannan abin wasa ne ko? Wayo na shiga uku wacece ake so din? Da gasken dan sarkin ingilar ne? Yanzu du ya wuce mu ya sauka a kan Muneerath ? Walahi ba zai yiwu ba, ai in kyan ne mun fita, in kirar ne mun fita, shikenan sai oga ya sakata makaranta mu ya kyalemu yanzu kuma ace ta yi miji mai kudi jinnin sarauta? Bazai yiwu ba walahi!"

Nan fa wani tashin hankalin ya kaure, domin wa'inda suke adawa da abin sun kasa boye adawarsu, haka kuma wa'inda suke farin ciki da abin sun fitar da farin cikinsu karara sun nuna a gaban kowa

Mama kam ta buga, ta kuma buga wayar Oga tana ringin aman baya dagawa dan ta sanar masa cewa summa ne fa Muneerath ta yi kuma gasu zasu bisu asibiti, aman sam wayar oga na ringin ya ki ya daga, a kan dole ta fice da hijab dinta domin dama tunda ta dawo hayacinta suka dora yarjajeniyar in dai fita ta kama dole shi walahi ya yafe ta je kawai, shi har wata kunya yake ji idan tana tambayarsa wai zata fita, kai mace mai tarbiya duniya ce

_____

Kawunnansu a kasa suke su dukansu biyun, tunda Oga ya yi magana ya kare Sarki ke kallonsa da mamaki da kuma al'ajabin abin
To wai ahi abinda yake tambayar kansa a ina suka hadu da junna yarinyar tasa da Sarkin Ingila? Lalle matar mutun du inda take sai Allah ya hada su ta hanyarsa mafi sauki a wajensa

To shi yanzun bai san ta inda zai fara ba gaskiya, daga zuwa ya nemi masalaha da yarinyar sai kuma ubanta ya fito da maganar nan?, Sai dai ya zama wajibi ya saurari korafin talakansa bale a gaskiya a wajenmu ba yi ake yi ba, ya ce a gabansa sau biyu ana rukunkume masa y'a, za'a bincika idan komai bai ahiga tsakaninsu ba a san yadda za'a yi gaskiya

Wayarsa ya bada umarnin a miko masa
Sai da ya fara duba kudin dake ciki domin kira Niger to Ingila ba abu ne na wasa ba koda hello ne kadai zaka ce bale doguwar hira ce gaskiya, kuma baya so su yita ta mesage ko ta whatsup

Gamsuwa ya yi da cajin kudin wayarsa kafin yake tura sako kamar haka" Asalamu alaikum, bukatar tataunawa da sarki a kan mahinmiyar maganar da ta shafi mai Girma Hs excelency HANJA"

Bayan ya gama ya ajiye wayar yana karra kallon yadda Oga ke kiririta da kafafuwansa yana dan kale kale, wai a haka an mugun yi masa gargadin ya nutsu fa idan ya samu kansa a gaban sarki, sai ya samu kansa da tunanin to yaya kuma tarbiyar yarinyar?

A nutse ya budi bakinsa , a gadarance da izar sarauta ya furta" Ko itace ta tafi aikin Hostess tare da Gimbiya KHADIJA?"

Ba wani irin a sada kan nan Oga ya saki murmushi yana kada kai ya ce" Ita da kanta, ai yarinyar tunda ta dauko kalar fatana na san ba karamar mutun bace"

Salihu ya yi saurin mintsininsa yana hararansa kasa kasa tare da tunanin Anya Oga ba zai saka su samu ladan bulala maimakun karin girma ba kuwa? Waye ya ce masa ana amsawa kai tsaye ba tare da an baka damar amsawar ba?

Kai sarki ya cire daga dubansa ya maida kan wayarsa da ta dauki ringin
Gannin kira ne daga masarautar ya saka shi yi masu alamun kan kowa ya yi shiru baya son hayaniya komai kankantarta

A nutse ya daga kiran ya gabatar da kansa sannan ya yi masu confirmen eh shine ya nemi da a hada shi da sarki kan maganar da ta shafi HANJA

Kamar da minti biyar wayar dakin Pah na ringin kafin ya daga a nutse ya yi salama yana rufe al'kur'anin da yake karantawa

Gaisawa suka yi sosai a mutunce kafin sarki ya ce" Dangane da ziyarar da Mai Girma Hanja ya kawo ne "
Sai kuma ya yi shiru yana tunanin me zai dora a kai

Pah a tausashe ya ce" Akoy wata damuwa ne ko yarinyar ta ki ta aminta da soyayarsa ne?"

Da mamaki Sarki ya ce" Dama ba soyayar suke yi ba?, Eh toh damuwar ba wata mai girma bace gaskiya sai dai ta fuskar da za'a fuskanceta ne, mahaifin yarinyar ne ya zo da maganar cewa yana bukatar a daura auren nan kawai ya juya da matarsa domin shi baya son .....baya son wasu dabi'u na rashin kunya a idannuwansa da suke nunawa su yaren a gabansa"

Da mamaki PAH ya ce" A daura aure kuma?, Wani irin aure ne haka kai tsaye ba shiri ba komai?, To ita yarinyar ta yarda tana sonsa ne zata iya rayuwa da shi ne? Dan a maganata da shi dai yana min korafin a kan me na hada tafiyar da mutanen da take so da kuma saurayinta, bayan na yi haka ne dan na kara isar masa da wani sakon cewa idan ya yi sake , saken zai gani, aman menene abin rashin kunyar da suka yin ne?"

Sai da Sarki ya dan yi gyaran murya kafin ya furta" Ya ce an rungumeta a cen cikin asibiti, sannan yanzun da kanta yarinyar ta fada kirjinsa ta rungume shi a gaban mutanen anguwa, ka san mu a nan bama haka Allah ya ja da kwana"

Murmushi ne ya subucewa Pah, ya ce" Dama sai da na fada masa naku al'adun sun bambanci namu, ya kiyaye, sai dai maganar ta fada jikinsa ta rungume shi shin da gaske ne?"

Sarki ya kallo wajen Oga ya ga shi kawai yake kallo yana murmushi da alama shima ya iya turancin ya ce" Eh haka kam ya fada, kuma haka abokinsa ya fada, yama ce tunda ta zo bata sha ko ruwa ba tana kukan ko yana kula wasu matan? Inaga soyaya suke yi ko nace ta yarda da soyayar tasa ne"

Wani murmushin Pah ya yi sannan ya dan yi shiru yana ta analysng din situation din
A nutse ya ce" Auren my PRINCE na so ace kaf kasashen duniya babu wanda bai halarta ba, na so a daura auren my hero a kasar saudiya, na so ace aurensa yana gefena mun saka fararan jalabiya mun dora hirami mu yo sujadah ana daurawa na bashi kujerarsa na sauka na rungume yar matata mu ci gaba da istgfari da neman gamawa da duniya lafia, Allah ya kara maka lafia Na so ace NANA KHADIJA na gefena ranar daurin auren yaronta dan na ga irin murmushin da zata yi idan ta ji yaronta ya zama mijin wata, watau shima mai gidan wata, zai bata farin cikinta da take ta mararin budar ido ta gani shine jika daga tsatson yaronta....." Shiru ya yi yana lumshe idannuwansa yana adiye damuwarsa hakan ya sa Sarki muryarsa a sanyaye ya ce" Allah ya karawa Gimbiya lafia, ya sa zakar jiki ne"

Pah kasa kasa ya amsa adu'ar kafin ya ja numfashi ya ce" kana gannin idan aka daura auren nan haka kai tsaye ba tare da an mata gayar da ta dace da komai ba an yiwa yarinyar adalci kuwa? Ka san fa mata yadda suke shirya aurensu da komai da komai"

Sarki cike da yarda da maganar da zai fada , dan shima fa gaskiya yana so a yi auren nan, taf a kasarsa Hanja ya fitar da mace? Ai abin murna ne dan haka ya ce" Ka san mu a nan iyaye na iya yankewa y'ayansu hukunci kai tsaye kuma su yi biyaya (uhum anya kuwa sarki ya san su waye Ogas familly?), Idan ya yanke aka yi ba zata taba tada kai ta nuna dan mi ba, gashi ya ce baya so a yi a kofar gidansa dan kar yan anguwa su ringa zaginta cewa yawon banza ta je abokin yin ya biyota ya aureta, ya fi so ya koma masu da maganar ai mijinta ta runguma , ka san lamarin wajen namu kennan, sannan a ganina kaima a yanzun ba zaka so a yi wani hayaniyar da duniya zata dauka duba da mamansa a asibiti, bama zaka samu nutsuwar yin hakan ba, shi din kansa ba zai samu ba"

Pah ya gyada kansa yana fahimtar maganar sarki domin shi yana cakuduwa da sarakan kasashe daban daban yana fahimta cewar kowace kasa da irin nasu al'adun, hakan ya sa sam bai ji wani abu dangane da lamarin da Oga ya gabatar ba, sannan adini bai hanna ba bale ace adini ya hanna a daura aure dan ba'a shirya bidi'a ba, dan haka ya ce" a fara shirin dukan abinda ya dace, a yi jiran saukar jirgin karfe biyar in sha Allah, za'a daura"

Daga haka suka yi salama Pah ya yi shiru ya shiga tunanin wa ya dace ya tura wakiltar daurin auren gudan jinninsa? Waye ya dace ya tura? Kanninsa kuma dan uwansa daya ya rage masa shi kuma ya bayana kansa a matsayin wanda yake adawa da au baki daya saboda kujerar sarautar, idan har ya tura shi lalle ya tura Hanja a bakin kura da kansa kennan?

Mikewa ya yi gannin lokaci na dan tafia dan ya lalubo ya ga wa ya dace ya tura kiran asibiti ya same shi da gagawa

□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
11/14/21, 12:54 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

Ba EDDITING

Da gagawa ya fito ya shiga mota aka kai shi

A lokacin da ya shiga docter ce ta tarbo shi tana farin ciki ta masa jagora ba tare da ta ce da shi komai ba

A lokacin da suka shiga suka tsaya a gaban gadon Mah tana kwonce ne, sai dai ba irin kwoncin da yake tardota kulun ba

A hankali ya ce" me yake saka ki farin ciki Docter?"

Likitar ta ce" Ta motsa kafarta da hannunta, ta buda idannuwanta harma mun cire mata abin bugun zuciyar "

Da wanin irin farin ciki ya karasa kusa da gadon a hankali ya duka ya dora hannunsa a saman nata ya jimke ba da karfi ba
Muryarsa a sanyaye yake fadin" Ki farka kin ji? Ki farka ki tarbi sarakuwarki da kanki, zan je a daura auren yaronki, ina so idan ya zo da matarsa rungume a jikinsa kema na rungume ki mu kwonta tare mu yi barci cikin nutsuwa, na so ma tura wani daurin aurensa, sai gashi Allah ya nuna min koda bana nan idan Allah ya yi zaki tashi zaki tashin ne, plz ki yi kokari kin ji? Ki kara kokari a kan wanda kike yi, ki tashi na fa hasken farin idannuwanki khalb"

Doctern waje ta fita cike da shaukinsu a zuciyarta, haka kuma zuciyarta cike da farin cikin kotsawar Mah

Pah bai kama hanya ba sai da ya tabatar tsaro ya wadaci wajen Mah haka kuma kula ta wadaceta, sannan ya umarta cewar bayan awa biyu da tafiyarsa a bada sanarwar za'a daura auren HANJA da matarsa Muneerath a africa kasar niger a yau, sannan a yada a social media

Tunda sakon Oga ya samu mama take zaune a tsakar gida bayan dawowarsu daga asibiti ta yi shiru tana kallon ikon Allah da kuma jiran gannin ikon Allah

Kasa kasa ya yi maganar cewa za'a daura auren Muneerath, bai bata damar fahimtarsa ba ya katse kiran, ga kuma Muneerath din da suka dawo daga asibiti da ita a falo a kwonce idannuwanta rufe ba irin yadda Saudat bata yi ba kan ta yi magana ta ki ta yi karshema sai ta shiga alamu na barci take yi bayan idannuwanta biyu,
Haka Hanja har cikin falon ya kaita a hannunsa a rungume ya shinfideta kafin yake tafia gida sarki bisa kira da ya samu wanda ya tafi da gagawa inda ahalin gidan da na anguwar suka samu damar sintiri sunna son gane me ake ciki ne wai?
Iyalan gidan kam sun yi fadan, sun yi masifar, sun yi yafe yaden maganar sun dawo yar zurru sunna kallon kallo kowa da abinda yake cikin cikinsa kuma yake son a bashi amsa aman maman Muneerath ta masu kunnen uwar shegu ta ba mahaukata ajiyarsu, hakama yayanta da ya zo gefe suka koma da mamanta ta masa bayanin abinda yake faruwa ya samu kansa da mata kallon anya kuwa tana da tabacin abinda take fada? Dan haka sai kawai ya garzaya ya nufi gidan sarkin duda ya san abu ne mai wahala a barshi ya shiga

Sai dai tun daga nesa ya ringa fara harda da maganar gannin irin taron al'umar da suka cike wajen , domin Sarki kamar jira yake ya yi gangami na mamaki, ya tara al'uma ta mamaki, ya cika wajen da abin mamaki inda aka baza tsaro aka shiga yanke yanke kamar cen dama an shiryawa wannan daurin aure, jama'a kuwa suka ce gasunnan ta ko'ina ba ji ba gani inda cen ciki kuma Sarki ya gama yiwa HANJA bayanin komai a nutse wanda abin ya nemi buga zuciyarsa dan a ba zata ya zo masa

Du irin kuncin da zuciyarsa ke ciki da ihun da Muneerath ta masa cewar zuwa ya yi ya kasheta? Zuwa ya yi ya yi wasa da zuciyarta? Me ta masa? Me ta tsare masa? Zuwa ya yi ya wulakantata dan ya ga ita ba kowa bace? Zuwa ya yi itama ya ga karshen tata rayuwar shine ya bilo mata da maganar soyaya? Ya daina taba ta, ya taimaketa ya daina kallonta, bata tunanin zata iya yarda cewar wai shi HANJA dan wane jikan wane zai diro kasarta da yake kyankyami, da ita kanta da yake yiwa kallon mahaukaciya ya ce wai yana sonta, du yan matan nan na kasarsu? Du yan matan nan na duniya? Babu inda zai saka kafa ya nemi mace a hanna masa , shine zai so har Oga?, Shin bai san Iman na sonsa bane? Dalilin son da fake masa ta tsaneta kamar ta kasheta har take fada mata yana taraya da wasu mata? Yanzu shi da baya jin tsoron Allah yake so su jona da ita ko me? Dan Allah ya rufa mata asiri ya barta ta iya da rayuwarta , kar ya hargitsa mata tunani, walahi ya fi karfinta.....
Sosai magangannunta suka rikita shi, har ya ji mamakin wai shi HANJA iman ke so? Lalle ya wulakanta kansa har ta kai yadda Iman ke tunanin ta kai macen da zai iya raba lokacinsa da ita? Lalle zina zubar da mutunci ce, yanzu yarinyar da yake yiwa kallon kanwa dan ta san ya kasance mai raba abin cikin wandonsa har ta kwadaitawa ranta? Shi ya tabata yarinyar nan karyata ne zai yi biyu ya zubawa tgr ta cinye kashin dake tare da fatarta sakamakon fadawa Muneerath sirinsa da ta yi kai tsaye

Ko daukotan nan da ya yi da farko wutsil wutsil ta fara kan ya sauke , da ya rungumeta kam a kunnenta ya rada mata cewa idan bata nutsu ba yana iya ladaftar da ita walahi
Shine fa ta yi luf a kirjinsa dan tana tsoron ya kuma furta mata kalmar so ya kara summar da ita, ita kam ta shiga uku ta lalace ta ga rayuwa gannin idannuwanta

Matsanancin farin ciki, da matsananciyar damuwa ne suka dirar masa harma ya kasa daukan tufafin da aka gabatar masa da rawani da sarkin sawanin da zai nada masa duda irin zumudin da yake kan ta ganshi da rawani yaya zasu kwashe? Tsoron rashin amsarta wa soyayarsa ya saka shi a gaba ainun harma ya fi damuwa da hakan fiye da komai

Shi dai ya san daurin auren nan daga Allah ne, damuwarsa yaya zai iya da rigimarta ne? Aman idan ya tuna ana daura aure ta zama tashi fa, shikenan bashi da wata damuwa ta kar a kwace masa ita, sai ya samu kwarin gwuiwa, a haka har Pah ya samu karasowa tare da dakarunsa shima inda duniya ta dauka ana ta neman hanyar da za'a yi magana da su abin ya gagara domin ba halin daga waya

Irin gaisuwar da suka saba suka yi da junna, a hankali Pah ya dan bubuga bayansa ya furta" Wani irin farin ciki kake ciki?"

Iskar bakinsa ya furzar ya furta" Da na fada mata ina sonta summa ta yi"..

Ido Pah ya zarro yana kallonsa , sai kuma ya yi dan murmushi a nutse ya ce" A haka za'a daura aurenka da shigar da ka zo da ita?"

Ajiyar zuciya ya sauke ya ce" Baka fahimta bane? Inaga fa bata so na"

Pah ya yi dan murmushi ya ce" To sai ka koya mata sonka, ka san dai ba zan taso na baro matata kwonce na zo dan halartar wannan daurin auren ba kuma na koma ba'a daura ba dan kawai yarona ya kasa tankwasa zuciyar matarsa?, Fushi take da kai dan kana kula wasu matan , tuni a nan kana da maki mai girman gaske, kaine zaka tankwasata ta gane cewar sai da kai fa zata kai labari....."

Kwarin gwuiwa ne ya same shi da nutsuwar zuciya, hakan ya sa ya sauke ajiyar zuciya ya bi bayan mahaifinsa yana karra wayar kansa da al'adun namu kasar, watau kasata mai albarka

Gari da yar ciki ce farare kal, basu sha wani muhun aiki ba so simple sai dai mai tsari

Bayan ya saka an gyara masa hannayen aka zo aka nada masa nadin Rawanin da aka bata lokaci ana yi har sai da ya gama gajiya da tsayar da kai waje daya inda Pah ke gefensa cike da kauna da shauki hakama mutanen da suke da damar hakan sunna gefensu, Attahir na daukan vidion dukan abinda ke faruwa har aka gama sannan ya mike tsaye

Sarki ne da kansa ya fara furta" MASHA ALLAH, ALLAH YA JA DA RAN SARKI HANJA MUHAMAD, ALLAH YA TAIMAKI SARKI YA KARE"

ai kam du suka shiga maimaitawa hakan ya saka Pah kuma sakin wani murmushin cike da shauki ya bada damar a karaso da akwatin dake hannaun baban mai bada tsaro wa Palas ya duka har kasa ya bude ya dago abin sama

Da ido HANJA ke kallon Pah, yana son nuna masa kar ya masa haka

Pah ya tsare shi da idannuwansa shima a nutse sannan a sanyaye ya ce" Da bakinka ka furta cewar zaka hau kujerarka idan na tashi sauka ko?"

HANJA ya rintse idannuwansa yana jin wani irin yam yam yam tun daga tsinin kafarsa har zuwa kansa, a hankali ya furta" Ya Allah ", a kasan zuciyarsa kuwa ta cika da fargabar wannan ranar harma ya fara tunanin ko dai ranar karshensa yake ganni haka da aka hado masa dukan fargabarsa a lokaci daya?

Pah ya karra fuskantarsa a sanyaye ya ce" Ka bani amsa "

HANJA ya kalli camerar da aka bude wace ya tabata a yanzu kowani lungu da sako na kasarsa ana haska su ne, kuma tabas ko a dokar daji yana da damar amsar sarautar nan, domin ba siyasa bace bale ace sai an yi zabe, kuma ba yau ba yan kasarsa ke korafin ya hau kan kujera ya ja kasarsu , shine ya tirje kan gaskiya sarauta ba tasa bace, shi ya fi son rayuwa irin ta inci, ya fita lokacin da ya ga dama, ya dawo lokacin da ya ga dama, ya yi barci awannin da ya ga dama ya kwonta da macen da ya ga dama
Sai gashi lokaci daya komai na son tsaya masa?

Jikin sarki har rawa yake na wannan baban al'amari dake faruwa a masarautarsa a baban dakin taronsa
Ai kam masarautarsa ta kuma kafa tarihi an nada sarkin ingila a cikinta, sannan za'a daura auren sarkin a cikinta? Kai abin alfahari ne

"HANJA, ka san talakawanka na kallonka, kuma sunna jira su ga shin zaka jagorance su ko zaka ki jagorantarsu? Ka sani idan baka hau ba dole zan maida sarauta

hannun Johnny domin na ajiye sarautar kasata a yau, dan na kai gajiya, shekaruna sun ja zan rungumi matata ne mu huta"

Idannuwansa da suka yi mugun ja ya sauke a kan fuskar PAH,
Ya maida sarauta hannun mutanen da suke da burin korar musulunci a kasar?, Ya maida sarautar hannun mutanen da basu tanadar mata kyakyawan abu ba? Baban budget din Johny shine fara gina gidan giyar da du wanda baya saka albashinsa ciki zai fuskanci mumunan hukunci a gidan horon masarautar, eh lalle ya yarda Pah ya gaji ta yadda gajiyar ta kai shi a yanzu baya tunanin sakamakon dake iya haifar masa

Idannuwansa ya lumshe a kasan zuciyarsa ya furta" TAWAKALTU ALLALAH"
YAna gama fada ya kai gwuiwoyinsa kasa sannan ya dukar da kansa

Kabara aka kwasa, musulmai kennan, inda masu kiran abinsu na coci suma suka fada da dukan karfinsu, wa'inda basu da adini kuwa suka gyada kai cike da ihun murnar ya amsa

PAH hawaye na fito masa ya dauki kourone din ta zinari ya dora saman kan Hanja bayan ya yi masa adu'a sannan ya kama hannayensa ya mikar da shi tsaye ya kuma amshi sandar zinarin da aka miko mai kauri daidai misali da kan Zaki jikinta mai kyan gaske sai walwali take kamar ta dauki ido ya kamo hannunsa na dama ya saka masa kafin ya nemi zubewa a gabansa dan hakan kowa zai yi a gabansa
Da wani irin hanzari Hanja ya tare shi yana jimke hannayensa a kausashe ya furta" Kar ka kafa wani laifin Abui"

Pah ya saki murmushi ga kuma hawaye a fuskarsa shabe shabe ya juya yana fadin" Allah ya ja da kwanakin sarkin kasata"

Wata irin busa aka saki tare da doka wata uwar ganga da suka zo da ita ta karfe wace ta bada wani kuka mai karfin gaske dukan wanda yake dan kasarsu ya gane me hakan yake nufi tun dag gida africa gar zuwa kasarsu kowa da yake haifafen kasar ya san me hakan yake nufi dan haka dy suka zubar da gwuiwarsu daya kasa dayar kuwa a tankwashe kusan a tatare sunna masu sada kawunnansu da maimaita abinda Pah ya fada

Hanja dake kallon live din da ake haskowa na kasarsa ya samu kansa da lumshe idannuwansa lokaci daya yana jin dukan lamura na sarauta na hawa kansa na ratsa jinnin jikinsa da bargonsa harma shi HANJA iza ta sarauta ta shige shi lokaci daya furucin bakinsa suka yi masa nauyi a nutse ya iya daga hannunsa na hagu kawai ya yi nuni da sunna iya tashi , wanda hakan ya tabatar masu ya amsa ya kuma hau

Ai kam daga nan shagali ya kaure a kasashe
Da yawan sarakuna suka fara aniyar zuwa kasata dan taya murna sannan su halarci daurin auren HANJA MUHAMAD tare da gannin wannan amarya mai kashin arzikin da ta janyowa kasartama arziki ba gidansu kadai ba □□
11/14/21, 12:54 PM - Allah Akbar: □□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□
DUTSE
□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□□

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

□□□□ *TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)*□□
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)□□

□□ *[T.M.N.A]* □□ □□□□□□

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 □□□ 7 □□□

Ba EDDITING

Kafin kiran sallar magariba DUBAN al'uma suka shaida daurin Auren MUNEERATH yar gidan Oga da HANJA MUHAMAD Sarkin kasar ingila, bisa sadaki mai albarka da kyautar uwa da uba mai gigita tunanin bawa

Ana daurin aure a waje ne a cen cikin gida Gimbiya da jakadiya da yan rakiya sun gama shirin zuwa dauko amarya a kawota masarautar kafin a daga da ita, domin a yanzu HANJA ya fi karfin ya kuma zuwa da kansa ko dan nauyin da ya hau kansa da irin bakin dake tare da shi

Ana gama daurin Aure Oga ya fashe da kuka yana talabe haba cike da tsoron Allahn da ya darsun masa ya shiga kallon Salihu ya ce" Salihu gaskiya ne dare daya Allah kan yi bature, yau gani ni Oga nine sirikin sarki? Yarinyar nan da ta tashi da maganar sarauta munai mata gani gani ashe itace sarautar gaba daya? Ka ga yau Salihu ni ogo nine ka kawowa kujera na zauna bayan a da gware muke da kai? Kai jama'a wayo duniya"

Salihu ya ce" Oga ai daukakar kennan, Allah ya baka kai dai ka gode kawai, yaya maganar boyewar yanzun mu je da makadan su shaida mijinta ta runguma dazu?"

Oga ya harare shi ya ce" Ai talaka yake gudun a fadi ba Muneerath ba, dan uban mai cewa ta rungumi kato ya gwada mana ya ga ikon Allah, makadan nan ce masu su shiga gaban motocin nan da aka ce a ciki za'a maida ni gida ni oga su kada min Kun gani Kun gani a kwalelen ku, oga ne wannan, kun gani kun gani a kwalelen ku, yar oga ce wannan!"

Salihu kam jirgi daya ya kawo su dan haka ya juya hankali kwonce yana baza babar riga da rawaninsa ya tafi dan isar da sakon abokinsa washagale wale dinsa

_____

Tartsatsin ihun da ta saka a lokacin da gidansu ya dauki shiru domin duk masu hayaniyar nan har matar oga fitar da su aka yi waje kwata kwata cewar kar su dami sarauniya Muneerath, daga mama sai matar yayanta da ta saka aka shigo mata da ita sun saka redio gaba sai zarar ido suke, ga saudat gefe rike da waya ta buda data ta saka duka amon wayar ta zauna a kusa da Muneerath din ta ajiye tana fasarawa su Mama da suka cika da matsanancin mamakin abubuwan dake faruwa , inda Muneerath ta yi likimo tana saurare domin ba fa haukacewa ta yi ba, ba kuma a shok take ba, tana dai tsoron buda ido a mata caaaaa ne ya sakat yin likimo din nan dan ta kula idan ta nuna a hayacinta take sai mama ta fara wanka mata marin yarda kato ya rungumota ya shigo da ita daki a gaban al'uma ba kunya ba tsoron Allah, ita kanta takan rasa me yake damunta da zarar ta yarda ya tabata an kare yanzu zata yi mukus da baki
Sunna sauraron ne har aka kawo inda aka kwashi maganar shaidar daurin aurenta da shi, wannan ya sakata fadowa daga kan kujerar ta saka masu ihun da ya saka Saudat sakin wayar hannunta ta mike a zabure, hakama mama ta saki redion ta fadi kasa itama ta mike tana toshe kunnayenta sunna kallon ikon Allah inda Muneerath sai da ta karasa wajen kafet sannan ta fadi kasa ta shiga shure Shure da birgima a kasa tana ihun ta mutu ta lalace ta ce" bana so, walahi bana so, kasheni zai yi, zaki ne da shi, sai son rike min hannu da rungumeni, walahi ba zan iya zuwa wani garin zaman aure ba, aikina fa? Iyayena fa? Walahi Oga da baya sona? Du cikin y'ayan nan ya rasa wa zai yiwa auren dole sai ni? Innalilahi wa inna ilaihi raj'une na shiga ukuna , tsoronsa nake, tsoronsu nake yo su dukansu, kuma Iman fa da take sonsa dan ubanta? Wayo na mutu ni Muneerath kennan na cuci Freind ko? Na ci amanarsa?"

Mama ta nufi wajen waya tana fadin" Aa bari dai ki shiga uku yanzu ina zuwa"

Da sauri matar yayanta ta ce" Kar mu yi haka da ke Nana, kina gani fa a halin da take ciki fa, dan Allah kar ki dauko abin dukan nan, yanzu fa Muneerath ta fi karfin ko ihu ne bare duka"

Mama ta zarro idannuwanta tana fadin" A kan wani dalili ta girmi duka? Dukanta zan yi na zaune yar banza na huta da sangarta da lalaci da iya shege, to kar ki so shin mana kema ubanki ba aureni ya yi bana sonsa ba? Gwarama shi ai , Muneerath ba sarkin ingila ba ko ke suka nada sarkin kece a gabana ni kuma uwarki, walahi ki mike a burgimar nan ko na fasa maki jiki yanzun nan !"

Kanta ta dan dago dan gannin an dai rike maman ko? Dan walahi bata son duka a rayuwarta sai in ta kama dole, aure ne dan tace bata so sai a daketa? In ba mamanta ba harda gori? Ina ita ina Hanja fisabililahi?

Saudat ta karaso da sauri tana kamata tana fadin" Ba kuka bane mafita MUNEERATH dan Allah ki tashi haka mana, Hanja ne fa, ke da kanki kin san yana son ki, ki duba ki ga irin matan dake bibiyarsa du ya saka kafa ya shure ya tardo ki har anguwar nan ya nemi soyayarki? Muneerath Hanja ne fa da muke barin jiki idan yana waje, dan kawai kina jin haushin abinda ya aikata ne wannan kuma ba ke kika isa ki hukunta shi ba, ya nemi yafiyar ubangijinsa a wuce wajen aman ki daina maganar wai bakya sonsa

Cikin muryar kuka ta ce" Ai damuwar kennan saudat, damuwar kennan, a kasarsu ne ake labewa da bindiga a harbe mutun, a kasarsu ne ake tareka a kashe banza, baka yi laifi bama an kasheka bale ka yi? Na tabata daya daga cikin tsinanun yan matan nasa zata sa bindiga ta kasheni kuma ta kashe banza dan ba yanda oga zai yi da ita!"

Ka zo na zo aka yi da gimbiya da makarabanta da su oga dake baza babar riga yana turo hula gaba

Fitowa ya yi ya yi tsaye a anguwa ya juya ya kuma juyawa ya bada damar a fadi abinda ya faru

Ai kuwa aka fada da babar murya inda dunma wanda bai ji ba ya ji, kafin ya nufi wajen jakadiya dake daria tana jiran ya iso

Yana zuwa ya shaida mata cewar yana zuwa bara ya fara shiga gidan

Ai kam haka ya tardo ana balin nan, dan haka ya ja ya tsaya yana karewa fuskar matarsa da furucinta fahimta, har ya gane cewar koda tana fushi da maganar daurin auren to fa bata kai wajen da zata jigatashi ba, dan haka da kwarin gwuiwa ya je ya nemi da matar yayan maman su Muneerath kan ta kau daga rike mama da take ta barta ta karasa wajen Yar ogan dan Allah

Ai kuwa rana kaucewa MUNEERATH ta dago kai,
Gannin da gaske an saki mama ta mike tsaye zurbat daga borin da take tana zarro ido da gudu ta zagaya bayan oga ta labe tana leken maman dake huci ta ce" Kai kuma a kan me ka daurawa y'ata aure kai tsaye haka? A kan kudi ne ko Oga?"

Oga ya girgiza kai da sauri ya ce" In a kan kudi ne na zama buta nana kowa ya shiga bayi da ji a tsarta min dati!, Gani na yi abin ya yi yawa, ana rungume a gabanmu tsakani da Allah , a gabanmu an yi a cen, an kuma maimaita a nan, a matsayina na uba mai kiyaye darajar y'ayansa na ga gwara na san da fatiha ake haka ko?"

Da sauri Muneerath dake bayansa ta ce" Oga Allah daya ba da wata manufa ba yake yin haka fa, asalima su gaisuwarsu ce haka walahi Oga shine dama tun a cen kake ce min haka na zama dama yar iska ce ni baka sani ba? Walahi ni ba yar iska bace Allah".....ta karashe tana fashewa da kuka tana kara labewa a bayan Oga

Oga ya ce" Yanzu dai ai du gardama ta kare da tonon asiri du ya kare, inma wanene dan iskan cikin ke da shi ba shikenan ba an yi an gama, kin ga motocin gidan sarki ne suka zo daukarta, dan Allah ku rufa min asiri ku shirya ku tafi, ni kam banki zan je na zuba dukiyar cen kar a biyo dare a kashe ni, domin idan muka zauna na fada maki abinda aka kawo dukiyar auren yar nan sai kin ji kamar ki haukace walahi"

Da kyar dai ya iya samu ya lalabasu da shi da su Saudat har akaiwa bakin iso suka shigo

Su da kansu sunna jiran shigowa su tardo wata aljana dan kyau suka yi kicibus da Muneerath, ba wai dan tana da muni bane, no, ya kasance ne idan aka ce ga matar sarki dole ka kala kuma ka yaba

Wanka kawai mama ta tsareta ta yi kafin ta saka abayar da suka zo mata da ita su luluba mata alkyaba mai masifar kyau tana walwali sannan suka aniya yi mata wanka da ruwan turare suka tarkata suka tafi aman banda mamansu domin sam ta ki binsu ta ce gaskiya ita kunya take ji ba ga matar yayarta ba, ta tafi kawai Allah ya kiyaye hanya

Sosai suka rungume junna da Muneerath tana ta faman fadin dan Allah ta nutsu ta bar magana sam sai a gaban idon sani, ta yi hakuri ta karbi tata salon rayuwar a haka zata ci riba

A nan ne Gombiya ta fadi maganar da ta sanyayar da gwuiwar mama ta saka mata madaukakin tsoro domin ta fada mata cewar" Bafa salama bace Hajia, kin san ba'a daura auren sarki bai kwonta shi ba, wannan ne kadai ya sa zamu mikata turaka daga nanma domin ko shirin amarya bamu yi ba tukunnan , har sai ta fito a turaka zamu dawo da ita gabanki da masu gyaranta ki shirya abinki fa kanki ku yi kyakyawar salama sannan a rakata kasar mijinta domin ko shi a yanzu ba zai so zuwa da ita kai tsaye ba tare da ya san me zai tarar a kasar tasa na tarbarsa ba, kin san rayuwarmu mudin ta sarkinmu ce, haka ta sarkinmu mudin tamu ce"

Sosai kwallah ta saukowa mama, tana kallo aka tafi da Muneerath wace ke ta kumbure kumburen an saka mata hannu a riga wai za'a shafa mata humura mai mayotte, ko a me suka dauketa? Ita bata iya shafa turare bane ko me? Kyale su ne take yo su dukansu, so take ta je ta same shi ya bata takarda!

A tsakiyar Gimbiya da Gimbiya mai dakin tsakiya take
Sunna rike da ita sosai har suka iya ratsa dogon coridor din da zai sada su da kofar turakar da aka yi gagagwar zuba dukan abin bukata a lokacin da Pah yake shaida dole su kwana dan ba zasu shiga kasar a yau yau ba, bama sa so a san tafiyarsu domin akoy hatsari mai girman gaske

Hakan ya sa bayan sun dawo daga sallah aka masa rakiya dakin da bai san me zai yi a cikinsa ba

Tunda ya shiga ya ja ya tsaya a gaban katon windows din ya harde hannunsa daya a bayansa ya kurawa wajen ido, har yanzu da rawaninsa a jikinsa da shadarsa domin ko alwallah da ya yi yana gamawa aka maida masa nadinsa, ga wata jaraba da aka bashi a jus Pah da kansa ya bashi wada bai san ita ce ta hargitsa yanayinsa ko kuma dan ya jima bai sadu da abin bane ya saka abinsa ya tashi ya mike masa sambal har yake neman hanna masa sukuni bayan zuciyarsa cike take da tunani, da baban alhinin irin abinda ya tunkaro rayuwarsa ba shiri ba tare da ya shiryawa hakan ba, a yau shine SARKIN kasarsa, sarautar da yake gujewa ta same shi, sannan a yau shine ya yi aure da macen da bata bashi amsar tana sonsa ko akasin hakan ba, haka kuma a yau shine tsaye a kasar da ba tashi ba ya ga duka wadinnan abubuwan ba tare da Mah dinsa a gefensa ba, watau Pah ya samu lagonsa ya daka son ransa babu mai rarashins, baima isa ya nuna yana da bukatar rarashin ba domin ya hau wajen da babu mai rarashinsa sai ko matarsa wace baya tunanin in yana gabanta, ya cika da tunanin shin a ina take? Me take? Yaya ta dauki maganar cewa shine mijinta? Yaya take tunanin rayuwa da shi har karshen rayuwarsu?

Dan bubugawar da aka yi ya saka shi dakatawa da tunaninsa aman kuma bai juyo ba

Daga bugawar nan shiru ne ya biyo baya ba'a kuma yin wani bugawar ba sai kamawa da aka yi aka bude kofar aka shigo

Ido ya rintse cike da mamakin wannan kuma wata irin dabi'a ce ta shigowa ba tare da an baka izinin hakan ba?
Shin shima yana cikin al'adunsu ne ko me?

"Asalamu alaikum" ta fada muryarta na rawa gannin sun juya sun barta sun ce ta shigo nan gashi ta shigo ta ga mutun da rawani kar dai dakin sarki aka kawota ya mata nasiha? Wayo Allah da sai ta maka Selfi da Shi koda a wayarsa ne dan ta tanadar a wajen ajiye hotunnanta na tarihi

A hankali ya juyo yana jin yadda zuciyarsa ta buga sakamakon jin muryarta cike da mamakin anya ita ce kuwa? Waye wannan ya masa wannan gift din mai girma da daraja?

Alkyabar dake jikinta har tana sharar kasa ya fara saukewa dubansa, kafin ya sauke kan dan kululun abin alkyabar dake ta rawa a gaban goshin nata dan ta sada kanta ne ba'a gani

Idannuwansa ya lumshe yanna jin yadda zuciyarsa ke fama da luguden kida , wannan dokawar da zuciyarsa ke yi anya ko dora masa couronne din nan da aka yi ya saka masa haka kuwa?

A hankali ya ringa takowa da takun kasaitar da ya hau kan takun bijimin namiji ya bada kala wajen haska taurarun sarki HANJA har ya karaso kusa da ita kadan kafin ya saka hannunsa na dama wanda baya rike da sandar ya dago habarta a hankali yana kallon kwayar idannuwanta da ta zazaro waje gaba daya a sanyaye ya furta" MY WIFE "

Wani irin abu ya kuma tsirga mata wanda nan take ta ji tamkar fitsari zai kubce mata hakan ya sa ta matse kafarta da kyar , muryarta na rawa cike da mamakin dama suma sarautarsu ana nada rawani tana kallonsa da madaukakin mamaki ta ce" You? "

Hanja ya lumshe idannuwansa yana kallonsa muryarsa cen ciki yana kallon fuskarta ba digon komai na shafar kwaliya ko wani abu, sai sansanyan kamshin da bai san me yasa yake son ya ji shi irin mugun jin nan ba domin sai wani irin sanyayar masa da gabai yake yana ta saka shi rawar zuciya, ya kure lubunnanta da kallo da irin yadda take dan son janye habarta daga hannunsa a sanyaye ya kuma furta" Can i?"

Ifannuwan nan nata masu ruwan na mage , watau masu color da suke karra yin lumlumlum din ni'ima da hasken farin cikinsu ta yiwa luuuuiii kafin a hankali ta budi bakinta da jiyar furta masa tambayar me yake tambayarta idan har zai iya yi? Sai ta samu kanta da hadiye maganar gaba daya a cikin cikinta a lokacin da ta ji wani irin abu mai shegen laushi, bayan shi ba auduga ba, batama san da me zara kwatantashi ba, yana fitar da dadadan kanshi da dumi dumi ya hade da nata leben da ko man lebe bata da shi ya yiwa rikon alewar zaki mai sunna Manta uwa
A hankali ya shiga tsotsar lebunanta idannuwansa lumshe har ya samu ta bude bakin nata dan tsabar kaduwa da zarro ido tana kallon girarakinsa , ya samu damar riko harshenta a bakinsa yana tsotsa hakan ya bata damar kuma zarro ido tana kallonsa kafin ta ji ya janye alkyabar dake jikinta ta fadi kasa gaba daya a hankali ya shiga yin baya baya da ita har ya danganata da jikin kofar da ta rufe, du bai bata damar fahimtar me suke ciki ba ya yar da sandar dake hannunsa ya saka hannun yana tatare diguwar abayarta kafin yake dora lalausan hannun nasa a kan cinyarta a hankali ya shiga shafawa ya shiga kokarin hawa sama da hannun nasa har ya kai wajen lafafen cikinta , nanma ya dan shafa a hankali wanda hakan ya saka Muneerath sadakarwa ta fara son tataro dukan ihun dake cikinta dan kurma masa shi ko zai saketa kar ta masa fitsari a jiki, inda shi kuma gaba dayansa kansa ya tsoshe a hankali ya kara yin sama da hannunsa har ya kai wajen mamanta da ko bra basu bari ta saka ba ya dora a sanyaye a saman maman nata ya shafa, ya kara shafa kafin ya riko dan kan a hankali ya dan mulmula kan wanda hakan ya saka MUNEERATH sakin..... .....

Iskanci ya tabata a gare ki yau dai yar gidan Oga bayan oga yana cen banki yana faman irge

Ku ji su, sun dage sai na kai karshe ko? To ba da ji ba jifan tsohuwa

11/15/21, 12:54 PM - Ummi Tandama :
DUTSE

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)

[T.M.N.A]

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 8

Saura kiris

Mulmulan kan da ya yi dan ya gane me yasa bashi da tsini ya saka Muneerath zarro ido tare da sauke wata munafukar kasalaliyar ajiyar zuciya ta yi raf da hannun nasa dake cikin rigar, ya ja , ta ja tana tana ta son ta ankarar da shi ya fa saketa me yake mata haka ne, dan Allah ya barta kar ya ilatata, kwakwaluwarta da zuciyarta na mata bugawar da take jin zuciyar tata zata kuma kokarin balowa ta fito daga kirjinta

Rigar tata ya kama da hannayensa biyu stil ya danne kirjinta da nasa dan kar ta kwace lebenta da yake yiwa tsotsan diban albarka,
ya shiga daga rigar har sai da ya mata shamata ta arziki kafin ya cire bakinsa da sauri ya zare rigar gaba dayanta sannan ya zuba mata narkakun idannuwansa a jikinta

Daga ita har shi ido suka zarro,, lokaci daya ta kurma ihu ta duke tana rufe mamanta da basu da wata girma sosai dan kiwa Muneerath a wajen da ta fi auki duwawu ne dima dima, maman basu da wani girman a zo a gani , a yan kwanakin da ta yi tare da Mah nema suka kara kumbura, aman duda haka sun fi na berayen jajayen mutanen da ya saba mu'amalanta, hakan ya saka shi zuba mata ido daga tsayen da yake yana kallon budaden duwawunta masu tudu da fadi da ta yi tsugunnon nan sai suka sake bajewa suka bada kala mai fuzga da pant din ciki mai ruwan fari kal wanda bashi da ko diz na alamun dati a tare da shi

Idannuwansa ya lumshe yana sauke boyayiyar ajiyar zuciya yana ta dadane lebensa kansa a gefe guda, kafin ya kuma juyowa ya zuba mata ido

Ajiyar zuciya ya kuma saukewa da sauri sauri ya warware nadin rawanin nasa ya jefar sannan ya cire babar rigar
Yana cirewa asirin wandonsa ya bayana, ba wai tsayuwar bane ya bayana , no, tudun ne ya bayana wanda wandon cikin irin mai rikewar nan ne sosai shi ya taimaka ya boye yannayinsa

A hankali ya duka yana iya yinsa dan kar ya nuna mata zalamarsa , shi walahi gaba daya yanzun ya fara tunanin anya ba Pah ne da wannan aikin ba? Burinsa idan ya amsa kiran sarki haka ya kasance cikaken magidanci, anya ba shine ya idasa nufinsa a saukake ba?

Hannayensa masu laushin gaske ya dora wajen kafadunta muryarsa a tausashe ya ce" Me kike boyewa haka Munarah?"

A tsorace ta dago ta sauke dubanta a kansa
Gaba dayansa yau ya mata wani irin girma fiye da da, bata taba ganninsa a irin wannan yannayin ba, tamkar ba Hanja dan gidan Mah ba
Abinda ya mata na tsotsar mata baki da kama mata mama kuma ya sakata a hali na matsananciyar kunya da tsoro da takaici, shi kam haka yake ne? Ba zai cenza ba hali ba dai ko, yanzun haka yake yiwa kowace mace?

Rigarta take laluba hakan ya sa ya lalubo ya dora mata a saman kafadarta sannan ya kuma zuba mata ido yana jin lamarinsa na sake hauhawa
Ya rasa gane me yasa yake jin koda a kallonta haka ya tsaya ya ji dadi a cikin zuciyarsa, bai san kallonace abu ne mai dadi sai a kan yarinyar nan, ya zama kamar wani gaula tana yi yana binta da kallo bale yanzu da take tube a haka?

A hankali ta ce" ka dan matsa na suturta jikina kunyarka nake ji HANJA wai meye haka? Ko tunani kake nima irinka ce? Ba bari mu yi maganar auren nan da aka ce an wani daura min, shikenan daga shigowata sai ka fara wannan abin da ni? Ni ce fa?"

Murmushi ya yi yadda du ta ki dago kanta tana masifa, maganar aurensu? Da wa da shi zata yi gardar aurensu? Lalle zai dauketa ya nuna mata bambancin soyayar jar fata mai jan kunne da wasu mazan kasarsu, lalle sai ya sakata ihun da bata taba yi ba a rayuwarta, lalle sai shayar da ita zumar da bata taba sha ba, haka kuma sai ya cire mata du wani namiji a ranta, sai kuma kunyar naj dake bashi mamaki, kunya? To ta mecece ita Kunyar kuma? Ta me? Dan ta zauna haka a gabansa? Tana nufin bata taba zama haka gaban kowa ba? Abun mamakin kuma shine irin yadda kunyar tata ke neman saka shi madaukakin nishadi da shaukinta

A hankali ya mike yana saka hannayensa ya dauketa gaba dayanta, hakan ya sa da sauri ta kifu tana kara rufe kirjinta a kasan zuciyarta kuwa fadi take' Yau na ga ikon Allah, yau na ga tashin hankali, anya mutumen nan yana da hankali kuwa?'

Saman lalausan bed din da ya dauki ni'imtacihar shinfida ya shinfideta, da sauri ta zabura ta yi zaune ta zubo kafafuwanta kasa still hannayenta rufe da kirjinta gaba daya jikinta na rawa ta ce" Marata ta rike, ka barni na je na yi fitsari ka ji?"

Idannuwansa ya lumshe daga karantarta da yake a hankali ya duka gabanta gaba dayansa murya shake yana dora hannayensa saman sambala sambalan cinyoyinta ya dan matsa ya ce" Bari na shanye mana "

Ido ta zarro ba shiri ta ce" Me din ?"

Sai da ya kalli wajen ya nuna da jajayen lebunnansa masu laushi kafin ya ce" Fitsarin "

A rikice da kuma karfi ta kawo hannunta a birkicen tunani ra zungure gaban goshinsa ta manta ta saki mamanta guda dan kidimewa ta ce" Astagfrullah, A'uzubilahi minna shaidannin rajim, kai kuma yau ko giya ka sha ne dan Allah? Ya rasulullahi, ya Allah abinda ke damun kwakwaluwar bawan nan naka kka masa maganinta tun kafin ya kasheni da haukan dake damunsa ba wanda ya san yana fama da shi bale a masa magani ya Allah, Allah in ba hauka ba waye zai sha fitsari, kai subahannalah wayo duniya"

Tana fada ne tana matse cinyoyinta, ita fa gani take gaba daya tamkar wani maye ne shi din ba'a sani ba, irin kallon nan da yake mata ga idannuwansa sun cenza kala sun nuna kusa yake da fara cinye mutane ai sai a hankali
Bata ankara ba ya dan dago kadan ya saka maman nan nata a bakinsa wanda zuwa yanzun kan ya fara curewa waje daya ya fara nuna alamun koda kuwa bata da ra'ayi shi yana da shi, a hankali ya fara tsotsa, sai dai bata bashi damar kasheta da ranta ba ta yi saurin janyewa tana dan yin baya da karra zarro idannuwanta gaba daya waje

Gannin fa idan ya ci gaba da son karantar Muneerath shine a cikin damuwa ya saka shi saka hannunsa daga tsugunan nan da yake ya wara kafafuwanta , wanda hakan ya sakata mantawa da abinda take rufewar ta damki hannayensa tana ihun fadin" Meye haka kuma wai? Daga ka taba nan sai ka taba cen kai sai halaya irin na wa'inda suka sha giya ? Lah ha ila ha ilalah Muhammadu rasulullahi sallalahu alaihi wa salam, kai meye haka wai? Kai ina ba da ni ba ka bari kar ka ciren wandona mamma da Oga su kashe ni"

Sam kin gane me take fada ya yi har sai da ya cire din ta dawo yanda bata son kasancewar
Numfashinta ne ya kusan daukewa a lokacin da ta ga tashin hankalin da bata taba zato ba, watau ya tura hannayenta baya a irin zaunen nan da take ya kawo tsaftatun lebunnansa da ya gama kazantar tsotsar baki da mamanta wannan karron ya kafa mata a wajen da bata taba sannin cewa wai ba baki ba idoma zai masa kallon yan dakiku dan kunyarsa da take ji ita da kanta, yau sai gata a gaban nasara, ya soma da yi mata abinda shima bai taba yiwa wata macen ba, ya dauki dukan makamansa na son halaka yar mutane ya kuwa fara kawo mata farmaki ba ji ba gani.....to yaya lafiyar kura ne balatana ta yi hauka?, Na biyama ya samu isashen lokacinsa bale na halak?.....

Sai da ta yi ihu kafin ta shide, da karfi ta janyo numfashi tana zarro ido tana kuma lumshewa kafin ta shiga kikifta ido domin du yadda ta so fuskantar abin, fahimtar abin, sai ya zo mata a bai bai, bai idasa halakata ba sai da ta samu kanta daa son karin wannan lamari , wai ita Muneerath yar gidan oga mai jin fitsari ce ta saki jiki ta wani karkata kai tana zarar ido kan dole da dole sai ta fahimci daga ina abin nan mai son sakata hauka ke taso mata? Kamar ba itace da farko tana turewa ba, sai gashi a yanzun ta samu kanta da kwontawa ta karra nutsuwa tana sauraron lamarin da ta kasa gane menene shi har sai da ta samu wani irin abu da ya taho mata ya sakata vibration kamar zata yi hauka hakan ya sa ta jimke shi, ta rike shi da kyar ta iya furta" Ka daina walahi mutuwa zan yi"
Shi da kansa irin yadda ta samu juisance a bayane sai da gaba daya jikinsa ya kara hautsinawa ya hau saman da baya zato

 ta rike shi ta kuma rike shi ta saki kukan da ya ratsa ko'ina na sasan jikinsa tana vibration da dukan jikinta har ya taso ya hayo gaba dayansa bayan ya cire abinda ya basu katanga ya yar , jikinsa har rawa yake ya yi mata rumfa yana kallon lebenta mai ruwan kasa kasa dake rawa dan tsabar shiga abinda bata saba ba, da kyar ya iya furta" Zaki yarda na fara aikata na alkairi, halatace, mai lada da ke? Kema daga yau da ni kadai zakina aikatawa ko, tunda dai ai mu musulmai ne, musulmi kuwa baya irin haka da zarar ya yi aure? MUNEERATH na kagu ki bani amsa, ki gyada min kai ko ki lumshen ido kin ji?"

Da ido take bin sajensa da fuskarsa da kallo, jikinta ya mutu murus hakama dukan wani tunaninta ya tsaya cak, me kuma zai yi yake tambayarta?, Kai kwakwaluwarta sai ta ringa son sannin me kuma zai mata irin mai dadin nan?, Ita fa a yi, kawai a yi, Allah ya ba kowama hakuri ashe haka abin yake take zagin masu yi? Kai jama'a □□

A hankali, a kuma rashin sani ta dan gyada masa kai tana shakar kanshin da suka garwaye nata da nasa suka bada wani irin dadadan kanshi
Sai da ya sauke ajiyar zuciya kafin ya lumshe idannuwansa ya kai lebensa wajen goshinta ya mana mata sansayen kiss sannan ya gangaro da bakinsa kusa da kunnenta a hankali kasa kasa sosai ya karanta adu'ar saduwa da iyali wace mahaifinsa ne da kansa ya fada masa cewa a yanzu idan har zai cewa iyalinsa ya kula, ya ringa karantar adu'ar nan a koda yaushe,
Jikinsa har yake yana tunanin me zai ji idan ya yi ba condom?
A hankali ya kara saka lebensa cikin kunnenta a sanyaye yana dan kara son dauke hankalinta haka kuma ya kai hannunsa wajen nan cike da mamaki yana karra jin yanda wajen ke da mugun santsi har abin na biyo yatsarsa sannan ga wani irin dumi ba sanyi karara ba irin yada ya saba ji a jikin wasun du da gumi irin na condom aman baya wani jin dumin da ya ji a harshensa a jikin MUNARAH
A hankali ya raba tsakiyarta ya samu ya gyara kafafuwanta da kyau da suke walwalin nutsatsiyar fatarta ya kara zubawa fuskarta ido yadda take dan murmushi da alamu ta fara kaunar lamarin

Ajiyar zuciya ya sauke da sauri kafin ya kuma yi mata rumfa ya fara neman hanyarsa

Tsai ta yi kafin ta bude idannuwan da take lumshewa ta sauke a kansa
A hankali ta ce" Hatara dai menene a wajen?"

Idannuwansa a rintse suke yana ta bada kokari hakan ya sa ta zile tana karra zarro ido ta ce" Kai na yanzu zafi walahi, a barshi kawai"

Wa ya ga a barshi, me din za'a barin? Ai kam ta ga aikin bari domin ko bakinta bata gama rufewa ba ya wawurota ya dawo da ita ya mata riko irin na an rike ka taf din nan ba zaka iya kwatar kanka ba sai na Allah ya kuwa kuma daidaita da karfi karfi

dabara dabara tun yana tunanin matsewa ne irin na wasu matan har ya gane cewa hanyar ce ba'a taba bi ba, hakan ya sa ya wani irin riketa a jikinsa ya barta bakinta bude a sake abinta tana zunduma ihu ta rike shi da dukan karfinta tana neman agajin ya saketa zafi alura mutuwa Wayo oga na mutu na lalace
Bata san mutuwa da lalacewa a gaba ba har sai da ya idasa shiga ya dan saurara a jikinta yana sauke ajiyar zuciya itama haka kafin ya shiga hakar rijiyarsa da dukan kuzarin da yake da shi da kwarewa a lamarin wanda ya tatara yakushi, ihu, kuka da magiyarta ya zuba a kwondon shara yake ta aikata aikinsa cikin nutsuwa da wata irin gigitar da bai taba tsintar kansa a ciki ba, dumi, santsi, rikewa suka hadu suka saka kwakwaluwarsa son auna wacece matar tasa,

"Ya salam." Shi ne abinda ya fad'a a k'asan zuciyarsa kawai, lallai kayan kampani daban suke da na shago, kamar yanda halak ta bambamta da haram, tabbas ya ji banbancin k'arara kuma a zahirance.

Irin nutsuwar da yake ji sai ta sha bambam da wacce yake samu a lokacin da yake tare da wasu matan, dan ya rantse da mahaliccinsa da za'a tambayeshi wani ya gansa a wannan yanayin da wata maccen da ba ta aurensa, zai ji kunya ya kuma nemi kar hakan ta faru, amma a yanzun sai yake jin wani shauk'i na daban da baya jin shakkar koma wanene ko wacece su ganshi a halin nan.

Iya nutsuwar zuci kawai da yake ji a yanzu ya ishe shi kwanciyar hankali, uwa uba kuma irin tsantsar gamsuwa da yake ji tana kwaranyo masa daga dukkan gabb'ansa, bai tab'a tarayya da wata mace ba har ya ji yana numfashi mai kama da kuka, amma a yanzu sai yake jin ihu yake so yayi da k'arfin da Allah ya hore masa, dan ko baya son haka ya lura iya sautin dake fitowa daga k'asan mak'oshinsa kawai mai kama da gurnani neman fallasashi yake.

A hanzarce ya sake gyara zaman kwanciyar da yayi a kanta ya k'ara d'an wara k'afafunta, kallon fuskarta yake yi yana kula hak'arta daga k'asa, inda d'aya hannunshi ke kan mamanta lokaci lokaci kuma ya kan d'an tsotsi d'ayan.

Sosai ya rik'e wuta ake ta abu d'aya a kan ta, wannan tsiwar da bakin rigimarta duk sai suka mutu, gata dai shi kan shi yana son sarara mata, amma kuma abun ya ci tura, rin dank'on dake jawoshi da wani santsi had'e da wani irin d'umi mai zautar da tunani kamar a zamanin mugun sanyi, sai ga shi ya ja lokaci mai tsayi har saida shi kan shi ya tabbatar lallai fa ta aikatu.

Sanda ya ji ruwan jikinshi na kan hanyar zuwa ne y shiga k'ara k'wak'umeta yana jijjiga, gumi ne ya shiga kwafanyo masa kamar yayi tsere na tsawon kilomitoci, zungurarta ya dinga yi da k'arfin daya fi na dazu yana tsiyaye mata ruwan jikinshi wanda k'arfin bala'in hakan har uasa shi kwantar da kanshi a k'irjinta yana ambaton sunan Allah.

Saida ya ji komai ya lafa ne ya sake gyara zamansa a jikinta yayi shiru, ba zato ba tammani wasu zafafen hawaye suka kwaeonyo daga kurmin idonshi zuwa kan mamanta da kan shi ke sama.

Shin wace irin baiwa ce Allah ya masa? Wane irin gata ne haka ubangiji ya masa a matsayinsa na mai zunubi?

Kunyar ubangijinsa bai taba masa yawa irin na yau ba,
Shin me ya yi ya samu wannan ribar ta rayuwa?
Ya kasance mazinaci sai ya samu tsarkakakiya?

Maganar Pah ne ta fado masa inda yake fadin "Hanja ita fa zina bashi ce, idan ka yiwa y'ar wata za'a yiwa taka, idan ka bi matar wata za'a bi taka , ka kiyaye" a da yana iya cewa yakam ji kamar ya ce da Pah idan ta je ta bi maza ai jikinta ne matsalarta ce, aman a yau sai ya ji wani irin tsoron a yiwa wannan haka

Wannan da ya gama tand'a ya haye ya sauka, sai yake jin idan wani ya kuma kallonta yana iya mutuwa, idan kuma bai mutu ba tabbas babu abinda zai hana ya zama tamkar mayunwacin zaki wajen kai farmaki ga duk wanda yayi k'ok'arin kallon masa gonarsa, dan zai zama mafad'acin da sai Pah yayi dana sanin bashi mulkin nan a yanzu

Kasancewar ya kusan kwana yana abu daya sai kuma ya sake zuba mata ido yana bege har sai da asuba ta sanyo kai kafin a hankali ya raba jikinsa da nata wanda ya dauki dumi sosai fiye da yadda ya saba jinsa

Cike da tausayawa a gareta ya tsaftace jikinsa sannan ya zauna ya shiga yabar gizo dan samo abubuwan da suka dace ya talafa mata da su kafin docter ya ganta

Ai kam ya samu din, dan haka ya zagine ya hada ruwan mai dumi sosai ya dawo wajen da ta dunkule waje daya tana fitar da wahalale Numfashi hadi da gajiyayiyar ajiyar zuciya ya kamata a hankali yana aukin bata hakuri ya dauketa cidak ya nufi bayin da ita

Cikin ruwan nan ya sakata ya tsuguna yana rike da itaa , a hankali yana shafar bayanta tare da bata hakuri

Muneerath ta gama yanke cewar a yau ba zata ga safe ba
Gaba daya duniyar ta bata mamaki da tsoro
Ashe haka maza suke?
Ashe haka ake abin nan?
Wannan shine zuwan da Saudat ta kwatanta mata
Wannan shine hakkun namijin da aka ce idan kika hannawa namiji hakinsa kina cikin tsinuwar ubangiji?
To ai ita daga wannan da aka yi ba kari
Ina ita ina karra wannan azabar?
Ya je ya kula duma wace yake son kulawar, ya yi kam ta yafe masa ba zata iya ba sam sam sam , ta kuma gane ya fita iya wulakanci ta sadakar ta yada makamanta

Yana gasata ne yana karra kaleta
Yakan mana mata kisss a goshinta , zuwa karan hancinta, harma ya sauko wajen lebenta
Yakan dan shafa shafafen cikinta aman yana kiyaye taba mamanta da matsawa kasanta kallo, domin har a yanzu zuciyarsa ba sauka ta yi daga kanta ba, hakama dukan wani lamari dake tare da shi idan da zai samu to da ya kara komai kankantar Karin kuwa

Sai da ya gamsu sannan ya cirota ya nemi da ta yi wankan tsarki

Zuwa lokacin tana jin dadi dadin jikinta, harma tana iya Motsawa da kanta

Duka yana jiranta a waje har ta gama ta fito ya taimaka mata ya zura mata doguwar rigarta sannan ya rungumeta a jikinsa a sanyaye ya furta" I love you MUNARAH"

A kasan zuciyarta fadi take' Na bi love u din da gudu ba sket, na ce na bi shi da gudu ba kamfai!, Aman wannan love u din akoy macuci marar kunya marar tausayi, ni yanzu ai ba zaka cuceni ba da maganar love u walahi, in dai gane hanya!'

HANJA ya mana mata kis a lebenta yana murmushi ya rufa mata alkyabarta a hankali ya ce" nan ne fa yake ciwo ba bakin ba, rabonki da magana tunda kika hadani da Mah, bakya tunanin ya dace ki budi bakinki yanzu anmatana?"

Harare ta watsa masa tana kara kumbura bakin nata hakan ya kara saka shi daria ya juya ya tayar da sallah

A dakin suka yo sallarsu suka gama, ya zaunar da ita saman kujera ya rage sanyin AC ya karasa ya tsaya gaban bed din yana tunanin ta inda zai fara gyaransa,

Juyowa ya yi ya sauke dubansa a kanta, nan sukai ido hudu da junna sai dai bata jima ba ta cire nata tana kumbura fuska

Karantarta yake kafin ya ce" Sai nake gannin kamar fushi kike yi da ni"

Allah yana ganni a tsorace take da shi, Allah yana ganni bata taba tunanin cewa akoy sanda a jikinsa ba sai jiya da ya wahalar da ita da ita, aman fa ba shi yake nufin Hanka ya shige mata hanci da dukunkune ba, ina
Dawo da dubanta ta yi tana kallonsa ta ce" Fushi? Fushima kake tambayana Hanja? Aman wuta nake da kai, walahi ban san kai din nan maketaci ne ba sai jiya, me na maka ni?"

A hankali ya ce" Toh fa"
Ta ce" Eh to fan!"
D
Murmushi ya yi ya ce" Ikon Allah"

Ta murguda baki ta ce" Kadanma ka gani, walahi kadan ka gani, ka dai bari mu hadu gani da oga ga kai zaka gane waye babana!, Kuma ka gyara shinfidar nan da kanka dan ba abinda zan maka ni kam ah tooooo".....ta karashe tana matsar kwallah, hakan ya saka shi juyi ya shiga yaye shinfidar yana farin ciki a zuciyarsa a bayane kuma ya ce" Thts my MUNARAH"

"Sunana Muneerath!" Ta fada tana karra daure fuska cike da tunanin lalle Saudat ta ci amanarta da bata rakota dakin nan ba, ina auntynsu ne da aka ce su zo tare su kwana tare? Matan nan farare kuma na sarki tabas sai ta harare su daya bayan daya kafin ta bi babanta

Ya dai yo wani abu ya kamata a nutse tana cika tana batsewa ya shinfidar da ita tare da rufa mata lalausan bargo yana kara murmushi da karra furta mata kalaman soyayar da ya zamanto furuci ga bakin nasara in dai yana so to fa zai ringa fada ne ba dare ba rana □□

Cen cikin barcinsu ya ringa jin vibration na wayarsa
Da kyar ya iya lalubota ya Daga ya karra a kunnensa yana shafa gashin kanta dake baje a saman kirjinsa

A hankali ya budi bakinsa ya ce" Pah, wani irin za'a koma da ita? A kan wani dalili fa?"

Pah ya ce" Ai haka suke yi, zasu je da ita a mata gyaran jiki daga baya za'a kawota mu kuma mi shiga shirye shiryen tafia

Kansa ya girgiza tamkar Pah din na gabansa a hankali ya ce" Ai kafata kafarta ni kam"

Ido Pah ya zarro ya ce"

Kifufu saura kiris

11/18/21, 2:36 PM - Allah Akbar:
DUTSE

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)

[T.M.N.A]

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

6 9

Kasa kasa ya ce" Kana ji Hanja, kar mu yi haka da kai, tun jiya na basu amanar eh ana iya komawa da ita, yaya zaka ce ba za'a maida masu yarinyarsu su shiryata kamar yadda suka saba ba, akoy gyaran amare da suke inaga sunna shirya yarensu ne dan zama da namiji, to me yasa zaka ce ba inda zata tafi?"

Hanja ya dan yi tsai shima kasa kasan ya ce" Wai Pah kana nufin banda haka har wani shiri suke karama matan?"

Pah ya dan yi murmushi kadan ya ce" Please son yanzu fa ka girma ka wuce a ringa rigima da gardama da kai, sun maka adalci da suka kawo maka ita a jiya, so plz ka shiryata zasu zo daukanta ne in ji mijin su"

Dan murmushi ya yi yana girgiza kansa a hankali ya ce" Pah u see, bata yi barci ko dis ba duka daren nan, nd ba sabawa ta yi ba, bana tunanin zan iya barinta tafia ko ina ne, Pah ka ga sarautar nan da ka dora min a jiya ko? Na dauka ban ce komai ba idan ka takura a kan maganar MUNARAH gaskiya zan ce wani abu, ka duba ka gani plz"

Pah ya shiga murza goshinsa yana kallon mai martaba dake sauraro yana murmushi
Katse kiran ya yi bayan ya ce masa yana zuwa
Ai kam yana kashewa Hanja ya shiga whatsup ya shige ccnt din Pah ya masa voice kamar haka" Pah ka duba mana, idan ta tafi kwana nawa zai shiga tsakanina da ita? Ba zata saba da wuri ba wahala ce zata yi ta sha, ni kuma ba zan iya ba"

Pah ya rasa me zai cewa sarki domin dukan abinda Hanja ya fada ya ji domin shima yana jin turancin hakan ya sa kawai ya dan kura masa ido, inda Sarki kuwa yake murmushin kasaita yana dan kada kansa ya juyar da dubansa gefe ya dauki wayarsa yana fadin bara ya kirayi mahaifin yarinyar su ji yaya zasu yi da shi?,

A lokacin OGA ya jima da farkawa sunna tsakar gidansa ana shawara, ko nace yana sanar masu abinda ya yanke wayarsa ta dauki tsuwa

Sai da ya mula kai ya karra irin na sababin masu kudin nan ya ce" Nana karanta min waye ne?"

Maman Muneerath dake zaune tana cikin farin cikin yannayin mijin nata da a yanzu al'amuransa ke sakata nishadi haka kuma yana birgeta a dukan abinda ya yi domin du tsiya baya takata haka kuma baya wulakantata, sannan du abinsa ya iya godiya ya iya yaba mata komai kankantar kyautata masa da zata yi kuwa baya yin kamar bai gani ba ta duba a bayane ta ce" Mai martaba ne Aban Muneerath"

Ya kuwa sakin murmushi ya ce" Daga ki saka shi a amsa kuwa, dan uwana ne, tunda aka daura auren nan na tabata cewa ko ba dade ko ba jima sai na zama magajin kujerarsa, abin ai na Allah ne"

Ita dai dagawar ta yi tana kallon yadda idannuwan kishiyarta suka kumbura suntum dan sakawa rai mugun abu a zuciya ta saka amsa kuwar ta ajiye

A nutse ya yi salama, inda oga ya amsa cike da ladabi ya ringa gaishe da sarki da su tambayar ya iyali ya waye waye har sai da sarkin ya gaji da amsawa kafin ya ce" Dangane da maganar dawo da Gimbiya Muneerath ne"

Sai da gaban Oga ya fadi da karfi ya ce" Ina? Na shiga uku me ta yi za'a dawo da ita tun yanzu? Kar dai ku ce min har ya saketa Innalilahi wa inna ilaihi raj'une"

Sarki ya yi sakayau da wayar a hannunsa yana kallon Pah da bai san me Oga ke fadi ba aman gaba daya hankalinsa a kan wayar so yake ya fahimta sai dai ba hali shi dai kuwar muryar Oga kadai yake ji a kunnensa

A nutse Sarki ya ce" Subahannalah, me ya kawo saki ana abin farin ciki?, Al'adun sarautar garinmu ne idan aka daurawa sarki mace sai ya kwontata sannan a maidata gidan iyayenta a mata gyara da kitso da kunshi, dalilin da ya saka aka daukota a jiyan nan kennan, yanzun maganar dawo da itan ne ake"

Oga ya shiga kifta ido a sanyaye ya ce" walahi gaba daya sai da na ji zan haukace, to yanzu Allah taimaki mai martaba idan aka dawo da yar Oga na mata me?, Dan Allah ka rufan asiri ku gyarata a cen ina al'adun na niger ne ba na ingila ba, ni yanzun haka maganar da nake maka gidan nawa ne na saka a kasuwa ake ta ciniki ana karawa domin ginanan nan na anguwar plateau ne na taya harma na biya kudin so nake kowace na siya mata motar hawa sai su ringa jana muna zuwa anguwa, to abindama ya dan kawo tangarda ita abokiyar zaman nata ne ta ce ina ita ina jan mota tsoro take ji, wai saboda haka ba za'a siyawa uwar Allah ja da ranta ba, ta manta ita ta nakudo abinta ta haifo, to mafanar ce ake yi ana karawa ka san mai kudi ba son hayaniya yake yi ba shine kaina ya fara ciwo, walahi ina son fitowa fadarma abin ya gagara sai nana ta yarda tukunnan, to yanzu mu da muke cikin wannan harlallar kar ku hada mu da Allah ja fa ranta dan Allah na roke ka Mai martaba"

Tunda ya kama zubar sarki yake karra mamaki da lamarin bawan Allahn har ya dasa aya kafin ya samu kansa da yin murmushi yana girgiza kai cike da mangarin rayuwar oga, watau shi bai biyo ta hanyar damuwa ba, idanma ka damun kanka
Gashi dai cikin ruwan sanyi sun samu mafita, sai dai duda haka sai ya ce" To ita mahaifiyar yarinyar ta yarda da hakan ne?"

Oga ya ce" Ai abinda na ce shine Allah kara maka lafia, ama bara mu ji ta bakinta ai tana jinmu a amsa kuwa muke....,"
Ya kuwa karkata ya ce" Nanata wai a kawo maki yar gidan oga gidan nan? Ai gwara su gyarata idan zasu tafi ma je mu ganta kin san yanzu fa ba koda yaushe ake iya bari a ga Allah ja da ranta ba"

Murmushi ta yi ta mike ta yi ciki dan walahi kasheta yake son yi da ranta, wai yanzun Muneerath din ce da yake lukawa ashar idan ta ki masa biyaya a wani abin ya maida Allah ja fa ranta?
Shima yar dariya ya yi yana talabe habarsa da fadin" Mace mai kunya duniya ce, kai jama'a"

Shi dai sarki gannin abin na Oga ba mai karewa bane sai ya masa salama sannan ya fuskanci Pah ya shaida masa ba za'a fitar da ita ba, aman dole su basu dama su mata gyara a nan koda na kwana biyu ne kafin su tafi da ita

A kan Dole Pah ya aminta da hakan shi ya shiga kokarin juyawa ya je ya yi sharar fage a gyara komai kafin Hanja din ya dawo domin ya kula ba fa zai bishi ba, dan haka ya daga masa kafa ya tabata Abinda bai taba samu bane ya samu

Da kyar ya iya ganar da Hanja cewar ya basu dama su gyaratan, saboda haka ya nemi alfarmar Sarki ya basu damar su ringa fita wajen gonakinsa da sauransu dan ya ga garin su matarsa da al'adunsu na yau da kulun a boye ba tare da an san fitarsa ba

Ai kam hakan ce ta faru, kusan karfe goma ya fita tare da su Sir Attahir dan tafia gannin gari da shiga lungu lungu sako sako na garin dan ya ga menene kasar Niger da al'adunsu

Sunna tafia babar matar sarki tare da masu gyara suka dira dakin Muneerath, tare da Saudat da matar uncle dinta
Da saudat aka fara barinta dan zuwa kai zannun gadonta baban daki, SANNAN a zo da dukan abubuwan shirinta , inda ta riki hannun saudat tana hawaye ta ce" Saudat yada kika san zan bar duniya"

Saudat ta ringa bubuga bayanta ta ce" Haba Muneerath ban sanki da ragwonci ba fa, dan Allah ki yi hakuri ba komai kin ji?, Babu abinda zai faru ki yi hakuri kin ji?"

Muneerath ta ce" Dole ki bani hakuri, dole ki bani tunda da saninki cewa dan gidan Mah bashi da wayau kika kyaleni baki fada min zuwarma mutun na daidai da kashe mutun ne"

Da sauri Saudat ta ce" Kar ki bayana sirrin mijinki, kin fa je islamiya kin san ba kyau, ki kiyaye furucinki a kan wannan lamarin, ki rike harshenki, kin ga ban taba yin aure ba , kuma Allah yana ganni ban taba sannin meye abin ba, ni dai a karatuna an fayace mana komai, sannan a makaranta an hanemu da bayana irin haka idan ta same mu da mazajen aurenmu, so dan Allah kar ki ringa fadin haka kin ji?"

Rai bace ta dago da kanta ta ce" To a maida ni gidanmu mana, na tabata Oga ya kasa barci dan bana kusa, ke ai kin san irin son da yake min"

Saudat kam dariya ce ta kubce mata, sai dai bata ce mata ga dalilin dariyarta ba cewar Oga ya hanna a kaita gidan, sai ce mata ta yi" Baki san Oga yana so ki zauna a dakinki ba?, Ai farin cikinsa ne ace kina dakinki kina kula da mijinki, dan Allah kar ki saka damuwa a ranki kin ji? Haba jarumar Mama"

Muneerath ta ringa gyada kai tana tunanin kawai Saudat dan bata ji abinda ta ji bane take mata wannan maganar, aman ba komai zata mata adu'ar itama ta ji idan ya so sai su jajantawa junna, aman ita kam ba ita ba d'a namiji ko a lahira ta yafe!

A lokacin da suka dawo dole Saudat ta koma falo aka bar masu gyara da Muneerath

Ai kam ta ga gyara, ta ji gyara, ta kuma tabata gyara
Dirzar fatarta ake kamar ba gobe
Ruwan dumin da aka sakata kuma ko na mai jego albarka
Tun tana dan jin zafin abinda ta dandana har ya bace bat ta dawo murmushi da jin yannayinta ya koma da sauki sosai
A haka suka zuba hade hadensu na itatuwa na gyara mai karawa amarya dandano a cikin wani sabon ruwan turaren suka bata damar zama a ciki ta kuwa shige ta zauna tana jin wani irin ni'imtacen kanshi na taso mata
Ita fa ba abinda yakr kasheta sai idan zasu cirota tumbur da suke saka alkyaba su kareta ana mata dan kirari, wollah sai ta ji wani irin dadi da daga kai na hawa kanta tana jin wani iri kamar wata sarauniya

A haka aka shigo da kujerar zama ta turare ana fitar da ita daga wannan aka bata damar zama sannan aka luluba mata bargo aka bar fuskarta da gashinta kadai a waje

A nan aka labtawa gashinta hadin lalen hausa wanda aka hada shi da sinadaren gyaran gashi aka kawo leda aka saka a kan ta daure gashi sanann aka kawo hadin gyaran lebe nanma aka shafa mata , aka ringa budewa ana lumda mata mayuka irin na gyaran jikin da suke hadawa da kayan hade hade irin namu na gida ana kara dumama jikinta wanda ita da kanta sai da ta ringa jin wani iri, gashi ana yi ana kawo hadin tsumi da danyen tatsa na nonon rakumi ana didirka mata wanda da farko wani

irin fitsari yelow ta yi kafin ta samu lafiyayen fitsari sannan ta ringa jin wani irin filing hade da tunanin irin tsotsan mangwaron da ya yiwa mamanta , nan da nan ta saki lafiyayiyar mika a ranta ta ayana' inama wancen kadai za yana min banda dayan?, Innalilahi to in ba bakin ciki irin na dan gidan Mah ba me ya hadani da sanda a nan?'

Lokaci suka bata mai tsayin gaske
Sun saba , aikinsu ne, ita din da bata saba ba kuwa sai aka ringa yi ana bata damar hutawa da cika cikinta
A nan an dirka mata su kaza, da jinjirayen tamtabaru, an bata lafiyayen magani haka an bata na feeling wanda ta kasa gane a kan me take so ya dan kara tsotsar abin nan? Sai dai ta tatara komai ta ajiye kan ziga ce irin ta shedan da yake kawata mata abin ya kaita ya barota a bata wahala yana gefe

Ba'a taba gashinta ba sai da suka gama gamsuwa da gyaran pp da kuma na jikinta sannan aka warware aka wanke lalen nan da ruwan dumi, hakan ya sa gashin ya fauki wata color shi ba baki sidik ba shi ba ja mai duhu ba, ya yi wani irin laushi da kyali tun basu kai ga saka shi a na'umar dumama gashi da busar da shi ba, aka saka masa abin nanadewar gashi aka saka shi a na'urar sannan aka shiga kunsa mata kunshin hausa a tafukan kaffafuwanta wanda wannan kuwa da saudat a gefenta sunna labarin aikinsu da manyansu da abokannan aikinsu sunna raha da wasa da daria hakan ya saka ta saki jikinta sosai gyara na ratsata sosai sannan akai mata na zane a hannayenta aka gyara akifunta sosai suma suke ta kyali, dama Muneerath ba baya ba wajen tsafta domin ita din mai tsafta ce sosai

Sai bayan magariba suka gama kimtsata, wannan shiri da akai mata aka saka mata wata sabuwar alkyaba ja mai hasken fararen duwatsu ta dauki turaran wuta aka dora mata farin dan kwali tas a saman ni'imtacen gashin kanta aka fitar da ita ta sha kyau har ta gaji furkarta dauke da simple mak'up an saka mata gashin ido a kan nata an diga mata abin nan mai kara hasken idannuwa sai kwayar cikin ta kara haska launinta

Saudat bakinta ya kasa rufuwa, kallonta kawai take har sai da ta ce" Ke wai hala na maki kama da aljanu ne?"

Saudat ta yi daria tana girgiza kai ta ce" Ba zaki gane bane, Muneerath kalarki kalar gimbiyar ne, ashe ke din kece asalin fasarar gimbiya a bayane, ba zan ce maki komai ba dan ba zaki gane ba, aman zan kara ce da ke Masha Allah, Allah ya kara gyara halitarki a gefen Oga Hanja"

Muneerath ta yi murmushi tana lumshe ido a lokacin da ta hango fuskarsa lokacin da yake tambayar ya yi?, Gaba daya yannayinsa yanayin kosashen zakin da ya fito ya yi kuwa ya saki gashinsa, saima da girar goshinsa suka hade waje daya lebensa ya karra cizawa a hasken pink a lokacin da jaraba ta ciyo shi
Da sauri ta kauda zancen sakamakon tsammmmm din da tsigar jikinta ta kwasa nan da nan ta ji tana son ta kara ganninsa a yannayin cen, har sai da Saudat ta daga wayar mamanta ta mike ta fice tana yiwa Muneerath alama da hannu dan zasu tatauna kan sunna ingila ita suke jira idan ta je suka ganta sai su dawo Niger

Murmushi Muneerath ta yi tana rungume jikinta, sai kuma ta daure fuska tana jin kamar wace take jin haushin tunawa cewar a haka fa ya tsotsi wata irin yadda ya tsotseta ko? Ya salam wannan wani irin abu ne sai ta ji kamar ta bara masu, sai kuma ta ji in dai zai dawo yada badalarsa a kanta ita daya kawai zata yi hakuri ya yi ta yi nata ita dayan

A wannan daren da ya dawo bayan rakiyar Pah da jin dadadan labarin da Pah ya bashi cewar Mah ta motsa har an cire mata abin numfashi ya tardo Muneerath a haka, gaba daya sai ya rasa inda zai tsoma kansa

Ka kazar amarcin da suka siya shi da Attahir cewar ana shigowa mata da shi maimakun flower a kasarmu da jus sai ya samu kansa da sakin ledar yana tunkarota domin dama sun yi salarsu ta isha'i a waje, haka itama sun yi ita da Saudat sai ta samu kanta da tsayawa tana kallonsa har ya karaso sannan ta dan ja baya ya nemi binta hakan ya sa ta ja tunga ta jimke hannunta tana zarro idannuwanta ta ce" Walahi yau ba zaka min kwace ba malan dakata ko na sakar maka naushi"

Murmushi ya saki yana kallon kunshin hannunta da ya haska a kan milk color din fatarta
Suit din rigarsa ya cire ya yar a nan ya ki dakatawan hakan ya sa ta kai masa naushin a saman kirjinsa da dukan karfinta tare da fadin" Tunaninka ba zan daka ba hala....." Sai kuma ta rike hannun nata da karfi ta ce" Wayo Allahna ya karya min hannu, wayo na mutu na lalace"

Hannun nata ya riko a hankali ya zagaye bayansa da su sannan ya kawo lebensa kusa da kunnenta muryarsa cen kasa kasa ya ce" I miss u so much matata, i love u my MUNARAH"

Muneerath ta lumshe idannuwanta a hankali tana kasa kasa da hannun nata har ya karasa wahen duwawunsa bata sani ba ta dan jimka da hannunta cikin wani mahaukacin shaukin goga mata sajensa da yake a wajen kunnenta
Har ga Allah bata taba cen da wata manufa ba sai ga Hanja yana neman fasarata da yar iska ce ita a lokacin da ya nuna alamun ta taba masa duwawu
Ita ina ita ina taba wajen nan fisabililahi kamar wace oga ya cewa jeki kya gani? Shine ya kara damko hannun nata ya maida saman duwawun nasa ya jimka da dan karfi sannan ya kai bakinsa wajen kunnenta a hankali ya furta" Aushhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhh touch me Khalb"
Tabas auren nasara ko kai na dan iska bane zaka iya ko ka aikata a lokacin da baka sani ba
A karro na biyu a dare na biyu dan rashin sannin ciwon kai ita Muneerath ta kuma sakin jiki ya rudeta da kalamansa masu sakata jin anai mata rawa a wajen fitsarinta , domin da kanta ta samu kanta da kangwabe kai ta ja zif din rigar da aka saka mata mai mutunci ta keta da kanta ta bashi damar kama yan bana bakwai din abubuwan dake kirjinta ya ringa saka masu albarka yana karawa

Tun sunna gane yaren junna a tsayen da suke har suka idasa zubewa kasa daga ita har shi din suka haukace inda ya ringa sinsinarta cike da zakuwa yana mamakin kanshin dake fita a dukan wani lungu da sako na jikinta har ya kai ga babar hajar inda a yauma ta ringa yarda da batun da yake gabatar mata har suka zo fannin anfani da sanda ta so ta ce a hakura hakanan , aman sai ya nuna mata komai na iya faruwa, ciki harda rasa rai domin ji yake idan bai yi yana iya mutuwa
Ita dama Allah ya yita mai tausayi, ta cika tausayin wanima bale dan gidan Mah?
Mah fa mamanta ce
Allah ta tuna ba wannan ba ko sama da wannan ya ce yana so ai ita mai hakura ta bashi ce ko dan Mah
Ai kam ta dage, ta tataro dukan jarumtarta ta sakar masa jikinta, inda shima ya yi iya yinsa dan saduwa da wajen cikin aminci da kula har dai ya idasa , nan fa zance ya cenza salo
Sam kasa tuna alkhairin da ta masa ya yi ya ringa hakarta yana kimarta tamkar ya samu rafkeken gida

Tun yana iya rike gurnaninsa har ya bayana ya ringa magiya da maimaita soyayarsa a kanta
Tambayarta yake wai me take mamana masa ne?
Ita kuma kuka take tana fadin ya sasauta mata kar ya kuma farkata shi bai san halaci bane?
Da wannan suka sasaba, suka yayada manufarsu suka aminta da lamarinsu suka kwana cikin farin ciki inda kazar bata samu ciyuwa ba sai da dare ya raba sosai ciki ya fara kiran masu ciroma

.... saura waya daya .... In sha Allah

11/22/21, 5:04 PM - Allah Akbar:
DUTSE

RUBUTAWA: *SAJIDA*

SADAUKARWA: *GA MASOYANA*

LABARINA NA: *10*

TAURARIN MARUBUTAN NIGER (ASSO.)
(Tsintsiya mad'aurinki d'aya)

[T.M.N.A]

https://www.facebook.com/Taurari-marubutan-niger-111773560677003/

Bismillahir-rahamanir-rahim

7 0

ALHAMDULILAH, ALHAMDULILAH, ALHAMDULILAH, ALHAMDULILAH, ALHAMDULILAH

A washe garima wunnin gyara akaiwa Muneerath, a wannan rana kuma mahaifiyarta da kanwarta na gefenta, haka kuma aminiyarta Amina da ta dawo daga bautar kasar da ta tafi ta samu labari ta zo kuma an bata damar shiga, hakan ya sa anai mata gyara bakinta ya ki ya rufu da ita da aminiyarta da kuma Saudat

Murmushi Amina ta yi tana girgiza kai ta ce" Tabas idan ka ji maraya rago, haka kuma lamari na ubangiji babu yadda baya kasancewa, idan Allah ya tsaya maka zaka

hadu da alkhairin rayuwar da baka taba tunanin cewar kai din jan zaka samu kanka a ciki ba"

Muneerath dake zaune cikin rufa ta bargo mai nauyin gaske anai mata hayaki marar yawa yana ratsata ta lumshe idannuwanta ta yi murmushi ta ce" Allah , shi ke gyara tuwon makaho, nakan yi tunanin ko barci nake na ringa mafarki irin wanda na saba?, Sai dai sensation din dake fito da kanta a zahiri kan sakani karra buda idannuwana, Amina HANJA ne mijina....kuma baya minti biyar idan muna tare bai ce min yana so na ba, na rasa ni me zan ce masa ya faranta masa, Allah ya wanke sarkin dogari ya bani"

Amina ta yi yar dariya tana kallon Saudat dake murmushin hirar tasu ta ce" Babu irin abinda ba'a cewa a kanta a kan dogari da son zama HOSTESS, ni kaina mun sha yin baran baran a hanyar makaranta idan ta tsayar da tafiyarmu ta dauko magangannun nan, sai na ga ta yaya? Ta ina?, Muna aji muna daukan darasi ta ce zata je gida kanta na ciwo, daga nan ban kuma ganninta ba, Oga ya ce wai ya samu waya wai ko za'a dauketa aikin masu raba abinci a cikin jirgi ko me?, Tun ina sa ran ta bilo har na zubawa sarautar Allah ido, har na yi tafia harkar bautar kasana a shekarata ta biyu, kin ga MUNEERATH ta cinma burinta a saukake"

" Ke ba a saukake ba kam, da adu'a ba dare ba rana, da naci, da kafiya, Amina na ga abubuwa ciki harda gani ga zaki.....kin san Hanja kiwon zaki yake yi, a ranar na fara dane jikin namiji da kaina " ta fada tana kauda kai

Amina ta girgiza kanta ta kalli saudat ta ce" Halin na nan "

Saudat ta ce" Ba zai kau ba kam har abada"

Dariya sukai su dukansu

A tare suka wuni, sai wajen yama aka ce ga Oga ya zo tafia da mama
Ai kam ta sha mamaki a lokacin da ta fita ta ga wani dan uban shada da Oga ya sha da wani gilas baki da hula harda agogo
Ido ta zuba masa da mamaki ta ce" Oga a ina ka samu kudaden nan na shiga uku"

Oga ta ce" To Allah ja da ranki hala ji kike na sadakin naki ne nake kashewa? To bari ki ji kyautar uwa da ta uba da aka bamu sai mu siye kaf anguwar nan da ita, bale kin ga mijinki da yake cen waje yana hawaye wai ko mamansa ta farka har sun yi vido cull ko me na ji sunna fada, ya tashi ya mike ya zaro takarda ya bani fara, kur'ani juwa da ta dibeni na kusa summa na zata ya karki ne, sai da aka duba min aka ce ai ba wannan bane, kudade ne ya zuba wai na godiyar na bashi y'a, walahi Yar oga sai gani ina so su barni na kai gwuiwoyina kasa na yo godiya sunna rikeni sunna hannani, kai na ci kuka na sha hawaye kamar ba gobe"

Muneerath ta girgiza kanta kawai , inda mamanta ta karra jadada mata abubuwan da ta fada mata a ciki na dangin su nasiha da kula da miji da sauransu, ita kuma ta ringa gyada kanta tana murmushi ta raka su baban filin wajen tanai masu byby abinta kan cewar ai ko gobe ta so ganninsu zata dawo ita da Hostesss ce kulun sunna cikin tafia

Ita dai Amina bata ce mata komai ba, hakama Saudat, suka koma ciki har lokacin da Hanja ya dawo ba a yadda akai zai dawo ba

Da farin ciki mai tsanani yake fada mata cewar Mah , Mah ce ta farka, Mah har sun yi vidio calll, Mah ta rikice da farin cikin jin ya aureta, haka kuma ya amshi sarauta,

gaba daya ya nemi rikice mata da son rukunkumeta a gaban au Saudat salon a yi gaba da ita a ce itama ta fara raba hali ta dauki halayan da ba nata ba watau
Inda suma suke kakawar da kai domin su dai a kasarsu ba'a sakin jiki a yi haka a gaban wani koda kuwa matarka ce
Gannin ya kasa samun kanta ya dauketa cidak ya yi ciki da ita, a guje suka fito sunna zarro ido kafin su bushe da daria Saudat na fadin" Kalarta irinta Allah ya bata abinta "

Amina ta yi murmushi tana girgiza kai ta ce" Tabas Allah na aiki da zuciyar bawa, Allah ya basu zaman lafia ya sa su kasance har a gidan aljanna cikin dankon soyaya da kula da junna"

Dukan wani masoyi ya kasance a cikin yan rakiya, Rungumarsu take tana fada masu cewar zata dawo a gobema idan tafia ta kama su, shi dai yana biye da ita sai ya yi murmushi a ransa yana ayana' haka fa '

A cikin yar tafiyar da suka yi, wada a cikin jirgin da a tunaninta iya su ne sai masu masu hidima , aka kara shirya shi kafin ya bude wata akwati da kansa ya sake ciro wata alkyaba mai ruwan zeba mai kyalkyali sasauka ya rufa mata a kan shigarta ta duguwar rigar lesh mai ruwan duhu da dan haske hasken fari kadan a jiki
Fuskarta ya karra kurewa da kallo yana jin ko a yanzu yana iya maimaita abinda ya yi jiya da dare da ita
Kanshin da take fitarwa na saka masa nutsuwa hakama kalar nutsatsiyar kwaliyar da akiwa fuskarta na saka masa jin nishadi idan yana kallonta

Daurin dan kwalinta ya karra shafawa yana ji a ransa sun masa adalci , sai dai baban burinsa ya saka kafarsa a gidansu ne, zai ce da Mah dan Allah ta saka matarsa a irin suturar da take sakawa, shi kam yana ga wannan shiga ta Mah dinsa itace shigar da ta fi dacewa ga kowace mace, rufe suturar jikinta zai sama masa nutsuwa

A hankali ya mana mata kiss a goshinta sannan ya dan lankwashe hannunsa kusa da cikinsa ya sanyo nata a ciki ya juya ya fara tafia da ita a hankali

Gaba daya idannuwanta ta wara, hakama dukan wani tunaninta ya nemi iyakancewa a lokacin da ta ga duban al'uma a laye a tsare, haka kuma manya manyan dakarun sojoji da bindigunsu wasun shigarsuma ba'a gannin fuskarsu sai iya lebensu da idannuwansu sun zagaye ko'ina sun rufe ko'ina

A hankali ta karra matse masa waje ta dan dago dan kallonsa
Sai dai yannayin fuskarsa sai da ya saka gabanta faduwa
Girma, daraja, ni'ima, duka ta ganni a fuskar mutumen dake dawainiya da yi mata hira ba dare ba rana, mutumen da ya bita har anguwar su oga ya bayana mata sirrin zuciyarsa, gaba daya sai ya so rikide mata ya cenza mata har ya kai daidai wani waje da zasu hau ita bata sani ba har sai da ya dan sasauta rikon da ya mata ya taimaka mata ta ankara cewar wani wajen ne zasu hau

Ajiyar zuciya ta sauke ta hau suka karasa gaban amsa kuwar da aka tanadar da wani farin teburi dan dogo da tissu a ajiye da dan abin goge hannun nan

A gefensa ya yi mata waje, a nan ta sauke dubanta a kan mutanen dake gabansu wa'inda suke tsaitsaye kowa cikin kyakyawar shiga irin tasu, watau mazan da suit, matayen kuwa daga mai dan bingilin sket, sai mai dan wando da riga dai da sauransu , haka kuma du sun saka huluna yawanci da dan flower a jiki mai kyau ba kalar na zuwa sutura ba

Namijin dake tsaye da takardar da akai masa rubutu ne ya mike ya gabatar da barka da zuwa wa sarki da kuma sarauniyar kasarsu, tare da nuna tarin Flowers din barka da zuwa da aka ajiye masu da kara yi masa barka na daurin aurensa, da sheda masa cewar sun tanadar masa biki na musaman idan ya huta tare da iyalinsa
Sannan ya bada damar a haudo surprise dinsu

Ai kam wannan surprisd din da aka tanadar masu baki daya ba komai bane sai Mah da PAH ke turata a saman kujerar tura mararsa lafia, domin ba wai garas ne ta mike kai tsaye ba, sai dai tafoar ce bata iya yi da kanta sai a hankali

Farin ciki, murna duka sun bayana a saman fuskokinsu, a hankali ya duka a gabam kujerar ya kama hannayenta a sanyaye ya ce" Mamanah"

Mah ta hade daria da kuka tana shafa gefen fuskarsa sanann ta riko hannun Muneerath ta hade da nasa ta ce" Jarumina, albarkana "

Su dukansu murmushi suka yi suka rungumeta, itama tana dan taping din bayansu sannan ya furta" Kin ga ya tirsasani ko?"

Pah ya yi yar dariya yana karra kallon mutanen dake gefe da gefe
Mah ta ce" Ya min adalci , ya cikan burina "

Sai da suka gama farin cikinsu sanann ya samu kansa da maida kansa da kansa ya fuskanci al'umar dake sauraron bayanansa

Dan murmushi ya yi ya karra duban wajen su Muneerath ya kafeta da ido kafin ya dan girgiza kansa a sanyaye ya ce" Tabas na ji tsoro mai karfin gaske a yan kwanakin nan da suka wuce da barazanar rasa mata biyu da suka fi soyuwa a zuciyata da duniyata ta tunkaro ni, sai dai gashi yau sunna gabana tare da ni sunna kuma saurarata, Ban san ko na cencenci zama sarkin kasata ba?, Domin ba dan ka zama prince ne zai zamana dole kai ya dace ka mulki kasarka, sai dai abinda ma koya a yan kwanakin nan sune sannin darajar lokaci, anfani da shi, mutunta dan adam, kare hakinsa, yabawa kokarinsa, talafa masa a dukan yinkurinsa, dan Adam yana da daraja ko wanene.....da wannan nake da burin Allaah ya dafa mani mu kasance a sauratar mulkin HANJA"

Tafi aka kwasa hakan ya saka Muneerath kara wangale baki da mamakin shikenan hala?, To kuma shikenan su sun gamsu?, Murmushi ta yi itama ta tafa dan kuwa ta gama yarda jan mutun na yarda da kalaman baki ba tare da an gita masa rantsuwa ba, ba kuma sai an nuna masa alkur'ani ba, haka kawai sai mutun ya ce da kai ya rantse da kan babansa ka yarda

Sosai ya ringa gaisawa da manyan kasar sunna masa barka, sai dai sam bai basu damar su kai kansu wajen matarsa ba, domin a yanzu baya jin in har zai iya hakura yana kallo wani ya rungumar masa hannun mata ko ya nemi hade kirjinsa da nata, sai a yanzu yake gannin lalle Pah yanaa gaskiya, a da sai ya ringa gannin kamar PAH din na wani irin abinda bai dace ba, aman a yanzu sai ya samu kansa dumu dumu da gudun hakan wa iyalinsa

Sun dauki dan lokaci kafin su nufi gida a mota daya gaba dayansu, inda HANJA ke rike da hannun Muneerath yana dan shafawa a hankali haka kuma gefensa na hagu Mah zaune cikin kyakyawar shigarta ta abaya baka sidik mai kyan gaske marar kyalkyali

A hankali Mah ta ce" Son, sai nake gannin kamar kana abu irin na mai kishi bayan kai ka ce ka waye baka san kishi ba"

Da farko yi ya yi kamar bai jita ba, sai kuma ya yi dan murmushi kasa kasa ya ce" A da ban san menene so din ba, haka kuma ban san darajarsa ba, a yanzu kuma bana jin zan iya kawar da ido a kan matata Mah, ina sontaa kuma ina kisshinta sosai"

Ko da suka isa gidan wata tarbar suka samu
Sai dai a yanzu kiri kiri Muneerath ta kalli HANJA a lokacin da ta kula da irin kallon da Iman ke masa ta ji wani irin abu na mata yawo a kai kamar zata hau bori da kakausar murya kasa kasa ta ce" Walahi ba gaisuwar larabawa ba, ko ta su waye kar ka yi da mataan dake wajen nan, ka ga karma ka rike hannayensu HANJA, idan kuwa ka yi in ban je na gaishe da wancen bodyguard din naka ta hanyar rungumeshi ba ni ba yar oga bace, ai gaisuwa ce ka yi na yi kawai"

Dan bakin nata da take maganar tana murmushi chau chau da shi ya kurawa ido kafin ya dago ya kafe sauran matayen dake masa oyoyo sunna jiran lamari na runguma ga kuma abinda mai shi din ta fada
Sai kawai ya hade hannayensa da nata ya yi mata murmushi ya ce" Na zabi kowa kar ya yi, dan bana son farkon fara aikina na ba Tgr naman mutun ta ci, wannan ba adalci bane"

Sai da gabanta ya fadi ta kale shi a zabure ta ce" Tgr, tana ina? Hala da kai take barci? Ni walahi ba zan iya kwonci da ita ba, idan kuma mukaa raba daki ai abin wancen fa da muke yi fa?"

Daria ta kubuce masa har ya so ya kasa hanna kansa kokarin rukunkumeta , sai dai gannin da gaske yake ta tsere gefen Mah ta kama kujerar Mah tana dan turata sukai ciki ta barshi da bakinsa

---

Sarauta yake yi da nasa salon da tsare tsarensa cikin aminci da kwonciyar hankali inda mahaifinsa ke gefensa yana taimaka masa da dukan abubuwan bukata, Mah dinsa na gefe tana karra talafa masa da shawarwari da adu'a, sannan matarsa na gabansa tana bashi dukan kulawar da ta dace

Karra kame kansa da yi , ya daina harkar biye biyen mata sai ya karra wanzar da lamari na shayi, da tsoron haye masa, harma da yawa kan masa ikirari da sunna *DUTSE AJIYAR ALLAH, KA FI KARFIN GARA*

Iman ta kama kanta, ta kwatanta har ciwo ta yi sai dai fahimtar da ta yi ba yarenta yake ganewa ba, matarsa kuwa ta mayar da ita taamkar mahaukaciya domin har tsokanarta take tana kuma bata tsoron cewa zafa ta fada masa ita ta fada mata maganar mata, sai kwata kwata ta nemi danganaa ta yafawa kanta harma ta fara ba samari damar zuwa wajenta dan ta fitar da gwaninta tunda zamtowa sarauniyar ingila ya gagareta kiri da muzu

Tashin hankali aka sha na rigimar aikinta
Sosai ta tayarwa da kowa hankali har sai da aka sadata da Oga da Mamanta inda Oga ya ja doguwar rantsuwa ya dire kan cewa idan ta tagawa sarki hankali a kan rabe raben kayan abinci a cikin jirgi in ba sai ya biya jirgi da aljihunsa ba ya zo ya ci yan garin babarta ba Allah ya sa kar ya ci zaben zama mai anguwar anguwarsa da yake nema, idan kuma wasa take gannin yake ga babarta ta fada mata

Ai kam mamantamaa maimakun ta saurareta sai ta rufe ido ta dora daga inda ya tsaya ta ce bataa cikin wannan shirme,

Gannin dai zasu karra rikita masa abarsa bayan rarashinta yake, lalabat yake kamar kwai,, domin tunda Mah ta kwatanta masa ba ita daya bace haka kuma kar a yi ta sani dana kar ta hanna kanta sukuni duba da haki zanen rai sai ya mayar da ita abu mai darajar daa ya fi tatalawa fiye da komai a duniyarsa,, baya wasa da laamarin yar Oga, baya wasa da soyayar yar oga , itace ta farko kuma yana fatan ta birne shi
Dan haka ya riko abinsa ya rungume a jikinsa sosai a sanyaye ya ce" Kin ga aiki ne da ni a nan, idan na ce zan bari na bijirewa Pah na koma tukin jirgi yaya kike so na gama da duniya ne? Ko har yanzu bakya sona bakya so na gama da duniya lafia ne?"

Da sauri ta girgiza kanta tana karraa cusa kanta a wajen wuyansa a sanyaye ta ce" Hanja ina sonka fa "

Idannuwansa ya lumshe dan jin dadin kalamanta, ta sha fada masa aman idan yana aikata mata aiki mai lada, a haka garas sai dai idan kubce mata maganar ta yi,
A hankali ya ce" Muneerath ina son ki sosai"

Dan murmushi ta yi a hankali ta ce" Shikenan ba zan kuma aikina ba?"

Yana shafa mararta yana karasawa kusa da gadonsu ya dan haya sama da hannunsa wajen abinda yake son cinma ya dan shiga lailaya a hankali ya ce" Zaki yi, idan kina tafia da mijinki sai ki bani ruwa na sha, ki bani abinci na ci, sannan ki dafan bujenki....."

Da sauri ta rufe masa baki tana jansa saman gadon suka fada da karfi sannan ta ja masu labulen jikin bed dinsu gannin ina tata son lekawa

Daga wannan na kawo karshen labarina mai sunna DUTSE a page 70 □□□□□□□□□□□□□□

Alhamdulilah alhamdulilah

YAH ALLAH KA YAFE MIN KURA KUREN DAKE CIKINSA, KA BANI LADAN DAKE CIKINSA ALLAHNA

DUKAN MAI SON CI GABA DA KARANTA LABARAINA YA GARZAYO YA BIYA KUDIN NASA WATAU *WATA KOKOWAR* A NAIRA DARI BIYU KACAL TA HANYAR YIN TRENSFER KO TURO KATIN MTN IN SHA ALLAH

GA NUMBER NAWA 93811618 SAJIDA □□□□□□□□